**Jamhuriyyar Misra Ta Larabawa**
**Ma'aikatar Awƙaf**

# HUDUBOBIN DA SUKA DACE DA ZAMANI

**Hukumar bayar da fatawa da bincike na da'awa, da hukumar karantarwar addini a Ma'aikatar Awƙaf- Misra**

**Tarjama**

**Saleh Abubakar Kaura, Zaria**

**Kulawa Da Gabatarwa**

**Farfesa Muhammad Mukhtar Juma'a**
**Ministan Awƙaf**

**Sunan Littafi: Hudubobin da suka dace da Zamani**

**Shafuka: (618)**

**Tsarawa: Hukumar bayar da fatawa da bincike na da'awa, da hukumar karantarwar addini a Ma'aikatar Awƙaf- Misra**

**Kulawa Da Gabatarwa: Farfesa Muhammad Mukhtar Juma'a – Ministan Awƙaf**

**Tarjama: Saleh Abubakar Kaura, Zaria**

**Bugu: Na Farko**

**Shekara: 1441 H / 2020**

**Hakkin Mallaka: Ma'aikatar Awƙaf - Misra**

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

## GABATARWA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga cikamakon Annabawansa da Manzanninsa, shugabanmu Annabi Muhammadu ɗan Abudullahi, da Alayensa da Sahabbansa, da waɗanda suka bi shiriyarsa har zuwa ranar sakamako, bayan haka:

A matsayin gudummuwar wajen yaɗa daidaitacciyar fahimta mai cike da haske da mabambanta harsunan duniya, muna cike da jin daɗin gabatar da juzu'i na farko na ***"Huɗubobin da suka dace da Zamani"*** da harshen Hausa, domin ya zamo guzuri na ilimi ga limamai da masu huɗuba waɗanda suke gabatar da huɗubar Juma'a da harshen Hausa. Muna kuma fatan ya zamo guzuri na ilimi da wayewa ga ɗaukacin masu magana da harshen Hausa a fagen daidaitacciyar fahimta mai cike da haske.

**Farfesa Muhammad Mukhtar Juma'a**
**Ministan Awƙaf**
**Shugaban Majalisar ƙoli ta addinin Musulunci**
**Mamba a cibiyar bincike na Musulunci**

**- 1 –**

## DALILAI GAMI DA TASIRIN KASANCEWA TARE DA ALLAH MAI GIRMA DA BUWAYA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Shi ne wanda ya halicci sammai da ƙasa da abubuwan da suke tsakaninsu cikin kwanaki shida, sannan ya daidaita akan al'arshi domin gudanar da mulkinsa, ya san duk abin da yake fakuwa a cikin ƙasa, da abin da yake fitowa daga gareta, da abin da yake saukowa daga sama, da ma wanda yake hawa saman, shi Allah yana da cikakkiyar masaniya akanku, da ma al'amurran da kuke ciki a duk inda kuke yana tare da ku, kuma Allah ya san abin da kuke aikatawa, tuni ya riske shi babu wani abu daga ciki da yake iya ɓuya masa)) [al- Hadid: 4]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Lallai zamantowa tare da Allah Maɗaukakin Sarki yana da ma'anoni iri - iri, a cikin waɗannan ma'anonin akwai na hararo Allah a dukan yanayi, akwai kuma na ƙarfafawa, na farkon

yana nufin irin yanda sanin Allah Maɗaukakin Sarki ya mamaye dukan halittunsa, Allah mai girma da buwaya yana cewa: **((Mabuɗan gaibi gaba ɗayansu suna wurinsa, babu wanda ya san su sai shi kaɗai, yana sane da duk wani abu da yake a tudu, ko a kogi, babu wani ganye da yake faɗi face ya san shi, kai hatta ƙwaya a cikin duhun ƙasa, ko wani abu busasshe, ko ɗanye face yana nan a bayyanannen littafi..))** **[al-An'am: 59]**, haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shin ba ka san cewa lallai Allah ya san abin da yake a sammai da abin da yake a ƙasa ba, babu wata ganawa ta sirri da take gudana tsakanin mutane uku, face ya zama na huɗunsu wajen sanin abin da suke ganawar da shi, ko mutane biyar, face ya zamo na shida, kai, da ma waɗanda ba su kai haka ba, da ma waɗanda suka wuce haka, face yana tare da su, ya san abin da suke ganawa akansa a duk inda suke, sannan kuma zai ba su labarin duk abin da suka aikata a ranar alƙiyãma, lallai Allah yana da cikakkiyar masaniya akan komai**)) **[al- Mujadalat: 7]**, haka ma mabuwayin Sarki yana cewa: **((Shin ashe wanda ya halicci komai ba shi ne ya san dukan halittarsa ba?! Shi ne masanin komai, manya da ƙanana, shi ne kuma ya san haƙiƙaninsu?!**)) **[al- Mulki: 14]**.

Na biyun kuwa yana nufin zamantowa tare da Allah Maɗaukakin Sarki ta hanyar ƙarfafa bawa, da ba shi dacewa da kariya, da taimako gami da kulawa, wannan kam Allah Maɗaukakin Sarki ya keɓance Manzanninsa, da Annabawansa, da waliyyai salihai ne da shi cikin bayinsa, lallai ayoyi da dama a cikin Alƙur'ani mai girma sun yi nuni zuwa ga wannan baiwa mai girma, ta kasancewa tare da Allah da zaɓaɓɓu daga cikin bayinsa suka samu, ga maganar da Allah Maɗaukakin Sarki

nan ya yi wa Annabawa biyu masu girma cikin Annabawansa - wato Sayyiduna Musa da Sayyiduna Harun (Alaihimas Salam), a inda yake cewa: **((Kai da ɗan uwanka ku tafi tare da ayoyi na, kada ku yi nauyin jiki wajen ambato na, ku tafi wurin Fir'auna saboda lallai ya wuce gona da iri, ku yi masa magana mai taushi da za ta iya sanya shi ya wa'aztu, ko kuma ya ji tsoron Allah. Sai suka ce: ya Ubangijinmu, lallai muna tsoron kada ya cutar da mu, ko kuma ya yi girman kai. Sai ya ce: kada ku ji tsoro, lallai ni ina tare da ku, ina ji, ina kuma gani..))** **[Taha: 42 – 46]**, kuma wannan kasancewa tare da Allah ne Annabi Musa (AlaiHis Salam) ya yi magana akanta lokacin da mutanensa suka zaci cewa Fir'auna da rundunarsa sun riske su, babu batun tsira daga zaluncinsa, sai suka ɗaga murya suna cewa: **((Lallai kam sun riske mu sun gama))** **[as- Shu'ara': 61]**, sai Sayyiduna Musa (AlaiHis Salam) ya amsa masu cikin yaƙini da sakankancewar Allah yana tare da shi, zai kuma ƙarfafe shi ya kuma taimake shi, cewa: **((Sai ya ce: ko kusa, lallai Ubangiji na yana tare da ni, zai kuma taimake ni))** **[as- Shu'ara': 62]**.

Ita ce dai kasancewa tare da Allah Maɗaukakin Sarki da ta faru da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da sahabinsa as-Siddiƙ (Allah ya ƙara yarda da shi), a lokacin hijira, inda Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) yake cewa: Ina tare da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) a cikin kogo, na hango ƙafafuwan mushrikai, sai na ce: Ya Manzon Allah, da a ce ɗaya daga cikinsu zai duba wurin ƙafafuwansa, da kuwa ya ganmu, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Haba Abubakar, mene kake zato da mutane biyun da Allah ne na ukunsu?!)**, akan haka ne ma Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((In ma ba ku taimaka wa Annabi Muhammadu**

**(SallalLahu alaiHi wa sallam) ba, to ku sani tabbas Allah ya riga ya taimake shi a lokacin da kafirai suka fitar da shi daga garin Makka su biyu, lokacin da suke cikin kogo da yake faɗa wa abokinsa cewa: kada ka damu, lallai Allah yana tare da mu, sai Allah ya saukar masa da natsuwa, ya kuma ƙarfafe shi da rundunar da ba ku iya ganinta, ya kuma sanya kalmar kafirai ta zamo a ƙasa, lallai kalmar Allah ita ce a sama, tabbas Allah cikakken mabuwayi ne, mai kuma cikakkiyar hikima)) [at- Tauba: 40].**

Wane abu ne ya kai girman a ce bawa yana tare da Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka, duk wanda yake tare da Allah, to ba shi da wata damuwa na mutane suna tare da shi, ko ba sa tare da shi, idan har bawa yana son ya sami kasancewa tare da Allah Maɗaukakin Sarki, to dole ne ya shiga wannan kusancin ta ƙofofin da suke isarwa zuwa ga haka, dole ne kuma ya cika sharuɗɗa da dalilan da za su ba shi daman samun haka, a cikin manyan ƙofofin akwai: **samar da cikakken imani da Allah Maɗaukakin Sarki,** mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai Allah yana tare da masu imani)) [al- Anfal: 19]**, shi kuwa imani -kaman yanda Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ambata ne- **(Ka gasgata samuwar Allah, da samuwar Mala'ikunsa da littattafansa da Manzanninsa, da ranar lahira, ka kuma yi imani da ƙaddara ta alhairi da ta sharri)**, imani na ainihi kuma shi ne wanda tasirinsa ya bayyana a rayuwar mutum, da mu'amalarsa tare da mutane, saboda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Musulmi na gaskiya shi ne wanda mutane suka kuɓuta daga sharrin harshensa, da na hannunsa, shi kuwa mumini shi ne wanda mutane suka amince masa a jininsu da dukiyoyinsu)**.

Haka ma a cikin ƙofofin akwai: **bawa ya samar wa kansa da tsoron Allah gami da matsayin Ihsani**, Allah mai girma da buwaya yana cewa: **((Lallai Allah yana tare da waɗanda suka ji tsoron Allah, da kuma waɗanda suke kyautatawa)) [an- Nahli: 128]**, a wani wurin kuma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku sani cewa lallai Allah yana tare da masu tsoron Allah)) [al-Baƙra: 194; at- Tauba: 36, 123]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Tabbas lallai Allah yana tare da masu kyautatawa)) [al-Ankabut: 69]**, shi tsoron Allah shi ne: aiwatar da duk wani abu da Allah Maɗaukakin Sarki ya yarda da shi, da kuma nesantar duk abubuwan da yake fushi da su, tsoron Allah ne matattara na dukan alhairai, lallai Alƙur'ani mai girma ya bayyana ma'anarsa a ayoyi da dama, kaman yanda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Kai, lallai mutane sun yawaita magana akan al'amarin alƙibla, kai kã ce ita ce alhairi ita ɗaya kacal, wannan kuma ba shi ne gaskiya ba, ba fuskantar wani sashe a gabãshi ko yammaci shi ne kashin-bayan addini ko matattara alhairi ba, matattara alhairi yana cikin abubuwa ne masu dama, wasu suna cikin rukunnan ingantacciyyar aƙida ne, wasu kuma suna cikin tushen ayyuka na gari da ibadu. Na farko shi ne: imani da Allah, da ranar tashin alƙiyama, da hisabi, da abubuwan da za su biyo bayan haka a ranar alƙiyama, da imani da mala'iku da littattafan da aka saukar wa Annabawa, da ma su kansu Annabawan. Na biyu shi ne: bayar da dukiya cikin jin daɗin rai ga talakawa makusanta da marayu da waɗanda buƙatu da rashi suka yi masu yawa, da matafiyan da guzuri ya yanke masu, ba su da abin da zai isar da su zuwa ga manufarsu, da masu roƙon mutane da buƙata ta tilasta masu yin haka, da kuma ciyarwa domin manufar**

**‘yanta bayi da ‘yanta wuyayensu ga barin bauta. Na uku: kiyaye sallah. Na huɗu: fitar da zakkar da aka wajabta. Na biyar: cika alƙawari a rai da dukiya. Na shida: haƙuri akan cutar da za ta faɗa wa rai ko dukiya, ko lokacin haɗuwa da abokan gaba a wurin yaƙi. Waɗanda suka haɗa waɗannan aƙidu da ayyuka na alhairi su ne waɗanda suka yi gaskiya cikin imaninsu, su ne waɗanda suka ji tsoron kafirci da ƙasƙanci, suka kuma nesance su)) [al- Baƙra: 177].**

Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Kada ku yi wa junanku hassada, kada kuma ku taya kaya da tsada da niyyar yaudarar masu saye, kada ku ƙetaci juna, kada ku juya wa juna baya, kada ku yi tayi akan cinikin juna, ku zamo bayin Allah 'yan uwan juna, shi Musulmi ɗan uwan Musulmi ne, ba ya zaluntarsa, ba kuma ya bayar da shi, ba kuma ya wulaƙanta shi, tsoron Allah yana nan –ya yi nuni zuwa ga ƙirjinsa sau uku- sharri ya kai sharri a ce mutum yana wulaƙanta ɗan uwansa Musulmi, Jinin Musulmi, da dukiyarsa, da mutuncinsa sun haramta wani Musulmi ya keta su).**

Shi kuwa “Ihsan” kaman yanda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana haƙiƙanin ma’anarsa da cewa: **(Ka bauta wa Allah kamar kana ganinsa, idan dai har kai ba ka iya ganinsa, to kuwa tabbas shi yana ganinka)**, a nan ne bawa yake samar da cikakken hararo da Allah Ubangiji mai girma da ɗaukaka a cikin dukan yanayinsa, ya kuma sami cikakken yaƙinin cewa lallai Ubangijinsa bai rafkana ga barinsa ba a cikin halin sirrinsa, ko a bayyane, a cikin dukan motsinsa da rashin motsinsa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shin bai san cewa Allah yana ganinsa ba ne?!)) [al- Alaƙ: 14].**

Haka ma a cikin ƙofofin kasancewa tare da Allah Maɗaukakin Sarki akwai: **haƙuri,** Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Ku yi haƙuri, lallai Allah yana tare da masu haƙuri))** **[al- Anfal: 46]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((Ka yi wa masu haƙuri albishir, su ne waɗanda idan wata masifa ta same su, sai su ce: mu da ma can bayi ne mallakar Allah Maɗaukakin Sarki, ku wurinsa za mu koma. Waɗannan kam, su ne suke da babban matsayi da rahama a wurin Ubangijinsu, lallai kam, waɗannan su ne shiryayyu))** **[al- Baƙra: 155 – 157]**, haka ma Allah mai girma da ɗaukaka ya ce: **((Ka yi haƙuri da hukuncin Ubangijinka na jinkirta masu da ya yi, da kuma cutarwarsu da take samunka, lallai kai ɗin nan kana ƙarƙashin kiyayewa da kulawarmu, makircinsu ba zai taɓa cutar da kai da komai ba, ka yi tasbihi tare da godiya ga Ubangijinka a lokacin da za ka tashi))** **[at- Tur: 48]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ka sani cewa akwai alhairai masu yawa a cikin yin haƙuri da abin da kake ƙi)**, shi haƙuri shi ne: hana rai damuwa, da hana harshe yin ƙorafi, da kuma hana gaɓoɓi rashin nuna godiyar Allah, wannan kuwa yana samuwa ne ta hanyar yaƙar zuciya, wannan shi ne mafi alhairin baiwa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(.. Duk wanda ya ƙoƙarta yin haƙuri, to kuwa Allah zai ba shi haƙuri, lallai ba a taɓa bai wa wani bawa wata baiwa da ta fi alhairi da yalwa sama da haƙuri ba)**.

Haka ma a cikin dalilan shiga cikin kasancewa tare da Allah Maɗaukakin Sarki akwai: **kasancewar zuciya a farke;** duk wanda zuciyarsa take a farke zai riski cewa lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana tare da shi a dukan yanayin da yake ciki, shin a halin tafiya ne, ko zaman gida, a ɓoye yake, ko a fili, shi Allah babu wani abu da yake iya ɓuya masa, sirri ko ƙarara

duka ɗaya suke a wurinsa, a wannan yanayin ne Annabin Allah Yusuf (AlaiHis Salam) ya kasance lokacin da aka kulle dukan ƙofofi, aka kuma samar masa da duk wasu dalilai na saɓon Allah, sai kuwa ya nemi tsari daga Ubangijinsa, da ya san cewa yana tare da shi a kowane yanayi, sai kuwa harshensa ya cigaba da maimaita: **((Lallai Allah shi ne Ubangijina da ya kyautata makoma ta, babu shakka tabbas azzalumai ba za su sami babban rabo ba))** **[Yusuf: 23]**, wannan ne kuma abin da matar Sarki ta faɗi, kaman yanda Alƙur'ani mai girma ya bayyana ta bakinta cewa: **((Haƙiƙa na neme shi sai ya nemi tsarin Allah..))** **[Yusuf: 32]**, lallai falalar kasancewa tare da Allah abu ne mai mai girma a lokacin da bawa ya mallaki tsoron Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka a duniya, sai kuma ya sami aminci ga barin azabarsa a ranar alƙiyama, Hadisi Ƙudusi ya zo cewa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Na rantse da buwaya ta, ba zan haɗa wa bawa na tsoro guda biyu ba, ba kuma zan haɗa masa aminci biyu biyu ba; idan ya aminta da ni a duniya, to kuwa zan tsoratar da shi a ranar alƙiyama, idan kuma ya ji tsoro na a duniya, to kuwa zan amintar da shi a ranar alƙiyama)**.

Haka ma bawa yana samun kusanci da Allah Maɗaukakin Sarki ta hanyar **ambaton Allah Maɗaukakin Sarki**: Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ku ambace ni, sai ni ma na ambace ku, ku gode mini, kada ku butulce mini))** **[al- Baƙra: 152]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: Ni kam ina nan yanda bawa na ya zace ni, ina tare da shi idan ya ambace ni, idan ya ambace ni a ransa, zan ambace shi a raina, idan ya ambace ni a cikin jama'a, zan ambace shi a cikin jama'an da suka fi nasa alhairi..)**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-----------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa baki ɗaya, da waɗanda suka bi shi da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai kasancewa tare da Allah Maɗaukakin Sarki yana da tasiri mai girma da bawa yake cin gajiyarsa a duniya da lahira, a cikin wannan gajiyar akwai: duk wanda ya sami kusanci da Allah mai girma da ɗaukaka, **to kuwa Allah zai kare shi daga dukan sharri, zai kuma warkar da shi ga barin dukan cuta**, Allah mai girma yana cewa: **((Su ne waɗanda wasu mutane suka ce masu: tabbas wasu mutane suna nan sun tattaru suna dakonku, saboda haka ku ji tsoronsu, sai hakan ya ƙara masu imani, sai suka ce: Mu kam Allah ya ishe mu, kai madalla da wakili Allah)) [Ali Imran: 173]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((Duk wanda ya miƙa al'amurransa zuwa ga Allah, to Allah zai yi masa komai, lallai Allah zai isar masa da nufinsa, tabbas shi mai zartar da abubuwan da yake so ne, lallai Allah ya sanya wa komai lokacin da ba zai ƙetare ba, da kuma iyakan da ba zai wuce ba)) [al- Talaƙ: 3]**; ma'ana: ya isar masa, Allah mabuwayi yana cewa: **((Ashe Allah bai isar wa bawansa ba?!)) [az- Zumar: 36]**, duk wanda ya dogara da Allah, ya kuma sakankance da isarsa,

to kuwa babu yanda maƙiya za su yi da shi, ba kuma zai taɓa rasa abin da duk ya nema ba, duk abin da yake so kuma ba zai taɓa yi masa fauti ba, a duk sanda muka tsaya a gaban maganar da Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗa wa Sayyiduna Musa (AlaiHis Salam) cewa: **((Kuma saboda komai za a yi maka a yi shi a ƙarƙashin kulawa ta))** [Taha: 39], da inda Allah mai girma yake cewa: **((Na zaɓe ka saboda kai na))** [Taha: 41], da kuma inda Allah mai girma da buwaya ya faɗa wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa: **((Ka yi haƙuri da hukuncin Ubangijinka na jinkirta masu da ya yi, da kuma cutarwarsu da take samunka, lallai kai ɗin nan kana ƙarƙashin kiyayewa da kulawarmu, makircinsu ba zai taɓa cutar da kai da komai ba))** [at- Tur: 48], da inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Ka yi wa waɗanda suka yi imani da Allah albishir ɗin cewa: lallai suna da wani babban matsayi na gaskiya a wurin Ubangijinsu..))** [Yunus: 2], a nan za mu riski girman matsayin kasancewa tare da Allah, da kuma falalar haka, da kyakkyawan tasirinsa.

Babu shakka samun kusanci da Allah Maɗaukakin Sarki, da kasancewa ƙarƙashin kulawarsa **hanya ce ta samun natsuwa da kwanciyar hankali da cikakken natsuwar zuciya mafi muhimmanci**, da kuma nesantar duk wani tashin hankali, da damuwa, gami da ƙunci; ta ma yaya ne mutumin da yake riƙo da sabubba zai shiga cikin damuwa, mutumin ya riga ya riski cewa komai yana hannun Allahn da duk abin da ya so cewa yake da shi ya kasance, kuma ya kasance nan take?!, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya kai wannan Annabi (SallalLãhu alaiHi wa sallam), ka ce –kana cikin halin miƙa-wuya ga Allah, kana kuma tabbatar da ƙarfin ikonsa- Ya**

**Ubangiji, kai –kaɗai ne- mamallakin dukan tasarrufi a cikin komai, kana bayar da mulki da iko ga wanda ka so, kana kuma sance shi ga wanda ka so, kana bayar da girma ga wanda ka so cikin bayinka, ta hanyar katartad da shi zuwa ga hanyar girma da dalilanta, kana kuma sanya ƙasƙanci da wulaƙanci ga wanda ka so, lallai kai kaɗai ne kake mallakan alhairi, babu wani abu da zai gajiyar da kai wajen zartad da abin da kake nufi, da abin da hikimarka a cikin tsarin halittunka ta tabbatar))** **[Ali Imran: 26]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Duk abin da Allah ya buɗa wa mutane na rahamarsa babu wanda ya isa ya hana, duk kuma abin da ya riƙe bai ba su ba, babu wanda ya isa ya ba su bayan shi, shi ne mabuwayi mai cikakkiyar hikima))** **[Fatir: 2]**.

Lallai idan zukatan bayi suka ji cewa suna tare da Allah Maɗaukakin Sarki, suka kuma hararo girmansa, **to kuwa babu shakka za su sami cikakken tsoro da aminci a cikin zukatansu, da kuma kyautata zaman tare, da tsaro na bai ɗaya;** domin idan bayi suka sakankance cewa ba za su taɓa iya ɓuya wa kallon da Allah Maɗaukakin Sarki yake masu ba, to kuwa rayuwarsu za ta daidaita, ɗabi'unsu kuma za su yi kyau, sai su zamo masu yi wa umurnin Ubangijinsu biyayya, masu kuma nesantar abubuwan da mai girma da ɗaukaka ya hana, su kuma tsaya a inda ya yi masu iyaka, su kuma yi riƙo da sabubba saboda su gyara duniyarsu da addininsu, sai mutum ya rayu cikin aminci tare da kansa, da iyalansa, da danginsa, da maƙwantansa, da abokan aikinsa ba, da abokan rayuwarsa, da ma al'ummarsa, da sauran mutane baki baki ɗaya, lallai wannan shi ne saƙon Musulunci da ya zo a matsayin rahama ga ɗaukacin halittu.

**Ya Allah Ubangiji muna roƙonka ka shigar da mu cikin kusancin nasararka da ƙarfafawarka, ka game mu da mayalwaciyar falalarka, ka lulluɓe mu da bargon ni'imominka, ka azurta mu da ikhlasi a cikin dukan al'amurranmu, ka kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya baki ɗaya.**

## -2-

## WANNAN SHI NE MUSULUNCI..

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Lallai aikata aikin alhairi yana tasowa daga nagartaccen imani ne, kuma mafin ingancin addini shi ne tsarkake zuciya saboda Allah Maɗaukakin Sarki shi kaɗai, ta yanda mutum zai aikata komai nasa domin Allah shi kaɗai, ba kuma tare da neman komai ba banda yardar Allah Mai girma da ɗaukaka, da haka ne kawai Allah zai daidaita masa fahimtarsa, a sakamakon haka kuma ya riski saƙon da Manzanni suka zo da shi, su kuma cigaba wajen wannan sifa ta aikata mafi kyawon ayyukan, suna masu koyi da baban Annabawa, Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm), saboda lallai addinin da ya zo da shi, shi ne addinin Allah, shi ne kuma addinin da a koda yaushe yake tattare da gaskiya, lallai Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm) cibiya ne da addinin Musulunci, da Yahudanci, da Kiristanci suke haɗuwa, saboda haka ku bi turbasa, lallai Allah ya karrama Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm) ya sanya masa suna "al-Khalil"))** **[an- Nisa'i: 125]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Lallai Musulunci na gaskiya shi ne miƙa – wuya, da biyayya da sallama al'amurra ga Allah Mai girma da buwaya, da soyayya, da bi, gami da koyi da Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam), da kyawon ɗabi'u, da ƙasƙantar da kai cikin tsoron Allah, da sauƙin kai, da sakin fuska wajen yin mu'amala da ɗaukacin mutane, da kuma tausayi da jinƙai, da kyakkyawan dangantaka tare da ɗaukacin halittu, da gina ƙasa, da samar da cigaba, lallai Musulunci tsari ne na rayuwa da mabiyansa suke amfani da shi a dukkan yanayin da suke ciki.

Lallai Musulunci addini ne da yake kira zuwa ga gyara kai, da kuma gyara duniya, da raya duniya da addini, bai wai rusa ta da sunan addini ba, addini ne da yake kira zuwa ga rahama, da tsaro, da aminci, da zaman lafiya ga ɗaukacin duniya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai ba mu aiko ka da saƙon ba, sai domin ka zamo rahama da ɗaukacin halittu))** **[al-Anbiya'i: 107].**

Lallai duk wanda zai yi wa rukunnan Musulunci da suka zo a Hadisin mala'ika Jibrilu (AlaiHis- Salam), lokacin da ya tambayi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) kallo na lura, musamman inda yake cewa: ya Muhammadu, mene ne Musulunci? Sai ya ce: **(Musulunci shi ne: ka shaida babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah, kuma tabbas Muhammadu Manzon Allah ne, ka kuma tsayar da Sallah, ka bayar da Zakka, ka yi Azumin watan Ramadhan, ka hajjanci ɗakin Allah idan ka sami dama..)**, duk wanda ya lura da wannan, zai fahimci cewa lallai rukunnan na Musulunci suna taka – muhimmiyar - rawa wajen samar da ɗan Adam nagari, idan har

ɗan Adam ya yi imani da kaɗaituwar Allah, ba shi da abokin tarayya, kuma ya yi imani da cewa lallai Shugabanmu Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) bawan Allah ne kuma Manzonsa, zai yi iya ƙoƙarinsa wajen tabbatar da wannan shaidawar, ta hanyar yi wa Allah biyayya, da kuma hararo Allah Maɗaukakin Sarki a cikin dukan yanayin da yake ciki, zai zamo mai bin dukan umurninsa, ya kuma nesanci dukan abubuwan da ya hana, ya kuma tsaya akan iyakan da ya iyakance, ba ya yin ƙasa - a - gwiwa wajen zartar da abubuwan da aka wajabta masa, ba kuma ya neman abubuwan da ba haƙƙinsa ba, haka kuma, ya yi iya abin da zai iya wajen kyautata koyi da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), yana mai yi wa mutane mu'amala kaman yanda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake mu'amala da su, ƙarƙashin rangwame, da jinƙai, da tawali'u, da sauƙin kai.

Lallai sallah ita ce babban rukuni daga cikin rukunnan Musuluci, wadda amfaninta yake dawowa zuwa ga bawa; tana hana shi aikata alfasha, ta kuma daidaita tafiyarsa akan hanyar Allah Maɗaukakin Sarki, hakan sai ya sanya Musulmi ya rayu cikin aminci, da zaman lafiya tare da kansa, da kuma tare da ɗaukacin al'umma, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ka karanta abin da aka yi maka wahayi na Alƙur'ani, ka kuma tsayar da sallah, lallai sallah tana hana alfasha, da abubuwan ƙyama, lallai ambaton Allah shi ne ya fi girma, Allah ya san abubuwan da kuke aikatawa)) [al- Ankabut: 45].**

Shi kuwa bayar da zakka yana ɗauke da fuskokin imani, da ayyukan jinƙai, da na mutuntaka; yana tsarkake zuciya daga ɗamfaruwa da tarkacen duniya, ta yanda mutum zai fahimci cewa, ita dukiya hanya ce ta biyan buƙatu, ba wai ita ce ƙarshen

manufa ba, kuma dama ce ta yin taimakekeniya, da sada zumunci, da damuwa da abubuwan da suke damun sauran mutane, ita al’ummar Musulma ta gaskiya ba ta san wani abu wai shi son kai ba, ba kuma ta san rashin nuna damuwa da damuwar al’umma, ko zura idanu ba tare da an ɗauki matakin kawo gyara ba, shi addininmu addini ne na baiwa, da kyauta, da sadaukar da kai, da fifita wasu akan kai, ba addinin rowa, da ƙoro, da ƙamƙamo ba, shi mumini mutum ne mai yawan baiwa, da kyauta, da karamci, a lokacin da Allah Maɗaukakin Sarki yake yabon al- Ansar (mutanen garin Madina) cewa ya yi: ((**Su kuwa mutanen da suka sauka garin Madina, suka zamo 'yan gari, suka kuma kyautata imaninsu tun kafin waɗanda suka yi hijira su zo masu, suna son Musulman da suka yi hijira zuwa gare su, ba kuma sa jin ƙyashin komai a cikin zukatansu game da abubuwan da aka bai wa "al-Muhajirun" na ganimar da aka samu ba tare da an yi yaƙi, ko ɗaura ɗammara don yin sa ba (al-Fai’u), suna kuma gabatar da buƙatun waɗanda suka yi hijira akan buƙatun kawunansu, koda kuwa suna tsananin buƙata. Duk wanda aka kiyaye shi –da kiyayewar Allah- daga barin tsananin ƙwauron zuciyarsa, to, lallai su ne suke da babban rabo cikin duk abin da suka so**)) **[al- Hashri: 9].**

Haka ma Azumi, shi ma yana daidaita ɗabi’un Musulmi, ta hanyar dawwama wajen hararo Allah Maɗaukakin Sarki, yana kuma horas da shi akan haƙuri, da jure wahalhalu, da ɗaukaka ran ɗan Adam, da girmama shi ta hanyar ƙaurace wa duk abubuwan da Allah Maɗaukakin Sarki ba ya so. Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(..Azumi garkuwa ne, idan ranar azuminku ya yi, kada ku yi zance batsa, kada**

**kuma ku yi faɗa- faɗa, idan wani ya zage ku, ko ya neme ku da faɗa, to ku ce: mu muna azumi..)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk bai bar maganar ƙarya, da aiki da ita ba, to babu ruwan Allah da barin cin abinci da abin sha da ya yi).**

Haka ma aikin Hajji, yana nufin mahajjanci ya lizimci tsarin rayuwa, da wasu ɗabi'u tun kafin hajjin nasa, da lokacin da yake gudanar da shi, da bayan kammala ayyukansa na ibadu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Hajji na kasancewa ne a wasu watanni da kuka sani, domin dai al'amarin Hajji sananne ne a wajenku tun zamanin Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm), wanda shi ne: watan Shawwal, da Zul- ƙi'ida, da Zul-haj, duk wanda ya ƙuduri aniyar aikin Hajji a cikin waɗannan watanni, ya kuma fara shi, to, ya kiyaye ladubbansa, cikin ladubban Hajji: lallai ne mai harama ya tsarkaka ga barin kusantar mata, da saɓo na zagi, da makamantan haka, haka ma ya nesanci gardama, da ba'a tare da waninsa cikin mahajjata, ya nesanci duk wani abin da zai kai zuwa ga faɗa, da husuma, duka wannan saboda mahajjanci ya fita daga harami yana cikin tsarkake zuciya, ya yi ƙoƙari matuƙa wajen aikata alhairi, da neman lada daga Allah, ta hanyar aikata ayyuka na gari, lallai Allah yana da cikakken masaniya game da haka, zai kuma saka masa akan haka, ku yi guzuri da tsoron Allah, da bin umurninsa, da nesantar haninsa; saboda lahirarku, lallai wannan shi ne fiyayyen guzuri, ku ji tsoron Allah akan abin da kuke aikatawa, da wanda kuke bari, kamar dai yadda hakan shi ne aiki da hankali da hikima, kada ku gurɓata ayyukanku da tabban son zuciya, da neman duniya))** **[al- Baƙra: 197]**, an ruwaito

Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Na ji Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya yi aikin Hajji, bai saki bakinsa wajen zancen batsa ba, bai kuma aikata fasiƙanci ba, to zai dawo tamkar ranar da mahaifiyarsa ta haife shi)**, haka ma dukan rukunnan Musulunci suna da tasirin da yake dawowa ga al'umma da alhairai, da aminci gami da zaman lafiya.

Haka ma, lallai duk mai lura zuwa ga wannan addini namu mai tsarki, zai fahimci cewa addininmu, addini ne na kyawawan ɗabi'u, saƙon da ya zo da shi ma ya zo da shi ne domin cika waɗannan kyawawan ɗabi'un, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(An aiko ni ne domin in cika kyawawan ɗabi'u)**, duk inda yake akwai gaskiya, da cika alƙawari, da amana, da biyayya, da sadar da zumunci, da baiwa, da kyauta, da taimako, da gwarzanta, da mutunci, da rashin cutar da mutane, da taimakon waɗanda suke cikin damuwa, da bayar da tallafi ga masu nema, da yaye damuwa ga waɗanda suke cikin baƙin- ciki, da tausayin dabbobi, to a nan ne akwai ingantaccen Musulunci da manufofinsa.

Lallai fahimtar jauharin Musulunci, da sanin sirrorin saƙonsa masu rangwame, da gane manufofinsa masu daraja, da kuma zartar da abubuwan da aka ganen a aikace daidai da sababbin abubuwan da suka faru a zamani, da abubuwan da zamanin yake buƙata, duka wannan abubuwa ne da suka wajaba a yi su wajen fuskantar ƙalubalen zamani, da kuma yi wa ƙungiyoyin 'yan ta'adda, da masu wuce gona da iri burki, da kuma yi wa tsattsauran ra'ayi ƙawanya, da kuma keta kurin daƙiƙanci, da na rashin fahimta, da ma na guɓatattun fahimta, da rashin faɗin zukata, da fita daga irin wannan ƙuncin zuwa

ga fage mafi faɗi, da yalwa gami da sauƙi, fagen da ya fi zamowa aiki da hankali da wayewa, ya kuma fi nuna basira da ganewa, ya kuma fi zartar da maslahar ƙasa da na mutane, da yaɗa ɗabi'un mutuntaka masu girma, waɗanda su ne suke tabbatar da tsaro, da aminci, da zaman lafiya, da kwanciyar hankali, da jin daɗin ɗaukacin bil'adama.

Babban abin da ya wajaba akan kowane Musulmi, ya kuma fi muhimmancin ya gabatar, shi ne: ya bayyana wa ɗaukacin mutane fuskokin girman addinin Musulunci, ta yanda duniya gaba ɗaya za ta fahimci cewa, lallai addinin Musulunci addini ne na zaman lafiya, da yake kira zuwa ga zaman lafiya, yake kuma girmama sha'anin zaman lafiya, ita kalmar "As-Salam" suna ne daga cikin sunayen Allah Maɗaukakin Sarki, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Shi ne Allah wanda babu abin bauta wa da gaskiya sai shi, ainihin mamallakin komai, cikakken da babu wata tawaya tare da shi, kuɓutacce ga barin abin da bai dace da shi ba, amintacce ga barin naƙasa..)) [al- Hashri: 23],** gaisuwar Musulunci ita ce: "As- Salam", mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Kada ku kuskura ku ce wa wanda ya yi maku sallama: kai ba mumini ba ne..)) [an- Nisa'i: 94]**, haka ma, gaisuwar 'yan aljanna a cikin aljanna ita ce: "As- salam", Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Mala'iku suna shiga wurinsu ta dukan ƙofofi suna ce masu: Amincin Allah ta tabbata a gare ku sakamakon haƙurin da kuka yi, kai madallah da sakamakon gidan lahira)) [ar- Ra'ad: 23 -24]**, haka a cikin addu'o'in da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake yi bayan kowace sallah yakan ce:

"اللَّهُمَّ أَنْتَ السَّلاَمُ ، وَمِنْكَ السَّلاَمُ ، تَبَارَكْتَ يا ذَا الْجَلاَلِ وَالإِكْرَامِ".

Lallai Musulunci addini ne da yake kiyaye ɗan Adam da karamarsa, ya hana yi – da - mutane, da annamimanci, yana hana hassada da ƙiyayya, ya hana wulaƙanta mutane, ya kuma hana kowace nau'i na cutarwa; shin ta hanyar magana ce, ko aiki, kai har ma da nuni, koda da yatsa ne, Allah mai girma da buwaya yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, kada wasu mazaje daga cikinku su yi wa wasu mazaje na daban izgilanci, mai yiwuwa ne su kasance mafiya alhairi a wurin Allah sama da masu izgilanci. Kada kuma mata muminai su yi wa wasu matan muminai izgilanci, mai yiwuwa ne waɗanda aka yi masu izgilancin su fi alhairi a wurin Allah sama da masu izgilancin. Kada wani sashenku ya aibata wani sashe, kada wani daga cikinku ya kira ɗan uwansa da suna, ko laƙabin da ba ya so, lallai a ambaci mumini da sunan fasiƙanci bayan ya sifantu da imani abu ne mai muni ƙwarai, duk wanda bai dawo daga rakiyar haka, ya bar abubuwan da aka hana ba, to lallai shi ne –shi kaɗai- yake zaluntar kansa da ma wasunsa))** **[al- Hujrat: 11]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya nuna ɗan uwansa da ƙarfe, to kuwa mala'iku suna la'antarsa har sai ya bari, koda kuwa ɗan uwansa na uwa ɗaya uba ɗaya ne)**, haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya hana duka, da yin zane a fuska, lokacin da (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ga wata dabba da zane a fuskarta, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Allah ya la'anci wanda ya yi mata zane..)**.

Lokacin da aka tambayi (SallalLahu alaiHi wa sallam) game da wata mata, mai yawan azumi da ƙiyamullaili, kawai dai tana cutar da maƙwabtanta, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **('Yar wuta ce)**, haka ma Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa

sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to kada ya cutar da maƙwabcinsa, wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya girmama baƙonsa, wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya faɗi alhairi, ko ya yi shiru)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

--------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kafa karantarwar Musulunci masu cike da rangwame, da ɗabi'unsa na karamci, da ƙa'idojinsa masu tsarki, a cikin zukatan sahabbansa, abin da har suka zamo masu manhajin rayuwa da suke mu'amalantar ɗaukacin mutane da su, ga Sayyiduna Ja'afar Bn Abuɗalib (Allah ya ƙara yarda da shi) nan ya tsaya a gaban an- Najjashi –Sarki Habasha-, yana bayyana masa wasu daga cikin waɗannan ƙa'idoji, da kyawawan ɗabi'u, yana bayyana masa su da wani salo mai cike da ƙayatarwa, da kalmomi masu cike da imani da yarda da kai, yana cewa: "**Ya mai martaba Sarki, a da mu mutane ne da muke bauta wa gumaka, muna cin mushe, muna halatta abubuwan da aka haramta, muna aikata alfasha, muna yanke**

**zumunci, muna cutar da maƙwabta, mai ƙarfi a cikinmu yana danne mai rauni, a haka muke, har Allah ya aiko mana da Manzo daga cikinmu, mun san danginsa, da gaskiyarsa, da amanarsa, da kamewarsa, sai ya kira mu zuwa ga Allah; domin mu kaɗaita shi, mu kuma bauta masa, mu kuma ƙaurace wa abubuwan da mu da iyayenmu muke bauta wa maimakonsa na duwatsu da gumaka, ya kuma umurce mu da yin gaskiya wajen magana, da kiyaye amana, da sadar da zumunci, da kyautata maƙwabtaka, da kamewa ga barin abubuwan da aka haramta da jinanai, ya kuma hana mu aikata alfasha, da zancen ƙarya, da cin dukiyar maraya, da yi wa kamammun mata ƙazafi, ya umurce mu da mu bauta wa Allah shi kaɗai, kada mu haɗa shi da kowa, ya umurce mu da yin sallah, da zakka, da azumi..".**

Lallai Musulmi na gaskiya ba ya ƙarya, ba kuma ya algushi, ba kuma ya ha'inci.. Musulmi na gaskiya shi ne wanda mutane suka kuɓuta daga sharrin harshensa, da na hannuwansa.. Mumini na ainihi shi ne wanda mutane suka amince masa akan juninsu, da mutuncinsu, da dukiyoyinsu, da kawunansu.. Musulmi na gaskiya shi ne wanda ɗabi'un Musulunci suke bayyana a mu'amalolinsa, babu komai tsakaninsa da mutane sai alhairi, da biyayya.. Idan muna son mu samar da ma'anar cikakken Musulmi, ba za mu taɓa samun ma'anar da ta fi alhairi, ta kuma game komai sama da yanda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ba shi ba, inda ya nuna cewa: shi ne wanda mutane suka kuɓuta daga sharrin harshensa, da na hannuwansa, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Shin ba na faɗa maku wane ne mumini ba? Shi ne wanda mutane suka aminta masa a dukiyoyinsu, da**

**rayukansu, shi kuma Musulmi shi ne: wanda mutane suka aminta daga sharrin harshensa da hannayensa, Mujahidi kuma shi ne: wanda ya sabar wa kansa da yi wa Allah biyayya, Mai hijira kuma shi ne: wanda ya ƙaurace wa ayyukan kura- kurai da na zunubai)**.

Lallai saƙon Musulunci, saƙo ne na jinƙai, da azanci, da rangwame, da tausayi, da yalwa, da kuma rashin daskarewa, saƙo ne na haɗa kai, ba na rarraba kawuna ba, yana kusanto da jama'a ne, ba tarwatsa su ba, shi Musulunci gaba ɗayansa adalci ne, dukansa tausayi ne, da rangwame, da sauƙi, da mutuntaka, duk wani abu da zai tabbatar da waɗannan ma'anoni masu girma, to yana kan gaba a Musulunci, duk kuma abin da zai ci- karo da su, to lallai ya ci- karo ne da Musulunci, da manufofinsa.

**Ya Allah Ubangiji, muna roƙon ka shiryatar da mu zuwa kyawawan ɗabi'un da babu mai shiryatarwa zuwa mafi kyawonsu sai kai.. Ka nesanta mu da munanan ɗabi'un da babu wanda zai iya nesanta mu da mafi muninsu sai kai, ka kiyaye mana ƙasashenmu, da 'yan ƙasashenmu, da sojojinmu, da 'yan sandanmu daga barin duk wani abin ƙi da muni.. Ya mafi tausayin masu tausayi.**

## -3-

## SAKAMAKON DA IMANI YAKE GADARWA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Lallai waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma aikata ayyuka na gari Ubangijinsu zai shiryatar da su sakamakon imaninsu, inda ƙoramu za su gudana ta ƙarƙashinsu a cikin aljannar ni'ima))** **[Yunus: 9]**. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Allah Maɗaukakin Sarki -cikin ni'imominsa- ne ya sanya a ɗaukacin ayyuka na gari da bayinsa za su yi, suna da sakamako mai kyau da suke samunsu, a cikin manyan ayyuka na gari, da suke barin tasiri mai kyau ga mutum, da ma al'umma baki ɗaya akwai: **Imani da Allah mai girma da buwaya,** lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana haƙiƙanin imanin da ya kamata kowace zuciyar mumini ta ƙunsa, ya bayyana haka ne a lokacin da mala'ika Jibril (AlaiHis Salam) ya tambaye shi game da imani, sai ya ce: **(Ka gasgata samuwar Allah, da samuwar Mala'ikunsa, da littattafansa, da Manzanninsa, da ranar lahira, ka kuma yi imani da ƙaddara ta alhairi da ta**

**sharri),** sai ya ce ka yi gaskiya. Shi imani ba wai kawai kalma ce da ake furtawa da harshe ba, a'a, imani ne a zuciya, da kuma furtawa da harshe, da kuma aikatawa da gaɓoɓi da jiki baki ɗaya, shi ne imani na gaskiya shi ne abin da ya sami matabbaci a cikin zuciya, ayyuka kuma suka tabbatar da haka ta hanyar bin abubuwan da Allah ya bayar da umurni, da nesantar abubuwan da ya hana.

Lokacin da wani mutum ya tambayi Imamul Hassan al-Basriy (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa: kai mumini ne? sai ya ce masa: shi imani iri biyu ne, in kana tambaya ta akan imani da samuwar Allah, da imani da mala'ikunsa da litattafansa, da Manzanninsa, da aljanna da wuta, da tashin alƙiyama da hisabi, to lallai ni mumini ne, amma idan kana tambaya ta game da maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **((Lallai muminai na gaskiya da a koda yaushe suke cikin hali na tsoron Allah, da yi masa biyayya, su ne waɗanda idan an ambaci Allah Maɗaukakin Sarki, zukatansu suke ƙyarma, su kuma cika da kwarjininsa, saboda haka ne ma a duk sanda aka karanta masu ayoyin Alƙur'ani mai girma sai imaninsu ya ƙara ƙarfi da tabbata, su kuma ƙara miƙa- wuya, da kuma ilimi, ba sa dogara da kowa sai Allah da ya halicce su, yake kuma ba su kariya da arziki.. Su waɗannan muminai na gaskiya ɗin suna tsayar da sallah, suna masu cika rukunnanta, cikin tsoron Allah da miƙa- wuya, domin su kasance a koda yaushe cikin ambatonsa, suna kuma ciyar da wani sashe na arzikin da Allah ya ba su a fagen jahadi, da biyayya, da taimakon marasa ƙarfi.. Lallai masu waɗannan sifofi su ne muminai na gaskiya..))** **[al- Anfal: 2 – 4]** ne, to wallahi ban sani ba, shin ina cikinsu, ko kuwa a'a?".

Shi imani na haƙiƙa shi ne wanda ya maƙwabtaci ƙuryar zuciya, ya kuma sami nasarar mallakar rai, tasirinsa kuma ya yi ƙarfi a ruhi, da hankali, da mutum a matsayinsa na shi kaɗai, da ma al'umma, to irin wannan imanin shi ne yake gadar wa bawa da **kyawawan ɗabi'u;** saboda shi imani da amana ɗan juma ne da ɗan jummai, ba sa rabuwa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu batun imani ga mutumin da ba shi da amana, babu kuma batun addini ga wanda ba ya kiyaye yarjejeniya)**, haka ma imani da kunya 'yan uwan juna ne, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Kunya da imani a haɗe suke da juna, idan aka ɗauke ɗaya, ɗayan ma ba zai yi saura ba)**, haka ma imani da gaskiya 'yan uwan juna ne, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Safwan Bn Salim (Allah ya ƙara yarda shi) ya ce: An ce wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam): **Shin mumini zai iya zama matsoraci? Sai ya ce: (Na'am), aka ce masa: Shi mumini zai iya zama marowaci? Sai ya ce: (Na'am), aka ce masa: shin mumini zai iya zama maƙaryaci? Sai ya ce: (A'a)**, wasu malaman ma da suke bayyana ma'anar imani cewa suka yi, shi ne: gaskiya, a inda suka ce: Imani na haƙiƙa shi ne ka faɗi gaskiya koda kuwa da ka zaci cewa za ta cutar da kai, kada kuma ka faɗi ƙarya kowa kuwa ka zaci cewa za ta amfane ka, a duk sanda ka sami kyawawan ɗabi'u na karamci, to ka tabbata sakamako ne na ingantaccen imani, shi mumini ba ya furta komai sai magana mai kyau, da take gyara al'amurra ba ɓatawa ba, take ginawa ba rusawa ba, take kuma rayawa ba lalatawa ba, saboda addininmu addini ne na kyawawan ɗabi'u, da kawo gyara, da ginawa, gami da raya ƙasa, duk wanda ya fi ka a cikin waɗannan, to kuwa ya fi ka a cikin addini.

Haka ma a cikin sakamakon da imani yake gadarwa akwai: **Natsuwa da kwanciyar hankali,** idan har imani ya sami wurin zama a cikin zuciyar ɗan Adam, to a lokacin natsuwa, da yaƙini, da kuma yarda ne za su cikata, sai ta sami sa'adar duniya da ta lahira, shi mumini na haƙiƙa ya san cewa duk abin da ya same shi, da ma can ba zai taɓa iya kauce masa ba, haka ma duk abin da ya rasa, da ma can ba zai taɓa iya samunsa ba, wannan ne kuma zai sanya ya rayu tsakanin muƙamin godiya a yanayin samu da jin daɗi, da kuma muƙamin haƙuri a yanayin rashi, da damuwa, sai zuciyarsa ta sami natsuwar cewa duk abin da Allah ya hukunta shi ne alhairi a gare ta, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Duk wanda ya yi imani da Allah, Allah zai shiryatar da zuciyarsa..)) [at- Taghabun: 11]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ina mamakin al'amarin mumini, gaba ɗayan al'amarinsa alhairi ne, babu wanda yake da haka in ba mumini ba; in abin alhairi ya same shi ya gode, sai hakan ya zama masa alhairi, idan abin ƙi, da na damuwa ya same shi ya yi haƙuri, kuma hakan ya zama masa alhairi)**.

Haka ma **imani yana katange mai shi daga aikata manyan laifuffuka**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mazinaci ba ya yin zinarsa a lokacin da yake a matsayin mumini, haka ma mashayin giya ba ya shan giyarsa a lokacin da yake a matsayin mumini, haka ma ɓarawo ba ya satarsa a lokacin da yake a matsayin mumini, haka ma ba ya ɗiban ganimar da za ta janyo hankulan mutane; saboda girmanta kafin a raba a lokacin da yake a matsayinsa na mumini)**. Haka ma mumini na gaskiya yake nesantar duk wani abu da zai cutar da sauran mutane, irin su izgilanci, da iya-

shege, da mummunan zato, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, kada wasu mazaje daga cikinku su yi wa wasu mazaje na daban izgilanci, mai yiwuwa ne su kasance mafiya alhairi a wurin Allah sama da masu izgilanci. Kada kuma mata muminai su yi wa wasu matan muminai izgilanci, mai yiwuwa ne waɗanda aka yi masu izgilancin su fi alhairi a wurin Allah sama da masu izgilancin. Kada wani sashenku ya aibata wani sashe, kada wani daga cikinku ya kira ɗan uwansa da suna, ko laƙabin da ba ya so, lallai a ambaci mumini da sunan fasiƙanci bayan ya sifantu da imani abu ne mai muni ƙwarai, duk wanda bai dawo daga rakiyar haka, ya bar abubuwan da aka hana ba, to lallai shi ne –shi kaɗai- yake zaluntar kansa da ma wasunsa**)) **[al- Hujrat: 11]**, haka ma mai girma da ɗaukaka ya ce: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku nesanci yin mafi yawan munanan zaton da ake yi wa mutanen kirki, lallai wasu sassa na zace-zace laifi ne da ya cancanci a yi uƙuba akansa, kada ku bibiyi neman sanin sirrin Musulmai, kada wani sashe naku ya ambaci wani sashe da abin da yake ƙi a lokacin da ba ya nan, shin akwai wani cikinku da yake son ya ci naman ɗan uwansa ɗanye bayan ya mutu? Lallai ba ku son haka, don haka ku nesanci yi da mutane; saboda daidai yake da cin namansu, ku kare kanku daga azabar Allah ta hanyar aiki da umurnin da ya bayar da nesantar abin da ya hana. Lallai Allah mai yawan amsar tuban masu tuba ne, mai kuma mayalwaciyar rahama ne ga talikai**)) **[al- Hujrat: 12]**, shi imani yana gadar da lafiyar zuciya, Allah mai girma yana cewa: **((Da ma a ce lokacin da kuka ji, muminai maza da mata sun yi wa**

**junansu zato na alhairi, su ce: wannan kam ƙarya ce bayyananniya?!))** **[an- Nur: 12].**

Haka ma a cikin sakamakon da imani yake gadarwa akwai: **ƙarfafa da nasara daga Allah Maɗaukakin Sarki**, shi imani na gaskiya yana sanya bawa ya zamo a tare da Allah mai girma da buwaya, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai Allah yana tare da muminai))** **[al- Anfal: 19],** kasancewa tare da Allah a nan yana nufin bayar da nasara, da taimako, gami da ƙarfafa, Allah mai girma da buwaya yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, idan kun taimaki addinin Allah, Allah zai taimake ku akan maƙiyanku, ya kuma tabbatar maku da al'amurranku))** **[Muhammad: 7]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((Lallai mu masu taimakon manzanninmu ne, da ma waɗanda suka yi imani a rayuwar duniya, da ma ranar da masu shaida za su tashi))** **[Ghafir: 51]**, a wani wurin kuma Allah mai girma yana cewa: **((Lallai taimakon muminai haƙƙi ne akanmu))** **[ar- Rum: 46],** haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Su ne waɗanda wasu mutane suka tsoratar da su a lokacin da suka ce masu: lallai abokan gabanku sun tanadar maku da wata babban runduna, saboda haka, ku kiyaye su, hakan bai sanya sun yi rauni ba, bai kuma sanya su karaya ba, maimakon haka ma imaninsu da Allah ne ya ƙaru, suka kuma sakankance da nasararsa, sai suka amsa masu da cewa: Allah ya ishe mu, shi ne majiɓincin al'amurran mu, shi kam madalla da wanda ake miƙa masa dukan al'amurra.. Sannan suka fita zuwa jahadi domin su gamu da wannan runduna mai girma, sai dai fa mushrikai sun tsorata da wannan gamuwar, sai muminai suka koma gida cike da nasarar samun ni'imar zaman lafiya, suna kuma kwaɗayin yin jahadi, da**

**kuma babban rabo da suka samu na ladansa, da kuma falalar da ya yi masu na jefa razani cikin zukatan abokan gaba, ta yanda babu ko ƙwarzane da ya same su, suka nemi yardar Allah, sai suka zamo sun cancanci ya ba su falalarsa, lallai Allah mai babban falala ne))** **[Ali Imran: 173 – 174].**

A cikin abin da imani yake gadarwa akwai: **shigar da soyayyar bawa da Allah mai girma da ɗaukaka yake yi a cikin zukatan halittunsa**, ta yanda za ka ga mumini na haƙiƙa mutum ne mai sauƙin kai, yana saurin sabo da mutane, yana kuma ɗinke dukan ɓaraka, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma aikata ayyuka na gari, da sannu Allah zai gadar masu da soyayyar halittu))** **[Maryam: 96]**, babu wani bawa da zai fuskanci Ubangijinsa da zuciya mai cike da imani na gaskiya, face Allah Maɗaukakin Sarki ya fuskantar da zukatan muminai zuwa gare shi, ya zo a cikin Hadisi Ƙudusi cewa: **(Idan Allah ya so bawa, sai ya kira mala'ika Jibrilu, cewa: Allah yana son wane, kai ma ka so shi, sai mala'ika Jibrilu ya yi yekuwa ga waɗanda suke sama cewa: Lallai Allah yana son wane, ku ma ku so shi, sai halittun sama su so shi, sannan Allah ya azurta shi da karɓuwa wajen halittun da suke ƙasa)**, haka ma ya zo a cikin Hadisi Ƙudusi cewa: Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Bawana ba zai gushe yana kusanta ta da nafilfili ba, har sai na so shi, idan na so shi zan zama masa jinsa da yake ji da shi, da ganinsa da yake gani da shi, da hannunsa da yake riƙe abu da shi, da ƙafarsa da yake tafiya da ita, idan ya roƙe ni, wallahi zan ba shi, idan kuma ya nemi tsari na, wallahi zan tseratar da shi).**

Haka ma imani **dalili ne na yaye damuwa, da kawar da bala'i, da yaye baƙin- ciki,** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Shin ba na faɗa maku abin da idan wani baƙin- ciki, ko bala'i daga cikin bala'o'in duniya suka faɗa wa wani daga ciki, idan ya yi addu'a da shi, za a yaye masa ba?), sai aka ce masa: Na'am, sai ya ce: (Addu'ar Zannun,**

﴿ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنتَ سُبۡحَٰنَكَ إِنِّي كُنتُ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٨٧ ﴾

**domin bayanta kai tsaye Allah Maɗaukakakin Sarki ya ce: ((Sai kuwa muka amsa masa, muka tseratar da shi daga baƙin ciki da damuwa, da ma haka muke tseratar da muminai)) [al-Anbiya': 87 – 88]**, wannan ya shafi ɗaukacin muminai.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Tsira da aminci su tabbata da amintaccen Annabi, ya Allah ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk waɗanda suka bi hanyarsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai a cikin manyan abubuwan da imani yake gadarwa akwai: **tabbatar da zaman lafiya da tsaro a cikin al'umma,** shi mumini na gaskiya a duk sanda imani ya sami wurin zama a cikin zuciyarsa; sai ya zamo muɓuɓɓugar aminci, da natsuwa, da kwanciyar hankali, sai mutane su aminta da shi a rayukansu, da dukiyoyinsu, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Musulmi na gaskiya shi ne: wanda mutane suka kuɓuta daga sharrin harshensa da hannunsa, mumini na gaskiya kuma shi**

**ne: wanda mutane suka amince masa akan dukiyoyinsu da mutuncinsu),** razana al'ummar da ba su ji ba, ba su gani ba, da zaluntarsu, ba halin mumini ba ne, koda kuwa ba Musulmai ba ne su, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya kashe kafirin amana ba zai ji ƙamshin aljanna ba, kuma ana jin ƙamshin ne tun a tazarar tafiyar shekaru arba'in)**.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana kore cikan imani ga duk wanda yake cutar da maƙwabcinsa, ko ya kwana a ƙoshe alhalin yana sane maƙwabcinsa ya kwana da yunwa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wallahi bai yi imani ba, wallahi bai yi imani ba, wallahi bai yi imani ba.. Sai aka ce: wane, ya Manzon Allah? Sai ya ce: wanda maƙwabcinsa bai aminta daga cutarwarsa ba)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mutumin da ya kwana a ƙoshe, amma maƙwabcinsa na kusa ya kwana da yunwa, alhalin yana sane, to lallai bai yi imani da ni ba),** shi imani na haƙiƙa shi ne yake sanya mai shi aikata ayyukan alhairi, da gabatar da taimako ga wasu, shi ne yake daidaita ɗabi'un mai shi, tasirinsa kuma ya bayyana a rayuwarsa, da sauran kai wa da komowarsa, da mu'amalarsa da ɗaukacin halittun Allah, yana mai nuna tausayi, da jinƙai ga ɗan Adam, da dabbobi, da abubuwa marasa rai, yana yin hakan ne saboda neman yardar Allah shi kaɗai, Allah mai girma yana cewa: **((Suna kuma ciyar da abinci -duk da suna so suna kuma matuƙar buƙatarsa- ga matalaucin da ya gajiya wajen nema, da ƙaramin yaron da ya rasa mahaifansa, da fursinan yaƙin da ba ya mallakar komai. Suna kuma faɗi a cikin zuciyarsu cewa: muna ciyar da ku ne kawai saboda biɗar yardan Allah, ba ma**

**son ku ba mu wani abu a maimakonsa, ko ku yi mana kyauta, haka ma ba ma son yabo daga gareku))** **[al- Insan: 8 – 9].**

Alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa:

"Idan imani ya salwanta babu sauran aminci, babu duniya ga wanda bai raya addini ba.. duk wanda ya yarda da rayuwar da babu addini a cikinta, to kuwa lallai ya yi mata abota ne da ƙarewa".

Lallai a cikin manyan sakamakon da imani da Allah Maɗaukakin Sarki yake gadarwa akwai: **abin da Allah mai girma da ɗaukaka ya tanadar wa bayinsa muminai a lahira,** na babban lada, da dawwamammiyar ni'ima, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma aikata ayyuka na gari Ubangijinsu sai shiryatar da su sakamakon imaninsu, inda ƙoramu za su gudana ta ƙarƙashinsu a cikin aljannar ni'ima))** **[Yunus: 9]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ka yi wa waɗanda suka yi imani, suka kuma aikata ayyuka na gari albishir da cewa suna da aljannar da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu..))** **[al- Baƙra: 25]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((Su kuwa waɗanda suka yi imani, suka kuma aikata ayyuka na gari, lallai waɗannan su ne 'yan aljanna, za kuma su dawwama a cikinta))** **[al- Baƙra: 82]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai waɗanda suka yi imani, suka kuma aikata ayyuka na gari, lallai mu kam ba ma tozartar da ladan duk wanda ya kyautata aiki))** **[al- Kahfi: 30]**, haka ma mabuwayin Sarki yana cewa: **((Lallai waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma aikata ayyuka na gari, suna da masauki a cikin aljannar Firdausi. Za su dawwama a cikinta, ba za su taɓa neman sauyi ba))** **[al- Kahfi: 107 – 108].**

Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗi a Hadisi Ƙudusi cewa: **(Na tanadar wa bayi na salihai da abin da ido bai taɓa gani ba, kuma kunne bai taɓa ji ba, bai kuma taɓa ɗarsuwa a zuciyar ɗan Adam ba, sannan Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya karanta: ((Rai bai san abin da aka tanada masa na jin daɗi a matsayin sakamakon abubuwan da suka aikata ba))** **[as- Sajada: 17].**

Lallai ya kamata mu tabbatar da imani a zukatanmu, da maganganunmu, da ayyukanmu, ta yanda tausayi, da taimakekeniyar juna, da gaskiya, da kunya, da baiwa, da kamewa za su game rayuwarmu, mu kuma nesanci ƙarya, da algushi, da ha'inci, da giba, da annamimanci, da zancen – kawai, da cin mutuncin mutane, mu kuma kiyaye hurumin rayuka, da haƙƙoƙin dukiyoyi, da na ƙasa, da kuma matsayinsu.

**Ya Allah Ubangiji, muna roƙon ka sanya mana soyayyar imani, ka ƙawata shi a cikin zukatanmu, ka munana kafirci, da fasiƙanci, da saɓon Allah a cikinsu, ka sanya mu cikin shiryayyu, ka kiyaye ƙasarmu, da sauran ƙasashen duniya.**

## -4-

## MA'ANAR AIKI NA GARI DA MUMMUNAN AIKI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Duk wanda ya aikata aiki na gari, to kansa ya yi wa, wanda ma ya munana aiki shi ma kansa ya yi wa, lallai Ubangijinka ba mai zaluntar bayi ba ne))** **[Fussilat: 46]**. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda yake faɗi a cikin abin da ya ruwaito daga Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka cewa: **(Ya ku bayina, ayyukanku ne dai ina kiyaye maku su, sannan in saka maku da sakamakonsu, duk wanda ya sami alhairi, to ya gode wa Allah, wanda kuma ya sami akasin haka, to kada ya zargi kowa sai kansa)**.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya karrama ɗan Adam, inda ya halicce shi aka mafi kyawon sura, ya kuma hura masa ruhinsa, ya kuma bambanta da sauran halittu ta hanyar ba shi hankali, ya kuma hore masa ɗaukacin halittu gaba ɗaya, ya kuma fifita shi akan halittunsa masu yawa da ya halitta, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai mun karrama ɗan Adam, muka kuma ɗauke shi a tudu, da a cikin kogi ta hanyoyin sufuri mabambanta, muka azurta su da kayan jin daɗi masu tsarki,**

**muka kuma fifita sosai shi akan da yawa daga cikin halittunmu)) [al- Isra'i: 70]**; lallai wannan ya kasance ne sakamakon irin yanda ɗan Adam ya ɗauki amana mai nauyin da aka bijirar wa sammai, da ƙasa, da duwatsu, suka kasa ɗauka, suka tausaya wa kawunansu saboda nauyin wannan amana; lallai ba wani abu ne wannan ba banda amanar takalifi, wadda ta wajabta gabatar da aiki na gari, da raya doron ƙasa, ga kuma ibadun da aka farlanta aiwatar da su, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Idan kuma kun gabatar da sallar, to ku bazama a bayan ƙasa saboda maslahohinku, ku nemi falalar Allah, ku yawaita ambaton Allah a zuci da baki, ko za ku sami babban rabo na alhairi a duniya da lahira)) [al- Juma'at: 10].**

Lallai ya kamata kowane Musulmi ya san cewa; duk wani abu da yake aikatawa a cikin rayuwarsa zai shiga cikin ma'aunin kyawawan ayyukansa ne, ko kuma cikin ma'aunin munanan ayyukansa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Duk wanda ya aikata alhairi koda gwargwadon ƙwayar zarra ne, zai ganshi a cikin littafinsa, zai kuma sami sakamako akansa. Haka ma duk wanda ya aikata sharri koda gwargwadon ƙwayar zarra ne shi ma zai ganshi, zai kuma sami sakamakonsa, Ubangijinka ba ya zaluntar kowa)) [az-Zalzalat: 7 -8]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((To, waɗanda suke saɓa wa umurnin sa su tsoraci ranar da kowane rai zai tarad da abin da ya aikata na alhairi a gabansa komin ƙanƙantarsa. Abin da ya aikata kuma na munanan abubuwa zai yi burin ina ma a ce akwai wata tazara mai nisa a tsakanin sa da su, ta yadda ba zai gan su ba, saboda munin su da kuma tsoron kada ya afka ciki. Lallai Allah yana tsoratar da ku**

**uƙubar sa, idan har kuka kuskura kuka fita daga wilayar sa, da take ita ce yin rangawame da rahama ga bayin sa))** **[Ali Imran: 30]**, ma'anar aiki a nan ya ƙunshi: duk wani abu da mutum zai gabatar na magana, ko aiki, sharaɗi dai shi ne: kafin kowane aiki ya zamo na ƙwarai, sai an yi shi saboda Allah Maɗaukakin Sarki kawai, sannan ya zamo an kyautata shi, Allah mai girma yana cewa: **((Ba a ɗaura masu wannan abu da yake kansu ba, sai domin ibadarsu ta kasance tsarkakakka saboda Allah, su kuma tsarkake masa addini, su karkace wa ɓata, su kuma tsaya sosai akan gaskiya, su kuma kiyaye sallah, su kuma bayar da zakka, wannan shi ne tsarin daidaitaccen addini))** **[al- Bayyinat: 5]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah yana son idan wani daga cikinku zai yi aiki ya kyautata aikin)**.

Babu shakka ma'anar aiki na ƙwarai a cikin Musulunci yana da faɗi matuƙa, ya ƙunshi duk wata ibada da Allah Maɗaukakin Sarki ya farlanta, irinsu: sallah, da azumi, da zakka, da hajji, da zikiri da sauransu, waɗannan su ne harsashen da dole ne kowane Musulmi ya aikata su, Allah mai girma yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku yi wa Allah ruku'u, ku kuma yi masa sujada, ku bauta wa Ubangijinku, ku kuma aikata aikin alhairi ko za ku sami babban rabo))** **[al- Hajji: 77]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ku tsayar da sallah, ku kuma bayar da zakka, ku yi wa Manzon Allah biyayya, ko za a yi maku rahama))** **[an- Nur: 56]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Tsarki rabin imani ne, ladan faɗin "al-Hamdu lilLãhi" yana cika mizani, ladan faɗin "SubhanalLãhi wa al-Hamdu lillahi" suna cika –ko yana cika- tsakanin sama da ƙasa, sallah haske ne, sadaka hujja ce,**

**haƙuri haske ne, Alƙur'ani hujja ne a gareka, ko akanka. Mutane gaba ɗaya suna wayan gari ne a cikinsu akwai: mai sayar da kansa, da mai 'yanta ransa, da mai halakar da shi).**

A cikin ayyuka na gari da suka kamata kowane Musulmi ya yi ado da su, akwai: **gaskiya, da yin maganganu masu daɗi, da yaɗa sallama** da sauransu, cikin dai abubuwan da za su sanya mutum ya zama na mutane, su ma su zama nasa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ka faɗa wa bayi na cewa su rinƙa yin magana da abin da shi ne ya fi kyau da alhairi..)) [a-Isra'i: 53]**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai mutumin da na fi so a cikinku shi ne: wanda ya fi kowa kyawawan ɗabi'u; mai sauƙin kai, wanda ya zama na mutane, su ma suka zama nasa...)**, haka ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana halin mumini a inda yake cewa: **(Na rantse da wanda rayuwar Muhammadu take hannunsa, lallai mumini tamkar ƙudar zuma yake, ta ci abu mai kyau, ta kuma fitar da abu mai kyau, ta kuma faɗi ba ta karya komai ba, ba kuma ta lalata komai ba)**.

Lallai aiki na gari bai taƙaita a wani ɓangare banda sauran ɓangarori ba; hasali ma duk abin da zai tabbatar da kyawawan ɗabi'un bil'adama, ya kuma bayar da gudummuwa wajen gina ɗinkakkiyar al'umma mai haɗin - kai, mai kuma tsarkin ruhi, inda soyayya da taimakekeniya za su mamaye ta ta ko'ina, ɗabi'un rangwame, da ƙauna, da tausayi su zamo sifa a gare ta, wannan ma aiki ne na gari, lallai addinin Musulunci yana kallon fita neman abinci da mutum yake yi, da niyya ya sami kamewa ga barin haramu, ya samu abincin da zai ciyar da 'ya'yansa, da iyalansa daga guminsa, addini yana kallon haka a matsayin aikin da bawa zai sami lada akansa, lallai Annabi

(SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya hakan daidai yake da fita saboda Allah, lokacin da wani mutum ya wuce ta gaban Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai sahabbai suka ga irin yanda yake kazar-kazar da nishaɗi, sai suka ce: ya Manzon Allah, ina ma fisabililLahi yake yi? Sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan ya fito ne domin ya nema wa ƙananan yaransa abinci, to ya fito ne fisabililLahi, haka ma idan ya fito ne saboda ya sami abin da zai iya ɗaukan nauyin iyayensa tsofaffi guda guda biyu, to ya fito ne fisabililLahi, haka ma idan ya fito ne domin ya nema wa kansa arziki domin ya samu ya kame, to lallai ya fito ne fisabililLahi, amma idan ya fito ne kawai saboda duniya ta ganshi, domin ya yi fankama, to a nan ya fito ne fisabilis-Shaiɗan).**

Lallai ya wajaba mu yi koyi da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), da kansa yake yi wa kansa aiki, ya kuma hidimta wa iyalansa, Ummul muminina Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) tana cewa: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) da kansa yakan ɗinke hancin takalminsa, yakan kuma ɗinke rigarsa, yake kuma yin aiki a gidansa kamar yanda kowannenku yake aiki a gidansa, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idan mutum ya ciyar da iyalansa, yana mai neman lada a wurin Allah, to haka sadaka ne a wurinsa)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Fiyayyen mutum a cikinku shi ne wanda ya fi zamowa alhairi ga iyalansa, ni ne kuma na fi zama alhairi ka iyalaina)**.

Haka ma **duk wani abu da mutum zai aikata ya amfani waninsa, shin kaɗan ne, ko mai yawa, na zahiri ne, ko na ma'ana**, duka suna cikin aiki na gari, Allah Maɗaukakin Sarki

yana cewa: **((A mafi yawan lokuta babu wani alhairi tattare da mutanen da suke ɓoye maganganun da suke yi a cikin zukatan su, ko waɗanda suke yi tsakanin su da juna; saboda sharri ne ake ɓoye shi, sai dai idan abin da aka ɓoyen ya zamo bayar da umurni ne da yin sadaka, ko aikata wani aiki mai kyau, ko daidaita tsakanin mutane da gyara zumunta, waɗannan kam duka alhairai ne, duk wanda ya aikata haka saboda neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki, to kuwa lallai Allah Maɗaukakin Sarki zai ba shi babban sakamako a nan duniya da lahira; saboda abin da ya aikata)) [an- Nisa'i: 114]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda yake da abin hawa bayan abin hawansa, to ya bayar da shi ga wanda ba shi da abin hawa, haka ma duk wanda yake da guzuri da ya wuce buƙatarsa, to ya taimaka wa wanda ba shi da guzuri)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kwaɗaitar da mutane akan hanyoyin alhairai masu yawa, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai ƙofofin alhairai suna da yawa, faɗin "SubahanalLahi", da faɗin "Alhamdu lilLahi", da faɗin "Allahu Akbar", da faɗin "La'ilaha illalLahu", da bayar da umurnin aikata abu mai kyau, da hana aikata abu mai muni, da kawar da abu mai cutarwa daga barin hanya, da fahimtar da kurma, da yi wa makaho jagora, da isar da mai tambaya zuwa ga abin nemansa, da tsaya wa wanda yake cikin tsananin buƙata, da rungumar masu rauni, duka waɗannan sadaka ne kake yi wa kansa)**, kuma dukansu suna cikin rukunin ayyuka na gari.

Haka ma: **gina al'umma, da kawo gyara, da raya ƙasa,** lallai addinin Musulunci yana kallon duk wani aiki da zai kai zuwa ga gina al'umma mai ƙarfi a matsayin aiki ne mai matuƙar

muhimmanci da daraja, lallai akwai kusan ayoyi ɗari uku da sittin a cikin Alƙur'ani mai girma da suka yi magana akan aiki, Allah Maɗaukakin Sarki ya kawo mana misalai na waɗanda suka gabatar da ayyuka na gari, Allah mai girma yana cewa: **((Allah shi ne ya halicce ku daga ƙasa, ya kuma nemi ku raya ƙasar..)) [Hud: 61]**, wannan yana tabbatar da cewa: waɗanda suke aiki a fannin noma, da masana'antu suna da lada gwargwadon irin ƙoƙarin da suka yi, da kuma irin abubuwan da suka sana'anta, wanda yake a matsayin ginshiƙi na rayuwa, kaman masana'antar ƙarafa, Allah mai girma yana cewa: **((Muka kuma halicci ƙarfe da yake da azaba da tsanani a wurin yaƙi, da kuma amfani mai yawa ga mutane a lokacin zaman lafiya, suna amfani da shi a wajen fannin ƙere- ƙere; domin su yi amfani da shi wajen maslaharsu da ayyukan rayuwarsu..)) [al-Hadid: 25]**, haka ma da ƙera jiragen ruwa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Muka yi masa wahayin ya ƙera jirgin ruwa a ƙarƙashin kulawar da wahayinmu..)) [al- Mu'uminun: 27]**, haka ma mai girma da ɗaukaka ya yi magana game da sana'ar saƙa tufafi, da mayafai, yana cewa: **((Kuma daga gashin tumaki, da gashin raƙuma, da gashin ƙadduwa ne kuke sana'an shimfiɗun da kuke jin daɗi da su na zuwa lokacin ajalinku)) [an- Nahl: 80]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya kuma samar maku da tufafin da ake saƙa shi da gashin tumakai, da auduga, da kittani da sauransu, da suke kare ku daga zafin rana, ya kuma samar maku da silakun da suke ba ku kariya daga tsanantar yaƙi da abokan gaba..)) [an- Nahl: 81]**, game da sana'ar jima ma yana cewa: **((Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ne ya sanya kuka zamo kuna da ikon gina**

**hema ta hanyar amfani da fatun dabbobi, da kuke iya zama a ciki, ku kuma ɗauke su a tafiye – tafiyenku..))** **[an- Nahl: 80]**.

Lallai aiki na gari bai taƙaita kawai da abin amfani ya shafi ɗan Adam kawai ba; **kai har da abubuwan da za su amfani dabbobi da abubuwa marasa rai ya ƙunsa,** lokacin da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya wuce ta wurin wani ramammen raƙumi, cewa ya yi: **(Ya jama'a, ku ji tsoron Allah akan waɗannan dabbobin da ba sa magana, in za ku hau su, ku suna cikin ƙoshin lafiya, in ma za ku bar su, ku bar su cikin ƙoshin lafiya)**, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wani mutum yana tafiya a hanya, sai ya ga wani reshe na ƙaya, sai ya kawar da shi, sai kuwa Allah ya gode masa, ya kuma gafarta masa)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai na ga wani mutum yana kai komonsa a cikin aljanna; sakamakon sare wata bishiya da ta tsiro tsakiyar hanya da ya yi, tana cutar da masu wucewa)**.

Shi kuwa mummunan aiki, ya haɗa da duk wani abu da yake fusata Allah Mabuwayin Sarki, yake kuma fitar da ɗan Adam daga farfajiyar gyara zuwa kwazazzaban ɓarna, inda zai fara nesantar ayyukan biyayya da aka farlanta, yana kuma aikata munanan ayyuka da alfasha, kaman saɓa wa iyaye, da ɓarnata dukiyoyi, da cin mutuncin mutane, **da kuma ka ga mutum ya yi watsi alhaki gami da ɗaukan nauyin iyalansa da ya rataya akansa, da rashin bai wa 'ya'yansa kulawar da ta kamata wajen ba su nagartacciyar tarbiyya**, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku tseratar da kawunanku da iyalanku ga barin shiga wuta..))** **[at- Tahrim: 6]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa:

**(Zunubi ya kai zunubi a ce mutum ya tozartar da waɗanda ciyar da su ya wajaba akansa..)**

Haka ma **ɓarna a bayan ƙasa yana cikin munanan ayyuka,** ta hanyar yaɗa gurɓatattun tunani, da yaɗa jita- jita da ƙarerayi, da tsoratar da mutanen da suke zaune lafiya cikin kwanciyar hankali, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ku kuskura ku yi ɓarna a bayan ƙasa bayan an gyara ta..))** **[al- A'araf: 56, 85]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Shi kawai uƙubar waɗanda suke yaƙar Allah Maɗaukakin Sarki da Manzonsa (SallalLãhu alaiHi wa sallam) idan suka yi wa tsarin shugabanci da hukunce-hukuncen shari'a tawaye, suka kuma cigaba da yin ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar tare hanya da yin fashi da makami, ko ƙwace dukiyoyin mutane: shi ne a kashe su idan sun kashe, a kuma tsire su idan suka yi kisa, suka kuma ƙwace dukiya, a kuma yanke hannayensu da ƙafafuwansu amma a saɓa tsakani idan sun tare hanya, suka kuma ƙwaci dukiya amma ba su yi kisa ba, a kuma kore su daga garin zuwa wani garin na daban, a kuma tsare su a gidan fursuna idan tsoratar da al'umma suka yi kawai. Wannan uƙubar ƙasƙanci ne da wulaƙanci a gare su a nan rayuwar duniya, a lahira kuma suna da azaba mai girma wadda ita ce azabar wuta))** **[al- Ma'idat: 33]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Kada ka nemi aikata ɓarna a bayan ƙasa, lallai Allah ba ya son maɓarnata))** **[al- Ƙasasi: 77]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Fiyayyen mutum a cikinku shi ne wanda alhairansa suke samun mutane, aka kuma aminta ga barin sharrinsa, mafi sharri a cikinku shi ne wanda alhairinsa ba ya samun mutane, ba kuma a aminta ga barin sharrinsa ba)**. Haka ma a cikin munanan ayyuka akwai:

**cutar da hanyoyin mutane,** wannan kam babban zunubi ne, saboda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Babu cuta babu cutarwa),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya cutar da Musulmai ta hanyar lalata hanyoyinsu, to kuwa la'anta daga gare su ta wajaba akansu)**.

Haka ma akwai: **duk wani abu da zai dasa ƙiyayya tsakanin mutane, da abubuwan da za su samar masu da damuwa ta zahiri da baɗini,** irinsu : giba, da annamimanci, da izgilanci, da iya shege, da jifan mutane da sunayen banza, da zagi, da alfasha wajen magana, da sauran abubuwan da addinin Musulunci yana hana aikata su, waɗanda suka yi hannun- riga da kyawawan ɗabi'un fiɗira da wayewa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mutumin da na fi ƙinsa a cikinku shi ne mai yawo da annamimanci a tsakanin mutane, mai kuma rarraba tsakanin masoya, mai neman aibin mutanen kirki)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

----------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai kowane aiki da bawa yake aikatawa yana da tasirin da yake dawo masa a duniya da

lahira, sakamakon aiki na gari shi ne: **kyakkyawar rayuwa a duniya da lahira,** Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Duk wanda ya aikata ayyuka na gari cikin maza da mata, yana cikin halin imani, to kuwa za mu raya shi rayuwa mai kyau, za kuma mu saka masu da ladansu sama da abin da suke aikatawa))** **[an- Nahl: 97]**, haka ma **ladan nasu zai cigaba da binsu har bayan wafatinsu**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ladan abubuwa bakwai suna bin bawa har bayan wafatinsa, yana cikin kabari: wanda ya karantar da ilimi, ko ya samar da gulabe daga kogi, ko ya haƙa rijiya, ko ya dasa dabino, ko ya gina Masallaci, ko ya gadar da Alƙur'ani, ko ya bar yaron da yake nema masa gafara bayan rasuwarsa)**, haka ma akwai: **ƙanƙare munanan ayyuka, da sauya su da kyawawa**, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai za mu ƙanƙare munanan ayyukan waɗanda suka yi imani, suka kuma aikata ayyuka na gari, za kuma mu saka masu da mafi kyawon abin da suke aikatawa))** **[al- Ankabut: 7]**, haka ma ga **babban lada, da kusantar Annabawa, da siddiƙai, da shahidai,** Allah mai girma yana cewa: **((Lallai waɗanda suka yi imani, suka kuma aikata ayyuka na gari, to lallai suna da masauki a cikin aljannar Firdausi))** **[al- Kahfi: 107]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((Duk wanda ya yi wa Allah Maɗaukakin Sarki da Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) biyayya, ya miƙa-wuya a gare su, ya yarda da hukuncinsu, to, yana cikin waɗanda Allah ya yi masu ni'imar shiriya da dacewa a duniya da lahira, cikin Annabawansa da mabiyansu da suka gasgata su suka kuma bi hanyarsu, da waɗanda suka yi shahada a hanyar ɗaukaka kalmar Allah, da salihan bayin da zukatansu da ayyukansu suka kyautatu,**

**wasu abokan tafiya ne suka fi waɗannan nagarta? Lallai abokin zamansu ba ya taɓewa, ba kuma ya ƙosawa da zantuttukansu))** **[an- Nisa'i: 69].**

Lallai kaman yanda aiki na gari yake da tasiri, haka ma mummunan aiki yake da tasirin da yake faɗawa kan mai shi a duniya da lahira, a cikin tasirin akwai: **ɓata, da ɗimuwa, da rashin saiti,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Hankali kuka rasa ne da ba za ku iya bambance tsakanin wanda shaiɗan ya ƙawata masa munanan ayyukansa ya ɗauka yana yi mai kyau ne, da wanda ya shiryu da shiryatarwar Allah, ya kuma ɗauki abu mai kyau a matsayinsa na abu mai kyau ba?!, lallai Allah yana ɓatar da wanda ya so cikin waɗanda suka rungumi hanyar ɓata, yana kuma shiryatar da wanda yake so cikin waɗanda suka zaɓi hanyar shiriya..))** **[Fatir: 8]**, haka ma a cikin tasirin akwai: **rayuwa cikin tsoro da rashin tabbas,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Duk wanda ya kawar da kai ga barin ambato na, to kuwa lallai yana da rayuwar ƙunci da matsi..))** **[Taha: 124]**, haka ma a cikin tasirin akwai: **mummunar makoma a ranar alƙiyama,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai waɗanda suke zaluntar marayu ta hanyar amsar dukiyar su ba gaira-ba-dalili, to, su sani cewa suna cin abin da zai kai su zuwa ga wuta ne, da sannu za a yi masu azaba da wuta mai tsananin zafi a ranar alƙiyama))** **[an- Nisa'i: 10]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya ci filin da ba nasa ba, babu gaira babu dalili, za a nutsar da shi a ciki ranar alƙiyama har zuwa ƙasan bakwai..)**

Lallai muna matuƙar buƙatar yin riƙo da duk wani aikin alhairi mai amfani, mu kuma nesanci duk wani sharri mai

cutarwa, mu kuma yi wa juna wasici da taimakekeniya, gami da gaskiya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ina rantsuwa da zamani; saboda yawan abubuwan da ya ƙunsa na ban mamaki da lura. Lallai kowane mutum yana cikin wani nau’i na asara; saboda rinjayar da son zuciya da sha’awa da suka taru suka yi masa yawa. Sai dai ban da waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma aikata ayyuka na gari, suka kuma yi ɗã’a da biyayya, suka kuma yi wa juna wasici da riƙo da gaskiya wajen i’itiƙadi da furuci da aiki, suka kuma yi wa juna wasici da haƙuri akan abubuwa masu wahala da suke bijiro wa duk wani wanda ya yi riƙo da addini, waɗannan kam, su ne masu tsira daga wannan asara, masu kuma babban rabo a duniya da lahira)) [al- Asri: 1 – 3].**

**Ya Allah Ubangiji ina roƙon ka datar da mu zuwa ga aikata alhairi, da nesantar abubuwan ƙi, da son miskinai, ka azurta mu da ikhlasi da amsar ayyuka, ka kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashe baki ɗaya.**

- 5 –

## AMBATON ALLAH DA TASIRINSA WAJEN DAIDAITA ƊAN ADAM

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Su ne waɗanda suka yi imani da Allah, zukatansu kuma suka sami natsuwa da ambaton Allah, da ma can da ambaton Allah ne zukata suke samun natsuwa))** **[ar- Ra'ad: 28]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya, cikakken mabuwayi mai hikima.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya umurci bayinsa da yawaita ambatonsa, ya kuma yi masu alƙawarin lada mai yawa akan haka, Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, ku ambaci Allah Maɗaukakin Sarki da ambato mai yawa, ku kuma yi masa tasbihi safiya da maraice))** **[al- Ahzab: 41 -42]**, haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Da masu ambaton Allah da yawa, mazansu da matansu, duka Allah ya tanadar masu da gafara da babban lada))** **[al- Ahzab: 35]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((Muminai su ne waɗanda idan aka ambaci Allah, sai zukatansu raurawa, idan kuma aka karanta masu ayoyinsa,**

**sai karatun ya yi sanadiyya ƙaruwar imaninsu, su a koda yaushe suna dogara da Ubangijinsu ne. Su ne waɗanda suke tsayar da sallah, suke kuma ciyar da wani sashe na abin da muka azurta shi da shi a hanyar ɗaukaka addinin Allah. Waɗannan kam su ne muminai na gaskiya, suna da muƙamai masu daraja a wurin Ubangijinsu, da yafe zunubai, da kuma arziki mai girma)) [al- Anfal: 2 -4].** Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kwaɗaitar da al'umma game da yawaita ambaton Allah Maɗaukakin Sarki, ya kuma zaburar da su akan haka, mai tsira da aminci yana cewa: **(Shin ba na ba ku labari akan mafi alhairi a cikin ayyukanku, da ya fi tsarki a wurin mamallakinku, darajarsa kuma tafi ɗaukaka a cikin darajojinku, abin da yinsa ya fi maku akan ku ciyar da zinare, da dukiya, ya kuma fi maku alhairi akan ku haɗu da maƙiyanku, ku kashe su, su ma su kashe ku ba?)**, sai suka ce: faɗa mana ya Manzon Allah, sai ya ce: **(Ambaton Allah),** haka ma lokacin da wani mutum ya zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: Ya Manzon Allah, dokokin Musulunci sun yi mini yawa, faɗa mini abin da zan riƙe shi gam, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Kada harshenka ya yi sakaci da ambaton Allah).**

Lallai ambaton Allah Maɗaukakin Sarki ibada ce mai matuƙar girma, mai kuma sauƙin aikatawa, falalarsa ya fi ƙarfin a lissafa, ko a ƙididdige, a cikin falalolinsa da suka zo mana akwai: Hadisin Sayyiduna Abu Sa'id al-Khudiry (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: wata rana Sayyiduna Mu'awiyya (Allah ya ƙara yarda da shi) ya fito ya ga wani majalisi a Masallaci, sai ya ce: zaman mene kuke yi haka? Sai suka ce: mun zauna ne muna ambaton Allah Maɗaukakin Sarki, sai ya ce: Don Allah ku faɗa

mini, shin babu wani abu da ya zaunar da ku sai haka? Sai suka ce: mun rantse da Allah babu abin da ya zaunar da mu sai haka. Sai ya ce: ba wai na nemi ku rantse saboda ina tuhumarku ba ne, ban san wani mutum da yake da matsayi irin nawa a wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) da ya kai ni ƙarancin Hadisi ba, lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fito wata rana sai ya sami majalisi na sahabbansa, sai ya ce: **(Mene ya zaunar da ku?)** sai suka ce: Mun zauna ne muna ambaton Allah, muna kuma gode masa akan shiryatar da mu zuwa ga Musulunci da ya yi, da kuma ni'imomin da ya yi mana, sai ya ce: **(Don Allah ku faɗa mini, shin babu wani abu da ya zaunar da ku sai haka?)** Sai suka ce: mun rantse da Allah babu abin da ya zaunar da mu sai haka. Sai ya ce: **(Ba wai na nemi ku rantse saboda ina tuhumarku ba ne, Mala'ika Jibrilu ne ya zo ya ba ni labarin cewa lallai Allah mai girma da buwaya yana yi wa mala'iku alfahari da ku)**.

Ambaton Allah shi ne rayuwar zukata, kuma shi ne zancen da Allah mai girma ya fi so, an ruwaito Hadisi daga Abu Musa (Allah ya ƙara yarda da shi), Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Misalin wanda yake ambaton Ubangijinsa, da wanda ba ya ambatonsa, tamkar rayayye ne da matacce)**, a lafazin da ya zo a Muslim, kuwa Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Misalin gidan da ake ambaton Allah a cikinsa, da gidan da ba a ambaton Allah a cikinsa, tamkar rayayye ne da matacce)**, Haka ma an ruwaito Hadisi daga Abuzarrin (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa: wata rana Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya tafi gaishe shi, sai ya ce: Ya Manzon Allah, iyaye ne biyu fansa ne a gare ka, wace magana

ce Allah Maɗaukakin Sarki ya fi so? Sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda Allah ya zaɓa wa mala'ikunsa:**

**"سُبْحَانَ رَبِّي وَبِحَمْدِهِ، سُبْحَانَ رَبِّي وَبِحَمْدِهِ".**

An ruwaito Hadisi daga Sumurat Bn Jundab, ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Maganar da Allah ya fi so guda huɗu ne:**

**"سُبْحَانَ اللهِ، وَالْحَمْدُ لِلّهِ، وَلَا إِلَهَ إِلّا اللهُ، وَاللهُ أَكْبَرُ"**

**babu laifi da duk wanda ka fara daga cikinsu.)**

Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(.. al-Mufarriduna kam sun yi gaba)**, sai muka ce: Ya Manzon Allah, su wane ne al-Mufarriduna? Sai ya ce: **(Masu ambaton Allah da yawa, mazansu da matansu)**; saboda haka ne ma ambaton Allah Maɗaukakin Sarki ya zamo shi ne wasiyyar da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi wa Sayyiduna Mu'az (Allah ya ƙara yarda da shi), a inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Ya Mu'az, wallahi lallai ina sonka)**, sai Mu'az ya ce: Iyaye na fansa ne a gare ka, ya Manzon Allah, wallahi ni ma ima sonka, sai ya ce: **(Ya Mu'az, ina maka wasici da kada ka bar faɗin**

**" اللّهُمّ أَعِنّي عَلَى ذِكْرِكَ وَشُكْرِكَ وَحُسْنِ عِبَادَتِكَ".**

**a ƙarshen kowace sallah).**

Lallai ambaton Allah Maɗaukakin Sarki ibada ce da take bin bawa a dukan yanayin da yake ciki, shi Musulmi an ba shi umurnin gabatar da shi a kowane lokaci, kuma a kowane yanayi, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai a cikin halittar da Allah ya yi wa sammai da ƙasa, da abubuwan da suke cikin su na ƙwarewa da gwaninta, da saɓanin da dare da rana suke da shi, na haske da duhu, tsawo da gajerta, akwai**

**bayyananannun ayoyin ga masu hakalin da suke iya riskar kaɗaitakar Allah da ikon sa. Shi kuwa sha'anin masu hankali –a koda yaushe- shi ne su halarto da girman Allah da buwayan sa cikin zukatan su, a kuma duk inda suke, shin suna tsaye ne, ko a zaune, ko a kwance….))** **[Ali Imran: 190 – 191]**, ita rayuwar Musulmi cike take da ambaton Allah, shin a cikin ibadunsa ne, ko ayyukansa, kai sallarsa ma ambaton Allah ne, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ka kuma tsayar da sallah saboda Ambato na..))** **[Taha: 14]**, haka ma Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ka kuma tsayar da sallah, lallai sallah tana hana alfasha, da abubuwan ƙyama, lallai ambaton Allah shi ne ya fi girma..))** **[al- Ankabut: 45]**, ma’ana: ita sallah tana da manufofi guda biyu masu matuƙar girma, **na farko:** tana hana alfasha, da ayyuka ƙyama, **na biyu kuma:** ambaton Allah Maɗaukakin Sarki ne ita, manufa ta biyu wadda ita ce ambaton Allah Maɗaukakin Sarki ita ce ta fi girma da daraja.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya shar’anta mana zikirori masu yawa da suka kamata Musulmi a koda yaushe ya dage wajen yinsu, an ruwaito Hadisi daga Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kasance a duk sanda ya wayi gari yakan ce:

**" اللّهُمّ بِكَ أَصْبَحْنَا ، وَبِكَ أَمْسَيْنَا ، وَبِكَ نَحْيَا ، وَبِكَ نَمُوتُ ، وَإِلَيْكَ النُّشُورُ"**

Idan kuma ya yammanta yakan ce:

**" اللّهُمّ بِكَ أَمْسَيْنَا ، وَبِكَ أَصْبَحْنَا ، وَبِكَ نَحْيَا ، وَبِكَ نموت ، وإليك المصير”**

Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda ya wayi gari ya ce:**

" اللّهُمّ مَا أَصْبَحَ بِي مِنْ نِعْمَةٍ أَوْ بِأَحَدٍ مِنْ خَلْقِكَ فَمِنْكَ وَحْدَكَ لَا شَرِيكَ لَكَ ، لَكَ الْحَمْدُ ، وَلَكَ الشُّكْرُ"

**to ya bayar da godiyar wannan ranar)**, wanda ma ya yi irin haka a lokacin da ya yammanta, ya bayar da godiyar wannan dare nasa, mene ne kuwa ya kai kyawawon a ce mutum ya fara ranarsa da ambaton Allah, ya kuma ƙare ranar da ambaton Allah, kuma ya zamo a tsakaninsu ya dawwama ambaton majiɓincin al'amurransa.

Haka ma akwai sigogi na zikiri da ake karantawa a lokacin fita daga gida, da lokacin shiga gida, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda kafin ya fita daga gidansa ya ce:**

" بِسْمِ اللّهِ توكّلْتُ عَلَى اللّهِ ، وَلَا حوْلَ وَلَا قُوةَ إلاّ بِاللّهِ"

**za a ce masa: an shiryatar da kai, an kuma isar maka, an kuma ba ka kariya daga dukan sharri, shaiɗan kuma zai nesance shi)**, an ruwaito Hadisi daga Ummu Salama (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) bai taɓa fita daga ɗaki na ba, face ya ɗaga fuskarsa sama ya ce:

"اللّهُم اني أعوذُ بِكَ أن أضِلّ أو أُضَلّ، أو أزلّ أو أُزَلّ، أو أَظْلِمَ أو أُظلَمَ، أو أجهَل أو يُجْهَل عَلَيّ"

Haka ma a cikin zikirorin da ake yi lokacin shiga gida akwai Hadisin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yake cewa: **(Idan mutum ya shiga gidansa, ya ce:**

"اللّهُمّ إِنّي أَسْأَلُكَ خَيْرَ الْمَوْلَجِ ، وَخَيْرَ الْمَخْرَجِ ، بِسْمِ اللّهِ وَلَجْنَا ، وَبِسْمِ اللّهِ خَرَجْنَا ، وَعَلَى اللّهِ رَبِّنَا تَوَكّلْنَا"

**sannan ya yi wa iyalansa sallama),** haka ma yana cewa: **(Yanzu cikinku za a sami wanda zai gaza samun lada dubu a rana?)** Sai wani daga cikin waɗanda suke zaune a gabansa ya ce: ta yaya ɗayanmu zai sami lada dubu? Sai ya ce: **(Zai yi tasbihi ɗari, sai a rubuta masa lada dubu, a kuma share masa zunubi dubu).**

Haka ma akwai zikirorin da ake karantawa lokacin cin abinci da shan abin sha, kaman faɗin **"BismilLah"** a lokacin farawa, da **"AlhamdulilLah"** a ƙarshe, an ruwaito Hadisi daga Umar Bn Abu Salama (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Na kasance yaro hadimi a gidan Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), hannu na yana shawagi a kwanon abinci, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce mini: **(Ya kai ƙaramin yaro, ka ambaci sunan Allah, ka kuma ci da hannunka na dama, ka kuma ci gabanka)**, idan Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) zai ci abinci yakan ce:

**"الْحَمْدُ لِلَّهِ الَّذِي أَطْعَمَنَا ، وَسَقَانَا ، وَجَعَلَنَا مُسْلِمِينَ"**

Haka ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sunnanta mana ambaton Allah Maɗaukakin Sarki a lokacin da za mu shiga kasuwa, ya kuma bayyana mana cewa hakan yana da babban lada, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda idan zai shiga kasuwa ya ce:**

**"لَا إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ وَحْدَهُ لَا شَرِيكَ لَهُ ، لَهُ الْمُلْكُ وَلَهُ الْحَمْدُ ، يُحْيِي وَيُمِيتُ ، وَهُوَ حَيٌّ لَا يَمُوتُ ، بِيَدِهِ الْخَيْرُ كُلُّهُ ، وَهُوَ عَلَى كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ"**

**za a rubuta masa lada miliyan ɗaya, a kuma share masa zunubi miliyan ɗaya, a kuma gina masa gida a aljanna).**

Haka ma ya kamata Musulmi ya rinƙa ambaton Allah a duk sanda ya ga wani abu da ya burge shi, yana mai cewa:

**"ما شاء الله لا قوة إلا بالله".**

Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Ina ma a ce lokacin da ka shiga gonarka cewa ka yi: Haka Allah ya so, babu wani ƙarfi sai na Allah..))** **[al- Kahfi: 39]**, haka ma a lokacin da aka ga waɗanda bala'i ya auka masu, ya kamata a gode wa Allah a cikin zuciya, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda kwatsam ya ga wanda bala'i ya faɗa masa, sai ya ce:**

**"الْحَمْدُ لِلَّهِ الَّذِي عَافَانِي مِمَّا ابْتَلَاكَ بِهِ ، وَفَضَّلَنِي عَلَى كَثِيرٍ مِمَّنْ خَلَقَ تَفْضِيلًا".**

**za a ba shi kariya ga barin faɗawa cikin wannan bala'in komin girmansa)**.

Haka ma shi Mumini a koda yaushe yana komawa zuwa ga Ubangijinsa a lokacin damuwa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Haka ma Annabi Yunus (AlaiHis Salam) lokacin da ya tafi bayan ya yi fushi, ya zaci ba za mu ƙuntata masa ba, sai kuwa ya tsinci kansa a cikin duhun cikin kifi, sai kuwa ya roƙi Ubangijinsa da cewa: Babu abin bautawa da gaskiya sai kai, na ambaci tsarki ya Ubangiji, lallai na kasance cikin azzalumai.. Sai kuwa muka amsa masa, muka tseratar da shi daga damuwar da ya tsinci kansa a ciki, da ma da haka ne muke tsiratar da muminai))** **[al- Anbiya'i: 87 -88]**, Idan damuwa ta sami Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan ce:

**"لاَ إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ العَظِيمُ الحَلِيمُ ، لاَ إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ رَبُّ السَّمَوَاتِ وَالأَرْضِ ، وَرَبُّ العَرْشِ العَظِيمِ".**

Waɗannan waɗansu rukunnai ne na zikirori da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sunnanta mana, duk wanda ya lizimce su, za su zamo masa shiriya, da tsira ga barin rafkana, da kuma kariya ga barin shaiɗan, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar da littafin da ma'anoninsa da lafuzzansa suka yi kama da juna wajen isa matuƙa a gagara da mu'ujiza, da kuma tsarin hukunce – hukunce, wa'azi da hukunce – hukunce suna kai-komo a cikinsa, kaman yanda ake yawan maimaita tilawarsa, fatun waɗanda suka jin tsoron Ubangijinsu suna raurawa a duk sanda suka yi ana karanta ayoyin azaba da narkon cikinsa, sannan kuma fatun nasu da zukatansu sukan yi laushi a lokacin da ake ambaton Allah, lallai wannan littafi da yake ƙunshe da waɗannan sifofi haske ne na Allah da yake bayar da shi ga wanda ya so, ya datar da shi zuwa ga hanyar imani da shi, duk wanda Allah ya ɓatar da shi – sakamakon sanin da ya yi na cewa da ma can zai juya wa gaskiya baya- to kuwa lallai babu wani mai shiryatarwa da zai tsamo shi daga wannan ɓata))** **[az- Zumar: 23]**, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ka ambaci Ubangijinka a cikin zuciyarka kana mai ƙasƙantar da kai, kuma a ɓoye, kai ba ka bayyana ta hanyar ɗaga murya ba, a safiya da maraice, kada kuskura ka zamo cikin marafkana))** **[al- A'araf: 205]**, Allah mabuwayi yana cewa: **((Duk wanda ya rafkana ga barin ambaton Allah mai yawan rahama, sai mu samar masa da shaiɗanin da zai abokatance shi))** **[az- Zukhraf: 36]**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da salami shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai ambaton Allah Maɗaukakin Sarki a wurin Sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) manhaji ne na rayuwa, da suke gabatarwa a aikace, saboda haka ne al'ummarsu ta zamo cike take da muraƙabar Allah Maɗaukakin Sarki, da kuma nesantar cutar da wasu, akan haka ne lokacin da Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya naɗa Sayyiduna Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ƙara yarda da shi) alƙalanci, Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya kwashe shekara ɗaya cur, ba tare da wani ya shirga da ƙara a wurinsa ba, a lokacin sai ya nemi Sayyiduna Abubakar as - Siddiƙ (Allah ya ƙara yarda da shi) da ya amince ya sauke shi daga alƙalancin, sai ya ce masa: wahalhalun alƙalanci ne suka sanya kake neman a sauke ka ya Umar?, Sai Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: ba haka ba ne ya Halifan Manzon Allah, kawai dai muminai ba su da wata buƙata daga gare ni, kowa daga cikinsu ya san haƙƙinsa, bai nemi sama da hakan ba, ya kuma san haƙƙin da yake akansa, bai yi nawa wajen sauke shi ba, kowa daga cikinsu yana so wa ɗan uwansa abin da yake so wa kansa, idan ba su ga ɗaya daga cikinsu ba, suna zuwa su san yanayin da yake ciki, idan ya yi rashin lafiya sukan gaishe shi, idan talauci ya kama shi, sukan taimake shi, idan ya nemi wata buƙata sukan taimaka masa, idan wata damuwa ta same shi, sukan yi masa jaje, da Allah ya

kyauta, addininsu nasiha ne, ɗabi'unsu kuma su ne: bayar da umurni da ayyuka masu kyau, da hana aikata munana, tun da kuwa haka ne, mene zai sanya su yi husuma? tun da kuwa haka ne, mene zai sanya su yi husuma?.

Lallai idan ambaton Allah Maɗaukakin Sarki ya sami wurin zama a cikin zuciyar bawa, ya kuma maimata shi da harshensa, gaɓoɓinsa kuma suka aikatar da shi a aikace, sai zuciyarsa ta sami "istiƙama", ya kuma sami yardar Allah Maɗaukakin Sarki, Allah mai girma kuma ya yi masa albarka a cikin arzikinsa, damuwarsa ta kwaranye, natsuwa da rahama kuma su mamaye ƙirjinsa..

**Ya Allah Ubangiji, muna roƙonka ka taimake mu wajen ambatonka da gode maka, da kuma kyautata yi maka bauta, ka kiyaye ƙasashenmu, ka yawalta masu arziki da tsaro da aminci, da ma sauran ƙasashen duniya baki ɗaya.. Amin.**

**- 6 –**

## MUHIMMANCIN DA ALƘUR'ANI YA BAI WA KYAWAWAN ƊABI'U

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Lallai wannan Alƙur'anin yana shiryatarwa zuwa ga hanya madaidaiciya, yana kuma yi wa muminan da suke aikata ayyuka na gari albishir ɗin cewa lallai suna da lada mai girma)) [al- Isra'i: 9]**. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai fuskokin girma da daraja a cikin Alƙur'ani mai girma sun wuce a ƙirga su, ko a lissafa, shi Alƙur'ani mai girma shi ne igiyar Allah mai ƙarfi, zikiri ne shi mai cike da hakimi, haske ne bayyananne, wanda ba ya jirkicewa, ɓata ba ta iya gegarsa ta kowace hanya, malamai ba sa iya ƙoshi da shi, ba kuma ya rududdugewa sakamakon yawan maimaitawa, abubuwan ban mamakin cikinsa ba sa ƙarewa, duk wanda ya yi magana da shi zai faɗi gaskiya, duk wanda ya yi aiki da shi zai sami lada, duk wanda ya yi hukunci da shi zai yi adalci, duk kuma wanda ya yi kira zuwa gare shi za a shiryatar da shi zuwa ga hanya

madaidaiciya, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Mun saukar maka da Alƙur'ani ne a matsayinsa na bayani na komai, kuma shiriya ne da rahama gami da albishir ga masu miƙa wuya zuwa ga Allah))** **[an- Nahl: 89]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ba mu bar komai wanda babu shi a cikin Alƙur'ani ba..))** **[al- An'am: 38].**

Lallai a cikin manyan fuskokin girma da daraja da Alƙur'ani mai girma ya muhimmanta akwai: kulawar da ya yi da gina kyawawan ɗabi'u a rayuwar mutum, a matsayinsa na shi kaɗai, da rayuwar al'ummomi, ta hanyar wasu tsare- tsare, da ƙa'idoji da suke tsara rayuwar ɗan Adam, waɗanda suke gina al'umma mai cike da haɗin kai, waɗanda suke da tsarkakan ruhi, da zukata, inda mazauna cikinsu za su ginu akan gaskiya, da amana, da tausayi, da adalci wajen mu'amalarsu da juna, kowa daga cikinsu ya yi amanna da sunnar samun saɓani tsakanin mutane, da kyautata rayuwar tare, da mutunta juna, da yin aiki tuƙuru wajen raya duniya ta hanyar addini, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku mutane, lallai mun halicce ku ne daga asali ɗaya wanda dukanku kuke daidai da juna, wannan asali kuwa shi ne Annabi Adam da Hauwa'u (Alaihimas-Salãm), ta hanyar auratayya ne kuma muka mayar da ku al'ummomi masu yawa da ƙabilu mabambanta; domin ku san juna, ku kuma yi taimakekeniya a tsakaninku, lallai wanda ya fi matsayi a wurin Allah duniya da lahira shi ne wanda ya fi ku tsoron Allah, tabbas ilimin Allah ya game komai, ƙwararre ne kuma wanda babu wani abu komin ƙanƙantarsa da zai ɓuya masa a cikin dukan al'amurra**)) **[al- Hujrat: 13]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Da Ubangijinka ya so da sai ya halicci mutane a matsayin al'umma ɗaya, sai dai**

**bai so hakan ba, saboda haka za su cigaba da zama a matsayin masu bambanci da juna, sai dai kawai wanda Ubangijinka ya tausaya masu..))** **[Hud: 118 – 119]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((Shi Allah Maɗaukakin Sarki, shi ne ya halicce ku daga ƙasa, ya kuma nemi da ku raya ta..))** **[Hud: 61]**.

Lallai duk mai duba ta lura ga ayoyin Alƙur'ani mai girma, tabbas zai fahimci cewa kyawawan ɗabi'un da Alƙur'ani mai girma ya yi kira zuwa gare su, ba irin waɗanda za a iya wadatuwa da su ba ne, ko kuma waɗanda za a yi aiki da su a wasu wurare banda saura ba, hasali ma rukuni ne na tabbatattun kyawawan ɗabi'un da ba sa sauyawa sakamakon sauyin zamani da wuri, babban abin da zai tabbatar da haka kuwa shi ne: waɗannan kyawawan ɗabi'u manhaji ne na rayuwar da Annabin (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya gudanar a aikace, ya kuma kwaɗaitar da mutane a kai, bayan ya kira su zuwa gare su, lokacin da aka tambayi Ummul muminina, Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) game da halayen Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ba ta lissafo wasu ɗabi'u mabambanta ba, ta fuskantar da mai tambayar ne zuwa ga Alƙur'ani mai girma, an ruwaito Hadisi daga Sa'ad Bn Hisham, game da maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **((Tabbas kana kan kyawawan ɗabi'u masu girma))** **[al-Ƙalam: 4]**, ya ce: Na tambayi Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita): Ya Ummul muminina, faɗa mini kyawawan ɗabi'un Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ta ce: kana karanta Alƙur'ani?, sai na ce: Ey, sai ta ce: **Lallai ɗabi'un Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) shi ne Alƙur'ani**, wannan faɗakarwa da Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta yi wa mai tambaya, wani ƙarin tabbatarwa ne akan lallai

Alƙur'ani da duk abubuwan da ya ƙunsa na aƙida, da shari'a, da ibadu, da mu'amaloli duka ginshiƙai ne na gina ɗan Adam akan turbar kyawawan ɗabi'u, kuma Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) shi ne babban misali na irin wannan ɗan Adam ɗin a dukan sha'anonin rayuwarsa.

A cikin muhimman kyawawan ɗabi'un da Alƙur'ani mai girma ya tabbatar akwai: **mutunta ɗan Adam, da kiyaye karamarsa, da kuma rashin wulaƙanta shi**, wannan kam umurni ne na Allah Maɗaukakin Sarki a cikin littafinsa mai girma, inda ya umurci kowane mumini da ya tsarkake kansa daga barin duk wani abu da zai cutar da waninsa, irinsu: izgilanci, da wulaƙanci, da munana zato, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, kada wasu mazaje daga cikinku su yi wa wasu mazaje na daban izgilanci, mai yiwuwa ne su kasance mafiya alhairi a wurin Allah sama da masu izgilanci. Kada kuma mata muminai su yi wa wasu matan muminai izgilanci, mai yiwuwa ne waɗanda aka yi masu izgilancin su fi alhairi a wurin Allah sama da masu izgilancin. Kada wani sashenku ya aibata wani sashe, kada wani daga cikinku ya kira ɗan uwansa da suna, ko laƙabin da ba ya so, lallai a ambaci mumini da sunan fasiƙanci bayan ya sifantu da imani abu ne mai muni ƙwarai, duk wanda bai dawo daga rakiyar haka, ya bar abubuwan da aka hana ba, to lallai shi ne –shi kaɗai- yake zaluntar kansa da ma wasunsa))** **[al- Hujrat: 11]**, haka ma mai girma da ɗaukaka ya ce: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku nesanci yin mafi yawan munanan zaton da ake yi wa mutanen kirki, lallai wasu sassa na zace-zace laifi ne da ya cancanci a yi uƙuba akansa, kada ku bibiyi neman sanin sirrin Musulmai, kada**

**wani sashe naku ya ambaci wani sashe da abin da yake ƙi a lokacin da ba ya nan, shin akwai wani cikinku da yake son ya ci naman ɗan uwansa ɗanye bayan ya mutu? Lallai ba ku son haka, don haka ku nesanci yi da mutane; saboda daidai yake da cin namansu, ku kare kanku daga azabar Allah ta hanyar aiki da umurnin da ya bayar da nesantar abin da ya hana. Lallai Allah mai yawan amsar tuban masu tuba ne, mai kuma mayalwaciyar rahama ne ga talikai))** **[al- Hujrat: 12]**, shi imani yana gadar da lafiyar zuciya, Allah mai girma yana cewa: **((Da ma a ce lokacin da kuka ji, muminai maza da mata sun yi wa junansu zato na alhairi, su ce: wannan kam ƙarya ce bayyananniya?!))** **[an- Nur: 12]**.

Haka ma a cikin kyawawan ɗabi'un da Alƙur'ani mai girma ya muhimmanta tabbatar da su akwai: **ɗabi'ar taimakekeniya, da rungumar marasa ƙarfi, da tausayin juna**, inda Allah Maɗaukakin Sarki ya umurci ɗaukacin al'umma da su yi taimakekeniya da juna akan turba na ayyukan alhairi, da tsoron Allah, Allah mai girma yana cewa: **((Ku yi taimakekeniya akan yi wa Allah biyayya da tsoronsa, kada ku yi taimakekeniya akan saɓon Allah da zalunci..))** **[al- Ma'idat: 2]**, lallai taimakekeniya tsakanin mutane da junansu ginshiƙi ne daga cikin ginshiƙan samun ƙarfi ƙasa, da tabbatar da tsaro ga 'yan ƙasa, kowane mutum yana da buƙatun da yake son ya cimma, yana kuma yin iya bakin ƙoƙarinsa wajen samar da su, idan har tsarin taimakon juna ya yaɗu a cikin al'umma, to kowa zai sami natsuwa da kwanciyar hankali, hasali ma kowa zai yi gaggawa wajen taimaka wa waninsa daidai ƙarfi da ikon da yake da shi, alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa:

"Su mutane suna cigaba ne da mutane 'yan uwansu, shin Larabawa ne ko waɗanda ba Larabawa ba, sashensu ne yake ƙarfafar sashe, kai ko da ba su fahimci haka ba, dukansu hadiman juna ne".

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) a wurare masu yawa cikin Hadisai masu tsarki ya bayyana muhimmancin taimakekeniya, kaman inda yake cewa: **(Misalin muminai wajen soyayyar junansu, da jinƙan junansu, da tausayin junansu tamkar jiki ne da idan wata gaɓa ta cutu, duka sauran jikin zai kamu da rashin barci, da kuma zafin ciwo)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Musulmi ɗan uwan Musulmi ne, ba ya zaluntarsa, ba kuma ya bayar da shi, duk wanda ya tsaya wajen biyan buƙatar ɗan uwansa, Allah zai tsaya masa wajen biyan buƙatarsa, duk wanda ya yaye wa Musulmi wani baƙin- ciki, Allah zai yaye masa baƙin- ciki daga cikin baƙin- cikin ranar alƙiyama, duk wanda ya suturta Musulmi, Allah zai suturta shi ranar alƙiyama)**.

A cikin waɗannan ɗabi'un akwai: **ɗabi'ar tunani, da aiki da hankali,** lallai Allah mai girma da buwaya ya umurci bayinsa da su rinƙa yin tunani a cikin halittun sammai da ƙasa, Maɗaukakin Sarki ya yabi masu tunani a inda yake cewa: **((Lallai a cikin halittar da Allah ya yi wa sammai da ƙasa, da abubuwan da suke cikin su na ƙwarewa da gwaninta, da saɓanin da dare da rana suke da shi, na haske da duhu, tsawo da gajerta, akwai bayyanannun ayoyin ga masu hakalin da suke iya riskar kaɗaitakar Allah da ikon sa. Shi kuwa sha'anin masu hankali –a koda yaushe- shi ne su halarto da girman Allah da buwayarsa cikin zukatansu, a kuma duk inda suke, shin suna tsaye ne, ko a zaune, ko a kwance, suna**

**tunani akan halittar sammai da ƙasa, da abubuwan da suke cikin su na ban mamaki, suna cewa: ya Ubangijin mu, lallai ba ka halicci waɗannan abubuwa ba sai domin hikimar da ka hukunta, kai ka tsarkaka ga barin tawaya, a'a, ka halicce su ne domin su zamo dalilai da za su yi nuni akan ikon ka, su kuma zamo alamu ne da za su nuna isar hikimar ka; saboda haka, ya Ubangiji ka tsare mu ga barin azabar wuta, ta hanyar katartad da mu zuwa ga hanyar yi maka biyayya)) [Ali Imran: 190 – 191]**, haka mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Shin ba za su yi duba na lura a cikin halittun da suke sammai da ƙasa ba ne?)) [al- A'araf: 185]**. Allah Maɗaukakin Sarki ya buɗe mana ƙofofin yin tunani da lura, yana cewa: **((Allah shi ne wanda ya ɗaukaka sama ba tare da turaku da kuke gani ba..)) [ar- Ra'ad: 2]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ka ce masu: yaya kuke gani idan da a ce Allah ya sanya maku rana ce ita kaɗai har zuwa ranar alƙiyama, wane ubangiji ne wanda ba Allah ba zai kawo maku daren da za ku sami natsuwa a cikinsa, shin ashe wannan bai isa ya sanya ku yi tunani ba?!)) [al- Ƙasasi: 72]**, haka ma ya umurce mu da yin tunani akan kawunanmu, Allah mai girma yana cewa: **((Shin ba za su yi tunani akan kawunansu ba ne?!)) [ar- Rum: 8]**, Allah mai girma yana cewa: **((A cikin halittar ƙasa kuma akwai dalilai na ƙarara da suke isar da wanda ya bi su zuwa ga yaƙini da tabbas. Kai, a cikin kawunanku ma akwai bayyanannun ayoyi, da kuka rafkana ga barinsu; domin haka ba ku ganin dalilansu ne?!)) [az- Zariyat: 20 – 21]**, lallai Alƙur'ani mai girma ya buɗe mana ƙofofin tunani a cikin duk wani abu da zai amfani ɗan Adam, shi wannan tunani ma ibada ne kaman yanda Sahabbai, da Tabi'ai (Allah ya ƙara yarda da su) suka fahimta, suka kuma riski manufarsa,

Sayyiduna Abuddarda'i (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **Tunanin sa'a ɗaya ya fi ƙiyamullaili alhairi**, Wahab Bn Munabbih (Allah ya ƙara masa rahama) yana cewa: **Mutum bai taɓa yin tunani mai tsawo ba face ya fahimta, bai kuma taɓa fahimta ba face ya sami ilimi, bai kuma taɓa samun ilimi ba face ya yi aiki da shi**.

Haka ma a cikin muhimman kyawawan ɗabi'un da Alƙur'ani mai girma ya muhimmanta akwai: **ɗabi'ar tattaunawa, da mutunta mutane,** ayoyi masu yawa a cikin Alƙur'ani suna karantar da al'umma, kai, suna karantar da ɗaukacin bil'adama zuwa ga muhimmancin tattaunawa a rayuwar mutane, lallai tattaunawa ne salon da Allah Maɗaukakin Sarki ya yardar wa Annabawa, da Manzanninsa a matsayin manhajin isar da saƙo ga mutane; saboda shi Musulunci ya yi imani da 'yancin yin addini, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shi al'amarin addini babu tilastawa a cikinsa, tuni shiriya ta bambanta da halaka..)) [al-Baƙra: 256]**, ga ma Annabin Allah Nuhu (AlaiHis Salam) nan yana yi wa mutanensa magana a ɗaya daga cikin lokacin mai tsawo da ya kwashe a rayuwarsa yana kira zuwa ga Allah, yana cewa: **((Ya ku mutane na, yaya kuke tunani idan ni nake kan gaskiyar da ta zo daga Ubangiji na, ya kuma ba ni rahama daga wurinsa, amma sai kuka ta ɓuya maku ba ku ganta ba, shin zan ƙaƙaba maku gaskiya ta ce da ƙarfi, alhalin kuna ƙinta?!)) [Hud: 28].**

Ga kuma Annabi Ibrahim (AlaiHis Salam) nan yana kafa wa gagararren sarki hujja, ta hanyar tattaunawa ta hankali, wanda Alƙur'ani mai girma ya naƙalto mana da cewa: **((Shin ba ka ga wanda ya makance ga barin ganin hujjojin imani, ya fara**

**jayayya da Annabi Ibrahim "Khalilul-Lah" (AlaiHis-Salãm) akan Allantakar Ubangijinsa da kaɗaituwarsa, ta yadda ji-ji da kansa akan mulkinsa –da Ubangijinsa ya ba shi- ya fitar da shi daga hasken halittar da aka halicce shi da shi zuwa duhun kafirci ba?, lokacin da Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm) ya ce masa: lallai Allah yana rayawa da matarwa ta hanyar busa rai cikin jiki da cire shi daga jiki, sai ya ce: Ni ma ina rayarwa, ina kuma matarwa ta hanyar afuwa da kisa, sai Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm) ya ce masa domin ya yanke wannan jayayya tare da shi: to, lallai Allah shi ne yake fito da rana daga mahudarta, to, kai ka fito da ita ta mafaɗarta, in dai kai Ubangiji ne kamar yadda kake riyawa, nan da nan sai ya ruɗe ya dakatar da jayayyarsa; saboda ƙarfin hujjar da ta bankaɗo gajiyawarsa da ruɗin da yake wa kansa, lallai Allah ba ya katartad da masu ƙememe da taurin-kai zuwa ga gaskiya))** **[al-Baƙra: 258]**, a irin wannan manhajin ne ma Annabi Musa (AlaiHis Salam) ya tafi a tattaunawarsa da Fir'auna, game da haka ne Allah mai girma da ɗaukaka yake cewa: **((Sai Fir'auna ya ce: wane ne kuma Ubangijin talikai? Sai Annabi Musa ya ce: Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu, in dai har kun gasgata haka za ku amfana. Sai Fir'auna ya ce wa waɗanda suke gefensa: ba kun ji ba?!, Sai Annabi Musa ya ce: Ubangijinku, kuma Ubangijin iyayenku na farko. Sai Fir'auna ya ce: Lallai wannan Manzon da aka aiko maku tabbas mahaukaci ne. Sai Annabi Musa ya ce: shi ne Ubangijin mahuda rana da mafaɗarta da abin da yake tsakanisu, in dai kuma da tunani za ku fahimci haka. Sai Fir'auna ya ce: Tabbas idan idan ka riƙi wani ubangiji ba ni bazan sanya ka cikin fursunoni))** **[as- Shu'ara'i: 23 – 29]**.

Lallai irin yanda Alƙur'ani mai girma ya ƙarfafa ɗabi'ar tattaunawa, tamkar wani kira ne zuwa ga ƙololuwar ɗaukaka, da mutunta juna, ba tare da la'akari da launin fata, ko addini, ko jinsi ba, kuma hakan tamkar yaƙi ne da kallo na girman kai, da ta'assubanci, da wariya, da jiji da kai, ganin cewa Alƙur'ani mai girma ya kiyaye wa ɗan Adam karamarsa a matsayinsa na ɗan Adam, ba wai domin wani abu daban ba, ya kuma tabbatar da asalinsa guda ɗaya, duk kuwa da bambanci da yake tsakaninsu, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai mun karrama ɗan Adam, muka ɗauke su akan tudu da a cikin kogi, muka kuma azurta su da kayan jin daɗi masu tsarki, muka fifita su sosai akan da yawa daga cikin halittunmu)) [al-Isra'i: 70]**, haka ma Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ya ku mutane, ku ji tsoron Ubangijunku da ya samar da ku daga rai ɗaya, daga kuma cikin wannan ran ya samar masa da abokin zama, daga kuma su ne aka sami maza da mata masu tarin yawa, dukan ku kuna komawa ne zuwa ga wannan ran guda ɗaya, ku ji tsoron Allah wanda da shi ne kuke neman taimako wajen biyan buƙatunku, kuma da albarkar sunansa ne wani sashe naku yake tambayar wani sashe wurin sauye-sauyen al'amurra, ku kuma kiyaye zumunta, kada ku soma ku yanke ta, shin ta kusa ce, ko ta nesa, lallai Allah mai sanya ido ne a cikin al'amurran ku, babu wani abu naku da zai ɓuya masa, zai kuma sãkã maku akan haka)) [an- Nisa'i: 1].**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai a cikin kyawawan ɗabi'un da Alƙur'ani mai girma ya yi kira zuwa gare su, akwai: **kame zuciya, da haɗiye fushi,** kowa ya san cewa ɗan Adam a wannan rayuwar ba zai taɓa kuɓuta daga yanayin da zai ɓata masa rai, ya kuma sanya ya fusata ba, lallai zuciyar ɗan Adam tana tasirantuwa da abin da ta ji, ko ta gani, saboda haka ne ayoyi da yawa suka zo a cikin Alƙur'ani mai girma suna kiransa zuwa ga kame zuciya, da haɗiye fushi; da rungumar hanyar yafiya, da rangwame, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku yi gaggawa wajen aikata ayyuka na gari; domin ku sami babban gafara daga Allah da yake mallakar al'amurran ku, ku kuma sami shiga aljannar da faɗin ta ya kai faɗin sama da ƙasa, an tattale ta ne saboda masu tsoron Allah da masu nesantar azabar sa. Su kuwa waɗanda suke ciyar da dukiyoyin su a lokacin da suke cikin yalwa da ƙunci; da lokacin da suke da iko, ko suke da rauni; domin neman yardar Allah, suke kuma hana zukatan su azabtar da wanda ya munana masu, suke kuma yafiya ga waɗanda suka yi masu laifi, lallai waɗannan suna cikin mutanen kirki masu kyautatawa; kuma lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana bai wa mutanen kirki da masu kyautatawa lada, yana kuma yarda da su))** **[Ali Imran: 133 – 134]**, haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa:

**((Kada mutanen kirkin masu wadatar cikinku su hana alhairansu ga waɗanda suka cancanta cikin makusanta, da miskinai, da waɗanda suka yi hijira saboda Allah sakamakon kowane irin dalili ne kuwa da ya shafe su, kaman idan sun yi masu ba daidai ba, kamata ya yi su yafe masu, su kuma kawar da kai ga barin mayar masu da martani, idan dai har kuna son Allah ya yafe maku kura-kurenku, to ku ma ku yafe wa waɗanda suka yi maku ba daidai ba, irin dai yanda kuke son Ubangijinku ya yi maku, ku yi sifantu da sifarsa, lallai shi mai mayalwaciyar gafara da rahama ne)) [an- Nur: 22]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kyawawan ayyuka ba za su taɓa yin daidai da munana ba, kai dai kawai tunkuɗe mummuna da abin da ya fi kyau, sai wanda akwai gaba a tsakaninka da shi ya zamo tamkar aboki na kusa, wannan abu kuwa babu mai samunsa sai waɗanda suka yi haƙuri, kai babu mai samun haka sai mai babban rabo)) [Fussilat: 34 – 35]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Duk wanda ya yafe, ya kuma gyara abin da ya ɓaci ladansa yana wurin Allah..)) [as- Shurah: 40]**.

A cikin kyawawan ɗabi'un akwai: **sulhunta masu husuma da juna,** ayoyi masu yawa a cikin Alƙur'ani mai girma sun bayar da umurnin sulhunta tsakanin mutane, suna kuma yi wa masu yin sulhun albishir da babban lada, Allah mai girma yana cewa: **((A mafi yawan lokuta babu wani alhairi tattare da mutanen da suke ɓoye maganganun da suke yi a cikin zukatan su, ko waɗanda suke yi tsakanin su da juna; saboda sharri ne ake ɓoye shi, sai dai idan abin da aka ɓoyen ya zamo bayar da umurni ne da yin sadaka, ko aikata wani aiki mai kyau, ko daidaita tsakanin mutane da gyara zumunta,**

**waɗannan kam duka alhairai ne, duk wanda ya aikata haka saboda neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki, to kuwa lallai Allah Maɗaukakin Sarki zai ba shi babban sakamako a nan duniya da lahira; saboda abin da ya aikata))** **[an- Nisa'i: 114]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Amma idan wasiyyar ta saɓa da adalci da daidaitacciyar hanyar da muka bayyana, ta yadda mai wasici ya haramta wa mabuƙaci ya bai wa mawadaci, ko ya bar makusanta ya kula da mabuƙatan waje waɗanda ba magada ba, sai shi wanda aka bar masa wasicin ya yi wani ƙoƙari akan hanyar alhairi ya yi sulhu tsakanin waɗanda aka yi masu wasicin domin ya dawo da wasicin kan hanyarta ta daidai, wannan babu wani laifi akansa a sauya wasicin da ya yi ta wannan fuskar, Allah ba zai kama shi akan haka ba, lallai Allah mai yawan gafara da rahama ne))** **[al- Baƙra: 182]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Suna tambayarka game da al'amarin marayu, da abin da Musulunci ya wajabta game da su, sai ka ce masu: lallai gyara al'amurran su alhairi ne a gare ku, ku da su, ku shigo da su cikin gidajenku, ku yi cuɗanya da su; saboda manufar gyara al'amurran su, ba ɓata su ko lalata su ba, su 'yan uwanku ne a rayuwar duniya, haka ne zai sanya ku yi cuɗanya da su. Lallai Allah ya san mai niyyar ɓarna a cikinku da mai niyyar gyara, saboda haka ku yi taka-tsantsan. Da Allah ya ga dama, da sai ya tsananta maku, ta yadda zai wajabta maku ɗaukan nauyin kulawa da marayu ba tare da kun yi cuɗanya da su ba, ko ya ƙyale su ba tare da ya bayyana abin da ya wajaba game da su ba, su tashi suna ƙin sauran al'umma, hakan kuma kamar ɓata al'umman ku ne da tsananta masu, saboda takura masu da ƙasƙantar da su da kuke yi ne zai sa su ƙulle ƙiyayya ga**

**jama'an da suke rayuwa a tsakanin su. Lallai al'amarin Allah buwayi mai rinjaye ne, kuma shi mai yawan hikima ne, ba ya shar'anta komai sai abin da yake akwai maslaharku)) [al- Baƙra: 220]**, Allah mabuwayin Sarki ya gargaɗi mai tsanani wa masu ɓata tsakanin mutane, Allah mai girma yana cewa: **((Idan tsoron Allah ya kasance shi ne tushe, to kuwa asara ta tabbata ga wasu mutane waɗanda abin da zukatan su suka ƙulle a zukatan su ya saɓa da abin da harsunan su suke furuci da shi, an ba su daɗin-baki wajen tsara magana, maganar su za ta burgeka wajen yin makircin su na janyo amfani a rayuwar duniya, a riyawar su suna ƙarfafa maka cewa, lallai Allah ya san gaskiyar zukatan su akan abin da suka faɗi da harsunan su, kuma tabbas su ɗin nan sun fi dukan sauran mutane tsananin yin husama da kai da kuma tsananta maka. Idan aka ɗaura shi a wani matsayi da zai zamana yana da wani iko, ba ya aiki domin kawo gyara, a maimakon haka ma aikin ɓarna da lalata amfanin gona, da lalata tsatso yake sanyawa a gaba, lallai Allah ba ya sonshi, domin dai lallai Allah Maɗaukakin Sarki ba ya son ɓarna. Idan -a lokacin- a ka yi masa nasiha da ya ji tsoron Allah, sai hankalinsa ya tashi, yana mai zaton cewa kana son ka rusa girma da darajarsa ne, hakan sai ya sake sanya shi ya aikata zunubin da ka hane shi; saboda taurin-kai da kangara, azabar jahannama ta ishe shi, tir da wannan matabbaci)) [al- Baƙra: 204 – 206].**

Lallai muna matuƙar buƙatar riƙo da kyawawan ɗabi'un da littafin Allah mai girma da ɗaukaka ya kira zuwa gare su, Manzonmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) kuma ya aiwatar da su a aikace, saboda mu isa zuwa ga inda kakanninmu suka kai

wajen cigaba da ɗaukaka, alhairin Allah ya kai zuwa ga Shauƙiy a inda yake cewa:

"Muddin ka ga al'ummomi sun wanzu, to ka tabbaci haƙiƙanin kyawawan ɗabi'u suka runguma, idan kuma suka ƙare, to kyawawan ɗabi'un ne suka ƙare".

**Ya Allah Ubangiji ina roƙon ka shiryatar da mu zuwa ga mafi kyawawan ɗabi'un da babu mai shiryatarwa zuwa gare su in ba kai ba, ka kiyaye mu da munanan ɗabi'un da babu mai kare mu ga barinsu in ba kai ba, ka kiyaye mana ƙasarmu da al'ummarmu, da sojojinmu da 'yan sandanmu, ka azurta mu da tsaro da aminci, da sauran ƙasashen duniya.**

## - 7 –

## KYAWAWAN ƊABI'U NA MUTUNTAKA A SURATUL HUJRAT

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya Manzon Allah ka ce masu: Ni dai kam Ubangiji na ya shiryatar da ni zuwa ga madaidaiciyar hanya, addini ne tsayayye, wato addinin da Annabi Ibrahim (AlaiHis Sallam) ya zo da shi, mai cike da nagarta, lallai bai taɓa kasancewa cikin mashrikai ba))** **[al-An'am: 161]**. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda yake cewa: **(Lallai an aiko ne kawai saboda in cika kyawawan ɗabi'u)**.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Alƙur'ani mai girma cike yake da ayoyi masu girma, da suke dasa harsashen kyawawan ɗabi'u, masu kuma girma, hasali ma akwai surorin da gaba ɗayansu sun zo ne domin su kafa al'umma mai daraja da mutuntaka, kamar dai suratul Hujrat, wadda ta kafa wasu gungu na kyawawan ɗabi'u masu girma, irinsu: **bincike domin tabbatar da gaskiya a cikin komai,** musamman idan al'amarin yana da jiɓi da harkokin mutane, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda**

**kuka yi imani, idan wani fãsiƙi ya ƙetare shari'ar Allah ya zo maku da kowane irin labari, to ku bincika ku tabbatar da gaskiyarsa; saboda kada ku cutar da wasu mutane –da ba ku san haƙiƙaninsu ba-, hakan sai ya sanya ku yi nadama akan abin da kuka aikata, kuna: ina ma ba mu aikata hakan ba, a lokacin da bayani ya bayyana cewa ba su da wani laifi))** **[al-Hujrat: 6]**, shi addinin Musulunci yana gina komai nasa ne akan yaƙini da tabbas, ga Annabi Sulaiman (AlaiHis Salam) nan lokacin da al- Huda-huda ya zo masa da labarin waɗanda suke bauta wa rana ba Allah ba, ya sifanta labarin da cewa labarin ne na gaskiya da yaƙini, duk da haka bai amshi maganar haka kawai ba, sai da ya sanya aka bincika, aka tabbatar, kaman yanda Alƙur'ani mai girma ya kawo mana ta bakinsa, Allah Mai girma yana cewa: **((Ya ce: za mu bincika mu gani, shin gaskiya ka faɗa, ko kuwa kana cikin maƙaryata))** **[an- Namli: 27]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Zunubi ya kai zunubi a ce mutum ya bayar da labarin duk abin da ya ji)**, Imam An- Nawawi (Allah ya ƙara masa rahama) ya ce: a al'adance mutum yakan ji gaskiya da ƙarya, saboda haka idan ya bayar da labarin duka abin da ya ji, to lallai ya yi ƙarya kenan, saboda ya bayar da labarin abin da bai faru ba, lokacin da wani mutum ya shiga wurin Sayyiduna Umar Bn Abdul'aziz (Allah ya ƙara masa rahama) ya faɗa masa labarin wani mutum, sai ya ce masa: in kana so sai mu bincika al'amarinka, in ƙarya ka yi, to kana cikin waɗanda suke cikin wannan ayar: **((Idan wani fãsiƙi ya ƙetare shari'ar Allah ya zo maku da kowane irin labari, to ku bincika ku tabbatar da gaskiyarsa..))** **[al- Hujrat: 6]**, idan kuma maganarka gaskiya ce, to kana cikin wannan ayar: **((Mai yawan aibata mutane, mai**

**yawan yi da mutane, mai yawan yawo da maganganu a tsakaninsu da niyyar ɓata zamantakewa))** **[al- Ƙalam: 11]**, idan kuma kana so za mu iya yi maka afuwa, sai ya ce: Ya Amiral muminina, a yi mini afuwa, ba zan sake ba. Lallai da a ce kowannenmu yana bincika gaskiyar abin da ya zo masa domin ya tabbatar da shi, kafin ya yi hukunci, ko kafin ya yaɗa, da kuwa jita- jita ta rasa tasirinta, da kuma masu yaɗa jita – jita sun daina yaɗa ta a cikin al'umma.

Haka ma a cikin manyan ɗabi'un da wannan sura ta dasa akwai: **Nesantar yi da mutane,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada wani sashe naku ya ambaci wani sashe da abin da yake ƙi a lokacin da ba ya nan, shin akwai wani cikinku da yake son ya ci naman ɗan uwansa ɗanye bayan ya mutu? Lallai ba ku son haka, don haka ku nesanci yi da mutane; saboda daidai yake da cin namansu, ku kare kanku daga azabar Allah ta hanyar aiki da umurnin da ya bayar da nesantar abin da ya hana. Lallai Allah mai yawan amsar tuban masu tuba ne, mai kuma mayalwaciyar rahama ne ga talikai))** **[al- Hujrat: 12]**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi), Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Shin ko kun san mene ne giba?)**, sai suka ce: Allah da Manzonsa ne suka fi sani, sai ya ce: **(Ka ambaci ɗan uwanka da abin da yake ƙi)**, sai aka ce: To idan abin da aka faɗin yana tare da ɗan uwan nawa fa?, sai ya ce: **(Idan abin da ka faɗin yana tare da shi, to ka yi gibarsa kenan, idan kuma ba shi tare da shi, to ka yi masa ƙarya kenan)**, lallai babu abin da zai ingiza mutum wajen yi da mutane banda shagaltuwa da aibin mutane da kawar da kai ga barin aibobinsa, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam)

yana cewa: (Mutum yana ganin ƙura a idon ɗan uwansa, alhalin ya manta da kututture da yake idonsa).

Hasali ma an buƙaci ɗan Adam da ya bai wa mutuncin ɗan uwansa kariya, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya kiyaye mutuncin ɗan uwansa, Allah zai kiyaye fuskarsa ga barin wuta a ranar alƙiyama)**.

Haka ma akwai: **ɗabi'ar nesantar zunɗe,** Allah mai girma yana cewa: **((Kada wani sashenku ya aibata wani sashe..)) [al-Hujrat: 11]**, ma'ana: kada ku aibata junanku, shi "Lamzu" yana kasancewa ne ta hanyar magana, "Hamzu" kuma a aikace ake yinsa, lallai Alƙur'ani mai girma ya hana aikata duka biyu, Allah yana cewa: **((Azaba mai tsanani da halaka sun tabbata ga duk wanda tãdarsa ne aibata mutane ta hanyar magana ko nuni, ko yake magana wajen cin mutuncin mutane)) [al-Humazat: 1],** su ne waɗanda suke sukar mutane, suna aibata su, suna kuma kiransu da sunayen da ba sa so, ko su jingina masu sifofin da suke ƙyama, wannan ayar gargaɗi take yi ga masu aibata mutane da maganganunsu, ko da aikinsu, inda Allah ya yi masu tanadin azaba mai tsanani akan haka, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abdullahi Bn Mas'ud (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Lokacin da aka umurce mu da yin sadaka, mukan tafi kasuwa mu yi dako, sai Abu Aƙil ya zo da rabin sa'i ɗaya, wani mutum kuma ya zo da sama da abin da ya kawo, sai munafukai suka ce: Allah ya fi ƙarfin sadakar da wancan ya kawo, shi kuma wannan riya ce kawai ya yi, sai ayar: **((Waɗanda suke aibata masu bayar da taimako cikin muminai a sadakar da suka bayar, da waɗanda ba su da shi sai abin da suka himmatu wajen samar da shi, sakamakon haka sai suna yi masu izgilanci, Lallai Allah ne zai saka masu da**

**sakamakon izgilancin, suna da azaba mai raɗaɗi a ranar alƙiyama)) [at- Tauba: 79]** ta sauka.

Haka ma a cikin ɗabi'un akwai: **rashin yi wa mutane izgilanci,** shi mumini na gaskiya ba ya yin izgilanci, Allah mai girma yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, kada wasu mazaje daga cikinku su yi wa wasu mazaje na daban izgilanci, mai yiwuwa ne su kasance mafiya alhairi a wurin Allah sama da masu izgilanci. Kada kuma mata muminai su yi wa wasu matan muminai izgilanci, mai yiwuwa ne waɗanda aka yi masu izgilancin su fi alhairi a wurin Allah sama da masu izgilancin..)) [al- Hujrat: 11]**, lallai addininmu ya hana mu aikata duk wani abu da zai cutar da wasu, a cikin sifofin mumini dole ne ya zamo ba mai cutar da kowa ba, babu abin da yake fitowa daga gare shi sai alhairi ga mutane, da kuma amfanar bil'adama.

Lallai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya hana aikata duk wani abu da zai cutar da wasu, shin da magana ne, ko aiki, ko nuni, a koda yaushe (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana yi wa mutane mu'amala ta yanda zai ɗaga darajarsu, da girmansu a idon jama'a, an ruwaito daga Ummu Musa ta ce: An ambaci Abdullahi Bn Mas'ud a gaban Aliyu, sai ya faɗi falalarsa, sannan ya ce: wata rana ya hau wata bishiya, yana son ya ciro wa abokansa, sai abokan nasa suka yi masa dariya saboda gajartar ƙafarsa, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mene ne kuke yi wa dariya? Lallai nauyinsa a mizani ranar alƙiyama ya fi nauyin dutsen Uhdu)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabinmu Muhammadu da Alayensa da Sahabbansa, da waɗanda suka biyo bayansu.

**Ya ‘yan uwana Musulmai:** Lallai a cikin mafi girman ɗabi’un da suratul Hujrat ta yi kira zuwa gare su akwai: **Girma ‘yan uwantaka da gyara tsakanin masu saɓani da juna**, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa ba wasu abu ne ba face 'yan uwan juna, waɗanda tuni imani ya haɗa zukatansu, ku daidaita tsakanin 'yan uwanku biyu saboda kiyaye 'yan uwanta na imani, ku samar wa kawunanku da wata katanga da za ta kare ku ga barin azabar Allah ta hanyar aiki da umurninsa da nesantar abin da ya hana, kuna masu fatan Allah ya yi maku rahama saboda tsoron Allah da kuke yi)) [al- Hujrat: 10]**, lallai gyara tsakanin masu husuma da juna yana ɗaya daga cikin manyan ɗabi’un da wannan sura mai girma ta yi kira zuwa gare shi, abin da addininmu yake kira wajen samar da al’umma dunƙulalliya mai haɗin kai, da rangwame wa juna, abin da zai kai zuwa ga tabbatar da ƙimar rayuwar tare, a wani yanayi na sabo da kuma kusanci, nesa da rikici gami da saɓani, lallai wannan shi ne maganin duk wani abu da zai kai zuwa ga rikici gami da saɓani.

A cikin rayuwar iyali ma Alƙur’ani mai girma ya yi kira da a duk sanda aka sami saɓani tsakanin ma’aurata, suka gaza warware shi a tsakaninsu, to a nemi waɗanda ake kyautata masu zaton kawo gyara daga cikin danginsu; domin su shiga tsakani, su yi masu sulhu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa:

**((Idan aka sami saɓani a tsakanin ma'aurata biyu, kuka kuma ji tsoron kada ya girma ya kai ga rikicin da zai kai su ga rabuwa, to, ku zaɓi masu sulhu guda biyu: ɗaya daga danginsa, ɗayan kuma daga danginta. In dai sun yi nufin kawo gyara, to, lallai Allah zai datar da su zuwa ga abin da yake shi ne alhairi ga ma'auratan, ko dai su cigaba da zaman auren cikin kyautata wa juna, ko kuma su rabu cikin mutunci. Lallai Allah yana riskar duk wani abu na zahiri da baɗinin da yake tattare da bayi))** **[an- Nisa'i: 35].**

Wannan ruhi na gyara ya cigaba zuwa cikin al'umma gaba ɗaya, domin a samar da nagartacciyar al'umma, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((A mafi yawan lokuta babu wani alhairi tattare da mutanen da suke ɓoye maganganun da suke yi a cikin zukatan su, ko waɗanda suke yi tsakanin su da juna; saboda sharri ne ake ɓoye shi, sai dai idan abin da aka ɓoyen ya zamo bayar da umurni ne da yin sadaka, ko aikata wani aiki mai kyau, ko daidaita tsakanin mutane da gyara zumunta, waɗannan kam duka alhairai ne, duk wanda ya aikata haka saboda neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki, to kuwa lallai Allah Maɗaukakin Sarki zai ba shi babban sakamako a nan duniya da lahira; saboda abin da ya aikata))** **[an- Nisa'i: 114].**

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana sakamakon kawo gyara da sulhu a cikin al'umma, da tasirin lalacewar dangantaka, a inda yake cewa: **(Shin ba na faɗa maku abin da darajarsa ya fi na sallah da sadaka ba?)** sai suka ce: Ey, ya Manzon Allah faɗa mana, sai ya ce: **(Daidaita tsakanin masu husuma da juna, lalacewar dangantaka ita ce:**

**mai aske komai, ba wai aske gashi nake nufi ba, ina nufin aske addini)**.

Lallai mumini na haƙiƙa shi ne wanda ya ɗauki gyara da sulhu suka zamo masa manhaji a rayuwa, duk inda aka same su, to alhairi yana nan a wurin, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai a cikin mutane akwai waɗanda su mabuɗai ne na alhairi, makullai ne kuma su na sharri, haka ma a cikin mutane akwai waɗanda su mabuɗai ne na sharri, kuma su makullai ne na alhairi, aljanna ta tabbata ga waɗanda Allah ya sanya mabuɗan alhairi a hannunsu, azaba kuma ta tabbata ga waɗanda Allah ya sanya mabuɗan sharri a a hannunsu)**.

**Ya Allah Ubangiji ka shiryatar da mu zuwa ga mafi kyawon ɗabi'un da babu mai shiryatarwa zuwa ga mafi kyawonsu sai kai, ka kiyaye mu daga barin munanan ɗabi'un da babu wanda yake kiyaye wa zuwa ga mafi muninsu sai kai, ka kiyaye mana ƙasarmu, da sauran ƙasashen duniya baki ɗaya.**

## - 8 –

## SUNNAR MANZON ALLAH DA MATSAYINTA A SHARI'A

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Duk hukunce-hukuncen da Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya zo maku da su ku riƙe su da kyau, abubuwan da ya hana ku kuma, ku barsu, ku samar wa kawunanku garkuwar da za ta kare ku ga barin fushin Allah, lallai Allah mai tsananin uƙuba ne))** **[al-Hashri: 7]**. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda yake cewa: **(Na bar maku abin da ida kuka riƙi shi da kyau, ba za ku ɓace ba har abada: littafin Allah da Sunnar Annabinsa)**.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah Mai girma da buwaya ya aiko Manzanni da Annabawa ne saboda su shiryatar da mutane, su riƙe hannunsu, su fitar da su daga cikin duhu zuwa haske, su tseratar da su daga hanyar halaka zuwa hanyar tsira da samu babban rabo, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai mun aiko da manzanninmu da muka zaɓe su, muka kuma ba**

**su wasu ƙarfafan mu'ujizozi, mun kuma saukar masu da littattafai waɗanda suke ƙunshe da hukunce-hukunce da shari'o'in addini, da ma'aunin da zai tabbatar da adalci wajen mu'amala; domin mutane su yi ta'amuli da adalci a tsakaninsu..**)) **[al- Hadid: 25]**, sannan Allah mai tsarki ya cike zurin saƙwanninsa da Sayyiduna Muhammadur RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam), ya zo ne kaman yanda Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Mai shaida, kuma mai albishir, kuma mai gargaɗi. Mai kuma kira zuwa ga Allah da izinin Allah, haske ne kuma mai haskakawa)) [al- Ahzab: 45 -46]**, ya zo da saƙon ƙarshe, wanda ya yi daidai da kowane zamani, da kuma kowane wuri, ya saukar masa da Alƙur'ani mai girma, littafi ne tsararre mai cike da hikima, kuma mu'ujiza, ɓata ba ta iya gegarsa ta kowace fuska. Sannan ya yi masa wahayin Sunna mai daraja da take fayyace bayanan da Alƙur'ani ya ƙunsa, tana yin ƙarin haske akansa, Allah mai girma yana cewa: **((Ba ya yin maganarsa akan son zuciya. Wahayi ne kawai ake yi masa)) [an- Najmi: 3 -4]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Mun kuma saukar maka da Alƙur'ani mai girma ne domin ka bayyana wa mutane abin da aka saukar masu, ko za su yi tunani)) [an- Nahl: 44]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ku sani cewa lallai an ba ni Alƙur'ani da kwatankwacinsa tare da shi..)**

Mai yi wa Alƙur'ani mai girma duba na lura zai ga cewa: Allah Maɗaukakin Sarki ya haɗa tsakanin umurninsa mai girma da ɗaukaka, da umurnin Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) a wurare masu yawa, Allah mai girma yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku amsa kiran Allah da Manzonsa idan ya kira ku zuwa ga abin da zai raya ku..)) [al-**

**Anfal: 24]**, ya kuma gwama tsakanin yardarsa mai girma da ɗaukaka da yardar Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) a inda yake cewa: **((Allah da Manzonsa ne suka fi cancanta su ne yardarsa inda su muminai ne na gaskiya)) [at- Taubat: 62].**

Kaman yanda Allah mai girma da buwaya ya gwama tsakanin yi masa biyayya da yi wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) biyayya, a inda Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Duk wanda ya yi wa Manzon Allah biyayya, to lallai ya yi wa Allah biyayya ne..)) [an- Nisa'i: 80]**, ya kuma sanya wannan biyayya ta zamo dalilin samun rahama, mabuwayin Sarki yana cewa: **((Ku yi wa Allah da Manzon Allah biyayya saboda ta yiwu a yi maku rahama)) [Ali Imran: 132]**, a wani wurin kuma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku yi wa Manzon Allah biyayya saboda ta yiwu a yi maku rahama)) [an- Nur: 56]**, wannan biyayya tana tabbata ne ta hanyar bin Sunnarsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya Manzon Allah, ka ce masu: idan dai har da gaske ne kuna son Allah, to ku yi mini biyayya, take Allah zai so ku, ya kuma gafarta maku zunubanku, lallai Allah mai yawan gafara da rahama ne)) [Ali Imran: 31].**

Lallai ɗaukacin malaman al'umma, da masana Fiƙhun cikinta sun haɗu akan cewa lallai Sunna hujja ce mai girma ta Shari'ar Musulunci, ita ce madogara ta biyu na hukunce – hukunce bayan littafin Allah Mai girma da buwaya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah kuma ya saukar maka da Alƙur'ani da Hikima, ya sanar da kai abin da ba ka sani ba, lallai da ma falalar da Allah ya yi maka mai girma ce)) [an- Nisa'i: 113]**, haka mai Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku matan Annabi, ku tuna da abin da ake karantawa na ayoyin**

**Allah da Hikima a ɗakunanku, lallai Allah mai yawan tausayi ne, mai kuma cikakken masaniya akan komai)) [al- Ahzab: 34],** Idan aka ce: Sunna mai girma ta ƙunshi: maganarsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), da aikinsa, da abubuwan da ya tabbatar, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai kuna da abin koyi mai kyau a rayuwar Manzon Allah, wannan fa ga wanda yake ƙaunar Allah da kuma kwaɗayin samun tsira a ranar lahira, yake kuma yawaita ambaton Allah kenan)) [al- Ahzab: 21],** wannan kuwa ya shafi dukan sassan rayuwarsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abdullahi Bn Amru (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: Da ina rubuta duk wani abu da na ji daga Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), da nufin in haddace shi, sai Ƙuraishawa suka hana ni, suka ce: yanzu rubuta duk abin da ka ji daga Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) kake yi, alhali Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan yi magana a halin yarda da halin fushi? Sai na daina, sannan daga baya na faɗa wa Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) abin da ya faru, sai ya yi nuni zuwa ga bakinsa da hannunsa, sai ya ce: **(Ka rubuta, na rantse da wanda rayuwa ta take hannunsa, babu abin da yake fita daga nan sai gaskiya)**.

Lallai Alƙur'ani mai girma shi ne ginshiƙin Shari'a na farko, Sunna mai tsarki kuma ginshiƙi na biyu, domin aikinta shi ne ƙarin haske, da sharhi, da kuma bayyana abin da ya zo a cikin littafin Allah mai girma da buwaya; saboda dai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) shi ne ya fi kowa sanin manufar Allah Maɗaukakin Sarki, hukuncinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) hukunci ne na Allah mai girma da ɗaukaka, Allah mai girma yana cewa: **((Sam bai kamata mumini, ko mumina su**

**zamo suna da zaɓin wani al'amari nasu a abin da Allah da Manzonsa suka hukunta ba))** **[al- Ahzab: 36]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Na rantse da Ubangijinka ba za a taɓa sanya su cikin muminai na gaskiya, masu yi wa Allah biyayya ba, har sai sun sanyaka ka zamo alƙali a tsakaninsu cikin abin da suka yi saɓani, sannan kuma ya zama babu wata damuwa a cikin zukatansu cikin hukuncin da ka yi, su kuma yi masa biyayya irinta muminai masu gasgatawa))** **[an- Nisa'i: 65]**, haka ma Allah mai tsarki yana cewa: **((Idan waɗannan munafukai suka ga wani abu na tsaro, ko na tsoro da yake da jiɓi da ƙarfin Musulmai, ko raunin su, sai su yayata shi da nufin ruɗar da Musulmai, ko jefa tsoro da razani a cikin zukatan su, ko saboda su isar da labarin su zuwa ga maƙiyan su, da a ce waɗannan munafukai sun mayar da duk wani al'amari na tsaro da tsoro zuwa ga Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) da shugabanni da manyan saahabbai da dakarun yaƙi, su kuma nemi sanin haƙiƙanin al'amari ta wurin su, da waɗannan da suke ƙoƙarin neman labarai da yaɗa su sun san gaskiya a wurin Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) da shugabanni..))** **[an- Nisa'i: 83]**, haka ma mai girma da ɗaukaka ya gargaɗi masu saɓa wa umurnin Manzonsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) a inda yake cewa: **((Lallai ne masu saɓa umurninsa su kiyaye kada wata fitina, ko azaba mai tsananin raɗaɗi su same su))** **[an- Nur: 63]**.

Lallai Sunnar Annabi mai daraja ta fayyace abubuwa masu yawa da suka zo a dunƙule cikin Alƙur'ani mai girma, umurnin yin sallah, da zakka da suka zo a cikin Alƙur'ani sun zo ne a dunƙule, Allah mai girma yana cewa: **((Ku tsayar da sallah, ku kuma bayar da zakka..))** **[al- Baƙra: 43, 83, 110; an- Nisa'i: 77; an- Nur: 56;**

**al-Muzammil: 20]**, ta yaya za mu tsayar da rukunnan Musulunci a cikin sallah, da zakka, da hajji ba tare da bayani daga Sunna mai tsarki ba? inda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana haka da cewa: **(Ku yi sallah kamar yanda kuka ga ina yin sallah)**, sai ya bayyana yanda ake yin sallah ta hanyar aikinsa, da kuma magaarsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) a inda yake cewa: **(Idan ka tashi yin sallah ka yi kabbara, sannan ka karanta abin da ya sawwaƙa cikin Alƙur'ani, sannan ka yi ruku'i ka natsu a cikin ruku'in, sannan ka ɗago ka daidaita a tsaye, sannan ka yi sujada ka natsu a cikin sujadar, sannan ka ɗago ka natsu a zaune, ka yi haka a dukan sallarka)**, a zakka ma Sunna ce ta fayyaye rassanta, da kuma bayyana nisabin zakka, haka ma hajji, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ku ɗauki ibadun aikin hajjinku daga gare ni)**, lokacin da wani mutum ya zo wurin Sayyiduna Imran Bn Hissain (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce masa: Waɗannan Hadisan da kuke karantawa kuna barin Alƙur'ani fa? Sai ya ce masa: Yaya za ka yi, kai da jama'anka idan kuka zo wurin Alƙur'ani, ta ina za ku san cewa sallar Azuhur raka'o'inta kaza ne, sallar la'asar ma raka'o'inta kaza ne, kuma yaushe ne lokacinta, sallar maghriba ma kaza ne? da tsayuwar Arfa, da jifan jamarat kaza ne..

Haka ma kaman yanda Sunnar Annabi take fayyace abin da ya zo a dunƙule a cikin Alƙur'ani mai girma, haka ma takan taƙaita abin da ya zo da shi a sake, kaman irin yanda ta ƙayyade wasiyya da kashi ɗaya cikin uku (sulusi), kuma ba a wasici ga magaji, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Sa'ad Bn Abiwaƙƙas (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zo gaishe ni a garin Makka da ba ni da lafiya, sai na ce: Ina da dukiya, shin zan iya wasici da dukiya ta gaba

ɗaya? Sai ya ce: **(a'a),** sai na ce: to rabi?, sai ya ce: **(a'a),** sai na ce: to kashi ɗaya cikin uku (sulusi)? Sai ya ce: **(Kashi ɗaya cikin uku, kai ai kuwa kashi ɗaya cikin uku yana da yawa, lallai ka bar magadanka cikin wadata ya fi ka bar su cikin talauci su koma suna roƙon mutane…)**, haka ma Sunnar Annabi ta bayyana cewa ba a yin wasici ga wanda yake da rabo a cikin gado, inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Babu wasici ga magaji)**, haka ma Sunna mai tsarki ta kawo haramcin haɗa mace da 'yar uwan mahaifinta, haka ma haramcin haɗa tsakanin mace da 'yar uwar mahaifiyarta, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ba a aure mace a haɗa ta da 'yar uwar mahaifinta, ko 'yar uwar mahaifiyarta).**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

---------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** A daidai lokacin da muke ƙara tabbatar da matsayi, da darajar Sunna, da kasancewarta hujja a Shari'ar Musulunci, a daidai wannan lokacin ne kuma muke bambance tsakanin Sunnonin Ibada, da kuma ayyukan al'ada da suke sassauyawa da sassauyawar zamunna da wurare, da al'adun mutane, irin waɗanda suke da jiɓi da tufafi, da

hanyoyin sufuri, da sauran abubuwan da suke da dangantaka da al'adun mutane, kowane zamani yana da al'adunsa da suka saɓa da zamanin da suka gabace shi, sam bai yi daidai da hankali a ce mu ɗaura mutane akan wata al'ada ta tafiya, ko sanya tufafi, ko cin abinci da hujjar koyi da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ba, madogarar al'adu suna komawa ne zuwa ga abubuwan da mutane suka saba da su, waɗanda suka yi daidai da zamani, gami da yanayi, matuƙar ba sun saɓa da tabbatattun hukunce – hukuncen da ba sa sauyawa ba ne, lokacin da Imam as- Shafi'iy (Allah ya ƙara masa rahama) ya bayyana rufe kai a cikin abubuwan da suke da jiɓi da mutunci, ya yi la'akari ne da yanayi gami da zamanin da yake ciki, amma a yanzu babu laifi game da hakan; saboda al'ada da yanda mutane suke kallon hakan ya sauya, hakan ba abin ƙyama ba ne a wurin mutane.

Muna kuma ƙara tabbatar da cewa lallai manyan maƙiyan Sunna abubuwa ne guda biyu; na farko: masu kasuwanci da addini, waɗanda suke sauya ma'anoninsa, suke kuma lanƙwaya Nassi ta yanda zai yi daidai da buƙatunsu, su zubar da jini, su kuma rusa abubuwa da sunan addini, suna kuma zaton wai abu mai kyau suke aikatawa, alhalin babu ruwan addini da su, waɗannan su ne masu tsirta da 'yan ba ni na iyan da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi mana gargaɗi akansu a inda yake cewa: **('Yan ba ni na iya sun halaka)**, ya faɗi haka har sau uku, an ruwaito Hadisi da Sayyiduna Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai babban abin da na fi ji wa al'umma ta tsoro shi ne munafuki a zuci, malami a harshe)**.

Na biyu: Waɗanda ba su amfana da hasken ilimi ba, ba kuma su bi hanyarsa ba, lallai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana hatsarinsu a inda yake cewa: **(Lallai Allah ba zai tunɓuke ilimi da ƙarfi daga bayi ba, kawai dai zai karɓi rayukan malamai ne, ta yanda idan babu wani malami da ya yi saura, sai mutane su ɗauki shugabanni jahilai, su tambaye, su kuma su yi masu fatawa ba tare da ilimi ba, su ɓace, su kuma ɓatar)**, Sam babu ruwan Sunna mai girma da duk wani wuce gona da iri da ya kauce ga barin hanyar rangwame, da wasaɗiyyar Musulunci da manhajinsa, da ma wuce gona da irin da yake inkarinta gaba ɗaya, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lokaci ya kusa da za a sami wani daga cikinku da za a kawo masa Hadisi na yana kishingiɗe a karagarsa, ya buɗi baki ya ce: littafin Allah ne kawai yake tsakaninmu da ku, duk abin da muka samu halal ne a cikinsa, za mu halatta shi, duk abin da yake haram ne a cikinsa kawai za mu haramta.. To bari ku ji, lallai duk abin da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya haramta daidai yake da abin da Allah ya haramta..))**.

Lallai wuce gona da iri, da kuma rashin muhimmanta abu; duka karkata ne da ya yi hannun riga da wasaɗiyyar Musulunci da manhajinsa, kuma hakan babban zaluntar Sunnar Annabi ne wadda take tafiya ƙud da ƙud da manufofin Alƙur'ani mai girma, idan mun fahimci manufofinta ne za mu iya isa zuwa ga manyan manufofin addininmu mai girma na bai ɗaya, wanda – babu shakka- gaba ɗayansa adalci ne, duk cikansa rahama, da rangwame, da sauƙi, da mutuntaka ne, lallai ɗaukacin malamai masana -na da na yanzu- sun tabbatar da cewa duk abin da zai tabbatar da waɗannan manyan manufofin yana cikin haƙiƙanin

Musulunci, duk kuma abin da zai ci karo da su, to babu shakka yana cin karo ne da Musulunci gami da manufofinsa.

Daga nan ne malamai masana suke taka rawa wajen daidaita gurɓatattun fahimtar karkatattu da masu wuce gona da iri, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Shi wannan ilimi masu adalci cikin kowane zamani ne suke ɗauke da shi, suna kore masa shigan burtun da maɓarnata suke yi masa, da tawilin da jahilai suke yi, da kuma sauya ma'anarsa da masu wuce gona da iri suke yi)**.

Lallai muna matuƙar buƙatar fahimtar Sunna ƙarƙashin manufofinta, kada mu zamo daskararrun da suke tuƙewa a zahirin Nassoshi kawai, ba tare da fahimtar manufofinsu da inda suka dosa ba, hakan kuwa zai samu ne ta hanyar karanta Sunna a ƙarƙashin manufofinta na zamanin Annabi mai girma, ta yanda za ta yi daidai da ruhin zamani, da kuma sababbin abubuwan da suke faruwa, karatun da zai kusanto da Sunnar Annabi mai girma zuwa ga mutane, wannan shi ne tajdidi wanda Sunna mai tsarki ta yi kira zuwa gare shi, a inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Lallai a duk farko shekaru ɗari Allah yakan tayar da wanda zai jaddada wa wannan al'ummar addininta..)**.

**Ya Allah Ubangiji ka datar da mu da fahimtar littafinka mai girma, da Sunnar Annabinka (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka sanar da mu abin da zai amfane mu, ka kuma amfane mu da abin da ka sanar da mu, ka kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya.**

## - 9 –

## RAYUWAR ANNABI (S.A.W) MISALI NE NA INGANTACCEN MUSULUNCI..

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake **cewa**: **((Lallai kuna da babban abin koyi mai kyau a cikin rayuwar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ga duk wanda yake fatan samun rahamar Allah, ya kuma yi imani da ranar lahira, sannan ya ambaci Allah da yawa))** **[al- Ahzab: 21]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa da waɗanda suka bi tafarkinsa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko manzonsa Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ne, domin ya zamo mai shiryatarwa, kuma mai gargaɗi, ya kuma yi kira zuwa ga Allah da izinin Allah, tabbas shi haske ne mai haskakawa bayi, ya aiko shi ne da saƙonsa na ƙarshe da ya game duk duniya, wanda kuma ya yi daidai da kowane zamani, da kuma kowane wuri, hakan yana nufin dole ne Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zamo babban misali na ingantacciyar karantarwar addinin Musulunci a wajen maganarsa, da

ayyukansa, da dukan al'amurransa, wannan kuwa ba wani abin mamaki ba ne, da ma can (SallalLahu alaiHi wa sallam) manhajin Alƙur'ani mai girma ya riƙe, wajen dangantakarsa da Ubangijinsa, da dangantakarsa da ɗaukacin mutane, duk kuwa da bambancinsu na jinsi, da na launi, da na addini, har hakan ya zamo masa jiki, lokacin da aka tambayi Ummul muminina Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) game da halayen Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), cewa ta yi: **(Ai ɗabi'unsa dukansu Alƙur'ani ne)**.

Duk wanda ya lura da tarihin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), zai ga cewa tabbas shi abin koyi ne a dukan halayensa, da maganganunsa, da ayyukansa, a cikin waɗannan fagage akwai **fagen gaskiya da amanarsa (SallalLahu alaiHi wa sallam):** Lallai (SallalLahu alaiHi wa sallam) mai gaskiya da riƙon amana ne a tsawon rayuwarsa, abin da ya kai har jama'arsa ce suka yi masa suna da mai gaskiya, kuma amintacce **(As- Sadiƙul Amin)**, tun kafin ma Allah ya aiko shi, game da haka ne malam Ahmad Shauƙiy yake cewa:

"Sun yi masa laƙabi da amintacce **"Amin"** tun yana ƙarami, shi kuwa ai dama amintacce ba zai taɓa zama abin tuhuma a maganarsa ba".

Lokacin da Hiriƙla -Sarki Roma- ya kira Abu Sufyan Bn Harb –kafin ya Musulunta- saboda ya tambaye shi akan Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sun yi tattaunawa mai tsawo a tsakaninsu, a cikin tattaunawar Hiriƙla ya ce wa Abu Sufyan: **Shin kuna tuhumarsa da ƙarya kafin ya fara faɗin abin da yake faɗi? Sai Abu Sufyan ya ce: a'a, sai ya ce: Shin yana yaudara? Sai Abu Sufyan ya ce: a'a, amma yanzu akwai wata yarjejeniya a tsakaninmu zuwa wani lokaci, ba**

**mu san mene zai yi a kai ba,** -ma'ana mun ƙulla yarjejeniya ta zaman lafiya, ba mu sani ba, shin zai cika, ko kuwa zai warware ba- sannan ya ce: ban sami wata dama na shigar da wani abu ba banda wannan kalma; ma'ana bai sami wata kafa da zai danganta wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) wani sharri ba sai wannan kalma.

Lallai ɗabi'ar riƙon amana ta fito fili ƙarara a tare da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) a dare hijirarsa mai albarka, inda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya umurci Sayyiduna Aliyu Bn Abuɗalib (Allah ya ƙara yarda da shi), da ya kwana a shimfiɗarsa, har zuwa safe, saboda ya mayar wa mutane da amanonin da suka ajiye a hannunsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), duk kuwa da irin tsantsar ƙiyayyar da suka nuna masa, suka kuma fitar da shi daga garinsa, suka cutar da shi, suka kuma cutar da sahabbansa (Allah ya ƙara yarda da su), suka ƙwace masu dukan abubuwan da suka mallaka; ya yi masu haka ne, saboda sam mumini ba ya ha'intar kowa ba, koda kuwa maƙiyansa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Idan kun ji tsoron cewa waɗanda kuka ƙulla yarjejeniyar zaman lafiya da su suna shirin yin ha'inci su warware yarjejeniyar, to ku nemi a warware yarjejeniyar da take tsakaninku ta hanyar sanar da su haka, lallai Allah ba ya son maha'inta))** **[al-Anfal: 58]**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ka mayar da amana ga wanda ya amince maka, kada ka ha'inci wanda ya ha'ince ka)**.

**Cika alƙawari a wurinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam):** Lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fi kowa cika alƙawari, bai taɓa musanta haƙƙin kowa da yake akansa ba, bai kuma taɓa mantawa da falalar da wani ya taɓa yi masa ba,

hasali ma ya saka wa duk wani da ya taɓa kyautata masa, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) kafin wafatinsa ya ce: **(Babu wani da yake da wata falala akanmu, face mun saka masa, in banda Abubakar, shi kam yana da falala akanmu da Allah ne zai saka masa a ranar alƙiyama)**.

A cikin alamun cika alƙawarinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) akwai dangantakarsa da Ummul muminina Sayyida Khadija (Allah ya ƙara yarda da ita); lallai yana sonta, yana kuma mutunta ta a lokacin da take a raye, da ma bayan wafatinta, a lokacin da (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake bayyana matsayinta cewa ya yi: **(Lallai Allah Maɗaukakin Sarki bai sauya mini ita da wadda ta fi ta alhairi ba, ta fa yi imani da ni a lokacin da mutane suka kafirce da ni, ta kuma saki mini dukiyarta a lokacin da mutane suka haramta mini dukiyarsu, Allah Maɗaukakin Sarki kuma ya azurta ni da 'ya'ya ta wurinta, a daidai lokacin da bai ba ni 'ya'ya daga sauran mata ba)**, Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) tana cewa: **Ban taɓa yin kishi da wata mata cikin matan Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) kaman yanda na yi kishi da Khadija ba, ban fa taɓa ganinta, amma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana yawan maganarta, kai, yakan ma yanka tunkiya, ya yayyanka ta gaɓa- gaɓa, sannan ya aika wa ƙawayen Khadija)**.

Haka ma a cikin abubuwan da suke nuna cika alƙawarinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) tare da waɗanda ba Musulmai ba akwai: maganar da ya yi a ranar yaƙin Badar, yana cewa: **(Da a ce Muƭamu Bn Addiyyu yana raye, ya kuma yi mini magana akan waɗannan fursunonin yaƙin, da kuwa na sake su)**, saboda shi Muƭamu Bn Addiyyu yana da wata falala ne akan

Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), domin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya shiga ƙasƙashin kulawarsa a lokacin da ya dawo tafiyarsa daga al-Ɗa'if.

Haka ma akwai: cika alƙawarin da ya yi wa maƙiyansa har a filin yaƙi, an ruwaito Sayyiduna Huzaifatul Yamaniy (Allah ya ƙara yarda da shi) yana yin bayani game da abin da ya hana shi zuwa yaƙin Badar, yana cewa: Ba wani abu ne ya hana ni zuwa yaƙin Badar ba, sai wata rana ni da mahaifi na mun fito, sai kafiran Ƙuraishawa suka kama mu, sai suka ce: kuna son ku tafi wurin Muhammadu ko? Sai muka ce: ba wurinsa za mu ba, garin Madina kawai muke son zuwa, sai suka sanya muka rantse da Allah akan kawai Madina za mu tafi, ba za mu shiga cikin tawagarsa mu yi yaƙi ba, sai muka zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), muka ba shi labarin abin da ya gudana, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ku tafi, za mu cika masu alƙawarin da muka yi da su, mu kuma nemi taimakon Allah akansu)**.

**Lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) babban abin misali da koyi wajen mu'amalarsa tare da matansa**, tabbas (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya rayu rayuwa mai kyau tare da matansa, inda dukan sifofin soyayya, da na tausayi, da na ƙasƙantar da kai, da na sauƙin kai suka bayyana a ciki, sam (SallalLahu alaiHi wa sallam) bai taɓa nuna wa matansa girman kai ba, bai nuna masu ji-ji da kai ba, hasali ma ya gudanar da mu'amalarsa da su ne cikin kyautatawa ƙarƙashin umurnin Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **((Ku rayu da su cikin kyautatawa..))** **[an- Nisa'i: 19]**, da ma inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((A cikin ayoyinsa ne –mai girma da ɗaukaka- ya halitta maku abokan zamanku daga cikinku, saboda ku sami**

**sukuni da natsuwa a wurinsu, ya kuma sanya soyayya da tausayi a tsakaninku, lallai a cikin wannan abu akwai ayoyi masu yawa ga mutanen da suke tunani))** **[ar- Rum: 21].**

Saboda haka ne (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zamo miji mai tsananin tausayi, da yake mu'amala mai sauƙi tare da matansa, a wani yanayi mai cike da burgewa na nuna mutuntaka da ya nuna tare da matarsa, an ga (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana share hawayen Ummul muminina Sayyida Safiyya (Allah ya ƙara yarda da ita), yana share hawayenta da hannayensa masu albarka, yana kwantar mata da hankali, Sayyiduna Anas Bn Malik (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **(Safiyya ta yi wata tafiya tare da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ranar tata ce, sai na yi jinkiri a tafiyar, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya tarbe ta tana kuka, tana cewa: ya ɗauko ni a taguwa mai nawa, sai kuwa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya hannayensa ya share hawayenta, yana kwantar mata da hankali)**.

**Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) babban abin koyi wajen mu'amalarsa tare da 'ya'yansa da jikokinsa,** wane uba, ko kaka ne matsayinsa ya kai na (SallalLahu alaiHi wa sallam)?!.. Yana ɗauke da dukan ma'anonin soyayya, da jinƙai, da tausayi wa 'ya'yansa da jikokinsa, Ummul muminina Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) tana cewa: **(Ban taɓa gani wani mutum da ya fi kama da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) a wajen shiru, da tausayi, da shiriya kaman Faɗimatu 'yar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ba, ta ce: Idan ta shiga wurin Annabi**

**(SallalLahu alaiHi wa sallam) sai ya miƙe, ya yi haba- haba da ita, ya kuma zaunar da ita a wurin zamansa..)**.

An ruwaito Hadisi daga Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Annabi (Sallallahu alaihi wa sallam) ya sumbaci Al-Hasan Ibn Aliyu (Allah ya ƙara yarda da su), a lokacin al-Aƙra'u Ibn Habis yana wurin, sai al-Aƙra'u ya ce: Tabbas ina da 'ya'ya goma, ban kuma taɓa sumbantar ko ɗaya daga cikinsu ba; sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kalle shi, ya ce: **(Wanda ba ya tausayi, shi ma ba za a ji tausayinsa ba)**. Wata rana (Sallallahu alaihi wa sallam) ya yi sujada, sai ya tsawaita sujadar, bayan ya kammala sallar, sai mutane suka ce: Ya Manzon Allah, ka yi wata irin sujada a sallarka da ba ka taɓa yin irinta ba, shin wani umurni ne aka ba ka? Ko kuwa wahayi ne yake sauka maka? Sai (Sallallahu alaihi wa sallam) ya ce: **(Babu ko ɗaya, ɗana ne ya hau kafaɗa ta, ba kuma na son in gaggauta sauke shi har sai ya gama abin da yake yi)**.

A nan muna son mu tabbatar da cewa: lallai hakan bai taƙaita kawai ga 'ya'yansa, da jikokinsa kawai ba, hakan wani manhaji ne da (Sallallahu alaihi wa sallam) yake mu'amala da ɗaukacin mutane akansa, ba ya bambance wani a tsakaninsu, yana kyautata wa kowa da kowa, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Usama Bn Zaid (Allah ya ƙara yarda da su), daga Annabi (Sallallahu alaihi wa sallam) cewa: yakan ɗauke shi, shi da al-Hassan, yana addu'a cewa: **(Ya Allah Ubangiji, lallai ina sonsu, ina roƙon ka so su)**, ga kuma Sayyiduna Anas Bn Malik (Allah ya ƙara yarda da shi) nan yana cewa: "Shekaru goma na kwashe ina yi wa Manzon (Sallallahu alaihi wa sallam) hidima, bai taɓa cewa da ni tir ba, bai taɓa cewa don me? A wani abu da

na aikata ba, a abubuwan da ban aikata ba kuma bai taɓa ce mini mene ya sanya ka bari ba?”.

**Lallai Annabi (Sallallahu alaihi wa sallam) babban abin buga misali da koyi ne wajen mu’amalarsa da sahabbansa,** yakan yi tarayya da su a cikin halin farin – ciki, da na baƙin-ciki, yakan kuma binciki waɗanda aka ɗauki lokaci ba a gansu ba, yaka kuma duba waɗanda ba su da lafiya, yana damuwa da al’amurransu, yana kuma la’akari da yanda suke ji a cikin dukan al’amurransu, an ruwaito Hadisi daga Simak Bn Harb (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Na ce wa Jabir Bn Samurat (Allah ya ƙara yarda da shi); Shin kukan zauna tare da Manzon Allah (Sallallahu alaihi wa sallam) kuwa? Sai ya ce: ƙwarai kuwa, sau da yawa ma ba ya tashi daga wurin da ya yi sallar Asubahi, har sai rana ta fito, idan ta fito sai ya tashi, sun kasance suna magana da junansu, har su taɓo abubuwan zamanin jahiliyya, su yi dariya, shi kuma (Sallallahu alaihi wa sallam) ya yi murmushi.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-----------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya ʻyan uwa Musulmai:** Kaman yanda Manzon Allah (Sallallahu alaihi wa sallam) ya zamo babban misali wajen gudanar da ingantaccen Musulunci a cikin mutuntakarsa, da ɗabiʼunsa, haka ma shi ɗin babban misali ne wajen daidaitonsa da wasaɗiyyarsa: duk wanda ya yi laʼakari da hukunce – hukuncen Shariʼar da Manzon Allah (Sallallahu alaihi wa sallam) ya yi kira zuwa gare ta, zai ga irin yanda manhajin daidaito da wasaɗiyya yake bayyana a dukan fagagenta, Ummul muminina Sayyida Aʼisha (Allah ya ƙara yarda da ita) tana cewa: **(Ba a taɓa bai wa Manzon Allah (Sallallahu alaihi wa sallam) zaɓi tsakanin wasu abubuwa guda biyu ba, face ya zaɓi wanda ya fi sauƙi a cikinsu, matuƙar ba saɓon Allah ba ne, idan saɓon Allah ne, ya fi kowa nesantarsa)**, Manzon Allah (Sallallahu alaihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai wannan addinin sauƙi ne, babu wanda zai tsananta addini face addinin ya fi ƙarfinsa, ku nemi dacewa a dukan ayyukanku, idan ba ku sami hakan ba, to ku kusanto zuwa ga yin daidai ɗin, ku yi wa junanku albishir, muddin kun kasance a haka, ku kuma nemi saʼa na gabatar da haka tun daga lokacin fitowar rana har zuwa lokacin walha, da bayan sallar Laʼasar zuwa Maghriba, da wani yanki na ƙarshen dare).**

Saboda kiyaye wannan al-wasaɗiyyar, da wannan daidaiton ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi gargaɗi akan duk wani abu da yake kai wa zuwa ga wuce gona da iri, musamman wuce gona da iri a cikin alʼamurran addini, saboda haka ne ya nuna rashin amincewarsa ga wasu daga ckin sahabbansa da suka suka wuce gona da iri a cikin ibada, abin da har ya fitar da su daga iyakar daidaito, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ya ku mutane, ahir ɗinku da wuce gona da iri a**

**cikin al'amurran addini, wuce gona da irin a cikin al'amurran addini shi ne ya halaka wađanda suka gabace ku)**.

Lallai muna matuƙar buƙatar yin koyi da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), da riƙo da shiryatarwarsa, da kuma bibiyan sawunsa wajen yađa saƙon haske, da shiriya tangaras kaman yanda Allah Mađaukakin Sarki ya saukar da shi zuwa ga đaukacin talikai, cikin sauƙi, da tausayi, da jinƙai, da hađin-kai, shi saƙon Musulunci đaukacinsa adalci ne, dukansa tausayi da jinƙai da rangwame ne, kuma amfani ne ga kowa da kowa, da gaba đayansa mutuntaka ne da jinƙai.

**Ya Allah Ubangiji ka azurta mu da soyayyarka, da soyayyar Manzonka (SallalLahu alaiHi wa sallam), da dukan aikin da zai kusanto da mu zuwa ga soyayyarka, ka sanya ƙasarmu cikin aminci da tsaro, da zaman lafiya, da ma sauran ƙasashen duniya baki đaya.**

- 10 –

## SHAIDAR ANNABI GA SAHABBANSA DA FALALARSU:

## DARUSSA DA IZINA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Da na farkon da suka yi gaba cikin mutanen da suka yi hijira daga Makka zuwa Madina, da mutanen da suka tarbe su a garin Madina, da waɗanda suka biyo bayansu cikin kyautatawa, duka Allah ya yarda da su, su ma sun yarda da Allah, Allah kuma ya tanadar masu da gidaje a aljanna da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za kuma su dawwama a cikinsu har abada, lallai wannan shi ne rabo mafi girma))** **[at- Tauba: 100].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai kaman yanda Allah Maɗaukakin Sarki yake zaɓan wanda ya so a cikin bayinsa; domin ya aiko shi da saƙonsa – daidai da irin yanda ya halicce su cikin tsarkin zuciya, da nagartaccen hankali, da karamci na ɗabi'a, da kyawawan ɗabi'u-, haka ma Allah mai girma da ɗaukaka yake zaɓa wa Annabawansa waɗanda suka dace su zamo masu sahabbai,

waɗanda za su bai wa saƙon da suka zo da shi kariya, waɗanda za su tsaya – tsayin – daka wajen isar da wannan saƙon cikin amana, da gaskiya, da sadaukar da kai a bayansu; Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah yana zaɓan Manzanni daga cikin Mala'iku da ma cikin mutane, lallai Allah mai yawan ji da gani ne))** **[al- Hajji: 75]**; saboda haka sahabban Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) suka zamo mafiya tsarkin zukata a cikin wannan al'umma, suka kuma fi kowa ilimi ba tare da yin ƙarfa- ƙarfa ba, wannan kam ba abin mamaki ba ne, domin su mutane ne da Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓe su domin su abokancin Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) wajen kafa addininsa, da kuma isar da shi zuwa ga talikai.

Lallai magana akan sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) magana ce akan zaɓaɓɓu a cikin mutane bayan Annabawa da Manzanni, an ruwaito daga Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) cewa: waɗanda ake nufi da zaɓaɓɓun Allah a inda yake cewa: **((Ka ce: lallai godiya ta tabbata ga Allah, aminci kuma ya tabbata ga bayinsa da ya zaɓa..))** **[an- Namli: 59]** su ne: Sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam). Haka ma an ruwaito daga Abdullahi Bn Mas'ud (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: **"Allah ya duba zukatan bayi, sai ya sami zuciyar Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ita ce mafi alhairin zukata, sai ya zaɓa wa kansa shi, ya aiko shi da saƙonsa, sannan ya sake duba zukatan bayi bayan zuciyar Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya sami zukatan sahabbansa su ne mafiya alhairan zukatan bayi, sai kuwa ya sanya suka zamo mataimaka Annabinsa, suna masu bai wa addininsa kariya, duk abin da Musulmai suka gan shi a matsayin abu mai kyau,**

**to haka yake mai kyau har a wurin Allah, haka ma abin da suka gan shi a matsayin mummuna, to haka yake mummuna har a wurin Allah"**. [Musnad Ahmad].

Lallai duk mai yi wa littafin Allah Maɗaukakin Sarki karatu na lura zai riski girman matsayi, da darajar sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), su ne fa mutanen da Allah Maɗaukakin Sarki ya yarda da su, ya kuma yi masu shaidar gaskiya a cikin imaninsu a inda yake cewa: **((Lallai tabbas Allah ya yarda da muminai a lokacin da suke yi maka mubaya'a da zaɓin kansu a ƙarƙashin bishiya, ya kuma san abin da yake cikin zukatansu na yin abu saboda Allah, da cika alƙawari ga saƙon da ka zo da shi, sai ya saukar masu da natsuwa, saboda kuma gaskiyarsu wajen mubaya'a da cika alƙawarin sulhun ne Allah ya yi gaggawar ɗaukaka darajarsu))** **[al- Fathi: 18]**, malamai masana Tafsiri suka ce: Allah ya san abin da yake cikin zukatansu na haƙuri, da gaskiya, da cika alƙawari, da biyayya, da kuma nagartacciyar basirarsu, da gaskiyar da Allah ya shiryatar da su zuwa gare ta.

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya tsarkake sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) a wurare masu yawa a cikin littafinsa mai girma, Allah mabuwayi yana cewa: **((Su ne waɗanda suka amsa kiran Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) na sake fara jahadi, bayan rauni mai girma da ya same su a yaƙin Uhdu, da suka yi haka sun kyauta, sun kuma ji tsoron saɓa wa umurnin Allah Maɗaukakin Sarki da Manzonsa (SallalLãhu alaiHi wa sallam), saboda haka, sai suka cancanci babban lada a gidan sakamako da ni'ima.. Su ne waɗanda wasu mutane suka tsoratar da su a lokacin da suka ce masu: lallai abokan gabanku sun tanadar maku da**

**wata babban runduna, saboda haka, ku kiyaye su, hakan bai sanya sun yi rauni ba, bai kuma sanya su karaya ba, maimakon haka ma imaninsu da Allah ne ya ƙaru, suka kuma sakankance da nasararsa, sai suka amsa masu da cewa: Allah ya ishe mu, shi ne majiɓincin al'amurran mu, shi kam madalla da wanda ake miƙa masa dukan al'amurra.. Sannan suka fita zuwa jahadi domin su gamu da wannan runduna mai girma, sai dai fa mushrikai sun tsorata da wannan gamuwar, sai muminai suka koma gida cike da nasarar samun ni'imar zaman lafiya, suna kuma kwaɗayin yin jahadi, da kuma babban rabo da suka samu na ladansa, da kuma falalar da ya yi masu na jefa razani cikin zukatan abokan gaba, ta yanda babu ko ƙwarzane da ya same su, suka nemi yardar Allah, sai suka zamo sun cancanci ya ba su falalarsa, lallai Allah mai babban falala ne)) [Ali Imran: 172 – 174]**, haka ma Allah mai girma da buwaya ya bayyana matsayin al-Muhajirun da al-Ansaru da cewa: **((Haka ma ana bai wa talakawa cikin waɗanda suka yi hijira, waɗanda aka raba su da gidajensu da dukiyoyinsu, suke kuma kwaɗayin samun ƙarin arziki daga Allah, gami da yardarsa, suke kuma taimakon Allah da kawunansu da dukiyoyinsu, lallai ana ba su abin da Allah ya bai wa Manzonsa na dukiyoyin mutanen alƙarya, lallai waɗannan su ne muminai.. Su kuwa mutanen da suka sauka garin Madina, suka zamo 'yan gari, suka kuma kyautata imaninsu tun kafin waɗanda suka yi hijira su zo masu, suna son Musulman da suka yi hijira zuwa gare su, ba kuma sa jin ƙyashin komai a cikin zukatansu game da abubuwan da aka bai wa "al-Muhajirun" na ganimar da aka samu ba tare da an yi yaƙi, ko ɗaura ɗammara don yinsa ba (al-Fai'u), suna kuma**

**gabatar da buƙatun waɗanda suka yi hijira akan buƙatun kawunansu, koda kuwa suna tsananin buƙata. Duk wanda aka kiyaye shi –da kiyayewar Allah- daga barin tsananin ƙwauron zuciyarsa, to, lallai su ne suke da babban rabo cikin duk abin da suka so))** **[al- Hashri: 8 -9].**

Kaman yanda ayoyin Alƙur'ani mai girma suka zo suka dawwamar da ambaton Sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yabo gami da jinjina masu kyau, haka ma ingantattun Hadisai sun shaidi girman matsayin da suke da shi a wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), da kuma irin yanda suka sadaukar da kawunansu, da kuma gaskiyar himmarsu, su ne fa waɗanda suka ƙarfafi Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), suka kuma taimaka masa, suka kuma bi hasken da aka saukar masa, suka kuma gabatar da soyayyarsa akan soyayyar kawunansu, da ta iyalansu, da ma ta mutane baki ɗaya, sai kuwa (SallalLahu alaiHi wa sallam) ba su mafi girmar lambar yabo, ya ɗaura masu mafi darajar kambu, inda ya yi masu shaida a matakai masu yawa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Fiyayyun mutane su ne mutanen zamani na, sannan masu biye masu, sannan masu biye masu)** [al-Bukhari da Muslim], haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Taurari aminci da tsaro ne ga sama, idan taurari suka bar sama, sai abin da ake maku alƙawari ya faru, Ni ma aminci ne da tsaro ga sahabbai na, idan babu ni sai abin da aka yi wa sahabbai na alƙawari ya faru, haka ma sahabbai na amince da tsaro ne ga al'umma ta, idan sahabbai na suka tafi sai abin da ake yi wa al'umma ta alƙawari ya faru)** [Muslim], haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ba za ku gushe a cikin alhairi ba matuƙar a cikinku**

**akwai waɗanda suka ganni, suka kuma abokace ni, na rantse da Allah, ba za ku gushe a cikin alhairi ba, matuƙar a cikinku akwai wanda ya ga wanda ya ganni, ya kuma abokaci wanda ya abokace ni, na rantse da Allah, ba za ku gushe a cikin alhairi ba matuƙar a cikinku akwai wanda ya ga wanda ya ga wanda ya ganni, ya kuma abokaci wanda ya abokaci wanda ya abokace ni)** [Musannaf Ibn Abi Shaibah], lallai wannan Hadisin bai fifita waɗanda suka biyo bayansu ba, sai domin darajar zama da sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam).

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya keɓance sahabbansa da yabo, gami da falala akan waɗanda suka zo a bayansu, musamman na farkon da suka riga isa zuwa gare shi daga cikin su, saboda haka ne ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda yafi tausayin al'umma ta a cikin al'umma ta shi ne Abubakar, wanda kuma ya fi ƙarfi wajen bin umurnin Allah shi ne Umar, wanda kuma ya fi gaskiya a wajen kunya shi ne Usman, wanda kuma ya fi iya Shari'a shi ne Aliyu Bn Abuɗalib, aminin cikin al'umma ta kuwa shi ne Abu Ubaidat Bn al- Jarrah, wanda ya fi kowa sanin halal da haram kuwa shi ne Mu'az, wanda ya fi kowa iya karanta Alƙur'ani shi ne Ubayyu, wanda ya fi sanin rabon gado shi ne Zaid)**, haka ma ranar da Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya hau dutsen Uhdu shi da Abubakar da Umar da Usman (Allah ya ƙara yarda da su), sai dutsen Uhdu ya raurawa saboda farin ciki da zuwan Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da sahabbansa, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ya Uhdu ka natsu, ba wasu ne akanka ba sai Annabi da Siddiƙi da Shahidai guda biyu)** [al-Bukhari], haka

ma a wani wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana matsayin Sayyiduna Abubakar da Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da su) da cewa: **(Lallai waɗanda suke daraja ta ƙasa suna hango masu manyan darajoji ne daga samansu, kaman yanda ake hango taurari daga sasannin sararin samaniya, Abubakar da Umar suna cikinsu, kai madallah da su)** [Sunan Ibn Majah].

Lallai (SallalLahu alaiHi wa sallam) a koda yaushe yana kwaɗayin bayyana matsayi, da darajar sahabbansa, inda yake bayyana girmansu domin ya ƙarfafe su, ya kuma ƙara masu himma; saboda su zamo abin koyi ga waninsu a cikin al'umma, a wani wuri sai ka ji (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana magana akan Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) da cewa: **(Kada ku cutar da ni ta hanyar cutar da aboki na, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko ni da shiriya da addinin gaskiya, kuka ce: ƙarya kake, Abubakar ya ce : ka yi gaskiya, ba domin Allah Maɗaukakin Sarki ya kira shi da aboki na ba, da na ɗauke shi a matsayin badaɗi, kawai dai 'yan uwanta ce ta Allah)** [al-Bukhari da waninsa, lafazin na at-Tabaraniy ne], game da Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) kuma ya ce: **(Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya gaskiya a harshen Umaru da zuciyarsa)** [Musnad Ahmad], game da Sayyiduna Usman (Allah ya ƙara yarda da shi) kuwa (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa ya yi: **(Shin ba zan ji kunyar mutumin da Mala'iku suke kunyarsa ba?!)** [Muslim], akan Sayyiduna Aliyu (Allah ya ƙara yarda da shi) kuwa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa ya yi: **(Kai nawa ne, ni ma naka ne)** [al- Bukhari da Muslim].

Lallai mai bibiyan Hadisan Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam) game da sahabbansa, da irin shaidar da ya yi masu zai ga cewa (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya buga babban misali na cika alƙawari, da soyayya ta gaskiya, da kyautata mu'amala ga sahabbansa, da wani irin yanayi da ba a taɓa samun irinsa a tarihin bil'adama ba, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan damu da damuwarsu, yana kuma matuƙar jinƙai a gare su, yana bibiyar lafiyar waɗanda ba sa nan, yana ziyartar marasa lafiyar cikinsu, yana kuma halartar jana'izarsu, yana kuma amsa kiransu, yana kuma yin shawara da su a cikin al'amurra, yana shimfiɗa masu bargon jinƙai da tausayi, yana biya masu bashin da yake kansu, yana kuma yi masu addu'a, su da 'ya'yansu, an ruwaito Hadisi daga Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: **Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya shiga wurin Usman Bn Maz'un (Allah ya ƙara yarda da shi) bayan ya rasu, sai kuwa ya rungume shi, ya sumbance shi, sannan ya yi kuka har sai da aka ga hawaye yana kwarara a fuskarsa.** [Musannaf Abdurrazzaƙ]. Wata rana bayan an kammala wani yaƙi tsakanin Musulmai da mushrikai, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya tambayi sahabbansa waɗanda bai gansu ba, ya ce: **(Shin akwai wanda kuka nema kuka rasa?)**, sai suka ce: Na'am, akwai wane, da wane, da wane, sannan ya sake cewa: **(Shin akwai wanda kuka nema kuka rasa?)**, sai suka ce: Na'am, akwai wane, da wane, da wane, sannan ya sake cewa: **(Shin akwai wanda kuka nema kuka rasa?)**, sai suka ce: a'a, sai ya ce: **(Ni kuwa ban ga Julaibib ba, ku tafi ku nemo inda yake)**, sai aka nemi shi a cikin waɗanda aka kashe, sai kuwa suka same shi a gefen mutane bakwai da ya kashe, kafin a

kashe shi, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zo inda yake ya tsaya, ya ce: **(Ya kashe mutane bakwai, sannan aka kashe shi, wannan kam nawa ne, ni ma nasa ne, wannan kam nawa ne, ni ma nasa ne)**, sannan (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ɗauke shi da damatsansa, babu wani abu da ya katange damatsan Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da jikinsa, har ya sanya shi a kabarinsa. [Muslim]. Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ni ne na fi cancanta da kowane mumini akan kansa, wanda duk ya rasu ya bar dukiya, to na iyalansa ne, wanda kuma ya bar bashi, ko ya bar waɗanda suke ƙarƙashin kulawarsa, to yana wuri na, yana kai na)** [Muslim].

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi wa ɗaukacin al'ummarsa wasici da girmama sahabbansa, ya kuma yi gargaɗin kada a kuskura cutar da su, ko tauye masu haƙƙoƙinsu, ya kuma bayyana cewa: sonsu alama ce ta sonsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), ƙinsu alama ce ta ƙinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), yana cewa: **(Ku kiyayi**

**cutar da sahabbai na, kada ku mayar da su abin jifa da kalaman da ba su dace ba a baya na, duk wanda ya so su, to kuwa lallai da soyayyata ce ya so su, duk kuma wanda ya ƙi su, to da ƙiyayya ta ce ya ƙi su, wanda duk ya cutar da su, ya cutar da ni, duk kuma wanda ya cutar da ni, ya cutar da Allah Maɗaukakin Sarki, wanda kuma ya cutar da Allah, to kuwa yana daf da ya kama shi)** [Ahmad da at-Tirmiziy]. Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Kada ku kuskura ku zagi sahabbai na, da a ce wani daga cikinku zai ciyar da zinaren da ya kai dutsen Uhdu a girma, ba zai taɓa iya kai wa daidai da ɗaya daga cikinsu ba, kai koda rabinsa a daraja)** [al-Bukhari]. Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓe ni, ya kuma zaɓi sahabbai na tare da ni, ya sanya mini wasu daga cikinsu suka zamo mataimaka, da masu tallafawa, da surukai, duk wanda ya zage su, to kuwa lallai la'antar Allah, da ta mala'iku, da ta ɗaukacin mutane ta tabbata akansa, Allah ba zai amshi nafilfili da farillan da ya aikata ba a ranar alƙiyama)**. [al-Mustadrak alas Sahihainiy].

Lallai duk wanda ya karanci tarihin sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) zai fahimci cewa lallai ba su isa zuwa ga wannan babban daraja, da matsayi ba, sai sakamakon ikhlasin da suka yi wa Allah Maɗaukakin Sarki, da kuma soyayya ta gaskiya da suke yi wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), da kuma irin yanda suka yaƙi zukatansu, da taimaka wa gaskiya, gami da ba ta kariya, da fifita maslahar al'umma akan maslahar kai, da kyawawan ɗabi'u, da mu'amalarsu da ɗaukacin mutane, a sakamakon haka, sai suka cancanci samun yabo, da jinjina daga Allah Maɗaukakin Sarki,

suka kuma cancanci soyayya da yarda daga Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa:

"Su kam zaɓaɓɓu ne a cikin mutane, ya kamata ka san darajarsu.. ya kai wanda ya yi katari, ka juri bin turbarsu ta shiriya".

Lallai sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) su ne suka riga kowa kawo sauyi a cikin rayuwa, wajen tarwatsa duhun ɓata, da zalunci, da kama- karya da suka cika duniya kafin aiko Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), suka sauya wannan yanayi da hasken wahayi zuwa ga gaskiya, da adalaci, da daidaito; saboda haka ne son sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zamo sunna, yi masu addu'a kuma hanya ce ta samun kusanci da Allah, koyi da su kuma tsani ne na zuwa wurin Allah, bin tarihin rayuwarsu kuma falala ce, Allah Mai girma da ɗaukaka yana faɗi –bayan ya bayyana sifofin al-Muhajirun da al-Ansaru- cewa: **((Su kuwa muminan da suka zo bayan "al-Muhãjirun" da "al-Ansãr" suna cewa ne: Ya Ubangijinmu ka gafarta mana zunubanmu, mu da 'yan uwanmu da suka riga mu yin imani, kada ka sanya ƙiyayyar waɗanda suka yi imani a cikin zukatanmu. Ya Ubangijinmu lallai kai mai yawan rangwame da rahama ne))** **[al- Hashri: 10]**, al-Imam ar-Raziy (Allah ya ƙara yi masa rahama) ya ce: lallai aikin waɗanda suka zo a bayan al-Muhajirun da al-Ansaru, shi ne: su yi masu addu'a, kuma su nema masu rahama.

A nan muna son mu ƙara ƙarfafa cewa: lallai yawaita magana akan darajar sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), da bayyana falalarsu, abu ne da yake

bayyana rawar da koyi mai kyau yake takawa a rayuwar 'ya'yanmu, da matasanmu, wanda ba za a taɓa iya wadatuwa da shi ba, domin tarbiyya ta hanyar yin koyi tana da matuƙar tasiri wajen dasa kyawawan ɗabi'u masu daraja da ɗaukaka, abu ne da yake kawo gyara a rayuwar zamantakewa, musamman a cikin matasa, da ƙananan yara. Lallai ya kamata matasanmu su yi riƙo da matsakaicin fahimta ta "al-Wasaɗiyya", wanda aka samo shi daga nagartacciyar fahimtar da sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) suka yi wa addinin Musulunci, su kuma yi aiki tuƙuru ta yanda za su ginu akan sifofin Musulunci da za su ba su daman iya ɗaukan alhakin saƙon da Musulunci ya zo da shi, domin su miƙa shi cikin amana, da jagorantar jirgin ruwan tsira, domin tsamar da al'umma daga ruɗu, da rashin tabbas da take ciki, da isar da su zuwa ga tudun- na- tsira, akan nagartacciyar hanya, mai cike da tsaro, da aminci, gami da kwanciyar hankali, da cigaba.

Ina ma mun iya sanin daraja da matsayi irin na sahabban Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), mu kuma yi koyi da ɗabi'unsu kyawawa, mu ɗauki ruhin sadaukar da kai, da baiwa da kyauta, da sadaukar da rayuwa, da dukiya, da 'ya'ya, mu koyi haka daga tarihin rayuwarsu, mu bi turbar da suka bi wajen raya doron ƙasa, da samar da cigaba, da amfanar da bayin Allah, abin da zai bayyana haƙiƙar ma'anar Musulunci da rangwamensa.

**Ya Ubangijinmu ka gafarta mana zunubanmu, mu da 'yan uwanmu da suka riga mu yin imani, kada ka sanya ƙiyayyar waɗanda suka yi imani a cikin zukatanmu.**

## - 11 –

## ƘAYATACCIYAR SURA TA RAYUWAR SAHABBAI..

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Da na farkon da suka yi gaba cikin mutanen da suka yi hijira daga Makka zuwa Madina, da mutanen da suka tarbe su a garin Madina, da waɗanda suka biyo bayansu cikin kyautatawa, duka Allah ya yarda da su, su ma sun yarda da Allah, Allah kuma ya tanadar masu da gidaje a aljanna da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, za kuma su dawwama a cikinsu har abada, lallai wannan shi ne rabo mafi girma))** **[at- Tauba: 100]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa da waɗanda suka bi tafarkinsa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓi Annabawansa da Manzanninsa masu tsarki daga cikin halittunsa, Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Allah yana zaɓan Manzanni daga cikin Mala'iku da ma cikin mutane, lallai Allah mai yawan ji da gani ne))** **[al- Hajji: 75]**, Haka ma mai girma da ɗaukaka ya zaɓa wa Manzanninsa mataimakan da za su agaza masu wajen isar da saƙon Ubangijinsu, babu shakka Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓa wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) wasu tsarkakan mutane, zaɓaɓɓun abokai, da suka yi

imani da shi, suka kuma ƙarfafa masa gwiwa, suka kuma taimaka masa, suka bi hasken da aka saukar masa, Sayyiduna Abdullahi Bn Mas'ud (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **"Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya duba zukatan bayi, sai ya zaɓi Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam), ya aiko shi da saƙonsa, ya kuma zaɓe shi da iliminsa, sannan ya duba zukatan sauran mutane bayansa, sai ya zaɓa masa sahabbansa, ya sanya suka zamo masu taimaka wa addininsa, waziran Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), duk abin da muminai suka ganshi a matsayin abu mai kyau, to mai kyau ne har ga Allah, duk kuma abin da muminai suka ganshi a matsayin mai muni, to mai muni ne har ga Allah"**..

Sai sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) suka zamo mafiya gaskiyar imani, da yawan ilimi, da fahimta, da kyautata aiki, sun ɗaga tutar addini zuwa ko'ina a bayan ƙasa, cikin hikima da kyakkyawan wa'azi, suka kuma isar da saƙonnin Ubangijinsu kaman yanda ya kamata, da haka sai suka cancanci su zamo zaɓin da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), an ruwaito daga Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) yana sharhi akan maganar Allah da take cewa: **((Ka ce: godiya ta tabbata ga Allah, amince kuma ta tabbata ga bayinsa da ya zaɓe su..))** **[an-Namli: 59]** cewa: su ne sahabban Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam), Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓa wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) su, su ne waɗanda suka kwankwaɗin manhajin Musulunci daga tsarkakakkiyar maɓuɓɓugarsa ta asali, ba kuma su kauce wa miƙaƙƙiyar hanyarsa ba..

Lallai rayuwarsu cike take da shafuka masu matuƙar yawa, da suke nuna yanda haƙiƙanin Musulunci yake a aikace, a cikin waɗannan shafuka akwai: **na tausayi da rahama**, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya dasa ɗabi'ar rahama da tausayi a cikin zukatan sahabbansa, a cikin alamun haka akwai wata rana da Sayyiduna Uyaina Bn Hisn ya ga Sayyiduna Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ɗora ɗaya daga cikin 'ya'yansa akan cinyarsa, yana sumbantarsa, sai Uyaina ya ce: kana Amirul muminina kuma, kana sumbatar yaro?! Da a ce ni ne Amirul muminina da babu yaron da zan sumbanta, sai Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: **To yaya na iya idan har Allah ya zare rahama daga cikin zuciyarka?! Lallai Allah yana tausayin masu tausayi ne a cikin bayinsa kawai**, wannan mataki da Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ɗauka, koyi ne ya yi da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) a abin da ya gudana tsakaninsa da al- Aƙra'u Bn Habis; lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sumbaci Sayyiduna al- Hassan Bn Aliyu (Allah ya ƙara yarda da su) a gabansa, sai al- Aƙra'u ya ce:. : Tabbas ina da 'ya'ya goma, ban kuma taɓa sumbantar ko ɗaya daga cikinsu ba; sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kalle shi, ya ce: **((Wanda ba ya tausayi, shi ma ba za a ji tausayinsa ba)).**

Haka ma Sahabban Manzon Allah (Allah ya ƙara yarda da su) abin koyi ne **wajen yafiya da rangwame,** mafi girma da darajar abin da zai bayyana haka shi ne abin da ya faru da Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) wajen yafiya da ya nuna wa Musɗah Bn Asasat, lallai Sayyiduna as- Siddiƙ (Allah ya ƙara yarda da shi) yana ciyar da shi saboda kusancin da yake da shi da shi, da kuma zamowarsa talaka, shi Musɗah

yana cikin waɗanda suka saki bakinsu akan Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita), lokacin da Allah ya wanke ta, sai Sayyiduna Abubakar ya yi nufin daina ciyar da Musɗah, sai Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar da ayar: **((Kada mutanen kirki, masu dukiya a cikinku su rantse akan hana kyautatawarsu ga waɗanda suka cancanta cikin 'yan uwa makusanta, da miskinai, da waɗanda suka yi hijira saboda Allah, da sauransu ta kowane irin dalili da ya shafe su, kaman idan sun yi masu ba daidai ba, kamata ya yi su yafe masu, su kawar da kai ga barin mayar masu da martani, idan dai har kuna son Allah ya yafe kura-kurenku, da munanan ayyukanku, to ku ma ku aikata abin da kuke son Ubangijinku ya yi maku ga waɗanda suka munana maku, ku ladabtu da ladubbansa, shi dai kam mai yawan gafara da rahama ne)) [an- Nur: 22],** sai as- Siddiƙ (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Ina so, wallahi na fi kowa son Allah ya gafarta mini, sai ya dawo ya cigaba da ciyar da Musɗah, yana mai cewa: wallahi ba zan taɓa hana ka ba har abada.

Haka ma akwai: **himma mai girma da kuma rige - rige wajen aikata ayyukan alhairi**, lallai sahabbai sun koyi zage dantse wajen himma, da rige -rige wajen ayyukan alhairi, da neman manyan matsayi na ƙololuwa a cikin komai ne daga Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), da ma can (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan za ku roƙi Allah, to ku roƙe shi al-Firdausi, ita ce matsakaiciyar aljanna, maɗaukakiyar aljanna kuma -ina gani- tana saman al- Arshin Mai yawan rahama, daga cikinta ne ƙoramun aljanna suke ɓuɓɓugowa)**, wannan ne ya sanya sahabbai masu daraja a koda yaushe suke rajin ganin kansu a manyan matsayi a cikin komai, Sayyiduna

Umar Bn al- Khadɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **(Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya umurce mu da mu yi sadaka, wannan ya zo ne a daidai lokacin da akwai wani kuɗi a tare da ni, sai na ce: yau kam zan zarce Abubakar, ya zamo na taɓa wuce shi a wata rana kenan, sai na kawo rabin dukiya ta, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: (Mene ka bar wa iyalanka?), sai na ce: kwatankwacin wannan, ya ce: sai Abubakar ya kawo duk abin da yake mallaka, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce masa: (Mene ka bari wa iyalanka?), sai ya ce: Na bar masu Allah da Manzonsa, sai na ce: ba kuwa zan sake yin gasa da kai ba har abada).**

Ga kuma sahabin nan mai girma Ka'ab Bn al- Aslamiy (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **Na kwana tare da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai na kawo masa ruwan alwalla da na biyan buƙatarsa, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce mini: (Tambayi abin da kake so), sai na ce: zama tare da kai a aljanna, sai ya ce: (Babu wani abin kuma?), sai na ce: wannan ne kawai, sai ya ce: (Ka taimaka mini akan kanka da yawan sujada)**.

Haka ma a cikin waɗannan surori masu ƙayatarwa akwai: **fifita wani akan kai, da kuma kamewa da yakana,** lallai mutanen Madina sun buga babban misali a fagen fifita wani akan kai, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: **wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce: ya Manzon Allah, ina cikin wani hali, sai ya aika wajen matansa, ba a sami komai daga wurinsu ba, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: (Wane zai amshi baƙwancinsa na**

**wannan daren, Allah kuma ya yi masa rahama?), sai wani mutum cikin mutanen Madina ya tashi, ya ce: ni ne, ya Manzon Allah, sai ya tafi wurin iyalinsa, ya ce wa matarsa: wannan baƙon Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ne, kada ki adana komai ga barinsa, sai ta ce: na rantse da Allah babu komai sai abincin yara, sai ya ce: idan yaran suna son su ci abincin dare, to ki lallaɓa su, har su yi barci, ki zo, ki kashe fitila, mu ɗaɗɗaure cikinmu a wannan daren, sai kuwa ta yi haka, sai da safe mutumin ya tafi wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: (Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya ji daɗi -ko ya yi murmushi- akan abin da wane da wance suka yi), sai Allah mai girma ya saukar da ayar: ((Suna fifita buƙatun wasu akan buƙatun kansu, koda kuwa suna cikin matsananciyar buƙata..)) [al- Hashri: 9].**

Haka ma a cikin wani yanayi mai ƙayatarwa da ya haɗe tsakanin ɗabi'un fifita wani akan kai na mutanen Madina "al-Asar (Allah ya ƙara yarda da su), da kuma ɗabi'ar kamewa da yakana na waɗanda suka yi hijira (Allah ya ƙara yarda da su), inda Sayyiduna Sa'ad Bn ar-Rabi' (Allah ya ƙara yarda da shi) ya yi wa Sayyiduna Abdurrahman Bn Auf (Allah ya ƙara yarda da shi) tayin zai raba dukiyarsa ya ba shi rabi, sai kuwa Sayyiduna Abdurrahman (Allah ya ƙara yarda da shi) ya nuna kamewa da yakana, ya ce: kawai nemi da ya nuna masa kasuwa, ya tafi ya yi iya yinsa wajen kasuwanci, har sai da ya zamo cikin waɗanɗa suka fi wadata a cikin masu halin garin Madina.

Haka ma akwai: **ɗabi'ar dawo wa gaskiya idan ta bayyana**, lallai sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) mutane ne masu

neman gaskiya, ba sa nuna girman kai wajen dawowa zuwa ga gaakiya, an ruwaito Hadisi daga Abu Mas'ud al- Ansariy (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: **wata rana ina dukan wani bawa na, sai na ji wata murya ta baya na ta cewa: (Ka sani, ya Abu Mas'ud, ikon da Allah yake da shi akanka, ya fi wanda kake da shi akansa), sai na waiga, sai na ga Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ne, sai na ce: Ya Manzon Allah, na 'yanta shi saboda Allah, sai ya ce: (Da a ce ba ka yi hakan ba, da kuwa wuta ta ci ka), ko (da wuta ta shafe ka)**.

Haka ma akwai: **cika alƙawari,** lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya dasa ƙimar cika alƙawari a cikin zukatan sahabbansa, ya kwaɗaitar da su wajibcin cika shi, ga Sayyiduna Mu'awiyya Bn Abu Sufyan (Allah ya ƙara yarda da su) nan a aikace; akwai yarjejeniya tsakaninsa da Romawa, sai Mu'awiyya (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ƙuduri aniyar zuwa kusa da ƙasar Romawa, ta yanda da zaran ranar da ƙarshen wannan yarjejeniya za ta zo, shi kuma ya faɗa masu ba tare da sun sani ba, sai wani daga cikin sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi sauri ya riske shi yana cewa: Allahu akbar, Allahu akbar, a dai cika alƙawari, kada a yi yaudara, da aka duba a ga wane ne yake wannan maganar, sai aka ga Sayyiduna Amru Bn Abasat (Allah ya ƙara yarda da shi) ne, sai Mu'awiyya (Allah ya ƙara yarda da shi) ya aika aka kira shi, ya tambaye shi, sai ya ce: na ji Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda yake da wata yarjejeniya ta aminci da tsaro tsakaninsa da wasu mutane, kada ya tsananta, kada kuma ya warware ta har sai lokacinta ya ƙare, ko kuma ya sanar da su cewa ya dakatar da yarjejeniyar)**, sai

Sayyiduna Mu'awiyya (Allah ya ƙara yarda da shi) ya dawo daga rakiyar shirinsa na farko.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai sahabban Manzon Allah (Allah ya ƙara yarda da su) abin koyi ne mai kyau na raya duniya ta hanyar addini, kowanne daga cikinsu yana da aikin da yake gabatarwa, ya kuma kyautata shi, kana ya ƙware a cikinsa, a cikinsu akwai ɗan kasuwa, akwai jagora, akwai kuma malamai masana, da sauransu, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda yafi tausayin al'umma ta a cikin al'umma ta shi ne Abubakar, wanda kuma ya fi ƙarfi wajen bin umurnin Allah shi ne Umar, wanda kuma ya fi gaskiya a wajen kunya shi ne Usman, wanda ya fi kowa sanin halal da haram kuwa shi ne Mu'az, wanda ya fi kowa iya karanta Alƙur'ani shi ne Ubayyu, wanda ya fi sanin rabon gado shi ne Zaid Bn Sabit, kowace al'umma tana da amini, aminin cikin wannan al'umma shi ne Abu Ubaidat Bn al-Jarrah)**.

Lallai ayyukan sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) suna da tasiri mai kyau da suka bari, kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana ƙarfafa masu gwiwa, yana kiran kowa daga cikinsu da abin da ya ƙware akansa, saboda girmama shi, da kuma girmama ilimin da yake da shi a fagen, a irin wannan ne lokacin da Sayyiduna Usman Bn Affan (Allah ya ƙara yarda da shi) ya shiga wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) a ranar yaƙin Tabuka, yana ɗauke da Dinare dubu, ya zuba su a gaban Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk abin da Usman ya aikata bayan wannan ba zai cutar da shi ba har abada)**.

Haka ma akwai: **Bincike da neman halal, da hararo Allah Maɗaukakin Sarki a cikin dukan al'amurra,** a cikin irin wannan akwai abin da ya faru da Sayyiduna Jarir Bn Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da shi); inda ya umurci hadiminsa da ya sayo masa doki, sai kuwa ya sayo masa akan kuɗi Dirhami ɗari uku, ya zo wurinsa da mai sayarwar saboda a ba shi kuɗin, sai Jarir ya ce wa mai dokin: dokinka ya wuce Dirhami ɗari uku, shin za ka sayar mini akan Dirhami ɗari huɗu? Sai ya ce: wannan kuma yanda ka gani, sai ya ce: dokinka ya wuce Dirhami ɗari huɗu, shin za ka sayar mini Dirhami ɗari biyar? Haka ya yi ta ƙara masa Dirhami ɗari - ɗari, har sai ya kai Dirhami ɗari takwas, ya kuwa saya a haka, sai aka yi masa magana akan haka, sai ya ce: Lallai na yi wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) mubaya'a akan yin nasiha ga ɗaukacin Musulmi).

Kowanne daga cikinsu ya san haƙƙinsa, ya kuma sauke shi, bai ƙetare haƙƙinsa ba, akan haka ne lokacin da Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya naɗa Sayyiduna

Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ƙara yarda da shi) alƙalanci, Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya kwashe shekara ɗaya cur, ba tare da wani ya shirga da ƙara a wurinsa ba, a lokacin sai ya nemi Sayyiduna Abubakar as - Siddiƙ (Allah ya ƙara yarda da shi) da ya amince ya sauke shi daga alƙalancin, sai ya ce masa: wahalhalun alƙalanci ne suka sanya kake neman a sauke ka ya Umar?, Sai Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: ba haka ba ne ya Halifan Manzon Allah, kawai dai muminai ba su da wata buƙata daga gare ni, kowa daga cikinsu ya san haƙƙinsa, bai nemi sama da hakan ba, ya kuma san haƙƙin da yake akansa, bai yi nawa wajen sauke shi ba, kowa daga cikinsu yana so wa ɗan uwansa abin da yake so wa kansa, idan ba su ga ɗaya daga cikinsu ba, suna zuwa su san yanayin da yake ciki, idan ya yi rashin lafiya sukan gaishe shi, idan talauci ya kama shi, sukan taimake shi, idan ya nemi wata buƙata sukan taimaka masa, idan wata damuwa ta same shi, sukan yi masa jaje, da Allah ya kyauta, addininsu nasiha ne, ɗabi'unsu kuma su ne: bayar da umurni da ayyuka masu kyau, da hana aikata munana, tun da kuwa haka ne, mene zai sanya su yi husuma? tun da kuwa haka ne, mene zai sanya su yi husuma?.

Lallai muna matuƙar buƙatar komawa zuwa kyawawan ɗabi'un waɗannan nagartattun abin koyi cikin sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), mu ɗabi'antu da ɗabi'unsu, saboda mu bayyana haƙiƙanin surar addinin Musulunci, addinin rahama da rangwame da mutuntaka, da zaman lafiya ga ɗaukacin bil'adama.

**Ya Allah Ubangiji ka kare mana ƙasarmu, da al'ummar ƙasar, da sojojinmu da 'yan sandanmu, ka haɓaka tattalin arzikin ƙasarmu da na sauran ƙasashe baki ɗaya.**

## - 12 –

## MUSULUNCI AIKI NE DA ƊABI'A: MISALAI DAGA RAYUWAR TABI'AI..

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Su kuwa muminan da suka zo bayan "al-Muhãjirun" da "al-Ansãr" suna cewa ne: Ya Ubangijinmu ka gafarta mana zunubanmu, mu da 'yan uwanmu da suka riga mu yin imani, kada ka sanya ƙiyayyar waɗanda suka yi imani a cikin zukatanmu. Ya Ubangijinmu lallai kai mai yawan rangwame da rahama ne)) [al- Hashri: 10]..** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa da waɗanda suka bi tafarkinsa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah mai girma da ɗaukaka yana zaɓan wasu daga cikin bayinsa, da za su yi wa addininsa aiki, su kuma tsarkake niyya a gare shi, da saƙon da ya aiko, game da haka ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayar da labarin cewa; zaɓaɓɓun cikin wannan al'umma su ne sahabbansa (Allah ya ƙara yarda da su), sannan tabi'ai masu biye masu, sannan tabi'uttabi'ina, wato waɗanda suka biyo bayan waɗanda suka biyo bayan sahabbai, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna

Abdullahi Bn Mas'ud (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Fiyayyun mutane su ne na zamani na, sannan waɗanda suke biye masu, sannan waɗanda suke biye masu..),** waɗannan su ne zaɓaɓɓun da aka sifanta su da alhairi, suka kuma ɗauki amanar ilimi, suke kore masa ƙarairayin masu wuce gona da iri, da ƙirƙirar mutanen - kawai, da tawilin jahilai, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya yabe su gaba ɗayansu, inda ya haɗa su tare da sahabban Manzon Allah (Allah ya ƙara yarda da su), ya kuma sifanta su da kyautatawa, ya kuma yarda da su, ya kuma yi masu alƙawarin gidajen aljannar da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Da waɗanda suke akan gaba na farko- fako, cikin waɗanda suka yi hijira, da waɗanda suka tarbe su, da ma waɗanda suka biyo turba irin tasu da kyautatawa, duka Allah ya yarda da su, su ma sun yarda da Allah, kuma Allah ya tanadar masu da aljannar da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinta, za su dawwama a cikinta har abada, kai lallai wannan babban rabo ne mai matuƙar girma)) [at- Tauba: 100].**

Tabi'ai su ne mutanen da suka fi kusa da zamanin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), lallai tabi'ai su ne al'ummar da suka zo bayan sahabbai, su kuma tabi'uttabi'ina su ne al'ummar da suka zo bayan tabi'ai (Allah ya ƙara yarda da su baki ɗaya). Alhairin Allah ya kai zuwa ga Imam al- Busairiy a inda yake cewa:

"Dukansu sun ɗosano ne daga Manzon Allah, ko dai tamkar kamfata ɗaya daga cikin kogi, ko kuma ɗan yayyafi daga mamako.."

Lallai tabi'ai sun abokanci sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su), sun yi karatu a gabansu, haka ma sahabban (Allah ya ƙara yarda da su) sun yi masu shaida a **fagen falala da ilimi;** ga Sayyiduna Abdullahi Bn Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) nan yana shaida akan Sayyiduna Sa'id Bn al- Musayyib (Allah ya ƙara yarda da shi) da cewa: **"Na rantse da Allah shi ɗin ɗaya ne daga cikin masu bayar da fatawa"**, sau da yawa yakan ce : **"Ku tambayi Sa'id Bn al- Musayyib; lallai ya zauna da salihan bayin Allah"**, Sayyiduna Sa'id Bn al- Musayyib ( Allah ya ƙara masa rahama) yakan bayar da fatawa a lokacin da akwai sahabbai a raye. Haka ma Sayyiduna Aɗa'u Bn Abu Rabah yana zama a majalisin bayar da fatawa a Makka bayan wafatin "Habarul Ummati", Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su), lokacin da Sayyiduna Abdullahi Bn Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya zo garin Makka, sai aka yi masa tambaya, sai ya ce: **"Haba mutanen Makka, yanzu za ku tattaro mini tambayoyi ne, alhali Ibn Abu Rabah yana cikinku?"**.

Lallai an san Tabi'ai da gaskiya **wajen soyayyarsu da Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam)**, a duk sanda Imam al-Hassan al-Basriy (Allah ya ƙara masa rahama) yake bayani akan "Hadisin Kututture", da irin yanda ya nuna begensa ga Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya fashe da kuka, yana mai cewa: **"Ya ku bayin Allah, katako ne fa yake begen Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ku ne kuka fi cancanta da haka, ku ne ya kamata ku yi shauƙin haɗuwa da shi"**, an tambayi Imam Malik (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa: yaushe ka taɓa jin karatu daga Ayyub al-Sakhtiyaniy? Sai ya ce: ya yi Hajji sau biyu, na kasance ina

hangensa da idona daga nesa, ba tare da na ji abin da yake faɗi ba, amma a duk sanda aka ambaci Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya fashe da kuka, har sai na ji tausayinsa ya kama ni.. Girmamawar da suke yi wa Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ta kai ga ba sa iya karanta Hadisinsa ba tare da suna cikin mafi kyawon kama, da yanayi ba, sun tarbiyyantar da masu bi masu akan haka, Abu Salamat al-Khuza'iy (Allah ya yi masa rahama) ya ce: A duk sanda Imam Malik Bn Anas zai fito domin bayar da karatu akan Hadisi yakan yi alwalla irin ta mai sallah, sannan ya sanya mafi kyawon tufafinsa, ya tsefe gemensa, da aka yi masa magana akan haka, sai ya ce: Da haka ina girmama Hadisin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ne.

A cikin Tabi'ai da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ambace su da alhairi akwai: **Uwaisu al-Ƙaraniy,** wanda yake tsananin yi wa mahaifiyarsa biyayya, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi wa sahabbansa magana akansa, ya ba su labarin cewa tabbas Allah yana amsar addu'arsa, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Umar Bn al-Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce; Na ji Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai a cikin mutanen da suka fi alhairi a cikin Tabi'ai akwai wanda ake kira da suna : Uwaisu, yana da mahaifiya, yana kuma da cutar Baras, ku nemi ya nema maku gafara)**, lokacin da tawagar ƙasar Yaman suka zo, Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) haka ya bazama cikinsu yana nemansa, har sai da suka haɗu, sai ya ce masa; ka nema mini gafara, sai ya ce: wane ne ni, kai ne ka fi cancanta ka nema mini gafara, kai fa sahabin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ne, bai dai gushe ba har sai da ya nema masa gafara.

Lallai Tabi'ai (Allah ya yi masu rahama) **sun koyi kyakkyawar fahimtar addini ne** daga sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ga Imam al- Hassan al- Basriy nan (Allah ya ƙara yarda da shi) –wanda ɗaya ne daga cikin manyan Tabi'ai- lokacin da aka tambaye shi da cewa: shin kai mumini ne? sai ya ce: "Imani kashi biyu ne; idan kana tambaya ta akan imani da samuwar Allah, da imani da mala'ikunsa, da litattafan da ya saukar, da Manzanninsa da aljanna da tashin bayan mutuwa da hisabi, babu shakka ni mumini ne, amma idan kana tambaya ta akan maganar da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Muminai su ne waɗanda idan aka ambaci Allah, sai zukatansu raurawa, idan kuma aka karanta masu ayoyinsa, sai karatun ya yi sanadiyya ƙaruwar imaninsu, su a koda yaushe suna dogara da Ubangijinsu ne. Su ne waɗanda suke tsayar da sallah, suke kuma ciyar da wani sashe na abin da muka azurta shi da shi a hanyar ɗaukaka addinin Allah. Waɗannan kam su ne muminai na gaskiya, suna da muƙamai masu daraja a wurin Ubangijinsu, da yafe zunubai, da kuma arziki mai girma))** **[al- Anfal: 2 – 4]**, to wallahi ban sani ba shin ina cikinsu, ko kuwa a'a, Imam al- Baihaƙiy ya yi ta'aliƙi akan haka da cewa: Imam al- Hassan bai tsaya kawai akan asalin imani ba, ya hararo kamalar imani ne, wanda saboda shi ne Allah ya yi wa masu shi alƙawari da gidan aljanna a inda yake cewa: **((Suna da muƙamai masu daraja a wurin Ubangijinsu, da yafe zunubai, da kuma arziki mai girma)) [al- Anfal: 4].**

Haka ma sun fahimci **sauƙi na addini, sun kuma aiwatar da shi a cikin rayuwarsu,** Imam Sufyan as- Sauriy yana cewa: Ilimi a wurinmu shi ne samun sauƙi daga wanda ya yarda da kansa, shi kuwa tsanantawa ai kowa ma ya iya. Haka ma al-

Azraƙ Bn Ƙais ya ce: wata rana muna gaɓar kogi a garin al-Ahwaz, ruwan cikin kogin ya ƙafe, sai Abu Burzat al- Aslamiy ya zo akan goɗiya, ya bar goɗiyar tasa ya kama sallah, sai goɗiyar ta gudu, shi ma sai ya sallame sallar, ya bi ta ya kamo abinsa, sannan ya dawo ya biya sallarsa, a cikinmu akwai wani mutum, sai ya fara cewa: ku fa kalli wannan dattijon, ya bar sallarsa saboda goɗiya! Sai ya waigo, ya ce: Tun sanda na rabu da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ban sami wanda ya ƙyare ni haka ba, sannan ya ce: Gida na yana da nisa, da na yi sallar na rabu da goɗiyar, ba zan iya komawa gida ba sai cikin dare. Lallai sun koyi haka ne daga Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), wanda ba a taɓa ba shi zaɓi tsakanin abubuwa guda biyu ba, face ya zaɓi mafi sauƙinsu, matuƙar ba saɓon Allah ba ne, shi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ne da kansa yake cewa: **(Ku sauƙaƙa, kada ku tsananta, ku yi albishir kada ku kure mutane)**, a wani wuri kuma yana cewa: **(Lallai sauƙi bai taɓa shiga cikin wani abu ba, face ya ƙawata shi, ba kuma a taɓa cire shi daga kowane irin abu ba, face ya aibata shi)**.

Haka ma sun aiwatar da ɗabi’un **tausayi da taimako da damuwa da damuwar wasu a cikin rayuwarsu**, alal misali ga Sayyiduna Aliyu Bn al-Hussain Bn Aliyu (Allah ya ƙara yarda da su) nan da yake ɗaukan nauyin talakawa masu yawa a asirce, ba tare da wani ya sani ba, lokacin da ya yi wafati ne suka rasa wanda zai ɗauki nauyinsu, da aka zo yi masa wanka ne aka ga bayansa cike da tabbai na ɗaukan buhunhunan da yake yi yana kai wa gidajen matan da suka rasa mazaje, da miskinai, ta nan ne suka gane cewa shi ne yake kawo masu abin

da suke buƙata cikin dare, an ce: a garin Madina yana ɗauke da nauyin gidaje ɗari.

Wannan tausayi gami da taimakon ba su tsaya kawai akan Musulmai ba, sai da hakan ya haɗe Musulmai da waɗanda ba Musulmai ba, ga Sayyiduna Umar Bn Abdul'aziz nan (Allah ya ƙara yarda da shi) ya rubuta wasiƙa zuwa ga gwamnansa na garin Basra cewa: **"Ka duba waɗanda shekarunsu suka ja, suke kuma da rauni, ba kuma su da abin hannu a cikin Ahluz Zimma ka ba su abin da zai kyautata masu rayuwa daga Baitul malin Musulmai"**, a nan ma ya yi koyi ne da Sayyiduna Umar Bn al-Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi), lokacin da ya ga wani mutum mai yawan shekaru cikin Ahlul kitabi yana roƙon mutane, sai ya ce: **"Wallahi ba mu yi wa wannan adalci ba, in mun amfana da ƙuruciyarsa, muka kuma yi watsi da shi a lokacin tsofarsa**", sannan ya sanya masa albashi na abubuwan da za su ishe shi daga Baitul maili. Ga ma Sayyiduna Khalid Bn al- Walid nan (Allah ya ƙara yarda da shi) a lokacin sulhun da ya yi da mutane garin "al-Hiyarat" ya rubuta cewa: **"Na sanya duk wani tsoho da ba zai iya yin aiki ba, ko wani bala'i ya faɗa masa, ko yana da wadata amma ya karayar arziki ya same shi, to a ɗauki nauyinsu daga Baitul malin Musulmai"**, dukansu a nan suna koyi ne da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sun kuma aiwatar da nagartacciyar fahimtar addini, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah ba ya hana ku girmama da sada zumuntanku da kãfiran da ba su yaƙe ku ba, ba kuma su fitar da ku daga gidajenku ba, lallai Allah yana son masu kyautatawa da kuma sada zumunta)) [al- Mumtahanat: 8].**

Lallai wannan tausayin bai taƙaita da mutane kawai ba, sai da ya haɗa da dabbobi da tsuntsaye da sauransu, Sayyiduna Umar Bn Abdul'aziz (Allah ya ƙara yarda da shi) ya rubuta wasiƙa zuwa ga gwamnansa na Misra yana masa wasiyya da tausayawa raƙuma, yana cewa: **Na sami labarin akwai wasu masu ɗaukan kaya a Misra da suke ɗaura wa raƙuma riɗili dubu, to idan wannan wasiƙar ta sadu da kai, kada a sake ɗaura wa raƙumi sama da riɗili ɗari shida**.

Haka ma ya yi wasici da kada a wulaƙanta su, kada kuma a doke su, duka wannan koyi ne da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam): lokacin da ya yi wa wani mai raƙumi wasici da raƙuminsa da cewa: **(Shin ba za ka ji tsoron Allah game da sha'anin wannan dabba da Allah ya huwace maka ita ba?!, ya kawo ƙarar kana azabtar da shi, kana kuma ƙasƙantar da shi)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

--------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai a cikin manyan sifofin da suka bambanta Tabi'ai da saura akwai: **yafiya da rangwame ga mutane, gami da sauƙin kai,** suna cikin waɗanda suka fi yawaita rangwame da sauƙin kai a wajen mu'amalarsu da

mutane, an ruwaito Sayyiduna Ƙatada yana cewa: mun shiga wurin Imam al-Hassan al- Basriy, lokacin yana barci, a kusa da kansa akwai wani kwando da akwai gurasa, da kayan marmari, sai kawai muka fara ci, sai ya farka ya ganmu, hakan sai ya sanya shi farin ciki, yana murmushi, yana karanta maganar Allah da take cewa: **((.. ko abokinku, lallai ba ku da wani laifi..))** **[an- Nur: 61]**. An ruwaito daga Jabir Bn Hazim (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce:  wata rana muna wurin Imam al-Hassan da tsakiyar rana, sai ɗansa ya ce: ku ɗan sauƙaƙa wa Shaihi mana, lallai kun ƙuntata masa, bai ko ci abinci da abin sha ba, sai ya ce: ka ƙyale su, Na rantse da Allah, babu abin da idanuwa suke son gani sama da su.

A cikin wannan ƙissar akwai **rashin ganin kai, da kuma sanin darajar ilimi, da girmama su, da kuma bayyana matsayin addinin Allah Maɗaukakin Sarki a cikin zukata**, ta yiwu hakan ya zamo darasi ga waɗanda suke shiga gaba – gaba wurin yin magana akan addinin Allah ba tare da ilimi ba, su ɓace, su kuma ɓatar da wasunsu, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Allah ba zai ɗauke ilimi ta hanyar cire shi daga cikin bayinsa ba, amma zai ɗauke ilimi ne ta hanyar amsar rayukan malamai, har ya zama babu wani malami da zai yi saura, sai mutane su ɗauki jahilai su shugabantar da su, a tambaye su, su bayar da fatawa ba tare da ilimi ba, su ɓace, su kuma ɓatar da waninsu)**.

Lallai Tabi'ai sun zamo abin koyi mai kyau ga shugabannin da suka zo a bayansu, ga Imam Maliki Bn Anas nan (Allah ya ƙara yarda da shi) nan -wanda ɗaya ne daga cikin tabi'uttabi'ina- a lokacin da Khalifa Abu Ja'afar al- Mansur (Allah ya yi masa rahama) ya nemi da a yi aiki da littafinsa "al-

Muwaɗɗa'a" a dukan garuruwan Musulunci, yana mai faɗa masa haka da cewa: Na yi niyyar in bayar da umurni akan litattafanka da ka wallafa –yana nufin al-Muwaɗɗa'a- na rubuta shi kofi- kofi, na aika da shi zuwa ga garuruwan Musulmai, in bayar da umurnin yin aiki da shi, kada a waiwayi wani littafi ba shi ba, a bar duk waninsa a fannin Hadisi, saboda -a gani na- asalin ilimi shi ne ruwayar mutanen Madina da iliminsu, sai Imam Malik ya ce masa: Ya Amiral muminina, kada ka yi haka, maganganu da yawa sun isa zuwa ga mutane, sun ji Hadisai masu yawa, sun ruwaito ruwayoyi, kuma kowane gari sun yi riƙo da abin da ya isa zuwa gare su na maganganu, suka kuma yi aiki da shi, da kuma shi ne suka gudanar da saɓanin da yake tsakaninsu da wasunsu, hana su yin aiki da abin da suka fahimta sunansa tsanani a cikin al'amarin addini, saboda haka ka ƙyale mutane akan abin da suke a kai, kowane gari da abin da mutanensa suka zaɓar wa kawunansu. Sai ya ce: Na rantse da Allah, in ka yarda mini zan aiwatar da haka.

A cikin abubuwan da suke bayyana **girman tawali'u da ƙasƙantar da kai, da kuma fahimtar addini** akwai abin da ya gudana tsakanin Imam as-Shafi'iy - (Allah ya ƙara masu yarda), da ɗaya daga cikin almajiransa "Yunus Bn Abdul'a'alaa", wata rana ana gabatar da darasi a Masallaci, sai aka sami saɓanin fahimta tsakanin sa da malaminsa Imam "Muhammad Bn Idris as-Shafi'iy" akan wata mas'ala... Sai ya tashi cikin fushi ya tafi gida abinsa... Cikin wannan daren sai "Yunus" ya ji ana ƙwanƙwasa masa ƙofa! Ya ce: wane ne a ƙofa? Sai mai buga ƙofar ya ce: Muhammad Bn Idris ne.. Yunus ya gama tunanin sa bai hararo wane ne Muhammad Bn Idris ba in banda Imam as-Shafi'iy... Sai kuwa ya buɗe ƙofa, ilai kuwa sai ya yi kaciɓir da

shi a bakin ƙofa.. Sai Imam as-Shafi'iy ya ce: Ya Yunus, akwai ɗaruruwan masaloli da fahimtar mu game da su iri ɗaya ce, shin ya kamata a ce mas'ala ɗaya ta raba mu?! Ya Yunus, kada ka zamo mai neman ya yi galaba a cikin kowane saɓani.. Sau da yawa "mallakan zukata" yafi "mallakan galaba da nasara" muhimmanci.. Ya Yunus, kada ka rusa gadar da ka ɗauki lokaci mai tsawo kana ginawa.. Mai yiwuwa wata rana za ka buƙaci ka dawo zuwa gare ta.. Gaskiya kana da haƙƙin ƙin kuskure a kowane lokaci.. Amma kada ka soma ka ƙi mai kuskure... Ka cika zuciyar ka da ƙin saɓon Allah.. Amma ka tausaya, ka kuma yafe wa mai saɓon Allah. Ya Yunus, ka ƙalubalanci magana, amma kuma ka girmama mai maganar.. Aikin mu shi ne: mu kawo ƙarshen cuta, ba wai mu kawo ƙarshen mara Lafiya ba.. Alhairin Allah ya kai zuwa ga Imam as- Shafi'iy a inda yake cewa:

"Ina son mutanen kirki duk kuwa da ba ni a cikinsu, ina son su ne domin ta yiwu albarkacinsu na sami ceto. Ina ƙin mutanen da tadarsu ita ce saɓa wa Allah, koda kuka sun kasance abokan tarayya ta a wurin kasuwanci."

A haka manyan malamanmu suka gudanar da rayuwarsu, sai suka zamo mafiya alhairin abin koyi a gare mu wajen riƙe amanar addinin Allah Maɗaukakin Sarki, da yi masa ingantacciyar fahimta, da ɗabi'antuwa da ɗabi'unsa, da kyautata isar da shi ga mutane cikin hikima, da azanci, da kyakkyawan wa'azi..

**Ya Allah Ubangiji ka sanya mu cikin waɗanda suke sauraran magana da kyau, su kuma ɗauki mafi kyawon cikinsa, lallai waɗanda suke da waɗannan sifofi su ne**

**waɗanda Allah ya shirye su, lallai waɗannan su ne masu tsantsan hankali.**

- 13 –

## RANGWAME DA SAUƘI: MANYAN ALAMU NA GIRMAN SHARI'AR MUSULUNCI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki sauƙi yake so maku, sam ba ya nufin ya tsananta maku)) [al-Baƙra: 185].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda a cikin Hadisinsa mai tsarki yake cewa: **(An aiko ni da addini mai cike da rangwame),** ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Babu shakka akan cewa: lallai alamun girma da darajar Shari'ar Musulunci sun wuce a ƙirga su, ko a yi masu iyaka, a cikin manyan waɗannan alamu da suka bambance Shari'ar Musulunci a cikin shari'o'i akwai: "Rangwame" da "Sauƙaƙawa" da dukan ma'anonin da waɗannan kalmomi suka ƙunsa, ba za ka taɓa cin karo da damuwa, ko wahala a cikinta ba, babu tsanani balle takura, samun tsanantawa daga wasu cikin mutanen da suke da dangantaka da Musulunci, da suka zaci cewa yin taka- tsantsan a cikin addini yana nufin a tsananta, inda da haka suka buɗe ƙofofin tsanantawa a cikin

al'umma, da sannu a hankali suka auka da mutane masu yawa cikin kwazazzaban wuce gona da iri, da tsauraran ra'ayoyi, duka wai da sunan riƙo da addini, ko kuma yin taka- tsantsan, har dai tsanantawa ta zamo wani fage da ake gasa akai a tsakaninmu mutane, inda rayuwarsu take nuna kaman wanda duk ya fi tsanantawa, to shi ne wanda ya fi riƙo da addini, shi ne kuma wanda ya fi tsoron Allah Maɗaukakin Sarki, samun irin waɗannan mutane ba zai zama suka ga addinin Musulunci ba, wannan dalili ne kawai da yake nuna irin yanda suka jahilci girman wannan addini, da rangwamensa, da sauƙinsa a inda Allah Mai girma yae cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki bai sanya maku wata damuwa, da wahala a cikin addini ba, addini ne na babanku Annabi Ibrahim (AlaiHis salam), tun farko shi ne ya kira da suna Musulmai, da ma yanzu; domin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi shaida akanku, ku ma ku yi wa sauran mutane shaida..))** **[al- Hajji: 78]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai wannan addinin sauƙi ne, babu wanda zai tsananta addini face addinin ya fi ƙarfinsa, ku nemi dacewa a dukan ayyukanku, idan ba ku sami hakan ba, to ku kusanto zuwa ga yin daidai ɗin, ku yi wa junanku albishir, muddin kun kasance a haka, ku kuma nemi sa'a na gabatar da haka tun daga lokacin fitowar rana har zuwa lokacin walha, da bayan sallar La'asar zuwa Maghriba, da wani yanki na ƙarshen dare)**, alhairin Allah ya kai zuwa ga Imam Sufyan as- Sauriy da yake cewa: Ilimi a wurinmu shi ne samun sauƙi daga wanda ya yarda da kansa, shi kuwa tsanantawa ai kowa ma ya iya…

Lallai rangwame a Shari'ar Musulunci ba kalma ce da ake faɗi da baki kawai, ko taken da ake rerawa ba, manhaji ne na

Ubangiji, hasali ma ƙa'ida ce da Allah Maɗaukakin Sarki yake mu'amala da bayinsa, wadda ya kuma ya umurce su da su yi amfani da ita a tsakaninsu da juna, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah ba ya ɗaura wa rai komai sai abin da zai iya))** **[al- Baƙra: 233, 286]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki sauƙi yake so maku, sam ba ya nufin ya tsananta maku))** **[al- Baƙra: 185]**, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki yana son ya sauƙaƙa maku ne ta hanyar shar'anta abubuwa masu sauƙi a gare ku, lallai Allah ya halicci ɗan adam ne a wani hali na raunin da ba ya iya wa sha'awarsa da karkatarsa zuwa ga abin da zuciya take so; saboda haka abin da zai yi daidai da shi, shi ne a sauƙaƙa masa wajen wajibai, kuma haka Allah ya ɗaura wa bayinsa, saboda falala da sauƙaƙawa))** **[an- Nisa'i: 28]**, a cikin ayar da tafi sanya kyakkyawan fata a cikin littafin Allah, Allah mai girma ya buɗe ƙofofin yafiya, da rahama ga ɗaukacin bayinsa, inda yake cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka ce Allah ya ce: Ya ku bayin da suke wuce gona da iri wajen aikata laifuffuka, kada ku kuskura ku ɗebe - ƙauna daga rahamar Allah, saboda lallai Allah yana gafarta gaba ɗayan zunubai, domin shi mai yawa gafara da jinƙai ne))** **[az- Zumar: 53]**, a wani wurin kuma yana cewa: **((Lallai Ubangijinka mai yawa gafara da tausayi ne..))** **[al- Kahfi: 58]**, haka ma yana cewa: **((Sai wanda ya tuba, ya kuma kyautata tubarsa, ya dawo daga rakiyar ɓoye gaskiya, inda ya riski al'amarinsa ta hanyar bayyanar da abin da yake ɓoyewa na sifofin Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) da na Musulunci, lallai Allah zai amshi tubar sa, ya kuma share**

**zunuban sa, shi ne kawai wanda yake amsar tuba daga bayin sa saboda tausayin sa da rahamar sa))** **[al- Baƙra: 160].**

An ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi), daga Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lokacin da Allah ya gama halitta, sai ya rubuta "Lallai rahama ta ta rigayi fushi ne" akan Al- Arshinsa)**, haka ma Ubangiji mai girma yana faɗi a cikin Hadisul Ƙudsiy cewa: **(Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: ya kai ɗan Adam, lallai kai ba za ka roƙe ni, ka kuma yi fata na gari daga gare ni ba, face na gafarta maka abin da ka yi, ba tare da na damu ba. Ya ɗan Adam, da a ce zunubanka za su kai ƙololuwar sama, sannan ka nemi gafarata, na gafarta maka. Ya ɗan Adam, kai ɗin nan da za ka zo mini da kura-kuren da za su cika ƙasa, ka sadu da ni ba tare da ka haɗa ni da wani wajen bauta ba, da kuwa na zo maka da gafara cikinta)**.

Haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya hori bayinsa da yin yafiya, da rangwame a wurare masu yawa a cikin littafinsa mai girma, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ka rungumi yafiya, ka kuma juri bayar da umurni da aikata abubuwa masu kyau, ka kuma kawar da kanka ga barin masu wauta))** **[al- A'araf: 199]**, haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kyawawan ayyuka ba za su taɓa yin daidai da munana ba, kai dai kawai tunkuɗe mummuna da abin da ya fi kyau, sai wanda akwai gaba a tsakaninka da shi ya zamo tamkar aboki na kusa, wannan abu kuwa babu mai samunsa sai waɗanda suka yi haƙuri, kai babu mai samun haka sai mai babban rabo))** **[Fussilat: 34 -35]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((To, su yafe, su kuma mayar da komai ba komai ba, shin ba ku son Allah ya**

**gafarta maku ne, lallai Allah mai yawan gafara da jinƙai ne)) [an- Nur: 22].**

Lallai duk mai nazari na lura a tarihin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) zai riske cewa: tabbas (SallalLahu alaiHi wa sallam) babban abin koyi ne ga al'ummarsa, da ma ɗaukacin bil'adama a fagen rangwame, da sauƙaƙa al'amurra, saboda haka ne Ummul- muminina Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) take cewa: **(Ba a taɓa bai wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) zaɓi akan wasu abubuwa biyu ba, face ya zaɓi wanda ya fi sauƙi a tsakaninsu, muddin dai ba saɓon Allah ba ne, idan saɓon Allah ne, to (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fi kowa nesantarsa, kuma Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) bai taɓa mayar da martani saboda kansa ba, sai dai idan an keta hurumin Allah, sai ya mayar da martani akan haka)**.

Bari mu kawo wasu misalai daga rayuwarsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) ta kira zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki cikin hikima, da azanci, da kuma kyautata wa'azi, an ruwaito Hadisi daga Anas Bn Malik (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: Wata rana ina wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai wani mutum ya zo wurinsa, sai ya ce: Ya Manzon Allah, na aikata abin da haddi ya hau kai na, ina roƙon a tsayar mini da haddi.. ya ce: bai tambaye shi akan abin da ya aikata ba, har lokacin sallah ya yi, ya yi sallah tare da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), bayan Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ƙare sallah, sai mutumin nan ya miƙe ya je wurinsa, sai ya ce: Ya Manzon Allah, na aikata abin da haddi ya hau kai na, ina son ka tsayar mini da hukuncin da littafin Allah ya tabbatar, sai ya

ce: **(Ba ka yi sallah tare da mu ba?)**, ya ce: Ey, sai ya ce: **(Lallai Allah ya gafarta maka zunubinka)**.

An ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa: wani Balaraben ƙauye ya tashi ya yi fitsari a Masallaci, mutane suka yo masa cã, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ku ƙyale shi, ku kwara guga ɗaya na ruwa a fitsarin nasa, masu sauƙaƙawa kawai aka aiko ku, ba a aiko ku a matsayin masu tsanantawa ba)**, haka ma an ruwaito daga Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: **An kawo wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ƙaramin yaro, sai ya yi masa fitsari a jiki, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya aka kawo masa ruwa ya zuba akansa**.

An ruwaito Hadisi daga Mu'awiyya Bn al-Hakam as-Sulamiy, ya ce: wani lokaci ina sallah a bayan Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai wani daga cikin mutane ya yi atishawa, sai na ce masa: "YarhamukalLah", sai mutane suka yi mini ƙuri da idanuwansu, sai na ce: ikon Allah, me kuma na yi da kuke kallo na? sai suka koma dukan cinyoyinsu da hannuwansu; da nufin in yi shiru, da na ga suna ƙoƙarin sanya ni in yi shiru, sai na yi shiru, lokacin da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya gama sallah –iyaye na biyu fansa ne a gare shi- wallahi ban taɓa ganin malami kafin shi, da bayan shi da ya kai shi iya koyarwa ba, bai ƙyare ni ba, bai kuma doke ni ba, bai kuma zage ni ba, abin da ya ce kawai shi ne: **(Wannan sallah ce da maganganun a tsakanin mutane bai halatta a cikinta ba, abin da ake yi a ciki kawai si ne: Tasbihi da Takbiri da karatun Alƙur'ani)**.

Babu shakka da za mu bibiyi littafin Ubangijinmu mai girma da ɗaukaka, da Hadisan Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) da za mu sami nau'o'i iri- iri na rangwame, da sauƙaƙawa, da jinƙan da za su kawo ƙarshen ɗaukacin nau'o'in wuce gona da iri, da tsauraran ra'ayoyi, da tashin hankula da duniya take fama da su a wannan lokacin, a **fagen Aƙida:** za mu sami cewa addinin Musulunci bai wajabta wa kowa shiga cikinsa ba, hasali ma ya kiyaye wa kowa 'yancin yin imani da duk abin da ya ga dama, Allah Mai girma yana cewa: **((Shi al'amarin addini babu tilas a ciki, lallai hanyar gaskiya ta riga ta bayyana da dalilai na fili ƙarara, haka ma hanyar ɓata..))** **[al-Baƙra: 256],** haka mai Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Da Ubangijinka ya ga dama, da ɗaukacin waɗanda suke a doron ƙasa sun yi imani, shin tursasa mutane za ka yi har sai sun zamo muminai?))** **[Yunus: 99].**

**A fagen Ibadu kuma:** Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi kira zuwa ga sauƙaƙawa, da rangwame, da kuma nesantar tsanani, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(A cikinku akwai masu kore jama'a, duk wanda zai yi wa mutane sallah, to ya sauƙaƙa, domin a cikinsu akwai: mara lafiya, da mai rauni, da kuma wanda yake da wata buƙata)**, lokacin da wasu suka kai ƙarar Sayyiduna Mu'az Bn Jabal (Allah ya ƙara yarda da shi) akan yana tsawaita masu a sallah, Annabin (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya karantar da shi, yana mai cewa masa: **(Yanzu -ya Mu'az- fitina za ka zamo wa mutane? –ya maimaita haka har sau uku- ka karanta "Was-shamsi waddhuhaha" da "Sabbismi Rabbikal A'ala" da makamantansu)**, a wata ruwayar kuma ya ce: **(Lallai akwai tsoho, da mai rauni, da mai wata buƙata duk suna sallah a**

**bayanka)**. An ruwaito Hadisi daga Anas Bn Malik (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: wata rana Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya shiga Masallaci, sai ya ga wata igiya ɗaure a tsakanin ginshiƙai guda biyu, sai ya ce: **(Wannan igiyar fa?)** sai suka ce: Igiyar Zainab ce, idan kasala ta kama ta sai ta ja ta, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(,A'a, ku kwance, kowa ya yi sallah cikin nishaɗinsa, idan kasala ta kama shi ya yi zamansa)**, an ruwaito Hadisi daga Jabir (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: a wani lokaci mun yi tafiya, sai wani dutse da aka jefe ya sami ɗaya daga cikinmu a kansa ya ji masa rauni, sannan kuma ya yi mafarki, sai ya tambayi abokan tafiyarsa cewa: shin akwai wani sauƙi da zan samu na in yi taimama? Sai suka ce: ai babu wani sauƙi, muddin dai za ka iya yin amfani da ruwa, sai kuwa ya yi wanka ya mutu, da muka zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) sai muka ba shi labarin abin da ya faru, sai ya ce: **(Sun kashe shi, Allah wadaransu, mene ya hana su yi tambaya idan ba su sani ba, ai maganin jahilci shi ne tambaya, taimama kawai ta ishe shi, ya kuma sanya ƙyalle ya rufe mikinsa, sannan ya shafe shi, ya kuma wanke sauran jikinsa da ruwa)**, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fuskantar da Sayyiduna Imran Bn Hussain (Allah ya ƙara yarda da shi) zuwa ga abin da zai yi lokacin da yake cikin rashin lafiya, ya ce masa: **(ka yi sallah a tsaye, idan ba za ka iya ba, ka yi a zaune, idan ba za ka iya ba, ka yi a kwance)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(An sanya ƙasa ta zamo wurin sallah, kuma mai tsarki a gare ni, duk wanda sallah ta riske shi a cikin al'umma a kowane wuri, to ya yi sallarsa)**, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana mana yanda ake rangwame a aikace, inda hakan kuwa ya zamo

tamkar wani haske da yake bayyana girman Musulunci, game da sallah wadda take cikin manyan rukunnan Musulunci, mun ji Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai nakan fara sallah da niyyar na tsawaitawa, sai in ji kukan ƙaramin yaro, sai na taƙaita sallah ta; saboda abin da na sani na tsananin damuwar da mahaifiyarsa za ta shiga sakamakon kukansa)**.

**A fagen mu'amala:** Shari'ar Musulunci ta yi kira zuwa ga rangwame, da sauƙaƙawa, da ɗauke damuwa, da wahalhalu a tsakanin mutane wajen saye da sayarwa, da biyan bashi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, kada wani sashe naku ya ci dukiyar wani sashe ba tare da haƙƙi ba, sai dai ya halatta ku yi kasuwanci a tsakanin ku, ta hanyar yarda, kada ku yarda ku halakar da kawunanku ta hanyar saɓa wa umurnin Ubangijnku, kada wani ya yarda ya kashe ɗan uwansa, babu wani rai da yafi wani, lallai Allah mai yawan tausayinku ne a koda yaushe)) [an- Nisa'i: 29]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Idan kuma aka sami mara-shi, ku ba shi bãshi, ku kuma jinkirta masa a lokacin biya har zuwa lokacin da zai sami wadata, ku ba shi sadaka ta hanyar yafe masa bãshin, ko yafe wani sashe na bãshin, hakan shi ne ya fi alhairi a gare ku, in dai kuna cikin masu ilimi da fahimtar maganar Allah mai girma da ɗaukaka da take karantar da ku mutunci da mutuntaka)) [al- Baƙra: 280]**, Annabinmu mai tsira da aminci yana cewa: **(Allah ya yi rahama ga mutum mai rangwame wajen sayarwa, da wajen saye, da wajen neman biyan bashi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Allah ya yi rahama ga bawa mai rangwame wajen biyan bashi, mai kuma rangwame wajen**

**amsar haƙƙinsa)**, rangwame a wajen sayarwa yana nufin: kada mai sayarwar ya zamo mai haɗama, mai neman ƙazamiyar riba, mai kuma ɓoye kayan amfani domin su yi tsada ya fito da shi, mai kuma tauye ma'auni.. Abin da rangwame a wajen saye yake nufi kuwa shi ne: mai saye ya zamo mai sauƙin kai tare da mai sayarwa, kada ya yi wa mutane ƙwange, rangwame wajen neman biyan bashi kuma shi ne: mutum ya nemi haƙƙinsa, ko bashin da yake bi cikin sauƙi da tausasa murya gami da rangwame.

Lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayar da labarin cewa yin rangwame a wajen mu'amala dalili ne na samun tsira a ranar lahira a inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Wani mutum ya shiga aljanna da rangwamensa a lokacin da yake biyan bashi, da lokacin da yake neman biyan bashi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(An yi wa wani mutum da ya gabace ku hisabi, amma ba a same shi ya taɓa aikata wani alhairi ba kwata- kwata, in banda kasancewarsa yakan cakuɗu da mutane, shi kuma mawadaci ne, sai yake umurtan yaransa da su rinƙa ɗaga ƙafa ga marasa shi, ya ce: Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: mu muka fi shi cancanta da yin haka, shi ma ku ɗaga masa ƙafa)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana bayar da labarin wasu daga cikin yanayin ranar tashin alƙiyama yana cewa: **(Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa; ku duba gidan wuta, shin a ciki akwai wani wanda ya taɓa gabatar da aikin alhairi? Sai a cikin wutar su sami wani mutum, sai ya ce masa: shin ka taɓa gabatar da aikin alhairi a rayuwarka? Sai ya ce: a'a, kawai dai ina yi wa mutane rangwame wajen sayarwa, sai Allah mai**

**girma da ɗaukaka ya ce: ku yi wa bawa na rangwame kaman yanda yake yi wa bayi na rangwame)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai ƙa'idar yin rangwame ba ta tsaya kawai a mu'amala tsakanin Musulmai da junansu ba, hasali ma hakan manhaji ne na rayuwa, da ta game kowa da kowa, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya bai wa ɗaukacin bayinsa muminai umurni na su kyautata mu'amala tare da mutane gaba ɗaya, yana cewa: **((Ku faɗa wa mutane magana mai kyau))** **[al- Baƙra: 83]**, haka ma mai tsarki da buwaya yana cewa: **((Allah ba ya hana ku girmama da sada zumuntanku da kãfiran da ba su yaƙe ku ba, ba kuma su fitar da ku daga gidajenku ba, lallai Allah yana son masu kyautatawa da kuma sada zumunta))** **[al- Mumtahanat: 8]**, a duk sanda aka yanka tunkiya a gida Sayyiduna Abdullahi Bn Umar (Allah ya ƙara yarda da su) yakan ce wa yaronsa: shin ka kai wa maƙwabcinmu Bayahuden nan kuwa? shin ka kai wa maƙwabcinmu Bayahuden nan kuwa?; don lallai na ji Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Jibrilu bai**

**gushe ba yana yi mini wasici da maƙwabci har sai da na zaci zai sanya shi cikin magada)**.

A cikin nau'o'in rangwame akwai rangwamen zuciya, ma'ana : baiwa da kyautar da take yi, da gabatar da alhairai ga ɗaukacin mutane, Imam as- Shafi'iy (Allah ya ƙara masa rahama) yana cewa:

"Ka suturta kanka da yawan kyauta, domin kowane aibi yana suturtuwa ne –kaman yanda aka faɗi- da yawan kyauta, kada ka taɓa yi wa maƙiya kallon ƙasƙanci, domin dariyar maƙiya bala'i ne, kada kuma ka yi fatan samun rangwame daga marowaci, domin dai mai ƙishi ba zai taɓa samun ruwa daga wuta ba".

**Ya Allah Ubangiji muna roƙon ka azurta mu da nagartacciyar fahimtar** addininmu**, ka shiryatar da mu, ka kuma shiryatar da wasu da shiriyarmu, ka sanya mu zamo dalilin shiriya ga waɗanda suka shiryu.**

## - 14 –

## HAƘƘOƘIN IYAYE DA MAKUSANTA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ubangijinka ya hukunta kada a bauta wa kowa sai shi kaɗai, su kuma iyaye a kyautata masu, idan ɗaya daga cikinsu, ko dukansu biyun sun manyanta kada ka kuskura ka ce da su: tir, ko kuma ka kyare su, ka dai faɗa masu magana mai girma.. ka yi masu duk abin da za ka iya na tausayi da jinƙai, ka yi addu'ar: ya Ubangijina ka yi masu rahama kamar yadda suka raine ni ina ƙarami))** **[al-Isra'i: 23 -24]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa da waɗanda suka bi tafarkinsa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai addinin Musulunci ya zo da saƙo mai cike da rangwame, saƙon yana kira zuwa ga manyan ɗabi'u, yana kuma shimfiɗa kyawawan tadodi, yana kuma shiryatarwa zuwa ga daidaitacciyar rayuwa, inda waɗannan kyawawan ɗabi'u da tadodi suke zamowa manhajin rayuwa da suke daidaita mizanin mu'amala ta gaskiya, da adalci, da tausayi, da soyayya, da mutuntaka tsakanin mutane, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai Allah yana bayar da umurni yin adalci, da**

**kyautatawa, da bayar da sadaka da kyauta ga makusanta, yana kuma hana aikata alfasha, da abubuwan ƙi da ƙyama, da zalunci, yana yi maku wa'azi ne ko za ku faɗaka))** **[an- Nahl: 90]**.

Lallai a cikin alamun girma da darajar shari'ar Musulunci akwai kasancewarta ta sanya ƙa'idoji da dokoki da kuma haƙoƙƙi na yin mu'amala tare da iyaye da makusanta; lallai iyaye biyu su ne **suka fi cancanta da girmamawa, gami da ba su kulawa ta musamman**, Allah Maɗaukakin Sarki a cikin littafinsa mai girma ya umurce mu da mu girmama iyaye, mu kuma kyautata masu, ya kuma gwama hakan da yin masa bauta da rashin haɗa shi da wani a wajen bauta, Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ku bauta wa Allah Maɗaukakin Sarki, kada ku kuskura ku haɗa shi da wani abu a wajen bauta, su kuma iyaye ku kyautata masu..))** **[an- Nisa'i: 36]**, haka ma kaman yanda Allah mai girma ya umurce mu da mu gode masa akan ni'imominsa, ya gwama wannan godiyar tasa da gode wa iyaye biyu; saboda irin girma da matsayi masu girma da suke da su, Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: Ayoyi guda uku sun sauka ne a gwame da abubuwa guda uku, ba za a karɓi kowane ɗaya daga cikinsu ba tare da ɗan uwan gwaminsa ba, a cikinsu akwai inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Cewa ka gode mini, haka ma ka gode wa iyayenka biyu..))** **[Luƙman: 14]**, duk wanda ya gode wa Allah, bai gode wa iyayensa biyu ba, to ba za a amsa masa ba.

Lallai addinin Musulunci ya ɗaukaka darajar iyaye biyu, **ya bayar da umurnin a yi masu biyayya, a kuma kyautata kulawa da su, da nuna masu tausayi da jinƙai**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abdullahi Bn Amr (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: wani mutum ya zo wurin Manzon Allah

(SallalLahu alaiHi wa sallam) yana neman ya yi masa izinin fita zuwa jahadi, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce masa: **(Shin iyayenka suna raye?)** Sai ya ce: Ey, sai ya ce: **(To, ka yi jahadi wajen yi masu biyayya)**.

Lallai 'ya'ya mata guda biyu na mutumin kirkin nan da ya zo a ƙissar Annabi Musa (AlaiHis Salam) sun buga babban misali na yi wa iyaye biyayya, da kuma kyautata masu, mahaifinsu ya tsufa sosai, ta yanda ba zai iya yin aiki ba, sai suka ɗauki alhakin yin aiki a madadinsa, ba kuma tare da sun nuna nukura da ƙosawa ba, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Lokacin da Annabi Musa (AlaiHis Salam) ya zo wurin ruwan mutanen Madyana, sai ya sami jama'a suna shayar da dabbobinsu, ya kuma ga wasu mata guda biyu a gefensu sun killace dabbobinsu, sai ya ce: mene ne ya faru? Sai suka ce: ba ma iya shayar da dabbobinmu har sai makiyaya sun kora nasu; saboda mahaifinmu dattijo ne mai shekaru))** **[al- Ƙasasi: 23]**.

An ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Jabir (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce : wani mutum ya ce: ya Manzon Allah, ina da dukiya da ɗa, kuma mahaifi na yana buƙatar dukiya ta, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Kai da dukiyarka duka na mahaifinka ne)**.

Lallai Sayyida Faɗima (Allah ya ƙara yarda da ita) babbar abar koyi ce mai matuƙar kyau wajen soyayya da girmamawa da tausayin da take yi wa mahaifinta Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), a duk sanda (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya je wurinta takan miƙe daga wurin zamanta, ta yi haba- haba da shi, ta kuma zaunar da shi a wurin zamanta, saboda murna da

farin ciki da zuwansa, da kuma girmama matsayinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam).

Haka ma addinin Musulunci **kaman yanda ya umurce mu da girmama iyaye biyu, da rashin cutar da su**, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Idan ɗaya daga cikinsu, ko dukansu biyun sun manyanta kada ka kuskura ka ce da su: tir, ko kuma ka kyare su, ka dai faɗa masu magana mai girma..))** **[al- Isra'i: 23]**, haka ma ya hana kowace irin kalma ta nukura da ƙosawa, koda kuwa kalmar tana ƙasa da kalmar "tir, ko kaico" ne, abin da ya fi ma shi ne kada mutum ya zamo sanadiyyar cutar da su, ko munana masu da kowane irin nau'i na munanawa, Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) ya faɗa wa wani mutum –a lokacin da yake yi masa nasihar yi wa mahaifinsa biyayya- cewa: "Kada ka shiga gaban mahaifinka idan kuna tafiya, kada ka zauna a wuri kafin ya zauna, kada kuma ka kira shi da sunansa, kada kuma ka jawo masa zagi", lallai bai kamata Musulmi ya zamo dalilin jawo wa iyayensa kowane irin cutarwa ba, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai laifi ne babban mutum ya zagi iyayensa)**, sai suka ce: ya Manzon Allah, ta yaya kuwa mutum zai zagi iyayensa? Sai ya ce: **(Mutum ne zai zagi mahaifin wani, shi kuma ya rama da zagin mahaifinsa, ko ya zagi mahaifiyar wani, shi ma ya rama da zagin mahifiyarsa)**.

Lallai addinin Musulunci ya yi wasici da yi wa iyaye biyu biyayya, da kuma kyautata zama tare da su, **koda kuwa ba su cikin addinin Musulunci**, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Idan sun tirsasa maka akan ka haɗa ni da wani abu da ba ka da masaniya akansa a wajen bauta, to kada ka yi masu biyayya; amma duk da haka ka zauna da su a rayuwar duniya**

**cikin kyautatawa..))** **[Luƙman: 15]**, wannan ne kuma abin da ya faru da Sayyiduna Ibrahim (AlaiHis Salam) a lokacin da yake kiran babansa, game da haka ne Allah mai girma yake cewa: **((Ka ambata masu labarin Annabi Ibrahim (AlaiHis Salam), lallai Annabi ne shi kuma siddiƙi, lokacin da ya ce wa babansa : ya babana, mene zai sanya ka bauta wa abin da ba ya ji, ba kuma ya gani, ba kuma zai iya tsinana maka komai ba? ya babana, Ni fa tabbas ilimin da ya zo mini bai zo maka ba, ka bi ni saboda in shiryatar da kai zuwa ga hanya madaidaiciya. Ya babana, kada ka bauta wa shaiɗan, lallai shaiɗan mai yawan saɓon Allah mai yawan rahama ne. ya babana, tabbas ina jin tsoron wata azaba daga Allah mai yawan rahama ta shafe ka, ta yanda za ka zamo wakilin shaiɗan))** **[Maryam: 41 – 45]..**

Ga ma Sayyida Asma'u Bint Abubakar (Allah ya ƙara yarda da su) nan, mahaifiyarta ta zo wurinta domin sada zumunci -a lokacin tana mushrika-, sai ta tambayi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) game da haka, ta ce: Ya Manzon Allah, mahaifiya ta ce ta zo wuri na tana son sada zumunci, shin na sada zumunci da ita kuwa? Sai ya ce: **(Ƙwarai kuwa, ki sada zumunci da mahaifiyarki)**.

Lallai yi wa iyaye biyayya yana da tasiri, da fa'idoji masu girma, da kuma manyan falala da bawa zai samu a duniya da lahira, a cikinsu akwai: **kasancewar yi wa iyaye dalili ne na samun yardan Allah Maɗaukakin Sarki**, lallai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Yardar Allah tana cikin yardar iyaye biyu, haka fushin Allah yana cikin fushin iyaye biyu)**.

Haka ma dalili ne na yaye damuwa da baƙin ciki, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya faɗa mana **labarin wasu**

**mutane uku da faɗowar ruwan sama ya tilasta masu fakewa a wani kogo da yake cikin wani dutse, sai wani dutse ya gangaro ya toshe kofar kogon da suke ciki ya rufe su, sai wasu daga cikinsu suka ce wa saura: ku tuno da ayyukan da kuka yi su saboda Allah shi kaɗai, mu roƙi Allah da su, ko Allah zai yaye mana wannan damuwa, sai ɗaya daga cikinsu ya ce: Ya Ubangiji, lallai ina da iyaye guda biyu da suka tsufa, ina kuma da yara ƙanana, ina yin kiwo saboda su, idan zan je wurinsu sai na tatsi nono na tafi masu da shi, sai in fara da bai wa mahaifa na kafin 'ya'ya na, wata rana sai na makara, ban dawo ba har yamma ta yi, sai na samu sun yi barci, sai na tatso nono kaman yanda na saba, sai na tsaya a kansu, ba na son na tashe su, ba kuma na son in fara bai wa yaran kafinsu, su kuma yaran suna ta juye- juye saboda yunwa a gefen ƙafafuwa na, har alfijir ya keto, Ya Ubangiji idan ka san wannan abu da na yi, na yi shi ne saboda neman yardarka, to ka tunkuɗe mana wannan dutsen ta yadda za mu iya hango sama, sai kuwa Allah ya tunkuɗe masu, suka hango sama…)**, inda biyayyar da yake yi wa iyayensa biyu ta zamo dalili na yaye masa damuwa, da samun tsira.

Haka ma wanda duk yi wa iyayensa biyayya, 'ya'yansa ma za su yi masa biyayya, domin ana yin sakamako ne da irin nau'in aikin da aka yi, Allah Maɗaukakin Sarki ya saka wa Sayyiduna Ibrahim (AlaiHis Salam) akan kyautatawar da ya yi wa babansa wajen kira ne da azurta shi da biyayyar ɗansa Sayyiduna Isma'il (AlaiHis Salam), lallai Alƙur'ani mai girma ya kawo mana bayani game da mafi girman sura daga cikin surorin yi wa iyaye biyayya da ɗa'a, Allah mai girma yana cewa: **((Lokacin da Sayyiduna Isma'il (AlaiHis Salam) ya kai**

**munzalin girma, sai mahaifinsa ya ce: Ya ɗana, na yi mafarkin ina yanka ka, yaya kake gani? Sai ya ce: ya babana, ka aikata abin da aka ba ka umurni kawai, da ikon Allah za ka same ni cikin masu haƙuri)) [as- Safat: 102].**

Kaman yanda yi wa iyaye biyayya yake da sakamako tun a nan duniya, haka ma **a lahira dalili ne na samun jin daɗin Musulmi, inda zai shiga aljanna,** wani mutum ya zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana neman izinin zuwa jahadi, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce masa: **(Shin kana da mahaifiya?)**, sai ya ce: na'am, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ka lizimce ta, aljanna na nan a wurin ƙafarta)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mahaifi shi ne mafificiyar ƙofar aljanna, in ka so ka kiyaye wannan ƙofar, ko kuma ka wofintar)**. Sayyiduna Abdullahi Bn Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce wa wani mutum: Shin kana jin tsoron shiga wuta, kuma kana son shiga aljanna? Sai ya ce: ey wallahi, sai ya ce: shin iyayenka biyu suna raye? Sai ya ce: mahaifiya ta tana nan, sai ya ce: na rantse da Allah, idan ka tausasa mata magana, ka kuma wadata ta da abinci, tabbas za ka shiga aljanna matuƙa ka nesanci manyan zunubai.

A nan muna ƙara tabbatar da cewa: duk wani abu da biyayya da kyautatawa da ka iya gabatar wa iyayenka, to ka sani ba za ka taɓa iyaye biyansu haƙƙinsu, ko ka saka masu ba, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ɗa ba zai iya saka wa mahaifinsa ba, sai dai idan ya same shi a matsayin bawa ya saye shi ya kuma 'yanta shi)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Kaman yanda addinin Musulunci ya yi wasicin a kyautata wa iyaye biyu, haka ma ya yi wasicin a kyautata wa makusanta, su ne waɗanda dangantaka ta kusanci ta haɗe su da mutum, Allah ya ba su wasu haƙƙoƙi, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Mazumunta su suka fi cancanta da junansu a cikin littafin Allah..))** **[al- Anfal: 75; al- Ahzab: 6]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya halicci halittu, bayan ya gama ne sai ya halicci mahaifa, sai ta ce: wannan shi ne muƙamin mai neman tsari daga gare ka akan yanke zumunci, sai ya ce: na'am, ashe ba za ki gamsu a ce na sadar da wanda ya sadar da ke, ya kuma yanke wanda ya yanke ki ba? sai ta ce: na yarda, sai ya ce: to haka ne**, sannan Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam ya ce: **(In kuna so, ku karanta maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: ((Ya ku munãfukai, da ma me ake jira daga gare ku a lokacin da kuka kawar da kawunanku ga barin yi wa Allah biyayya banda yin ɓarna a bayan ƙasa, da yayyanke zumunta? Waɗannan su ne waɗanda Allah ya nesanta su ga barin rahamarsa, sai ya kurumtar da su ga barin jin gaskiya, ya kuma makantar da idanuwarsu ga barin ganin hanyar shiriya. Shin sun makance ne ba sa**

**fahimtar shiryatarwa ta Alƙur'ãni Mai girma!.))** **[Muhammad: 22 – 23].**

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: Allah mai girma da ɗaukaka da yake cewa: **(Ni ne Allah, ni ne kuma Arrahman, na halicci mahaifa, na kuma samo mata suna daga cikin sunaye na, duk wanda ya sadar da ita, zan sadar da shi da rahama, wanda kuma duk ya yanke ta zan yanke shi ga barin rahama)**.

Sadar da zumunci ga makusanta **yana tabbata ne da ziyararsu, da kuma bincika halin da suke ciki, da taimaka masu,** Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Bai wa miskinai sadaka yana da ladan sadaka, amma bai wa makusanta kuwa yana da lada biyu; na sada zumunci da kuma sadaka)**, haka ma sadar da zumunci yana tabbata da amsa gayyatarsu, da zuwa duba marasa lafiyan cikinsu, da halartar jana'izarsu, haka ma ya kamata a girmama manyan cikinsu, a kuma tausaya wa ƙananan cikinsu, da zama lafiya cikin yafiya akan duk abin da ya shafe su, da kuma yi masu addu'a.

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya sadar da zumunci ya zamo **dalili na sanya albarka a cikin rayuwa, da yalwan arziki,** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda yake son Allah ya tsawaita rayuwarsa, ya kuma yalwata arzikinsa, to ya yi wa iyayensa biyu biyayya, ya kuma sadar da zumuncinsa)**. Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ba mu labarin cewa sada zumunci **dalili ne gafarta zunubai**, lallai wani mutum ya zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce: ya Manzon Allah, lallai na aikata babban zunubi, shin ina da daman tuba kuwa? Sai (SallalLahu alaiHi

wa sallam) ya ce masa: **(Shin kana da mahaifiya a raye?)** sai ya ce: a'a, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Shin kana da inna a raye?)**, sai ya ce: na'am, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(To, ka yi mata biyayya)**.

Dole ne mutum ya nesanci yanke zumunci, ya kuma nesanci sakanya mummunan abu da mummunan abu, kamata ya yi ya zamo mai yafiya da rangwame, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mai sadar da zumunci ba wai shi ne wanda in an yi masa ya rama zumuncin da aka yi masa ba, a'a, mai sadar da zumunci shi ne wanda idan an yanke zumunci ya sada shi)**, haka ma wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce: ya Manzon Allah, ina da makusanta da nake sadar da zumunci da su, su kuma suna yankewa, ina kyautata masu, su kuma suna munana mini, ina haƙuri da su, su kuma suna yi mini wauta, sai ya ce: **(Idan dai haka kake kamar yadda ka faɗa, to tamkar kana ciyar da su toka ce mai tsananin zafi, kuma Allah ba zai daina taimakonka akansu ba, matuƙar ka dawwama a haka)**.

Lallai addinin Musulunci ya hana yanke zumunci, ya kuma yi gargaɗi akan mummunan ƙarshen da yake jiran mai yankewar a duniya da lahira, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu wani zunubin da ya fi cancanta a gaggauta yi wa mai shi uƙuba tun a duniya, a kuma tanada masa wata uƙubar a lahira kaman zalunci da yanke zumunci)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mai yanke zumunci ba zai shiga aljanna ba)**.

Ya kamata mu ji tsoron Allah akan iyayenmu maza da mata, mu sadar da zumuncinmu, mu kuma kyautata wa ɗaukacin mutane.

**Ya Allah Ubangiji muna roƙon ka datar da mu zuwa ga yi wa iyayenmu maza da mata biyayya, ka kuma sanya mu cikin masu sadar da zumunci, ka kiyaye mana al'ummarmu, ka tsare mana ƙasarmu, ka yalwata arzikinmu da zaman lafiyarmu da ma na sauran ƙasashe baki ɗaya.**

**- 15 –**

## WAJIBIN ƊALIBI DA NA MALAMI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Allah yana ɗaukaka darajar muminai masu tsarkake shi a wurin bauta, da waɗanda aka ba su ilimi, duka Allah yana ɗaukaka darajarsu, Allah yana da cikakkiyar masaniya akan abin da kuke aikatawa)) [al-Mujadalat: 11].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya, shi ne cikakken masani, mai hikima.

Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, Annabi mai girma da ba ya rubutu da karatu. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa, masu fararen gaɓoɓin alwalla a ranar alƙiyama, da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Muna gab da shiga sabuwar shekara ta karatu, muna roƙon Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya ta zamo shekarar ƙoƙari da jajircewa, da samun nasara ga ɗaukacin 'ya'yanmu, babu shakka addinin Musuluci ya bai wa ilimi babban muhimmanci, da kulawa ta musamman, da shi ne zukata suke rayuwa, basira kuma take haske; domin ilimi yana kai mai yinsa matsayin zaɓaɓɓu, da manyan muƙamai a duniya da lahira, da shi ne ake

sada zumunci, a kuma san halal da haram, da shi ne Allah Maɗaukakin Sarki ya ɗaukaka wasu mutane, inda ya mayar da su shugabanni, kuma jagorori a cikin alhairai, ana bibiyan iliminsu, ana kuma koyi da ayyukansu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa sallam), ka ce masu: shin za a daidaita waɗanda suka sani, da waɗanda ba su sani ba?..))** **[az- Zumar: 9]**.

Lallai muhimmancin da addinin Musulunci ya bai wa ilimi, da kwaɗaitarwa zuwa gare shi yana bayyana ne a farkon ayoyin da suka sauka cikin Alƙur'ani mai girma, inda Allah Mai girma da ɗaukaka yake cewa: ((**Ya Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa sallam), ka karanta abin da aka yi maka wahayi, kana buɗe karatun naka da sunan Ubangijinka da shi kaɗai ne kawai yake da ikon halitta. Ya samar da ɗan adam ɗin da yake da cikakken jiki da ilimi ne daga gudan jini. Ka cigaba da karatu, lallai Ubangijinka mai yawan karamci yana ganin girma da darajarka, ba zai taɓa taɓar da kai ba. Shi ne ya sanar da ɗan Adam yadda zai yi rubutu da alƙalami, a da bai san haka ba. Ya sanar da ɗan adam abin da bai taɓa ko hararo su a zuciyarsa ba))** **[al- Alaƙ: 1 – 5]**, farkon wahayi shi ne bayar da umurni da a yi karatu, shi kuma karatu shi ne farkon ƙofar ilimi, sannan aka yi nuni zuwa ga alƙalami, wanda shi ne wasilar rubuta ilimi da gadar da shi; hakan kuma faɗakar da mutane ne akan falalar ilimi, da kwaɗaitarwa da kira ne zuwa ga nemansa.

Lallai ilimi yana da babban matsayi, haka ma malamai suna da matsayi mai girma, ba domin ilimi da malamai ba da mutane sun ɓace, shi ilimi haske ne da yake haskaka wa mai shi haƙiƙanin al'amurra, malamai a cikin mutane tamkar taurari ne

a sararin samaniya da ake gane komai da su, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shin wanda ya san cewa abin da Ubangijinka ya saukar maka shi ne gaskiya zai yi daidai da makaho?! Lallai masu hankali ne kawai suke wa'aztuwa))** **[ar-Ra'ad: 19]**, a nan kaman Allah Maɗaukakin Sarki ya kasa mutane ne a wannan aya zuwa gida biyu: masani, da kuma makaho; inda ya sanya ilimi ya zamo kishiya ga makanta, ido a nan yana nufin ido a ilimi da sani, ba wai idon gani ba, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ai al'amarin da ma ba idanuwa ne suke makancewa ba, kawai dai zukatan da suke cikin ƙiraza ne suke makancewa))** **[al- Hajji: 46]**, sannan Alƙur'ani mai girma ya ɗaukaka darajar ilimi, ya kira shi da suna "Sultan", Allah mai girma yana cewa: **((Su ne waɗanda suke jayayya a cikin ayoyin Allah ba tare da wani ilimi ya zo masu ba, wannan laifi kam ya yi girma a wurin Allah, da ma wurin waɗanda suka yi imani da Allah..))** **[Ghafir: 35].**

Lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana matsayin ilimi da falalar nemansa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya bi hanyar neman ilimi, to Allah zai bi da shi hanyar aljanna, lallai Mala'iku suna shimfiɗa fuka- fukansu saboda amincewa da mai neman ilimi, lallai ɗaukacin abubuwan da suke sama da ƙasa, da kifaye a cikin ruwa suna nema malami gafara, lallai falalar malami akan mai bauta tamkar falalar wata ɗan daren goma sha huɗu ne akan sauran taurari, lallai malamai magada Annabawa ne, domin Annabawa ba su gadar da dinare da dirhami ba, sun dai gadar da ilimi ne, wanda ya yi riƙo da shi kam lallai ya sami babban rabo),** an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuzarrin (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce:

Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce mini: **(Ya Abuzarrin, ka wayi gari kana mai koyan aya ɗaya daga cikin littafin Allah ya fi maka alhairi akan ka yi sallah raka'a dubu, kai ka wayi gari kana mai koyon babi ɗaya cikin babukan ilimi -shin an yi aiki da shi ko ba a yi- ya fi maka alhairi akan ka yi sallah raka'a dubu)**.

Imam Aliyu (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **"Ilimi ya fi dukiya alhairi; domin ilimi gadinka yake yi, ita kuwa dukiya kai ne kake gadinta, ilimi sarki ne, ita kuwa dukiya mulkinta ake yi, dukiya na raguwa idan ana cinta, shi kuwa ilimi yana ƙaruwa ne idan ana bayar da shi"**.

Lallai ilimi yana da wasu manyan kyawawan ɗabi'u da ladubba, da suka kamata mai nemansa, da mai bayar da shi su yi ado da su; muhimmai daga cikin su akwai: **Yi domin Allah Maɗaukakin Sarki,** dole ne malami da ɗalibi su nemi yardar Allah da ilimin da suke yi, su kuma nesanci riya, da ji- da jiyarwa, ilimi yana da wata ɓoyayyiyar sha'awa, wadda idan ta sami wuri a cikin zuciyar bawa, sai son bayyana, da neman shuhura, da neman a gabatar da shi a cikin komai su mallake zuciyarsa, ta yiwu hakan ma ya yi tasiri a cikin rayuwarsa, ya koma yana yi wa mutane girman kai, lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya gargaɗe mu akan duka wannan, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda duk ya nemi ilimi domin ya yi wa wawaye burga, ko ya yi takara da malamai, ko domin ya jawo hankulan mutane zuwa ga kansa, to kuwa yana wuta)**.

A cikin waɗannan ɗabi'u da ladubba akwai: **Ƙasƙantar da kai "Tawali'u"**, Imam Malik ya rubuta wasiƙa zuwa ga Halifa Rashid cewa: **"Idan ka koyi ilimi, to ya kamata a ga tasirinsa a**

**tare da kai, ta wajen ilimi, da natsuwa, da shiru, da kwarjini"**; domin sam ilimi da girman kai ba za su taɓa yin inuwa ɗaya ba, ba kuma a bayar da ilimi idan ana saɓon Allah, kawai ana samun ilimi ne idan aka neme shi, yana kuma ƙaruwa ne da tsoron Allah, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku ji tsoron Allah, sai Allah ya ba ku ilimi, lallai Allah mai cikakkiyar masaniya ne akan komai)) [al- Baƙra: 282]**, da ma dai can ana cewa: **"Wanda ya yi aiki da abin da ya sani, Allah zai sanar da shi ilimi abin da bai sani ba"**, lallai aiki sharaɗi ne na samun ilimin ladunni, inda Maɗaukakin Sarki yake bayani akan bawa na gari a cikin suratul Kahfi, Allah mai girma yana cewa: **((Sai suka sami wani bawa daga cikin bayinmu da muka ba shi rahama daga wurinmu, muka sanar da shi ilimi daga gare mu)) [al- Kahfi: 65]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Sai muka fahimtar da Annabi Sulaiman (AlaiHis Salam) wannan hukunci, dukansu (Sulaiman da Dawud) mun ba su Annabta da ilimi)) [al- Anbiya'i: 79]**, game da Annabi Yahya (AlaiHis Salam) Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Ya Yahya, ka riƙe littafin da muka ba ka da ƙarfi, lallai mun ba shi Annabta tun yana ƙarami, haka ma mun ba shi haƙuri da sauƙin kai, gami da tsarki daga wurinmu, da ma can shi mai tsoron Allah ne)) [Maryam: 12 – 13]**, haka ma mai girma da ɗaukaka ya faɗi ta bakin mala'iku cewa: **((Mun ambaci tsarkinka ya Ubangiji, lallai ba mu da wani ilimi, sai abin da ka sanar da mu)) [al- Baƙra: 32]**.

A cikin waɗannan ɗabi'u da ladubba akwai: **Yin ado da ɗabi'ar natsuwa**, ganin cewa ilimi yana da ƙawa, da kwarjini, da girmansa, a cikin alamun da suke nuna haka akwai: shiga mai kyau, da tsabta, da sanya turare, da kuma nesantar

wuraren ƙaranta, da inda ake maganganun banza, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai nagartacciyar shiriya, da nagartaccen shiru da kamewa, da yin komai daidai gwargwado, kaso ɗaya ne cikin kaso ashirin da biyar na Annabta)**.

Malami a wurin mai tambaya tamkar likita ne a wurin mara lafiya, dole ne ya sauƙaƙa masa, ya kuma yi riƙo da hannayensa zuwa ga tundun shiriya, da hanyoyin da su ne daidai, An ruwaito Hadisi daga Mu'awiyya Bn al-Hakam, ya ce: wani lokaci ina sallah a bayan Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai wani daga cikin mutane ya yi atishawa, sai na ce masa: "YarhamukalLah", sai mutane suka yi mini ƙuri da idanuwansu, sai na ce: ikon Allah, me kuma na yi da kuke kallo na? sai suka koma dukan cinyoyinsu da hannuwansu; da nufin in yi shiru, da na ga suna ƙoƙarin sanya ni in yi shiru, sai na yi shiru, lokacin da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya gama sallah –iyaye na biyu fansa ne a gare shi- wallahi ban taɓa ganin malami kafin shi, da bayan shi da ya kai shi iya koyarwa ba, bai ƙyare ni ba, bai kuma doke ni ba, bai kuma zage ni ba..

Haka ma akwai wasu al'amurra da ya zama wajibi ɗalibin ilimi ya sifantu da su, manya daga cikinsu akwai:

* **Ƙwaɗayin neman ilimi, da naciya akansa ba tare da gazawa ko ƙosawa ba**, kada ya ɓata lokaci akan abin da ba zai yi amfani ba, da ma an ce: **shi ilimi ba zai ba ka wani sashe na shi ba sai idan ka ba shi dukanka,** lokacin da aka tambayi Imam as- Shafi'iy (Allah ya ƙara masa rahama) akan: yaya ƙwaɗayinka da ilimi yake? Sai ya ce: nakan ji kalmar da ban taɓa ji ba, sai gaɓoɓi na su yi burin ina ma dukansu suna da

kunnuwa domin su ji irin daɗin da kunne yake ji, sai aka ce masa: yaya kake ka haba - haba da shi? Sai ya ce: irin haba – habar mai tara dukiya, ga kuma rowa yake yi idan ya sami kuɗi, sai aka ce masa: yaya kuma kake nemansa? Sai ya ce: irin neman da mace take yi wa ɗanta ɗaya tilo da ba ta da waninsa da ya ɓace..

* **Girmama malami da ganin mutuncinsa,** kada ɗalibi ya yi wa malami maganar da ba ta dace ba, ko ya aikata masa wani abu da bai kamata ba, Imam as- Shafi'iy (Allah ya ƙara masa rahama) ya ce: Nakan buɗe shafin takarda a gaban Imam Malik (Allah ya ƙara masa rahama) cikin sauƙi saboda kwarjininsa; gudun kada ya ji hayaniyarta, Imam Ar- Rabi' (Allah ya ƙara masa rahama) ya ce: wallahi ban taɓa ƙumajin in sha ruwa Imam as- Shafi'iya yana kallo na ba; saboda kwarjininsa, alhairin Allah ya kai zuwa ga Ahmad Shauƙiy da yake cewa:

"Ka miƙe wa malami, ka girmama shi kaman yanda ya kamata, domin ya kusa ya zama Manzo.."

Babu shakka muna matuƙar buƙatar samun dukan ilmomin da za mu raya rayuwarmu ta duniya, kaman yanda muke matuƙar buƙatar ilmomin da za mu daidaita al'amarin addininmu, ba mu da lokacin da ba ma buƙata, domin bincike na ilimi a fannin samar da sababbin abubuwa da ƙere - ƙere a yau ya zama wajibi, ko za mu samu mu riski tarago, ko mu riski wani sashe na abubuwan da suka yi mana nisa, saboda haka, dole ne kowannenmu ya sifantu da ruhin kawo cigaba, da na rige – rige, da hangen nesa, ko alal aƙalla, ya zamo muna da burin mayar da al'ummarmu zuwa zamanin manya, wato iyayenmu, da kakanninmu da suka yi ƙaura domin neman ilimi, suka kuma yi ƙoƙari wajen samar da shi, har suka kai

ƙololuwarsa, suka zamo jigogi a cikin dukan ilmomin da suka shiga cikinsa, wanda a ƙarshe ya zamo tamkar tsabtacciyar maɓuɓɓuga, kuma mahanga da ya haskaka wa ɗaukacin al'ummomin da suka zo a bayansu, ya zamo takenmu a koda yaushe shi ne:

"Muna gini ne kaman yanda iyayenmu suka yi gini, muna kuma aikata irin abin da suka aikata."

Dole ne malami da ɗalibi su sifantu da kyawawan ɗabi'u, ta yanda ayyukansu za su yi daidai da abubuwan da suke faɗi, muddin ana buƙatar hakan ya yi tasiri a cikin al'umma, lallai lokacin da al'umma da haɗe tsakanin ilimi, da aiki, da nagarta a ɗabi'u, sai ta rayu cikin izza da ɗaukaka a tsakanin al'ummomi, duk inda aka sami haɗuwar kyawawan ɗabi'u, da ilimi, to cigaba da haɓakar tattalin arziki yana nan a wurin..

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabinmu Muhammadu, da Alayensa da Sahabbansa, da waɗanda suka bi tafarki irin tasu har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai addinin Musulunci ya ɗaukaka darajar ilimi, da masu ilimi a dukan ɓangarori, shi ilimi mai amfani ya ƙunshi dukan ilmomin da suke amfanar mutane a cikin al'amurransu na addini, da na duniya, saboda haka ne muke gani maganar Allah Maɗaukakin Sarki da take cewa: **((Lallai masu tsoron Allah a cikin bayinsa su ne malamai))** **[Fatir: 28]** ta zo ne a lokacin da ake magana akan

ilmomin duniya, a inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Ya kai mai hankali, shin ba ka ga cewa Allah ya saukar da ruwa daga sama, kuma shi ne Allah ya fitar da kayan amfanin gona masu mabambanta launuka, akwai: ja, da fatsi - fatsi, da mai daɗi da mai ɗaci, da mai tsarki da mai muni, haka a cikin duwatsu akwai wanda yake da hanyoyi da layuka farare, da baƙaƙe da suka saɓa da juna wajen tsanani ko rauni.. A cikin mutane, da dabbobi, da raƙuma, da shanaye, da tumakai, ma ga su nan mabambanta launuka a wajen sifa da girma da launi, babu masu yin tunani na tadabburi a cikin wannan abu na ban mamaki, masu kuma jin tsoron mahaliccinsu sai malamai da suke iya riskar sirrorin da suke cikin waɗannan halittu, lallai Allah mai rinjaye ne da muminai suke tsoronsa, mai kuma yawan ƙanƙare zunuban waɗanda suka koma zuwa gare shi ne)) [Fatir: 27 -28]**, da inda Allah mai girma yake faɗi: **((Lallai a cikin halittar da Allah ya yi wa sammai da ƙasa, da abubuwan da suke cikin su na ƙwarewa da gwaninta, da saɓanin da dare da rana suke da shi, na haske da duhu, tsawo da gajerta, akwai bayyanannun ayoyin ga masu hakalin da suke iya riskar kaɗaitakar Allah da ikonsa. Shi kuwa sha'anin masu hankali –a koda yaushe- shi ne su halarto da girman Allah da buwayansa cikin zukatansu, a kuma duk inda suke, shin suna tsaye ne, ko a zaune, ko a kwance, suna tunani akan halittar sammai da ƙasa, da abubuwan da suke cikin su na ban mamaki..)) [Ali Imran: 190 -191].**

Haka ma abin da ake nufi da ilimi mai amfani shi ne duk wanda yake amfanar mutane a rayuwarsu ta duniya, da ta lahira, a cikin ilmomin Shari'a, ko na harshen Larabci, ko ilimin likitanci, da na harhaɗa magunguna, ko kimiyya da fasaha, ko

ilimin taurari, da na ƙere - ƙere, ko na makamashi da sauran ilmomi, shi ilimi shi ne ginshiƙin gina ɗan kishin ƙasa mai kawo cigaba, da haɓaka rayuwa, dalilin haka kuwa shi ne maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **((Ku tambayi masana idan har ba ku sani ba...))** **[an- Nahl: 43; al- Anbiya'i: 7]** kalmar "zikiri" a nan tafi ƙarfin a taƙaita ta da wani ilimi banda saura, abin yana da faɗin da ya ƙunshi duk wani ilimi mai amfani, babu shakka muna matuƙar buƙatar dukan ilmomin da za mu raya duniyarmu, kaman yanda muke buƙatar ilmomin da za mu daidaita al'amarin addininmu da su..

Ta yiwu abin da ya fi zama wajibi akan malamai a wannan zamanin shi ne su tsaya tuƙuru wajen gyara munanan fahimtar da aka yi wa addini, da gyara gurɓataccen fahimtar da aka yi wa Musulunci da Musulmai, da kuma aiki tuƙuru wajen yaɗa nagartaccen fahimta da tunani na Musulinci.. Muna roƙon Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya mu zamo cikin masu kawo wannan gyarar, ya kuma sanar da mu abubuwan da ba mu sani ba, ya kuma tuna mana abubuwan da muka manta, ya kuma datar da mu a cikin komai..

- 16 –

## AL'UMMAR IƘRA'.. AL'UMMAR KYAUTATA AIKI:

## TSAKANIN MALAMAN AL'UMMA DA MALAMAN FITINA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka ce masu: shin waɗanda suka sani za su yi daidai da waɗanda ba su sani ba?! lallai masu hankali ne kawai suke hankalta)) [az- Zumar: 9]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Lallai addinin Musulunci ya kwaɗaitar akan a nemi ilimi, ya kuma zaburar da mutane akan nuna ƙwazo da bajinta wajen nemansa, babu abin da ya fi tabbatar da haka sama da kasancewar farkon abin da ya sauka na Alƙur'ani mai girma shi ne maganar da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Ya Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa sallam), ka karanta abin da aka yi maka wahayi, kana buɗe karatun naka da sunan Ubangijinka da shi kaɗai ne kawai yake da ikon halitta. Ya samar da ɗan Adam ɗin da yake da cikakken jiki da ilimi ne daga gudan jini. Ka cigaba da karatu, lallai Ubangijinka mai yawan karamci yana ganin girma da**

**darajarka, ba zai taɓa taɓar da kai ba. Shi ne ya sanar da ɗan Adam yadda zai yi rubutu da alƙalami, a da bai san haka ba. Ya sanar da ɗan adam abin da bai taɓa ko hararo su a zuciyarsa ba))** **[al- Alaƙ: 1 -5]**; farkon umurnin da wahayi ya zo da shi daga Allah shi ne: umurni da a yi karatu, wanda shi ne farkon ƙofar ilimi, sannan bayan haka kuma, aka yi nuni zuwa ga alƙalami, wanda shi ne hanyar rubuta ilimi, da naƙaltarsa, wannan wata faɗakarwa ce ga ɗaukacin mutane akan bayanin falalar ilimi, da kwaɗaitarwa zuwa ga nemansa, da kuma zaburar da al'umma zuwa gare shi, kuma wannan bayyananniyar ishara ce akan cewa addinin Musulunci addini ne na ilimi da sani, kuma wannan al'umma, al'umma ce ta ilimi da samar da cigaba.

Haka ma an kira sura kacaukan a cikin Alƙur'ani mai girma da sunan "al-Ƙalam", Ubangiji mai girma da buwaya ya fare ta da cewa: **((Nún: Baƙi ne cikin babbaƙun Larabci da wasu surorin Alƙur'ãni Mai girma suka fara da su; domin ƙalubalantar masu ƙaryatawa da kuma faɗakar da masu gasgatawa. Ina rantsuwa da alƙalamin da mala'iku da wasunsu suke rubutu da shi, da abin da ma suke rubutawa na alhairi da abubuwa masu amfani))** **[al- Ƙalam: 1]**; saboda ƙarfafa muhimmancin kayan da ake amfani da su wajen neman ilimi, da hanyoyin da ake bi a same shi, darajar ilimi ta kai daraja a ce Allah Maɗaukakin Sarki bai umurci Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) da ya nemi ƙarin wani abu a duniya ba, sai ilimi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka ce: Ya Ubangiji ka ƙara mini ilimi))** **[Taha: 114]**; hasali ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya fita zuwa neman ilimi a matsayi ɗaya da fita

zuwa ga ɗaukaka kalmar Allah, ya kuma bayyana cewa nuna ƙwazo wajen nemansa dalili ne daga cikin dalilan shiga aljanna, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda ya fita domin neman ilimi, to yana kan hanyar Allah ne har sai ya dawo)**, a wani wuri kuma yana cewa: **(Duk wanda ya bi hanyar neman ilimi, to kuwa Allah Maɗaukakin Sarki zai sauƙaƙe masa hanyar zuwa aljanna)**, lallai ilimi ginshiƙi ne daga cikin ginshiƙan gina ƙasashe, da shi ne al'umma take farkawa, ta kuma cigaba, da shi ne ɗan Adam yake samun matsayi, da ƙololuwar daraja.

Lallai Alƙur'ani mai girma ya girmama matsayin malamai –kowa a fagensa-, Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki yana ɗaukaka darajar muminai masu tsarkake shi a wurin bauta, da waɗanda aka ba su ilimi, duka Allah yana ɗaukaka darajarsu, Allah yana da cikakkiyar masaniya akan abin da kuke aikatawa)) [al- Mujadala: 11]**, kaman yanda a wani wurin kuma Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa malamai shaidar tsoronsa, Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai masu tsoron Allah a cikin bayinsa su ne malamai, lallai Allah mabuwayi ne mai kuma yawan gafara)) [Fatir: 28],** saboda girman darajarsu, da matsayinsu ne Allah Maɗaukakin Sarki ya girmama su da yin shaida akan mafi girman abin da ake yi wa shaida, Allah mai girma yana cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki ya shaida cewa lallai shi ne wanda ya kaɗaita da Allantaka, ya kuma bayyana haka –ta hanyar abubuwan da ya yaɗa a cikin halittu masu ɗauke da dalilai gami da ayoyin da mai hankali ba zai musanta su ba- cewa: shi kaɗai yake, ba shi da abokin tarayya, tsayayye ne shi akan al'amurran halittun sa cikin adalci. Mala'ikunsa tsarkaka ma**

**sun tabbatar da haka, haka ma malamai sun san haka, sun kuma yi yaƙini da shi cewa, Allah Maɗaukakin Sarki shi ne ya kaɗaita da Allantakan da babu wani da zai yi galaba akansa cikin al'amurransa, hikimarsa kuma ta game komai)) [Ali Imran: 18].**

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya tabbatar da haka, hakan ya sanya ya bayyana malamai a matsayin magada Annabawa wajen shiryatar da mutane, da sanya su akan daidaitacciyar turba, da riƙo da hannayensu zuwa ga hanyar gaskiya da haske, da gyara, da kuma gina cigaba, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai malamai magada Annabawa ne; su dai Annabawa ba su gadar da dinarai, da dirhamai ba, ilimi kawai suka gadar, duk wanda ya yi riƙo da shi, to kuwa lallai ya riƙi babban rabo)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai falalar malami akan mai bauta, kaman falalar wata ɗan daren sha huɗu ne akan sauran taurari)**.

Babu shakka malaman da Allah mai girma da ɗaukaka ya girmama sha'aninsu, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) kuma ya yabe su, su ne malaman al'umma na gaskiya, waɗanda suka san girman amanar da suke ɗauke da ita, wato amanar ilimi, da amanar kira zuwa ga Allah, da amanar bayani, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ya Allah ka haskaka fuskar mutumin da ya ji maganata, ya kuma kiyaye ta, sannan ya isar zuwa ga waninsa kaman yanda ya ta..)**, lallai malaman al'umma su ne suka fahimci ɗabi'ar wannan aiki da Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓe dominsa, ba aikin neman abinci da ilimi ko da addini ba ne, saƙon da suke isarwa ya fi ƙarfin haka nesa ba kusa ba, Allah Maɗaukakin

Sarki yana faɗi ta bakin shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka ce masu: Ban fa tambaye ku wani lada ba, wannan saƙo naku ne, ni lada na yana wurin Allah, shi kuma mai shaida ne akan komai))** **[Saba'i: 47]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗi ta bakinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka ce masu: Bana fa tambayar ku wani lada ba, sai dai kawai wanda yake son ya kama hanyar Ubangijinsa da abin da yake gabatarwa na sadaka da sauransu))** **[al- Furƙan: 57]**, haka ma yana faɗi da bakin Annabawansa: Nuhu, da Hudu, da Saleh, da Luɗu, da Shu'aib (Alaihimus Salam) cewa: **((Bana fa tambayar ku wani lada ba, lada na kawai yana wurin Ubangijin talikai ne))** **[as- Shu'ara'i: 109, 127, 145, 164, 180]**, duka siga ɗaya ce da take tabbatar da manufa ɗaya, da manhaji ɗaya, da kuma gaskiyar niyya tare da Allah Maɗaukakin Sarki, da kuma cikakken yi masa ikhlasi shi kaɗai.

Lallai malaman al'umma na gaskiya su ne waɗanda suka bayar da lokacinsu, da ƙoƙarinsu, da ayyukansu wajen hidimta wa addininsu, da ƙasarsu, suka sanya mutane akan manhajin daidaito "al-Wasaɗiyya", da rangwame, da tausayi, kiransu zuwa ga Allah ya yi sanadiyyar samar da al'umma mai amfani, al'ummar da take ginawa, ba mai rusawa ba, mai raya ƙasa, ba mai lalatawa ba, al'ummar da take mutunta kyawawan ɗabi'un ɗan Adam, take kuma girmama karamarsa, take rayuwa da ɗaukacin mutane cikin zaman lafiya, da aminci, da tsaro, da kwanciyar hankali, wannan kam shi ne ilimi mai amfani da zai zamo taska ga mai shi bayan wafatinsa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idan mutum ya rasu,**

**gaba ɗayan ayyukansa sukan tsaya in banda guda uku: sadaka mai cigaba da amfanar al'umma, ko ilimin da ake amfana da shi, ko ɗa na kirki da zai riƙa yi masa addu'a)**, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan nemi tsarin Allah akan ilimin da ba shi da amfani, ilimin da ba ya ginawa, ba kuma ya raya ƙasa, ba kuma ya saita ɗabi'u, da tsarin rayuwa, saboda haka ne (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan ce: **(Ku roƙi Allah ilimi mai amfani, ku kuma nemi tsarinsa akan ilimin da ba shi da amfani)**, a cikin addu'o'insa (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan ce: **(Ya Allah Ubangiji ina neman tsarinka akan ilimin da ba shi da amfani, da zuciyar da ba ta tsoron Allah, da ran da ba ya ƙoshi, da addu'ar da ba a amsa)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa baki ɗaya, da duk waɗanda suka bi shi da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai malaman al'umma na gaskiya su ne ma'abota nagartacciyar shiriya, masu shiru mai alfanu, masu daidaito da rashin ɓata lokaci, waɗanda suke ɗauke da tutar "al-Wasaɗiyya" a kowane zamani, **suna masu kore wa addinin Allah ƙarairayin masu wuce gona da iri, da tawilin jahilai, da kutsen maɓarnata**.

Su kuwa malaman fitina da suka ɗauki addinin Allah a matsayin matakala ta biyan buƙatun kawunansu, da cimma manufofinsu, waɗannan kam su ne waɗanda suka kutsa cikin addinin Allah ba tare da shayi ba, suka yi ta fitar da fatawowin marasa amfani da suke cutar da al'umma, suke kuma rarraba kawunan jama'a, ba haɗa kawunansu ba, suke kuma rusa al'umma, ba gina su ba, suke buɗe wa al'umma ƙofar kafirta juna, wanda addinin Musulunci ya tsoratar da al'umma game da bi ta ciknta, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk mutumin da ya ce wa ɗan uwansa: kafiri, to ɗaya daga cikinsu ya zama, idan wanda aka faɗa masa haka yake, shi kenan, idan kuma ba haka yake ba, za ta dawo kan wanda ya faɗa)**.

Lallai manhajin malaman fitina shi ne tsanani, da tashin hankali, da ƙuntata wa mutane; kuma wannan manhaji ne da ya yi hannun - riga da rangwamen Musulunci, da daidaitonsa "al-Wasaɗiyya", lallai addinin Musulunci ya ɗauke wa mutane dukan damuwa, ya kuma yaye masu dukan wahala, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki bai sanya maku damuwa a cikin addini ba..))** **[al- Hajji: 78]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ku yi wa mutane albishir, kada ku kuskura ku aikata abin da zai nesanta su, ku sauƙaƙa, kada ku tsananta)**, lallai tsanantawa a wajen bayar da fatawa ya saɓa da daidaito, gami da "al-Wasaɗiyya", waɗanda su ne sifofin da suka bambanta addinin Musulunci -mai daraja- da sauran addinai, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kaman haka ne ma mukan sanya kuka zamo madaidaiciyar al'umma; saboda ku zamo shaidu ga sauran mutane..))** **[al- Baƙra: 143]**, ita kalmar "al-Wasaɗiyya" tana

nufin: adalci, da daidaito, da nesantar wuce gona da iri, wanda shi ne sababin halakar al'ummomi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ya ku mutane, ahir ɗinku da wuce gona da iri a cikin al'amurran addini, domin lallai abin da ya halakar da waɗanda suka gabace ku shi ne wuce gona da iri a cikin al'amurran addini)**, Imam Sufyan as- Sauriy (Allah ya ƙara masa rahama) ya ce: Mu ilimi a wurinmu shi sauƙin da ya zo daga fahimta, shi kuwa tsanani ai kowa ma ya iya.."

A nan ma za a iya haɗe malaman fitina da malaman boge da suke magana ba tare da ilimi ba, ba su kuma faɗaka da buƙatar a ce al'umma ta yi matuƙar riƙo da sabubba ba, ba kuma su fahimci cewa raya doron ƙasa yana cikin muhimman manufofin addini ba, kuma sauran mutane ba za su taɓa mutunta addininmu ba, muddin ba mu yi nasara a cikin al'amurranmu na duniya ba, idan mun yi nasara akan al'amurran duniyarmu, sai mutane su girmama addininmu da duniyarmu, waɗanda ba su fahimci haka ba, sai suka karkatar da wa'azozinsu wajen yin gargaɗi game da duniya, abin da har ya kai ga mafi yawan mutane sun sami mummunar fahimta game da dangantakar duniya da addini, da kuma wajibcin yin riƙo da sabubba, suka yi wa zuhudu mummunar fahimta, akan wai ƙaurace wa rayuwa, suna masu kawar da kai akan maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **((Ya Ubangijinmu, ka ba mu kyakkyawan rayuwa a nan duniya, a lahira ma ka ba mu kyakkyawar makoma, ka kiyaye mu ga barin azabar wuta)) [al-Baƙra: 201].**

Lallai muna ƙara tabbatar da cewa kutsawa cikin bayar da fatawa ba tare da cancanta ta ilimi ba ɓata ce bayyananniya,

mene ya kai girma, da yawan cutar da bayar da fatawa ba tare da ilimi ba ta jawo wa al'umma, an ruwaitoo Hadisi daga Sayyiduna Jabir Bn Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da su), ya ce: Mun fita wata tafiya, sai dutse ya sami ɗaya daga cikinmu, kansa ya fashe, sannan kuma ya yi mafarki, ya tambayi abokan tafiyarsa: shin ina da daman in yi taimama kuwa? Sai suka ce: ai ba ka da wani sauƙi, muddin kana da ikon taɓa ruwa, sai kuwa ya yi wanka, a sakamakon haka sai ya rasu, lokacin da muka dawo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai aka ba shi labarin abin da ya faru, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Sun kashe shi, Allah wadaransu, ina ma da sun tambaya tun da ba su sani ba, ai maganin jahilci shi ne tambaya, ya ishe shi ya yi taimama, yana mai rufe wajen mikin da ƙyalle, sannan ya shafe shi, sannan ya wanke sauran jikinsa)**.

Lallai muna matuƙar buƙatar a ce kowa daga cikinmu ya tsaya a fagensa, yana mai himma cikin abin da ya iya, saboda tsoron Allah Maɗaukakin Sarki, da kuma girmama ilimi, da kuma girmama hatsarin da yake tattare da kalma, domin da sau da yawa kalma ɗaya tak da mutum zai furta –ba tare da ilimi ba- takan zama sanadin rusa abubuwa da lalata su, da ɓarna a bayan ƙasa, shiru ya fi alhairi akan maganar da cutarwa take yi, ba amfanarwa ba, da a ce wanda bai sani ba zai yi shiru, da kuwa an kawo ƙarshen saɓani, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(.. Duk wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya faɗi alhairi ko kuma ya yi shiru..)**

**Ya Allah Ubangiji ka nuna mana gaskiya, ka kuma ba mu ikon binta, ka kuma nuna mana ƙarya, ka ba mu ikon nesantarta, ka sanar da mu abin da zai amfane mu, ka kuma**

**amfane mu da abin da ka sanar da mu, ka ƙara mana ilimi, ka kiyaye ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya.**

## - 17-

## NA'UYI DA ALHAKIN DA ALLAH YA ƊAURA AKAN BAYI (MAS'ULIYYA)

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Lallai mun bijirar da amanar taklifi zuwa ga sammai, da ƙasa, da duwastu, duka suka ƙi ɗauka, suka kuma ji tsoron wannan amanar, sai ɗan Adam ne kawai ya ɗauka, da ma can shi mai yawan zaluntar kansa ne, da bai san abin da zai iya da wanda ba zai iya ba))** **[al- Ahzab: 72]**.. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya karrama ɗan Adam, inda ya halicce shi da ikonsa, sannan ya sanya masa ruhinsa, ya kuma umurci mala'ikunsa da su yi masa sujada, ya kuma fifita shi akan halittunsa da abubuwa masu yawa, cikin waɗannan abubuwan akwai: ɗaura masa taklifi na shari'a da ya yi, babu wani mutum da Allah ya mallaka masa hankali, face akwai alhakin da ya rataya a wuyarsa, haka ma akwai matsayin da ya ba shi a rayuwar zamantakewa, kowane mutum yana ɗaukan

wani sashe na alhaki a cikin rayuwa gwargwadon iko, da kuma irin nauyin da Allah ya ɗaura masa.

Babu shakka mas'uliyya "nauyi" da Allah yake ɗaura wa bayi, alhaki ne da yake a wuyansu, kafin ya zamo wani girma ko matsayi, duk mai yi wa irin wannan nauyin kallon wani matsayi, ko girma ne aka ba shi, yana mai neman shugabanci ta kowace irin hanya, to kuwa a mafi yawan lokaci, shi ne wanda santsin shugabanci yake jansa zuwa ga kwazazzabai da ramukan da suke cike da hatsari, duk kuma wanda ya ɗauki hakan a matsayin alhaki da nauyi, ko a matsayin aiki da aka ɗaura masa, to kuwa lallai zai sami taimako daga wurin Allah Maɗaukakin Sarki wajen sauke wannan nauyi da yake a wuyarsa, saboda haka ne, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake ce wa Sayyiduna Abdurrahman Bn Samra: **(Ya Abdurrahman, Kada ka kuskura ka nemi shugabanci; domin idan ba ka nema ba, aka ba ka, sai a taimake ka wajen sauke nauyin da yake tattare da shi, idan kuma sai da ka nema ne aka ba ka, sai a bar ka da wayonka),** an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuzarrin (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: Na ce: Ya Manzon Allah, ba ka ba ni shugabanci ba? ya ce: sai ya dafa kafaɗa ta, sannan ya ce: **(Ya Abuzarrin, ka san kai mutum ne mai rauni, shi kuma shugabanci amana ne, a ranar alƙiyama kuma ƙasƙanci ne da nadama, sai dai kawai ga wanda ya amshe shi bayan cancanta, ya kuma sauke nauyin da yake a kansa).**

Ɗaukan nauyi yana da surori iri- iri, a ciki akwai: **Ɗaukan nauyin gida "iyali"**: Lallai gida yana da muhimmiyar rawar da yake takawa, wajen samun kwanciyar hankali, da haɗin kan al'umma, gida ne harsashen farko na gina al'umma, shi ne

kuma wuri na farko na bai wa al'umma kariya, lallai Allah zai tambayi iyaye biyu ne akan alhakin da ya ɗaura masu na gina iyali, da kuma samar da natsuwa da kwanciyar hankali a cikinsu, ta hanyar sauke nauyin da ya rataya a wuyansu, da haƙƙoƙin da suke a kansu.

Lallai addinin Musulunci ya bayyana waɗannan wajibai da haƙƙoƙin, ya kuma rarraba su tsakanin mutanen da suka cikin gida, kowa da abin da yake a kansa, a inda Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Dukanku masu kulawa ne, kuma kowa za a tambaye shi akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi: Shugaba mai kulawa ne, za kuma a tambaye shi akan waɗanda yake shugabanta, namiji ma mai kulawa ne a cikin iyalansa, za kuma a tambaye shi akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi, mace ma mai kulawa ce a gidan mijinta, za kuma a tambaye ta akan nauyin da aka ɗaura mata na kulawa, hadimi ma mai kulawa ne da dukiyar uban gidansa, za kuma a tambaye shi akan nauyin da aka ɗaura masa alhakin kulawa da shi, dukan ku masu kulawa ne, za kuma a tambayi kowa a akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi),** nasarar gida, da samun kwanciyar hankali a cikinsa ya dogara ne akan kiyaye waɗannan wajibai, da haƙƙoƙi tsakanin mutanen da suke cikinsa, da rashin yi masu riƙon- sakainar - kashi, ko wuce - gona - da - iri.

Saboda haka, alhakin da ya rataya akan mutanen gida, alhaki ne da suke cika junansu, haƙƙoƙi ne da wajibai, da girmama juna, ta yanda kowa daga cikinsu zai sauke nauyin da yake a kansa cikin soyayya da amana, duk wanda ya yi wa haƙƙoƙi da wajibai riƙon sakwa- sakwa, to kuwa Allah

Maɗaukakin Sarki zai tambaye shi akan: shin ya kiyaye su, ko kuwa ya tozartar da su? Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah zai tambayi kowane mai kiwo akan abin da aka ba shi kiwon, shin ya kiyaye shi ne, ko kuwa ya tozartar da shi, kai har sai an tambayi mutum akan iyalan gidansa),** haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai zunubi ya kai zunubi, a ce mutum ya tozartar da wanda yake ɗaukan nauyinsa).**

A cikin irin wannan nauyin akwai: **alhakin da yake tattare da aikin da mutum yake yi**: lallai al'amarin alhaki, ko nauyi yana ƙara girma ne daidai da nauyin da yake akan mutum, duk sanda wannan alhakin ya faɗaɗa, sai sifofin da ake buƙata su ƙara girma, irinsu: cancanta, da isarwa, da ƙwarewa, da amana, da kuma ikon gabatar da dukan abubuwan da irin wannan matsayin yake buƙata; ta yadda mutum zai yi wa kansa hisabi da kansa, mutane ma su tambaye shi, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya tambaye shi akan abin da ya ɗaura masa na nauyi, Annabinmu (SallaLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu wani mutum da za a ba shi shugabancin mutane goma zuwa sama, face an zo da shi filin tashin alƙiyama, hannayensa a ɗaure da wuyarsa, adalcinsa ne zai kwance shi, ko kuma zaluncinsa ya halaka shi).**

Kaman yanda ya kamata ga duk wani da zai shugabanci mutane, ko wanda aka ba shi wani aiki, ya sani cewa lallai an ba shi umurnin kyautata aikin da aka ɗaura masa, ya kuma sanya tsoron Allah Maɗaukakin sarki a ciki, dole ne ya sani cewa yana ta'amuli ne da dukiyar al'umma, saboda haka ya yi abin da ya dace da aikin da yake akansa, kada ya kuskura ya ci

- hanci da rashawa, ko ya kutsa cikin abin da ya haramta a gare shi, koda kuwa da wani irin suna ake kiran yin hakan.

A nan muke ƙara ƙarfafa cewa: sam bai kamata ga shugaba ya zamo ya dogara akan wasu, ba tare da bibiya na diƙin- diƙin a dukan ɓangarorin ayyukan da suke ƙarsashinsa ba, komin yanda yake kallon ƙanƙancin aiki da sauƙinsa; domin nuna halin - ko - in - kula a abubuwan da wasu suke zaton cewa ƙanana ne, shi ne yake sanadiyyar faruwar ɓarna da cutarwa masu yawa, dole ne mu fahimci cewa amincewa da mutune ba ya nufin rashin bibiya, bibiyar ayyuka kuma ba ya nufin rashin amincewa.

Haka ma dole ne kowane shugaba ya zaɓi mataimaka amintattu, masu juriya da za su taimaka masa, ya zaɓi waɗanda suka cancanta, yana mai gabatar da wanda ya fi dacewa, duk wanda ya bai wa wani mutum wani nauyi a cikin al'umma, alhalin a cikinsu akwai wanda ya fi shi cancanta da wannan muƙami, ko aikin; to kuwa babu shakka ya ha'inci Allah da Manzonsa, ya kuma ha'inci ƙasa, ya kuma ha'inci amanar da aka ɗaura masa.

Haka ma a cikin surorin ɗaukan nauyi akwai: **ɗaukan nauyi da alhakin al'umma:** Lallai addinin Musulunci ya sanya wasu ƙa'idodji na rayuwar zamantakewa, da mutane suke rayuwa a ƙarƙashinsu cikin wani yanayi, na kwanciyar hankali, inda soyayya, da girmama juna, da kuma taimakon juna tsakanin masu hannu da shuni da marasa shi suke yi wa irin wannan rayuwa inuwa, duka a ƙarƙashin daidaito da yake a tsakanin bil'adama baki ɗaya, da haka sai al'umma ta zamo tamkar jiki ne guda ɗaya.

Mai lura da rayuwar mutane a yau, zai ga cewa a cikinsu akwai talakan da ba shi da abin da zai kawar da yunwar da take damunsa, akwai kuma mara lafiyar da ba shi da ikon saya wa kansa magani, ga kuma zawarawa, da marayu masu rauni, da kuma waɗanda ba su da wanda yake ɗaukan ɗawainiyarsu, lallai biya wa waɗannan buƙatunsu da maslahohinsu, alhaki ne da ya rataya a wuyan al'umma, da shari'a, da gwamnati, hasali ma wannan yana cikin abin da ake kira "Fardhu kifaya", wanda idan wasu suka gabatar, sun sauke wa saura nauyin, idan kuma ba a sami wanda ya ɗauka ba, sai ɗaukacin al'umma ta zamo ta aikata zunubi, saboda haka ne, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Duk wanda ya kwana a ƙoshe, alhali maƙwabcinsa na gefensa ya kwana da yunwa, yana kuma sane da haka, to lallai bai yi imani da ni ba).**

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa salla) ya girmama sauke wannan nauyi na rayuwar zamantakewa, inda ya bayyana cewa: biya wa mutane buƙatunsu shi ne yake gaba da i'itikafi a cikin Masallacinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), an ruwaito Hadisi daga Abu Sa'idul Khudriy (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Wata rana muna halin tafiya tare da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai wani mutum ya zo akan abin hawansa, sai ya fara jujjuyawa dama da hauni, yana kallon ko'ina, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda yake da abin hawa bayan abin hawansa, to ya bayar da shi ga wanda ba shi da abin hawa, haka ma duk wanda yake da guzuri da ya wuce buƙatarsa, to ya taimaka wa wanda ba shi da guzuri),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai mutumin da Allah Maɗaukakin Sarki ya fi sonsa shi ne wanda ya fi amfanar mutane, kuma mafi alhairin aiki a wurin**

**Allah Maɗaukakin Sarki shi ne: farin cikin da ka shigar a cikin zuciyar Musulmi, ko ka yaye masa damuwa, ko ka biya masa bashin da ake binsa, ko ka kori yunwar da take damunsa, na rantse da Allah, in tafi biya wa ɗan uwana wata buƙata tasa, ya fi alhairi akan in yi i'itikafi a cikin wannan Masallacin –yana nufin Masallacin Madina- na tsawon wata ɗaya.. duk wanda ya tafi tare da ɗan uwansa akan wata buƙata tasa, har buƙatar ta biya, to kuwa lallai Allah zai tabbatar da diga- digansa a ranar da ƙafafuwa suke zamewa).**

Lallai (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana matuƙar kwaɗayin bibiyar sahabbansa wajen biya wa mutane buƙatunsu, da kuma tsayawa akan sai sun isa zuwa ga maslahohinsu, yakan yi tambaya domin ya san wanda ya aikata irin haka, da masu yin koyi da haka, wata rana Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wane ne a cikinku ya wayi gari da azumi?)**, sai Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Ni ne, sai ya ce: **(Wane ne a cikinku yau ya raka janaza?),** sai Sayiduna Abubakar ya ce: Ni ne, sai ya ce: **(wane ne a cikinku yau ya ciyar da miskini?)** sai Sayyiduna Abubakar ya ce: Ni ne, sai ya ce: **(wane ne a cikinku ya tafi gaishe da mara lafiya a yau?)** Sayyiduna Abubakar ya ce: Ni ne, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Waɗannan ɗabi'u ba su taɓa tattaru a tare ga mutum ba, face ya shiga aljanna).**

Haka ma a cikin sururin ɗaukan nauyi akwai: **alhaki, ko haƙƙoƙin ƙasa**: lallai ƙasarmu tana da haƙƙoƙi akanmu, akwai nauyin ta mai girma da ya rataya a wuyanmu; wajen ba ta kariya, da yin aiki tuƙuru wajen ɗaukaka darajarta, da cigabanta, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya raini Sahabbansa akan cewa: sadaukar da kai, da dukiyoyi, wajen

kiyaye hurumin ƙasashe da wuraren ibada jahadi fisabililLahi ne; babban abin da yake nuna haka shi ne, irin yanda Allah Maɗaukakin Sarki ya ɗaukaka darajar waɗanda suka bayar da rayuwarsu wajen kare addininsu da ƙasarsu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai Allah ya sayi rayukan muminai, da dukiyoyinsu daga gare su, akan lallai zai ba su aljanna, suna yaƙar waɗanda suka auka masu da yaƙi fisabililLahi, su kashe, a kuma kashe su, lallai Allah ya yi masu alƙawari na gaskiya a cikin littattafan Attaura da Injila da Alƙur'ani..)) [at-Tauba: 111]**

Haka ma a cikin alhaki, ko haƙƙoƙin ƙasa da suke akanmu akwai, yin aiki domin raya ƙasar, da ɗaukaka darajarta da cigabanta, wajen fifita maslahar al'umma akan maslahar mutum shi ɗaya, da haɗa ƙarfi da ƙarfe, da gusar da saɓani na rikici, da rashin kawo rabuwar kawuna, ta yanda gaba ɗayan al'umma za su zamo abu ɗaya, wajen zartar da umurnin Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **((Ku yi riƙo da igiyar Allah, kada ku soma ku rarraba..)) [Ali Imran: 103]**, da inda Allah Mai girma da ɗaukaka yake cewa: **((Kada ku soma ku yi rikici a tsakaninku, balle ku sami rashin nasara, kwarjininku kuma ya tafi a banza, ku yi haƙuri, lallai Allah yana tare da masu haƙuri)) [al- Anfal: 46].**

Dole ne mu sani cewa lallai akwai ranar da za a ce: **((Ku tsayar da su, lallai kam sai an tambaye su)) [as- Safat: 24]**, dole mu hararo maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **((Rana ce da za a bijiro da ku zuwa ga hisabi, babu wani sirri da kuke ɓoyewa da zai ɓuya daga gare ku)) [al- Haƙat: 18]**, shin sirrin ƙarami ne, ko babba; Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai kyakkyawan aiki, ko mummuna da mutum yake**

**aikatawa, koda ya zamo daidai da ƙwayar zarra ne saboda ƙanƙanta, ya kuma zamo an ɓoye shi a cikin zuciya, ko akan wani dutse, ko ma a ina ne a cikin sammai, da ƙasa, to kuwa lallai Allah zai bayyana shi, ya kuma yi hisabi akansa, lallai Allah mai luɗufi ne da babu wani abu da yake iya ɓuya masa, mai cikakkiyar masaniya ne akan haƙiƙanin komai)) [Luƙman: 16].**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

--------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa gaba ɗaya, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** 'Yan sa'o'i kaɗan ne suka rage mu tarbi wani lokacin mai cike da alhairai da albarka, lokacin gabatar da ayyukan biyayya, wato watan Sha'aban mai albarka, watan da a cikinsa ne ake bijirar da ayyuka zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki, saboda haka ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake keɓance shi da yawaita ibadu, da kuma ayyukan biyayya, da kusantar Allah mai tsarki, inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake yawaita yin azumi a cikinsa, abin da har ya jawo hankalin Sahabbansa (Allah ya ƙara yarda da su), suka tambaye sirrin wannan muhimmantawa da yake yi wa watan Sha'aban, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Usama

Bn Zaid (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: Na ce: Ya Manzon Allah, ban taɓa ganin ka yi azumi a wani wata kaman yanda kake yi a watan Sha'aban ba, sai ya ce: **(Wannan ai wata ne da mutane suke rafkana ga barinsa, da yake a tsakiyar watannin Rajab da Ramadhan, kuma wata ne da a cikinsa ake ɗaukaka ayyuka zuwa ga Ubangijin talikai, saboda haka ne, nake son a isar da ayyuka na a lokacin da nake azumi).**

An karɓo Hadisi daga Ummul muminina, Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan yi azumi har mu zaci ba zai sha ruwa ba, yakan kuma sha ruwa har mu zaci ba zai yi azumi ba, ban taɓa ganin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya cika azumin wani wata ba, sai watan Ramadhan, ban kuma taɓa ganin ya yawaita azumi a cikin wani wata kamar yanda yake yawaitawa a cikin watan Sha'aban ba.

Haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya keɓanci watan Sha'aban da wani dare mai albarka, da Allah yake duba zuwa ga bayinsa, yake yi masu kallo na rahama da jinƙai, ya kuma yi masu falala ta hanyar gafarta zunubansu, da suturta aibinsu, wannan dare shi ne daren **"Tsakiyar watan Sha'aban",** an ruwaito Hadisi daga Abu Musa al- Ash'ariy (Allah ya ƙara yarda da shi), cewa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai a daren tsakiya na watan Sha'aban Allah yana yin wata duba, da yake gafartawa ɗaukacin halittarsa, banda mai shirka da mai gaba)**, a wata ruwayar kuma: **(Lallai Allah yana yi wa bayinsa wata duba a dare tsakiyar watan Sha'aban; yana gafarta wa muminai, ya kuma jinkirta wa kafirai, ya kuma bar masu ƙiyayya da ƙiyayyarsu har sai sun yi watsi da ita).**

Lallai ya kamata mu ribaci waɗannan kwanaki masu albarka ta hanyar yawaita ayyukan biyayya, da ayyukan alhairi, da neman kusanci zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki, muna masu yi wa maganar Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) biyayya, a inda yake cewa: **(Lallai Ubangijinku yana da wasu kamfata da yake yi a wasu kwanaki na shekara, saboda haka ku bijirar da kawunanku zuwa gare ta, ta yiwu idan wannan kamfatar ta sami ɗaya daga cikinku, ya zamo ba zai taɓa halaka har abada).**

**Ya Ubangiji Allah muna roƙon ka taimaka mana wajen yawaita ambatonka, da yawaita gode maka, da kuma kyautata yi maka bauta.**

**- 18 –**

## MA'ANAR YARJEJENIYAR BAYAR DA AMINCI A WANNAN ZAMANI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ku cika alƙawurra; domin lallai tabbas za a tambaye ku akan alƙawurran da kuka ɗauka)) [al- Isra'i: 34].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda a cikin Hadisinsa mai tsarki yake cewa: **(Fiyayyun bayin Allah a wurin Allah su ne waɗanda suke cika alƙawurran da suka ɗauka tare da kyautatawa)** ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai addinin Musulunci addini ne na bayar da tsaro da aminci, addini ne na zaman lafiya da salama, addini ne na biyayya da kyautatawa, babu shakka akan cewa ɗabi'ar cika alƙawari ɗabi'a ce mai girma a cikin ɗabi'u da mutuntaka, da ita ce akan ƙarfafa yarda tsakanin mutane, hakan kuma ya samar da tsaro gami da aminci tsakanin al'umma da junansu, a kuma sami haɓakar taimakekeniya da soyayya, da cigaba tsakanin al'ummar da take rayuwa a wuri ɗaya, a dalilin haka ne ɗabi'ar

cika alƙawari ta zamo wani kaso mai girma cikin kason imani, dalili ne cikin dalilan gaskiya da kyautatawa, ladabi ne mai girma da ake yi wa Ubangiji, ɗabi'a ce babba a cikin ɗabi'un Annabawa, tsari ne mai muhimmanci a cikin tsare- tsaren Musulunci.

Lallai addinin Musulunci ya umurci mabiyansa da su dinga yin ado da ɗabi'ar cika alƙawurran da suka ƙulla, da yarjeniyoyin da suka shiga har aka rattaba hannu a kansu, ya ƙarfafa wannan, ƙarfafawa irinta wajibci, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku cika alƙawurra; domin lallai tabbas za a tambaye ku akan alƙawurran da kuka ɗauka)) [al- Isra'i: 34],** haka ma Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ku cika alƙawurran Allah idan kun ɗauka, kada ku kuskura ku warware alƙawurran bayan kun riga kun ƙarfafa su, domin dai kun riga kun sanya Allah ya zamo maku lamuni, lallai Allah yana da cikakkiyar masaniya akan abin da kuke aikatawa)) [an- Nahl: 91]**; ma'anar wannan aya ita ce: dole ne ku cika dukan wani alƙawari da kuka ɗauka, wanda kuka wajabta wa kawunanku, shin wannan alƙawarin tsakaninku da Allah Maɗaukakin Sarki ne, ko kuma tsakaninku da mutane 'yan uwanku, kada ku kuskura ku warware alƙawurran da kuka ƙarfafe su da rantsuwa, har ta kai ga kun sanya Allah ya zamo shi ne lamuninku a cikin wannan alƙawarin, duk wanda ya ƙulla wani alƙawari, to dole ne ya mutunta wannan alƙawarin, duk wanda ya ɗauka wa wani alƙawari, tilas ya cika.

Haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana cewa lallai masu cika alƙawwurran da suka ɗauka, da yarjeniyoyin da suka ƙulla su ne masoyansa, su ne masu gaskiya da tsoron Allah a cikin halittarsa, Allah mai girma yana cewa: ((**Tabbas**

**kafirai sun shata wa Allah ƙarya; domin duk wanda ya bayar da haƙƙin waninsa da yake akansa, ya biya a lokaci kamar yanda suka yi alƙawari, ya kuma ji tsoron Allah, bai tauye ba, bai kuma yi taurin bãshi ba, lallai zai rabauta da soyayyar Allah; domin dai ya ji tsoronsa)) [Ali Imran: 76]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Da masu cika alƙawari a rai da dukiya, da masu haƙuri akan cutar da za ta faɗa wa rai ko dukiya, ko lokacin haɗuwa da abokan gaba a wurin yaƙi. Waɗanda suka haɗa waɗannan aƙidu da ayyuka na alhairi su ne waɗanda suka yi gaskiya cikin imaninsu, su ne waɗanda suka ji tsoron kafirci da ƙasƙanci, suka kuma nesance su)) [al- Baƙra: 177],** haka ma Allah mai girma ya bayyana cewa su ne masu babban lada, da za su gaje aljannar ni'ima, a inda yake cewa: ((**Shi kuma duk wanda ya cika alƙawarin da ya yi wa Allah –ta hanyar cika mubaya'arsa- to lallai Allah zai ba shi lada mai matuƙar girma)) [al- Fathi: 10]**, a wani wuri a cikin littafin Allah, mai girma da buwaya ya sake bayyana wannan lada mai girma da cewa: ((**Su ne kuma waɗanda suke kiyaye amanonin shari'a da na bayi, da kuma duk wani abu da suka ɗauka wa Allah alƙawari, ko suka ɗauka wa mutane, ba sa ha'inci, ba kuma sa warware alƙawari.. Su ne kuma waɗanda suke tsayawa tare da gaskiya a wajen shaidarsu, ba sa ɓoye abin da suka sani.. Su ne kuma waɗanda suke kiyaye sallolinsu, suke yinsu kamar yadda suka kamata.. Masu waɗannan kyawawan sifofi suna aljanna cikin karamcin Allah Maɗaukakin Sarki)) [al- Ma'arij: 32 – 35].**

Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya girmama darajar cika alƙawari, ya kuma yi gargaɗi akan warware alƙawari, da rashin cika shi; saboda ha'inci da rashin cika alƙawari dalilai na

ɓacin ƙasa da al'umma, suna kuma kai wa zuwa ga samar da rashin yarda a tsakanin mutane, kana kuma amana ta tozarta, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Alamun munafuki guda uku ne: idan ya yi magana ya yi ƙarya, idan ya yi alƙawari ya saɓa, idan an amince masa ya yi ha'inci)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wajibi ne Musulmai su tsaya akan sharuɗɗan da suka sanya a tsakaninsu, sai dai idan sharaɗin ya haramta halal ne, ko kuma ya halatta haram)**. Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi gargaɗi game da uƙubar yaudara, inda yake cewa: **(Idan Allah ya tattara mutanen farko da na ƙarshe a ranar alƙiyama, ana ɗaga wa kowane mayaudari tuta, sai a ce: wannan yaudarar wane ɗan wane kenan),** Imam Ibn Kasir (Allah ya ƙara masa rahama) ya ce: Hikimar da take cikin yin haka ita ce: ganin cewa ya yi yaudarar ne a ɓoye, mutane ba su sani ba, amma a ranar alƙiyama zai bayyana a fili inda kowa zai ga abin da ya aikata, wannan ne zai bayyana wa mutane yaudara da ha'incin da aka daɗe ana aikata, Allah zai kunyata su a bainar jama'a.

A cikin alƙawurran da Shari'a mai girma ta ƙarfafa wajen bayar da umurnin a cika su, a kuma nesanci duk wani abu da zai sanya a warware su akwai: **"alƙawari ko yarjejeniyar aminci"**, ma'anar haka a zamance shi ne: izini, ko bizar da ƙasa take bayarwa, wanda yake ɗauke da bayar da izini ga wasu mutane na wata ƙasar ta daban na su shiga cikin ƙasarta, shin da niyyar yawon buɗe ido ne, ko ziyara, ko ma domin zama a ƙasar, daidai da yanda dangataka take tsakanin ƙasa da ƙasa, ko saboda yarjejeniyar ƙasa da ƙasa na yin mu'amala ta doflomasiyya da makamantansu, ko yarjeniyoyin da aka yi tsakanin ƙasashe biyu ta kowace irin hanya da aka amince da

ita, wadda doka ta lamunta, wanda ake amfani da ita a ƙasar mai amsar baƙon, daidai da dokokinta na cikin gida, da zaran mutum ya sami izinin zama, ko biza ta shiga ƙasa, to kuwa zai zamo yana da haƙƙi da hurumi a cikin ƙasar, wannan alƙawari na aminci da ƙasar ta ba shi ya zamo wajibi akan ɗaukacin 'yan ƙasa su kiyaye shi, da ma mazauna ƙasar, sam bai halatta a warware shi ba, ko a yi masa wani wala- wala, ko kuma a yi masa riƙon – sakainar – kashi, sam hakan bai halatta ba a shari'ance, ko a dokance, duk wani ɗan ƙasa da ya ga wani abu da yake barazana ga tsaron ƙasarsa, ko abin da ya saɓa wa doka da oda na ƙasar, to abin da zai iya kawai shi ne, ya sanar da hukumomin da abin ya shafa, domin a samu a hukunta mai yi, daidai da yanda doka da gindaya, domin babu wani mutum da yake da ikon hukunta shi akan abin da ya aikata, ko kuma a yi masa abin da ba daidai ba, in har aka yi haka, to abin sai ya zamo hauragiya da rashin tabbas da tsari.

Abin da kowa ya sani ne cewa, lallai cika alƙawurra na amana da tsaro abu ne da yake wajibi a shari'ance, da dokance, kishin ƙasa da mutuntaka ma suna wajabta cika alƙawurra, idan har addininmu mai girma ya ɗaukaka darajar cika alƙawarin aminci da tsaro akan kowane Musulmai, - musamman ma ganin cewa zimmar Musulmai a koda yaushe ɗaya ce, ma'ana: duk alƙawarin da ɗaya daga cikinsu ya ɗauka, to zai zama wajibi ne Musulmai su cika wannan alƙawari, to ina kuma ga alƙawarin da ya zamo yarjejeniya da shari'a gami da doka suka haɗu suka samar da shi, inda suka ƙarfafa juna? Babu shakka irin wannan alƙawari yana kan kowa da kowa, dole ne a cika shi, ba a warware shi, ko a tozarta shi ba, kai har yunƙurin sauya shi ma bai halatta ba.

Lallai addinin Musulunci ya bai wa alƙawurra da yarjeniyoyi kariya ta musamman, addini ne da bai san algushi, ko yaudara da cin amana ba, a tarihin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), da na sahabbansa (Allah ya ƙara yarda da su) kaf, babu inda suka taɓa hana wani aminci na tsaro akan kansa, babu kuma inda suka taɓa warware irin wannan alƙawari na aminci bayan sun bayar, Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗa wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa: **((Idan ma kun ji tsoron ha'inci na warware yarjejeniya da kuka ƙulla daga wasu mutane, to ku sanar da su cewa kun fita daga cikin wannan yarjejeniyar kaman yanda kuka ƙulla, saboda lallai Allah ba ya son maha'inta masu warware alƙawurra)) [al- Anfal: 58]**, haka ma lokacin da akwai yarjejeniya tsakanin Sayyiduna Mu'awiyya Bn Abu Sufyan (Allah ya ƙara yarda da su) da Romawa, Mu'awiyya ya ƙuduri aniyar zuwa kusa da ƙasar Romawa, ta yanda da zaran ranar da ƙarshen wannan yarjejeniya za ta zo, shi kuma ya faɗa masu ba tare da sun sani ba, sai wani daga cikin sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi sauri ya riske shi yana cewa: Allahu akbar, Allahu akbar, a dai cika alƙawari, kada a yi yaudara, da aka duba a ga wane ne yake wannan maganar, sai aka ga Sayyiduna Amru Bn Abasat (Allah ya ƙara yarda da shi) ne, sai Mu'awiyya (Allah ya ƙara yarda da shi) ya aika aka kira shi, ya tambaye shi, sai ya ce: na ji Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda yake da wata yarjejeniya ta aminci da tsaro tsakaninsa da wasu mutane, kada ya tsananta, kada kuma ya warware ta har sai lokacinta ya ƙare, ko kuma ya sanar da su cewa ya dakatar da yarjejeniyar)**, sai Sayyiduna Mu'awiyya (Allah ya ƙara yarda da shi) ya dawo daga rakiyar

shirinsa na farko, kai ma girman wannan addini namu na Musulunci yana ƙara bayyana a fili ne a cikin umurnin da Allah Maɗaukakin Sarki ya bai wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), na ya maƙwabtaci duk wanda ya nemi yin maƙwabtaka da shi a cikin aminci, koda kuwa mushiriki ne shi, ya kuma ba shi kariya da tsaro, kai ma koda mayaƙi ne a filin daga, Allah Mai girma da buwaya yana cewa: **((Idan wani daga cikin mushirikai da Allah ya ba ku umurnin ku yaƙe su ya nemi aminci daga wurinka domin ya saurari kiranka, to ka ba shi aminci saboda ya saurari maganar Allah, idan ya shiga Musulunci, to yana cikinku, idan kuma bai shiga ba, to ku isar da shi zuwa ga wurin da zai sami aminci da tsaro akan kansa, lallai wannan hukunci –na amintar da duk wanda ya nemi aminci saboda ya saurari maganar Allah- sakamakon yanda ya jahilci addinin Musulunci ne a farko, da kuma neman saninsa a haƙiƙaninsa)) [at- Tauba: 6].**

Lallai Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya riga ya dasa wannan nagartacciyar ɗabi'a da take tabbatar da tsaro da aminci ga ɗaukacin bil'adama da maganarsa, da kuma aikace, a inda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Babu batun imani ga mutumin da ba shi da amana, babu kuma batun addini ga wanda ba ya kiyaye yarjejeniya)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya kashe kafirin amana ba zai taɓa jin ƙamshin aljanna ba, kuma lallai ana jin ƙamshinta ne tun daga tazarar tafiyar shekaru arba'in)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Musulmi na gaskiya shi ne: wanda mutane suka kuɓuta daga sharrin harshensa da hannunsa, mumini na**

**gaskiya kuma shi ne: wanda mutane suka amince masa akan rayukansu da dukiyoyinsu).**

Lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya buga babban misali na cika alƙawari, har a tare da maƙiya, an ruwaito Sayyiduna Huzaifatul Yamaniy (Allah ya ƙara yarda da shi) yana yin bayani game da abin da ya hana shi zuwa yaƙin Badar, yana cewa: Ba wani abu ne ya hana ni zuwa yaƙin Badar ba, sai wata rana ni da mahaifi na mun fito, sai kafiran Ƙuraishawa suka kama mu, sai suka ce: kuna son ku tafi wurin Muhammadu ko? Sai muka ce: ba wurinsa za mu ba, garin Madina kawai muke son zuwa, sai suka sanya muka rantse da Allah akan kawai Madina za mu tafi, ba za mu shiga cikin tawagarsa mu yi yaƙi ba, sai muka zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), muka ba shi labarin abin da ya gudana, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ku tafi, za mu cika masu alƙawarin da muka yi da su, mu kuma nemi taimakon Allah akansu)**.

Saboda haka, muna ƙara tabbatar da cewa wajibi ne mu kiyaye alƙawurra, da yarjeniyoyin da ƙasarmu da ƙulla tare da duk wanda ya shigo ƙasarmu, dole ne mu haɗa kai wajen bai wa jininsu, da mutuncinsu, da dukiyoyinsu, da sirrinsu kariya, haka ma wajibi ne mu yi masu kyakkyawan tarba, mu karrama su; domin mu nuna masu irin yanda muke son su fahimci girman addininmu, da zurfin cigabanmu, da ƙimar mutuntakarmu, abin da zai sanya su sami kyakkyawar sura game da addininmu, da ƙasarmu, da al'ummarmu, wannan shi ne halin al'ummomin da suka waye, suke kuma da cigaba..

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai addinin Musulunci addini ne na adalci, da rangwame, da kuma kyautata rayuwar tare, shi Musulmi a koda yaushe tsaro ne da aminci, salama ne da zaman lafiya suke sauka a duk inda ya tafi, shin a ƙasarsa ne, ko a wajen ƙasarsa, idan Musulmi ya tafi wata ƙasa, shin ta Musulmai ce, ko wadda ba ta Musulmai ba, to bizar da ƙasar ta ba shi -a matsayin yarjejeniyar aminci akan kansa- a gefe ɗaya kuma tana nufin aminci ne daga gare shi zuwa ga mutanen ƙasar da ya tafi; hakan zai ba su aminci akan kawunansu, da dukiyoyinsu, hakan kuma yana nufin ya yi wa dokokin ƙasar biyayya sau da ƙafa, ya sauke duk wani abu da ya rataya a wuyansa cikin gaskiya da amana, haramun ne ya amshi dukiyoyinsu ba tare da haƙƙi ba, haramun ne ya keta hurumin mutuncinsu, ko ya yaudare su ta kowace irin hanya, zai kiyaye waɗannan ne domin ya zamo jakada na alhairi ga addininsa, da ƙasarsa, da cigaban ƙasarsa da tarihinsa, da zaran ya shiga wannan ƙasa, to alƙawarin Allah Maɗaukakin Sarki ya hau wuyansa, dole ne kuma ya cika, gudun kada ya faɗa cikin waɗanda Allah Maɗaukakin Sarki yake magana akan su da cewa: **((Su ne waɗanda suke warware alƙawarin da suka**

**ɗauka wa Allah bayan sun riga sun ƙarfafa shi da rantsuwa, suke kuma yanke abubuwan da Allah Maɗaukakin Sarki ya bayar da umurnin a sadar, suke kuma yin ɓarna a bayan ƙasa, waɗannan kam la'anannu ne, kuma suna da mummunar makoma))** **[ar- Ra'ad: 25]**, Imam as - Shafi'iy (Allah ya ƙara masa rahama) yana faɗi a cikin littafin "Al- Ummu" cewa: Idan mutum ya shiga ƙasar da ba ta Musulmai ba a ƙarƙashin alƙawarin aminci da suka ba shi, to sam bai halatta ya ɗauki komai daga cikin dukiyoyinsu ba, shin kaɗan ne ko mai yawa, koda kuwa suna cikin halin yaƙi da Musulmai; domin lallai idan har sun ba shi aminci, to su ma sun aminta daga gare shi, saboda kuma kasancewar babu abin da ya halatta ya yi a lokacin da yake cikin amincinsu sai abin da ya halatta ya aikata tare da dukiyoyin Musulmai.. Alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa:

"Shi fa cika alƙawari tada ce ta mutane masu karamci, warware alƙawari kuma tada ce ta mutanen banza.. Ni a wuri na babu wani abu da za a sanya shi cikin kyawawan ɗabi'u da ya wuce kiyaye soyayya da alƙawurra.."

**Ya Allah Ubangijinmu, ka shiryatar da mu zuwa ga kyawawan ɗabi'un da babu mai shiryatarwa zuwa gare su sai kai, ka kuma kiyaye mu daga barin munanan ɗabi'un da babu mai kiyayewa daga barinsu sai kai..**

- 19 –

## KIYAYE AL'AMURRA DA MASLAHAR AL'UMMA NA BAI ƊAYA..

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya ku muminai, ku yi taimakekeniya a tsakaninku wajen aikata alhairi, da wajen dukan ayyukan biyayya da ɗa'a, kada ku kuskura ku yi taimakekeniya wajen aikata saɓo, da ƙetare iyakokin Allah, ku kiyayi uƙubar Allah da kamunsa, lallai Allah mai tsananin uƙuba ne ga duk wanda ya saɓa masa)) [al- Ma'ida: 2]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa da waɗanda suka bi tafarkinsa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai addinin Musulunci ya gina daula ta haƙiƙa, ya samar mata da ƙa'idoji, ya kuma sanya mata ginshiƙai, sannan ya kwaɗaitar da a kiyaye ta, a kuma ba ta kariya, hasali ma ya shigar da ba ta kariya da kiyayewa cikin wajiban da suka wajaba ga ɗaukacin waɗanda suke rayuwa a cikinta, damuwa da ita aiki ne na gaba ɗayan al'umma, a duk sanda ƴan ƙasa suka sami fahimta, da wayewa game da ƙima, da darajar wajibai na gaba ɗayan da hatsarin da yake tattare da haka, to a

lokacin ne taimakekeniya, da haɗin kai suke ƙaruwa; saboda a ba ta kariya, abin da hakan zai kai ga samar da cikakken ƙarfi ga ginin wannan al'umma guda ɗaya, a kuma ji cewa tabbas al'umma ce guda ɗaya take rayuwa a matsayin gangan jiki ɗaya, wanda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kira zuwa gare shi, a inda yake cewa: **(Shi mumini a wurin mumini tamkar gini ɗaya ne da sashensa yake ƙarfafa sashe, sai kuwa ya haɗa ƴan yatsunsa)**, da inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Misalin muminai a wajen soyayyar juna, da tausayin juna, da jinƙan juna tamkar gangar jiki ɗaya ne, wanda idan wata gaɓa ta kamu da cuta, sai sauran jikin shi ma ya kamu da rashin barci da kuma raɗaɗi)**.

Babu shakka kan cewa, a ɗaya daga cikin muhimman hanyoyin kiyaye wajiban da suke akan ɗaukacin al'umma akwai: **gabatar da maslahar al'umma mai faɗi da amfaninsa yake samun ɗaukacin al'umma, akan keɓantacciyar maslaha mara faɗi da amfani ya taƙaita kawai akan masu ita,** ana yin haka ne domin a tsarkake zukatan bil'adama daga barin sharrin son kai, saboda ita maslaha ta bai ɗaya, ta haɗa da duk wani abu na zahiri da na ma'ana, da za su samar da rayuwa ga al'umma gaba ɗaya, su kuma jawo masu alhairi, da amfani na gaba ɗaya, su kuma tunkuɗe sharri, da ɓarna ga barinsu, su kuma kai zuwa ga bai wa ƙasa kariya, da kiyaye kwanciyar hankali, da kiyaye iyakokin ƙasa, babu shakka samar da jin daɗin al'umma baki ɗaya shi ne abin da "Fiƙhul aulawiyyat" ya ƙunsa.

**Lallai Alƙur'ani mai girma ya tabbatar da cewa: kiyaye maslahar** al'umma ta bai ɗaya, da gabatar da ita akan keɓantacciyar maslaha shi ne manhajin ɗaukacin Annabawa da

Manzanni, Allah Maɗaukakin Sarki bai aiko wani Annabi, ko Manzo ba, sai domin ya samar da jin daɗi ga mutanensa, ya samar masu da alhairi, ba tare da ya jira wani lada, ko amfani na duniya daga gare su ba, Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗi ta bakin Annabinsa Nuhu (AlaiHis Salam) cewa: **((Ya ku mutane na, ba na tambayarku wani lada akan abin da nake gabatar maku, babu kuma yanda za a yi in kori waɗanda suka yi imani da Allah, saboda lallai za su haɗu da Ubangijinsu, kai jama'a, ni fa ina ganin ku mutane ne masu wauta)) [Hud: 29]**, Haka ma mai girma da ɗaukaka ya faɗi ta bakin Annabinsa Hudu (AlaiHis Salam) cewa: **((Ya ku mutane na, ba na tambayarku wani lada akan abin da nake gabatar maku, lada na yana wurin wanda ya halicce ni, shin ashe ba za ku yi tunani akan hakan ba?!)) [Hud: 51]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗi ta bakin Sayyiduna Shu'aib (AlaiHis Salam) cewa: **((Gyara kawai nake so daidai gwargwadon yanda zan iya, babu wani nasara da zan samu in ba daga Allah ba, da shi kawai na dogara, kuma wurinsa na dosa)) [Hud: 88].**

Lallai Shari'ar Musulunci mai girma ta zo da abubuwan da suka yi daidai da hankali, suka kuma dace da shi ne, sai ta kwaɗaitar da aikata abubuwan da ɗabi'arsu shi ne samar da maslahar al'umma, ƴan ƙasa ta bai ɗaya, irinsu: **samar da abubuwan da al'umma take matuƙar buƙata, da kuma la'akari da fahimtar yanayin da ake ciki**, ta yadda idan buƙatar al'umma a lokacin ita ce a gina asibitoci, da samar da magunguna ga talakawa, da ba su kulawa ta musamman, to hakan shi ne ya fi zamowa wajibi, idan kuma buƙatar al'umma a lokacin ita ce a gina makarantu, da cibiyoyin ilimi, da gyara su, da samar masu da kayan aiki, da bayar da tallafi ga ɗaliban

ilimi, to hakan shi ne zai fi zama wajibi, idan kuma abin da aka buƙata shi ne sauƙaƙa wa talakawa hanyar yin aure, da biya wa waɗanda bashi ya yi masu kanta bashin da yake kansu, da yaye damuwa ga waɗanda suke cikin matsi, to hakan sai ya zamo shi ne ya fi zamowa wajibi, saboda biya wa mutane buƙatunsu, da tsaya masu wajen samar masu da buƙatunsu na rayuwa, wajibi ne na Shari'a, kuma haƙƙi ne na zamowarsu ƴan ƙasa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk mutumin da ya kwana a ƙoshe, maƙwabcinsa yana cikin yunwa, alhalin yana sane, to bai yi imani da ni ba)**.

Haka ma akwai: **kiyaye dukiyar al'umma**, ganin cewa mallaka ce ta ɗaukacin ƴan ƙasa, hurumin da dukiyar al'umma take da shi, ya fi hurumin da dukiyar ɗaiɗaikun mutane take da shi; saboda yawan haƙƙoƙin da suka rataya shi ita, da kuma yawan masu mallakar, saboda haka ne addinin Musulunci ya yi gargaɗi mai tsanani game da lalata ta, ko sace ta, ko cutar da ita, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Duk wanda ya ɓoye wani abu na ganima zai kawo shi a ranar alƙiyama, sannan a bai wa kowane rai sakamakon abin da ya aikata, lallai ba za a zalunce su ba))** **[Ali Imran: 161]**, dukiyar gwamnati mullaka ce ta ɗaukacin mutane, ba mallaka ne na wasu gungun mutane daga cikinsu ba, masu riƙe da madafun iko amintattu ne wajen kiyaye ta, da kuma tattara ta, da isar da ita ga waɗanda suka cancanta, sam bai halatta wani ya wawuri wani abu daga ciki da ba nasa ba, saboda yin hakan ha'inci ne da zalunci, da cin dukiyar mutane da ɓarna..

Haka ma addinin Musulunci ya bayar da umurnin **kiyaye wurare mallakar al'umma**, irinsu: wuraren ibada, da makarantu, da asibitoci, da lambuna da sauransu, ganin cewa

mallaka ne na ɗaukacin al'umma, amfaninsu yana komawa ne zuwa ga kowa da kowa, ya kuma yi gargaɗi mai tsanani akan yi masu ta'adi, ko tozartar da su, da lalata su, da kowane irin nau'i na lalatawa, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Kada ku kuskura ku yi ɓarna a bayan ƙasa bayan an gyara ta...)) [al-A’araf: 56, 85]**; gudun ma kada wani ya riya cewa, ya halatta ya amfana da dukiyar al'umma ta hanyar da yake so, irin yadda ya ga dama, yana mai da'awar cewa ai "na mu duka ne", wannan fahimta ce ta kuskure, abin da ya wajaba shi ne: kiyaye ɗaukacin kayan al'umma, da ba su kariya, da kuma ƙoƙarin bunƙasa su, da samar masu da cigaba, saboda ba mallaki ne wani banda sauran mutane ba, ba kuma na wasu jama'a ne a wani zamani ba, hasali mallakinmu ne baki ɗaya, da ma al'umma masu zuwa a bayanmu..

Haka ma akwai: **kiyaye hanya, da tsare haƙƙoƙinta**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ahir ɗin ku da zama akan hanyoyi)** sai suka ce: ya Manzon Allah, wuraren zamanmu ne da muke yin hira da junanmu, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan kun dage sai kun zauna a majalisan, to ku bai wa hanya haƙƙoƙinta)**, sai suka ce: mene ne haƙƙoƙinta? Sai ya ce: **(Runtse idanuwa, da rashin cutar da mutane, da mayar da sallama, da kuma bayar da umurni da aikata alhairi da hana munanan ayyuka)**, haka ma Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Shi imani ya kasu kashi saba'in -ko sittin- ne, mafi girman kason shi ne faɗin "La'ilaha illalLahu", mafi ƙanƙantarsu kuma shi ne kawar da abubuwa masu cutarwa daga barin hanya, lallai kunya ma kaso ne daga cikin imani)**..

Haka ma akwai: **gabatar da hidimar bautar ƙasa** da yake cikin muhimman wajibai da mutum zai gabatar wa addininsa, da ƙasarsa, dalili ne da yake nuna kishin ƙasa, da gaskiyar dangantaka da ita, yana kuma nuna soyayyar da yake yi mata, daraja da ƙimar ƙasa da mutunci a wurin Musulmi ba su ƙasa da na ransa, ko na addininsa, da dukiyarsa, ko abubuwan da yake mallaka, kuma hakan yana dasa ma'anonin mazakuta, da jarumtaka, da mutunci, da kyawawan ɗabi'un za addininmu na Musulunci ya zo da su, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idanuwa guda biya kam wuta ba za ta taɓa shafansu ba; idon da ya yi kuka saboda tsoron Allah, da idon da ya kwana gadi saboda Allah)**.

Haka ma a cikin maslahohi na bai ɗaya da ya zama wajibi a kula da su -domin kiyaye al'amurran da suka shafi ɗaukacin al'umma- akwai: **kiyaye yarjeniyoyin da suke tsakanin daula da wasu ƙasashe, ko da ƙungiyoyi da gamayyar ƙasashen waje,** lallai dole ne duk wani mataki na fiƙhu, ko na bayar da fatawa, ko na tunani, ko na da'awa su zamo ayyuka ne a gwamnatance, da shugaban al'umma, ko wanda yake wakiltarsa zai gabatar, dole ne waɗanda za su yi magana akan irin waɗannan al'amurra su yi la'akari da dukan abubuwan da suka shafi zamantakewa, da na ƙasa, da ma waɗanda suka shafi ƙasa da ƙasa, da suke da jiɓi da abin da za su yi magana akansa, gudun kada a fitar da wasu ra'ayoyi, da fatawa ta gaggawa, kuma ta mutum ɗaya, a cikin abubuwan da suka shafi al'umma, da za su ci karo da abin da yake a ƙasa, ko su ci karo da dokokin ƙasa da ƙasa, da yarjeniyoyin ƙasa da ƙasa, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya umurce mu da cika alƙawari a inda yake cewa: **((Ya ku waɗanda kuka imani, ku cika alƙawurran da**

**kuka ƙulla..))** **[al- Ma'ida: 1]**, wannan ayar ta game komai da komai, ta haɗa duka yarjeniyoyi, da alƙawurran da mutum zai ɗauka wa waninsa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Musulmai suna nan akan sharuɗɗansu, sai dai idan sharaɗin ya haramta halal, ko kuma ya halatta haram)**.

Ga ma Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya umurci Abu Basir (Allah ya ƙara yarda da shi) da ya koma, bayan sulhun Hudaibiyya, daidai da yarjejeniyar da take tsakaninsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) da Ƙuraishawa, duk kuwa da cewa akwai yiwuwar wannan sahabi ya fuskanci cutarwa; ya yi hakan ne saboda kiyaye alƙawarin da ya yi wa Ƙuraishawa, wannan a wani ɓangare kiyaye alƙawarin da aka ɗauka ne, a wani ɓangaren kuma rinjayar da maslahar al'umma ne akan maslaha ɗaiɗaiku..

Lallai yin magana akan abubuwan da suka shafi al'umma, ba tare da ilimi, da fahimta ba, yana da mummunan tasiri da yake yi wa daula, domin yakan sanya tsaron ƙasa cikin garari, kwanciyar hankalin al'umma kuma ya shiga cikin ruɗani, ƙasar kuma za ta zamo abin izgilanci ga sauran mutane, sai a yi ta samun ruɗani, waɗanda ba su da masaniya akan abubuwa su ma su tsoma bakunansu akan al'amurra da ba su sani ba, mene ya kai yawan masu yaɗa ƙarairayi, da suke ɓarna a bayan ƙasa, ba kuma sa iya gyara komai a cikinta, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya umurce mu da mu mayar da komai zuwa ga masu shi, a inda mai girma da ɗaukaka yake cewa: **((Idan waɗannan munafukai suka ga wani abu na tsaro, ko na tsoro da yake da jiɓi da ƙarfin Musulmai, ko raunin su, sai su yayata shi da nufin ruɗar da Musulmai, ko jefa tsoro da razani a cikin zukatan su, ko saboda su isar da labarin su zuwa ga maƙiyan**

**su, da a ce waɗannan munafukai sun mayar da duk wani al'amari na tsaro da tsoro zuwa ga Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) da shugabanni da manyan saahabbai da dakarun yaƙi, su kuma nemi sanin haƙiƙanin al'amari ta wurin su, da waɗannan da suke ƙoƙarin neman labarai da yaɗa su sun san gaskiya a wurin Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) da shugabanni. Lallai ba domin falalar da Allah ya yi maku na tabbatar da zukatanku akan imani, da daƙile fitina, da kuma rahamarsa na damƙa maku dukan dalilan da za su sanya ku sami nasara ba, da mafi yawanku sun faɗa cikin tarkon shaiɗan, babu waɗanda za su tsira daga halakarwarsa sai mutane kaɗan daga cikin ku)) [an- Nisa'i: 83].**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai ma'anar "maslahar al'umma" ta zarce duk wani abu da mutum a shi ɗaya yake muhimmantawa, zuwa abubuwan da ɗaukacin mutane suke muhimmantawa, saboda haka ne al'amarin da ya shafe ta ba wai na kowa da kowa ba ne, malamai masana da suka fahimci ƙima da darajar abin da aka ɗaura masu na ayyuka da suke da

jiɓi da tsaron ƙasa, da rayuwar mutane, da maslahohinsu, da arzikin ƙasashe, da yanayin da take ciki a yankin da take, da ma matsayinta a duniya, da al'amurranta na siyasa, da na zamantakewa, da na tsaro, da na ilimi da sauransu, da malamai, lallai mujtahidai masu ijtihadi su ne: masana masu hangen nesa, waɗanda idan suka yi ijtihadi a fagen iliminsu, suka kuma yi kuskure suna da lada ɗaya, idan kuma suka yi daidai suna da lada biyu, ma'anar haka ta gicciye kuma ita ce: idan duk wanda ba malami ba ya yi ijtihadi a fagen da bai da masaniya akansa, to idan ya yi dace ma yana da zunubi ɗaya, sakamakon kutsawa wajen yin magana akan abin da ya jahilta, idan kuma ya yi kuskure a ijtihadin nasa, to yana da zunubai biyu, ɗaya na kuskuren da ya tafka, ɗayan kuma na ƙumajin aukawa cikin abin da ya san ba shi da masaniya akansa; wannan ya faru shi saboda irin yanda addinin Musulunci ya raji wajen girmama malamai masana, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ku tambayi malamai masana idan dai har ba ku sani ba))** **[an- Nahl: 43; al- Anbiya'i: 7]**, malamai masana su ne: masana fannonin ilimi, kowa a fagensa, daidai da buƙatarsa da ake yi.

Saboda haka ne **aka hana yin gaggawar bayar da fatawa ba tare da ilimi, ko wani dalili na Shari'a ba,** Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Wane ne ya kai azzalumi ne ya kai wanda yake ƙirƙira wa Allah ƙarya ba tare da ilimi ba zalunci, kawai saboda ya ɓatar da mutane, lallai Allah ba ya shiryatar da mutanen da suka zamo azzalumai))** **[al- An'am: 144]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Kada ku kuskura ku faɗa wa abubuwan da bakunanku suka ga dama ta hanyar ƙarya cewa: wannan halal ne, wannan kuma haramun ne, kawai saboda**

**ku ƙirƙira wa Allah ƙarya, lallai waɗanda suke ƙirƙira wa Allah ƙarya ba za su taɓa samun rabo ba. Ɗan jin daɗi ne ƙanƙani za su yi a duniya, suna kuma da azaba mai tsananin raɗaɗi a lahira)) [an- Nahl: 116 -117]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk mutumin da ya bayar da fatawa ba tare da ilimi ba, to zunubin wanda aka bai wa fatawar yana kansa)**, shi ya sanya manyan sahabbai da tabi'ai (Allah ya ƙara yarda da su) suke guje wa bayar da fatawa, saboda sun san hatsarin da yake tattare da yin haka; ga Sayyiduna Abubakar as- Siddiƙ nan (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **"wace sama ce za ta yi mini inuwa, kuma wace ƙasa ce za ta ɗauke ni, idan na yi magana akan littafin Allah ba tare da ilimi ba?!"**, lokacin da aka tambayi Imam as- Sha'abiy (Allah ya ƙara yarda da shi) game da wata mas'ala, sai ya ce: ban sani ba, sai abokansa suka ce masa: lallai kam mun ji maka kunya, sai ya ce: amma dai mala'iku ba su ji kunya ba a lokacin da suka ce: **((Ba mu da ilimi sai abin da ka sanar da mu..)) [al- Baƙra: 32]**, Abdurrahman Bn Abulaila ya ce: Na riski al- Ansar cikin sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wwa sallam) har su ɗari da ashirin, akan tambayi ɗaya daga cikin akan wata mas'ala, ya miƙa ta zuwa ga wani, shi ma ya miƙa ta zuwa ga waninsa, har ta gama zagayawa ta dawo wa na farkon.

**Kiyaye al'amurran da suka shafi ɗaukacin al'umma alhaki ne da yake a kan kowa,** kowa a matsayin da yake a kai, da kuma irin damar da yake da ita, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Dukanku masu kulawa ne, kuma kowa za a tambaye shi akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi: Shugaba mai kulawa ne, za kuma a tambaye shi akan waɗanda yake shugabanta, namiji ma mai kulawa ne**

**a cikin iyalansa, za kuma a tambaye shi akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi, mace ma mai kulawa ce a gidan mijinta, za kuma a tambaye ta akan nauyin da aka ɗaura mata na kulawa, hadimi ma mai kulawa ne da dukiyar uban gidansa, za kuma a tambaye shi akan nauyin da aka ɗaura masa alhakin kulawa da shi, dukan ku masu kulawa ne, za kuma a tambayi kowa a akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi).**

Mutane masu yawa ba sa muhimmanta abubuwan da suke faɗi, ko suke rubutawa, ko abubuwan da suke aikatawa na yaɗa rubuce – rubucen wasu a shafukan sadarwa da sada zumunta na zamani, ta ma yiwu wasu su kalli hakan a matsayi wani abu na raha da barkwanci, ba su fahimci cewa ƙirƙirar jita – jita, da yaɗa ta a tsakanin mutane, hanya ce daga cikin hanyoyin da maɓarnata suke amfani da ita wajen yaƙi da masu gaskiya ba, abin da yake kai ga ka ga al'ummar da take tamkar gangar jiki ɗaya, ta koma tana shakka da junanta, wasu daga cikin suna cutar da wasu; saboda haka ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai ƙarya ta kai ƙarya a ce mutum yana bayar da labarin duk abin da ya ji..)**.

Idan dai har yin magana akan dukan abubuwan da mutum ya ji nau'i ne cikin nau'o'in ƙarya, da ake yi wa mutum azaba mai tsanani akanta a ranar lahira, to yaya kuma muke zaton abin zai kasance ga wanda yake bayar da labarin abin da bai gani da idonsa, bai kuma ji da kunnuwansa ba, hasali ma ba shi da masani akan haka, ƙarya ne kawai da ƙage?!. Lallai akwai kalmomi masu yawa -da suke karaɗe duniya- da za su zamo dalilai na yi wa mai su azaba a ranar alƙiyama, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai bawa zai iya**

**furta kalmar neman yardar Allah, da ma bai mayar da hankali zuwa gare ta, hakan kuma ya zama dalilin samun ɗaukakar darajarsa a wurin Allah, haka ma bawa zai iya furta kalmar da za ta jawo fushin Allah, ba kuma tare da ma ya mayar da hankali zuwa gare ta ba, hakan kuma ya zamo sanadiyyar aukawarsa cikin jahannama),** lallai wannan yana buƙatar yin taka- tsantsan, da bi a hankali, da rashin kutsawa cikin abubuwan da ba mu da masaniya akansu, ko bayar da fatawa ba tare da ilimi ba.

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya ba mu umurni na tabbatar da labari ta hanyar bincike, da rashin biye wa maɓarnata akan abubuwan da suke yaɗawa, dole ne mu binciki duk wani labari da ya zo mana, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: ((**Ya ku waɗanda kuka yi imani, idan wani fãsiƙi ya ƙetare shari'ar Allah ya zo maku da kowane irin labari, to ku bincika ku tabbatar da gaskiyarsa; saboda kada ku cutar da wasu mutane –da ba ku san haƙiƙaninsu ba-, hakan sai ya sanya ku yi nadama akan abin da kuka aikata, kuna: ina ma ba mu aikata hakan ba, a lokacin da bayani ya bayyana cewa ba su da wani laifi)) [al- Hujrat: 6]**, haka ma Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Yin abu cikin taka- tsantsan abu ne daga Allah, gaggawa kuma daga shaiɗan ne)**, a wani wurin kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Yin taka- tsantsan a cikin komai, banda aiki lahira)**.

Lallai muna matuƙar buƙatar samar da wayewa da fahimta game da "al'amurran da suka shafi ɗaukacin al'umma", da rinjayar da maslahar al'umma, mu kuma riski irin girman hatsarin gadan- zaren da ake shirya mana, ake kuma son mu ta rufta da mu, kaman yanda ya faru da wasunmu, ya kamata mu

wa'aztu da wasunmu, kada mu kuskura mu bai wa maƙiyan addininmu da ƙasarmu kowace irin dama, mu tsaya akan gaskiya, tsintsiya maɗaurinki ɗaya, gudun kada mu rufta cikin makircin da ake ƙulla mana. Mu yaɗa yarda da juna a tsakaninmu, mu kuma yi taimakekeniya akan kowane aikin alhairi da amfaninsa zai shafi dukan mutane baki ɗaya.

**Ya Allah Ubangijinmu, muna roƙon ka datar da mu zuwa ga sauke wajiban da ka ɗaura mana game da ƙasashenmu, ka kiyaye mana al'ummarmu, da shugabanninmu, da sojojinmu da 'yan sandan mu, ka sanya ƙasashenmu cikin kariyarka da amincinka, ka yalwata arziki da jin daɗinsu, da ma sauran ƙasashen duniya baki ɗaya.**

- 20 –

## KASUWANCI: ƘA'IDOJI DA LADUBBA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Halaka ta tabbata ga masu tauye ma'aunai…. Su ne waɗanda idan za su auni kaya daga mutane suke cika ma'auni har ya yi tsororiya… Idan kuma su za su aunar wa mutane sai su cuce su ta hanyar tauye masu haƙƙoƙinsu… Shin waɗannan masu tauye ma'aunin ba su tunanin cewa lallai za a tashe su bayan mutuwa ne… A wata rana mai tsananin ban tsoro. Ranar da mutane za su tashi zuwa ga Ubangijin talikai domin fuskantar hukuncinsa.)) [al-Mutaffifina: 1-6]**.. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa, da waɗanda suka bi turbarsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Allah Maɗaukakin Sarki ya shar'anta wa bayinsa cinikayya na saye da sayarwa ne, saboda su isa zuwa ga wata manufa, su kuma kai zuwa ga kawar da buƙatu, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Allah ya halatta kasuwanci, ya kuma haramta riba)) [al- Baƙra: 275]**. Babu shakka tun fil'azal mutane suka saba da yin kasuwa da suke musayance kayan amfani a tsakaninsu, kuma ta hakan ne suke biya wa junansu buƙatunsu da

maslahohinsu, hasali ma ayar Alƙur'ani mai girma ta zo domin ta tabbatar da cewa lallai hakan sifa ce daga cikin sifofin ɗan Adam, Allah Mai girma yana cewa: **((Ai kafinka ba mu aiki wani daga cikin manzanni ba, face suna cin abinci, suna kuma zuwa kasuwa…))** **[al- Furƙan: 20]**, Alƙur'ani mai girma ya ruwaito abin da mushrikai suke faɗa wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam): **((Mene ya sami wannan Manzon ne da yake cin abinci, yana kuma zuwa kasuwa?))** **[al- Furƙan: 7]**, Allah Maɗaukakin Sarki ya kawo ƙissar As'habul Kahfi, inda yake bayyana halin da suke ciki, cewa: **((Ku aiki ɗaya daga cikinku zuwa cikin gari da wannan kuɗi, ya duba mafi kyawon abinci ya sayo mana…))** **[al- Kahfi: 19]**.

Lallai yanayin kasuwanni ɗaya ne daga cikin hanyoyin zartar da haƙiƙanin Musulunci a aikace, idan kana neman ka san tasirin ibada a rayuwar ɗan Adam, to ka tafi kasuwa, haka ma idan ka neman ka yi hukunci akan gaskiyar sifantuwa da sifofin addini, shin na gaske ne, ko kuwa na yaudara, shi ma abin da za ka yi kawai shi ne, ka duba yanayin mutumin wajen mu'amalarsa ta saye da sayarwa, saboda haka ne lokacin da wani mutum ya ce wa Sayyiduna Umar Bn al-Kaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi), ya yi masa shaida, sai Sayyiduna Umar ya ce masa: Ni fa ban sanka ba, kuma rashin saninka da ban yi ba, ba zai cutar da kai da komai ba, saboda haka ka kira wanda ya sanka. Sai wani mutum cikin jama'a ya ce: Ni na san shi. Sai ya ce: da mene ka san shi? Ya ce: Na sanshi ne da adalci gami da falala. Sai ya ce: Maƙwabcinka na kusa ne shi, da har ka san yanda yake gudanar da rayuwarsa dare da rana, da kuma lokacin shigowarsa da fitarsa? Sai ya ce: a'a. ya ce: Shin ka yi mu'amala ta dinare da dirhami (kuɗi) da shi, waɗanda da su ne

ake gane tsantsenin bawa? Sai ya ce: a'a. ya ce: Shin tafiya ta taɓa haɗa ka da shi, wanda a cikinta ka iya gane kyawawan ɗabi'unsa? Sai ya ce: a'a. Sai ya ce: in kuwa haka ne, to lallai ba ka san shi ba. sannan ya ce wa mutumin: ka tafi ka zo da wanda ya sanka.

Lallai mu'amala ta saye da sayarwa tana bayyana sifantuwa da addini na gaskiya, da kuma na ƙarya da yaudara, inda ta hakan ne ake gane sifantuwar ta baba- rodo, da kuma sifantuwa da addini ta gaskiya; Allah kaɗai ya san yawan waɗanda suke zikiri da harsunansu domin su yaudari mutane, alhali ko kusa da zikiri a haƙiƙa ba su yi ba! Allah kaɗai ne ya san yawan mutanen da suke ɓuya a bayan sifofin addini; saboda riya da jiji- da kai, ko suka ɗauki hakan a matsayin hanyar samun abin duniya, ko kuma suna amfani da hakan domin su tallata hajarsu, sun dogara da irin yanda mutane suke son addini, da kuma irin yanda mutane suka aminta da masu addini.

Cikin irin wannan sura ta yaudara: akwai kirar wasu abubuwa da sunayen da ba su dace da su ba, da niyyar ruɗar mutane da addini, ko yin kasuwanci da shi, inda a haƙiƙanin al'amari abin ba haka yake ba, kawai an shigar da addini ne domin a sami kuɗi, lallai mai yin haka yana cutar da addininsa ne, yana kuma bai wa mutane mummunar sura akan addini, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: ((**A cikin mutane akwai wasu waɗanda abin da zukatan su suka ƙulle ya saɓa da abin da harsunan su suke furuci da shi, an ba su daɗin-baki wajen tsara magana, maganar su za ta burgeka wajen yin makircinsu na janyo amfani a rayuwar duniya, a riyawarsu suna ƙarfafa maka cewa, lallai Allah ya san gaskiyar zukatansu akan abin**

**da suka faɗi da harsunansu, kuma tabbas su ɗin nan sun fi dukan sauran mutane tsananin yin husama da kai, da kuma tsananta maka. Idan aka ɗaura su a wani matsayi da za su zamana suna da wani iko, ba sa aiki domin kawo gyara, a maimakon haka ma aikin ɓarna da lalata amfanin gona, da lalata tsatso suke sanyawa a gaba, lallai Allah ba ya sonsu, domin dai lallai Allah Maɗaukakin Sarki ba ya son ɓarna)) [al-Baƙra: 204 – 205].**

Lallai addinin Musulunci ya shimfaɗa wasu ƙa'idoji da ladubba a cikin harkar kasuwanci da suka kamata Musulmi ya sifantu da su a lokacin da yake saye da sayarwa, a cikin waɗannan ladubba akwai: **zikirin Allah da kyautata hararo shi wajen mu'amala,** shi zikirin Allah abu ne da ya zamo wajibi Musulmi ya lizimce shi a koda yaushe, ana kuma yinsa ne da harshe da kuma gaɓoɓi, akwai addu'ar da aka bai wa Musulmi maza da mata umurnin karantawa kafin shiga cikin kasuwa, lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda sanda zai shiga kasuwa ya karanta:**

**لَا إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ وَحْدَهُ لَا شَرِيكَ لَهُ ، لَهُ الْمُلْكُ وَلَهُ الْحَمْدُ، يُحْيِي وَيُمِيتُ ، وَهُوَ حَيٌّ لَا يَمُوتُ ، بِيَدِهِ الْخَيْرُ كُلُّهُ، وَهُوَ عَلَى كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ..**

**to kuwa lallai Allah zai ba shi lada miliyan ɗaya, ya kuma share masa munanan ayyukansa miliyan ɗaya, sannan kuma ya gina masa gida a aljanna)**, a nan muna ƙara tabbatar da cewa, lallai zikirin Allah bai taƙaita akan zikirin da ake yi da harshe ba kawai; ya haɗa har da hararo Allah a cikin kowane yanayi, wajen neman halal da nesantar haramun.

A cikin ladubban ma akwai: **riƙo da gaskiya da nesantar ƙarya,** shi da ma tun asali Musulmi mutum ne mai gaskiya a kowane irin yanayi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya**

**ku waɗanda kuka yi imani da Allah, ku ji tsoron Allah, ku kuma kasance tare da masu gaskiya))** **[at- Tauba: 119]**, an nemi ya kasance a haka ne, har a halin saye da sayarwa a kasuwanni, sam bai halatta Musulmi ya tallata hajarsa ta hanyar ƙarya ba, domin yin haka dalili ne na ɗebe albarka a duniya, da kuma koro daga rahamar Allah Maɗaukakin Sarki a lahira, zunubin yana ƙara girma da tsanani a sanda mutum ya yi rantsuwa akan ƙarya domin kawai ya ci dukiyar waninsa, saboda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mai saye da mai sayarwa suna da zaɓi mutuƙar ba su rabu ba, idan suka yi gaskiya a tsakaninsu, sai a sanya masu albarka a cikin kasuwancinsu, idan kuma suka yi wa juna rufa- rufa, suka yi ƙarya, sai a sance albarka a cikin kasuwancinsu)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mutane uku kam, Allah ba zai yi masu magana ba a ranar alƙiyama, ba kuma zai kalle su da rahama ba: mutumin da ya rantse akan ya sayi haja sama da yanda ya saya, alhali ƙarya yake yi, da mutumin da ya yi rantsuwa ta ƙarya domin ya ci dukiyar Musulmi, da mutumin da ya hana raguwar ruwa ga waninsa, Allah zai ce masa: Lallai a yau zan hana maka falala ta, kaman yanda ka hana falalar da ba kai ka yi shi da kanka ba ga waninka),** a wata ruwayar kuma: **(Mai sayar da hajarsa ta hanyar rantsuwa akan ƙarya),** haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya yi rantsuwa alhalin ya san ƙarya yake yi, saboda kawai ya ci dukiyar Musulmi, to kuwa zai haɗu da Allah yana fushi da shi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan ce wa Sahabbansa: **(Ahir ɗinku da yawan rantsuwa wajen ciniki, domin yin haka yana sance albarka, sannan kuma ya lalata dukiya).**

Haka ma a cikin waɗannan ladubba da ƙa'idoji akwai: **kiyaye amana da kuma samun yarda tsakanin masu ciniki da junansu, da rashin yin algushi,** amana a nan tana nufin yin komai na harkar saye da sayarwa a fili, wanda hakan zai gadar da samun cikakkiyar yarda tsakanin ɓangarorin guda biya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: ((**Sai dai ya halatta ku yi kasuwanci a tsakaninku, ta hanyar yarda…))** **[an- Nisa'i: 29],** lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce wa Sayyiduna Usman Bn Affan (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa: **(Idan za ka saya ka daidaita ma'auni, idan za ka sayar ma ka cika ma'auni)**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Sa'ib (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: Na zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai mutane suka yi ta yabo na, suna faɗin alhairi a kaina, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ni na fi ku saninsa);** sai na ce: Gaskiya ne na rantse da Allah: ka kasance abokin tarayya da ni a kasuwanci, madalla da abokin tarayya irinka, ba ka ɓoye aibi, ba kuma ka ba'a.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya gargaɗi masu lalatattun zukata, da ba su hararo Ubangijinsu a kan al'amurra, ya kuma gargaɗi duk wani da gurɓatacciyar zuciyarsa take ƙawata masa ya yaudari mutane, ya ci dukiyarsu ta hanyar ɓarna da algushi, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya yi mana algushi ba shi a cikinmu).**

Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fuskantar da abokan cinikayya da su sanya amana da gaskiya su zamo su ne harsashen cinikayya a tsakaninsu, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Allah yana cewa: Ni ne na ukun masu cinikayya guda biyu, muddin ɗaya daga cikinsu bai ha'inci abokin**

**cinikayyarsa ba, idan ya yi ha'inci, sai in fice daga tsakaninsu**).

A cikin ladubban akwai: **rashin tauye ma'auni,** ma'anar tauye ma'auni shi ne: mutum ya cika ma'auni har ya wuce ƙima a lokacin da zai sayi kaya daga mutane, idan kuma zai siyar sai ya rage girman ma'aunin, ma'auni a nan na nufin duk wani abu da ake gwaji, gami da awo da shi, da mutane suke ta'amuli da shi a tsakaninsu, Allah Maɗaukakin Sarki ya bayar da umurni a cika ma'auni cikin adalci a cikin littafinsa mai girma, a inda mai girma da ɗaukaka yake cewa: **((Ku cika ma'auni idan za ku aunar, ku yi awon da daidaitaccen ma'auni, yin hakan shi ne ya fi alhairi da nagartaccen fassara)) [al- Isra'i: 35],** Allah Maɗaukakin Sarki kuma ya yi alƙawarin narko ga wanda duk ya tauye ma'auni, yana cewa: **((Halaka ta tabbata ga masu tauye ma'aunai…. Su ne waɗanda idan za su auni kaya daga mutane suke cika ma'aunai har ya yi tsororiya… Idan kuma su ne za su aunar wa mutane sai su cuce su ta hanyar tauye masu haƙƙoƙinsu)) [al- Mutaffifina: 1 – 3].**

Lallai Annabin Allah Shu'aib (AlaiHis Salam) ya gargaɗi jama'ansa da su nesanci zaluntar mutane a cikin kayansu, su kuma nesanci tauye ma'aunai, kaman dai yanda Alƙur'ani mai girma ya hakaito, Allah Mai girma yana cewa: **((Mutanen garin Madyana kuwa, mun aika masu da ɗan uwansu Shu'aib, sai ya ce: ya ku mutane na, ku bauta wa Allah, ba ku da wani Ubangiji bayansa, lallai hujjoji sun zo maku daga Ubangijinku, ku cika ma'aunai, kada ku zalunci mutane a cikin kayansu, kada ku yi ɓarna a bayan ƙasa bayan an gyara ta, yin haka shi ne abu mafi alhairi a gare ku, muddin dai ku muminai ne na gaskiya)) [al- A'araf: 85].**

A cikin ladubban kasuwa akwai: **rashin kutsawa cikin haƙƙoƙin wasu,** saboda haka ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya hana yin ciniki akan cinikin mutane, yana cewa: **(Kada wani daga cikinku ya kuskura ya yi ciniki a cikin cinikin ɗan uwansa),** a wata ruwayar kuma yana cewa : **(Kada ya yi ciniki a cikin cinikin ɗan uwansa, kada ya yi tayi akan tayin ɗan uwansa, har sai dai idan shi ne ya yi masa izini, ko kuma ya bar cinikin),** yin hakan yana cikin manyan ladubban masu daraja a cikin harkar saye da sayarwa, kada ya kwarzanta wa mai saye hajarsa ba akan gaskiya ba, haka ma kada ya kore wa ɗan uwansa masu saye, ta hanyar aibata hajar ɗan uwansa ɗan kasuwa, saboda kawai a sayi tasa hajar.

Haka ma a cikin surorin tauye haƙƙoƙin wasu akwai: **saye kaya a ɓoye su, har sai sun yi tsada,** wanda haka wargi ne da abincin mutane, yana kuma cutar da ƙasa da ma 'yan ƙasa baki ɗaya, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu mai ɓoye kayan amfani saboda su yi tsada sai mai kuskure)**, lallai mai yin haka mutum ne da son kai ya yi masa kanta, sai ya zaɓi kansa a maimakon ya fifita waninsa, ya kuma manta cewa ƙarin ribar da zai samu ta hanyar ɓoye kayan buƙata, har sai ya yi ƙaranci a kasuwanni, sannan ya fito da shi ya sayar da tsada haramun ne, kuma shi wannan kuɗi na haramun shi ne "suhtu" da zai yi kaca- kaca da shi a rayuwar duniya, kuma shi ne zai janyo masa la'anta da kora daga rahamar Allah a lahira, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk mutumin da ya ɓoye wa Musulmai abubuwan buƙatarsu saboda su yi tsada, to kuwa Allah zai jarabce shi da cuta, da kuma tarwatsewar dukiya),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya ɓoye**

**abinci domin ya sayar da tsada har na tsawon kwanaki arba'in, to kuwa lallai ba shi ba Allah Maɗaukakin Sarki, Allah Maɗaukakin Sarki ma ba shi ba shi, duk mutanen wani yankin da wani daga cikinsu ya wayi gari da yunwa, to kuwa lamunin Allah Maɗaukakin Sarki zai nesance su).**

A nan muna son mu ƙara tabbatar da cewa: lallai sanya ido a cikin kasuwanni alhaki ne da yake akan gwamnati, dole ne duka ofisoshi da ma'aikatun da abin ya shafa su yi taimakekeniya da juna wajen daƙile laifuffukan algushi, da na ɓoye kayayyakin buƙata saboda a sayar da su da tsada, da kuma na cutar masu sayen kayayyakin da ake yi, domin kawo ƙarshen waɗannan ɗabi'u marasa kyau yana taimaka wa wajen samun kwanciyar hankali a cikin al'umma, yana kuma bayar da gudummuwa wajen haɓaka tattalin arziki, da fifiko wajen nagarta a ciki da wajen ƙasa, shi kuwa algushi ƙofa ce daga cikin ƙofofin cin- hanci da rashawa, da kuma rusa ƙarfin tattalin arzikin ƙasashe.

Muna kuma ƙara tabbatar da cewa: lallai sanya ido a kasuwanni amana ce babba, alhaki ne mai girma da yake a wuyan wanda aka ɗaura masa wannan mas'uliyya, kuma lallai Allah mai girma da ɗaukaka zai tambayi kowa akan alhakin da aka ɗaura masa, shin ya kiyaye shi, ko ya tozatar da shi.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma

Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya ‘yan uwa Musulmai:** Lallai wadata mutane da abinci da abin sha, da kayayyakin buƙatunsu, mas’ala ce ta rayuwar zamantakewa mai girma, haka abu ne da yake akan gaba a cikin haƙƙoƙin bil’adama; domin babu yanda za a iya hararo wata rayuwa ta karamci ba tare da mutum ya sami natsuwa a cikin abincinsa, da magungunansa ba, saboda haka, dole ne a haɗa ƙarfi da ƙarfe a yaƙi dukan nau’o’in algushi, da na ɓoye kayan buƙata saboda su yi tsada, musamman ma a abubuwan da suka shafi abinci da magunguna.

Lallai ɗan kasuwan da ya fahimci addininsa da kyau ne, tasirin ibadunsa na sallah da azumi da sauransu suke bayyana a cikin gaskiyarsa da amanarsa, da yawan waɗanda suke yin azumin da ba su da komai a cikinsa in ba yunwa da ƙishin-ruwa ba, haka ma, da yawan masu ƙiyamullailin da ba su da komai in ba wahala da hana ido barci ba, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana girman matsayin ɗan kasuwan da ya riƙe gaskiya da amana, da irin ƙololuwar darajar da yake da ita, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ɗan kasuwa mai gaskiya kuma amintacce yana tare da Annabawa da siddiƙai da shahidai),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mafi tsarkin dukiya ita ce : dukiyar ‘yan kasuwan da idan za su yi magana ba sa ƙarya, idan kuma an amince masu ba sa ha’inci, idan kuma suka yi alƙawari, ba sa saɓawa, idan kuma za su sayi haja, ba sa aibata ta, idan kuma za su sayar ba sa kwarzanta ta, idan kuma akwai haƙƙi**

**akansu ba sa nawa, idan kuma haƙƙinsu yana kan wasu ba sa takurawa).**

Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayar da labarin cewa ɗan kasuwa mai gaskiya yana cikin inuwar al'arshin Allah Maɗaukakin Sarki a ranar da babu inuwa sai inuwarsa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ɗan kasuwa mai gaskiya yana ƙarƙashin inuwar al'arshi a ranar alƙiyama).**

Lallai muna matuƙar buƙatar yin taimakekeniya da juna saboda biyan buƙatun al'umma gaba ɗaya, domin mu duka ne za mu amfana da haka, ta yanda kowanne daga cikinmu zai yi wa ɗan uwansa kallo da idanuwan rahama, ya so masa abin da yake so wa kansa, hakan ya kai zuwa ga mai sayarwa ya yi wa mai saye gaskiya, kai ka ce shi ne mai sayen, haka ma mai saye ya yi wa mai sayarwa gaskiya, kai ka ce shi ne mai sayarwar, lallai hakan babban alama ne na imani, inda Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Imanin kowane ɗayanku ba ya cika har sai ya so wa ɗan uwansa abin da yake so wa kansa).**

**Ya Allah Ubangijinmu ka wadata mu da halal, ka nesanta mu da haram, ka isar mana da falalarka akan falalar waninka..**

## - 21 –

## RUHIN AIKI CIKIN JAMA'A DA ƘA'IDOJINSA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ka ce masu: ku yi aiki kawai, da sannu Allah da Manzonsa da sauran muminai za su gani, da kuma sannu za a komar da ku zuwa ga masanin abubuwan da suke a ɓoye, da waɗanda suke a fili, shi kuma zai ba ku labarin dukan abubuwan da kuke aikatawa)) [at- Tauba: 105].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai ba a gina al'umma da yawan surutu, ko yawan rera take, ana gina al'umma ne da ilimi, gami da baiwa da kuma sadaukar da kai, a cikin muhimman hanyoyin gina al'umma da cigabanta, akwai: aiki tuƙuru cikin inganci da nagarta, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ka ce masu: ku yi aiki kawai, da sannu Allah da Manzonsa da sauran muminai za su gani, da kuma sannu za a komar da ku zuwa ga masanin abubuwan da suke a ɓoye, da waɗanda suke a fili, shi kuma zai ba ku labarin dukan abubuwan da kuke aikatawa)) [at- Tauba: 105]**, haka ma

Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana son idan ɗayanku zai yi wani aiki, to ta kyautata shi)**, lallai addini, da kishin ƙasa duka suna matuƙar buƙatar jajircewa, da himma wajen aiki, da samar da sakamako mai kyau, musamman ma ganin cewa addininmu, addini ne na aiki tuƙuru da kuma kyautata aikin.

Duk da cewa mutum a shi ɗaya shi ne muhimmin ginshiƙi wajen gina al'umma, sai dai rawar da yake takawa ta haƙiƙa ba za ta cika ba, sai ta hanyar haɗa aikinsa da na sauran mutanen da suke rayuwa a cikin al'umma, ganin cewa ɗan Adam zai iya zartar da wasu ayyuka, amma dai idan aka gwama tunaninsa da tunanin waninsa, aka kuma haɗa ƙoƙarinsa da ƙoƙarin waninsa, to babu shakka aikin da za a zartar zai fi girma, da kuma amfanar mutane; saboda haka ne addinin Musulunci ya girmama matsayin aikin tare, ya sanya shi a cikin muhimman ginshiƙai na gina ƙasashe da cigaba, saboda ta haka ne ake amfana da dukan ƙarfin da ake da shi, ake kuma haɗa himma wuri ɗaya, ake kuma yin taimakekeniya wajen cimma manyan manufofi na bai- ɗaya da suke ɗauke da alhairai masu yawa ga mutane, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ku yi taimakekeniya akan yi wa Allah biyayya da tsoronsa, kada ku yi taimakekeniya akan saɓon Allah da zalunci..)) [al- Ma'ida: 2].**

Mai duba ta lura ga ayoyin Alƙur'ani mai girma, zai ga cewa lallai akwai ayoyi masu yawa da suke kwaɗaitarwa akan yaɗa ruhin ayyukan tare, da gabatar da ayyuka na bai ɗaya, a cikin waɗannan ayoyin akwai inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: ((**Ya ku mutane, ku bauta wa Ubangijinku wanda ya fãre ku, sannan ya halicce ku, ya kuma haɓaka ku, kamar yadda ya halicci waɗanda suka gabace ku, lallai shi ne**

**mahaliccin komai. Mai yiwuwa idan kun yi haka za ku shiga cikin sahun girmama Allah, da halarto da shi a kowane lokaci, in kun yi haka sai zukatanku su tsarkaka, su kuma yi wa gaskiya biyayya da ɗa'a, su kuma tsoraci mummunar makoma))** **[al- Baƙra: 21]**, game da sallah da take ita ce mafi girman ibada a cikin addini kuma yana cewa: **((Ku kuma tsayar da sallah..))** **[al- An'am: 72]** inda ayar ta zo da sigar jam'i, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ya waɗanda kuka yi imani, ku yi ruku'i, ku kuma yi sujada, ku bauta wa Ubangijinku, ku aikata ayyukan alhairi ko za ku sami babban rabo))** **[al- Hajji: 77]**, haka ma mai girma da ɗaukaka ya yi wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) magana da cewa: **((Ya kai wannan Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ka cigaba ta kiyaye abokantakarka da sahabbanka muminai, da suke bauta wa Allah shi kaɗai safe da yamma a koda yaushe, suna neman yardar Allah, kada idanuwanka su kauce ga barinsu zuwa ga masu musu, cikin kafirai da niyyar jin daɗi da kayan ƙawa na duniya a tare da su, kada ka amsa kiran waɗanda muka sanya zukatansu suka rafkana ga barin ambantonmu, waɗanda hakan ya faru ne sakamakon munin shirinsu, suka kuma zamo bayin son zuciyarsu, inda ɗaukacin ayyukansa suka yi nesa da daidai, na ka kori talakawan muminai daga majalisarka))** **[al- Kahfi: 28]**, Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku yi riƙo da igiyar Allah gaba ɗayanku, kada ku soma su rarraba..))** **[Ali Imran: 103]**. Mai girma da ɗaukaka ya gargaɗe mu akan rarrabuwa a inda yake cewa: **((Ku yi Allah da Manzonsa biyayya, kada ku kuskura ku yi rikici, sai rashin nasara ya same ku, kwarjininku ya tafi, ku yi haƙuri, lallai Allah yana tare da masu haƙuri))** **[al- Anfal: 46]**.

Lallai babu shakka cewa, gabatar da ayyuka da ruhi na jama'a, abu ne da yake ƙarfafa soyayya, da ƙauna, da 'yan uwantaka, da kuma ƙara kusanto da al'umma da junansu, inda a ƙarshe za su zamo kaman yanda Allah Mai girma ya sifantasu da cewa: **((Lallai wannan al'umma taku, al'umma ce guda ɗaya..)) [al- Anbiya'i: 92; al- Muminuna: 52]**, hakan kuma ya gasgata maganar Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yake cewa: **(Misalin muminai wajen soyayyar junansu, da jinƙan junansu, da tausayin junansu, kaman jiki ne da idan wata gaɓa da cutu, sai sauran jiki ya kamu da rashin barci gami da raɗaɗin ciwo)**, lokacin da wani shehi ya yi nufin karantar da 'ya'yansa muhimmancin haɗin kai, da bayyana masu cewa hakan shi ne yake samar da ƙarfi na haƙiƙa, ya kuma tsoratar da su hatsarin da yake tattare da rarrabuwar kawuna, kuma hakan shi ne sababin tozarta, da tarwarsewa, sai ya kawo masu ɗaurin ƙirare, ya kuma ce: a cikinku wane ne zai iya karya wannan ɗaurin ƙiraren a yunƙuri ɗaya ko yunƙuri biyu?, kowa daga cikinsu ya yi abin da zai iya, amma bai sami nasara ba, sai ya kwance ɗaurin ƙiraren ya rarraba wa 'ya'yansa, kowannensu aka ba shi icce ɗaya, ya kuwa karya shi a tashi ɗaya, sai ya ce masu:

"Ƙiraren kibiya sun fi ƙarfin a karya su a lokacin da suke a ɗaure a wuri ɗaya, amma idan aka rarraba sai a karya su ɗaya bayan ɗaya.."

Lallai Alƙur'ani mai girma ya kawo mana misalai masu kyau, da suke kwaɗaitarwa akan aikin tare, ya kuma bayyana irin tasirin aikin tare wajen zartar da manyan manufofi, alal misali: ga Sayyiduna Ibrahim (AlaiHis salam) lokacin da Allah Maɗaukakin Sarki ya umurce shi da ya gina Ka'aba mai daraja,

ya tafi wurin ɗansa Annabi Isma'il (AlaiHis salam) ya ce masa: Allah ya ba ni wani umurni. Sai ya ce: ka aikata abin da Ubangijinka ya ba ka umurnin aikatawa. Sai ya ce: za ka taimaka mini kuwa?. Sai ya ce: ƙwarai, zan taimaka maka. Sai ya ce: lallai Allah ya ba ni umurnin in gina masa ɗaki a nan. A lokacin ne suka gina ginshiƙan wannan ɗaki, inda Annabi Isma'il (AlaiHis salam) yake ɗauko duwatsu, Annabi Ibrahim (AlaiHis salam) kuma yana gini, sai suka haɗu suka gina farkon ɗakin da aka samar a bayan ƙasa domin bauta wa Allah Maɗaukakin Sarki, lallai Alƙur'ani mai girma ya dawwamar da wannan muhimmin abu mai girma a inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka ambata masu lokacin da Annabi Ibrahim da Annabi Isma'il (Alaihimas Salam) suke gina ginshiƙan Ka'aba, suna addu'a cewa: Ya Ubangijinmu ka amshi wannan aiki daga gare mu, domin dai kai mai yawan ji ne, mai kuma cikakken masaniya))** **[al- Baƙra: 127]**..

A cikin suratul Kahfi ma, Ubangijinmu mai girma da buwaya ya ba mu labarin wani babban misali na taimakekeniya, da kuma cika juna, da kuma yin aiki da ruhin jama'a a ƙissar Zul Ƙarnaini, lokacin da wannan adalin Sarki ya kai zuwa wa ga wasu mutane da shi ya sansu, amma su ba su sanshi ba, suka nemi taimakonsa, ya kuma amsa masu akan abin da suka nema, amma kuma duk da haka, sai da ya ɗaura masu nauyin yin taimakekeniya tare da shi, ya shigar da su wajen zartar da abin da suka nema, ya yi amfani da ƙarfinsu, inda dukansu suka taka rawa wajen gina wannan babban gini, wanda ya zamo sanadin ba su kariya daga cutarwar Yajuju da Majuju, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Har sai da suka**

**isa wani wuri mai nisa tsakanin duwatsu guda biyu –a tafiyarsa ta biyu-, a can ne ya tarar da wasu mutane da ba sa iya fahimtar abin da ake faɗa masu sai da ƙyar gami da wahala, lokacin da suka fahimci yana da ƙarfi sai suka nemi da ya gina masu wata katanga da za ta shiga tsakaninsu da Yajuja da Majuja, wasu jama'a ne da suke kawo masu hari, su lalata masu ƙasa, su kuma rusa komai, sun nemi hakan ne akan su ba shi wani lada a makwafin wannan aikin. Sai ya amsa masu da cewa: lallai baiwar da Allah ya yi mini na dukiya, da iko sun fi alhairi akan abin da kuke yi mini tayi. Sai kuwa ya fara aikin samar da wannan katanga, ya kuma nemi da su taimaka masa da duk abin da za su iya, na ma'aikata da kayan aiki, domin ya samar masu da abin da suka buƙata. Ya nemi da su tattaro masa guraguntsin ƙarafa, suka kuwa tara masa abin da ya buƙata, sai kuwa ya gina masu wata doguwar katanga da ta yi daidai da tsawon duwatsu guda biyu, sannan ya umurce su da su hura mata wuta, suka kuwa hura har sai da ƙarafan nan suka narke, sai kuwa ya zuwa mata narkakkiyar dalma, ta zamo katangar ƙarfe mai inganci. Waɗannan masu kawo harin ba su iya su haura wannan katanga ba saboda tsawonta, ba kuma su iya su huda ta ba saboda nagartarta..))** **[al- Kahfi: 93 – 97]**

Haka ma KalimulLah, Annabi Musa (AlaiHis salam), ya roƙi Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka akan ya ƙarfafi gwiwarsa da ɗan uwansa Haruna (AlaiHis salam); domin ya taimaka masa wajen sauke nauyin da Allah Maɗaukakin Sarki ya ɗaura masa, a inda Allah Maɗaukakin Sarki yake faɗi a harshen Sayyiduna Musa (AlaiHis salam) cewa: **((Annabi Musa (AlaiHis salam) ya ce: Ya Ubangiji, ka haskaja ƙirji na, ka kuma sauƙaƙe mini**

**al'amari na, ka warkar mini da in'inar harshe na, ta yadda mutane za su fahimci zance na, ka kuma samar mini da mataimaki daga dangi na, Ina nufin Haruna ɗan uwana, da zai ƙarfafa mini gwiwa, in sanya shi cikin al'amurra na, ta yanda za mu tsarkake ka sosai, mu kuma ambace ka da yawa, lallai kai masanin halin da muke ciki ne..))** [Taha: 25 – 35].

Haka ma mai duba ta lura zuwa ga tarihin Annabi mai cike da daraja, zai ga shafuffuka masu haske na taimakekeniya, da ayyukan tare a cikin rayuwar Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da sahabbansa masu girma, Sayyiduna Usman Bn Affan (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **(Wallahi mun abokanci Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) a halin tafiya da halin zaman gida, ya kasance yana taimakekeniya da mu a cikin abu kaɗan da mai yawa)**.

Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan yi tarayya da su wajen ayyuka da gini da kansa, yana kuma kwaɗaitar da su wajen haɗin kai, da rashin rarrabuwa, game da ranar al-Handaƙ ne Sayyiduna al-Barra'u Bn Azib (Allah ya ƙara yarda da shi) yake cewa: **Na ga Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) a ranar al- Ahzab yana ɗaukan ƙasa, kai har turɓaya ta rufe farin fatar cikinsa, yana cewa : (Ya Ubangiji ba domin kai ba, da ba mu shiryu ba, da ma ba mu gasgata samuwarka ba balle mu yi sallah, saboda haka ya Allah ka saukar mana da natsuwa, ka tabbatar da mu idan muka haɗu da maƙiya, lallai waɗannan sun zalunce mu, ya Ubangiji idan sun nufe mu da wata fitina ka kare mu)**..

Lokacin da Sayyiduna Salmanul- Farisiy (Allah ya ƙara yarda da shi) ya nufi dasa dabinai ɗari uku; domin yan fanshi kansa daga ƙangin bauta, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa

sallam) ya faɗa wa sahabbansa cewa: **(Ku taimaki ɗan uwanku)**.. Sai Salmanu (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: sai kuwa suka taimaka mini da dabinai, sai ka ga mutum ɗaya ya kawo iccen dabinai talatin, wani ya kawo ashirin, wani goma sha biyar, kowa yana kawo gwargwadon abin da yake da shi, har dai aka tara dabinai ɗari uku, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya umurce ni da in haƙa masu ramuka, ya ce: **(Idan ka gama, ka zo ka faɗa mini, ni da kai na zan dasa su da hannu na)**. Ya ce: sai na haƙa masu ramuka, abokai na ma suka taimaka mini, da muka gama, sai na tafi na faɗa masa, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fita tare da ni, muna kusanto masa da iccen dabino, shi kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana dasawa da hannunsa.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yabi ƙabilar Ash'ariyyawa sosai; saboda ruhin aikin tare da suke da shi, wanda yake bayyana a ayyukansu a lokuta masu wahala, a inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Lallai idan guzurin Ash'ariyyawa ya ƙare a lokacin da suka tafi yaƙi, ko abincin iyalansu a cikin gari ya yi ƙaranci, sai su harhaɗa abin da ya rage masu a wuri ɗaya, sannan su sake rabawa a tsakaninsu daidai wa daidai, su kam daga gare ni suke, ni ma daga gare su nake).**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

--------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma

Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai aikin taren da muke haƙilon tabbatuwarsa, shi ne wanda yake gina al'umma, ba mai rusa su ba, yake kuma haɗa kan al'umma, ba rarraba kawunansu ba, shi ne wanda aka gina shi akan halattattun ginshiƙan da Shari'a ta zo da su, irinsu taimakon da yake gudana tsakanin mutanen da suke rayuwa a cikin al'umma ɗaya, ta yanda ba za a sami mai jin yunwa, ko wani mai buƙata ba a cikinsu ba, ko kuma akan ginshiƙan tarbiyya da na ilimi, kaman taimakekeniyar da malamai suke yi a cikin bincike - bincikensu na ilimi, da taimakekeniyar da ɗalibai suke wajen zartar da ayyukan karatunsu, ko akan ginshiƙai na kishin ƙasa; domin ciyar da ƙasa gaba akan ɗaukacin fagage..

Ba wai aikin da aka gina shi akan kiraye - kirayen da suka haɗu akan kisa, da rusa garuruwa, da zubar da jini, da rusa ƙasashe, da ƙoƙarin raunanata, ko ma kifar da ƙasa ba, waɗannan dai kiraye - kirayen da aka gina su akan kare-rayi da ƙirƙirar sharri, da sauya gaskiya.. kiraye - kirayen da babu ruwansu da addini, ko kishin ƙasa, da kyawawan ɗabi'u.

Lallai aikin taren da muke rajin ganin faruwarsa, shi ne: nagartaccen aikin da aka samar da shi domin amfanuwar addini, da ƙasa, da mutuntaka, abubuwa ne guda biyu da ba sa rabuwa da juna, lallai muna matuƙar buƙatar dasa irin wannan ruhi a cikin zukatan 'ya'yanmu, ta yanda zai zamo masu manhajin rayuwa da za su gudanar da rayuwarsu akansa, hakan kuma ya yi sanadiyyar yaɗuwar soyayya, da taimakon

juna a cikin al'umma ɗaya, mu ciyar da al'ummarmu gaba zuwa matakin da ya dace da ita a dukan fagage.. Lallai muna ƙara tabbatar da cewa a duk sanda ruhin aikin tare ya kukkutsa a cikin al'umma Musulma, to takan gabatar da ayyukan da ba a taɓa zaton samuwarsu ba, tarihi ne babban dalilin da yake tabbatar da wannan maganar..

**Ya Allah Ubangiji, ka tabbatar mana da tsaro a cikin ƙasashenmu, ka datar da malamanmu, da shugabanninmu, ka kiyaye mana ƙasashenmu daga makircin masu makirci, da ɓarnar maɓarnata..**

## - 22 –

## DALILAI NA ZAHIRI DA NA BAƊINI WAJEN YAYE BALA'I..

## DA WAJIBCIN YI WA SHUGABANNI BIYAYYA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangiji talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya Ubangijinmu, gare ka muka dogara, kuma zuwa gare muka mayar da dukan al'amurranmu, makomarmu ma tana wurinka ne))** **[al-Mumtahanat: 4].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa tsira da aminci da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai jarrabawa Sunna ce daga cikin Sunnonin Allah mai girma da buwaya a cikin halittu, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai mu, mun halicci ɗan Adam ne daga maniyyin da yake ƙunshe da sinadarai mabambanta, domin daga baya mu jarabce shi ta hanyar umurni da hani, sai muka mayar da shi mai ji da gani; domin ya ji ayoyi, ya kuma ga dalilai))** **[al- Insan: 2].**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya samar da wasu dalilai na zahiri, da na baɗini da suke kai wa zuwa ga yaye bala'o'i; **su dalilai na zahirin** da suka zama wajibi a rungume su –kaman su ne komai da komai- dukansu dalilai ne na ilimi, da matakan

kar – ta- kwana na masana fanni, da ƙwararru, da zartar da faɗakarwa gami da umurnin ma’aikatun gwamnati, lallai yi wa shugaba biyayya, ko waɗanda suke wakiltan shugaba, ko masu wakiltan ma’aikatun gwamnati abu ne da ya zama wajibi, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ku yi wa Allah biyayya, ku kuma yi wa Manzon Allah biyayya, da shugabanni daga cikinku…))** **[an- Nisa’i: 59]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((Ku tambayi masana idan dai har ba ku sani ba))** **[an- Nahl: 43; al- Anbiya’i: 7]**; kalmar: **“Ahlaz Zikr”** a nan tana nufin masana, kuma ƙwararru na kowane fanni; saboda haka dole ne a nesanci yin katsalanda a cikin ayyukan ma’aikatun gwamnati, kowanne a fagen ayyukanta.

**Haka ma a cikin dalilai na zahiri akwai: muhimmanta tsabta;** lallai addinin Musulunci ya muhimmanta tsabta a dukan fagage, inda ya sanya ta zamo wajiba a cikin Shari’a; domin kiyaye ɗan Adam daga cututtuka, da annoba, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai Allah yana son masu yawan tuba, yana kuma son masu yawan tsarki))** **[al- Baƙra: 222]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Tsarki rabin imani ne..)**, a wani wurin kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ku tsarkake farfajiyarku..)**, farfajiya a nan ta ƙunshi: farfajiya ta gida, da ta makaranta, da ta kamfunna, da ta hanyoyi, da dandula da sauransu. **Haka ma addinin Musulunci ya bai wa waken hannaye muhimmanci na musamman** a duk sanda za a yi alwalla, Allah mai girma yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani: idan har kun yi nufin tashi domin yin sallah ba kuma ku da alwalla, to ku yi alwalla, kuna masu wanke fuskokinku, da hannayenku zuwa gwiwar hannu, ku kuma shafi kawunanku –duka ko kuma**

**wani sashe- ku kuma wanke ƙafafuwanku zuwa idon sawu. Idan kuma a lokacin da za ku tashi yin sallah ɗin kuna cikin halin janaba ne sakamakon kusantar iyali, to ku wanke gaba ɗayan jikinku da ruwa)) [al- Ma'ida: 6]**, wanke hannaye biyu tare da gwiwowinsu, ɗaya ne daga cikin farillan alwalla, bugu da ƙari kuma, Sunna ne a wanke hannaye sau uku a lokacin fara alwalla, sannan kuma kurkurar baki, sannan shaƙar ruwa a hanci, sannan wanke fuska, sannan a sake wanke hannaye tare da gwiwowinsu a karo na biyu a nan farali ne, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idan ɗaya wani cikinku ya farka daga barcinsa, kada ya shigar da hannayensa a cikin ƙwaryar tsarki har sai ya wanke su sau uku)**, haka ma "Mustahabi" ne mutum ya wanke hannayensa kafin cin abinci da bayan cikin abinci; wannan yana ƙara tabbatar da cewa; lallai babu cin karo tsakanin ilimi da addini, kiyaye lafiyar ɗan Adam yana kan gaba cikin manyan manufofin addini, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Babu cuta, babu cutarwa)**, saboda haka dole ne a bi dukan matakan kariya, da na riga- kafin da aka samar domin hana yaɗuwar cututtuka da annoba, kaman nesanta gaisuwa ta rungumar juna, ko ta sumbantar juna, a rage musafaha, a kuma nesanci taro da cincirundon jama'a.

A nan muna son mu ƙara tabbatar da cewa: lallai a cikin masifu, da jarrabawowi masu tsanani ne ake gane haƙiƙanin mutane, da ainihin ɗabi'unsu, **dole ne mu zamo masu tausayi da jinƙan juna**, mu nesanci duk wata haɗama da son kai, mu nesanci ɓoye kayayyakin amfani da 'yan kasuwa suke yi; domin su yi tsada, ko haɗama da son kai da masu saye suke yi wajen saye kayayyaki sama da buƙatarsu, abin da yake kai wa

zuwa ga dagula harkar kasuwanci, da lalata dangantakar da take tsakanin hajar da aka sanya a kasuwa, da kuma irin nema, ko buƙatar da mutane suke yi zuwa gare ta, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu mai ɓoye kayayyakin amfani saboda farashinsu ya hau sai mai kuskure..)**, haka ma a wani wurin (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mai ɓoye kayan amfani saboda farashinsu ya hau la'ananne ne)**, a wani wurin kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu wani daga cikinku da zai sami cikakken imani har sai ya so wa ɗan uwansa abin da yake so wa kansa)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabinmu Muhammadu da Alayensa da Sahabbansa, da waɗanda suka biyo bayansu.

**Ya 'yan uwana Musulmai: Su kuwa dalilai na baɗini** da suka kamata a koda yaushe mu muhimmanta su, a cikinsu akwai: **kyakkyawar dogara da Allah**, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ka dogara ga Allah shi kaɗai, lallai Allah yana son masu dogaro da shi)) [Ali Imran: 159]**, shi dogaro da Allah ba kishiyar aiki da sababi ba ne, lallai wani mutum ya ce wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam): In ɗaure ta, sannan in dogara da Allah, ko kuwa in sake ta sannan in dogara da Allah? (yana nufin taguwarsa) sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce masa: **(Ka ɗaure ta, sannan ka dogara da Allah)**, abin da ya wajaba akan mu a wannan lokacin shi ne:

mu yi aiki da dukan dalilai, gami da sabubban samun lafiya, da riƙo da matakan da ilimi suka samar, sannan kuma mu miƙa dukan al'amurranmu zuwa ga Allah mai girma da buwaya, wanda mulkin komai yake hannunsa, wannan shi ne tawakkali na gaskiya, ba riƙon sakainar kashi ba.

Haka ma a cikinsu akwai: **addu'a da ƙasƙantar da kai a gaban Allah mai girma da buwaya,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ina ma a ce lokacin da tsananinmu ya zo masu sun ƙasƙantar da kansu a gabanmu..)) [al- An'am: 43]**, lallai muna matuƙar buƙatar mu ƙasƙantar da kawunanmu da gaskiya - gaba ɗayanmu- a gaban Allah Maɗaukakin Sarki, saboda ya yaye wannan bala'in ga barin ƙasashenmu, da mutanen ciki, da ma duniya baki ɗaya, ya kuma sanya wannan bala'in ya zamo mana wata dama ce ta bitar dangantakar kowannenmu da Ubangijinsa.

Haka ma akwai: **kowanne mutum ya katange kansa da zikirin Allam Maɗaukakin Sarki**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu wani bawa da zai karanta "BismilLahil Lazi la yadhurru ma'a ismihi shai'un fil ardhi wa la fis sama'i wa huwas sami'ul alim" safiyar kowace rana, da yammacin kowane dare, sau uku, sannan kuma wani abu ya cutar da shi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda ya sauka a wani gida, sai ya karanta: "A'uzu bikalimatil Lahit taamaati min sharri ma khalaƙa" babu abin da zai cutar da shi har zuwa ya tashi daga gidan)**, haka ma akwai: **sadaka,** Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ku kiyaye dukiyoyinku da zakka, ku yi wa marasa lafiyanku magani da sadaka, ku yi wa bala'i tattali da addu'a)**.

**Ya Allah Ubangiji ka ba mu lafiya a cikin bayinka da ka ba su lafiya, ka jiɓinci al'amurranmu a cikin bayinka da ka jiɓinci al'amurransu, ka kiyaye mu daga sharrin abin da ka ƙaddara, ka kiyaye ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya.**

- 23 –

## GUDANAR DA KOMAI AKAN ƘA'IDAR BIN SABABI:

## SUNNA CE TA ALLAH MAƊAUKAKIN SARKI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ka ce masu: ku dai kawai ku yi aiki, da sannu Allah da Manzonsa za su gani, haka ma sauran muminai, da sannu za a mayar da ku zuwa ga masanin abubuwan da suke a ɓoye da waɗanda suke a fili, ya kuma ba ku labarun abubuwan da kuke aikatawa))** **[at- Tauba: 105]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya wa ɗaukacin halittunsa wasu sunnoni, da dokoki da suke tafiya akansu, da ma wasu ƙa'idoji da ba sa sauyawa, abu na biyu ba zai taɓa riga na farko ba, haka ma na farko ba zai noƙen da har na biyu ya riga shi bayyana ba, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Ba zai taɓa yiwuwa rana ta riski wata ba, haka ma dare ba zai taɓa riga rana fitowa ba, kowanne daga cikinsu yana tafiya ne akan gwadabensa na daban))** **[Yasin: 40]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗi: **((Ba za ka taɓa samun sauyi a**

**cikin sunnar Allah ba, kai ma ba za ka taɓa samun jirkita a cikin sunnar Allah ba))** **[Fatir: 43]**, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya waɗannan sunnoni ne su zamo wani ma'aunai, da ƙa'idoji da za su daidaita rayuwa, da kuma su ne za a sami daman raya ƙasa, da ba ta kariya, wanda hakan ɗaya ne daga cikin manufofin halitta, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah shi ne ya halicce ku daga ƙasa, ya kuma nemi da ku raya ta..))** **[Hud: 61]**, haka ma Allah mabuwayi yana cewa: **((Kada ku kuskura ku yi ɓarna a bayan ƙasa bayan an riga an gyara ta..))** **[al- A'araf: 56, 85]**, babu shakka duk al'ummar da ta fahimci haƙiƙanin waɗannan sunnoni na Ubangiji, ta kuma yi aiki akan saninta, za ta ɗaukaka, ta kuma sami cigaba, koda kuwa ba Musulma ba ce, kai koda ma ba ta da wani addini kwata – kwata; saboda waɗannan sunnonin ba su san alfarma da kamun ƙafa, ko kusanci da wata halitta ba.

Lallai a cikin waɗannan sunnoni na halitta da Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya akwai: **gudanar da komai akan sababi;** lallai Allah Maɗaukakin Sarki ne ya halicci sabubba da abubuwan da sabubban suke haifarwa, ya kuma bayar da umurnin yin aiki da sababi wajen gudanar da kowane irin abu, idan har aka sami sababi, to kuwa za a sami sakamakon sababi, wannan doka ne da ya game komai da komai, babu wani a cikin halittu –a kuma dukan zamunna da wurare- da bai bin wannan dokar, komai yana da sababi, wuta sababi ne na ƙuna, haka ma kisa sababi ne na mutuwa, haka ma noma da iri sababi ne na samun amfanin gona, abinci sababi ne na ƙoshi, ƙoƙari da ijtihadi sababi ne na samun nasara, kasala da nauyin jiki sababi ne na koma- baya da rashin nasara, da sauransu.

Lallai umurnin da Allah Maɗaukakin Sarki ya bayar na neman arziki ta hanyar aki a bayan ƙasa, umurni ne na farali a addini, wajibi ne na shari'a, kuma yin hakan nuna kishin ƙasa ne, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shi ne wanda ya sanya ƙasa ta zamo maku sauƙaƙƙa, ku yi tafiya a sasanninta, ku ci daga cikin arzikin Allah da ya fitar maku daga gareta, zuwa gare shi -shi kaɗai- za ku koma domin sakamako)) [al-Mulki: 15]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Idan kuma kun gabatar da sallar, to ku bazama a bayan ƙasa saboda maslahohinku, ku nemi falalar Allah, ku yawaita ambaton Allah a zuci da baki, ko za ku sami babban rabo na alhairi a duniya da lahira)) [al- Juma'a: 10]**, wannan shi ne ma'anar da addinnin Musulunci yake nufi da neman arziki a bayan ƙasa ta hanyar aiki tuƙuru da ijtihadi, da raya doron ƙasa, ba mu da wata hujja ta zamowar mu a baya, ba mu da wani dalili akan haka, in ba kasala da son jiki, da ci-baya ba.

Duk wanda zai yi la'akari da tarihin Annabawa da salihan bayan Allah zai ga irin yanda suke ƙoƙari wajen yin aiki da sababi a cikin komai na rayuwarsu, ga Annabi Nuhu (AlaiHis Salam) nan kafinta ne, bayan ya ɗauki shekaru masu yawa yana kira zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki, Allah Mai girma da ɗaukaka ya ba shi umurnin ƙera jirgin ruwa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ka ƙera jirgin ruwa a ƙarƙashin kulawarmu, da kuma wahayin da za mu yi maka, kada ka kuskura ka yi mini magana akan azzalumai, tabbas sunansu dilmiyayyu)) [Hud: 37]**, abu ne mai yiwuwa Allah Maɗaukakin Sarki ya tseratar da shi ba tare da wani sababi, ko aiki ba, sai dai Allah a nan ya koya mana yanda ake bin sababi sau da ƙafa, sai kuwa Annabi Nuhu (AlaiHis Salam) ya amsa umurnin

Ubangijinsa, ya kuma fara ƙera jirgin ruwan da aka ba shi umurni, bai yi jinkiri, ko nawa ba, duk kuwa da izgilancin da mutanensa suka fara yi masa game da haka, Allah Maɗaukakin Saki yana cewa: **((A haka kuwa ya fara ƙera jirgin ruwa, a duk sanda masu faɗa a jin cikin mutanensa suka wuce ta masana'antarsa, sai su riƙa yi masa izgilanci akan haka, sai shi kuma ya ce masa: idan kun yi mana izgilanci a yau, mu ma gobe za mu yi maku izgilanci kaman yanda kuka yi mana))** **[Hud: 38]**, ya cigaba da aikinsa, sai kuwa Allah Maɗaukakin Sarki ya saka masa da tseratar da shi, da sauran muminai daga barin mutanensa.

Haka ma Annabi Dawud (AlaiHis Salam) maƙeri ne, Allah ya sanar da shi wata sana'a da za ta amfane shi, ta kuma amfani mutanensa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Tabbas mun bai wa Annabi Dawud (AlaiHis Salam) falala daga wurinmu da muka ba shi hikima, da littafi, sai muka ce: Ku duwatsu ku maimaita tasbihin da yake yi, haka ma mun hore masa tsuntsaye da suke maimaita irin yanda yake tsarkake Ubangiji Allah, mun kuma hore masa baƙin ƙarfe inda yake taushi a wurinsa, yana sana'anta abin da yake so da shi. Mun yi masa wahayin ya sana'anta silaku masu yalwa da za su bayar da kariya daga harin maƙiya, ya kuma kyautata sana'anta su, inda ya shigar da haƙoran cikin junansu, sannan muka faɗa masa, shi da iyalansa cewa: ku aikata abin da zai amfane ku, ya kuma amfani al'ummarku, lallai ina ganin abubuwan da kuke aikatawa babu wani abu daga ciki da zai ɓuya mini))** **[Saba'i: 10 – 11]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ɗan Adam bai taɓa cin wani abinci da yafi**

**wanda ya same shi da guminsa ba, lallai Annabi Dawud (AlaiHis Salam) ma guminsa yake ci).**

A cikin ƙissar Annabi Yusuf (AlaiHis Salam) ma riƙo da sababi, da yin tsari mai kyua su ne dalilan da suka sanya ƙasa, da ma 'yan ƙasa suke tsira daga bala'in yunwa mai halakarwa, wanda hatsari da babu makawa ya auku in ba an mutunta sababi, da ɗaukan mataki kafin faruwarsa ba, lallai Annabi Yusuf (AlaiHis Salam) ya yi riƙo da sababi, ya kuma samar tsari mai dogon zango, na tseratar da ƙasar daga annobar yunwa da ta doso wa duniya baki ɗaya, a dalilin haka kuwa sai ƙasar ta sami haɓakar tattalin arziki, da tsaro, da ƙarfin tsumi da tanadi, sauran mutanen duniya kuma –daga baya- suka yi wa Misra tsinke; domin su amfana da alhairanta, lallai Alƙur'ani mai girma ya faɗi haka, ta bakin Annabi Yusuf (AlaiHis Salam) a inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Ya ce: shekaru bakwai za ku yi a jere –kaman yanda kuka saba- kuna noma, duk abin da kuma samu ku bar shi a cikin zangarniyarsa, in banda kaɗan ɗin da za ku ci. Daga baya kuma, wasu shekaru bakwai ɗin masu tsanani za su biyo baya da za ku ci abin da kuka riga kuka adana, kuna masu rage kaɗan gudun ko ta-kwana, sannan bayan haka kuma sai shekarar da mutane za su nemi taimako ta zo, a cikin ne kuma amfanin gona zai fara bayyana))** **[Yusuf: 47 -49].**

Ga ma Sayyida Maryam (AlaiHas Salam) nan da arziki mai yawa yake zuwa mata, abin da har sai da Annabin Allah Zakariyya (AlaiHis Salam) ya kamu da mamaki, har ya ce mata –kaman yanda Alƙur'ani mai girma ya kawo ta bakinsa- cewa: **((Duk sanda Annabi Zakariyya (AlaiHis-Salãm) ya shiga wajen da take bauta, sai ya sami kayayyaki na marmarin da**

**ba lokacin su ne ba, sai ya ce- yana cike da mamaki- ya Maryam, ina kika sami wannan arzikin? Sai ta ce: Ai wannan kaɗan ne cikin falalar Allah, Allah ya riga ya sanya Annabi Zakariyya (AlaiHis-Salãm) shi ne mai kula da ita. Arzikinta yana zuwa mata ne babu adadi, ba kuma lissafi))** **[Ali Imran: 37]**, a wani yanayin kuma, duk da rauni da wahalar raɗaɗin da take ciki, sai da Allah Maɗaukakin Sarki ya umurce ta da girgiza tushen dabino domin 'ya'yan dabinon su faɗo mata, da Allah Maɗaukakin Sarki ya so su faɗo mata ba tare da wani aiki ba, da ya yi, sai dai bai yi hakan ba; saboda ya koya mana yanda aiki rungumar aiki tuƙuru, da kuma riƙo da sababi, Allah mai girma yana cewa: **((Ga bishiyar dabino nan kusa dake, ki girgiza ta, 'ya'yan dabinon ɗanye masu daɗi za su faɗo miki))** **[Maryam: 25]**, alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa:

"Ka dogara da Allah mai yawan rahama a cikin dukan al'amurra, kada ka taɓa fatan samun gajiyawa wajen nema; ashe ba ka ga cewa Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗa wa Maryam cewa: **((Ga bishiyar dabino nan kusa dake, ki girgiza ta, 'ya'yan dabinon ɗanye masu daɗi za su faɗo miki))** **[Maryam: 25]** ba?! Da ya so ta samu ba tare da girgizawa ba, da ta samu, amma dai komai yana da sababi".

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya buga mana babban misali wajen riƙo da sababi a tafiyarsa ta hijira mai albarka, inda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya koya wa al'ummarsa cewa: lallai kyakkyawan tsari, da nagartaccen shiri abubuwa ne da suka wajaba a yi su, muddin ana buƙatar nasara, da kuma kaucewa matsaloli, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya samar da abin hawa guda biya, ya kuma zaɓi aboki kuma amini a wannan tafiya, ya kuma tsara lokaci,

ya kuma zaɓi hanyar da zai bi wajen wannan hijira tasa, sai ya fita da daddare daga gidan Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi), ya kuma zaɓi ɗan jagora da ya san hanya, saboda ya yi imani da zaɓen mutumin da ya fi cancanta akan komai, da kuma yin amfani da daman da ake da ita, komin bambancin ra'ayi, da tunani da yake tsakani, kai komin bambancin addini ma kansa, sannan ya umurci Sayyiduna Amir Bn Fuhair (Allah ya ƙara yarda da shi) da ya bibiye su, yana share sawun ƙafafuwansu da dabbobinsa, wannan ma riƙo ne da sababi, duk kuwa da yana da cikakkiyar masaniyar cewa Allah Maɗaukakin Sarki zai kare shi, shi da abokin tafiyarsa, kawai dai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi nufin ya karantar da mu ce cewa lallai sunnar Allah Maɗaukakin Sarki a cikin halittunsa tana wajabta yin riƙo da sababi, sannan bayan haka kuma a miƙa al'amari ga Allah mai girma da buwaya.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

---------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa baki ɗaya, da duk waɗanda suka bi shi da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai riƙo da sababi ba kishiyan dogaro da Allah Maɗaukakin Sarki ba ne, duk wanda ya san haƙiƙanin dogaro da Allah zai yi iya bakin ƙoƙarinsa wajen riƙo

da sabubba, mai dogaro da Allah na haƙiƙa shi ne wanda yake riƙo da sabubba, yake kuma iya bakin ƙoƙarinsa wajen bin sababi, sannan daga ƙarshe ya miƙa al'amurra zuwa ga Allah, wanda shi ne mai datarwa, da mai kuma falala gami da taimako, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kai kawai muke bauta wa, kuma gare muke neman taimako))** **[al- Fatiha: 5]**, a wani yanayi na dogaro da Allah a aikace kuma, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Da za ku dogara da Allah kaman yanda ya kamata, da kuwa Allah ya azurta ku, kaman yanda yake azurta tsuntsu, yakan wayi gari cikinsa a ɗame, ya kuma yammanta a ƙoshe)**, tsuntsu ba ya adana abinci balle abin sha, sai dai duk da haka, ba ya nawa wajen neman arziki, tun safe yake fara fita nema wajen bincike da biɗa, ya kuma dawo bayan Allah Maɗaukakin Sarki ya azurta shi da abin da zai ishe shi daga cikin falalarsa, yakan fita yana kai komo, wannan kuwa fiɗira ce ta halitta, ta inda koda yana da abin da zai ishe shi a gaba ɗayan rayuwarsa, ba zai yi kasala, ya zauna ya huta ba, a'a zai cigaba da fita nema a kowace safiya..

Lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan sanar da sahabbansa haƙiƙanin ma'anar riƙo da sababi, yana kuma hana su zama kawai, ba tare da himma ba, zaman da cuta take gadarwa ba amfanarwa ba, lallai ba za mu wuce gona da iri ba, idan muka faɗi cewa: lallai zunubi muke aikatawa, muna kuma zaluntar kawunanmu da 'ya'yanmu; saboda rashin yin riƙo da sabubba gami da dalilan cigaba da bunƙasa, addininmu addini ne na ilimi da cigaba da halara da kyau, da amfanar ɗaukacin mutane baki ɗaya, wani mutum ya ce: ya Manzon Allah, shin in saki taguwa ta, in dogara da Allah?, ko in ɗaure ta, sannan in dogara da Allah? Sai (SallalLahu alaiHi wa sallam)

ya ce: **(Ka ɗaure ta, sannan ka dogara da Allah)**, sai kuwa ya ɗaure taguwarsa, yana mai riƙo da sababi; domin ya sami lamunin kiyaye ta, barinta kawai a sake zai sauƙaƙa wa ɓarayi yin sata, ya kuma kai zuwa ga rasa taguwar.

**Ya Allah Ubangiji ka datar da mu zuwa ga abubuwa masu kyau ga addininmu, da kuma ɗaukakar al'ummarmu, da cigaban ƙasashenmu, da sauran ƙasahen duniya..**

- 24 –

## RANGWAME AƘIDA NE DA TSARIN RAYUWA

Godiya ɓta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki sauƙi yake so maku, sam ba ya sonku da wahala..))** **[al- Baƙra: 185]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa, da waɗanda suka bi turbarsa da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zo da saƙo ne zuwa ga dukan duniya, saƙon da ya ɗauki rangwame, gami da sauƙi a matsayin manhaji na rayuwa, babu matsi a cikin al'amarin addini, babu wahala da takura a cikin wajibai, babu tsanani, babu tsangwama, Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Sam Allah bai sanya maku wahala da damuwa a cikin al'amarin addini ba))** **[al- Hajji: 78]**, haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai wannan addinin sauƙi ne, babu wanda zai tsananta addini face addinin ya fi ƙarfinsa, ku nemi dacewa a dukan ayyukanku, idan ba ku sami hakan ba, to ku kusanto zuwa ga yin daidai ɗin, ku yi wa junanku albishir, muddin kun kasance a haka, ku kuma nemi sa'a na gabatar da haka tun daga lokacin**

**fitowar rana har zuwa lokacin walha, da bayan sallar La’asar zuwa Maghriba, da wani yanki na ƙarshen dare)**, shi rangwame a cikin Shari’ar Musulunci ba wai kawai kalma ce da ake faɗinta da baki, ko take da ake yawan maimaitawa ba; aƙida ce da Musulmi yake rayuwa da ita, ya mayar da ita manhaji na rayuwarsa, haka ma rangwame ƙa’ida ce daga cikin ƙa’idojin da Allah Maɗaukakin Sarki ya umurci bayinsa da su sanya ta a cikin mu’amalar da take tsakaninsu da juna, hasali ma ya sanya rangwame ya zamo dalili na samun yardar Allah, da gafararsa, gami da rahamarsa, Allah mai girma yana cewa: **((Tabbas su yafe, su kuma yi rangwame, shin ba ku son Allah ya gafarta maku ne?))** **[an- Nur: 22]**.

Lallai abin da muke nema shi ne: rangwame ya zamo wani tsari ne na rayuwarmu, saboda Musulunci ya yi kira zuwa ga a yi rangwame ne a aikace, a wurare masu yawa a cikin Alƙur’ani mai girma, Allah mai girma da ɗaukaka ya kira bayinsa zuwa ga yin yafiya da rangwame, Allah mabuwayi yana cewa: **((Babu yanda za a yi a daidaita tsakanin abu mai kyau da mummuna, kai dai kawai ka saka duk wani abu da aka yi maka da abu mafi kyau, idan ka yi haka za a sami abokin gabanka ya zamo tamkar masoyi na kusa))** **[Fussilat: 34]**, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya aiwatar da rangwame a aikace tsakaninsa da mutane, inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zamo babban abin koyi ga al’ummarsa, da ma ɗaukacin bil’adama a duk faɗin duniya, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ni fa rahama ne da Allah ya ba ku kyauta)**, Ummul muminina, Sayyida A’isha (Allah ya ƙara yarda da ita) tana cewa: **(Ba a taɓa bai wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) zaɓi tsakanin abubuwa guda**

**biyu ba, face ya zaɓi mafi sauƙin ciki, matuƙar ba saɓon Allah ba ne, idan saɓon Allah ne kuma ya fi kowa nesantarsa..)**.

Tambayar da ta kamata kowannenmu ya yi wa kansa cikin gaskiya ita ce: shin muna aiwatar da wannan aƙidar a rayuwar ta yau da kullum? Shin mun sanya ta ta zamo manhaji na mu'amala a tsakaninmu da juna, da ma tsakaninmu da ɗaukacin mutane? Shi rangwame ɗabi'a ce mai kyau da ya kamata kowane Musulmi ya yi aiki da shi a dukan fagagen rayuwa, kaman irin **rangwamen da yake tsakanin ma'aurata biyu**: lallai dangantaka ta aure tana cikin mafiya girman dangantaka ta mutuntaka, aya ce daga cikin ayoyin Allah Maɗaukakin Sarki, tabbas Allah mai girma da ɗaukaka ya bayyana cewa wannan dangantaka ta ginu ne akan soyayya da tausayi da kuma kyautata zamantakewa, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai a cikin ayoyinsa ne –mai girma da ɗaukaka- ya halitta maku abokan zama na aure, domin ku sami natsuwa da su, ya kuma sanya soyayya da rahama a tsakaninku..))** **[ar-Rum: 21]**, haka ma Mai girma da ɗaukaka ya ce: **((Ku rayu da su a cikin kyautatawa, idan ma kun ƙi su, to abu ne mai yiwuwa ku ƙi wani abu, Allah kuma ya sanya alhairi mai yawa a tare da shi))** **[an- Nisa'i: 19]**, haka ma buwayi gagara misali yana cewa: **((Su ma mata suna da haƙƙoƙi akan mazajensu irin yanda su mazajen suke da haƙƙoƙi akan matansu cikin kyautatawa))** **[al-Baƙra: 228]**, ma'ana: suna da haƙƙoƙin da dole ne mazajensu su kyautata rayuwar zamantakewa da su cikin kyautatawa, kaman dai yanda hakan ma ya wajaba akansu game da mazajensu, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mafi alhairi a cikinku, shi ne wanda ya fi kyautatawa iyalansa, ni ne kuma na fi ku kyautata wa iyalai na)**, a wurare da yawa

Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi wasici game da al’amarin mata, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Kada mumini ya ƙi mumina, idan ya ƙi wata ɗabi’a tata, zai so wata ɗabi’ar)**, ma’ana kada ya tsane su, haka ma mata ne ƙarshen abin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi wasici akansu kafin ya yi wafati, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ku yi wasici da a kyautata wa mata)**.

Lallai ya kamata rangwame ya zamo tsari ne na rayuwa tsakanin ma'aurata biyu, ya kuma zamo doka ta mutuntaka da za ta tsara rayuwa, mene ya kai kyawon abin da Sayyiduna Abuddarda'i (Allah ya ƙara yarda da shi) ya faɗa wa matarsa (Allah ya ƙara yarda da ita), yana cewa: "Idan kika ga na yi fushi, to ku lallashe ni, ni ma idan na ga kin yi fushi zan lallashe ki a ƙarƙashin wani tsari na musanyen mutuntaka da aka gina shi akan adalci da rangwame a haɗe”.

* **Rangwame tare da maƙwabta:** Allah mai girma yana cewa: **((Ku bauta wa Allah Maɗaukakin Sarki shi kaɗai, kada ku kuskura ku haɗa shi da kowa wajen Allantakarsa da gabatar masa da ibada. Ku kuma kyautata wa mahaifa ba tare da gajiyawa ba, ku kuma kyautata wa ‘yan uwa makusantanku da marayu, da waɗanda suka talauce sakamakon gajiyawa, ko sakamakon aukawar wani bala’i a cikin dukiyoyinsu.. A kuma kyautata wa maƙwabci makusanci na dangi, da maƙwabci makusanci wanda ba na dangi ba, da abokin aiki ko tafiya ko abokin zama..)) [an- Nisa’i: 36]**, sau da yawa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan yi wasici akan maƙwabci, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mala'ika Jibrilu bai gushe ba yana yi mini wasici da maƙwabci, har sai da na zaci zai sanya shi a cikin magada)**,

haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya girmama maƙwabcinsa)**, haka ma an ji (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wallahi bai yi imani ba, wallahi bai yi imani ba, wallahi bai yi imani ba)** sai aka ce: Ya Manzon Allah, wane kenan? Sai ya ce: **(Wanda maƙwabcinsa bai aminta daga sharrinsa ba)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Fiyayye a cikin abokai shi ne wanda ya fi kyautata wa abokinsa, fiyayyen a cikin maƙwabta shi ne wanda ya fi kyautata wa maƙwabcinsa)**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mutumin da yake kwana a ƙoshe maƙwabcinsa na gefensa kuma cikin yunwa ba mumini ba ne)**.

**Haka ma ya kamata a sami rangwame a tsakanin abokan aiki,** a jami'o'i, da makarantu da sauransu, lallai Alƙur'ani mai girma ya dasa dangantaka tsakanin ɗaukacin mutane, Allah mai tsarki yana cewa: **((Ya ku mutane, lallai mun halicce ku ne daga asali ɗaya wanda dukanku kuke daidai da juna, wannan asali kuwa shi ne Annabi Adam da Hauwa'u (Alaihimas-Salãm), ta hanyar auratayya ne kuma muka mayar da ku al'ummomi masu yawa da ƙabilu mabambanta; domin ku san juna, ku kuma yi taimakekeniya a tsakaninku, lallai wanda ya fi matsayi a wurin Allah duniya da lahira shi ne wanda ya fi ku tsoron Allah, tabbas ilimin Allah ya game komai, ƙwararre ne kuma wanda babu wani abu komin ƙanƙantarsa da zai ɓuya masa a cikin dukan al'amurra))** **[al- Hujrat: 13]**, kuma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) shi ne ya fi kowa nuna kyawawan ɗabi'u tsakaninsa da ɗaukacin mutane, da tsakaninsa da sahabbansa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan kyautata mu'amala tare da su, yakan tafi ya duba marasa

lafiyansu, yakan bincika labarin waɗanda aka ɗauki lokaci ba a gansu ba, yakan gabatar da sadaka ga talakawan cikinsu, yakan kuma biya masu basussukan da suke kawunansu, ya kuma biya masu buƙatunsu, yakan kuma yafe wa waɗanda suka yi kuskure a cikinsu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Saboda rahamar da Allah yake yi maka, kai da su ne, ya sanya ka zamo mai sauƙin-kai, ba ka zamo mai kakkausar magana akan kuka-kurensu ba, da ka zamo mai ƙyeƙasasshiyar mu'amala, mai kuma busasshiyar zuciya da sun tarwatse sun bar ka, saboda haka, ka cigaba da kawar da kai ga barin kura-kurensu, ka nema masu gafara, ka nemi shawarwarinsu cikin al'amurra, kana mai mutunta ra'ayoyinsu cikin abin da ba a saukar maka da wahayi akai ba..))** **[Ali Imran: 159].**

*** Rangwame a hanyoyi da abubuwan sufuri:** mutum zai iya fuskantar cutarwa daga waninsa; saboda wasu mutane wauta ne da su, akwai kuma masu ƙeƙasassun zukata, akwai kuma masu yafiya da rangwame, akwai masu ƙarfi, akwai kuma masu rauni, akwai masu jure wa wautar wasunsu, akwai kuma marasa juriya, saboda haka, abu ne mai matuƙar kyau a sami mutum ya mu'amalanci duka waɗannan ɗabi'u da haƙuri gami da rangwame, inda martaninsa zai zamo a koda yaushe cikin sauƙi da ladabi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Su bayin Allah mai yawan rahama su ne waɗanda suke tafiya sannu a hankali a bayan ƙasa, idan ma masu wauta suka takale su, sai su mayar masu da sallama))** **[al- Furƙan: 63]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ba za ku shiga aljanna ba har sai idan kun riga kun yi imani, ba kuma za ku yi imani ba har sai kun so juna, shin ba na nuna maku**

**abin da idan kuka aikata shi za ku so juna ba?, to ku yaɗa sallama a tsakaninku)**. Haka ma ya kamata a kiyaye dokokin hanya da na abubuwan sufuri, irinsu bayar da wurin zama ga masu yawan shekaru, da masu rauni, da mata, da kuma kiyaye haƙƙoƙin mutane, da yi masu mu'amala cikin sauƙi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Shi sauƙi bai taɓa shiga cikin wani abu ba face ya ƙawata shi, ba kuma a taɓa cire shi daga kowane irin abu ba face ya sanya ya yi muni)**.

*** Haka ma a cikin alamun wannan rangwame akwai rangwame wajen ciyar da dukiya**: lallai ciyar da dukiya alama ne na imani da Allah da Manzonsa, alama ne na gyaruwar mutum da tsayuwarsa akan daidaitacciyar hanya, da shi ne ake gane muminai, a kuma samu kusancin zukata, da kuma shi ne bawa yake samun ayyukan alhairi da biyayya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ba za ku taɓa samun biyayya da ayyukan alhairi ba har sai kun ciyar da dukiyar da kuke so..)) [Ali Imran: 92]**, lallai ciyar da talakawa da miskinai alama ne na sauƙin kai da kyawawan ɗabi'un mutum, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mai yawan baiwa yana kusa da Allah, yana kuma kusa da aljanna, yana kuma kusa da mutane, ya kuma yi nesa da wuta)**.

*** Haka ma akwai rangwame wajen saye da sayarwa da biyan bashi**: Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ya Allah ka yi rahama ga mutum mai sauƙin kai wajen sayarwa, da wajen saye, da wajen biyan bashi)**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Irbadh Bn Sariya (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Na sayar wa Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da matashin raƙumi, sai na zo in amshi kuɗi, sai na ce: Ya

Manzon Allah, na zo ne na amshi kuɗin matashin raƙumi na, sai ya ce: **(Haka ne, lallai ba zan biya ba sai da sababbin dirhamomi)**, sai ya ce: ya kuwa biya da mafi kyawon biya, sai wani Balaraben ƙauye ya zo, ya ce: Ya Manzon Allah, ka biya ni matashin raƙumi na, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ba shi babban raƙumi da yafi nashi shekaru, sai ya ce: Ya Manzon Allah, ai wannan ya fi matashin raƙumi na girma, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Fiyayye a cikin mutane shi ne wanda ya fi su alhairi wajen biyan bashi)**.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kwaɗaitar akan aikata duk wani abu da suke tabbatar da rangwame gami da sauƙi, yake kuma tabbatar da ma'anonin 'yan uwantaka ta mutuntaka, da kusanto da mutane da juna, irin su: yafe wa waɗanda ba su da shi, ko jinkirta masu, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda ya jinkirta wa marashi biyan bashin da yake binsa, ko kuma ya yafe masa, to kuwa Allah zai yi masa inuwa a inuwarsa)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Akwai wani mutum da yake bai wa mutane bashi, yakan ce da yaronsa: idan ka je wurin wanda ba shi da shi, ka ɗaga masa ƙafa, saboda mu ma Allah ya ɗaga mana ƙafa, sai kuwa ya haɗu da Allah ya yafe masa)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi

masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa baki ɗaya, da waɗanda suka bi shi da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai a cikin manyan alamun rangwame, kuma mafi sauƙin yi akwai: **rangwame wajen furta kalamai masu daɗi,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku faɗa wa mutane magana mai kyau..))** **[al- Baƙra: 83]**, haka ma Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ka faɗa wa bayi na cewa: su rinƙa faɗin maganar da ta fi kyau..))** **[al- Isra'i: 53]**, ita kalma mai daɗi ana yi wa ɗaukacin mutane ne, ba tare da la'akari da bambancin launi, da na jinsi, da na addini ba; wannan yana nuna kyakkyawar tarbiyya, da kyawawan ɗabi'u, da ma dai tuni ana cewa: **"Kyakkyawan ɗabi'a abu ne mai sauƙi: sakin fuska ne, da kuma tattausar magana"**.

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya umurci Sayyiduna Musa (AlaiHis Salam) da ya faɗa wa Fir'auna magana mai daɗi, duk kuwa girman kai da taurin kan da yake da su, Allah mai girma ya ce: **((Ku tafi wurin Fir'auna saboda lallai ya wuce gona da iri, ku yi masa magana mai taushi da za ta iya sanya shi ya wa'aztu, ko kuma ya ji tsoron Allah))** **[Taha: 43 -44]**, haka ma ya kamata a nesanci duk wani zancen kawai, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Su ne waɗanda suke kawar da kai ba barin zancen kawai))** **[al- Muminuna: 3]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku ji tsoron Allah, ku kuma faɗi daidaitacciyar magana))** **[al- Ahzab: 70]**, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Shin ba ka ga yanda Allah ya buga misali da kalma mai daɗi da bishiya mai daɗi da tushenta ya kama ƙasa, rassanta kuma suka yi sama ba, tana yin 'ya'ya a dukan lokaci da izinin Ubangijinta, lallai Allah yana buga wa**

**mutane misalai ne ko za su wa'aztu))** [Ibrahim: 24 -25], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai bawa zai iya furta kalmar neman yardar Allah da ma bai mayar da hankali zuwa gare ta, hakan kuma ya zama dalilin samun ɗaukakar darajarsa a wurin Allah, haka ma bawa zai iya furta kalmar da za ta jawo fushin Allah, ba kuma tare da ma ya mayar da hankali zuwa gare ta ba, hakan kuma ya zamo sanadiyyar aukawarsa cikin jahannama...),** kaman yanda tilas ne a nesanci duk wani nau'i na alfasha wajen furuci, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai shi mumini ba mai yawan la'antar mutane ba ne, ba kuma mai yawan sukan mutane ba ne, ba kuma mai yawan alfasha ba ne, ba kuma mai yawan zancen kawai ba ne)**.

Lallai rangwame wani abu ne da yake a tsakiyar abubuwa guda biyu kishiyoyin juna; yana tsakanin tsanani, da rashin muhimmanta abu, kuma duka biyun sun yi hannun riga da manhajin Musulunci na al- Wasaɗiyya, wanda yake ƙunshe da nau'o'i iri- iri na rangwame, da sauƙi, da yin abu a hankali, waɗanda a take suke kawo ƙarshen duk nau'o'in tsauraran ra'ayi, da wuce gona da iri, da rashin muhimman abubuwa.

**Ya Allah Ubangiji, muna roƙon ka azurta mu da rangwame a cikin maganganunmu, da ayyukanmu, da mu'amalolinmu, da dukan al'amurranmu, ka daidaita tsakaninmu, ka kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashe baki ɗaya.**

- 25 –

## LADUBBA NA BAI ƊAYA DA TASIRINSU WAJEN CIGABAN AL'UMMA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ka ce masu: Lallai ni kam Ubangiji na ya shiryatar da ni zuwa ga miƙaƙƙiyar hanya, addini ne tsayayye da Annabi Ibrahim mai bautan Allah yake a kai, lallai ba ni a cikin masu haɗa Allah da wani wajen bauta))** **[al- An'am: 161].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai al'ummomin da suka cigaba, da manyan ƙasashe su ne waɗanda suka rungumi ladubba na bai ɗaya a matsayin manhajin rayuwa, ba a lissafa waɗannan ladubban cikin zantuttukan cike wuri marasa fa'ida, saboda babu yanda za a yi a raba su da tsarin kyawawan ɗabi'u, da tadodi na mutuntaka, wannan ne kuma abin da ya yi daidai da addininmu mai daraja, da ya zo ya kafa wasu manyan ladubba da suke tsara

dangantakar ɗan Adam da Ubangijinsa, da ma dangantakarsa da saura halittu baki ɗaya.

**Tsabta** na cikin waɗannan ladubba, lallai addinin Musulunci ya muhimmanta tsarkin jiki, da na tufafi, da na wuri, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani: idan har kun yi nufin tashi domin yin sallah, ba kuma ku da alwalla, to ku yi alwalla, kuna masu wanke fuskokinku, da hannayenku zuwa gwiwar hannu, ku kuma shafi kawunanku –duka ko kuma wani sashe- ku kuma wanke ƙafafuwanku zuwa idon sawu. Idan kuma a lokacin da za ku tashi yin sallah ɗin kuna cikin halin janaba ne sakamakon kusantar iyali, to ku wanke gaba ɗayan jikinku da ruwa, idan kuma ba ku da lafiyar da har hakan zai hana ku yin amfani da ruwa, ko kuma kuna halin tafiyar da samun ruwa zai yi maku wahala, ko kuma lokacin da kuka dawo daga biyan buƙatunku na bayan gida, ko kuma kuka kusanci mata ga shi kuma ba ku sami ruwa ba, to a nan, sai ku yi taimama da ƙasa mai tsarki, ta hanyar shafar fuskokinku da hannayenku da ita. Ba wai Allah yana son ya ƙuntata maku ne da wannan umurni nasa ba, ya dai shar'anta maku haka ne saboda ku zamo masu tsarki a zahiri da baɗini, ya kuma cika maku ni'imominsa na shiriya da bayani da kuma sauƙaƙawa; domin ku gode masa akan shiriyar da ya yi maku, da kuma cika maku ni'imomin da ya yi, ta hanyar dawwama a wajen yin masa biyayya))** **[al- Ma'ida: 6]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Tufafinka ma ka tsarkake su))** **[al- Mudassir: 4]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan ɗayanku ya tashi daga barci, kada ya tsoma hannunsa a ƙwaryar ruwa, har sai ya wanke shi sau uku..)**, haka ma

(SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ku kiyaye mala'anta)**, sai suka ce: Ya Manzon Allah, mene ne mala'anta? Sai ya ce: **(Mutumin da yake bayan gida akan hanyar mutane, ko a inuwar da suke hutawa)**.

Lallai addinin Musulunci ya haɗe tsakanin **tsabta ta ƙarara ta zahiri, da tsabta ta ma'ana ta baɗini**, ya sanya tsarki na ƙarara ya zamo ɗaya daga cikin dalilai, ko sabubba ne na samun tsarki na ma'ana, idan mutum ya kiyaye tsabtar jikinsa, to hakan zai zamo sanadi na gafarta masa zunubansa, saboda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idan bawa Musulmi –ko mumini- ya yi alwalla, ya wanke fuskarsa, to dukan kura- kuren da ya aikata da idanuwansa za su fita tare da ruwan –ko tare da ɗigon ƙarshe na ruwan-, idan ya wanke hannuwansa ma duka kura- kuren da ya aikata da hannuwansa za su fita tare da ruwan –ko tare da ɗigon ƙarshe na ruwan-, haka ma idan ya wanke ƙafafuwansa, dukan kura-kuren da ya tafi da ƙafuwansa ya aikata za su fita tare da ruwan –ko tare da ɗigon ƙarshe na ruwan-, har dai ya tsarkaka ga barin zunubai)**, lallai kaman yanda addinin Musulunci ya muhimmanta tsabtar mutum a karan kansa, haka ma ya muhimmanta tsabta ta gaba ɗaya, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ku tsabtace farfajiyarku)**, farfajiya a nan ta haɗe gida, da makaranta, da masa'anta, da wuraren tarurruka, da wuraren shaƙatawa na al'umma, haka ma ta haɗe hanyoyi, da dandamulla da sauransu, dole ne a kiyaye su, da rashin zuwa waɗannan wurare da abin da bai dace ba, da kuma barinsu sama da yanda aka same su cikin tsabta, da bayar da gudummuwa wajen tsabtace su.

Haka ma **girmama tsari** yana cikin waɗannan ladubba, dole ne kowace al'umma ta zamo tana da wasu ƙa'idoji da tsare-tsare na adalci, waɗanda da su ne ake auna ɗabi'un mutanen ciki, su kuma kiyaye wa ɗan Adam haƙƙoƙinsa, a gefe ɗaya kuma, su ɗaura masa wasu wajibai da zai aikata, da haka sai a samar da maslaha ta bai ɗaya da amfaninta zai game dukan al'umma, duk mai lura da yanda manyan ƙasashe, da al'ummomin da suka cigaba suke, zai tabbatar da cewa: lallai sun kai wannan matsayi da suka kai ne, sakamakon girmama dokoki, da riƙo da su wajen aiwatar da komai, hakan yana nufin girmama haƙƙoƙin mutane, da kuma dokar samun haƙƙi bayan sauke wajibi, da yi wa mutane mu'amala da irin abin da yake son a yi masa mu'amala da shi, lallai waɗannan suna cikin cikar imani, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Imanin ɗayanku ba zai cika ba, har sai ya so wa ɗan uwansa abin da yake so wa kansa)**, lallai wannan alhaki ne da ya shafi kowa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Dukanku masu kulawa ne, kuma kowa za a tambaye shi akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi: Shugaba mai kulawa ne, za kuma a tambaye shi akan waɗanda yake shugabanta, namiji ma mai kulawa ne a cikin iyalansa, za kuma a tambaye shi akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi, mace ma mai kulawa ce a gidan mijinta, za kuma a tambaye ta akan nauyin da aka ɗaura mata na kulawa, hadimi ma mai kulawa ne da dukiyar uban gidansa, za kuma a tambaye shi akan nauyin da aka ɗaura masa alhakin kulawa da shi, dukan ku masu kulawa ne, za kuma a tambayi kowa a akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi),** da girmama tsari, gami da bin dokoki ne adalci yake jagoranci, ruhin soyayya, da ƙauna,

da taimakon juna kuma su yaɗu, a sakamakon haka sai ɗaukacin al'umma su samu ni'imar zaman lafiya, da tsaro, gami da kwanciyar hankali.

**Kiyaye abubuwan da mutane ba sa so** ma yana cikin waɗannan ladubba, domin addinin Musulunci ya zo ne saboda ya tsarkake tsarin rayuwa, ya ɗaukaka shu'urin mutane, ya kuma harhaɗa zukata daidai da wasu ƙa'idoji da ba a samun saɓani akansu tsakanin mutane, da kuma girmama al'adun mutane, da abubuwan da suka saba da su, lallai Shari'ar Musulunci ta tabbatar da duk wani abu mai kyau da zukatan mutane ba sa ƙyamansu, ta kuma haramta duk wani mummunan abu da yake cutar da su, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Su ne waɗanda suke bin Manzo, kuma Annabin da ba ya rubutu da karatu, wannan dai da sunansa da sifofinsa sunan nan a wurinsu a rubuce a cikin Attaura da Injila, wanda yake umurtansu da aikata abubuwa masu kyau, yake kuma hana su aikata munanan abubuwa, yake halatta masu abubuwa masu tsabta, yake kuma haramta masu munanan abubuwa..))** **[al- A'araf: 157].**

Haka ma **mutum ya yi daidaito wajen tufafinsa da abincinsa da abin shansa, da nesantar ɓarna da shari'a ba ta so, ko bayyana da sifar da ba ta dace ba**, duka suna cikin ladubban, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Ya ku 'ya'yan Annabi Adam, ku yi ado domin zuwa kowane Masallci, ku kuma ci ku sha, kada ku kuskura ku yi ɓarna, lallai shi Allah ba ya son maɓarnata))** **[al- A'araf: 31]**, haka ma girmama lokaci, da cika alƙawurra, Allah mai girma yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku cika alƙawurran da kuka ƙulla..))** **[al- Ma'ida: 1]**, haka ma wajibi ne a kiyaye abubuwan da zukatan mutane ba

sa amsa a wajen aiki, da sanyan tufafi, da shiga, an ruwaito Hadisi daga Sasyyiduna Jabir (Allah ƙara yarda da shi) cewa: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya hana mutum ya ɗaura ƙafarsa ɗaya akan ɗaya a lokacin da yake kwance a rigingine. Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: (Idan hancin takalmin ɗayanku ya tsinke, to kada ya yi tafiya da ɗaya warin, har sai ya gyara), wannan yana nufin sam bai kamata mutum ya yi tafiya da talkami ƙafa ɗaya ba, saboda kiyaye abin da mutane ba sa so.

Haka ma a cikin ladubban akwai: **mutum ya kiyaye kada wata murya, ko wani aiki da mutane suke ƙyamata su fito daga gare shi**, an ruwaito Hadisi daga Ibn Umar (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: wani mutum ya yi getsa a gaban Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) –saboda ƙoshi da cika cikinsa-, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ka kame getsarka; saboda wanda ya fi ƙoshii a duniya, shi ne wanda yunwarsa za ta fi tsawaita a ranar alƙiyama)**, duk da cewa hakan ba haramun ba ne, amma dai ya saɓa da abin da mutane suke so, abin da ya fi hakan muni kuma shi ne, mutum ya cutar da mutane ta hanyar yin amfani da abubuwan da aka haramta da suke barin wari a bakuna, ko a tufafi, haka ma dole ne mutum ya kiyaye duk wani aiki, ko magana da sauransu da yake yi gudun kada su cutar da waninsa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai za a tambayi mutum game da jinsa, da ganinsa, da zuciyarsa baki ɗaya))** **[al- Isra'i: 36]**.

Haka ma **yi wa mutane magana mai kyau, da zaɓan kalmomi masu daɗi** suna cikin ladubba na bai ɗaya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ka faɗa wa bayi na cewa: su rinƙa faɗin maganar da ta fi kyau, lallai shaiɗan ne yake ɓata**

**tsakaninsu, tabbas shaiɗan mai yi wa ɗan Adam bayyananniyar ƙiyayya ne))** **[al- Isra'i: 53]**, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Kalma mai daɗi sadaka ce)**; a cikin yin amfani da kalamai masu daɗi akwai: yin amfani da lafuzzan da ba za su nesanta juna ba, wata rana Sayyiduna Umar Bn al-Khaɗɗabi (Allah ya ƙara yarda da shi) ya wuce ta wurin wasu mutane da suka kunna wuta, bai ce masu: "Assalamu alaikum ya ma'abotan wuta" ba; a maimakon haka sai ya ce: "Assalamu alaikum ya ma'abotan haske".

Haka ma akwai **girmama abubuwan suka shafi mutane, da rashin yin katsalandan a cikin abubuwan da su shafe mu ba**, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ka soma ka shiga cikin abin da ba ka da ilimi akansa, lallai za a tambayi mutum game da jinsa, da ganinsa, da zuciyarsa baki ɗaya))** **[al-Isra'i: 36]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(A cikin abubuwan da suke nuna kyautatuwar Musuluncin mutum, akwai: barin abubuwan da ba su shafe shi ba da yake yi)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai a cikin muhimman ginshiƙan ladubba na bai ɗaya, da suke taka rawa wajen ɗaukakar al'umma akwai: **Kunya,** ɗabi'a ce mai girma a Musulunci, tana hana mai ita aikata dukan wani abin zargi, ya kuma sanya shi ya nesanci duk wani abu mai muni, ya kiyaye shi daga coge, lallai Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana kunya a matsayin tana cikin dukan saƙwannin da suka zo daga Allah Maɗaukakin Sarki da suka gabata, ya bayyana haka ne a inda yake cewa: **(Lallai a cikin abubuwan da mutane suka tarar na zantuttukan Annabawan farko akwai: idan ba ka jin kunya, to ka aikata duk abin da ka ga dama).**

Lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya wuce ta wurin wani mutum Balansare, yana yi wa ɗan uwansa wa'azi akan kunya, (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa ya yi: **(Ƙyale shi kawai!, ai lallai kunya tana cikin imani)**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abdullahi Bn Nas'ud (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ku ji kunyar Allah kaman yanda ta kamata)**, sai muka ce: Lallai muna jin kunyar Allah, mun gode Allah, sai ya ce: **(Ba wannan nake nufi ba; ita jin kunyar Allah kaman yanda ta kamata ita ce: ka kiyaye kai da abubuwan da ya ƙunsa, da ciki da abubuwan da ya tattara, a kuma tuna da mutuwa da ƙarewa, duk wanda yake son lahira, zai bar kayan ƙawa na duniya, duk wanda ya aikata haka, to kuwa lallai ya jin kunyar Allah kaman yanda ta kamata)**, ita kunya tana hana mai ita zamewa, shi mara kunya babu wani abu da zai ba shi kariya, alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa:

"Mutum zai rayu cikin alhairi matuƙar ya ji kunya, domin itace zai dawwama matuƙar ɓawonsa yana nan. Na rantse da Allah babu wani alhairi a rayuwa, da ma duniya baki ɗaya idan kunya ta yi ƙaura. Idan har ba ka jin tsoron abin da zai zo a ƙarshen dare ba, ba kuma ka ji kunya ba, to ka aikata abin da kake so).

Haka ma a cikin muhimman ginshiƙan ladubba da suke taka rawa wajen cigaban al'umma da ɗaukakarta akwai: **mutunci,** ita wannan kalma ce da ta game dukan ma'anonin mazakuta, tana nufin: kyawawan sifofi, da nagartattun ɗabi'u, da bayar da alhairai ga mutane, da kiyaye kai daga aukawa cikin ƙazanta, da kiyaye harshe ga barin alfasha, da zantuttukan da ba su dace ba, da nesantar duk wani abu da zai sanya a nemi hanzari a gaba, da ma dai tuni aka ce: "Duk wanda ya yi mu'amala da mutane ba tare da ya zalunce su ba, ya kuma yi masu magana ba tare da ya yi masu ƙarya ba, ya kuma yi masu alƙawari bai saɓa ba, to kuwa lallai yana cikin waɗanda mutuncinsu ya cika, adalcinsu ya bayyana, zama da su kuma ya zama dole, aka kuma haramta cin namansu".

**Mutuncin mutum ne yake sanya shi ya zamo mai sauƙin kai a zahiri da baɗini, yana mai hararo Ubangijinsa a halin sirri da bayyane**, ba ya bayyana a gaban mutane da sifa mai kyau, idan kuma ya keɓe ya keta hurumin da Allah ya haramta, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai na san wasu mutane a cikin al'umma ta da za su zo da kyawawan ayyuka tamkar dutsen Tihama, fari a ranar alƙiyama, sai Allah ya mayar da shi ba a bakin komai ba, 'yan uwanku ne, daga cikinku suke, suna amfana da dare kaman yanda kuke**

**amfana; kawai dai idan suka keɓe ne sai su riƙa keta hurumin abubuwan da Allah ya haramta)**.

Shi kuwa yi wa mutane mutunci yana kasancewa ne ta hanyar **gabatar masu da taimako, da kiyaye, gami da samar masu da maslahohinsu, da so masu abubuwan da kake so wa kanka,** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Musulmi ɗan uwan Musulmi ne, ba zai zalunce shi ba, ba kuma zai bayar da shi ba, duk wanda ya tsaya wajen biya wa ɗan uwansa buƙatarsa, Allah zai tsaya masa wajen biyan buƙatarsa, duk wanda ya yaye wa Musulmi wani baƙin ciki, Allah zai yaye masa baƙin ciki daga cikin baƙin cikin ranar alƙiyama, duk wanda ya suturta Musulmi Allah zai suturta shi ranar alƙiyama)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mutumin da Allah ya fi sonsa a cikin mutane, shi ne wanda ya fi amfanar mutane, fiyayyen aikin da Allah ya fi so shi ne shigar da farin cikin a cikin zukatan Musulmai, ko yaye masu damuwa, ko biya masu bashin da yake kansu, ko a yaƙi yunwan da suke ji, wallahi na fi son na tafi wajen biyan buƙatar ɗan uwa na sama da in yi ittikafi a wannan Masallaci; -yana nufin Masallacin Madina- na wata ɗaya)**.

Lallai addinin Musulunci ya tabbatar da **wasu ladubba masu girma da daraja**, waɗanda matuƙar kowace al'umma ta yi riƙo da su, to kuwa za ta kai labari a fagen cigaba, da ɗaukaka, gami da samun nasara, wannan kam sunnar Allah ce da ba ta sauyawa, ba kuma ta jirkata, lallai muna matuƙar buƙatar riƙo da waɗannan ladubban, mu zartar da su a tsarin rayuwarmu da juna, saboda mu ji daɗi a duniya da lahira.

**Ya Allah Ubangiji muna roƙon ka nuna mana abubuwan da za su amfane mu a duniya da lahira, ka datar da mu wajen**

**aikata abubuwan da za su amfani ƙasarmu, ka kuma kiyaye mana ƙasarmu da al'ummarmu da jami'an tsaronmu.**

- 26 –

## LADUBBA DA HAƘƘOƘI NA BAI ƊAYA DA TASIRINSU WAJEN GINA AL'UMMA DA CIGABA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ka ce masu: Lallai ni kam Ubangiji na ya shiryatar da ni zuwa ga miƙaƙƙiyar hanya, addini ne tsayayye da Annabi Ibrahim mai bautan Allah yake a kai, lallai ba ni a cikin masu haɗa Allah da wani wajen bauta))** **[al- An'am: 161].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda a cikin Hadisinsa yake cewa: **(Ubangiji na ne ya yi tarbiyya ta, ya kuma kyautata yi mini tarbiyya)**. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Addinin Musulunci ya zo da wani cikakken manhaji da yake tsara dangantakar mutum da Ubangijinsa, da dangantakarsa da sauran mutane, da dangantakarsa da ɗaukacin halittu, babu shakka Shari'ar Musulunci tana cike da tsare- tsare na bai ɗaya da suka bayar da gudummuwa matuƙa wajen ɗaukakar al'umma, da cigabanta, gami da haɓakarta, a cikin waɗannan ladubba akwai: **ladabin neman izini,** Lallai addinin Musulunci

ya shar'anta neman izini, inda ya sanya shi cikin ladubban Musulunci da suke kiyaye keɓantuwar mutane, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, kada ku soma ku shiga gidajen da ba naku ba, har sai kun nemi izini, kun kuma yi sallama wa masu su, yin wannan shi ne mafi alhairi a gare ku, ko za ku wa'aztu ku tuna))** **[an- Nur: 27]**, haka ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya karantar da mu yanda ake neman izini da kuma ladubbansa, inda a cikin abubuwan da ya koyar da mu akwai: mai neman izinin ya fara da sallama, sannan ya faɗi sunansa, wani mutum ya nemi izini ya shiga wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) lokacin yana ɗaki, sai ya ce: In shigo? Sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce wa hadiminsa: **(Tafi wajen wancan mutumin, ka koya masa yanda ake neman izini, ka ce masa: ka ce: Assalamu alaikum, in shigo?)** sai mutumin ya ji shi, sai ya ce: Assalamu alaikum, in shigo?, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi masa izini, sai ya shiga. An ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Jabir (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Na zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai na ƙwanƙwasa ƙofa, sai ya ce: **(Wane ne?)** sai n ace: Ni ne, sai ya ce: **(Kai ne, kai ne!)** kaman bai so hakan ba.

Haka ma a cikin waɗannan ladubba akwai: **rufe, ko kawar da idanu, da rashin ƙura wa ƙofa ido,** (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ai da ma an shar'anta neman izini ne saboda ido)**. An ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Sa'ad Bn Ubada (Allah ya ƙara yarda da shi), yana cewa: ya nemi izini alhalin yana fuskantar ƙofar, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce masa: **(Kada ka nemi izini kana mai fuskantar**

**ƙofa)**, haka ma an ruwaito cewa: **Idan Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zo bakin ƙofa yana son ya nemi izini, ba ya fuskantar ƙofar, sai ya tsaya ko dai a dama, ko hagu, idan an yi masa izini shi kenan, in ba a yi ba ya juya**.

**Haka ma a cikin manyan ladubba da Musulunci ya kwaɗaitar akansu akwai: Ladubban hanya, da wuraren taruwar mutane,** lallai addinin Musulunci ya bai wa hanya wasu haƙƙoƙi, da suka wajaba a kiyaye, inda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Ahir ɗinku da zaman a kan hanyoyi)**, sai suka ce: Ya Manzon Allah, ba mu da yanda za mu yi; domin nan ne wajen hirarmu, inda muke magana da junanmu, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan kun dage sai kun zauna a wurin, to ku bai wa hanya haƙƙinta)**, sai suka ce: mene ne haƙƙin? Sai ya ce: **(Kawar da ido, da rashin cutarwa, da mayar da sallama, da yin umurni da ayyukan alhairi, da hana munana)**. Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Imani ya kasu kaso saba'in da wani abu –ko sittin da wani abu-, mafi girmansa shi ne faɗin *"La'ilaha illalLah"*, mafi ƙanƙantarsa kuma kawar da abu mai cutarwa daga hanya, kunya ma kaso ne daga cikin imani)**, ya zama dole ga wanda yake amfana da hanya, ko wani wuri na amfanin mutane, ya kiyaye wajen rashin ɗaga murya, ko yin magana da muryar da za ta damu mutane, da rashin yin dariya da muryar da akwai cutarwa ga wasu, da rashin jefa ƙazanta, ko wani abu mai cutarwa a kan hanya, ya zamo yana sanya su a wuraren da aka tanada domin haka, hasali ma dolensa ne idan ya ga ire- iren hakan ya kawar da su, haka ma dole ne ya nesanci duk abin da zai hana yin amfani da hanyar kaman yadda ta kamata, koda kuwa ta

hanyar cutar da masu wucewa ne ta hanyar kallo, ko tsokana ta harshe, ko yin haka a aikace.

A cikin irin waɗannan ladubban akwai **ladubban tsafta,** lallai addinin Musulunci ya sanya tsarki, da tsafta na jiki, da na tufafi, da na wuri sun zamo abubuwan da ba zai taɓa yiwuwa a cire su daga shari'arsa ba, daidai da ƙimarsu a rayuwar mutane, da kuma cigabansu; saboda haka ne addinin Musulunci ya kwaɗaitar da wasu ladubba da za su sanya hai'ar mutum ta fito da kyau, ta yanda ba zai zama abin ƙyama ga sauran mutane ba, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya yabi muminan da suke kaffa- kaffa akan tsaftar jikkunansu, masu tsarkake zahirinsu da baɗininsu, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai Allah yana son masu yawan tuba, yana kuma son masu yawan tsarki))** **[al-Baƙra: 222]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah mai tsarki ne, yana son abu mai tsarki, mai tsafta ne yana kuma son abu mai tsafta…)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Tsarki rabin imani ne..)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ga wani mutum gashinsa ya yi batsai, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Shin wannan bai sami abin da zai natsar da gashinsa ba ne?)**, ya kuma ga wani ya sanya tufafi marasa tsafta, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Shin wannan bai sami abin da zai wanke tufafinsa ba ne?)**.

Haka nan a cikin waɗannan ladubba akwai: **ladubban tattaunawa,** lallai tattaunawa hanya ɗaya ce daga cikin hanyoyin kusanta da juna, da gyara fahimtoci, lallai addinin Musulunci ya buɗe ƙofofin tattaunawa tsakanin mutane gaba ɗaya; domin su sada su da shiriya, gami da gaskiya, ba tare da damuwa, ko wani ƙaidi ba, sai dai duk da haka, dole ne a

nesanci sukan juna, da yi wa juna izgilanci, ko tozartawa a cikin tattaunawa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ka tattauna tare da su da abin da yafi kyau..)) [an- Nahl: 125],** haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ka faɗa wa bayina: Su faɗi abin da yafi kyau..)) [al- Isra'i: 53],** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mumini ba mai yawan sukan mutane ba ne, ba kuma mai yawan la'antarsu ba ne, ba kuma mai alfasha ba ne, ba kuma mai kalaman batsa ba ne)**, dole ne tattaunawar ta zamo a yanayi mafi kyau, a gina ta akan ginshiƙi na ilimi, da bincike na gaskiya, da kuma kulawa da hali, gami da yanayin da ake ciki.

Haka ma akwai; **tattabatar da labari, da jinkirtawa kafin a yaɗa shi,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, idan wani fãsiƙi ya ƙetare shari'ar Allah ya zo maku da kowane irin labari, to ku bincika ku tabbatar da gaskiyarsa; saboda kada ku cutar da wasu mutane –da ba ku san haƙiƙaninsu ba-, hakan sai ya sanya ku yi nadama akan abin da kuka aikata, kuna: ina ma ba mu aikata hakan ba, a lokacin da bayani ya bayyana cewa ba su da wani laifi)) [al-Hujrat: 6]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Bin abubuwa a hankali abu ne daga Allah, gaggawa kuwa daga shaiɗan take zuwa)**, da inda yake cewa: **(Yin jinkiri a komai banda a cikin aikin lahira)**, a wani wurin yana cewa: **(Mutum ya kai matuƙa a ƙarya idan yana yayata duk abin da ya ji)**, a cikin ladubban akwai: rashin maimaita jita- jita, ko yin ruwa - da - tsaki a cikinta, domin yawan maimaitawar tamkar bayar da gudummuwa ne wajen yaɗa ta, lallai jita – jita tana ƙara yaɗuwa ne idan ta sami harsunan da suke maimaita ta, da kuma kunnuwan da suke sauraranta, da kuma zukatan da suke

karɓanta, suke kuma gasgata ta, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lokacin da kuke furta shi da harsunanku, kuma da bakunanku kuke faɗin abin da ba ku da cikakkiyar masaniya a kai, kuna ganin hakan abu ne mai sauƙi, alhali a wurin Allah abu ne mai matuƙar girma..)) [an- Nur: 15]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to kada ya cutar da maƙwabcinsa, wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya girmama baƙonsa, wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya faɗi alhairi ko ya yi shiru)**.

**A cikin manyan ladubban da addinin Musulunci ya zo da su akwai: kwantar da murya,** ma'anar haka kuwa shi ne: kada mutum ya ɗaga muryarsa sama da ƙima a gaban waɗanda suke sama da shi, a cikin wasiyyoyin da Luƙmanul Hakim, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ka taƙaita tafiyarka, ka kuma kwantar da muryarka, domin lallai muryar da aka fi ƙi ita ce muryar jaki)) [Luƙman: 19]**. Tabbas Allah Maɗaukakin Sarki ya yabi waɗanda suke kwantar da muryoyinsu, musamman a halarar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) da cewa: **((Lallai waɗanda suke kwantar da muryoyinsu ƙasa a majalisin Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) saboda girmama shi, waɗannan –su kaɗai- su ne waɗanda Allah ya tsarkake zukatansu saboda tsoron Allah, a zukatan nasu babu wani wuri wanda ba na tsoron Allah ba, suna da mayalwaciyar gafara da za ta share dukan zunubansu, da kuma lada mai yawa)) [al- Hujrat: 3].**

**Haka ma a cikin ladubban akwai: shiryatar da wanda ya ɓace hanya**, ma'ana: shiryatar da shi wajen bayyana masa hanya, ko haɗa shi da ɗan jagora da zai kai shi inda yake nema,

Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ahir ɗinku da zaman a kan hanyoyi)**, sai suka ce: Ya Manzon Allah, ba mu da yanda za mu yi; domin nan ne wajen hirarmu, inda muke magana da junanmu, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan kun dage sai kun zauna a wurin, to ku bai wa hanya haƙƙinta)**, sai suka ce: mene ne haƙƙin? Sai ya ce: **(Kawar da ido, da rashin cutarwa, da mayar da sallama, da yin umurni da ayyukan alhairi da hana munana, da shiryatar da wanda ya ɓace hanya)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-----------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Akwai wasu ladubban na bai ɗaya masu matuƙar muhimmanci da ya kamata kowane Musulmi ya yi ado da su, a cikinsu akwai: **taimakon wanda yake cikin matsala da damuwa,** domin Musulunci ya sanya haka a cikin ayyuka mafiya karamci da ake kusantar Allah Maɗaukakin Sarki da su, an riwaito Hadisi daga Abuzarrin (Allah ya ƙara yarda da shi), shi kuma daga Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Babu wani rai na ɗan Adam face akwai sadakar da zai bayar a kowace rana)**, sai aka

ce : ya Manzon Allah, ta ina za mu sami abin da za mu yi sadaka da shi? Sai ya ce: **(Lallai ƙofofin alhairi yawa ne da su, "Tasbihi", da "Tahmidi", da "Takbiri", da "Tahlili", da bayar da umurni da aiki mai kyau, da hana mummunan aiki, da kawar da abu mai cutarwa akan hanya, da jiyar da kurma, da yi wa makaho jagora, da nuna wa mai neman wani abu abin da yake nema, da yin tafiya domin yaye wa wanda yake cikin damuwa damuwarsa, da yin amfani da dukan ƙarfinka wajen taimaka wa mai rauni, duka wannan sadaka ne kake yi wa ranka)**. [Ibn Hibban]..

Haka ma a cikin ladubban akwai: **taimakon masu rauni da masu buƙatu na musamman (naƙasassu)**, domin irin wannan taimakon maslaha ce ga mawadaci kafin ya zamo maslaha ga talaka, domin a samar da daidaito a cikin rayuwa, maganar Sayyiduna Aliyu (Allah ya ƙara yarda da shi) ne dalilinmu, yana cewa: "Allah ya wajabta samar da abincin talakawa ne a cikin dukiyar mawadata, babu talakan da zai ji yunwa, face sakamakon rowar mawadaci, kuma lallai Allah Maɗaukakin Sarki zai tambaye su akan haka". Irin wannan bayar da kulawar cigaba ne mai muhmanci a ƙasa, lallai kulawa da su haƙƙi ne da ya wajaba akan al'umma, lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana kusa da waɗanda zukatansu suka rusuna, mai kuma yawan tausayi ne ga duk wanda yake tausayin bayinsa, ba ya tozartar da kowane irin aikin alhairi, koda kuwa magana mai daɗi ne, Manzon Allah ( SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Kada ka soma ka ga ƙanƙancin wani aikin alhairi, kai koda haɗuwa da ɗan uwanka ne da sakakkiyar fuska)**, haka ma Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Shin ma wai za a taimake ku ne, a kuma ba ku arziki ba domin masu raunin**

**cikinku ba?!)**, lallai Allah zai taimaki bawa, muddin bawan yana taimakon ɗan uwansa..

A cikin waɗannan ladubba akwai: **girmama babba,** ta hanyar rausasa masa, da kuma rashin yi masa rashin kunya, dole ne a kula da girman shekarunsa, da kuma kasancewarsa wanda ya riga kasancewa a cikin addinin Musulunci, a ba shi girmansa da matsayinsa, haka shi ma babban an umurce shi da tausaya wa na ƙasa da shi, da nuna masu jinƙai, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu wani Musulmi da zai girmama mai furfura, face Allah ya hore masa wanda zai girmama shi idan ya kai shekarunsa)**, wannan kam wani shafi ne da yake nuna girma, gami da darajar Musulunci da jinƙansa, da rangwamensa, da adalcinsa, inda ya muhimmanta girmama ɗan Adam, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya yi wa mai furfura, da mahaddacin Alƙur'ani, da shugaba mai adalci ladabi, a matsayin hanya ɗaya ce daga cikin hanyoyin girmama Allah Maɗaukakin Sarki, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai a cikin girmama Allah akwai girmama Musulmi mai furfura, da mahaddacin Alƙur'ani da haddarsa bai kai shi zuwa ga wuce-gona- da – iri ba, sannan kuma bai ƙaurace wa Alƙur'anin ba, da kuma girmama shugaba mai adalci)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda bai tausaya wa ƙaramin cikinmu ba, bai kuma girmama babban cikinmu ba, bai kuma bayar da umurni da aikata abu mai kyau, da hana mummuna ba, ba shi a cikinmu)**.

Lallai ingantacciyar fahimta game da rangwamen Musulunci ba ta sharɗanta sai mai furfurar ya zamo Musulmi ba, domin ya zo a Hadisi cewa Manzon Allah (SallalLahu

alaiHi wa sallam) ya bayar da wani kaso ga wani gidan Yahudawa, kuma suna amsa a duk sanda ake rabawa. Ga kuma Sayyiduna Umar Bn Abdul'aziz (Allah ya ƙara yarda da shi) ya rubuta wa ɗaya daga cikin gwabnoninsa a Basra cewa: A ɓangarenka ka duba waɗanda suka tsufa, suka sami rauni, ya zamana samunsu ya ɗan ja da baya cikin kafiran amana, ka ba su abin da zai gyara al'amurransu daga Baitul - malin Musulmai..

**Haƙƙin al'umma ne akan ɗaiɗaikun mutanen ciki ne su kiyaye manyan maslahohin al'umma,** alal misali, idan muka ɗauki mas'alar ƙaruwar yawan al'umma, za mu iya tabbatar da abubuwa guda biyu:

**Na farko:** Wani yana kallon idan yana da iko, kuma ya zamo mawadaci.. shi ikon da ake nufi ba wai ya taƙaita akan kuɗi ne kawai ba, abu ne da ya haɗa da iko na kuɗi, da na iya tarbiyya, da duk abubuwan da hakan ya ƙunsa na ɓangarorin kulawa, ba kuma iko na mutum ɗaya ne abin kallo ba, a'a, abu ne da ya zarce ikon mutum a matsayinsa na shi ɗaya, ya kai ga iko daula wajen samar da dukan muhimman abubuwan da al'umma take buƙata, waɗanda mutane a ɗaiɗaikunsu ba za su iya samar wa kawunansu ba, saboda haka, daga nan za mu gane cewa lallai ikon da ƙasa, ko daula take da shi, shi ne muhimmin abin dubawa wajen magana akan ƙaruwar yawan al'umma, duk wanda kawai kansa ya sani, to sam ma bai cancanci da ya rayu ba.. Mummunan tasirin ƙarin yawan al'umma mara kan gado ba wai yana tsayawa akan mutum, ko dangi ɗaya ba ne kawai, a'a, abu ne da yake cutar da ƙasashen da ba sa amfani da ilimi wajen warware mas'alar ƙaruwar yawan haife - haife, haka ma ba a gwada yalwa, ko ƙunci a wannan mas'alar da mutane

ɗaiɗaiku nesa da yanayin ƙasashe, da kuma ƙarfin ikon tattali da suke da shi..

**Na biyu:** Lallai ƙanƙanuwar al'umma mai ƙarfi tafi alhairi akan al'umma mai tarin yawa da kuma rauni da ba ta iya taɓuka komai, wadda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sifanta ta da yayin da ruwan sama yake korowa, saboda yanayin da wasu ƙasashen suke ciki na gazawa wajen samar da muhimman kayan aiki, a ɓangarorin lafiya, da ilimi, da abubuwan more rayuwa, ga kuma yawa, shi ne zai kai su zuwa ga yawan karmamin da ruwa ya koro, kowane mai hankali ya san cewa idan aka sami cin karo tsakanin kyautata abu da yawaitarsa, to babu shakka kyautatarsa ne abin gabatarwa akan yawaitarsa, a nan ne kaɗan mai ƙarfi ya zarce yawa mai rauni sau dubu..

Saboda yawan da ya gadar da rauni, ko jahilci, ko ci baya, wanda ya zamo nauyin da ƙarfin da ƙasa take da shi ba zai iya ɗauka ba, hasali ma bai kamata ta ɗauka ba, to irin wannan yawan ne Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sifanta da yawan karmami, da yayin da babu wani amfani a tare da shi, yawa ne mai cutarwa, ba mai amfanarwa ba..

**Ya Allah Ubangijinmu, ka shiryatar da mu zuwa ga kyawawan ɗabi'un da babu mai iya shiryatar da mu zuwa gare su sai kai.. Ka kuma nesanta mu da munanan ɗabi'un da babu mai iya nesanta mu da su sai kai, ka sanya mu zamo cikin tsarkakan bayinka...**

- 27 –

## GINA INGANTACCEN TATTALIN ARZIKI DA TASIRINSA WAJEN WANZAR DA KWANCIYAR HANKALIN AL'UMMA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Allah shi ne ya halicce ku daga ƙasa, ya kuma nemi da ku raya ta))** **[Hud: 61]**, Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaidawa cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu bawansa ne, kuma Manzonsa, bayan haka:

Lallai tattalin arziki mai ƙarfi muhimmin jigo ne cikin jiga-jigan daula, ginshiƙi ne mai ƙarfi da ƙasa ba za ta iya gina komai ba idan babu shi, da ƙarfin tattalin arziki ne ƙasashe suke iya sauke nauyinsu na cikin-gida da na waje, suke kuma iya samar da nagartacciyar rayuwa ga 'yan ƙasa, a duk sanda tattalin arzikinsa ya yi rauni, to kuwa talauci da cututtuka, da rashin tabbas a rayuwa, da ƙaruwar matsaloli ne za su yaɗu, ɗabi'u za su gurɓace, laifuffuka za su yawaita, kuma hakan zai zamo wata dama ce ga maƙiya da suke jiran kowace irin dama, domin su yi amfani da ita wajen durƙusar da ƙasa, da jefa ta cikin ruɗani da rikicin da ba su da iyaka, saboda haka ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) a bayan kowace sallah

yake neman Allah ya yi masa tsari da talauci, yana cewa: **(Ya Ubangiji ina neman ka yi mini tsari da kafirci, da talauci, da azabar kabari)**.

Lallai duk al'ummar da ba ta iya samarwa da mallakan abincinta, da tufafinta, da magangunanta, da makamanta, to kuwa ba ta iya mallakan komai cikin sha'aninta, ba ta da ra'ayin kanta, ba ta da wata daraja da ƙima, masu hikima suna cewa: Ka kyautata wa duk wanda ka ga dama sai ka zamo sarkinsa, ka wadatu ga barin duk wanda ka ga dama, sai ka zamo sa'ansa, ka buƙaci duk wanda ka ga dama, sai ka zama bawansa.

Lallai addininmu mai daraja ya karantar da mu cewa, lallai hannu da yake a sama, yafi hannun da yake a ƙasa alhairi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: (Hannun sama yafi hannun ƙasa alhairi), haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: (Mai bayarwa shi ne a sama, mai roƙo kuma shi ne a ƙasa), kuma ko shakka babu, kan cewa wannan ma'anar ta game al'ummomi, da ma'aikatu, da iyalai, da ɗaiɗaikun mutane, babu wata al'umma, ko ma'aikata, ko iyali da za su cigaba sai sun bi wasu ƙa'idoji, a cikin ƙa'idojin akwai:

**Aiki wajen samar da abubuwan da ake buƙata:** A nan ba wai kawai ana buƙatar samar da abin da ake buƙata ba ne, har da kyautatawa wajen samarwa da shi, da inganta shi, da kuma ƙawata shi, da shiga fagagen da suka fi muhimmanci, waɗanda suka fi kawo alhairai ga tattalin arzikin ƙasa, lallai shari'a ta yi umurni da a yi aiki, a kuma samar da abubuwan buƙata, kuma haka wajibin ƙasa ce da ya hau kanmu, Allah mai girma da ɗaukaka ya bayar da umurnin a bazama cikin ƙasa; domin neman arziki, bayan an gabatar da haƙƙin Allah Maɗaukakin

Sarki, Allah mabuwayi yana cewa: **((Idan an kammala sallah, to ku bazama a cikin ƙasa, ku nemi falalar Allah, ku ambaci Allah sosai, ko za ku sami babban rabo))** **[al- Juma'a: 10]**, da aiki ne ake iya raya ƙasa, a kuma samar da halifancin da ɗan Adam yake yi a cikinta, da aiki ne mutum yake iya kare mutuncinsa, mai aiki sai dai ya bayar, shi ba ya roƙo, yana ciyarwa, ba kuma ya bara, babu shakka Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) sanya abin da mutum ya same shi da guminsa a cikin mafificin abin da zai iya sanyawa a cikin uwar hanjinsa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ɗan Adam bai taɓa cin wani abinci da yafi wanda ya same shi da guminsa ba, lallai Annabi Dawud (AlaiHis Salam) ma guminsa yake ci).** Lallai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya gargaɗi mutanen da suka zaɓi kasala da zaman hutu, da kuma yin bara wajen roƙon mutane, ya gargaɗe su da sharri, gami da azabar da za su same su, a inda yake cewa: **(Mutum ba zai gushe ba yana roƙo, har sai ya haɗu da Allah babu kunya a fuskarsa)**, Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: Ahir ɗinku da neman hutu, yin haka rafkana ne ɗungurungun ɗinsa.

Lallai addinin Musulunci ya ɗaukaka darajar aiki, inda ya sanya shi a matsayin mafi girma ibadu, wanda shi ne jahadi domin ɗaukaka kalmar Allah Maɗaukakin Sarki, bawa yana samun lada sakamakonsa, da a ce zai rasu a lokacin da yake neman arzikinsa, to kuwa lallai ya rasu ne akan hanyarsa ta yi wa Allah biyayya, an karɓo Hadisi daga Ka'ab Bn Ujrat (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: wani mutum ya wuce ta wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai Sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) suka ga irin yanda yake kazar-kazar da nishaɗi, sai suka ce: ya Manzon Allah, ina ma

fisabililLahi yake yi? Sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan ya fito ne domin ya nema wa ƙananan yaransa abinci, to ya fito ne fisabililLahi, haka ma idan ya fito ne saboda ya sami abin da zai iya ɗaukan nauyin iyayensa tsofaffi guda guda biyu, to ya fito ne fisabililLahi, haka ma idan ya fito ne domin ya nema wa kansa arziki domin ya samu ya kame, to lallai ya fito ne fisabililLahi, amma idan ya fito ne kawai saboda duniya ta ganshi, domin ya yi fankama, to a nan ya fito ne fisabilis- Shaiɗan)**. Game da kira zuwa ga yin aiki ne Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Idan lokacin tashin alƙiyama ya yi, alhali akwai iccen dabino a hannun ɗaya daga cikinku, idan dai har ya sami dama na ya dasa shi, to ya dasa)**.

Lallai (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan samar da mafita ga matsalar rashin aikin yi, da kuma yin amfani da duk wani ƙarfi da ake da shi, an karɓo Hadisi daga Anas Bn Malik (Allah ya ƙara yarda da shi), wani mutum cikin mutanen Madina “al-Ansar” ya zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana roƙonsa, sai ya ce masa: **(Shin babu komai a gidanka ne?)**, sai ya ce: akwai, tufafi ne da muke sanya wani daga ciki, sauran kuma mu shimfiɗa, da kuma ƙwaryar da muke shan ruwa, sai ya ce: **(Je ka kawo mini su),** ya ce: sai kuwa ya kawo su, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ɗauke su da hannunsa, ya ce: **(Wane ne zai sayi waɗannan?)** sai wani mutum ya ce: Ni ne, na saya dirhami ɗaya, sai ya ce: **(Wane zai yi ƙari akan dirhami ɗaya?)** har sau biyu, ko sau uku, sai wani mutum ya ce: na saya dirhami biyu, sai kuwa ya ba shi, ya amshi dirhami biyu ya miƙa wa wannan mutumin Madina, sai ya ce masa: **(Ka sayi abinci da dirhami ɗaya, ka bai wa**

**iyalanka, ɗayan kuma ka sayo ruwan guduma ka kawo mini)**, sai kuwa ya kawo, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya gyara masa ƙota da hannunsa, sanna ya ce masa: **(Ka tafi ka yi ta yin icce kana sayarwa, kada ka yarda ka dawo nan sai bayan kwanaki goma sha biyar)**, sai kuwa wannan mutumi ya tafi yana ta yin icce yana sayarwa, ya dawo da dirhami goma a hannunsa, ya ware wasu ya sayi tufafi, wasu kuma ya sayi abinci, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wannan kam ya fi akan ka zo ranar alƙiyama da wata alama a fuskarka, lallai roƙo bai halatta ba sai ga mutane uku: Ga wanda talauci ya tsananta masa, da kuma wanda bashi ya yi masa yawa, da kuma wanda diyya ta hau kansa, in bai bayar ba za a yi masa ƙisasi).**

**Rashin almubazzaranci:** Rashin yin almubazzaranci ginshiƙi ne wajen raya ƙasa, da samar da cigaban al'umma, lallai shari'ar Musulunci ta yi kira ga mabiyanta da su nesanci yin ɓarna, su kuma kyautata hanyar amfani da ni'imomin da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi masu a dukan ɓangarorin rayuwa, inda Allah mai girma da ɗaukaka yake cewa: **((Kada ka yi almubazzaranci da ya wuce ƙima, lallai masu almubazzaranci 'yan uwa ne na shaiɗan, shi kuwa shaiɗan mai tsananin kafirce wa Ubangijinsa ne)) [al- Isra'i: 26 -27]**, yana kuma cewa: **((Ku ci, ku sha, amma kada ku yi ɓarna, lallai Allah ba ya son maɓarnata)) [al- A'araf: 31]**, ƙarƙashin samun daidaito wajen yin amfani da arziki ne Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Ɗan Adam bai taɓa cika wani masaki mafi sharri da ya wuce cikinsa ba, 'yan lolomi kaɗan da za su ba shi karsashi sun ishe shi, in kuma ya zama dole, to ya raba cikinsa zuwa gida uku, kashi ɗaya na abinci, kashi**

**ɗaya na abin sha, kashi ɗaya kuma na numfashi).** Lallai mun tabbatar da cewa rashin almubazzarancin bai taƙaita kawai a fagen abinci da abin sha ba, a'a, ya karaɗe dukan ɓangarorin tattalin arziki, irin su ruwa, da wutan lantarki, da iskar gas, da sauran dukan abubuwan da muke amfani da su a rayuwarmu ,irinsu maganguna da sauransu, wannan shi ne abin da addinai suka kira mu zuwa ga gare shi, shi ne kuma abin da muka samu a cikin maganar Allah ta bakin Annabi Yusuf (AlaiHis Salam): **((Ya ce: za ku yi noma shekaru bakwai a jere, amfanin da kuka samu, ku bar shi a cikin zangarniyarsa, in banda kaɗan ɗin da za ku ci)) [Yusuf: 47]**, wannan kira ne zuwa ga ƙara yawan aiki ta hanyar yin aiki tuƙuru, da kuma rashin yin almubazzaranci daidai gwargwado, inda Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((in banda kaɗan ɗin da za ku ci)) [Yusuf: 47]**, bai ce "in banda wanda za ku ci ba".

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

---------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakon Annabawa da da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu, da Alayensa da Sahabbansa, da kuma waɗanda suka bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana a Musulunci:** Babu shakka babban ginshiƙi wajen gina ingantaccen tattalin arziki shi ne mutane su sauke dukan nauyin da ya rataya a wuyarsu, da kuma su nesanci mummunar ɗabi'ar nan ta ƙoƙarin amfana da hidindimun da ake gabatarwa ba tare da sun biya abin da ya rataya a kansu ba,

ko ƙaƙarin amfanuwa, da rashin biyan kuɗinsu, duk wanda yake amfana da abubuwa, ba kuma ya iya samar da su, ko yake amsar albashi, alhalin ba ya aiki, yake kuma amfana da hidindimun da ake gabatarwa, ba tare da ya biya kuɗin hakan ba, to kuwa lallai ne ya sani cewa yana da hannu wajen ci bayan ƙasarsa, da wajen durƙusar da tattalin arzikin ƙasa, ginshiƙin da yake ɗauke da tattalin arzikin ƙasa shi ne yanda 'yan ƙasa suke tasarrufi, da za mu buga misali da wutan lantarki, sai mu ce: an yi lokacin da wutar lantarki ta zamo mana matsala, sakamakon ɗauke wutar da ake yawan yi, hakan ya kai zuwa ga taɓarɓarewar hidindimun da ake gabatar wa 'yan ƙasa, abin da ya yi mummunan tasiri a ma'aikatun tattalin arziki na ƙasa, a gefe ɗaya kuma 'yan ƙasa suka ji a jikinsu, Amma –maganar gaskiya ita ce- ma'aikatar wutar lantarki ba za ta iya samar da wutar lantarki, da kuma kyautata ta ba, a daidai lokacin da 'yan ƙasa suke ƙin biyan kuɗin wutar lantarkin da suka amfana da ita, abin da biyan ne kawai zai sanya ma'aikatar da kamfanoninta su ƙara cigaba da sabunta waɗannan hidindimun, bugu da ƙari, su samar da kayayyakin da ake buƙata domin gudanar da aikin gyara tashoshi, da ma samar da sababbi, da kuma samar da makamashin da ake buƙata wajen haka, amma idan mutane suka biya kuɗin hidimar da ake gabatar masu, to a nan ne ma'aikatar za ta iya cigaba da gabatar da hidindimun da take gabatarwa, da kuma sabunta su, haka al'amarin yake a fannin jiragen ƙasa, da jiragen ƙarƙashin ƙasa, da sauran hidindimun da ake gabatarwa.

Ƙaurace wa biyan kuɗin hidindimun da ake gabatarwa da wasu mutane suke yi, ko kuma ƙoƙarinsu na cewa su ne kawai

za su amfana da su banda sauran mutane, lallai abubuwa ne da suka yi hannun-riga da karantarwar addini, da ma tsare- tsaren tattalin arziki masu adalci, hakan kuma yana kai wa ne zuwa ga durƙusar da ƙarfe tattalin arzikin ƙasashe, ta ma yiwu hakan ya kai zuwa ga faɗuwar tattalin arzikin a ƙasa warwas, inda haka yake nufin faɗuwar ƙasar.

Saboda haka, biyan duk wani abu da ya rataya a kanmu, a kuma cikin lokaci wajibi ne na shari'a; domin wannan shi ne yarjejeniyar da aka ƙulla tsakaninmu da masu gabatar mana da waɗannan hidindimun, irin su kamfanin wutar lantarki, da hukumar da take samar mana da ruwa.. sam bai halatta a ƙaurace wa biyan ba, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya umurce mu da cika alƙawari a inda yake cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, ku cika alƙawurranku))** **[al- Ma'ida: 1]**, wannan ayar mai girma ta game duk wani alƙawari da mutum zai ƙulla da waninsa.

A Hadisi mai girma, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Musulmai kam suna nan akan sharaɗin da suka yi a tsakaninsu, sai dai idan sharaɗin ya haramta halal, ko sharaɗin da ya halatta haram)**, a wata ruwayar: **(Musulmai suna kan sharaɗin da suka yi a tsakaninsu)**, lallai waɗanda suke ƙaurace wa biyan abin da suka ƙulla yarjejeniya a kansa, suna amfana da shi, amma ba sa biyan abin da ya rataya a wuyansu, sun munana ta fuskoki biyu: na farko: rashin cika alƙawari, na biyu kuma: suna amfana ne da haƙƙoƙin da ba nasu ba, suna kuma guje wa biyan abin da yake a wuyansu..

Saboda haka, ƙaurace wa biyan kuɗin hidindimun da ake gabatarwa haramun ne a shari'ance; domin rashin cika sharaɗin

da aka ƙulla ne a yarjejeniyar da aka yi, kuma wofintar da haƙƙoƙi ne, sannan kuma raunata ma'aikatun gwamnatoci ne.

Lallai muna ƙara tabbatar da muhimmancin yawaita shirye-shiryen da za su bayar da kariya ga al'ummarmu, kaman yanda muke ƙarfafa cewa: dole ne waɗannan hidindimun su isa zuwa ga waɗanda suka cancanta, musamman waɗanda suka fi buƙata, kuma dole ne kowa ya ɗabi'antu da ɗabi'un addini na kyawawan ɗabi'u, wanda bai cancanta ba ya kawar da kai, ya bar wannan shirin ya isa zuwa ga waɗanda suka cancanta.

**Ya Ubangiji ka taimake mu wajen sauke wajiban ƙasarmu da suke rataye a wuyanmu, ka kare Misrarmu, da saura ƙasashen duniya.**

- 28 –

## FIƘHUN GINA ƘASASHE

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ku yi taimakekeniya akan yi wa Allah biyayya da tsoronsa, kada ku yi taimakekeniya akan saɓon Allah da zalunci..))** **[al- Ma'ida: 2]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya, cikakken mabuwayi mai hikima.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Babu shakka kan cewa ɗaukacin al'ummomi suna aiki ne domin gina ƙasa mai ƙarfi da take da kwanciyar hankali, suna kuma yin hakan ne da dukan ƙarfi da arziki, gami da ikon da Allah ya ba su, saboda su isa zuwa ga manufofinsu, lallai gina ƙasashe ilimi da yake buƙata da ƙwarewa da sani, da kuma hango dukan yanayi da ƙalubalen da suke fuskantarsu, akwai bambanci mai girma tsakanin fiƙhun gina mutum a matsayinsa na shi kaɗai, ko gina wata ƙungiya, da fiƙhun gina ƙasashe da gudanar da su a wannan duniya mai matuƙar saurin sauyawa, duniyar da ba ta san komai ba sai ƙawance, da gammaya na siyasa, da na tattalin arziki, da na ilimi, inda dokoki da yarjejeniyoyin ƙasa da ƙasa suke hukunta tsakanin ƙasashen da suka cikinsu, lallai mai hankali ba zai taɓa iya kawar da

idanuwansa ga barin su ba, balle kuma daula, ko ta ce ba za ta yi ta'amuli da su ba, ko kuma ta nesanci tsara al'amurranta ƙarƙashin abubuwan da suke gudana a aikace ba.

Lallai ƙasa kariya ce, ƙasa aminci ne, ƙasa yarda da juna ne, ƙasa kwanciyar hankali ne, ƙasa tsari ne, ƙasa ma'aikatu ne, ƙasa wani gini ne na tunani, da siyasa, da tattalin arziki, da tsari da dokoki, idan babu ƙasa, to kuwa babu abin da za a samu sai tashin hankali da rashin tabbas.

**A cikin muhimman ginshiƙan gina ƙasashe akwai:** ƙarfafa ma'aikatun gwamnati, da kuma girmama doka da oda a ƙasa, ta yanda za a mutunta kundin tsarin mulki da adalci, wannan kuwa yana buƙatar dukan 'yan ƙasa su mutunta dokoki da tsare – tsaren ƙasa, da kiyaye dokokin zirga – zirga, da rashin karya ƙa'idojin tafiya a hanyoyi, ko yin gudun da ya wuce ƙima, da sauransu, cikin ƙa'idoji da dokokin da keta su karya dokokin hanya ne da shiga haƙƙoƙin mutane, wanda kuma hakan zai iya kai wa zuwa ga rasar da rayuka, ko jikkata mutane, ko shigar da su cikin razani, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ku somaku jefa kawunanku cikin halaka, ku kyautata, lallai Allah yana son masu kyautatawa)) [al- Baƙra: 195]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu cuta babu cutarwa)**.

Lallai kiyaye tsari da mutunta shi yana bayar da gudummuwa mai yawa wajen gina ƙasa mai ƙarfi gami da kwanciyar hankali; saboda dole ne a sami dokoki da ƙa'idoji a kowace al'umma da za su tsara rayuwar mutane, su kuma kiyaye wa ɗan Adam haƙƙoƙinsa, kuma kowa ya wajabta wa kansa sauke nauyin da yake a kansa, idan har aka rasa mutunta

tsari, da bin doka da oda, to lallai ƙasashe ba za su sami tabbatuwa ba, ba kuma za a isa zuwa ga adalci ba.

Lallai mutunta dokoki, da yi masu biyayya babban ginshiƙi ne na gina ƙasa, lallai samar da dokoki kariya ne ga ɗaukacin ‘yan ƙasa; saboda ba za a iya hararo wanzuwar ƙasa cikin zaman lafiya, da kwanciyar hankali, ba tare da mutunta dokoki, da bin su sau da ƙafa ba, dole ne kowane mutum ya ɗauki alhakin da ya rataya a wuyarsa wajen tabbatar da maslahar ɗaukacin al’umma da kowa da kowa ne zai ci amfaninta, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Dukanku masu kulawa ne, kuma kowa za a tambaye shi akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi: Shugaba mai kulawa ne, za kuma a tambaye shi akan waɗanda yake shugabanta, namiji ma mai kulawa ne a cikin iyalansa, za kuma a tambaye shi akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi, mace ma mai kulawa ce a gidan mijinta, za kuma a tambaye ta akan nauyin da aka ɗaura mata na kulawa, hadimi ma mai kulawa ne da dukiyar uban gidansa, za kuma a tambaye shi akan nauyin da aka ɗaura masa alhakin kulawa da shi, dukan ku masu kulawa ne, za kuma a tambayi kowa a akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi),** duk al’ummar da kowa ya kula da alhakin da ya rataya a wuyansa, to kuwa babu shakka al’umma ce dunƙulalliya, inda kowa ya san irin rawar da zai taka, yana kuma mutunta waninsa, lallai muna matuƙar buƙatar mutunta tsari da bin doka da oda, da kiyaye haƙƙoƙin sauran mutane, muddin dai muna son adalci ya karaɗe ko’ina, kowa ya ɗanɗani ni’imar aminci da tsaro gami da kwanciyar hankali, mu kuma sami ƙasarmu akan matsayin da ya yi daidai da ita a cikin al’ummomin duniya.

**A cikin manyan ginshiƙan gina ƙasashe akwai**: samar da tattalin arziki mai ƙarfi, lallai yana cikin muhimman jigogin da ba a iya gina ƙasa sai da su, tattalin arziki mai ƙarfi shi ne zai bai wa ƙasa dama na sauke alƙawurran da suke a kanta na cikin gida da na waje, ya kuma ba ta dama ta samar da rayuwa cikin karama ga ɗaukacin 'yan ƙasa, idan kuma tattalin arziki ya yi rauni, sai talauci da cututtuka su yaɗu, rayuwar mutane ta shiga cikin garari, kyawawan ɗabi'u su gurɓace, laifuffuka su yawaita, hakan kuma ya zamo wata dama ga maƙiya da suke dakon ƙasashe a koda yaushe, masu aiki wajen durƙusar da ita, da jefa ta cikin tashin hankalin da ba shi da ranar ƙarewa, lallai duk al'ummar da ba ta iya samar da muhimman abubuwan da take buƙata, ta yanda za ta riƙa dogara da waninta, to kuwa lallai ba ta da ra'ayin kanta, haka ma babu abin da za ta iya taɓukawa..

Lallai tattalin arziki mai ƙarfi ga ƙasa shi ne zai ba ta daman rayuwa cikin karama da izza a tsakanin ƙasashe; saboda haka ne ma addinin Musulunci ya muhimmanta kuɗi; ganin cewa shi ne ƙashin bayan rayuwa, rayuwa ba za ta tafi ba sai da shi..

**Gina ƙasashe ta ɓangaren tattalin arziki yana matuƙar buƙatar kyautata aiki, da kuma ƙara yawan samar da kayan amfani,** babu wata al'umma, ko ma'aikata, ko gida da zai sami cigaba, sai da aiki gami da kyautata aikin, ba wai kawai aiki da ƙara yawan abin da ake samarwa ne abin buƙata ba, dole ne a kyautata aikin, sannan a yawaita abin da ake fitarwa ta yanda tasirinsa na tattalin arziki zai shafi ɗaukacin 'yan ƙasa baki ɗaya, lallai Ubangijinmu ya zaburar da mu zuwa ga aiki, da kuma neman arziki a bayan ƙasa, Allah Maɗaukakin yana cewa: **((Idan aka gama sallar ranar juma'a, to ku bazama a bayan**

**ƙasa ku** nemi **falalar Allah, ku ambaci Allah da yawa, ko za ku samu babban rabo..))** **[al- Juma'a: 10]**, Mai girma da ɗaukaka ma yana cewa: ((**Shi ne wanda ya sanya ƙasa ta zamo maku sauƙaƙƙa, ku yi tafiya a sasanninta, ku ci daga cikin arzikin Allah da ya fitar maku daga gareta, zuwa gare shi -shi kaɗai-za ku koma domin sakamako**)) **[al- Mulki: 15]**, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya abincin da ya fi alhairi ga bawa shi ne wanda ya samar da shi da guminsa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ɗan Adam bai taɓa cin abinci mafi alhairi sama da wanda ya samar da shi da guminsa ba, lallai Annabin Allah Dawud (AlaiHis Salam) ya kasance yana cin abin da guminsa ya samar masa ne)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mutumin da ya yammanta yana mai dogaro da abin da ya samu da guminsa, to ya yammanta ne a matsayin wanda aka gafarta masa)**.

Game da kira zuwa ga yawaita samar da abubuwan da ake buƙata kuwa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idan da alƙiyama za ta tashi alhali a hannun ɗaya daga cikinku akwai iccen dabino, idan har ya sami daman dasa shi kafin ta tashi, to ya dasa..)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Musulmi ba zai taɓa dasa wata bishiya, ko ya shuka wata shuka, ta yanda tsuntsu, ko mutum, ko wata dabba za su ci daga ciki ba, face hakan ya zamo masa sadaka)**, lallai da ayyuka da kuma samar da abubuwan buƙata ne ƙasashe suke rayuwa, a kuma kiyaye mutuncinsu da karamarsu.

**Haka ma a cikin muhimman ginshiƙan gina ƙasashe akwai: samar da wayewa a fagagen al'adu, da addini, da tunani, da ilimi,** lallai rashin wayewa, ko ƙarancinsa ba za su taɓa bayar da gudummuwa wajen gina ƙasa mai ƙarfi da

kwanciyar hankali ba, saboda haka ne dole wayewar al'umma ta ƙaru, ra yanda kowa zai san abubuwan da suka wajaba akansa, da kuma haƙƙoƙinsa..

Wannan yana nufin a samar da ilimin da shi ne zai daidaita zukata, da tsarin rayuwar ɗaukacin al'umma, ta hanyar tarbiyyar ɗabi'u, da wayewa mai amfani, da kuma yaƙi da jahilci, saboda haka, dole ne ma'aikatun gwamnati su haɗa ƙarfi wajen samar da wayewar al'umma a fagagen al'adu, da addini, da tunani, da ilimi, abin da zai bai wa mutane daman sanin girman ƙalubalen da suke fuskantar ƙasa, da kuma yin aiki domin fuskantarsu, da kuma ƙalubalantar jita - jita, da mayar masu da martanin da zai daƙile tasirinsu tun ba su girma ba, da kuma rashin sauraron ƙare-rayi da jita - jitan da suke tayar da fitina, da niyya kawo rikici da tashin hankali a ƙasarmu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, idan wani fãsiƙi ya ƙetare shari'ar Allah ya zo maku da kowane irin labari, to ku bincika ku tabbatar da gaskiyarsa; saboda kada ku cutar da wasu mutane –da ba ku san haƙiƙaninsu ba-, hakan sai ya sanya ku yi nadama akan abin da kuka aikata, kuna: ina ma ba mu aikata hakan ba, a lokacin da bayani ya bayyana cewa ba su da wani laifi)) [al-Hujrat: 6].**

Haka ma dole ne mu zamo a farke idanuwanmu a buɗe, mu wa'aztu da wasunmu, mu kuma fa'idanta da tajribobin rayuwa da ƙwarewarmu akansu, tun ba yanzu ba Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, to ku yi taka - tsantsan...)) [an- Nisa'i: 71]**, haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ba a sarar mumini a**

**rami ɗaya har sau biyu)**, mu kuma sani cewa gina daula, da kuma ba ta kariya amana ne da ta rataya a wuyarmu baki ɗaya, kowa a fagensa za wurin aikinsa, muna kuma ƙara tabbatar da cewa lallai ginin ba zai taɓa kammaluwa ba, sai an daƙile duk wani yunƙuri na 'yan a fasa kowa ya rasa, wani mawaƙi yana cewa:

"Zuwa yaushe ne wannan ginin zai kai ƙarshe, muddin dai kana gini ne waninka kuma yana rusawa.."

Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ka taimaki ɗan uwanka a lokacin da yake azzalumi, ko lokacin da ake zaluntarsa, sai wani mutum ya ce: ya Manzon Allah, na san yanda zan taimake shi idan ana zaluntarsa, to yaya zan yi idan kuma shi ne azzulumin, yaya zan iya taimakonsa? Sai ya ce: ka katange shi, ko ka hana shi zaluncin, wannan shi ne taimakonsa)**, dole ne kowa daga cikinmu ya kame hannayen duk wani za zai aikata abin da zai kai zuwa ga karya doka, ko wanda zai cutar da maslahar ƙasa, kowa a daidai da inda yake da ikonsa, uba ya hani ɗansa, ɗan uwa ya hana ɗan uwansa, aboki ya hana abokinsa, kada mu zamo 'yan ba ruwanmun da ba mu san abubuwan da suke gudana a yankinmu ba, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Kada ku soma ka zamo 'yan amshin shata; kuna cewa: in mutane sun kyautata mu ma mu kyautata, in kuma sun yi zalunci, mu ma mu yi zalunci, ku dai kawai ku samar wa da kawunanku matsaya, in mutane sun kyautata, ku ma ku kyautata, in kuma sun munana, ku kada ku yi zalunci)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Misalin mutumin da yake tsaye akan iyakokin Allah, da wanda ya auka cikinsu, kaman mutanen da suka shiga cikin jirgin ruwa ne, wasu suka samu**

**wuri a sama, wasu kuma suka samu a ƙasa, sai ya zamana idan na ƙasan suna buƙatar ruwa sai sun biyo ta wurin waɗanda suke samansu, sai suka ce: da za mu huda wani wuri a inda muke, ta yanda ba za mu dami waɗanda suke samanmu ba, idan na saman suka barsu suka aikata abin da suka yi nufi, dukansu za su halaka, idan suka hana su, sai su tsira, sai dukansu ma su tsira)**.

Zamowar mutum mutumin kirki akan kansa, ba zai wadatar ba, a halin da muke ciki dole ne a cira gaba da matakin zamowa na kirki zuwa matakin kawo gyara ga ɗaukacin al'umma, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((A mafi yawan lokuta babu wani alhairi tattare da mutanen da suke ɓoye maganganun da suke yi a cikin zukatan su, ko waɗanda suke yi tsakanin su da juna; saboda sharri ne ake ɓoye shi, sai dai idan abin da aka ɓoyen ya zamo bayar da umurni ne da yin sadaka, ko aikata wani aiki mai kyau, ko daidaita tsakanin mutane da gyara zumunta, waɗannan kam duka alhairai ne, duk wanda ya aikata haka saboda neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki, to kuwa lallai Allah Maɗaukakin Sarki zai ba shi babban sakamako a nan duniya da lahira; saboda abin da ya aikata)) [an- Nisa'i: 114]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai Ubangijinka ba zai taɓa halakar da alƙarya kawai saboda zalunci ba, alhalin mazauna cikinta suna kawo gyara..)) [Hud: 117]**, lallai kawo gyara hanya ce ta Annabawa da Manzanni, da kuma shi ne ake samun tabbacin gina ƙasashe, da kiyaye haɗin kansu, da zamowarsu al'umma ɗaya, saboda bil'adama su rayu cikin aminci da tsarkin zukata, ba tare da rikici, ko rarrabuwar kawuna ba, ba kuma tare da tashin hakali,

ko ta'addanci ba, ba kuma tare da ɓarna a bayan ƙasa ta hanyar kisa da lalata kayan amfani ba..

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-----------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da salami shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwana Musulmai: A cikin muhimman ginshiƙan gina ƙasa da ba ta kariya akwai: gina rayuwar zamantakewa,** lallai addinin Musulunci ya mayar da hankali akan ƙarfafa dangantakar zamantakewa tsakanin al'umma, da taimakon juna, gami da tausayi tsakanin 'yan ƙasa ɗaya, da rashin cutar da sauran mutane, a ƙarƙashin maganar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yake cewa: **(Imanin ɗayanku ba zai cika ba, har sai ya so wa ɗan uwansa abin da yake so wa kansa)**, da maganarsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yake cewa: **(wallahi bai yi imani ba, wallahi bai yi imani ba, wallahi bai yi imani ba.. Sai aka ce: wane, ya Manzon Allah? Sai ya ce: wanda maƙwabcinsa bai aminta daga cutarwarsa ba),** a wani Hadisin kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mutumin da ya kwana a ƙoshe, amma maƙwabcinsa na kusa ya kwana da yunwa, alhalin yana sane, to lallai bai yi imani da ni ba)**.

**A cikin hanyoyin da ake bi wajen gina rayuwar zamantakewa akwai : ƙarfafa dangantakar iyalai**, abin da zai

kiyaye iyali da gida, lallai gida ne tobalin farko da ake gina rayuwar zamantakewa, gida ne ke bayar da kariya ga ƙananan yara, da kuma bunƙasar jikkinansu, da hankulansu, a gida ne ake samun ɗabi'un soyayya, da tausayi, gami ta taimaka wa marasa ƙarfi, a gida ne ake samun kyawawan ɗabi'u masu karamci, bege da ƙauna suke kukkutsawa ko'ina, sai dai duk da haka, al'amarin bai tsaya a nan ba, domin lallai akwai alhaki da ya rataya a wuyan gida wajen bayar da kariya ta musamman ga yaran da suke tasowa a cikinsa, domin Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Zunubi ya kai zunubi a ce mutum ya tozartar da wanda yake kulawa da shi)**.

Wane tozartarwa ne kuwa ya kai mutum ya wofintar da 'ya'yansa da suke su ne zuciyarsa, ta yanda zai miƙa su a hannun gurɓatattun tunani, ko zuwa ga ɓatattun ƙungiyoyi, ba kuma tare da ya sauke wajibin da ya rataya a wuyarsa na wayar da su game da hatsarurrukan da suke kewaye da mu ba, haka ma dole ne mu bayyana masu abubuwan da suka wajaba a kansu game da ƙasarsu, lallai kishin ƙasa gadonsa ake yi, Ahmad Shauƙiy yana cewa:

"Muddin muna raye za mu ba ki kariya, idan kuma mun rasu za mu gadar wa 'ya'yanmu su cigaba.. Ya Misra akanki za mu rasu, kaman yanda muka rayu a cikinki, ke ɗin ne dai za ki wanzu mu za mu fanshe ki".

**Haka ma a cikin muhimman ginshiƙan gina ƙasa akwai: ɗaukaka kyawawan ɗabi'u, da kuma kyawawan tadodi,** lallai duk al'ummomi da cigaban da ba a gina su akan kyawawan ɗabi'u ba, to al'umma ce ta je-ka na- yi ka, haka ma cigabanta na mai haƙin rijiya ne, hasali ma tana ɗauke da gatarin da zai

rusa ta, ya kawo ƙarshenta ne, tun ranar da aka fara samar da ita, da kyawawan ɗabi'u ne Musulmi yake hawa matakai na imani, ma'aunansa su yi rinjaye a wurin Allah, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu wani abu da ya fi sanya ma'aunin bawa mumini yin rinjaye a ranar alƙiyama kaman kyakkyawar ɗabi'a, lallai Allah yana ƙin mai alfasha, mai yawan zance kawai..)**, lokacin da aka tambayi (SallalLahu alaiHi wa sallam) game da abin da ya fi yawan shigar da mutane aljanna? Sai ya ce: **(Tsoron Allah, da kyakkyawan ɗabi'a)**, a wani wurin kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) kyawawan ɗabi'u a matsayin ma'auni na cikan imani, ko naƙasarsa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(A cikin muminai wanda imaninsa ya fi cika shi ne: wanda ya fi su kyawawan ɗabi'u…)**.

Lallai kyawawan ɗabi'u suna katange mai su daga faɗawa cikin alfasha, da kalmomi masu muni, Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: **((Misalin mummunar kalma tamkar mugunyiyar bishiya ce da aka ɗofana ta a saman ƙasa, ba ta da sauyoyi da za su tabbatar da ita)) [Ibrahim: 26]**.

**Muna roƙon Allah Maɗaukakin Sarki ya shiryatar da mu zuwa ga kyawawan ɗabi'u, da kalmomi masu daɗi da tsarki, ya kuma dawwamar mana da ni'imar tsaro da aminci da kwanciyar hankali, ya kuma kiyaye mana ƙasashenmu daga barin dukan munanan abubuwa da na ƙi. Amin.**

## - 29 –

## AMFANAR AL'UMMA A MA'AUNIN SHARI'A

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ku yi taimakekeniya da juna akan ayyukan biyayya da tsoron Allah, kada ku kuskura ku yi haɗa baki wajen saɓon Allah da zalunci))** **[al- Ma'ida: 2].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai masu yi wa hukunce - hukuncen Shari'ar Musulunci ingantacciyar fahimta za su ga cewa lallai hukunce – hukuncen sun zo ne domin biyan buƙatun bayi, da na ƙasa, da kuma ɗaukaka ruhin ɗan Adam zuwa ga babban matsayi, duk abin da zai biya buƙatun al'umma, to kuwa ya yi daidai da Shari'a, koda kuwa bai zo a Nassi ƙarara ba, duk kuma abin da ya ci - karo da maslahar al'umma, da amfanarsu, to kuwa lallai ba shi da asali a cikin Shari'ar Allah mai cike da tsarki.

Lallai addinin Musulunci bai san son – kai, da rashin shiga cikin ayyukan jama'a al'umma, ko nuna halin ko in kula ba, bai kuma san rinjayar da maslahar tsiraru akan maslahar al'umma

ba, abin da addinin Musulunci ya sani shi ne: abubuwan da al'umma gaba ɗaya ne za su amfana, da baiwa ta gaskiya, da taimakekeniya akan biyayya da tsoron Allah, waɗanda aka haɗa su da soyayya, da kuma fifita al'umma akan kai, har dai al'umma ta sami cigaban da ta sanya a gaba, a kuna samar da taimakekeniya tsakanin masu hali da marasa shi, ya zamana aikin da mutum yake yi, yana yi ne domin amfanar al'umma, hakan kuma ya zamo sanadiyyar ƙarfafa soyayya, da kishin ƙasa a cikin zukatan 'yan ƙasa, su ji kansu tamkar jiki ɗaya da idan wata gaɓa ta cutu, duka sauran gaɓoɓi za su kamu da rashin barci da raɗaɗi, alhairin Allah ya kai zuwa ga Ahmad Shauƙiy da yake cewa:

"Ƙasa ce da matasan cikinta suka rasu; domin ita ƙasar ta rayu, suka gusa domin al'ummarsu su rayu.."

Lallai babu shakka duk mai duba ta lura zuwa ga littafin Allah Maɗaukakin Sarki, zai fahimci cewa lallai babban manufa ta shar'anta wa mutane hukunce - hukunce ita ce tabbatar da maslahohin al'umma, ta hanyar jawo masu alhairi, da duk wani abu da zai amfane su, da kuma tunkuɗe masu duk wani abu mai cutarwa da yake da sharri ne, lallai Alƙur'ani mai girma ya tabbatar da cewa: kiyaye maslahar al'umma, da biya masu buƙatu shi ne manhajin Annabawa da Manzanni baki ɗaya, lallai Allah Maɗaukakin Sarki bai aiko kowane Annabi da Manzo ba, sai domin jin daɗin al'ummarsa, da kuma samar masu da dukan alhairi, ba tare da ya jira kowane irin fa'ida, ko amfani na duniya ba, Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗi ta bakin Annabi Nuhu (AlaiHis Salam) cewa: **((Ya ku mutane ne, ba fa kuɗi nake nema a wurinku ba, lada na yana wurin Allah ne kaɗai..)) [Hud: 29]**, haka ma Allah mai girma ya faɗi ta bakin

Annabinsa Ya'aƙub (AlaiHis Salam) cewa: **((Ya ku mutane na, ba fa kuɗi nake nema a wurinku ba, lada na yana wurin wanda ya halicce ni ne, ya kamata ku fahimci haka..))** **[Hud: 51]**. Ga ma Khalilur – Rahman, Annabi Ibrahim (AlaiHis Salam) yana roƙon Ubangijinsa Mai girma da ɗaukaka da wata addu'a, da take bayyana irin yanda yake kai - goro - da - mari wajen nema wa al'ummarsa alhairi, da kuma duk wani abu da zai amfane su, yana cewa: **((Ya Allah Ubangiji, ka sanya wannan garin cikin aminci da tsaro, ka azurta mutanen cikinsa -da suka yi imani da Allah da ranar lahira- da abinci iri - iri...))** **[al-Baƙra: 126]**, kuma kowa ya sani cewa abin da ake nufi da gari a wannan ayar shi ne mutanen garin. Haka ma ya roƙa masu arzikin da zai wadatar da su ga barin buƙatuwa zuwa ga waninsu, domin idan ƙasa ta zamo cikin aminci da tsaro, kuma ya zamana duk abubuwan da mutane suke buƙata akwai su a ciki, hakan babu shakka yana taimaka wa mazauna garin wajen yi wa Allah Maɗaukakin Sarki biyayya, cikin natsuwar zukata, da kwanciyar hankali, za kuma su yi aiki wajen samar da manufar Allah Maɗaukakin Sarki ta halitta, ta hanyar raya doron ƙasa, da kawo gyara a cikinta, domin Allah mai girma yana cewa: **((Shi Allah Maɗaukakin Sarki, shi ne ya halicce ku daga ƙasa, ya kuma nemi da ku raya ta..))** **[Hud: 61]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Kada ku yi ɓarna a bayan ƙasa bayan an riga an gyara ta...))** **[al- A'araf: 56, 85]**.

Lallai shari'ar Musulunci da Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zo da ita, ta zo ne domin ta ɗaukaka darajar wannan ƙa'ida ta mutuntaka, da kawo gyara a cikin al'umma, domin ta kafa ƙa'idojin kiyaye rayuwar zamantakewa a ƙarƙashin zaman lafiya, da kwanciyar hankali,

da kuma cigaban al'umma, da ɗaukakarta, ta hanyar gabatar da abin da amfaninsa zai karaɗe al'umma, akan taƙaitaccen amfanin da zai taƙaita da mutum ɗaya, ku wasu 'yan tsiraru, da kuma tsattsara abubuwa daidai da muhimmancinsu domin rayuwa ta tabbata, lallai tarihin rayuwar Annabi mai daraja da tsarki, da ta sahabbai masu karamci, cike suke da irin wannan babban abu da yake tabbatar da abin da muka ambata, alal misali:

An ruwaito Hadisi daga Ummul Muminina A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: (Da mun so mu ƙoshi da kuwa mun ƙoshi, amma dai kawai Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana fifita waninsa akan kansa), lallai (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana fifita waninsa akan kansa, da akan ma iyalan gidansa, duk kuwa da tsananin buƙatar da suke da shi, an ruwaito Hadisi daga Abu Sa'id al- Khudriy (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: wata rana muna kan tafiya tare da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai wani mutum ya zo akan abin hawansa, ya ce: sai ya fara kalle – kalle dama da hauni, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda duk yake da abin hawa ƙarin akan wanda yake a kai, to ya bai wa wanda ba shi da abin hawa, wanda duk yake da ƙarin guzuri akan guzurinsa, to ya bayar da shi ga wanda ba shi da guzuri)**, ya ce: haka ya yi ta faɗi nau'o'i iri – iri na dukiya, har sai da muka ga kaman babu wani da yake da haƙƙin ya mallaki sama da abin da yake buƙata.)

Hadisi ya zo a cikin Sahihul Bukhari, da Sahihu Muslim daga Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: Wata baiwar Allah miskiniya, ta zo wuri na tana ɗauke da 'ya'yanta guda biyu, sai na ba ta dabinai guda uku, sai kuwa ta bai wa

kowanne daga cikinsu dabino ɗaya, ta ɗauki ɗayan dabinon za ta kai bakinta, sai 'ya'yan nata suka nemi ta ƙara masu, sai kuwa ta raba masu wannan dabino da ta so ta kai bakinta, sai wannan abu da ta yi ya burge ni, na kuwa faɗa wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) abin da wannan mata ta yi, sai ya ce: **(Lallai Allah ya yi mata alƙawarin aljanna, ko ya 'yanta ta ga barin wuta)**, idan har wannan shi ne sakamakon wadda ta fifita 'ya'yanta akan kanta, ina kuma ga wanda ya fifita masu rauni da mabuƙata da miskinai?!

Ga kuma Sayyiduna Usman Bn Affan (Allah ya ƙara yarda da shi) a shekarar da aka yi fari, lokacin da talauci da yunwa suka addabi Musulmai, sai aka kawo hajarsa daga garin Sham, ga ta nan raƙuma dubu ne suke ɗauke da "burri" da "zabibi" (busasshen inabi), sai 'yan kasuwan Madina suka yi masa tsinke, sai ya ce masu: mene kuke so? Sai suka ce masa: lallai ka san mene muke so, ka sayar mana da wannan haja da ta zo maka, domin ka san irin yanda mutane suke buƙatarsu, sai ya ce: cikin soyayya da karamci, ribar nawa za ku sanya mini? Sai suka ce: akan kowane dirhami ɗaya za mu ƙara maka dirhami biyu, sai ya ce masu: an ba ni ribar da ta fi haka, sai suka ce : dirhami huɗu? Sai ya ce: an ba ni ribar da tafi haka, suka ce: dirhami biyar, sai ya ce: an ba ni ribar da ta fi haka, sai suka ce masa: Ya Abu Amru, a Madina babu wasu 'yan kasuwa bayan mu, babu kuma wanda ya riga mu zuwa wurinka, saboda haka wane ne ya yi maka wannan ƙari? Sai ya ce: Lallai Allah ya ba ni goma akan kowane dirhami ɗaya, shin za ku yi mini ƙari akan haka? Sai suka ce: a'a, sai ya ce: Na sanya Allah ya zama shaida, lallai duka abin da raƙuman nan suke ɗauke da su na bayar da shi sadaka ga miskinai da talakawan Musulmai.

Haka ma lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi nuni wa sahabbai da su sayi rijiyar Rumata, kasancewar ta ta wani Bayahude ne da ya wuce gona da iri wajen sanya kuɗin ruwanta da tsada, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wane zai sayi rijiyar Rumata, ya zamo ba shi da bambanci da sauran Musulmai wajen ɗibar ruwanta?)**, sai Sayyiduna Usman (Allah ya ƙara yarda da shi) ya tafi wurin wannan Bayahude ya nemi ya sayar masa, sai ya ƙi ya sayar masa duk cikanta, sai ya sayi rabinta akan kuɗi dirhami dubu goma sha biyu, ya kuma miƙa ta ga ɗaukacin Musulmai, sai ya zamana Sayyiduna Usman yana da kwana ɗaya, kwana ɗaya kuma na Bayahude. Idan ranar Sayyiduna Usman ta zo, sai Musulmai su ɗebi abin da zai ishe su na kwanaki biyu. Da Bayahuden ya ga haka, sai ya ce: ka ɓata mini rijiya ta, sai ɗaga ɗaya rabin, sai kuwa Sayyiduna Usman (Allah ya ƙara yarda da shi) ya saya akan kuɗi dirhami dubu takwas, a nan Sayyiduna Usman (Allah ya ƙara yarda da shi) ya amsa kiran Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ne ya sayi wannan rijiyar, saboda kiyaye maslahar al'ummar Musulmai baki ɗaya.

A zamanin Sayyiduna Umar Bn al- Khaɗɗaɗ (Allah ya ƙara yarda da shi), lokacin da Masallacin Harami ya yi wa mutane kaɗan, (Allah ya ƙara yarda da shi) ya tirsasa wa masu maƙwabtaka da Masallacin a kan su sayar da gidajensu, ya ce: **"Ku ne kuka zauna a Ka'aba, ba Ka'aba ne ya zauna akanku ba".**

Haka ma Sayyiduna Usman Bn Affan (Allah ya ƙara yarda da shi) ya yi a karo na biyu, ya ce: **"Lallai haƙuri na ne ya ruɗe ku, domin Umar ya yi maku haka amma ba ku ce komai ba"**, sannan ya bayar da umurnin a tsare su a matsayin "ta'aziri",

inda hakan yana nuna halaccin ƙwace mallakar mutum ɗaya, ko ta wasu ʻyan tsiraru saboda maslahar al'umma, kaman faɗaɗa hanyoyi, da maƙabartu, ko gina Masallatai, da samar da manyan katangu masu bayar da kariya, da gina hukumomin al'umma, irinsu: asibitoci, da makarantu, da sansanonin ʻyan gudun hijira, da makamanta haka; domin akan gabatar da maslahar al'umma akan maslahar mutum ɗaya, ko ta ʻyan tsiraru.

A nan muna ƙara tabbatar da cewa: lallai ingantacciyar fahimtar addini ta tabbatar da cewa a cikin sururin amfanar al'umma, da addininmu mai girma ya kwaɗaitar akai, ya kuma kira mutane zuwa ga su, akwai: lura da halin da mutane suke ciki, da kuma jera abubuwan da suke buƙata daidai da muhimmancin buƙatar al'umma, idan mutane suna buƙatar a gina masu asibitoci, da wuraren shan magani na talakawa da ba su kulawa ne, to hakan shi ne akan gaba, idan kuma al'umma tana buƙatar a gina makarantu ne, da cibiyoyin ilimi da tsattsara su yanda suka kamata, da bayar da kulawa ta musamman ga ɗaliban ilimi, to hakan shi ne a kan gaba, idan kuma an fi tsananin buƙatar sauƙaƙa wa marasa shi hanyar yin aure, da biyan bashin wanda bashi ya yi masu kanta, da yaye damuwar masu damuwa, to hakan shi ne akan gaba.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga cikamakin Annabawansa da Manzanninsa, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai

Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa (SallalLahu alaiHi wa sallam). Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai addinin Musulunci ya bai wa jera ayyuka daidai da muhimmancinsu, da buƙatuwa zuwa gare su muhimmanci, kai har a fagen gabatar da ayyuka na gari, idan an sami cin - karo tsakanin maslahar al'umma da ta mutum ɗaya, ko ta 'yan tsirarun mutane, to addininmu ya bayar da umurnin a gabatar da maslahar al'umma a kan gaba, domin maslahar al'umma ta kowa da kowa ce, amfaninta zai game gaba ɗaya, ita kuwa maslahar mutum ɗaya, ko ta 'yan tsiraru masu shi kawai za ta amfana, da a ce za a sami wani mutum da yake aiki a wata ma'aikata, da yake amsar albashi akan aikin nasa, amma kuma yakan kwashe tsawon dare wajen yin sallah da ƙiyamullaili, idan rana kuma ta yi, ya tafi wajen aikinsa a gajiye, ya kasa gabatar da aikin da ya wajaba akansa, ya zamo maslahar wannan ma'aikata ta lalace saboda shi, da ma maslahar al'ummar da wannan ma'aikatar take hidimta wa, shin wannan ba tozartar da amana, da cin dukiyar mutane ta hanyar ɓarna, da kuma riƙon sakainar kashi wa wajiban da suka rataya akansa ba ne? Da haka ya wofintar da wajiban da suka rataya a wuyarsa saboda nafilfili, kuma babu shakka yin hakan rashin fahimtar manufofin addini ne, alhairin Allah ya kai zuwa ga Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi), lokacin da yake jinyarsa da ya yi wafati a cikinta ya yi wa Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) wasici, a ciki yana cewa: **"Ka sani cewa, Allah yana da ayyukan da ya sanya su da**

**daddare, ba ya amsarsu idan aka gabatar da su da rana, yana kuma da ayyukan da da rana ne ya sanya su, ba ya amsa idan aka gabatar da su da dare, kuma lallai ba ya amsar nafila har sai a gabatar da farali.."**

Lallai ingantacciyar fahimtar addinin Allah Maɗaukakin Sarki da za ta yi daidai da zamaninmu da kuma halin da ake rayuwa a aikace, ta kuma kiyaye da lura da halayen mutane da buƙatunsu, ta sanya dole ne kada wurin fahimtar wasu mas'alolin Fiƙhu a tsaya kawai akan abubuwan da jinsu kawai aka yi, aka haddace, ba tare da an yi ninƙaya, ko zurfafa nazari akan manufofin "Fiƙhul Maƙasid", ko jera abubuwa, kowanne gwargwadon muhimmancinsa da buƙatuwa zuwa gare shi, ko halin da ake ciki, abin da dai zai iya yin sanadiyyar kore manyan manufofin Shari'ar Musulunci..

Ƙarƙashin irin wannan fahimta ta manufofin umurnin Shari'a mai tsarki, da kuma tsara, gami da jera muhimman abubuwa ne, muke ƙara tabbatar da cewa: lallai samar wa mutane da abubuwan da suke buƙata yana gaba da yawaita maimaita aikin Hajji da Umura; saboda ita biya wa mutane da al'umma buƙatunsu, ta hanyar sauƙaƙa wa matalauci, da biya masa buƙatunsa, ko bayar da sadaka a gare shi da abin da zai fitar da shi daga halin matsi, ko biya wa wanda bashi ya yi masa kanta bashin da ake binsa, duka suna cikin farillan kifaya, kuma kowa ya sani cewa gabatar da faralin kifaya yana gaba da gabatar da dukan nafilfili, cikinsu har da yawan maimaita ibadun Hajji da Umura.

Lallai muna matuƙar buƙatar yi wa addininmu ingantacciyar fahimta, da riskar girman hatsarin da yake tunkararmu, hakan kuma ya kai mu zuwa ga saurin gabatar da

ayyukan da za su amfani ɗaukacin al'umma akan ayyukan da ɗaiɗaikun mutane kawai suka shafa, ko ma mutum ɗaya tilo, idan ayyukan suka ci karo da juna, za mu yi hakan ne muna masu yi wa addininmu biyayya, muna kuma kwaɗayin cigaba da ƙasashenmu zuwa ga matakan da suka dace da su, suka kuma yi daidai da zamanin 'ya'yanmu.

**Ya Allah Ubangiji ka kare mana ƙasashenmu, da jama'anmu, da jami'an tsaronmu da suke hana idanuwansu barci wajen ba mu tsaro, ka kare mu daga dukan sharri da abubuwan ƙi.**

- 30 –

## MA'ANAR SHAHADA TSAKANIN GASKIYA DA ƘARYA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Kada ku soma ku kira wanda aka kashe shi a wajen ɗaukaka kalmar Allah da sunan "matacce", a'a, rayayyu ne su, ku ne dai ba ku sani ba)) [al-Baƙra: 154]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki a cikin sunnoninsa ya hukunta cewa: yakan zaɓi waɗanda ya so daga cikin bayinsa, ya ɗaukaka darajarsu, ya kuma fifita al'amurransu, ya kuma kwarara masu karamcinsa da albarkarsa, ya yawaita masu kyaututtukansa da jinƙansa.. Babu shakka matsayin shahada ɗaya ne daga cikin muƙaman wannan zaɓi da Allah mai girma da ɗaukaka yake yin bai wa da shi ga wanda ya so a cikin halittarsa, Allah mai tsarki yana cewa: **((Duk wanda ya yi wa Allah da Manzon Allah biyayya, to lallai waɗannan su ne suke tare da waɗanda Allah ya yi masu ni'imomi cikin**

**Annabawa da Siddiƙai da Shahidai da mutanen kirki, lallai zama da waɗannan kam abu ne da ya yi kyau matuƙa..))** **[an-Nisa'i: 69]**, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Saboda Allah ya sanar da waɗanda suke yi imani, ya kuma ɗauki shahidai daga cikinsu…))** **[Ali Imran: 140]**.

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya keɓance shahidai da darajoji masu yawa, a cikin waɗannan darajoji akwai:

**Girman matsayinsu da kusancinsu da Allah, da kuma lada da ni'imomin da ya tanada masu,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Su kuwa shahidai suna da lada, gami da haske a wurin Ubangijinsu…))** **[al- Hadid: 19]**, lallai wannan babban matsayi da daraja ne gami da kusanci da Ubangiji, kuma babban lada ne mai haɗe da cikakken haske da zai baibaye su ta ko'ina, Imam Masruƙ (Allah ya yi masa rahama) ya ce: Wannan matsayi ne da aka keɓanci shahidai da shi, babu abin da yake nuna irin wannan matsayi, kaman irin yanda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi kwaɗayin samun shahada a wajen ɗaukaka kalmar Allah Maɗaukakin Sarki, saboda Allah ya ba shi ladan wannan babban matsayi, an ruwaito (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Na rantse da wanda rayuwa ta take hannunsa, wallahi na yi burin a kashe ni a hanyar ɗaukaka kalmar Allah, sannan a sake raya ni, sannan a sake kashe ni, sannan a sake raya ni, sannan a sake kashe ni, sannan a sake raya ni, sannan a sake kashe ni)**; wannan kuwa saboda girman abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya tanadar wa shahidai ne.

**A cikin darajojin da Allah ya keɓanci shahidai da su akwai:** kasancewarsu a raye a wurin Ubangijinsu yana azurta su, rayuwa ba irin rayuwarmu ba, rayuwa ce da ta fi ƙarfin

tunanin ɗan Adam ya iya riskarta, bugu da ƙari, ga shi suna cikin zukata al'umma a raye, ba a mantawa da ambatonsu, komin daren-daɗewa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ku soma ku kira waɗanda aka kashe su a wajen ɗaukaka kalmar Allah da sunan "matattu", a'a, ayayyu ne su, ku ne dai ba ku sani ba)) [al- Baƙra: 154]**, An karɓo Hadisi daga Sayyiduna Jabir Bn Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya haɗu da ni, sai ya ce: **(Ya Jabir na ga duk jikinka ya yi sanyi ne?)** sai na ce: Ya Manzon Allah, mahaifi na ne ya yi shahada, ya kuma bar ƙananan yara, ga bashi a kansa, sai ya ce: **(Shin ba na yi maka albishir da abin da mahaifinka ya taras ba?)**, sai na ce: Na'am ya Manzon Allah, a yi mini albishir, sai ya ce: **(Allah bai taɓa yin magana da kowa ba, sai ta bayan hijabi, amma mahaifinka raya shi Allah ya yi, ya kuma yi magana da shi ba tare da hijabi ba),** ma'ana shi da shi ba tare da shamaki, ko ta hanyar ɗan saƙo ba, sai ya ce masa: **(Ya bawana, yi burin da kake so, ni kuwa zan ba ka),** sai ya ce: ya Ubangiji ina roƙon ka sake raya ni, a kashe ni saboda kai a karo na biyu, sai Ubangiji mai girma da ɗaukaka ya ce: **(Ai lallai na riga na hukunta cewa in an taho wurinmu babu komawa)**, sai ya ce: sai aka saukar da wannan ayar: **((Kada ka soma ka zaci cewa waɗanda aka kashe su wajen ɗaukaka kalmar Allah matattu ne, a'a, a rayayyu ne su a wurin Ubangijinsu yana azurta su)) [Ali Imran: 169].**

**A cikin darajojin da Allah ya keɓanci shahidai da su akwai kuma: labarin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayar na karamci mai girma da Allah Maɗaukakin Sarki yake yi wa shahidai**, gami da kyaututtuka masu daraja, a Hadisin da

(SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Shahidi yana da tagomashi guda shida a wurin Allah: A daidai lokacin da ɗigon jininsa ya ɗiga ana gafarta masa zunubansa, za kuma a nuna masa mazauninsa a aljanna, za kuma a tseratar da shi ga barin azabar wuta, za a amintar da shi daga barin babban razani na ranar alƙiyama, za kuma a yi masa ado da tufafin imani, za kuma a aura masa matan aljanna "Hurul in", za kuma a ba shi dama ya ceci mutane saba'in daga cikin danginsa)**, da kuma inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Na rantse da wanda rayuwa ta take hannunsa, ba za a taɓa ji wa wani rauni a hanyarsa ta ɗaukaka kalmar Allah ba –Allah kaɗai ya san wanda ake ji wa rauni dominsa- face ranar alƙiyama ya zo da launi irin launin jini, amma ƙamshinsa na almiski ne).**

A nan muna ƙara tabbatar da cewa babu wanda zai sami wannan matsayi, da ƙololuwar daraja da Allah mai girma da ɗaukaka ya tanadar wa shahidai, sai shahidai na gaskiya, domin akwai shahidai na gaskiya, akwai kuma waɗanda aka kashe su a banza, shahidi na gaskiya shi ne wanda yake bai wa ƙasarsa kariya daga duk wani ɗan ta'adda, yake kuma sadaukar da rayuwarsa saboda ita, domin kare turɓayarta, da bai wa 'yan uwansa da duk wani da yake rayuwa a ƙasarsa kariya saboda neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki, darajar ƙasa da mutunci, ba sa ƙasa da darajar rai, da addini, da dukiya, suna cikin manyan manufofin da Shari'ar Musulunci ta ƙarfafa wajen wajibcin ba su kariya, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam ya ce: **(Duk wanda aka kashe shi wajen kare dukiyarsa shahidi ne, wanda aka kashe shi wajen kare iyalansa, ko wajen kare ransa, ko wajen kare addininsa, to lallai shahidi**

**ne shi),** wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) sai ya ce: Ya Manzon Allah, ya kake gani idan wani mutum ya zo yana son ya ƙwace mini dukiya ta? Sai ya ce: **(Kada ka ba shi dukiyarka)**, sai ya ce: idan ya yaƙe ni fa?, sai ya ce: **(Ka yaƙe shi)**, sai ya ce: to idan ya kashe ni fa?, sai ya ce: **(Ka zama shahidi)**, sai ya ce: idan na kashe shi fa?, sai ya ce: **(Ya shiga wuta)**.

Shi kuwa wanda aka kashe shi a banza da yake sheƙar da jinin waɗanda ba su ji ba, ba su gani ba, ba kuma tare da wata hujja ba, yake kuma shigar da tsoro a cikin zukatan 'yan ƙasa, yake kuma barazana ga tsaronsu da amincinsu, yake kuma aiki wajen yaɗa ɓarna da tashin hankali a doron ƙasa, yake sanya amintattun 'yan ƙasa cikin garari ta hanyar ƙunar- baƙin- wake, da tayar da nakiyoyi na ta'addanci da babu wani addini da zai lamunci haka, kuma babu wani hankali da zai yarda da haka, wannan kam lallai ba shahidi ba ne, sifanta shi da shahidi a nan ƙarya ce kawai, babu ƙamshin gaskiya a ciki, sauya magana ce daga wurinta na asali..

Lallai bayanin da cibiyar addinin Musulunci ta Al-Azhar ta fitar a ranar 23/2/2019 domin raddi akan wasu abubuwa da ƙungiyoyin 'yan ta'adda suke faɗi, bayanin ya tabbatar da cewa shahidai na gaskiya su ne waɗanda suke bai wa ƙasarsu kariya ga barin kowane irin 'yan ta'adda, suke kuma sadaukar da kawunansu domin bai wa doron ƙasarsu da ma sararin samaniyar ƙasar, da iyalansu da masu rayuwa a cikin ƙasar kariya, ba waɗanda suke tsoratar da 'yan ƙasarsu, suka kuma barazana ga tsaronsu da amincinsu, suke kuma yaɗa ɓarna da tashin hankali a ko'ina a faɗin ƙasa ba.

Kowa ya san cewa wajibi ne Musulmi ya zamo mai cika alƙawari, kuma mai son ƙasarsa, mai ba ta kariya da duk abin da yake da shin a Magana, ko aiki, kuma lallai son ƙasa yana cikin imani, wannan ne abin da aƙidar Musulunci da Sunnar Annabi suke tabbatarwa, hasali ma duk wani mai ingantacciyar fiɗira, da lafiyayyen hankali akan haka yake.

Babu shakka hukumar bayar da fatawa ta ƙasar Misra ta fitar da fatawowi iri- iri da suke sifanta ire – iren waɗannan ayyuka da ta'addanci, kuma aikata su wani nau'i ne daga cikin nau'o'in kashe kai, wanda yake cikin manyan laifuffuka da zunubai a wurin Allah Maɗaukakin Sarki; domin wanda ya aikata haka jahili ne da ya auka da rayuwarsa zuwa ga halaka, Allah Maɗaukaki yana cewa: **((Kada ku soma ku kashe kawunanku))** **[an- Nisa'i: 29],** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda ya kashe kansa da makami, to za a ba shi wannan makamin nasa a hannunsa ya yi ta soka wa cikinsa a cikin wutan jahannama zai kuma dawwama a cikinta har abada),** Imam an- Nawawi ya yi wa wannan Hadisin babi na musamman a sharhin da ya yi wa "Sahihu Muslim", yana cewa: "Babin tsaurara haramci akan mutum ya kashe kansa, kuma duk wanda ya kashe kansa da wani abu, to za a yi masa azaba da shi a cikin wuta", irin wannan mutumi da masu kama da shi ne ayar nan take magana akansu: **((Wanda aka ƙawata masa mummunan aikinsa sai ya ganshi a matsayin kyakkyawa..))** **[Fatir: 8].**

A nan muna son mu bayyana cewa: masu aikata irin waɗannan ayyuka na ƙunar- baƙin wake mabiya ne na masu wuce gona da iri cikin Khawarijawa, da waɗanda suke bin hanya irin tasu cikin ƙungiyoyin da suke ɓatar da mutane,

waɗannan dai da suke kafirta al'umma, suke kuma halatta jininsu.

Lallai bin hanyar tayar da nakiyoyi, da rusa gidajen al'umma da lalata kayayyakinsu, da bin hanyar kisan mummuƙe da kisan gilla, da ƙunar baƙin wake duka abubuwa ne da suka haramta a cikin shari'ar Musulunci, babu wani saɓani a kan haka, domin dai duka sun saɓa da Nassoshin addini da suke bayyana wajibcin kiyaye rayuwa da ƙasa da dukiyoyi, lallai Shari'ar Musulunci mai daraja ta haramta mutum ya halaka kansa ta kowace hanya, ta haramta mutum ya sanya rayuwan mutane a cikin garari, ta haramta yin ɓarna a bayan ƙasa..

Lallai addinin Musulunci ya ƙarfafa wajen bayyana haramcin zubar da jini, da kuma wajibcin kare rayuka, gamammiyar huɗubar da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi a ranar "Hajjatul wada'i" ta fara ne da cewa: (Lallai haramun ne ku yi wa junanku ta'addanci a cikin jininku da dukiyoyinku da mutuncinku, kaman yanda yaƙi ya haramta a wannan rana, da wannan gari da kuma wannan wata, kada ku yarda ku zamo kafirai –ko ɓatattu- a bayan ba ni, ko koma kuna kashe junanku), a wani Hadisin kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mutum zai cigaba da zama cikin sauƙi a addininsa matuƙar ba ya zubar da jinin da Allah ya haramta a zubar da shi ba ne)**, An karɓo Hadisi daga Abdullahi Bn Umar (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: Na ga Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana ɗawafi a Ka'aba, yana cewa: **(Wane abu ne ya kai ki ƙamshi, kuma wane ƙamshi ne ya kai naki?.. wane abu ne ya kai ki girma, kuma wane girma ne ya kai naki?, Na rantse da wanda rayuwar Muhammadu take**

**hannunsa, wallahi alfarmar mumini na dukiyarsa da jininsa sun fi alfarmarki a wurin Allah, kuma wallahi muna zaton hakan alhairi ne).**

Lallai addinin Musulunci ya hana a kashe ran da Allah ya haramta a kashe ba tare da wani dalili ba, ya kuma tanadi azaba mai tsanani ga duk wanda ya kuskura ya aikata haka, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: ((**Lallai duk wanda ya kashe mumini da gangan, saboda ta'addanci, ya kuma ga haka yana** mai **ganin cewa ya aikata halal, to, sakamakon da zai yi daidai da wannan babban laifi shi ne shiga cikin wutar jahannama da dawwama a ciki, Allah kuma zai yi fushi da shi, ya kore shi daga rahamarsa. Lallai Allah ya tanadar masa da babbar azaba a ranar lahira, tabbas wannan shi ne babban laifin da ba shi da tamka a duniya))** **[an- Nisa'i: 93].**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

--------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Tsira da aminci su tabbata da amintaccen Annabi. Ya Allah ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk waɗanda suka bi hanyarsu da kyautatawa.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai isa zuwa ga manyan manufofi a cikin rayuwa yana buƙatar sadaukar da kai gwargwadon girman waɗannan manufofin da darajarsu, babu sadaukar da kan da ya kai mutum ya miƙa rayuwarsa wajen bai wa ƙasarsa da mutuncinsa da karamarsa kariya.

A yanzu ɗin nan da muke sake miƙa jinjina ga "Ranar shahidai" ta duniya, dole ne mu ƙara tunatar da kawunanmu

da waɗanda rayukansu suka koma zuwa ga Allah mai girma da ɗaukaka, waɗanda suka sami babban rabo a cikin sojojinmu jarumai, da 'yan sandanmu masu ƙwazo, da sauran 'yan ƙasanmu masu daraja da suka rasa rayukansu a fagen ƙalubalantar 'yan ta'adda rundunonin sharri.

Waɗannan su ne shahidai gwazara na gaskiya, akwai bambanci mai girma tsakanin gaskiya da ƙarya, waɗannan su ne gwarazan da suka raya ruhin karama da mutunci da izza da ɗaukaka a cikin zukatanmu, su ne suka iya ɗaura Misra a matsayinta da kwarjininta, har yanzu ba su daina sadaukar da kawunansu wajen yaƙi da ta'addanci da 'yan ta'adda ba, ba su daina yaƙi da ƙungiyoyin da suke kafirta Musulmai ba, ƙungyoyin da suke ɓatattu ne kuma masu ɓatar da mutane, kuma lallai muna da yaƙinin cewa nasarar Allah Maɗaukakin Sarki tana tare da mu.

Lallai muna yi wa kawunanmu fatan samun shahada wajen kare ƙasarmu, saboda me ba za mu yi wannan fata ba? alhalin (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya roƙi Allah ya ba shi shahada da gaskiya, to kuwa Allah zai kai shi matsayi irin na shahidai, koda kuwa a shimfiɗarsa ne ya rasu).**

Lallai wajibin ƙasarmu da yake a kanmu gaba ɗaya a wannan lokacin shi ne: mu bai wa ƙasarmu kariya daga duk wani maƙiyi ko hatsari da yake barazana ga zaman lafiyarmu, mu kuma cigaba da aiki da duk irin ƙarfin da Allah ya ba mu wajen gina ƙasarmu, addininmu addini ne da yake sana'anta fannin rayuwa ba fannin mutuwa ba, addini ne na gini da raya ƙasa, ba addinin ɓarna da rusa rayuwar al'umma ba, dole ne mu haɗa kai domin daƙile duk wani sharri da makirce- makirce

mabambanta da ake ƙullawa ƙasarmu, makirce- makircen da manufarsu ita ce: su durƙusar da Misra da al’ummar Misra… dole ne ‘yan ƙasa na gari su fito su sadaukar da kawunansu wajen kare rayukansu da jininsu da dukiyoyinsu domin su kare ƙasarsu, lallai Misra ita ce garkuwar Larabawa, kuma ƙahon zuciyar Musulunci, ba ta kariya abu ne da shari’a ta wajabta, haƙƙi ne na addini, cin mutuncin Misra, cin mutuncin Musulunci ne a fakaice, yunƙuri ne na raunana ƙasashen Musulmai, ya zama dole mu tsaya a sahu ɗaya wajen ba ta kariya ga barin ɓarnar maɓarnata, da makircin makira, da muguntar mugaye.

**Ya Ubangiji ka azurta mu da yin shahada wajen ɗaukaka kalmarka, ka sanya mu zamo cikin nagartattun bayinka, ka kare mana ƙasarmu daga dukan makirce – makirce da abubuwan ƙi.. Amin.**

- 31 –

## MA’ANAR SHAHADA DA MATSAYIN SHAHIDAI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Su kuwa shahidai suna da lada gami da haske a wurin Ubangijinsu))** **[al- Hadid: 19]**. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana da **bayin da ya zaɓe su, kuma keɓance su da darajar shahada**, Allah mai girma yana cewa: **((An yi haka ne domin Allah ya jarrabi muminai; a kuma bambance waɗanda suka tabbata akan imani, a kuma karrama wasu mutane da matsayin yin shahada akan hanyar sa..))** **[Ali Imran: 140],** saboda girma da darajar shahada ne ma’anonin sunayenta suka yawaita, shahidai ne su; saboda Allah Maɗaukakin Sarki da Mala’ikunsa (Alaihimus Salam) sun yi masu shaidar cancantar shiga aljanna.. Shahidai ne su, saboda su rayayyu ne a wurin Ubangijinsu da yake azurta su.. Shahidai ne su saboda suna ganin abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya tanadar masu na ni’imomi, shahidai ne su saboda sun ga gaskiyar alƙawarin da Allah mai girma ya yi masu, da ma

wasu ma'anonin masu kyau, waɗanda suke ƙara wa kalmar shahada girma da daraja, suke kuma bayyana matsayin shahidai a wurin Ubangijinsu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai ayyukan waɗanda aka kashe su wajen ɗaukaka kalmar Allah ba za su taɓa ɓaci ba. Da sannu Allah zai shiryatar da su, ya kuma natsar masu da zukatansu. Zai kuma shigar da su aljannar da ya yi masu bayani))** **[Muhammad: 4 – 6]**.

Babu abin da ya kai a yi fata na gari wajen samun rahamar Allah, sama da **mutumin da ya sadaukar da rayuwarsa saboda ƙasarsa**, da ba ta kariya, ya kuma rasu saboda haka, inda zai sami matsayin shahada, wannan kam kasuwanci ne mai riba da sam babu asara a ciki, Allah Mai girma yana cewa: **((Lallai tabbas Allah Maɗaukakin Sarki ya sayi rayukan muminai da dukiyoyinsu akan zai ba su aljanna..))** **[at- Tauba: 111]**, lallai muƙamin shahada ɗaya ne daga cikin manyan muƙamai a wurin Allah Maɗaukakin Sarki.

Ita shahada akan hanyar Ubangiji Maɗaukakin Sarki ta kasu kashi – kashi ne, mafi girma da matsayin cikinsu, ita ce **shahadar da ake yi wajen fuskantar maƙiya, saboda bai wa ƙasa kariya, da neman yardar Allah mai girma da buwaya,** Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya fi so sama da ɗigo biyu, da kuma tabbai biyu; ɗigon hawayen da ya fito sakamakon tsoron Allah, da ɗigon jinin da aka sheƙar saboda Allah Maɗaukakin Sarki, tabbai biyun kuma su ne: tabon da aka ji wa mutum akan hanyar Allah, da tabon alamar farali daga cikin farilan da Allah mai girma ya farlanta)**.

Akwai nau'o'i na shahada da ba sa ƙasa da daraja gami da matsayin wannan, a cikinsu akwai: **duk wanda ya yi shahada**

**wajen bai wa ƙasarsa kariya, ko bai wani wani abu na cikin kayan albarkatun ƙasa kariya, ko ta dalilin aikinsa da yake yi domin cigaban ƙasa**; kaman ɗan sanda da yake tsare wuraren ibada, da wanda yake kare masu zuwa yawon shaƙatawa a ƙasarmu, da wanda yake bai wa wuraren kayan tarihi kariya, wanda zai yi shahada saboda ikhlasinsa wurin gabatar da aikinsa, da fatansa na ganin ya gabatar da aikinsa kaman yanda ya kamata, da duk wanda yake bin irin wannan gwadaben, to dukansu suna yi ne fisabililLah, kaman ma'aikacin da yake kiyaye dukiyar al'umma, ya kuma yi shahada saboda haka.

Haka ma **wanda aka kashe wajen bai wa kansa kariya, ko bai wa waninsa, ko wajen kare mutuncinsa, ko mutuncin waninsa, ko wajen kare dukiyarsa, ko dukiyar waninsa**, shi ma shahidi ne, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda aka kashe shi wajen kare dukiyarsa shahidi ne, wanda aka kashe shi wajen kare ransa shahidi ne, wanda aka kashe shi wajen kare addininsa, wanda aka kashe shi wajen kare iyalansa shahidi ne),** duka waɗannan suna bai wa ƙasarsu, da albarkatun cikinta ne kariya, suna kare dukiyoyi, da rayuka, da mutuncin da addinin Musulunci ya haramta yi masu ta'addanci, ya kuma bayar da umurnin a kiyaye su, a kuma ba su kariya, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Jinin Musulmi da dukiyarsa da mutuncinsa sun haramta wani Musulmi ya keta su)**.

Ganin cewa shahada wata babbar kyauta ce da Allah mai girma da buwaya yake bayar da ita ga mafifitan halittunsa, bayan Annabawa, da Manzanni, hakan ya sanya suke a mafifincin matsayi a ranar alƙiyama, a cikin sakamakon da shahada take gadarwa akwai: **lalali shahidai ba sa fuskantar**

**tsanani wurin rasuwa**, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Shahidi ba ya jin zafin kisa, sai gwargwadon irin yanda kowannenku yake jin sukar allura)**, **suna kuma samun aminci ga barin azabar kabari da fitinar cikinsa,** wani mutum ya ce: Ya Manzon Allah, mene ya sanya dukan muminai ana fitinarsu a cikin kabari, in banda shahidi shi kaɗai?, sai ya ce: **(Ai kuwa sarar takubban da suke kansa sun isa fitina)**, haka ma **ayyukansu na gari ba sa yankewa har abada**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ana dakatar da ayyukan duk wanda ya rasu banda wanda yake ribaɗi saboda Allah, shi kam lallai za a cigaba da bunƙasa ayyukansa har zuwa ranar alƙiyama, a kuma ba shi aminci ga barin azabar kabari)**, **suna kuma da lada mai yawa, da manyan kyaututtuka**, lallai shi shahidi **"Ana gafarta masa ne tun farkon tunkuɗowar jininsa, za kuma a nuna masa mazauninsa a aljanna, a kuma tseratar da shi ga barin azabar kabari, a kuma amintar da shi ga barin razani mafi girma".**

Haka ma za a tashi shahidi a ranar alƙiyama ne cikin karamci, inda zai rinƙa ƙamshin almiski, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Na rantse da wanda rayuwa ta take hannunsa, ba za taɓa ji wa wani rauni a hanyarsa ta ɗaukaka kalmar Allah ba –Allah kaɗai ya san wanda ake ji wa rauni dominsa- face ranar alƙiyama ya zo da launi irin launin jini, amma ƙamshinsa na almiski ne).**

**Wannan kenan, ina neman wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki..**

-----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabinmu Muhammadu da Alayensa da Sahabbansa, da waɗanda suka biyo bayansu.

**Ya ʻyan uwana Musulmai:** Lallai shahidanmu masu tsarki za su cigaba da dawwama a cikin tarihin al'umma, a matsayin misalai na sadaukar da kai, da gwarzantaka, da daraja, da kuma zamowarsu abin koyi, **Allah Maɗaukakin Sarki ya so ne ya karrama su da rayuwa ta haƙiƙa, ta kuma har abada, rayuwar da ba ta da kama**, Allah Mai girma yana cewa: **((Kada ku taɓa zaton cewa waɗanda aka kashe akan hanyar Allah matattu ne, a'a, a raye suke, rayuwar da Allah ya bar wa kan sa sani, suna nan wurin Ubangijin su ana azurta su da arziki mai faranta rai da Allah ne kawai ya sani. Farin-ciki da murna sun lulluɓe fuskokin su sakamakon abin da Allah ya ba su na wasu abubuwa da aka keɓance su da su saboda falalar sa, suna kuma farin-ciki da murna da 'yan uwan sun da suka bari a raye a duniya suna tsaye akan hanyar imani da jahadi, da cewa lallai babu tsoron wani abin ƙi da zai same su, ba kuma sa baƙin-ciki saboda wani abu da suke so da ya kuɓuce masu. Fuskokin shahidai suna walƙiya saboda baiwar da Allah ya yi masu na ni'imar shahada, da ni'imar aljanna, da babban karramawar da aka yi masu, lallai shi Allah ba ya tozartar da ladan muminai))** **[Ali Imran: 169 -171]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ruhinsu suna cikin wasu korayen tsuntsaye, suna da fitilu da suke rataye a Al'arshi, suna kai- komonsu a cikin aljanna zuwa duk inda suke so, sannan su dawo zuwa wurin waɗannan fitilun, sai Ubangijinsu ya yi masu wata duba, ya ce: Shin akwai wani**

**abu da kuke sha'awa? Sai su ce: wane abu ne kuma za mu ji sha'awarsa, alhalin ga mu muna kai – komonmu a cikin aljanna zuwa duk inda muke so, aka yi masu haka har sau uku, da suka ga ba za a ƙyale su ba tare da tambaya ba, sai suka ce: Ya Ubangiji, muna son a mayar da ruhinmu cikin gangar jikkunanmu, saboda a sake kashe mu akan hanyarka, sa ya ga ba su da wata buƙata, sai ya barsu)**.

Lallai duk wanda ya roƙi Allah mai girma da buwaya shahada da gaskiya tare da ikhlasi, Allah Maɗaukakin Sarki zai kai shi matsayinta, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya roƙi Allah shahada da gaske, Allah zai kai shi muƙamin shahidai, koda kuwa ya rasu akan shimfiɗarsa)**, duk wanda aikinsa shi ne bai wa addininsa da ƙasarsa kariya, da kiyaye albarkatun ƙasar, aka kuma kashe shi akan hanyar Allah, to shahidi ne shi.

Madalla da duk wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓe shi, ya ba shi shahada, ya girmama shi da abokantakar Annabawa da Siddiƙai da salihai, wane kusanci da abokantaka ne suka kai wannan, Allah mai girma yana cewa: **((Duk wanda ya yi wa Allah Maɗaukakin Sarki da Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) biyayya, ya miƙa-wuya a gare su, ya yarda da hukuncinsu, to, yana cikin waɗanda Allah ya yi masu ni'imar shiriya da dacewa a duniya da lahira, cikin Annabawansa da mabiyansu da suka gasgata su suka kuma bi hanyarsu, da waɗanda suka yi shahada a hanyar ɗaukaka kalmar Allah, da salihan bayin da zukatansu da ayyukansu suka kyautatu, wasu abokan tafiya ne suka fi waɗannan nagarta? Lallai abokin zamansu ba ya taɓewa, ba kuma ya ƙosawa da zantuttukansu)) [an- Nisa'i: 69].**

**Ya Allah Ubangiji ka yi rahama ga shahidanmu, ka kiyaye mana ƙasarmu, da sauran ƙasashen duniya.**

- 32 –

## FALALAR SHAHADA DA ALHAKIN IYALAN SHAHIDAI AKANMU

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Kada ku taɓa zaton cewa waɗanda aka kashe akan hanyar Allah matattu ne, a'a, a raye suke, rayuwar da Allah ya bar wa kan sa sani, suna nan wurin Ubangijin su ana azurta su da arziki mai faranta rai da Allah ne kawai ya sani. Farin-ciki da murna sun lulluɓe fuskokin su sakamakon abin da Allah ya ba su na wasu abubuwa da aka keɓance su da su saboda falalar sa, suna kuma farin-ciki da murna da 'yan uwansun da suka bari a raye a duniya suna tsaye akan hanyar imani da jahadi, da cewa lallai babu tsoron wani abin ƙi da zai same su, ba kuma sa baƙin-ciki saboda wani abu da suke so da ya kuɓuce masu. Fuskokin shahidai suna walƙiya saboda baiwar da Allah ya yi masu na ni'imar shahada, da ni'imar aljanna, da babban karramawar da aka yi masu, lallai shi Allah ba ya tozartar da ladan muminai)) [Ali Imran: 169 – 171].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya halicci ɗan Adam ne domin ya raya ƙasa, ya kuma gyara ta, kuma Allah mai girma da buwaya ya kiyaye wa ɗan Adam duk wani abu da zai taimaka masa wajen wannan rayawar, ya kuma kewaye ran ɗan Adam –wanda shi ne taklifi yake hawa kansa- da wata katanga da ta sanya yin masa kowane irin ta'addanci –ko ɓarna a bayan ƙasa- daidai yake da yi wa ɗaukacin bil'adama ta'addaci, duk kuma wata kariya –ko gyara a bayan ƙasa- da za a yi wa ran ɗan Adam daidai yake da bayar da kariya, gami da kawo gyara ga ɗaukacin bil'adama, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Duk wanda ya kashe rai ba ta hanyar ƙisasi ba, ko ya aikata ɓarna a bayan ƙasa, tamkar ya kashe ɗaukacin mutane gaba ɗaya ne, wanda kuma ya raya rai guda ɗaya tamkar ya rayar da ɗaukacin mutane gaba ɗaya ne)) [al- Ma'ida: 32].**

Manufar raya doron ƙasa, da bunƙasa ta tana cikin manyan manufofin da ba sa tabbatuwa sai da sadaukar da kai mai girma daga mutanen da suka yi wa addininsu da ƙasarsu ikhlasi, suka kuma san ƙimar addininsu da ƙasarsu, da kuma ƙimar rayuwa cikin zaman lafiya, da kwanciyar hankali, sai suka sadaukar da kawunansu, da dukiyoyinsu; domin isa zuwa ga wannan manufar, suka shiga cikin wani kasuwanci mai riba tare da Ubangijinsu mai girma da ɗaukaka, wannan kuwa kasuwanci ne da ba zai taɓa yin tazgaro ba, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai Allah ya sayi rayukan muminai, da dukiyoyinsu daga gare su, akan lallai zai ba su aljanna, suna yaƙar waɗanda suka auka masu da yaƙi fisabililLahi, su kashe, a kuma kashe su, lallai Allah ya yi masu alƙawari na gaskiya a cikin littattafan Attaura da Injila da Alƙur'ani, wane ne ya fi Allah cika alƙawarinsa; saboda haka ku yi albishir da**

**wannan kasuwanci da kuka yi da shi, wannan kam shi ne babban rabo mai girma))** **[at- Tauba: 111]**, sai aka saka masu da jinsin irin abin da suka aikata, inda Allah ya tabbatar masu da mafi alhairin abin da suka nufi su samar wa waninsu, a sakamakon haka sai Allah Maɗaukakin Sarki ya azurta su da rayuwa mai cike da kyau, da daɗi, da kwanciyar hankali, ta kuma har abada, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ku soma ku kira waɗanda aka kashe su a wajen ɗaukaka kalmar Allah da sunan "matattu", a'a, rayayyu ne su, ku ne dai ba ku sani ba))** **[al- Baƙra: 154].**

Shahada wajen ɗaukaka kalmar Allah muƙami ne mai matuƙar girma, manufa ce daga cikin manya manufofin da ba sa faruwa sai ga zaɓaɓɓun Allah Maɗaukakin Sarki a cikin bayinsa, Allah mai girma yana cewa: **((Ya zaɓi shahidai daga cikinku..))** **[Ali Imran: 140]**, lallai shahada baiwa ce daga Allah mai girma da ɗaukaka zuwa ga wanda yake sonsu a cikin halittunsa bayan Annabawa, da siddiƙai, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Duk wanda ya yi wa Allah da Manzon Allah biyayya, to lallai waɗannan su ne suke tare da waɗanda Allah ya yi masu ni'imomi cikin Annabawa da Siddiƙai da Shahidai da mutanen kirki, lallai zama da waɗannan kam abu ne da ya yi kyau matuƙa..))** **[an- Nisa'i: 69]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana tseratar da su daga barin azabar kabari, da kuma razanin ranar alƙiyama, lallai wani mutum ya ce: Ya Manzon Allah, mene ya sanya ake fitinan muminai a cikin kaburbura kawai banda shahidai? Sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ai sarar takubban da suka ratsa kawunansu sun isa fitina)**, lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya tambayi Mala'ika Jibrilu (AlaiHis Salam) game da ayar da take cewa:

**((Sai aka hura ƙaho, take duk wanda yake a sama da ƙasa ya ɗimauce, sai dai kawai waɗanda Allah ya so..))** [az- Zumar: 68], **(su wane ne waɗanda Allah bai so ya razanar da su ba?) sai ya ce: (Su ne shahidai)**, lallai matsayin shahidai ya kai matsayi a maganar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yake cewa: **(Kowane mamaci aikinsa yakan tuƙe, in banda masu zaman dako wajen ɗaukaka kalmar Allah, su kam ladan ayyukansu za su cigaba da gudana har zuwa lokacin da za a tashe domin alƙiyama)**.

Saboda haka ne duk wanda Allah ya azurta shi da shahada, ya kuma ga falala da matsayin da aka tanada masa, yake fatan ina ma a ce yana da daman dawowa duniya; domin ya sake samun shahada ɗaya bayan ɗaya, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai babu wani daga cikinku da zai shiga aljanna, ya kuma so ya sake dawowa duniya, koda kuwa yana mallakan komai da yake a doron ƙasa banda shaihdi, shi kam yana burin ya sake dawowa a kashe shi sau da yawa, saboda irin karamcin da ya tarar)**, babu abin da ya fi nuni zuwa ga wannan falalar kamar maganar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yake cewa: **(Na rantse da wanda rayuwa ta take hannunsa, wallahi na yi burin a kashe ni a hanyar ɗaukaka kalmar Allah, sannan a sake raya ni, sannan a sake kashe ni, sannan a sake raya ni, sannan a sake kashe ni, sannan a sake raya ni, sannan a sake kashe ni)**.

Saboda haka ne sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) suka fi kowa kwaɗayin samun shahada, lallai suna matuƙar rajin samunta, suna kuma rige- rige wajen riskarta, ga Sayyiduna Amru Bn al-Jamuh (Allah ya ƙara yarda da shi) nan, sahabi ne na Annabi, kuma gurgu, ya yi fatan ya tafiya yaƙin Badar,

Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) bai aminta masa ba; saboda lalurar gurguntaka da yake da ita, a lokacin yaƙin Uhdu sai ya ce wa 'ya'yansa: ku ɗauke ni mu tafi, sai suka ce masa: Ai Manzon Allah ya ɗauke maka fita yaƙi, sai ya ce masu: ai kuwa ba ku isa ba! Ranar Badar kun hana ni shiga aljanna, yanzu ma so kuke ku hana shiga a ranar Uhdu? Ya dage sai da ya fita, ya zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce: ya Manzon Allah, shin duk wanda aka kashe shi a yau zai shiga aljanna? Sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ey),** sai ya ce: Na rantse da wanda numfashi na yake hannunsa, ba zan koma zuwa ga iyalai na ba, har sai na shiga aljanna, sai Sayyiduna Umar Bn al-Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce masa: Ya Amru, banda cika wa Allah baki, Sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: (Umar ka yi a hankali, a cikin mutane akwai waɗanda idan ya rantse da Allah akan abu, to kuwa Allah zai kuɓutar da su, Amru Bn al-Jamuh yana cikinsu, zai shiga aljanna da gurguntakarsa).

Ganin cewa Musulunci addini ne na mutnci, da gwarzantaka, da mazakutantaka, da kamewa, da kiyaye rayuka, da mutunci, da dukiyoyi, da haƙƙoƙi, saboda haka ne kiyaye duka waɗannan suke cikin imani, bai wa waɗannan kyawawan ɗabi'u da ladubba tsaro da kariya suna cikin manyan manufofinsa, duk wanda ya rasu akan hanyarsa na tabbatar da waɗannan abubuwa, to kuwa shahidi ne shi, ita shahada ba ta taƙaita kawai akan nau'i guda ɗaya ba; a'a nau'o'i ne iri- iri, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda aka kashe shi wajen kare dukiyarsa shahidi ne, wanda aka kashe shi wajen kare addininsa shahidi ne, wanda aka kashe shi wajen kare ransa shahidi ne,**

**wanda aka kashe shi wajen kare iyalansa shahidi ne shi),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(.. wanda aka kashe shi shahidi ne, wanda gini ya ruso masa shahidi ne, wanda ciwon ciki ya yi sanadiyyar rasuwarsa shahidi ne, wanda ruwa ya ci shi shahidi ne, wanda namun daji suka kashe shi shahidi ne, wanda maciji, ko kunama suka sare shi ya rasu shahidi ne, wanda ya cutar tarin- fuka "tuberculosis" ta yi sanadiyyar rasuwarsa shahidi ne, haka ma wanda ya rasu a filin dakon hana maƙiya saƙat saboda ɗaukaka kalmar Allah shahidi ne, mai biƙi ma shahida ce, wanda ya rasu akan shimfiɗarsa, amma yana son kalmar Allah ta ɗaukaka, kalmar kafirai kuma ta ƙasƙanta shi ma shahidi ne)**, haka ma ba a hana mutumin da ya roƙi Allah samun shahada da niyya ta gaskiya, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda ya roƙi Allah ya ba shi shahada da gaskiya, to kuwa Allah zai kai shi matsayi irin na shahidai, koda kuwa a shimfiɗarsa ne ya rasu).**

Lallai shahidi na gaskiya shi ne wanda ya rungimi gaskiya, ya kuma tsarkake niyyarsa, ya kuma sadaukar da rayuwarsa saboda Allah, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce: **(Wanda ya yi yaƙi saboda kalmar Allah ta ɗaukaka shi ne yake yi fisabililLah),** lallai shahidi yana da babban matsayi a duniya da lahira, a duniya za a ambaci sunansa da jinjinawa, a kuma gadar da haka ga al'ummomi masu tasowa a matsayin abin buga misali wajen sadaukar da kai, da mazakutantaka, da girma, lallai da sannu shahidanmu za su cigaba da wanzuwa a cikin hankulanmu, da zukatanmu, muna tuna su da jinjinawa da ganin girmansu, komin nesa da yawan al'ummomin da za su zo a baya kuwa, a ranar lahira kuma, haka za a tashe su cikin

alfahari, da girma da ƙayatarwa, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Na rantse da wanda rayuwa ta take hannunsa, ba za a taɓa ji wa wani rauni a hanyarsa ta ɗaukaka kalmar Allah ba –Allah kaɗai ya san wanda ake ji wa rauni dominsa- face ranar alƙiyama ya zo da launi irin launin jini, amma ƙamshinsa na almiski ne)**.

Lallai shahidanmu masu tsarki sun sadaukar da kawunansu ne saboda wasunsu su rayu, sun kuma bar iyalansu a bayansu, tabbas suna da wasu haƙƙoƙi da wajibai akanmu, a cikinsu akwai: **dole ne mu girmama su, muna masu jinjina masu a sakamakon irin abin da iyayensu suka gabatar,** lallai babu wanda zai san falalar masu falala sai mai falala, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shin sakamakon kyautatawa zai zamo wani abu ne ba kyautatawa ba?))** **[ar- Rahman: 60]**, haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ba ya gode wa mutane, to kuwa ba ya gode wa Allah)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya yi maku abin kirki, to ku saka masa, idan ba ku sami abin da za ku saka masa da shi ba, to ku yi masa addu'a ta yanda za ku ji cewa kun saka masa)**, wane abin kirki ne kuwa ya kai mutum ya miƙa rayuwarsa saboda ya fanshi ƙasarsa da mutuncinsa.

A cikin haƙƙoƙinsu da suke a kanmu akwai: **kada mu bari su ji cewa sun rasa uba mai ɗaukan nauyinsu,** za mu yi haka ne ta hanyar ɗaukan nauyinsu, da zama tare da su a wasu lokuta, da sanya masu farin ciki, da kyautata yi masu mu'amala, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan ɗauki nauyi iyalan shahidai, ya kuma bai wa 'ya'yansu kulawa, haka ya yi wa iyalan Sayyiduna Ja'afar Bn Abuɗalib (Allah ya

ƙara yarda da shi) da ya yi shahada a rana yaƙin Mu'uta, ya bar yara ƙanana, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ɗauki nauyinsu, ya kula da su cikin rausasawa da tausayi, ya riƙe su bayan wafatin mahaifinsu.

**Wannan kenan, ina neman wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki..**

------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Tsira da aminci su tabbata da amintaccen Annabi, ya Allah ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk waɗanda suka bi hanyarsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai a cikin abubuwan da suka wajaba akanmu game da iyalan shahidanmu akwai: **dole ne mu samar masu da rayuwa mai cike da aminci da kwanciyar hankali,** tabbas iyayensu sun yi shahada ne saboda su samar mana da rayuwa, kuma lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya lamunce wa duk wanda yake bayar da kulawa ta musamman ga iyalan shahidai da 'ya'yansu, ya lamunce masu samun lada, inda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Duk wanda ya ɗauki nauyi samar wa mai yaƙi saboda Allah kayan yaƙi, to shi ma ya yi yaƙin, duk kuma wanda ya wakilci mayaƙi a cikin iyalansa cikin alhairi, to shi ma ya yi yaƙin)**, abin ake nufi da ya wakilce shi a cikin iyalansa shi ne: ya ɗauki nauyinsu, ya ba su kulawa, ya samar masu da abubuwan da suke buƙata, sakamakon haka sai ya sami lada irin na wanda ya yi shahada, haka ma kulawa da iyalansu yabawa ne da abin da suka gabatar, kuma tamkar mun sauke wani sashe ne na abin da ya wajaba akanmu, Hadisi ya zo a

cikin Sahihul Bukhari daga Zaid Bn Aslam, shi ma daga babansa, ya ce: **wata rana ni da Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) mun fita zuwa kasuwa, sai wata mata mai ƙaramin shekaru ta yi sauri ta zo wurin Umar, ta ce: ya Amiral Muminina, mijina ya rasu ya bar mini ƙananan yaran da ko ƙafafuwan tumaki ba za su iya girkawa ba, ba kuma su da koda gona guda ɗaya, ba su kuma da dabbobin da za su rinƙa tatsar nono daga gare su, ina tsoron kada damisa ta cinye su, ni 'yar Jafafu Bn Ima'u al- Ghifariy ce, mahaifina ya halarci sulhun Hudaibiyya tare da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai Umar ya tsaya tare da ita, bai wuce ba, sannan ya ce: maraba da wannan dangantaka ta kusa, sannan ya tafi zuwa wurin raƙumin Zuhair da yake a ɗaure a gidan, sai ya ɗaura masa buhu biyu da ya cika su da abinci, sannan a tsakiyarsu ya ɗaura kuɗi da tufafi, sannan ya miƙa mata da kayan gaba ɗaya, ki ja wannan ki tafi, ba zai ƙare ba Allah zai kawo maku wani alhairin, sai wani mutum ya ce: ya Amiral muminina ka cika mata fa, sai Umar ya ce masa: kai dai kuwa tir, wallahi kaman ina ganin mahaifinta da ɗan uwanta sun yi wa wata katanga ƙawanya, sannan suka buɗe ta, a dalilin haka muka sami ganima, har muka sami rabo daga ciki.**

A wannan abu da ya faru, mun ga irin yanda Amirul muminina Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) ya bayyana mana abin da ya wajaba mu aikata game da shahidai, dole ne mu faɗi ayyukan alhairin da suka aikata, sannan kuma ya bayyana mana abin da ya wajaba mu yi wa iyalansu bayan babu su, abu ne da za mu iya yinsa a wannan zamanin a aikace, dole ne –mutane a ɗaiɗaiku, da ma cibiyoyi- mu bayar da cikakkiyar kulawa da 'ya'yan shahidai, saboda mu sanya su ji

daɗi, mu kuma nuna yabawa ga ayyukan da iyayensu suka gabatar.

Haka ma a cikin wajiban: **dole ne mu kyautata ilmantar da 'ya'yansu, mu kuma ba su muƙaman da suka cancanta,** a nan mu yi koyi da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam); lallai yana bayar da kulawa ga iyalan shahidai, yana ɗaukan nauyin 'ya'yansu kaman yanda ya kamata, alal misali ga irin yanda (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi wa Sayyiduna Usamat Bn Zaid nan (Allah ya ƙara yarda da su); mahaifinsa, Sayyiduna Zaidu Bn Harisat (Allah ya ƙara yarda da shi) ya yi shahada a ranar yaƙin Mu'uta, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ɗauke shi, ya kula da tarbiyyarsa, da ba shi ilimi, har sai da ya zamo mafi ƙanƙantar kwamandan yaƙi a tarihi gaba ɗaya, lokacin koda shekaru ashirin bai kai ba, inda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ba shi jagorancin yaƙi, a cikin waɗanda yake jagoranta akwai manyan sahabbai, game da haka ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan ma kun soki jagorancinsa, to da ma can haka kuka soki jagorancin mahaifinsa kafin shi, na rantse da Allah ya cancanci ya yi jagoranci, duk kuwa da cewa yana cikin mutanen da na fi so, lallai wannan ma yana cikin mutanen da na fi so a bayansa)**.

**Muna kuma yi wa iyalan shahidai, da 'ya'yansu albishir** da kiyayewa gami da kulawar da Allah Maɗaukakin Sarki yake masu, saboda karamcin iyayensu, lallai alƙawarin Allah ba ya tashi, lallai Allah yana jiɓintar al'amurran salihan bayinsa, **lallai Allah ya sanya wannan gyaruwa ta iyayensu zai dawo wa 'ya'yansu da alhairi a duniya da lahira,** lallai Allah ya wakilta bayinsa salihai guda biyu; saboda wasu yara marayu su biyu;

waɗannan salihan su ne: Sayyiduna Musa, da Sayyiduna Khidhir (Alaihimas Salam), domin su kiyaye masu dukiyarsa da taskar da aka bari masu, duka wannan saboda a karrama iyayensu ne guda biyu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shi kuwa wannan katanga na wasu yara marayu ne su biyu a wannan garin, a ƙarƙashinsa akwai wata taska tasu, mahaifinsu mutumin kirki ne, sai Allah Ubangijinka ya nufi su girma su kai ƙarfinsu, su samu su fito da taskar tasu, wannan kam tausayi da rahama ne daga Ubangijinka, ba wai da yin kai na na yi ba..)) [al- Kahfi: 82]**. A lahira kuma, Ubangijinsu zai haɗa su da iyayensu saboda ya karrama su, koda kuwa aikinsu ya yi ƙaranci, Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Waɗanda suka yi imani, suka kuma sami babban daraja, 'ya'yansu kuma suka bi hanyarsu da imani, koda kuwa ba su kai darajar iyayensu ba, za mu sada su da zuriyarsu; domin mu kwantar wa iyayen da hankali, ba kuma tare da mun tauye masu komai na ladan ayyukansu ba, ba kuma za a ɗaura wa iyayen nasu komai na laifin zuriyarsu ba; saboda kowane mutum shi ne zai ɗauki alhakin aikinsa, ba za a kama waninsa da shi ba)) [at- Tur: 21].**

Dole ne mu san cewa: lallai sadaukar da kan da shahidanmu suka yi abin tinƙaho ne ga ƙasarmu, abin alfahari a zuciyar kowane ɗan ƙasa mai kishin ƙasa, sakayyar wannan sadaukar da kai shi ne kowanne daga cikinmu ya zamo sojan ƙasa a fagen da yake, ya yi iya abin da zai iya wajen hidimta wa ƙasa, dukanmu mu haɗu a sahu ɗaya wajen ƙarfafa sojojinmu da 'yan sandanmu da sauran ma'aikatun gwamnati, muna ƙara tabbatar da cewa ma'aikatun gwamnatinmu su ne tudun- na-tsira ga al'ummarmu, dole ne mu fito mu ƙalubalanci masu kira

zuwa ga fitina, da tashin hankali cikin ƙungiyoyin masu wuce gona da iri, da na 'yan ta'adda, waɗanda ma sam ba su yi imani akwai ƙasa, ko daula ba, waɗanda suke gabatar da maslahar ƙungiyoyinsu akan maslahar daula, lallai waɗannan ƙungiyoyi babban hatsari ne da yake ƙalubalantar addininmu da daularmu, saboda haka ƙalubalantarsu, da kawo ƙarshen gurɓattun tunani da fahimtarsu wajibi ne na addini, da na ƙasa, da na mutuntaka.

**Ina roƙon Allah mai girma da buwaya, ya lulluɓe shahidanmu da mayalwaciyar rahamarsa, ya kuma kiyaye mana ƙasarmu, da sojojinmu, da 'yan sandanmu, da ɗaukacin 'yan ƙasa daga dukan abin ƙi.**

- 33 –

## MATSAYIN SHAHIDAI DA SADAUKAR DA KAI

## WAJEN KARE ƘASA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Kada ku soma ku kira wanda aka kashe shi a wajen ɗaukaka kalmar Allah da sunan "matacce", a'a, rayayyu ne su, ku ne dai ba ku sani ba))** **[al-Baƙra: 154]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya, cikakken mabuwayi mai hikima.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Lallai a 'yan kwanakin nan ne al'ummar ƙasar Misra suke gabatar da bikin tunawa da ɗaya daga cikin ranaku masu girma da daraja a tarihinsu, ranaku ne daga cikin ranakun Allah Maɗaukakin Sarki, da Allah Ubangijinmu ya yi wa Misra baiwa da nasarar ƙwato ƙasarta, da karamarta a lokaci ɗaya, lallai waɗannan ranaku su ne ranakun tunawa da nasarorin ranar Shida ga watan Oktoba, a shekarar 1973, wanda ta yi daidai da ranar goma ga watan Ramadhan, 1393 bayan Hijira, wannan gagarumar nasara da sojojin Misra suka nuna bajinta a fagen gwarzantaka, da sadaukar da kai, inda nagartattun ɗabi'un

aƙidar imani da Allah Maɗaukakin Sarki, da gasgata kai gami da yarda da akai, da ƙarfin niyya, da himma wajen isa zuwa ga manufa na sojojin Misra suka fito fili duniya ta shaida.

A duk sanda manufofi suka zamo masu girma, da daraja, da nagarta; to kuwa haka ake samun sadaukar da kai shi ma ya zamo babba, kuma mai daraja, babu abin da ya kai sadaukar da kai da rayuwa, saboda neman shahada wajen ɗaukaka kalmar Allah Maɗaukakin Sarki daraja, inda mutum zai bayar da rayuwarsa saboda bai wa addininsa, da ƙasarsa, da mutuncinsa kariya, yana mai kare iyakokin ƙasar; saboda ya sami ƙololuwan muƙami, wanda shi ne muƙamin Shahada.

Lallai muƙamin shahada kyauta ce daga Ubangiji, baiwa ce daga mahalicci mai girma da ɗaukaka, da Allah yake bayarwa ga wanda yake so a cikin bayinsa, bayan Annabawa da siddiƙai, Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Duk wanda ya yi wa Allah da Manzon Allah biyayya, to lallai waɗannan su ne suke tare da waɗanda Allah ya yi masu ni'imomi cikin Annabawa da Siddiƙai da Shahidai da mutanen kirki, lallai zama da waɗannan kam abu ne da ya yi kyau matuƙa..))** **[an-Nisa'i: 69]**, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya zaɓi mutum; saboda ya zama shahidi, babban dalili ne da yake nuna cewa Allah ya yarda da shi, wane daraja ce kuwa ta kai wannan darajar?! Lallai Alƙur'ani mai girma ya yi nuni zuwa ga haka a inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Ya kuma zaɓi shahidai daga cikinku..))** **[Ali Imran: 140]**, shi shahidi ya sadaukar da rayuwar ne saboda neman yardar Allah Ubangijinsa, da bai wa ƙasarsa kariya, ya kuma fifita lahira akan duniya, ya kuma yi nasara da galaba akan sha'awarsa, da abubuwan da yake kwaɗayi, ya faɗa filin daga saboda ya fanso addini da ƙasa.

Muna taya shahidi murna da jin dadin samun wannan matsayi mai albarka, lallai kasuwanci nasa ya yi riba, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai tabbas Allah Maɗaukakin Sarki ya sayi rayukan muminai da dukiyoyinsu akan zai ba su aljanna, suna yaƙar waɗanda suka yaƙe akan hanyarsu ta yi wa Allah biyayya, su kasha, a kashe su, wannan kam alƙawari ne na gaskiya da aka yi masu a cikin litattafan Attaura da Ingjila da Alƙur'ani..)) [at- Tauba: 111]**, madalla da wannan ciniki mai girma da karamci da sakamakonsu shi ne aljanna, a Hadisi ya zo cewa : Ummu Rabi'i 'yar al-Barra'u –wato Ummu Harisat Bn Suraƙa- ta zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ta ce: Ya Annabin Allah, ba ka ba ni labarin halin da Harisat yake ciki ba?, -da ma an kashe shi ne a ranar yaƙin Badar, inda aka harbe shi da kibiyar da ba a san wanda ya harbo ba-, in yana aljanna, in yi haƙuri, in kuma ba haka na yi kuka iya iyawa ta, sai ya ce: **(Ya Ummu Harisat, ai aljannar ma ba ɗaya ba ce, kuma ɗanki ya samu Firdausa maɗaukakiya).**

Lallai shahidi na gaskiya shi ne wanda ya tsarkake niyyarsa, ya kuma sadaukar da rayuwarsa saboda Allah, ya miƙa ransa wajen ɗaukaka kalmar Allah, da bai wa ƙasarsa kariya, da ɗaga tuta da darajar ƙasarsa, an ruwaito Hadisi daga Abu Musa al-Ash'ariy (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: Wani mutum ya zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce: Mutum ne yake yaƙi domin neman ganima, da mutumin da yaƙi saboda a faɗi, da mutumin da yake yaƙi domin ya bayyana matsayinsa, wanne ne a cikinsu yake yi fisabililLah? Sai ya ce: **(Wanda ya yi yaƙi saboda kalmar Allah ta ɗaukaka shi ne yake yi fisabililLah)**.

Haka ma shahidi na gaskiya shi ne mutumin da ba ya karɓar kowane irin ƙasƙanci, ba ya yarda da wulaƙanci da tozarta, yana kuma ɗaukan matakin mayar da martani ga duk wanda ya yi yunƙuƙrin yi masa ta'adi a dukiyarsa, ko kayansa, an ruwaito Hadisi daga Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) sai ya ce: Ya Manzon Allah, ya kake gani idan wani mutum ya zo yana son ya ƙwace mini dukiya ta? Sai ya ce: **(Kada ka ba shi dukiyarka)**, sai ya ce: idan ya yaƙe ni fa?, sai ya ce: **(Ka yaƙe shi)**, sai ya ce: to idan ya kashe ni fa?, sai ya ce: **(Ka zama shahidi)**, sai ya ce: idan na kashe shi fa?, sai ya ce: **(Ya shiga wuta)**.

Haka ma shahidi na gaskiya shi ne wanda yake bai wa ƙasarsa, da mutuncinsa, da iyakokin ƙasa kariya, bai wa ƙasa, da mutunci kariya a wurin Musulmi na gaskiya, daidai yake da bai wa rai, da addini, da dukiya kariya; saboda shi kansa addini yana buƙatar ƙasar da za ta rungume shi, ta kuma ba shi kariya, an ruwaito Hadisi daga Sa'id Bn Zaid (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda aka kashe shi wajen kare dukiyarsa shahidi ne, wanda aka kashe shi wajen kare iyalansa, ko wajen kare ransa, ko wajen kare addininsa, to lallai shahidi ne shi).**

Ta nan ne ma'anar shahada ta haɗe da sadaukar da kai wajen ɗaukaka kalmar Allah, a dukan yanayin da ake buƙatar kare addini, da ɗaukaka kalmar Allah Maɗaukakin Sarki, da kare ƙasa, domin kiyaye ta hanyar mayar wa da duk wani mai ta'adi da aniyarsa, saboda son ƙasa yana cikin imani.. kai madalla da shahidan da suka keta shingen maƙiya, inda hakan ya dawwamar da sunansu a cikin tarihi, mutanen da suka ƙosar

da Misra da tsarkakan jinanansu, ruhinsu kuma suka tafi wurin Allah Maɗaukakin Sarki, suka rabauta da yardarsa, da ni'imomin da Allah mai girma da ɗaukaka ya yi masu alƙawari, muna roƙon Allah ya sanya mu cikin shahidai.

**Lallai shahada a hanyar yi wa Allah Maɗaukakin Sarki biyayya tana da amfani masu yawa da girma, a cikin amfaninta akwai: labarin da Allah Maɗaukakin Sarki ya bayar a cikin littafinsa na cewa lallai shahidai rayayyu ne a wurin Ubangijinsu da yake azurta su a koda yaushe,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ku taɓa zaton cewa waɗanda aka kashe akan hanyar Allah matattu ne, a'a, a raye suke, rayuwar da Allah ya bar wa kan sa sani, suna nan wurin Ubangijinsu ana azurta su da arziki mai faranta rai da Allah ne kawai ya sani. Farin-ciki da murna sun lulluɓe fuskokinsu sakamakon abin da Allah ya ba su na wasu abubuwa da aka keɓance su da su saboda falalarsa, suna kuma farin-ciki da murna da 'yan uwan sun da suka bari a raye a duniya suna tsaye akan hanyar imani da jahadi, da cewa lallai babu tsoron wani abin ƙi da zai same su, ba kuma sa baƙin-ciki saboda wani abu da suke so da ya kuɓuce masu. Fuskokin shahidai suna walƙiya saboda baiwar da Allah ya yi masu na ni'imar shahada, da ni'imar aljanna, da babban karramawar da aka yi masu, lallai shi Allah ba ya tozartar da ladan muminai)) [Ali Imran: 169 -171]**, haka ne, lallai rayayyu ne su ba matattu ba, lallai ana azurta su, kuma wannan arziki nasu yana zuwa ne daga Allah Maɗaukakin Sarki, lallai suna farin- ciki da murna da abubuwan da Allah ya ba su; suna can a aljannar dawwama, inda a cikinta akwai abubuwan da idanuwa ba su taɓa gani ba, kunnuwa ma ba su taɓa ji ba, hasali ma ba su taɓa ɗarsuwa a

cikin zuciyar wani mutum ba, suna kuma yi wa 'yan uwansu da za su zo bayansu albishir da: babu baƙin ciki, babu damuwa, duka cikinta albishir ne da falala da kuma ni'ima.

An karɓo Hadisi daga Sayyiduna Jabir Bn Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya haɗu da ni, sai ya ce: **(Ya Jabir na ga duk jikinka ya yi sanyi ne?)** sai na ce: Ya Manzon Allah, mahaifi na ne ya yi shahada, ya kuma bar ƙananan yara, ga bashi a kansa, sai ya ce: **(Shin ba na yi maka albishir da abin da mahaifinka ya taras ba?)**, sai na ce: Na'am ya Manzon Allah, a yi mini albishir, sai ya ce: **(Allah bai taɓa yin magana da kowa ba, sai ta bayan hijabi, amma mahaifinka raya shi Allah ya yi, ya kuma yi magana da shi ba tare da hijabi ba),** ma'ana shi da shi ba tare da shamaki, ko ta hanyar ɗan saƙo ba, sai ya ce masa: **(Ya bawana, yi burin da kake so, ni kuwa zan ba ka),** sai ya ce: ya Ubangiji ina roƙon ka sake raya ni, a kashe ni saboda kai a karo na biyu, sai Ubangiji mai girma da ɗaukaka ya ce: **(Ai lallai na riga na hukunta cewa in an taho wurinmu babu komawa)**, sai ya ce: sai aka saukar da wannan ayar: **((Kada ka soma ka zaci cewa waɗanda aka kashe su wajen ɗaukaka kalmar Allah matattu ne..)) [Ali Imran: 169].**

**Haka ma a cikin amfanin shahada akwai:** manyan muƙamai har guda shida da shahidai suke da su a wurin Ubangijinsu, kaman yanda ya zo a Hadisin da al-Miƙdamu Bn Ma'ad Yakarib (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ruwaito, ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Shahidi yana da tagomashi shida a wurin Allah: A daidai lokacin da ɗigon jininsa ya ɗiga ana gafarta masa zunubansa, za kuma a nuna masa mazauninsa a aljanna, za kuma a tseratar da shi ga**

**barin azabar wuta, za a amintar da shi daga barin babban razani na ranar alƙiyama, za kuma a yi masa ado da tufafin imani, za kuma a aura masa matan aljanna "hurul in", za kuma a ba shi dama ya ceci mutane saba'in daga cikin danginsa).**

**Haka ma a cikin nau'o'in karamci da Allah yake yi wa shahidi akwai**: kasancewar mala'iku ne suke yi masa inuwa da fuka- fukinsu; an ruwaito Hadisi daga Jabir Bn Abdullah (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: An kawo mahaifi na wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) –ma'ana bayan ya yi shahada a ranar yaƙin Uhdu- an yi gundiya – gundiya da shi, aka ajiye shi a gabansa, na je in buɗe fuskarsa, sai jama'a ta suka hana ni, sai Annabi ya ji muryar wata mai kururuwa, sai ya ce: **(Saboda mene kike kuka?, kada ki yi kuka, har yanzu mala'iku suna yi masa inuwa da fuka- fukansu)**.

**Haka ma a ciki akwai:** kasancewa shahidin da ya rasa ransa wajen ɗaukaka kalmar Allah zai shiga aljanna ne tare da tawagar farko da za su shige ta, ba tare da hisabi, ko azaba ba, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abdullahi Bn Amru Bn al-As (Allah ya ƙara yarda da su), ya ce: Na ji Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah Maɗaukakin Sarki zai kira aljanna a ranar alƙiyama, sai ta zo da kayan ado, gami da na ƙawa, sai ya ce: Ina bayina da suka yi yaƙi domin ɗaukaka kalma ta, aka kuma kashe su akan hanyarsu ta ɗaukaka kalma ta, aka kuma cutar da su akan hanyarsu ta ɗaukaka kalma ta, suka yi jihadi domin ɗaukaka kalma ta, ku shiga aljanna, sai kuwa su shiga ba tare da hisabi, ko azaba ba, sai mala'iku su zo su ce: Ya Ubangijinmu, mu muna yi maka tasbihi dare da rana, muna kuma tsarkake**

**ka.. su wane ne waɗannan da ka fifita su akanmu? Sai Ubangiji mai girma da ɗaukaka ya ce: waɗannan su ne suka yi yaƙi saboda ni, aka kuma cutar da su saboda ni. Sai mala'iku su shiga wurinsu ta dukan ƙofofi, suna cewa ((Amincin Allah ta tabbata a gare ku sakamakon haƙurin da kuka yi, kai madallah da sakamakon gidan lahira))**.

**Haka ma a cikin amfanin shahada akwai:** kasancewar shahidai a matsayi mafi girma, da kyau a cikin aljanna, an ruwaito Hadisi daga Samurat Bn Jundabi (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(A daren jiya na ga wasu mutane biyu sun zo wurina, suka hau da ni kan wata bishiya, suka shigar da ni wani gida da yafi kowanne kyau da falala, ban taɓa ganin wanda ya fi shi kyau ba, sai suka ce mini: wannan kuma gidan shahidai ne)**.

Saboda waɗannan abubuwa ne ya zama shahidi ne kawai yake burin ya sake dawowa duniya, a sake kashe shi saboda Allah, kaman yanda ya zo a Hadisin da Sayyiduna Anas (Allah ya ƙara yarda da shi) ya kawo, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Babu mutumin da zai shiga aljanna ya kuma zamana yana son ya dawo duniya, ya zamo yana da duk abin da yake a doron ƙasa sai shahidi, shi ne kawai yake burin ya dawo duniya, a sake kashe shi har sau goma; sakamakon abin da ya gani na karamci),** a wata ruwayar kuma: **(Saboda abin da ya gani na falalar shahada)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

---------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da salami shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai isa zuwa ga manyan manufofi, da samun manyan matsayi a cikin wannan rayuwar suna buƙatar manyan sadaukar da kai saboda haka, lallai babu shakka girman manufofi da darajarsu, suna nuni zuwa ga girman sadaukar da kai, da girman darajar haka, wannan ne kuma halin duk wanda ya sadaukar da rayuwarsa saboda addininsa, da kuma ƙasarsa.

Lallai abin da ya wajaba akanmu game da ƙasarmu mai daraja, da addininmu nagartacce shi ne: mu haɗa ƙarfi da ƙarfe baki ɗayanmu, wajen kiyaye tsaron ƙasarmu, da kuma ba ta kariya daga dukan wani azzalumi ɗan ta'adda, ko wata barazana da take nuna mata yatsa, dole ne mu buɗe idanuwanmu da kyau; domin kiyaye tsaron ƙasashenmu, mu kuma haɗa kawunanmu baki ɗaya; domin ƙalubalantar duk wani wanda zuciyarsa take riya masa yi wa ƙasashenmu ƙumaji, kowa daga cikinmu ya yi haka gwargwadon ikonsa, a kuma da'irar nauyi, gami da alhakin da yake akansa.

Madalla da sojojinmu gwaraza da suka yi riƙo da igiyar Allah, suka kuma gasgata alƙawarin da Allah ya yi masu, suka kuma tsaya tsayin - daka cikin imani da yaƙini, suka ƙetare da ƙasarmu zuwa ga tudun- na- tsira na haɓakar gina ƙasa, da tattalin arziki, gaisuwa da jinjina zuwa ga sojojinmu jajirtattu a wannan rana ta nasara mai girma.

Lallai muna da rawar da za mu taka, shi ne mu cigaba da aiki tuƙuru har mu isa zuwa ga gaɓar samar da ayyukan raya ƙasa, da na jin daɗin al'umma, mu yi aiki wajen samar da abubuwan da muke buƙata da kawunanmu, domin mu tabbatar wa da ɗaukacin duniya cewa: tabbas 'ya'ya da jikokin waɗanda suka ƙetare katangar Barlin, suka kuma ƙetare wutar da aka kunna a irin wannan ranar, a shirye suke su yi duk abin da ya kamata wajen samar da tsaro, da aminci, da manyan ayyukan raya ƙasa, da jin daɗin al'umma, da izinin Allah Maɗaukakin Sarki, a shirye suke wajen tsaya a sahu ɗaya a bayan shugabanninmu na siyasa masu hikima, da gwarazan sojojinmu, da 'yan sandanmu masu kishin ƙasa, da sauran ma'aikatun gwamnatinmu.

**Ya Allah Ubangiji ka kiyaye mana ƙasarmu, ka kuma dawwamar mana da ni'imar tsaro da aminci, ka kuma yi mana arizki mai tarin yawa da amfani.**

- 34 –

## ABOKANTAKA DA TASIRINSA WAJEN GINA AL'UMMA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Abokai a wannan ranar maƙiya juna suke komawa in banda masu tsoron Allah)) [az-Zukhraf: 67].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah mai girma ya halicci ɗan Adam da son rayuwar zamantakewa, yana rayuwa a cikin al'ummar da yake, ya tasirantu da ita, ya ku damu da damuwarta, kaman yanda yake farin ciki da farin cikinta, ta hanyar wasu sifofi da Allah ya hore masa, waɗanda suka saɓa da na waninsa, lallai zaman tare, da kuma gwaje – gwaje, suna da bayyanannun tasiri a tunani, da tsarin rayuwar ɗan Adam, kuma su ne dalilan da suke iyakance makomarsa, da ma jin daɗinsa na duniya da na lahira..

Lallai babu shakka muna matuƙar buƙatar tsayayyen mutum da ya sifantu da cikakkun sifofin mutuntaka, ya kuma kai ƙololuwa a kishin ƙasa, muddin dai muna son mu samar da

al'ummar da gini za ta yi ba rusawa ba, al'ummar da za ta raya doron ƙasa, ba wadda za ta lalata komai ba, al'ummar da za ta gabatar da maslahar ƙasa ta bai ɗaya akan kowace irin maslaha..

Lallai Shari'ar Musulunci mai daraja ta bayar da umurnin kyautatawa wajen samar da al'umma, domin ta zamo wayayyiya, mai iya sani ƙalu-bale, da hatsarin da take fuskanta, take kuma kyautata iya tunkarar wahalhalun rayuwa, take kuma taka- tsantsan da fitintunu, da shubuhohi, Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ku tsoraci fitanar da ba za ta tsaya akan waɗanda suka jawo ta daga cikinku ba kawai..)) [al-Anfal: 25].**

Haka ma Shari'ar Musulunci ta umurci ɗan Adam da ya zamo mutum mai ƙarfi, bai mai inda- inda ba, mutumin da zai fahimci abubuwa masu amfani, ya kuma bi hanyar gaskiya, ba ya zamo ɗan - abi - yarima a - sha kiɗa ba, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Kada ku soma ka zamo 'yan amshin shata; kuna cewa: in mutane sun kyautata mu ma mu kyautata, in kuma sun yi zalunci, mu ma mu yi zalunci, ku dai kawai ku samar wa da kawunanku matsaya, in mutane sun kyautata, ku ma ku kyautata, in kuma sun munana, ku kada ku yi zalunci)**.

Babu shakka akan cewa a cikin muhimman abubuwan da suke da tasiri matuƙa wajen samar da ɗan Adam akwai: Abokantaka, lallai mutum yakan tasirantu da abokin zamansa, ya zamo ya sifantu da sifofinsa wajen tunani, da imani, da tsarin rayuwa, da ayyukan da yake yi, lallai Shari'a, da hankali, da abubuwan da suke faruwa yau da kullum sun tabbatar da haka...

Wannan kenan, lallai abokanta ta gari tana da tasiri matuƙa wajen samar da nagartacciyar al'umma da za ta amfani addininta, da ƙasarta, da al'ummarta, akan irin wannan tsari ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya raini Sahabbansa masu karamci, waɗanda Sayyiduna Abubakar as- Siddiƙ (Allah ya ƙara yarda da shi) yake daga cikinsu, a ma sahun farko, lallai ya buga babban misali na burgewa wajen kyautata abokantaka da ba ta cikakkun haƙƙoƙinta, a lokacin da mutanen Makka suka ce masa: Abokinka fa yana riya cewa an yi tafiya da shi a daren jiya zuwa Baitul Maƙdisi, ya tafi ya dawo!, cikin yaƙini da cikakken aminci da Abokinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya amsa masu da cewa: **In dai ya faɗi haka, to lallai gaskiya ne; ni fa na gasgata shi a cikin abin da ya fi haka sarƙaƙiya, na gasgata shi akan wahayin da yake zuwa masa daga Allah.**

Haka sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) suke da junansu, su ne babban abin koyi wajen nagartacciyar abokantaka da aka gina ta akan 'yan uwantaka, da fifita wani akan kai, da riƙo da haɗin kai, da ayyuka masu amfani, da soyayya da ƙaunar juna, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna An- Nu'uman Bn Bashir (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Misalin muminai wajen soyayya, da tausayi, da jinƙan junansu kwatankwacin gangan jiki ne guda ɗaya; wanda idan wata gaɓa ta kamu da cuta, sauran jikin zai kamu da rashin barci da raɗaɗi)**.

Haka ma abokantaka ta gari tana da falala, da albarka a duniya da lahira, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana da Mala'iku masu daraja da suke kara-kaina, suna neman majalisan da**

**ake ambaton Allah, idan sun sami majalisin da ake ambaton Allah, sai su zauna tare da su, su kuma yi masu inuwa da fuka-fukansu, har su cike tsakaninsu da saman duniya, idan kuma sun tashi, sai su hau sama, ya ce: sai Allah mabuwayin Sarki Ya tambaye su, alhalin shi ne ya fi sanin halin da suke ciki: daga ina kuke? Sai su ce: mun zo ne daga wurin bayinka da suke a doron ƙasa, suna yi maka "Tasbihi", suna kuma yi maka "Kabbara", suna "Hailala", suna gode maka, suna kuma roƙonka, ya ce: Mene suke roƙo na? Sai su ce: suna roƙon ka ba su aljannar ka ce, sai ya ce: sun taɓa ganin aljanna ta ce? Sai su ce: a'a, ya Ubangijinmu, sai ya ce: da kuma a ce sun ga aljanna ta fa? Sai su ce: suna kuma neman tsarinka, sai ya ce: akan Mene suke neman tsari na? Sai su ce: suna neman tsari ne daga wutarka ya Ubangiji, sai ya ce: sun taɓa ganin wuta ta ce? Sai su ce: a'a, sai ya ce: da a ce kuma sun ga wuta ta fa? Sai su ce: suna kuma neman gafara daga gare ka, ya ce : sai ya ce: Lallai na gafarta masu, na kuma ba su dukan abubuwan da suka roƙa, na kuma tseratar da su daga barin abin da suka nemi a tseratar da su akansa, ya ce: sai su ce: akwai wane a cikin su mai yawan kuskure ne, ya zo wucewa ne kawai sai ya zauna tare da su, ya ce : sai ya ce : saboda shi na gafarta masu, ai su mutane ne da da duk wanda ya zauna da su ba zai taɓe ba)**.

A cikin ribar da abokantaka ta gari take gadarwa akwai: **zamowanta dalili na soyayyar Allah Maɗaukakin Sarki,** da rabauta da aljanna, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi), daga Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), cewa: **(Wani mutum ya ziyarci ɗan uwansa a wani ƙauye, sai Allah ya tsayar da Mala'ika**

**akan hanyarsa, lokacin da ya zo inda yake, sai ya ce: ina za ka tafi? Sai ya ce: ina son in tafi wurin wani ɗan uwa na ne a wannan ƙauye, sai ya ce: shin kana da wata buƙata ce a wurinsa da kake rainonta? Sai ya ce: a'a, kawai da ina sonsa ne saboda Allah Maɗaukakin Sarki, sai ya ce: Ni ɗan saƙon Allah ne zuwa gare ka, Lallai Allah ya so ka kaman yanda ka so shi saboda shi)**.

**Haka ma abokantaka dalili ne na a tashi mutum tare da waɗanda yake abokantaka a ranar alƙiyama**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Anas Bn Malik (Allah ya ƙara yarda da shi), cewa: wani mutum ya tambayi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) game da tashin alƙiyama, sai ya ce; Yaushe ne tashin alƙiyama? Sai ya ce: **(Mene ka tanadar mata?)**, sai ya ce: babu komai, kawai dai ni na san ina son Allah da Manzonsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce: **(Lallai kana tare da abin da kake so)**, Sayyiduna Anas ya ce: ba mu taɓa farin ciki da wani abu kaman yanda muka yi farin ciki da maganar da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yake cewa: **(Lallai kana tare da abin da kake so)** ba, Sayyiduna Anas ya ce: Ni dai kam ina son Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), da Abubakar, da Umar, ina kuma fatan in kasance tare da su, sakamakon son da nake yi masu, koda kuwa ban yi aiki irin nasu ba.

Alhairin Allah ya kai zuwa ga Imam as- Shafi'iy da yake cewa:

"Ina son salihan bayi, duk kuwa da ba ni cikinsu, ta yiwu a dalilin wannan soyayyar na samu a cece ni albarkacinsu.. Ina ƙin mutumin da tadarsa ita ce bayyana saɓon Allah, koda kuwa abokin kasuwanci na ne shi".

Haka ma a cikin ribar abokantakar mutane na ƙwarai akwai: **tunawa da Allah Maɗaukakin Sarki,** hakan kuma yana gadar da alhairan duniya da na lahira, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: An ce: ya Manzon Allah, waɗanne abokan zama ne suka fi alhairi? Sai ya ce: **(Wanda ganinsa yake tuna maku da Allah, maganganunsa kuma suke ƙarar ku da ilimi, ayyukansa kuma suke tuna maku da lahira)**.

Shi aboki na gaskiya madubi ne ga ɗan uwansa, yana zaburar da shi wajen aikata alhairi, yana kuma hana shi aikata sharri, yana kuma son masa irin abin da yake so wa kansa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ina rantsuwa da zamani; saboda yawan abubuwan da ya ƙunsa na ban mamaki da lura. Lallai kowane mutum yana cikin wani nau'i na asara; saboda rinjayar da son zuciya da sha'awa da suka taru suka yi masa yawa. Sai dai banda waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma aikata ayyuka na gari, suka kuma yi ɗã'a da biyayya, suka kuma yi wa juna wasici da riƙo da gaskiya wajen i'itiƙadi, da furuci, da aiki, suka kuma yi wa juna wasici da haƙuri akan abubuwa masu wahala da suke bijiro wa duk wani wanda ya yi riƙo da addini, waɗannan kam, su ne masu tsira daga wannan asara, masu kuma babban rabo a duniya da lahira))** **[al- Asri: 1 -3],** an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Anas (Allah ya ƙara yarda da shi), daga Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ka taimaki ɗan uwanka a lokacin da yake zalunci, da lokacin da ake zaluntarsa)**, sai muka ce: Ya Manzon Allah, mun san yanda za mu taimake shi idan ana zaluntarsa, amma yaya za mu iya taimaka masa idan yana zalunci? Sai ya ce: **(Ku hana shi yin zalunci, wannan shi ne ka**

**taimake shi)**, wannan shi ne abin da aboki na gari yake yi wa abokinsa idan ya gan shi ya kauce wa gaskiya, ya kama gwadaben shaiɗan da son zuciya, sai ya yi masa nasiha, ya kuma bayyana masa gaskiya, ya kuma yi masa wasici da abin da ya kamata ya aikata, ya kuma gargaɗe shi akan mummunan sakamakon yin nesa da Allah mai girma da buwaya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Sai abokinsa mumini ya ce masa: yanzu zuciyarka ce za ta riya maka ka kafirce wa Ubangijinka da ya halicci asalin Annabi Adam daga turɓaya, sannan ya zama maniyya, sannan ya mayar da kai cikakken mutum? Idan ma har ka yi taƙama da dukiyarka da danginka, to ya kamata ka tuna da Ubangijinka, da ma asalinka wanda shi ne yanɓu. Ni dai kam abin da zan ce shi ne: lallai wanda ya halicce ni, ya kuma halicci dukan halittu shi ne Allah Ubangiji na, ni bawansa ne shi kaɗai, ba zan taɓa haɗa Ubangiji na da wani a wajen bauta ba. Da a ce lokacin da ka shiga gonarka, kana kallon abubuwan da suke ciki, cewa ka yi: wannan shi ne abin da Allah ya so, babu ƙarfi na wajen samar da shi sai da taimakon Allah, hakan sai ya zamo godiyar da take samar da lamunin dawwamar ni'imomin da aka yi maka. Sannan ya ce: ko dai don ka ganni ban kai ka yawan dukiya da 'ya'ya masu taimako ba ne? Ta yiwu Ubangiji na ya ba ni mafi alhairin gonarka a duniya da lahira, ya kuma turo wa gonarka wata ƙaddara da ya hukunta daga sama, ta zamo faƙon da babu wani tsiro da zai iya fitowa daga cikinta, kuma ƙafa ma ba ta iya taka ta.. Ko kuma ya sanya ruwan cikinta ya yi ƙasa sosai, ta yanda ba za a taɓa iya isa zuwa gare shi ba, ba za ka iya fitar da shi domin yin ban ruwa ba. Lallai Allah ya gaggauta yi wa kafirin hukunci, sai kuwa**

**abubuwan da suke halaka amfanin gona suka zagaye gonarsa, suka kuma halaka ta, suka yi ɗaiɗai da tushenta, sai kuwa ya koma yana jujjuya hanayensa saboda nadama, da cizon yatsa, akan abin da ya kashe wajen raya gonar tasa, a ƙarshe kuma wannan halaka ta faɗa mata, ya kuma yi nadamar ina ma a ce bai haɗa Ubangijinsa da wani a wajen bauta ba))** **[al- Kahfi: 37 -42].**

Alhairin Allah ya isa zuwa ga wanda yake cewa:

"Lallai abokinka na gaskiya shi ne wanda yake tare da kai, wanda yake cutar da kansa domin ya amfane ka, wanda idan bala'in zamani ya yi waɗa- waɗa da kai, shi zai watsar da al'amarinsa saboda kawai ya tattara ka".

Kaman yanda abokantaka ta gari take da tasiri mai kyau mai kuma amfani a duniya da lahira, haka ma abokantaka ta banza take da mummunan tasiri wajen gina al'umma mara ma'ana, rusasshiya, karkatacciya, wannan kuwa yana da mummunar cutarwa a rayuwar duniya, da kuma mummunan ƙarshe a gobe alƙiyama, abokanta ta banza tana rusa duk wani kyakkyawan ɗabi'a, ta ma share duk wata tada mai kyau, ta kuma lalata yara da matasa, ta kuma daƙile duk wani aiki na cigaba, ta kuma kai zuwa ga yaɗa jita- jita, da ɓata da fitintunu, shi abokin banza aikinsa shi ne ya ɓatar da abokinsa ta hanyar cusa masa gurɓatattun aƙidu, da karkatattun tunani, lallai Alƙur'ani mai girma ya Ambato mana wani bayyanannen yanayi na abokin banza, Allah mai girma yana cewa: **((Sai wasu daga cikin waɗannan salihan bayi suka fara tambayar junansu akan yanda suka kasance a duniya. A lokacin ne wani daga cikinsu ya ce: ina da wani aboki cikin mushrikai da suke haɗa Allah da wani a wajen bauta da yake yin gardama da ni akan**

**al'amarin addini, da abubuwan da Alƙur'ani mai girma ya zo da su. Yana cewa: shin kai kana cikin waɗanda suke gasgata tashin bayan mutuwa, da hisabi, da kuma sakamako? Shin bayan mun ƙare, mun zamo turɓaya, da ƙasusuwa za a sake raya mu; domin a yi mana hisabi, a kuma saka mana akan abubuwan da muka gabatar na ayyuka? Sai muminin ya faɗa wa abookan zamansa: ya ku 'yan aljanna, shin ba ma leƙa 'yan wuta don in ga abokin zama na a duniya ba? Sai kuwa ya wulƙa idanuwansa zuwa ga wuta, ya kuma ga tsohon abokinsa a tsakiya ana yi masa azaba da ita. A lokacin da ya ganshi sai ya ce: Na rantse da Allah da ka kusa ka halakar da ni a duniya da na bi ka cikin kafircinka da saɓon Allahnka, da ba domin ni'imar da Ubangiji na ya yi mini na shiriya, da datarwa da ya yi mina na yin imani da Allah da ranar lahira ba, da kuwa na zamo irinka cikin waɗanda za a bijirar da su zuwa ga azaba. Yanzu shin mu za mu dawwama cikin ni'ima a aljanna, ba za mu taɓa mutuwa ba, in banda mutuwarmu ta farko a duniya, ba kuma za a yi mana azaba ba bayan mun shiga aljanna? Lallai wannan abu da Allah ya ba mu na karamci a aljanna wallahi shi ne babban rabo, kuma mafi girma tsira akan abin da ake yi mana gargaɗi da shi na azabar Allah tun muna duniya. Saboda irin wannan ni'ima da muminai suka rabauta da ita na karamci a ranar alƙiyama ne ya kamata masu aiki a duniya su zage dantse, su riski irin abin da suka riska..))** **[as- Safat: 50 -61]**, haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ranar alƙiyama ne wanda ya zalunci kansa –da kafirci, gami da saɓa wa Manzanni- zai ciji yatsarsa saboda nadama, da da- na- sani, yana faɗin: kaico na, ina ma da na bi Manzanni, na bi hanyar aljanna, na kauce wa hanyar wuta?**

**Yana faɗin haka cikin nadama akan bin waɗanda suka yi sanadiyyar ɓacewarsa: ina ma a ce ban gasgata wane da na miƙa masa ragamar kai na ba? Lallai ga shi wannan aboki ya nesantar da ni daga ambaton Allah, da karatun Alƙur'ani bayan Allah ya sauƙaƙe mini haka. Da irin haka ne shaiɗan yake bayar da ɗan Adam, ya jefa shi cikin abubuwan da suke sanadiyyar halakar da shi))** **[al- Furƙan: 27 – 29]**, lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sifanta mana abokin banza da mai hura zuga-zigi na wuta a inda yake cewa: **(Misalan aboki na gari, da abokin banza, kamar mai sayar da turaren almiski ne, da mai hura zuga- zigi, shi mai sayar da almiski ko dai ya ba ka kyauta, ko kuma ka saya a wurinsa, ko kuma ka sami ƙamshi mai daɗi, shi kuma mai hura zuga-zigi, ko dai ya ƙona maka tufafi, ko kuma ka kwashi ƙauri mara daɗi)**.

Haka ma abokantaka ta banza tamkar wani gatari ne na rusa kai da zaluntar wasu, mafi hatsarin ciki shi ne wanda zai ja ka zuwa ga ɓatattun ƙungiyoyin da suke kira zuwa ga rusa ƙasa, gami da aikata ɓarna a bayan ƙasa, da masu janka zuwa ga shaye- shayen ƙwayoyi, ko sabawa da su, ta hanyar maganganusu, ko ayyukansu, domin dukansu su biyun za su sallama ka ne zuwa ga hanyar halaka, da wutar jahannama, da fushin Allah Maɗaukakin Sarki a duniya da lahira.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

---------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da

abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, da kuma waɗanda suka bi turba irin tasu har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Dole ne mu nesanci abokan banza, kada mu kuskura mu cakuɗu da su, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar maku da Alƙur'ani mai girma akan cewa da zaran kun ji ana kafirce wa ayoyin Allah, ana kuma yi masu izgilanci, to kada ku zauna tare da masu yin haka, sai idan sun shiga wata maganar wadda ba kafirci da izgilanci ba, in kuwa kuka zauna tare su a wannan hali, to kuwa ba ku da bambanci da su, lallai Allah zai harhaɗa munafukai da kafirai gaba ɗayansu a cikin wutar Jahannama))** **[an- Nisa'i: 140]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Idan ka ga waɗanda suke kutsawa cikin ayoyinmu da wargi gami da wasanni ka kawar da kanka ga barinsu, har sai idan sun shiga wata maganar wadda ba wargi da wasa da ayoyinmu ba, idan ma shaiɗan ya mantar da kai wannan umurni na ƙaurace wa masu wannan hali, to da zaran ka tuna kada ka zauna tare da mutanen da suke azzaluman kawunansu ne))** **[al- An'am: 68]**. Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ɗan Adam yana kan addinin abokinsa ne, kowa daga cikinku ya duba wanda zai yi aboki da shi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Kada ka yi aboki sai da mumini, kada kuma kowa ya ci abincinka sai mai tsaron Allah)**, an ruwaito daga Sayyiduna Abdullahi Bn Mas'ud (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: "Ku kula da mutane ta hanyar abokansu, lallai mutum ba ya yin

abokantaka sai da wanda yake burge shi", alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa :

"Idan ka kasance a cikin mutane, to ka abokanci zaɓaɓɓun cikinsu, kada ka kuskura ka abokanci ƙasƙantattun cikinsu, balle ka ƙasƙanta tare da ƙasƙantattu. Kada ka tambayi kowa akan wani mutum, kai dai kawai ka duba abokinsa; domin kowane aboki yana koyi ne da abokinsa".

A nan muna son mu ƙara tabbatar da cewa: gina ɗan Adam ta hanyar nagartacciyar abokantaka, alhaki ne da yake a wuyan gaba ɗayan al'umma; dole ne al'umma ta haɗa ƙarfi da ƙarfe wajen samar da haka, kuma dole ne kowa ya riski girman wannan alhaki, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Dukanku masu kulawa ne, kuma kowa za a tambaye shi akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi: Shugaba mai kulawa ne, za kuma a tambaye shi akan waɗanda yake shugabanta, namiji ma mai kulawa ne a cikin iyalansa, za kuma a tambaye shi akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi, mace ma mai kulawa ce a gidan mijinta, za kuma a tambaye ta akan nauyin da aka ɗaura mata na kulawa, hadimi ma mai kulawa ne da dukiyar uban gidansa, za kuma a tambaye shi akan nauyin da aka ɗaura masa alhakin kulawa da shi, dukan ku masu kulawa ne, za kuma a tambayi kowa a akan abin da aka ɗaura masa nauyin kulawa da shi)**, dole ne tun farko a kula da tarbiyya, da bai wa ƙananan yara masu tasowa kulawa ta musamman a gida, da makaranta, da Masallaci, da sauran cibiyoyin zamantakewa, da na tarbiyya, da na tunani, da na yaɗa labarai, da aikin jarida, dole ne a haɗa dukan ƙoƙari domin bai wa yara da matasa kariyar da za ta hana su aukawa cikin tsattsauran ra'ayi, da

ƙungiyoyin yaudara masu rusa al'umma, dole ne a yi aiki domin dasa kishin ƙasa a cikin zukatansu, lallai bai wa 'ya'yanmu, da matasanmu kulawa, da yin tarayya da su wajen zaɓan abokai babban amana ne, kuma alhaki ne mai girma, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, ku kiyaye kawunanku da iyalanku daga shiga wuta..)) [at- Tahrim: 6]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai Allah zai tambayi duk wani wanda aka ɗaura masa alhakin kulawa akan abin da aka ɗaura masa, shin ya kiyaye shi, ko kuwa ya tozartar da shi? Kai za a tambayi mutum har akan iyalan gidansa)**.

**Ya Allah Ubangiji, ka azurta mu da abokai na gari, ka kuma tabbatar mana da abin da hakan yake haifarwa ya Ubangijin talikai..**

- 35 –

## HIMMA MAI GIRMA ITA CE HANYAR CIGABAN AL'UMMOMI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ku yi gaggawa wajen yin rige-rige zuwa ga wata gafara daga Ubangijinku, da kuma aljannar da take da faɗi matuƙa, faɗin nata kamar sammai da ƙasa, an samar da ita ne saboda waɗanda suka gasgata Allah da Manzannisa, lallai wannan babban sakamako falala ne daga Allah, da yake bayar da ita ga wanda ya so a cikin bayinsa, lallai Allah shi kaɗai ne mai falalar da ta fi ƙarfin tunani ya sifanta)) [al- Hadid: 21].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai ɗaukacin karantarwar addinin Musulunci mai ƙayatarwa, da ɗaukaka tana kirar mutane zuwa ga himma, da ƙoƙari, da ijtihadi, da raya ƙasa, tana kuma hana duk wani nau'o'i na kasala, da nauyin jiki, da ɓarna, **lallai duka waɗannan sun zo a cikin saƙwannin Allah da suka gabata,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ko kuwa ba shi da**

**labarin abin da yake cikin littafin Annabi Musa (AlaiHis-Salãm)?!. Da Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm) wanda ya kai matuƙa wajen cika alƙawarin da ya ɗauka wa Allah; na cewa: Babu wani rai da zai ɗauki zunubin wani rai?!. Kuma lallai mutum ba shi da wani abu face sakamakon abin da ya aikata.. Kuma da sannu za a bayyana aikinsu a ranar alƙiyãma kowa ya gani; saboda a girmama wanda ya kyautata ayyuka, a kuma ƙasƙantar da wanda ya munana.. Sannan a saka wa mutum akan aikinsa da cikakken sakamako)) [an- Najmi: 36 – 41]**, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana irin yanda ya kamata himma ta kasance wajen ƙarfi a inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Lallai Allah mai yawan karamci ne, yana kuma son karamci, da manyan kyawawan ɗabi'u, yana ƙin ƙasƙantattun ɗabi'u)**, Sayyiduna Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: **"Kada ku ƙasƙantar da himmarku, ni kam ban ga waɗanda suke zamowa jana- ba ya ba, sai waɗanda himmarsu ta yi ƙaranci"**, da ma dai tuni an ce: alamar da take nuna cikan hankali ita ce: himma mai ƙarfi. Alhairin Allah ya kai zuwa ga Abuɗɗayyib al- Mutanabbiy a inda yake cewa:

"Ni a cikin aibobin mutane ban ga wanda ya kai gazawar waɗanda suke da dama wajen kammala abubuwan da suka fara ba".

Lallai ƙarfafa himma bai taƙaita da wani fage banda saura ba; ya kamata ya shiga cikin kowane fanni da fage na abubuwan da ɗan Adam yake aikata a rayuwarsa, **kaman a fagen Ibada**: lallai Shari'ar Musulunci mai daraja ta kwaɗaitar akan yin rige- rige da gagagwa a fagen ibada, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku yi rige- rige zuwa ga**

**gafarar da take zuwa daga Ubangijinku, da aljannar da faɗin ya kai faɗin sama da ƙasa, duka an tanade su ne ga masu tsoron Allah))** **[Ali Imran: 133]**, lallai Allah Maɗaukakin sarki ya bayar da lamuni na lada mai yawa ga duk wanda ya yi ƙoƙari da himma wajen bauta masa, Allah mai girma yana cewa: **((Duk wanda yake biɗar ladan lahira, ya kuma yi himma wajen isa zuwa gare shi, alhalin yana matsayinsa na mai imani da Allah, to kuwa lallai waɗannan su ne ake yaba wa ayyukansu))** **[al- Isra'i: 19]**.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana da himma mai girma a dukan fagagen rayuwarsa, **a wurin ibadarsa,** Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka ya yi masa magana da cewa: **((Ya kai mai lulluɓe kai da tufafinsa. Ka tashi da daddare ka yi sallah a mafi yawan dare, ban da ɗan kaɗan daga ciki. Ka tashi tsawon rabin dare, ko ka ɗan taƙaita kaɗan daga rabin daren, ta yadda zai kai kashi ɗaya bisa uku (1/3) na dare. Ko ka yi ƙãrí kaɗan akan rabin daren ta yadda zai zamo ka tashi a kashi biyu cikin uku (2/3) na daren, ka karanta Alƙur'ãni Mai girma a cikin tsanaki, kana mai bayyanar da haruffansa, kana kuma tsayawa a wajajen tsayawa, ka yi cikakken karatu ba tare da tawaya ba. Ya kai wannan Manzo, lallai da sannu za mu saukar maka da Alƙur'ãni da yake ƙunshe da umurni da hani da wajiban ayyuka masu yi wa zukata nauyi da wahala))** **[al- Muzammil: 1 – 5]**, saboda haka ne (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake tsayuwar dare, har ƙafafuwansa suka kumbura, da aka tambaye shi game da haka, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ashe ba na zamo bawa mai yawan godiya ba?)**.

Lallai sau da yawa (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan kwaɗaitar, ya kuma zaburar da sahabbansa, da al'ummansa

wajen himma, da gabatar da ayyukan da suka fi na kowa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idan za ku roƙi Allah, to ku roƙe shi ya ba ku aljannar Firdausi, domin ita ce matsakaiciyar aljanna, kuma mafi ɗaukaka a ciki, tana saman al- Arshin mai yawan rahama, daga cikinta ƙoramun aljanna suke ɓuɓɓugowa)**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Rabi'at Bn Ka'ab (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: (Nakan kwana a wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai wata rana na kawo masa ruwan alwalla, da abubuwan da yake buƙata, sai ya ce mini: **(Ka roƙi abin da kake so),** sai n ace: Ina roƙonka zama da kai a aljanna, sai ya ce: **(Akwai kuma wani abin banda wannan?),** sai na ce: wannan ne kawai, sai ya ce: **(To ka taimake ni akan kanka da yawaita sallah)**.

Girmar himma a fagen ibada tana nufi: **gabatar da ita yanda ta kamata, kuma tasirinta ya bayyana a rayuwar mutum da ɗabi'unsa,** kada ya zamo mai ƙarya, kada ya ha'inci kowa, kada kuma ya yi wa kowa algushi, kada ya ci dukiyar mutane ta hanyar ɓarna, da haka ibadar tasa ta haɗe ta manufarta ta asali kenan, sai rayuwarsa ta zamo ta tsayu akan addini madaidaici.

A cikin muhimman fagagen himma akwai fagen **ilimi,** lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya umurce mu da mu roƙi Allah Maɗaukakin Sarki ya ba mu ilimi mai amfanin da tasirinsa zai game ɗaukacin halittun Allah Maɗaukakin Sarki, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ku roƙi Allah ya ba ku ilimi mai amfani, ku kuma nemi tsarinsa ga barin ilimin da ba shi da amfani)**, sau da yawa yakan yi addu'a da cewa: **(Ya Allah Ubangiji, ina neman tsarinka ga barin ilimin da ba shi da amfani..)**, shi ilimi mai amfani shi ne makami na ainihi da yake sanya ƙasa ta sami ƙarfi, da kuma shi

ne al'ummomi suke cigaba, babu wata al'umma da ta sami ɗaukaka da cigaba, sai da ta mallaki ilimi, babu kuma wata al'umma da ta samu ci-baya face kasala a fagen ilimi ne ya mayar da ita ta zamo jana- baya.

Lallai Sahabbai da Tabi'ai (Allah ya ƙara yarda da su) **suna ƙololuwar himma a fagen neman ilimi,** ga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) nan, mutum ne mai girmar himma a fagen neman Hadisai, yakan ce: Noma gonaki, da saye da sayarwa a kasuwanni ba su shagaltar da ni ga barin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ba; kawai dai nakan nemi Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanar da ilimi..), Sayyiduna Abudullahi Bn Umar (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce:  Ya Abuhuraira, ka fi mu lizimtar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka kuma fi mu sani Hadisansa. Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: Nakan ji labarin cewa akwai wani Hadisi a wurin wani mutum, na tashi na fi wurinsa, in tarar yana barcin ƙailula, sai ni ma in yi matashi da mayafi na a ƙofar gidansa, iska ta yi ta buɗa ƙura a fuska ta, har dai ya fito ya ganni, ya ce: Ya Baffan Manzon Allah, mene yake tafe da kai? Mene ya sa ba ka aiko na zo wurinka ba? sai in ce: a'a, ni ne ya fi kamata in zo wurinka, sai in tambaye shi game da Hadisin. Isma'il Bn Yahya ya ce: Na ji Imam as- Shafi'iy (Allah ya ƙara masa rahama) yana cewa: Na haddace Alƙur'ani lokacin da nake da shekaru bakwai, na kuma haddace littafin "al- Muwaɗɗa'" lokacin da nake da shekaru goma. Haka ma Imam Ahmad Bn Hanbal (Allah ya ƙara masa rahama) ya haddace Hadisai miliyan ɗaya, haka ma an ce: Imam an- Nawawiy yakan gabatar da darussa goma sha biyu a rana.

Kaman yanda tsofaffin malamanmu suka bayar da himma wajen ɗaukan amanar ilimi a ɗaukacin fagagensa, **haka ma suka isar da shi zuwa ga mutane yanda ya kamata**, saboda neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki, da amfanar da ɗaukacin bil'adama, saboda haka sai sunayensu da himmominsu suka wanzu a ƙwaƙwalwar tarihi, da ma can Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shi kuwa kumfa ai haka yake tafiya a iska, abin da zai amfani mutane kuma sai ya zauna a ƙasa..)) [ar- Ra'ad: 17].**

Haka ma a cikin fagagen himma akwai: **aiki,** lallai shari'ar Musulunci ta girmama sha'anin aiki, ta ɗaukaka matsayinsa, ta inda har Alƙur'ani mai girma ya haɗe tsakanin ibada da aiki, ya sanya suka zamo a gwame da juna, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Idan kuma kun gabatar da sallar, to ku bazama a bayan ƙasa saboda maslahohinku, ku nemi falalar Allah, ku yawaita ambaton Allah a zuci da baki, ko za ku sami babban rabo na alhairi a duniya da lahira)) [al- Juma'a: 10]**, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa duk wanda ya kyautata aikinsa alƙawari na samu kyakkyawar rayuwa a duniya, da kuma dawwamammiyar ni'ima a lahira, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Wanda duk ya aikata ayyuka na gari cikin maza da mata alhalin yana da cikakken imani, to kuwa tabbas za mu raya shi rayuwa mai matuƙar kyau, kuma tabbas za mu saka masu da ladan da ya fi abin da suke aikata wa kyau)) [an- Nahl: 97],** haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma aikata ayyuka na gari suna da mazaunai a cikin gidan aljannar Firdausi)) [al- Kahfi: 107].**

Babu abin da ya fi bayyana matsayin aiki kaman kasancewar ɗaukacin Annabawa (Alaihimus Salam) duka suna da ayyukansu, Annabi Adam, da Annabi Ibrahim, da Annabi Luɗu (Alaihimus Salam) manoma ne, Annabi Nuhu (AlaiHis Salam) kafinta ne, Annabi Idris (AlaiHis Salam) tela ne, Annabi Salihu (AlaiHis Salam) ɗan kasuwa ne, Annabi Dawud (AlaiHis Salam) maƙeri ne, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai mun bai wa Annabi Dawud (AlaiHis Salam) wata falala daga wurinmu ta hanyar ba shi hikima da littafi, sai muka ce: ya ku duwatsu ku rinƙa maimaita tasbihinsa a duk sanda ya yi, mun kuma hore masa tsuntsaye da suke amsa tsarkake Allahn da yake yi, mun kuma sanya ƙarfe ya yi taushi a hannunsa, yana sarrafa shi yanda yake so. Mun yi masa wahayin ya ƙera silaku masu yalwa da za su bayar da kariya ga barin hare- haren maƙiya, ya kuma kyautata saƙa su ta hanyar shigar da ƙarfen cikin hancunan juna, sai kuma muka umurce shi, shi da jama'ansa da cewa: ku sana'anta abubuwan da za su amfane ku, da ma wasunku a fagen alhairi da gyara, lallai ina da cikakkiyar masaniya da duk abubuwan da kuke aikatawa, babu abin da zai ɓuya mini daga ciki))** **[Saba'i: 10- 11]**, lallai shi ɗan Adam yana samun matsayi, da daraja ne ta hanyar abin da ya fi ƙwarewa akansa, ya kuma fi kyautata shi, lallai aiki ya fi roƙe – roƙe nesa ba kusa ba, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mutum ya yi icce ya ɗauka a bayansa ya fi masa alhairi akan ya roƙi wani, da zai ba shi, ko ya hana shi)**.

Ba wai kawai kowane irin aiki ake buƙata ba, a'a, abin da ake buƙata shi ne **a kyautata aikin,** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah yana son idan wani**

**daga cikinku zai yi aiki ya kyautata shi)**, (SallalLahu alaiHi wa sallam) a koda yaushe yana son ya ga kowa yana da aikin yi mai kyau, da zai amfani kansa, ya kuma amfani waninsa, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wajibi ne kowane Musulmi ya yi sadaka)**, sai aka ce: Idan bai sami abin da zai yi sadakar ba fa? Sai ya ce: **(Ya yi aiki da hannunsa ya sami abin da zai amfani kansa, sannan kuma ya yi sadaka)**, sai aka ce: idan bai da ikon yin aikin fa? Sai ya ce: **(Ya taimaka wa wanda buƙata ta tilasta masa)**, aka ce: idan bai yi ba fa? Sai ya ce: **(Ya bayar da umurnin aikata alhairi da adalci)**, aka ce: idan bai iya yin hakan ba fa? Sai ya ce: **(Ya kame ga barin aikata sharri, domin hakan ma sadaka ne a gare shi),** ya kwaɗaitar da wanda ya gaza yin aiki da ya kame cutarwarsa ga barin mutane, inda hakan ma kansa aiki ne da za a sami lada akansa; saboda ya tseratar da mutane ga barin sharrinsa, da cutarwarsa.

A cikin mafiya girman himmomi akwai: **himma wajen hidimta wa al'umma**, da taimako masu rauni, da masu neman taimako, da biya wa mabuƙata buƙatunsu, da saurin kai tallafi da taimako, lallai wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce: Ya Manzon Allah, wane mutum ne Allah ya fi sonsa, kuma wane aiki ne Allah Maɗaukakin Sarki ya fi so?, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai mutumin da Allah Maɗaukakin Sarki ya fi sonsa shi ne wanda ya fi amfanar mutane, kuma mafi alhairin aiki a wurin Allah Maɗaukakin Sarki shi ne: farin cikin da ka shigar a cikin zuciyar Musulmi, ko ka yaye masa damuwa, ko ka biya masa bashin da ake binsa, ko ka kori yunwar da take damunsa, na rantse da Allah, in tafi biya wa ɗan uwana wata**

**buƙata tasa, ya fi alhairi akan in yi i'itikafi a cikin wannan Masallacin –yana nufin Masallacin Madina- na tsawon wata ɗaya.. duk wanda ya tafi tare da ɗan uwansa akan wata buƙata tasa, har buƙatar ta biya, to kuwa lallai Allah zai tabbatar da diga- digansa a ranar da ƙafafuwa suke zamewa).**

**Wannan kenan, ina neman wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki..**

--------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Tsira da aminci su tabbata da amintaccen Annabi, ya Allah ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk waɗanda suka bi hanyarsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai a cikin muhimman fagagen da ya kamata ɗaukacinmu mu yi rige- rige, kuma kowwanmu ya zamo mai ƙarfin himma a ciki akwai: **hidimta wa ƙasa,** lallai hidimta wa ƙasa yana cikin imani; Allah Maɗaukakin Sarki ya umurce mu da yin rige – rige a fagagen alhairi, da amfanarwar da tasirinsa zai koma zuwa ga ƙasa, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ku yi rige – rige wajen aikata alhairai, wurin Allah gaba ɗayanku za ku koma ya ba ku labarin dukan abubuwan da kuke saɓani akansu))** **[al- Ma'ida: 48]**, lallai Allah Mai girma da ɗaukaka ya yabi bayinsa da suke rige- rige wajen bayar da alhairai ga mutane, mai girma da ɗaukaka ya bayyana cewa irin wannan alhairin yana amfanar mai yinsa a duniya da lahira, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai sun kasance suna rige – rige wajen aikata alhairai, suna roƙonmu cikin wani yanayi na fata da tsoro, lalali suna matuƙar jin tsoronmu))** **[al- Anbiya'i: 90]**, da girman

himma, da kuma kwaɗayin amfanar da mutane, da kuma cikakken amincewa da falalar Allah Maɗaukakin Sarki da dacewarsa.

Haka ma a cikin manyan himmomi akwai: **himma wajen gina ƙasa,** da kuma ɗaukan nauyin zamantakewa, da rige – rige wajen ayyukan biyayya da ɗa'a; ta hanyoyin gyara Masallatai, da gina makarantu, da asibitoci, da samar da magunguna ga marasa lafiya, duka waɗannan suna cikin sadakokin da ladansu ba sa yankewa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ladan abubuwa bakwai suna bin bawa har bayan wafatinsa, yana cikin kabari: wanda ya karantar da ilimi, ko ya samar da gulabe daga kogi, ko ya haƙa rijiya, ko ya dasa dabino, ko ya gina Masallaci, ko ya gadar da Alƙur'ani, ko ya bar yaron da yake nema masa gafara bayan rasuwarsa)**.

Mene ne ya kai girma a rinƙa samun **rige – rige a tsakaninmu wajen hidimtawa ƙasar da take ɗauke da mu, ƙasar da dukanmu muna cin alhairanta**, mu rige – rige wajen samar da haɗin – kai, da wayewa, da tausayin juna, mu gabatar da taimakonmu ga kowa da kowa, ƙasa dai tamu ce gaba ɗayanmu, za ta cigaba ne da mu, lallai iko da ƙarfinmu ba su ƙasa da na wasunmu, mu fa al'umma ce da take da tarihin cigaba da asali, dole ne mu san cewa yin zarra a komai, da kuma kutsawa cikin abubuwa masu wahala, da rashin- ganin – kai su ne hanyoyinmu, shi da ma abubuwa masu girma suna rataye da abubuwan ƙi, ba a isa zuwa ga maslaha da alhairai sai ta hanyar ƙoƙari da kuma juriya. Alhairin Allah ya kai zuwa ga Abuttamam a inda yake cewa:

"Na duba babban hutu, amma ban hango shi ba, sai a gadar wahalhalu".

**Ya Allah Ubangiji ka azurta mu da himma mai girma da za ƙa kai mu zuwa ga ƙololuwa, da falala, da cigaba, da ɗaukaka a cikin abubuwan da za su amfane mu a duniya da lahira, ka kiyaye mana addininmu, da ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya.**

- 36-

## GINSHIƘAN GINA ƘASASHE

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya RasulalLahi –SallalLahu alaiHi wa sallam- ka ce masu: Ku yi aiki kawai, Allah da Manzonsa da muminai ne da sannu za su gani, da kuma sannu za a mayar da ku zuwa ga masanin abubuwan da suke a ɓoye da na sarari, ya ba ku labarin abubuwan da kuke aikatawa)) [at- Tauba: 105]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda a Hadisinsa mai girma yake cewa: **(Da alƙiyama za ta tsaya alhali akwai iccen dabino a hannun wani daga cikinku, in dai ya sami dama ya dasa kafin ta tsaya, to ya dasa**). Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai a cikin manyan ginshiƙan Musulunci da muhimman karantarwarsa akwai: so da kishin ƙasa, da ba ta kariya, da kuma yin aiki tuƙuru wajen cigabanta da haɓaka darajarta, babu girma da darajar da suka kai mutum ya zamo mai ainihin kishin ƙasarsa, mai kuma yin duk abin da zai iya wajen gina ta, da ɗaukaka darajarta, duk wata al'umma da ta sami cigaba a

fagen ilimi da halara, to babu shakka, za ka tarar akwai nagartattun gwaraza da zukatansu suke cike da son ƙasashensu, waɗanda su ne suka tsaya mata, suka zage dantse wajen gabatar da ayyukan da ƙasar da ma al'umma suke amfana da su, lallai ƙasarmu mai daraja ta cancanci dukan alhairai daga 'ya'yanta, ita ce fa zuciyar ƙasashen Larabawa da na Musulunci, ita ce garkuwar al'umma da takobinta, ita ce ganuwar da take bai wa al'umma kariya ga barin hatsurran ta'addanci da manyan ƙalubale, saboda haka, ba ta kariya, da kuma yin aiki tuƙuru wajen cigabanta suka zamo wajibai a addinance, kuma alhaki ne na ƙasa da ya rataya a wuyanmu, ita ce asalin duk wani cigaba, garin da Allah ya aiko Manzanni masu yawa, ita ce garin da Allah ya gwama sunanta da tsaro gami da aminci a cikin Alƙur'ani mai girma, Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗi ta bakin Shugabanmu Annabi Yusuf (AlaiHis Salam) cewa: **((Ku shiga Misra –da yardar Allah- cikin aminci)) [Yusuf: 99]**.

Allah ya jiƙan Salahuddin as-Safdiy da yake cewa:

"Duk wanda ya ga doron ƙasa da yankunan da suke cikinta, ya ga mutane da jinsunansu da nau'o'insu, amma bai ga Misra da mutanen Misra ba, to lallai haƙiƙa bai ga duniya ba, bai kuma ga mutane ba…"

Babu shakka, cigaba da kuma gina ƙasa, da aiki ba dare ba rana su ne suke bai wa al'umma lamunin samun izza da karama da mutunci a idon duniya, sai dai kuma gina ƙasa ba zai yiwu da yawan maganganu, da mafarke- mafarke, gami da burace- burace kawai ba, dole ne a yi aiki tuƙuru a yi gumi, a kuma sadaukar da kai, a kuma yi riƙo da duk wani sababi na cigaba da ɗaukaka ƙasa, a cikin muhimman waɗannan dalilan

akwai: **Fahimtar ƙalubale:** lallai fahimtar matsayi gami da ƙimar ƙasa, da kuma fahimtar ƙalubalen da suke fuskantarta, da hatsarurrukan da suke zagaye da ta ita, duka abubuwa ne da suke buƙatar a san girman waɗannan ƙalubale da suke fuskantarmu, domin idan ba mu san waɗannan ƙalubalen ba, ba kuma mu fahimce su ba, ba za mu iya samar masu da nagartattun mafita da magunguna ba.

Lallai fahimtar matsayi, gami da darajar ƙasa, da kuma fahimtar manyan ayyuka da take gabatarwa, da wajibcin ƙarfafa daula, da nuna mata goyon baya, da kuma aiki tuƙuru wajen cigabanta da ɗaukaka darajarta, abubuwa ne muhimmai daga cikin ginshiƙan samar da ƙasa mai ƙarfi, rukuni ne daga cikin rukunnai kishin ƙasa da bai wa duk wani abu da yake da jiɓi da ita kariya.

Haka ma fahimtar muhimmancin ƙasa yana nufin mu tsaya tsayin – daka wajen gyara gurɓatattun fahimtar da ƙungiyoyin 'yan ta'adda suka yi ta ƙoƙarin dasa su a cikin zukatan al'umma, inda suka yi amfani da su wajen sanya shakku, da raba tsakanin al'umma da shugabanninsu, duk kuwa da cewa karantarwar addini tana shiryatar da mu zuwa ga girmama shugaba adali, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai a cikin girmama Allah akwai girmama Musulmi mai furfura, da mahaddacin Alƙur'ani da haddarsa bai kai shi zuwa ga wuce- gona- da – iri ba, sannan kuma bai ƙaurace wa Alƙur'anin ba, da kuma girmama shugaba mai adalci),** Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya shugaba mai adalci a cikin mutane bakwai da Allah zai yi masu inuwa da Al'arshinsa a ranar da babu wata inuwa sai inuwarsa, inda Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Allah zai yi wa mutane bakwai**

**inuwa a ranar da babu inuwa sai tasa....)** a farkonsu sai ya faɗi: **shugaba mai adalci..**

A cikin muhimman ginshiƙan gina ƙasa akwai: **Sadaukar da kai wajen hidimta wa ƙasa,** kishin ƙasa na haƙiƙa ba wai kawai shi ne rera taken ƙasa, da kuma yawan surutu a kai ba, kishin ƙasa tsari ne na rayuwa, da cika zuciya da halin da ƙasar take fuskanta, da jin raɗaɗin abubuwan da suke damunta, da kuma yin farin - ciki da duk abubuwan da za su kai ƙasar zuwa ga tudun- na- tsira, da kuma zama cikin shiri a koda yaushe wajen sadaukar da kai domin cigaban ƙasa.

Bai wa ƙasa kariya, da sadaukar da kai saboda ita, suna cikin manyan abubuwan da Shari'a ta wajabta, kuma wajibi ne na ƙasa da yake rataye a wuyar duk wanda yake rayuwa a doron ƙasarta, samanta kuma take yi masa inuwa, son ƙasa bai taƙaita kawai a so na zuci ba, dole ne a gani a aikace ta hanyar zamowa ɗan ƙasa na gari, mai amfanar kansa da amfanar al'ummarsa, saboda haka dole ne a sadaukar da kai, saboda ƙasa ta zamo cikin ƙarfi da izza, zamowar mutum ɗan ƙasa yana wajabta masa yin tinƙaho da ƙasarsa, ya kuma yi taimakekeniya da sauran 'yan ƙasa wajen kiyaye ƙasa, domin samun kwanciyar hankali da natsuwar ƙasashe abu ne da yake tabbatar da manufar da Allah Maɗaukakin Sarki ya halicci halittu akansa, domin yana kai wa zuwa ga raya ƙasa, da ɗaukaka addini, da tsayar da ibadu, lallai ba a Shar'anta jahadi a Musulunci ba, sai domin a bai wa ƙasashe kariya, da kuma daƙile zalunci da ta'addancin da suke fuskantar ƙasa; saboda haka ne ma Allah Maɗaukakin Sarki ya ɗaukaka darajar mutanen da suke miƙa rayuwarsu wajen bai wa ƙasashensu kariya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya sayi**

**rayukan muminai da dukiyoyinsu daga wurinsu akan zai ba su aljanna, suna yaƙar waɗanda suka yaƙe su saboda suna ɗauka kalmar Allah, su kasha, a kashe su, lallai Allah ya yi masu alƙawari na gaskiya akan haka a cikin litattafan Attaura da Injila da Alƙur'ani..))** [at- Tauba: 111]**.**

Haka ma a cikin muhimman ginshiƙai na gina ƙasashe da cigaba akwai: **Aiki tuƙuru da kuma kyautata aikin:** Lallai addinin Musulunci ya ɗaukaka matsayin aiki, inda ya sanya shi ya zamo ƙofa daga cikin ƙofofin ibada, kai ma, a cikin ibadun yana ƙololuwar ibadu; saboda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sifanta aiki da cewa jahadi ne a wajen ɗaukaka kalmar Allah, an ruwaito Hadisi daga Ka'ab Bn Ujrat (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: wani mutum ya wuce ta wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai Sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) suka ga irin yanda yake kazar-kazar da nishaɗi, sai suka ce: ya Manzon Allah, ina ma fisabililLahi yake yi? Sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan ya fito ne domin ya nema wa ƙananan yaransa abinci, to ya fito ne fisabililLahi, haka ma idan ya fito ne saboda ya sami abin da zai iya ɗaukan nauyin iyayensa tsofaffi guda guda biyu, to ya fito ne fisabililLahi, haka ma idan ya fito ne domin ya nema wa kansa arziki domin ya samu ya kame, to lallai ya fito ne fisabililLahi, amma idan ya fito ne kawai saboda duniya ta ganshi, domin ya yi fankama, to a nan ya fito ne fisabilis- Shaiɗan)**.

Lallai addini da kishin ƙasa sun wajabta mana yin aiki tuƙuru wajen samar da abubuwan da ƙasa take buƙata, hasali ma addininmu, addini ne na aiki da kuma kyautata aiki, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shi ne wanda ya halicci**

**mutuwa da rayuwa; domin ya jarabba ku: shin wane ne daga cikinku yafi kyautata aiki, lallai Allah mabuwayi ne mai kuma yawan gafara)) [al- Mulki: 2],** haka ma yana cewa: ((**Ya ku waɗanda kuka yi imani, idan aka kira sallah ranar Juma'a, to ku tafi ambaton Allah, kuna masu kwaɗayin samun lada, ku bar kasuwanci, wannan abu da aka ba ku umurni shi ne zai fi maku amfani in dai har kun sani. Idan kuma kun gabatar da sallar, to ku bazama a bayan ƙasa saboda maslahohinku, ku nemi falalar Allah, ku yawaita ambaton Allah a zuci da baki, ko za ku sami babban rabo na alhairi a duniya da lahira… Idan suka ga wata hãjã ta kasuwanci, ko wani wasa, sai su watse su bar ka a tsaye kana huɗuba, ka ce: lallai falala da ladan da suke wurin Allah sun fi alhairi akan wasanni da kasuwanci, lallai Allah shi ne fiyayyen masu azurtawa, ku nemi arzikinsa ta hanyar yi masa biyayya)) [al- Juma'a: 9 -11],** Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu abincin da yafi abincin da mutum ya saya da guminsa, lallai Annabi Dawud (AlaiHis Salam) yana cin guminsa ne)**.

A nan muna ƙara tabbatar da cewa: lallai addininmu na Musulunci ba wai ya nemi da mu yi aiki kawai ba ne, a'a, sai da ya nemi da mu kyautata aikin cikin nagarta da inganci, domin Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai mu ba ma tozartar da ladan wanda ya kyautata aiki)) [al- Kahfi: 30],** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah yana son idan za ku yi aiki ku kyautata shi).**

A cikin muhimman ginshiƙai na gina ƙasashe da cigabansu akwai: **Ilimi da na nagartaccen shugabanci:** lallai kowane gini yana buƙatar ilimi da kuma ƙwarewa, da zurfi ma a cikin ilimin, ba wai kawai saboda mutum yana da sha'awar yin gini

ba, idan muka duba cikin Alƙur'ani mai girma, da Hadisai masu tsarki za mu ga cewa suna ƙarfafa wajibci samun sharaɗin cancanta da kuma samar da aikin cikin amana, Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗi ta bakin Annabi Yusuf (AlaiHis Salam) cewa: **((Ku sanya ni a wurin taskokin ƙasa, lallai ni mai tsanani kiyaye amana ne, ina kuma da cikakkiyar masaniya akan haka)) [Yusuf: 55]**, haka ma Allah mai girma da ɗaukaka ya faɗi ta bakin 'yar Annabi Shu'aib tana faɗi akan shugabanmu Annabi Musa (AlaiHis Salam) cewa: **((Baba, ka yi jinga da shi, da ma fiyayyen wanda ya kamata a yi jinga da shi, shi ne: mutum mai ƙarfi, kuma amintacce)) [al- Ƙasasi: 26].**

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi gargaɗi gami da naɗa, ko ɗaura wanda bai cancanta ba a wani matsayi, ya bayyana hakan a matsayin alama ce daga cikin alamomin tashin alƙiyama, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idan aka damƙa abu a hannun waɗanda ba su cancanta ba, to ku tsumayi tashin alƙiyama),** waɗanda suka cancanta a kowane fage, su ne: waɗanda suke da ƙwarewa, gami da amana.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana sanya Sahabbansa da masu jagoranci a cikinsu, kowa gwargwadon saninsa da kuma ikon da yake da shi wajen sauke nauyin da yake tattare da aikin da za a ba shi, ba ya naɗa mutum saboda ganin ido, ko kusanci na jini, ko kuma saboda kawai yana sonsa, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuzarrin (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: Na ce: Ya Manzon Allah, ba ka ba ni shugabanci ba? ya ce: sai ya dafa kafaɗa ta, sannan ya ce: **(Ya Abuzarrin, ka san kai mutum ne mai rauni, shi kuma shugabanci amana ne, a ranar alƙiyama kuma ƙasƙanci ne da**

**nadama, sai dai kawai ga wanda ya amshe shi bayan cancanta, ya kuma sauke nauyin da yake a kansa),** haka ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya faɗa wa Sayyiduna Abdurrahman Bn Samra cewa: **(Ya Abdurrahman, kada ka kuskura ka nemi shugabanci; domin idan ba ka nema ba, aka ba ka, sai a taimake ka wajen sauke nauyin da yake tattare da shi, idan kuma sai da ka nema ne aka ba ka, sai a bar ka da wayonka).**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa gaba ɗaya, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai a cikin muhimman ginshiƙai da asali na gina ƙasashe akwai: **Ɗaukaka kyawawan ɗabi'u da aiwatar da su a aikace,** duka al'ummomi da cigaban da ba a gina su akan ginshiƙin kyawawan ɗabi'u ba, to tun ranar gina su aka cakuɗa su da abin da zai rusa su, tamkar dai masu kitso da ƙwarƙwata.. alhairin Allah ya isa zuwa ga wanda yake cewa:

"Idan aka jarrabi mutane da cibaya wajen ɗabi'u, to kawai a zauna domin fara amsar ta'aziyyarsu, a shirya wa kukan mutuwarsu.."

Wani ma yana cewa:

"Ai ba wata abu ce al'umma ba, sai kyawawan ɗabi'u, muddin akwai su, to al'umma tana nan, idan kuma ka ga ta durƙushe, to ɗabi'u ne suka durƙushe a cikinta.."

Lallai kyawawan ɗabi'u suna da matsayi mai girma a cikin Musulunci, da su ne Musulmi yake hawa kan muƙamai da darajoji na imani, da su ne ma'aunai suke rinjaye a ranar da za a bijirar da kowa a gaban Allah Makaɗaici, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu wani abu da ya kai kyawawan ɗabi'u nauyi a cikin ma'aunin aikin bawa mumini a ranar alƙiyama, lallai Allah yana ƙin mai alfashan da harshensa ba shi da burki),** lokacin da aka tambayi (SallalLahu alaiHi wa sallam) akan mafi yawan abubuwan da suke shigar da mutane aljanna? Sai ya amsa da cewa: **(Tsoron Allah da kyawawan ɗabi'u).**

Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya kyawawan ɗabi'u a matsayin ma'auni na cikan imani da tawayarsa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda imaninsa yafi cika a cikin muminai shi ne: wanda yafi su kyawawan ɗabi'u…),** Mai tsira da aminci yana cewa: **(Ka ji tsoron Allah a duk inda kake, ka bibiyi munanan ayyuka da kyawawan ayyuka sai su share su, ka kuma yi mu'amala da mutane da kyawawan ɗabi'u).**

Lallai kyawawan ɗabi'u suna sabar wa mai su da dukan alhairai, irinsu: tausayi, da son alhairai ga mutane, da aiki tuƙuru domin amfanar mutane, da amfanar ƙasa da 'yan ƙasa, ba tare da son kai ba, lallai addininmu ya ginu ne akan fifita wasu akan kai, da kuma son yin baiwa, ba akan son kai, da rowa, gami da ƙwauro.

Haka ma a cikin ginshiƙan gina ƙasashe da cigabansu akwai: **Adalci,** lallai ana gina ƙasashe ne akan adalcin da yake daidaita mutane gaba ɗayansu akan haƙƙoƙi da wajibai, ba tare da an fifita wani akan wani ba, wannan shi ne umurnin da Allah Maɗaukakin Sarki ya bayar a cikin littafinsa mai girma, a inda yake cewa: **((Lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana bayar da umurnin a yi adalci, a kuma kyautata, a kuma bai wa makusanta wani sashe na dukiya, ya kuma hana yin alfasha da abubuwan ƙi da mugunta, lallai yana yi maku wa'azi ne ku za ku hankaltu..)) [an- Nahl: 90],** tun ba yau ba aka ce: Lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana taimakon adalar ƙasa, koda kuwa ta kafira ce, amma ba ya taimakon azzalumar ƙasa, koda kuwa ta Musulmai ce; domin da a ce da gaske daula ce Musulma da ba ta yarda da zalunci, ko ta ginu akansa ba, saboda haka ne ma wasu suka ce: Lallai ta yiwu ƙasashe su wanzu idan suka gwama kafirci da adalci, amma bas a wanzu idan suka gwama Musulunci da zalunci; saboda Musuluncinsu a irin wannan hali na je-ka- na- yi- ka ne, bay a ɗauke da ma'anar Musulunci na haƙiƙa, wayam yake a cikinsa babu manyan karantarwarsa na gaskiya da adalci, da rashin yarda da zalunci da mugunta, da sauran abubuwan da suka yi kama da haka.

**Ya Allah Ubangiji ka ba mu cikakken tsaro a cikin ƙasashenmu, ka kuma datar da shugabanninmu masu jiɓintar al'amurranmu, ka kiyaye ƙasarmu daga dukan sharri da ɓarna..**

- 37 –

## HAƊIN KAN ƘASA NE HANYAR SAMUN ƘARFINTA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ku yi riƙo da igiyar Allah gaba ɗayanku, kada ku kuskura ku rarraba)) [Ali Imran: 103]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Lallai Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zo da saƙon da **yake kira zuwa ga haɗin kai, da kusanto da juna, yana kuma hana rarrabuwan kawuna, da rikice – rikice,** da wannan saƙon ne ya tattaro gungunan Larabawa da suke faɗa da juna, ya mayar da su suka zamo al'umma ɗaya, ya kuma ƙulla 'yan uwantaka ta imani a tsakaninsu, ya haɗa tsakanin zukatansu da mahaɗin soyayya, Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Su muminai 'yan uwan juna ne..)) [al-Hujrat: 10]**, haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah ne ya haɗa tsakanin zukatansu, da za ka ciyar da duk dukiyar da take bayan ƙasa gaba ɗaya, ba za ka iya haɗa tsakanin zukatansu ba, Allah ne dai ya haɗa tsakaninsu, saboda shi da ma can mabuwayi ne shi, mai yawan hikima)) [al- Anfal: 63]**, haka ma kaman yanda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya

bayar da umurnin soyayya, da tausayi, da jinƙan juna, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Misalin muminai wajen soyayyar junansu, da jinƙan junansu, da tausayin junansu tamkar jiki ne da idan wata gaɓa ta cutu, duka sauran jikin zai kamu da rashin barci, da kuma zafin ciwo).**

Lallai **wannan hadin kan bai taƙaita kwai tsakanin Musulmai da junansu ba; abin ya haɗe ɗaukacin mutane,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku mutane, lallai mun halicce ku ne daga asali ɗaya wanda dukanku kuke daidai da juna, wannan asali kuwa shi ne Annabi Adam da Hauwa'u (Alaihimas-Salãm), ta hanyar auratayya ne kuma muka mayar da ku al'ummomi masu yawa da ƙabilu mabambanta; domin ku san juna, ku kuma yi taimakekeniya a tsakaninku, lallai wanda ya fi matsayi a wurin Allah duniya da lahira shi ne wanda ya fi ku tsoron Allah, tabbas ilimin Allah ya game komai, ƙwararre ne kuma wanda babu wani abu komin ƙanƙantarsa da zai ɓuya masa a cikin dukan al'amurra)) [al-Hujrat: 13]**, wannan ne abin da Alƙur'ani mai girma ya yi magana akansa, a lokacin da yake magana akan 'yan uwantaka ta mutuntaka tsakanin Annabawa da waɗanda suka saɓa da su a aƙida, kaman yanda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Adawa ma mun aika masu da ɗan uwansu Hudu..)) [al- A'araf: 65; Hud: 50]**, da inda Allah mai girma yake cewa: **((Samudawa ma mun aika masu da ɗan uwansu Salihu..)) [al- A'araf: 73; Hud: 61]**, da inda Allah mai girma yake cewa: **((Mutanen Madyana ma mun aika masu da ɗan uwansu Shu'aibu..)) [al- A'araf: 85; Hud: 84; al- Ankabut: 36]**, bayan Allah Maɗaukakin Sarki ya ambaci ƙissoshin Annabawan da suka gabata, sai mai girma da ɗaukaka ya ce: **((Lallai wannan ita al'ummarku, al'umma ce**

**guda ɗaya, kuma ni ne Ubangijinku, saboda haka ku ji tsoro na))** **[al- Muminuna: 52]**, haka ma Maɗaukakin Sark yana cewa: **((Lallai wannan ita al'ummarku, al'umma ce guda ɗaya, kuma ni ne Ubangijinku, saboda haka ku bauta mini))** **[al- Abiya'i: 92]**, Imam al- Baghwiy (Allah ya ƙara masa rahama) ya ce: Allah ya aiko ɗaukacin Annabawa ne; domin su tsayar da addini, da kuma haɗa kawunan al'umma, da nesantar rarrabuwan kawuna da saɓani.

Babu shakka akan cewa: **kiran da Musulunci yake yi zuwa ga haɗin kai, da zama a matsayin tsintsiya maɗaukin ɗaya, da nesantar rarrabuwan kawuna, da son kai, ɗaya ne daga cikin dalilan da suka kiyaye ƙarfin ƙasa, da zaman lafiyar al'umma;** saboda shi mutum komin ƙarfinsa idan dai a cikin al'umma mai rauni yake rayuwa, to kuwa shi ma mai raunin ne, a gefe ɗaya kuma, idan aka sami mutum mai rauni a cikin al'umma mai ƙarfi, to shi ma zai sami ƙarfi daga cikin ƙarfin al'ummar da yake rayuwa a cikinta; saboda haka ne addinin Musulunci ya ɗaukaka matsayin ɗan ƙasa, ya kuma tabbatar da cewa: ita ƙasa ta ɗaukacin 'ya'yanta ne, tana kafuwa ne da su duka; haɗin kan ƙasa kuma yana nufin rashin rarrabuwar kawuna tsakanin 'ya'yanta saboda addini, ko launi, ko jinsi, Balarabe ba shi da wani fifiko akan wanda ba Balarabe, haka ma farin mutum ba shi da wani fifiko akan baƙin mutum, sai na tsoron Allah, da ayyuka na gari, ta haka ne aka samar da yarjejeniyar Madina, wadda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya tabbatar da ita tare da Yahudawan Madina; inda ya bai wa Yahudawa dukan haƙƙoƙin da Musulmai suke da shi na 'yanci, da tsaro, da zaman lafiya, ya kuma ɗaura masu alhakin yin tarayya da Musulmai wajen bai wa garin Madina kariya, a wani yanayi

mai ƙarfi na tabbatar da cewa: ita ƙasa a Musulunci tana ƙunshe ne da ɗaukacin 'ya'yanta, ta yalwace su dukansu, matuƙar kowa ya kiyaye abin da ya wajaba akansa, gami da alhakin da ya rataya a wuyansa.

Haka ma addinin Musulunci ya ɗaukaka ƙimar aikin tare da ruhi na jama'a, ya kuma sanya tsayawa a sahu ɗaya, da haɗa ƙarfi da ƙarfe, da yin watsi da saɓani a matsayin wani abu da ya zama wajibi akan al'umma, a kowane zamani, da kuma kowane wuri, wannan umurnin Allah Maɗaukakin Sarki ne a cikin Alƙur'ani mai girma, a inda yake cewa: **((Ku yi riƙo da igiyar Allah gaba ɗayanku, kada ku kuskura ku rarraba))** **[Ali Imran: 103]**, Haka ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah ya yarda maku da abubuwa guda uku, ya kuma ƙi abubuwa guda uku daga gare ku; ya yarda maku da: ku bauta masa kada ku haɗa shi da kowa wajen bauta, da kuma ku yi riƙo da igiyar Allah gaba ɗayanku kada ku kuskura ku rarraba, ya kuma ƙi maku: gulma, da yawan tambayar halayen da mutane suke ciki, da ɓarnata dukiya)**, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya buga misalin al'umma wajen haɗin kanta, da yanda take jin juna, da taimakon juna, ya kwatanta ta da tsayayyen gini, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Shi mumini da mumini tamkar gina ne guda ɗaya, da sashe yake ƙarfafa sashe, sai ya shigar da 'yan yatsunsa cikin juna)**.

Lallai Alƙur'ani mai girma ya ba mu misalai na haɗin kan da ya yi sanadiyyar bai wa ƙasa kariya, da zaman lafiya ga al'umma, alal misali: ga Sayyiduna Yusuf (AlaiHis Salam) nan da ya samar da wani nagartaccen tsari, kuma ɗaukacin al'umma suka haɗu suka yi taimakekeniya a tsakaninsu; domin

isa zuwa ga manufarsu, suka zartar da tsarin a ƙasa, suka yi iya iyawansu wajen taimakekeniya, da haɗin kai, daidai da yanda aka tsara tsarin, suna masu kwaɗayin isa zuwa ga manufarsu da suka shata, hakan kuwa sai ya yi sanadiyyar ƙaruwar arziki, da haɓakar tattali, da tsaro, da ƙarfin tsumi da tanadi ga ƙasar, mutane kuma suka yi wa ƙasar tsinke saboda su sami alhairan Misra, Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗi ta bakin Annabi Yusuf (AlaiHis Salam) cewa: **((Ya ce: shekaru bakwai za ku yi a jere – kaman yanda kuka saba- kuna noma, duk abin da kuma samu ku bar shi a cikin zangarniyarsa, in banda kaɗan ɗin da za ku ci. Daga baya kuma, wasu shekaru bakwai ɗin masu tsanani za su biyo baya da za ku ci abin da kuka riga kuka adana, kuna masu rage kaɗan gudun ko ta- kwana, sannan bayan haka kuma sai shekarar da mutane za su nemi taimako ta zo, a cikin ne kuma amfanin gona zai fara bayyana))** [Yusuf: 47 – 49].

Haka ma addinin Musulunci ya yi kira, ya kuma kwaɗaitar akan duk wani abu da yake zama sanadiyyar haɗin kai, da daidaita sahu, ya yi kira zuwa ga tausayi, da jinƙai, da rangwame, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Saboda rahamar da Allah yake yi maka, kai da su ne, ya sanya ka zamo mai sauƙin-kai, ba ka zamo mai kakkausar magana akan kuka-kurensu ba, da ka zamo mai ƙyeƙasasshiyar mu'amala, mai kuma busasshiyar zuciya da sun tarwatse sun bar ka, saboda haka, ka cigaba da kawar da kai ga barin kura-kurensu, ka nema masu gafara, ka nemi shawarwarinsu cikin al'amurra, kana mai mutunta ra'ayoyin su cikin abin da ba a saukar maka da wahayi akai ba, idan ka ɗauri aniyar zartar da wani al'amari bayan shawarwari, to, ka zartar da shi kana mai dogaro da Allah; saboda lallai Allah yana son wanda yake**

**miƙa al'amurran sa zuwa gare shi))** **[Ali Imran: 159]**, lallai tausayi, da jinƙai, da rangwame dalilai ne na haɗin kai, da ƙara kusantar juna, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai wannan addinin sauƙi ne, babu wanda zai tsananta addini face addinin ya fi ƙarfinsa, ku nemi dacewa a dukan ayyukanku, idan ba ku sami hakan ba, to ku kusanto zuwa ga yin daidai ɗin, ku yi wa junanku albishir, muddin kun kasance a haka, ku kuma nemi sa'a na gabatar da haka tun daga lokacin fitowar rana har zuwa lokacin walha, da bayan sallar La'asar zuwa Maghriba, da wani yanki na ƙarshen dare)**, a wani wurin kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai an aiko ni ne da addini mai rangwame).**

Haka ma ya yi kira zuwa ga yaɗa soyayya, da zaman lafiya tsakanin 'yan ƙasa ɗaya, duk kuwa da bambancin addini da yake tsakaninsu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah ba ya hana ku girmama da sada zumuntanku da kãfiran da ba su yaƙe ku ba, ba kuma su fitar da ku daga gidajenku ba, lallai Allah yana son masu kyautatawa da kuma sada zumunta))** **[al-Mumtahanat: 8]**, akan wannan karantarwa ta Alƙur'ani mai girma ne, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake mu'amala da waɗanda ba Musulmai ba, saboda haka ne (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake kyautata masu, yake kuma amsar kyautar da suke ba shi, yake kuma amsa gayyatarsu, ya kuma tafi ya gaishe da mara lafiyar cikinsu; duka saboda ya bayyana rangwamen wannan addini, da kuma kiyaye haɗin kan ƙasa, da zamanta a matsayin tsintsiya maɗaurinki ɗaya.

Lallai abin da ya wajaba akanmu a wannan lokaci, ya kuma fi komai cancantar a gabatar, suna tilasta wa ɗaukacin 'yan ƙasa na gari, waɗanda suka fahimci yanayin da ake ciki, da su tsaya

a sahu ɗaya wajen samar wa ƙasarsu duk abubuwan da take buƙata, kowa a fagensa, likitoci su yi taimakekeniya da junansu wajen samar wa ƙasarsu duk abubuwan da take buƙata a fagen likitanci, masana dokoki, da injiniyoyi, da manona, da malaman makaranta, da sauran fagage da sana'o'i ma haka, kowanne ya haɓaka ruhin baiwa, da sadaukar da kai a cikin al'umma, kowa a fagensa, wasu su gudanar da aiki da ƙarfinsu, wasu kuma su ciyar da dukiyarsu, wasu kuma su karantar da mutane, zai zamo da haka an yi amfani da dukan ƙarfi, da baiwar da Allah ya azurta ƙasa da su kenan wajen hidimta wa ƙasa, wannan kuma yana cikin haƙiƙanin addininmu, inda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi mana magana da gamammiyar sigar da ba ta bar kowa ba, Allah mai girma yana cewa: **((Shi ne wanda ya sanya ƙasa ta zamo maku sauƙaƙƙa, ku yi tafiya a sasanninta, ku ci daga cikin arzikin Allah da ya fitar maku daga gareta, zuwa gare shi -shi kaɗai- za ku koma domin sakamako))** **[al- Mulki: 15]**, haka mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Idan kuma kun gabatar da sallar, to ku bazama a bayan ƙasa saboda maslahohinku, ku nemi falalar Allah, ku yawaita ambaton Allah a zuci da baki, ko za ku sami babban rabo na alhairi a duniya da lahira))** **[al- Juma'a: 10].**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi

masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai duk mai bibiyan tarihi da kyau zai fahimci cewa: tabbas rarrabuwan kawuna, da saɓani dalilai ne na samun rashin nasara, da rauni, tabbas Alƙur'ani mai girma ya gargaɗe mu akan haka, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada nuna-halin-ko-in-kula ga umurni da ayyukan alhairi, da hani kan munanan ayyuka, da za su haɗa ku akan alhairi da addinin gaskiya, ya sanya ku zamo kamar waɗanda suka yi biris da umurni da aikata ayyukan alhairi, da hani kan munanan ayyuka, a sakamakon haka sai suka rarrabu ƙungiya-ƙungiya, suka yi saɓani a cikin addinin su, bayan bayyanannun hujjoji da suke bayyana gaskiya sun zo masu, lallai waɗannan da suka rarrabu suka kuma yi saɓani suna da azaba mai girma))** **[Ali Imran: 105]**, haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ku kuskura ku yi rikici, sai rashin nasara ya same ku, kwarjininku ya tafi, ku yi haƙuri, lallai Allah yana tare da masu haƙuri))** **[al- Anfal: 46]**, lallai rarrabuwan kawuna, da rashin tsayuwa akan abu guda ɗaya abu ne da yake tafiyar da kwajinin al'umma, ya kuma gadar mata da rauni, gami da ƙasƙanci, lallai gargaɗi game da rarrabuwan kawuna ya kai gargaɗi a ce: duk wanda ya mutu a wannan yanayi, to ya yi mutuwar zamanin jahiliyya ne.

Saboda haka ne addinin Musulunci ya yaƙi duk wata ɗabi'a da za ta kai zuwa ga rarrabuwan kawuna, da rashin zama akan kalma ɗaya, saboda haka Musulunci **yana hana nuna wariya, wadda ɗaya ce daga cikin abubuwan da ta'assubancin jahiliyya mai muni yake gadarwa**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai an hana ku girmanka zamanin**

**jahiliyya, da yawan yin alfahari da iyaye, mumini mai tsoron Allah ne kawai, da kuma fajiri mara rabo, dukanku 'ya'yan Adam ne, shi kuma Adam daga ƙasa yake)**, haka ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana cewa mutane daidai wa daidai suke wajen haƙƙoƙi da wajibai, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ya ku mutane, ku sani Ubangijinku ɗaya ne, babanku ma ɗaya ne, ku sani Balarabe ba shi da wani fifiko akan wanda ba Balarabe ba, haka ma wanda ba Balarabe ba ba shi da wani fifiko akan Balarabe, farin mutum ba shi da fifiko akan baƙin mutum, haka ma baƙin mutum ba shi da wani fifiko akan farin mutum sai da tsoron Allah..)**

**Ya Allah Ubangiji ka haɗa kawunanmu, ka kuma daidaita zukatanmu, ka datar da mu zuwa ga abin da kake so, ka kuma yarda shi, ka azurta mu da ikhlasi a wajen magana da aiki, ka kiyaye mana ƙasarmu, ka ɗaukaka darajarta a duniya.**

- 38 –

## HAƘƘOƘIN MATASA DA WAJIBANSU

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Lallai su matasa ne da suka yi imani da Ubangijnsu, sai kuwa muka ƙara masu shiriya)) [al-Kahfi: 13]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati, da aminci, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Lallai samartaka marhala ce mai matuƙar muhimmanci a cikin marhalolin rayuwar ɗan Adam, lokaci ne na ƙarfin jiki, da nunan hankali, da kazar- kazar, da nishaɗi, da baiwa, da yalwatacciyar fata ta gari, da fuskantar rayuwa, babu shakka matasa su ne ginshiƙin al'umma, su ne zuciyarta da take bugawa, su ne madogararta mai ƙarfi, babu wanda zai musanta muhimmiyar rawar da matasa suke takawa wajen gina ƙasashe, da cigabansu, da ɗaukakansu.

Lallai Alƙur'ani mai girma ya bayyana marhalar samartaka a matsayin marhalar da take tsakiyar rauni guda biyu; raunin yarantaka, da raunin tsufa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah wanda ya halicce ku daga rauni, sannan bayan wannan raunin ya sanya maku ƙarfi, sannan bayan ƙarfin kuma ya sanya maku wani raunin gami da furfura..)) [ar- Rum:**

**54]**, saboda haka ne ake bayar da Annabta da Manzanci a shekarun samartaka, Allah Maɗaukakin Sarki ya ba mu labarin Sayyiduna Yusuf (AlaiHis Salam) da cewa: **((Lokacin da ya kai ƙarfinsa, sai muka ba shi Annabta da ilimi, da ma can haka muke saka wa masu kyautatawa)) [Yusuf: 22]**, haka ma ya ba mu labari game da Sayyiduna Musa (AlaiHis Salam) da cewa: **((Lokacin da ya kai ƙarfinsa, ya cika, sai muka ba shi Annabta da ilimi, da ma can haka muke saka wa masu kyautatawa)) [al-Ƙasasi: 14]**, Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: **"Allah bai aiki wani Annabi ba, sai matashi, bai kuma bai wa wani malami ilimi ba, sai a lokacin da yake matashi.."**, ga Annabi Ibrahim "Khalilur Rahman" nan (AlaiHis Salam) da ya ƙalubalanci masu bautan gumaka a lokacin da yake matashi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Suka ce: mun ji wani matashi yana maganarsu, sunansa Ibrahim)) [al-Anbiya'i: 60]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya yi ishara zuwa ga kaifin hankali, da basirar Sayyiduna Sulaiman (AlaiHis Salam) a lokacin da yake matashi, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Sai kuwa muka ganar da Annabi Sulaiman game da al'amarin, dukansu, shi da Annabi Dawud mun ba su Annabta da ilimi..)) [al- Anbiya'i: 79]**, haka ma ga Annabin Allah Musa (AlaiHis Salam), a lokacin da yake ganiyar samartaka, da ƙarfi, gami da riƙon amanarsa, abin da har ya sanya 'yar mutumin kirkin nan ta yi magana akan haka, kaman yanda Alƙur'ani mai girma ya ba mu labari ta bakinta, a ayar da Allah mai girma yake cewa: **((Ɗaya daga cikinsu ta ce: Ya babana, ka yi jinga da shi, lallai shi ne zai zama mafi alhairin waɗanda ka yi jinga da su, ka ga dai ga ƙarfi, ga kuma riƙon amana)) [al-Ƙasasi: 26]**, Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa Sayyiduna Yahya

(AlaiHis Salam) magana ta ya riƙi amanar ilimi, ya kuma ɗauki wahalhalun isar da saƙo cikin ƙarfi, da himma ta samartaka, Allah mai girma yana cewa: **((Ya Annabi Yahya (AlaiHis Salam), ka riƙi wannan littafi da ƙarfi, mun riga mun ba shi Annabta tun yana ƙarami))** **[Maryam: 12]**.

Saboda muhimmancin wannan marhala ta rayuwa ce, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana cewa, lallai Allah Maɗaukakin Sarki zai tambayi bawa game da ita a ranar alƙiyama, ya yi haka ne, saboda ya yi himma ya amfana da ita, ya ribace ta wajen aikata abubuwan da za su amfane shi, su kuma amfani mutane, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ƙafafuwan bawa ba za su gushe ba a ranar alƙiyama, har sai an tambaye shi akan abubuwa guda huɗu: rayuwarsa, ta yaya ya ƙarar da ita? Da samartakarsa, ta yaya ya gudanar da ita? Da dukiyarsa, ta yaya ya tara, kuma ta yaya ya kashe? Da iliminsa, shin ya yi aiki da shi?)**.

Lallai addinin Musulunci ya muhimmanta matasa matuƙa, ya sanya masu wasu haƙƙoƙi, da wajibai, **suna da haƙƙin a ba su ilimi, a kuma sanya su akan hanya, a ba su kyakkyawan horaswa**, Alƙur'ani mai girma ya ba mu labarin abin da ya gudana tsakanin Luƙmanul Hakim da ɗansa, inda ya dasa ɓangarorin addini a zuciyarsa, ya kuma zaburar da shi wajen kawo gyara, da yawan baiwa, da yin ado da kyawawan ɗabi'u, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya RasulalLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka faɗa masu lokacin da Luƙman ya faɗa wa ɗansa, yana mai yi masa wa'azi cewa: ya kai ɗan ƙaramin ɗana, kada ka kuskura ka haɗa Allah da wani a wajen bauta, lallai haɗa Allah da wani a wajen bauta zalunci ne mai girma))** **[Luƙman: 13]**, mai girma da ɗaukaka yana

cewa: **((Ya kai ƙaramin ɗana, lallai kyakkyawan aiki, ko mummuna da mutum zai aikata -komin ƙanƙantarsa-, koda kaman ƙwayar zarra ce, ya kuma kasance a ɓoyayyen wuri, kaman cikin dutse, ko a sammai da ƙasa, to ka sani, Allah zai bayyanar da shi, ya kuma yi hisabi akansa, lallai Allah mai luɗufin da babu wani abu da zai iya ɓuya masa ne, masanin haƙiƙanin komai da komai. Ya kai ƙaramin ɗana, ka kiyaye sallah, ba kuma bayar da umurnin a aikata duk wani abu mai kyau, ka kuma hana aikata duk wani abu mai muni, ka kuma yi haƙuri da duk wani tsanani da zai same ka, lallai da ma abubuwan da Allah ya bayar umurni akansu suna cikin abubuwan da ya kamata a riƙe su da ƙarfi. Kada ka ɗaga wa mutane kai saboda girman kai, kada kuma ka yi taƙama a bayan ƙasa, lallai Allah ba ya son duk wani mai fankama da yake alfahari da kansa. Ka sanya tafiyarka a bayan ƙasa ta zamo tsaka- tsakin sauri da tafi laƙai- laƙai, ka kwantar da muryarka, saboda muryar da aka fi ƙi ita ce muryar jaki, farkonsa shaƙar iska ne, wannan kuma abin ƙi ne, ƙarshensa kuma fitar da iska ne, shi ma abu ne da ake matuƙar ƙinsa)) [Luƙman: 16 – 19].**

Haka ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake yi wa matasa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana matuƙar damuwa da su, yana kuma yin duk abin da ya kamata wajen ba su ilimi da horaswa, yana kuma dasa ƙa'idojin addini masu girma a cikin zukatansu, da hankulansu, da son ilimi, da yin nasara a cikinsa, an ruwaito Hadisi daga Abdullahi Ibn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: wata rana ina bayan Annabi (SallalLãhu alaiHi wa sallam), sai ya ce: **(Ya kai wannan ƙaramin yaro, zan sanar da kai wasu kalmomi: ka kiyaye**

**Allah, sai Allah ya kiyaye ka, ka kiyaye Allah, sai ka same shi a gabanka, idan za ka yi roƙo, ka roƙi Allah, idan za ka nemi taimako, ka nemi taimakon Allah, ka sani cewa, da a ce dukan al'umma za su haɗu a kan su amfane ka da wani abu, ba za su iya amfanarka da komai ba, sai abin da Allah ya rubuta maka, da a ce kuma za su haɗu a kan su cutar da kai da wani abu, ba za su iya cutar da kai da komai ba, sai da abin da Allah ya rubuta maka, an ɗage alƙaluma, takardu kuma sun bushe).**

Bayan an samar masu da nagartaccen ilimi, da horaswa mai kyau, sai **haƙƙin matasa na sanya su a madafun iko ya taso, kowa a wurin da ya fi dacewa, daidai ƙwarewarsa, da cancantarsa, a sanya su a muƙamai na aiki, da jagoranci, da iya ɗaukan mas'uliyya,** wannan ne abin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi, a inda ya yi amfani da ƙarfi, gami da kazar- kazar ɗin matasa, ya sanya su a cikin gwagwarmayar rayuwa; lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya aminta da matasan da ba su wuce shekaru ashirin ba a da'awarsa, alal misali: ga Sayyiduna al- Arƙam Bn Abul – Arƙam nan (Allah ya ƙara yarda da shi), wanda gidansa ya zamo wa Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), da sahabbai -masu girma- amintacciyar cibiya a farkon fara da'awar Musulunci, haka ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya naɗa Sayyiduna Usama Bn Zaid (Allah ya ƙara yarda da su) a matsayin kwamandan rundunar Musulmai, a lokacin bai wuce shekaru goma sha takwas a duniya ba.

Sayyiduna Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) **yakan gayyaci matasa zuwa majalisarsa, inda suke zama a tare da dattijai, yana kuma neman shawarwarinsu a cikin komai**, yakan ce: **"Kada ƙarancin shekarunku ya hana ku**

**bayar da shawara da faɗin ra'ayinku, saboda shi ilimi ba ruwansa da ƙarancin shekaru, ko yawansu, Allah yana bayar da shi ga wanda ya so ne"**, saboda haka ne majalisarsa take ƙunshe da matasa irinsu: Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su), wanda Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) yake magana akansa da cewa: **"Lallai yana da harshe mai yawan tambaya, da kuma zuciya mai aiki da hankali"**.

Abin bai taƙaita kawai ga matasa maza ba, **matasa mata ma suna da gudummuwa -da kowa ya shaida- wajen samar da cigaban Musulunci,** suna da rawar da suka taka a lokacin zaman lafiya, da ma lokacin yaƙi, irinsu: Sayyida Asma'u Bint Abubakar (Allah ya ƙara yarda da su), da irin gudummuwar da ta bayar wajen hijirar Annabi, ita ce take kai wa Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), da mahaifinta (Allah ya ƙara yarda da shi) abinci da abun sha a wannan hijira tasu mai albarka, hasali ma, mata suna da rawar da suka taka a lokaci mafi tsanani da wahala, a fagen daga, inda suke shayar da mayaƙa ruwa, suke kuma yi wa waɗanda suka jikkata magani, kaman yanda haka ya faru a ranar yaƙin Uhudu, Sayyiduna Anas (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: **"Da ido na, na ga A'isha Bint Abubakar, da Ummu Sulaimin suna ɗauke da tuluna a bayansu, suna shayar da mayaƙa, sannan su sake komawa su ciko, sannan su ɗauko su shayar da mayaƙa"**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa, da Sahabbansa baki ɗaya, da duk waɗanda suka bi shi da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai abubuwan da suka wajaba akan matasa suna da yawa, da farko dai: **Dole ne su katange kawunansu da ilimi, gami da wayewa, neman ilimin kuma ya zamo mai cigaba ba tare da tsayawa ba**, shi ilimi a koda yaushe ƙara cigaba da bunƙasa yake yi, dole ne matasanmu su tafi daidai da zamani, da kuma abubuwan da suke faruwa, su kuma kula matuƙa da abubuwan da za su ba su fifiko a komai, da kuma abubuwan da ƙasa take buƙata, za su yi haka ne ta hanyar yawaita shiga shirye –shirye, da kwasa - kwasai da za su sami ƙwarewar da ta kamata, ta yanda za su zamo a shirye suke su fuskanci kowane irin ƙalubale, lallai Allah Maɗaukakin Sarki bai buƙaci Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) da ya nemi ƙarin wani abu na duniya ba, banda ilimi, mai girma da ɗaukaka ya faɗa wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka ce: Ya Ubangiji ka ƙara mini ilimi))** **[Taha: 114]**.

Abu na biyu: **Himma wajen amfana da ƙwarewar wasu, da kuma nesantar ruɗi gami da girman kai,** lallai ya kamata matasa su amfana da hikimomi, gami da ƙwarewar waɗanda suka gabace su, cikin masana, kuma gogaggu a fagagensu, lallai dangantakar da take tsakanin tsofaffi, da masu tasowa, ba dangantaka ce ta nesantar juna, ko faɗa, da rikici, da raina juna

ba, a'a, dangantaka ce ta cika juna, da yi wa juna nasiha, dole ne matasanmu su nesanci ruɗi, da girman kan da yake rusa al'umma, ba gina ta ba, ruɗin da yake halaka mai shi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ka yi tafiyar taƙama a bayan ƙasa, domin har abada ba za ka taɓa iya huda ƙasa ba, ba kuma za ka taɓa iya kere duwatsu a tsawo ba)) [al- Isra'i: 37]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Abubuwa guda uku dalilai ne na halaka: tsananin ƙoron da mai shi yake yi mata biyayya, da son zuciyar da ake bi, da kuma jiji da kan da mutum yake yi da ra'ayinsa)**.

Na uku: **Sabonta niyya wajen hidimta wa addini da ƙasa,** shi ɗan Adam yana samun lada ne gwargwadon ikhlasinsa a cikin aiki, da kuma gaskiyar niyyarsa, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Shi aiki ba ya inganta sai da niyya, kuma kowane mutum zai sami abin da ya yi niyya ne...)**.

Na huɗu: **Amfani da dama ta hanyar ƙara ƙoƙari, da kuma fahimtar cewa hanyar fa tana da nisa, amanar kuma tana da nauyi**, wannan kuwa saboda kasancewar muna rayuwa ne a zamanin da yake gudu da sauri ƙwarai da gaske, waɗanda ba su da himma da ƙwazo a cikin ayyukansu, da wajen zartar da ayyukan da aka ɗaura masu, ba su da wuri a wannan duniyar, idan dai har muna son mu isa zuwa ga buƙatunmu, mu isa zuwa matakan da muke so wa kawunanmu, da ƙasashenmu, to dole ne mu yi iya abin da za mu iya wajen gabatar da ayyukanmu.

Na biyar: **Mu saka wa ƙasar da ta raine mu, ta kuma ba mu ilimi, ta kuma ba mu dukan damammaki;** lallai ƙasa tana da haƙƙi akan 'ya'yanta da suka rayu a turɓayarta, suka kuma sami horaswa daga gare ta, suke kuma da abubuwan tarihin da ba za

su taɓa mantawa da su ba daga gare ta, kamata ya yi guzurinmu a koda yaushe ya zamo shi ne naciya da jajircewa, makaminmu kuma ya zamo shi ne ilimi da ƙirƙirar sababbin abubuwa, takenmu kuma ya zamo shi ne kishin ƙasa, da yawan baiwa, mu yi duka wannan, saboda hidimta wa ƙasarmu, da ba ta kariya.

**Ya Allah Ubangiji, ina roƙon ka albarkaci matasanmu, ka kiyaye su daga dukan sharri, ka datar da su wajen ayyukan gina ƙasa, da cigabanta, ka shiryatar da su zuwa dmga gyara ƙasa, da 'yan ƙasa, ka kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya baki ɗaya.**

- 39 –

## HATSARIN YAƊA ƘARE- RAYI DA JITA – JITAA CIKIN AL'UMMA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, ku ji tsoron Allah, ku kuma yi daidaitacciyar magana, idan kuka yi haka sai Allah ya gyara maku ayyukanku, ya kuma gafarta maku zunubanku, ku sani duk wanda ya yi wa Allah da Manzonsa biyayya, to kuwa tabbas rabauta da babban rabo)) [al- Ahzab: 70 -71].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai faɗar da take tsakanin gaskiya da ƙarya daɗaɗɗiya ce, tun lokacin da aka samar da ɗan Adam a doron ƙasa, kuma haka al'amarin zai cigaba da kasancewa, har zuwa lokacin da Allah Maɗaukakin Sarki zai gaje ƙasa da abubuwan da suke cikinta, a cikin fitattun hanyoyin da masu yi wa ɓata rakiyar suke amfani da su, wajen yaƙar masu gaskiya, akwai: ƙirƙiro ƙarya, da yaɗa ta a tsakanin mutane.

Babu shakka kalma amana ce, kuma alhaki ne mai girma, shin wannan kalma karanta ta aka yi ta hanyar jaridu, da makamantansu, ko jinta aka yi ta hanyar rediyoyi, ko ma ganinta aka yi ta telebijin. Lallai ba wani abu ne jita- jita ba, face kalmar da ake yaɗa ta a tsakanin mutane, inda mai rauni da cuta a cikin zuciya yake fitar da ita, ko wata hukuma, ko ƙungiya cikin rundunonin sharri da suke gabatar da ayyukansu ta ƙarƙashin ƙasa, sai su sanya ta a harsunan mutane, su kuma su yi ta maimaita ta ba tare da sun bincika, sun tabbatar da ita ba, sai hakan ya yi tasiri mai muni a cikin hankulan mutane, a yi ta yaɗa munanan tunani da suke rusa al'umma, da gurɓatattun aƙidu, ta yanda al'umma za ta wayi gari, ta kuma yammanta cikin damuwa da shakku, kai har ma tsaro ya gushe, amincin da yake tsakanin mutane ya yi rauni, inda za ka ga al'ummar da a asalin take tamkar gangan jiki ɗaya, ta koma tana tsoron junanta, wasu na ƙasƙantar da wasu daga ciki; saboda haka ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai ƙarya ta kai ƙarya a ce mutum yana bayar da labarin duk abin da ya ji..)**, idan dai har yin magana akan dukan abubuwan da mutum ya ji nau'i ne cikin nau'o'in ƙarya, da ake yi wa mutum azaba mai tsanani akanta a ranar lahira, to yaya kuma muke zaton abin zai kasance ga wanda yake bayar da labarin abin da bai gani da idonsa, bai kuma ji da kunnuwansa ba?!.

Lallai addinin Musulunci ya ɗauki ƙwaƙƙwaran mataki akan jita – jita da masu yaɗata, inda ya sanya hakan a matsayin ɗabi'ar da ta yi hannun – riga da kyawawan ɗabi'u, da nagartattun tadodi da Shari'ar Musulunci ta zo da su, hakan ya faru ne lokacin da Musulunci ya umurci mabiyansa da su

kiyaye harsunansu daga yaɗa duk wani abu da zai haifar da fitina, ya kuma gadar da zaman ɗar- ɗar a tsakanin al'umma, ya kuma umurce su da yin gaskiya a cikin maganganunsu, da kiyaye harsunansu, da kuma yin bincike domin tabbatar da gaskiya, ko rashin gaskiyar abubuwan da suke zuwa kunnuwansu, saboda gudun kada su zamo dalilai na yaɗa fitina, da kawo ɓarna a cikin al'umma, da cin mutuncin mutane, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, ku ji tsoron Allah, ku kuma kasance tare da masu gaskiya a koda yaushe)) [at- Tauba: 119]**, haka ma Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ba ya furta wani lafazi face akwai mala'ika mai kiyayewa da yake a shirye koda yaushe domin rubuta maganarsa)) [Ƙaf: 18]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ka soma ka bi abin da ba ka da masaniya akansa, lallai za a tambaye ka akan ji, da gani, da zuciya baki ɗaya)) [al- Isra'i: 36]**, a Hadisin Sayyiduna Mu'az Bn Jabal (Allah ya ƙara yarda da shi), bayan Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana masa farillan Musulunci, da ƙofofin alhairi, sai ya ce masa: **(Shin ba na faɗa maka jigon al'amari da ginshiƙinsa da ƙololuwarsa ba?).** Na ce: faɗa mini ya Manzon Allah, ya ce: **(Jigon al'amari shi ne: Musulunci, ginshiƙinsa kuma: Sallah, ƙololuwarsa: jahadi)…** sannan ya ce: **(shin ba na faɗa maka abin da ya game duka ba?).** Na ce: faɗa mini ya Manzon Allah, sai ya kama harshensa, sai ya ce: **(ka kame wannan).** Na ce: ya Annabin Allah! Shin za a kama mu da abin da muka yi magana da shi? Ya ce: **(Zauna nan, shin akwai abin da yake kifa fuskokin mutane)** ko ya ce: **(karan hancin mutane a wuta ban da abubuwan da harsunansu suka girba?).**

Lallai yaɗa jita – jita ɗabi'a ce ta munafukai, da suke amfani da ita wajen biyan buƙatunsa na raunana tsaro, da kuma tarwatsa haɗin kan ƙasa, da kawo cikas a haɓakar tattalin arzikinta, da durƙusar da tsaro gami da kwanciyar hankalin al'umma, da yaɗa ruhin rashin nasara, da na ɗebe – ƙauna, da shu'umanci a cikin zukatan 'yan ƙasa, musamman matasa, lallai Alƙur'ani Mai girma ya kira masu wannan hali da suna: "masu yaɗa sharri"; saboda masu yaɗa sharri suna son su yaɗa munanan labarai ne, da na fitina da za su kawo tashin hankali a cikin al'umma, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Idan dai har munafukai, da waɗanda cuta ta ci zukatansu, da masu yaɗa sharri a cikin garin Madina ba su shiga taitayinsu ba, to kuwa za mu ba ka umurnin yaƙarsu, sannan kuma ba za su sake yin maƙwabtaka da kai a cikinta sai na ɗan ƙanƙanin lokaci))** **[al- Ahzab: 60]**.

Jita – jita ɗaya ne daga cikin salon yaƙe- yaƙe, da har Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) bai tsira daga gare shi ba, lallai mushrikai sun yaƙi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ta hanyar yaɗa jita- jita; domin su baƙanta kiransa, suka kuma ɓata masa suna, sun ƙirƙiri ƙaryar yaɗa cewa: wai (SallalLahu alaiHi wa sallam) matsafi ne, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Sai kafirai suka ce: wannan matsafi ne mai yawan ƙarya))** **[Sad: 4]**, haka ma saboda ƙarya suka yaɗa cewa shi mawaƙi ne, kuma mai taɓin hankali, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Suna kuma cewa: yanzu za mu bar allolinmu ne kawai saboda mawaƙi kuma mai taɓin hankali?!))** **[as- Safat: 36]**, a wasu lokuta kuma suka yaɗa cewa boka ne shi, sai Allah Maɗaukakin Sarki ya mayar masu da martani akan waɗannan ƙare- rayi nasu, yana cewa: **((Lallai tabbas Alƙur'ãni daga Allah ne zuwa ga**

**harshen Manzo mai babban matsayi. Alƙur'ãni ba maganar mawaƙi ba ne, kamar yadda kuke riyawa, kaɗan ne ƙwarai ake samun imanin cewa Alƙur'ãni daga Allah ne a cikin zukatanku. Kuma Alƙur'ãni ba surkullen bokaye ba ne, kamar yadda kuka sani, kaɗan ne ƙwarai waɗanda suke da tunani da lura da za su bambance tsakaninsu a cikinku. Shi kam saukakke ne daga wanda yake samar wa halittu da rayuwa gami da raino)) [al- Haƙat: 40 – 43].**

A ranar yaƙin Uhdu ma mushrikai yaɗa jita – jitar cewa an kashe Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) suka yi, saboda suna son su rarraba kan Musulmai, su raunana ƙarfinsu, sai kuwa sahun Musulmai ya girgiza, zukatansu suka yi sanyi, wasu daga cikinsu suka gudu, wasu kuma suka ajiye makamansu, wasu kuma suka tsaya suka tabbata tare da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam).

A ranar yaƙin "Hamra'ul Asad" ma haka mushrikai suka yaɗa jita – jitar cewa Ƙuraishawa sun tanadi wani babban runduna; domin auka wa garin Madina, da yaƙar Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da sahabbansa, amma dai wannan jita – jita ba ta sanya Musulmai sun yi ko- gezau ba, suka tabbata akan addininsu, sai kuwa Allah Maɗaukakin Sarki ya yabe su da cewa: ((**Su ne waɗanda wasu mutane suka tsoratar da su a lokacin da suka ce masu: lallai abokan gabanku sun tanadar maku da wata babban runduna, saboda haka, ku kiyaye su, hakan bai sanya sun yi rauni ba, bai kuma sanya su karaya ba, maimakon haka ma imaninsu da Allah ne ya ƙaru, suka kuma sakankance da nasararsa, sai suka amsa masu da cewa: Allah ya ishe mu, shi ne majiɓincin al'amurran mu, shi kam madalla da wanda ake miƙa masa**

**dukan al'amurra. Sannan suka fita zuwa jahadi domin su gamu da wannan runduna mai girma, sai dai fa mushrikai sun tsorata da wannan gamuwar, sai muminai suka koma gida cike da nasarar samun ni'imar zaman lafiya, suna kuma kwaɗayin yin jahadi, da kuma babban rabo da suka samu na ladan sa, da kuma falalar sa da ya yi masu na jefa razani cikin zukatan abokan gaba, ta yanda babu ko ƙwarzane da ya same su, suka nemi yardar Allah, sai suka zamo sun cancanci ya ba su falalar sa, lallai Allah mai babban falala ne))** **[Ali Imran: 173 – 174]**.

A ranar yaƙin Hunain ma haka aka yaɗa cewa an kashe Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai kuwa Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya tsaya da kansa, ya ƙalubalanci wannan jita- jitar, yana maimaita cewa: **(Ni ne Annabi babu ƙarya, Ni ne ɗan Abdulmuɗallabi)**.

Lallai maimaita jita – jita, da yaɗa ta suna da hatsari mai girma da duk wani mai hankali ba zai rasa sanin haka ba, suna halatta jinanai, da dukiyoyi, da mutunci, suna kuma yin sanadiyyar sanya rayuwar mutane cikin garari, kashe Khalifa Sayyiduna Usman Bn Affan (Allah ya ƙara yarda da shi) babban dalili ne akan haka, miyagu sun yi masa ƙawanya ne sakamakon jita – jita, da ƙare- rayin da Bayahuden nan Abdullahi Bn Saba' ya ƙirƙira, kai har ma suka hana shi ruwan da zai sha, duk kuwa da cewa shi ne ya sayi rijiyar Rumata da kuɗin aljihunsa, an ruwaito daga Na'ilat –matar Sayyiduna Usman (Allah ya ƙara yarda da shi)- ta ce: Ranar da aka kashe Usman a cikinsa, yana azumi a ranar da kafin wannan ranar, lokacin buɗa – bakinsa, ya nemi su ba shi ruwa ya sha, ba su ba shi ba, sai ya yi barci ba tare da ya yi buɗa – baki ba, lokacin

sahur sai na tafi wurin wasu maƙwabtanmu, na tambaye su ruwan sha, sai suka ba ni tulu ɗaya, sai na kawo masa, na ɗan girgiza shi ya farka, sai na ce masa: ga ruwan sha, sai ya ɗaga kansa, sai ya ga alfijir ya keto, sai ya ce: yau ma na wayi gari da azumi, lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zo mini ta wannan rufin da ruwan sha, sai ya ce mini: **(Ya Usman, sha)**, sai na sha har ya ishe ni, sannan ya ce: **(Ƙara)**, sai na sha har na ji ya ishe ni, sannan ya ce: **(Su waɗannan mutane za su yi yawaita akanka, idan ka yaƙe su za ka yi nasara akansu, idan kuma ka ƙyale su za ka yi buɗa – baki a wurinmu, a ranar kuwa suka shiga inda yake suka kashe shi)**.

Lallai abubuwa masu yawa sun sauya a wannan zamanin namu, wannan ƙazamiyar sana'a ta yaɗa jita – jita, ta ɗauki sababbin salo iri – iri, da surori mabambanta, musamman ganin irin yanda aka sami cigaba mai girma, kuma mai sauri game da hanyoyin sadarwa na zamani, da na ilimin kimiyya da fasaha, abin da ya sanya jita – jita tafi yaɗuwa, da kuma saurin isa zuwa ga mutane, ta kuma fi yin mummunan tasiri, hasali ma ta zamo hanya ce mai zaman kanta, cikin hanyoyin yaƙe –yaƙe, yanzu yaƙi bai tsaya a fuska ɗaya ba, ba taƙaita kawai akan amfani da soji kawai, ko jami'an tsaro kawai ba, kai bai ma taƙaita kawai akan bayanan leƙen – asiri, da tsohuwar ma'anar da aka sani na tsare – tsaren leƙen asiri ba, lallai an sami cigaba game da hanyoyin yaƙe- yaƙe, inda ake amfani da makamin jita – jita, da ƙirƙirar ƙarai-rayi, abin da ya zamo wani abu ne na musamman da ake karantarsa, a kuma nazarce shi, a kuma horas da mutane akansa, inda wasu ƙungiyoyi da akwai alamun tambaya game da su, suka ƙware wajen bayar da horaswa akan haka, suke kuma ɗaukan ma'aikata a shafukan

sadar da zumunta, tare da amfanin da iya abin da za su iya na matsin lamba, da ƙawanya na siyasa, da na tattalin arziki, da ma na azabtar da zukata, da naciya wajen ƙoƙarin baƙanta shugabanni a wurin al'umma, da cuna su akansu, da ƙasƙantar da jigogin da abubuwan da ƙasa ta yi nasarar samar da su, da sanya shakku akan nasarori, da rashin ƙimanta su, da harhaɗuwar ƙungiyoyi, da gungun 'yan ta'adda, da yunƙurin kutsawa cikin cibiyoyi da ma'aikatun gwamnati, da tayar da ɗabi'un da suke kai wa zuwa ga rarrabuwar kawuna, duka ƙarƙashin nazari da bincike na ban mamaki, da kuma ba su ayyukan a kafafen sadarwa na zamani, da kuma yin amfani da buƙatun mutane da ba za su iya haƙurin juriya game da su ba, da yunƙurin murguɗa manufofin al'umma, da aikin wajen durƙusar da kwarjinin shugabanni, da sanya shakku akan malamai, da jagororin al'umma masu kishin ƙasa a fagagen tunani, da na al'adu, da ƙarfafa masu adawa da su, da kuma isar da saƙwannin tsoratarwa a sarari, ko a ɓoye ga waɗanda suka yi riƙo da manhajinsu wajen kishin ƙasa, ta hanyar bayyana makomar duk wanda bai yi masu biyayya ya shiga cikin masu zartar da wannan ƙazamin tsari, ya kuma miƙa da ragamarsa a hannunsu ba.

Babu shakka jajircewa, da juriya wajen ƙalubalantar wannan goguwar abu ne da yake matuƙar buƙatar aƙida, da imani, gami da kishin ƙasa na gaskiya, da kuma tsantsar imani da Allah da ba shi da iyaka, saboda mutane da yawa ba sa damuwa idan sun yaɗa wasu labarai, da ƙididdiga, ko ƙissoshi ba tare da sun tabbatar da gaskiyarsu, ko sanin ina ne asalinsu ba, da haka sai su zamo sun taka - rawa wajen yaɗa fitina, da kunna wutarta,

lallai yaɗa kalmomin ƙarya da ba su da wani tushe na gaskiya, ko rubuta su, su isa ko'ina a faɗin duniya za su iya zama dalilai na yi wa bawa azaba a ranar alƙiyama, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai bawa zai iya furta kalmar neman yardar Allah da ma bai mayar da hankali zuwa gare ta, hakan kuma ya zama dalilin samun ɗaukakar darajarsa a wurin Allah, haka ma bawa zai iya furta kalmar da za ta jawo fushin Allah, ba kuma tare da ma ya mayar da hankali zuwa gare ta ba, hakan kuma ya zamo sanadiyyar aukawarsa cikin jahannama...)**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

---------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da salami shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai addinin Musulunci ya sanya manhaji mai cike da hikima da zai bai wa al'umma kariya daga cututtukan jita - jita, muhimman alamun wannan manhaji sun haɗa da:

* **Wajibcin tabbatarwa da gaskiyar labarai,** da yin taka tsantsan kafin yaɗa su a cikin al'umma, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, idan wani fãsiƙi ya ƙetare shari'ar Allah ya zo maku da kowane irin labari, to ku bincika ku tabbatar da gaskiyarsa; saboda kada ku cutar**

**da wasu mutane –da ba ku san haƙiƙaninsu ba-, hakan sai ya sanya ku yi nadama akan abin da kuka aikata, kuna: ina ma ba mu aikata hakan ba, a lokacin da bayani ya bayyana cewa ba su da wani laifi))** **[al- Hujrat: 6]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Taka tsantsan yana zuwa ne daga Allah, gaggawa kuwa tana zuwa ne daga shaiɗan)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Taka tsantsan a cikin komai in banda aikin lahira)**.

* **Rashin yaɗa jita - jita** ta kowace hanya da za a karanta, ko a saurara, ko a gani; domin yaɗa ta bayar da gudummuwa ne wajen yaɗa ta, lallai jita - jita tana ƙara yaɗuwa ne idan ta sami harsunan da za su yi ta maimaitawa, da kunnuwan da za su saurare ta, da kuma zukatan da za su amshe ta su kuma gasgata ta, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lokacin da kuke furta ta da hasunanku, kuma da bakunanku kuke faɗin abubuwan da ba ku da masaniya akansu, kuna zaton hakan abu ne ƙarami, alhali babban abu ne a wurin Allah))** **[an- Nur: 15]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to kada ya cutar da maƙwabcinsa, wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya girmama baƙonsa, wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya faɗi alhairi, ko kuma ya yi shiru)**..

* **Wajibcin haɗin kai tsakanin 'yan ƙasa, da kuma gabatar da kyautata zato a duk sanda aka ji jita - jita akansu, da rashin saurin tuhumarsu**, Allah mai girma yana cewa: **((Ina ma a ce a lokacin da kuka ji ta, muminai maza da mata sun yi wa kawunansu zato na alhairi, suka ce: wannan kam ƙarya ce a bayyane..))** **[an- Nur: 12]**, lallai an bai wa Musulmi umurnin ya kyautata zato, ya ɗauki duk wani abu da wani zai yi ta fuskar

kyautata zato; saboda mummunan zato cuta ce mai hatsari da take fata - fata da rayuwa, ta hanyar sanya rashin tabbas, da yaɗa husuma a tsakanin mutane, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi gargaɗi game da haka, a inda yake cewa: **(Ahir ɗinku da zato, domin lallai zato shi ne zancen da ya fi kowane zance zamowa ƙarya, kada ku binciki sirrin mutane domin amfanin kawunanku, kada kuma ku binciki sirrin mutane domin amfanin waninku, kada ku yi hassada, kada ku juya wa juna baya, kada ku ƙi juna, ku zamo bayin Allah 'yan uwan juna)**.

* **Neman taimakon ƙwararru wajen bayyana gaskiya, da rashin yin gaggawa wajen zartar da hukunci akan al'amurra,** Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗi a lokacin da yake sifanta munafukai cewa: ((**Idan waɗannan munafukai suka ga wani abu na tsaro, ko na tsoro da yake da jiɓi da ƙarfin Musulmai, ko raunin su, sai su yayata shi da nufin ruɗar da Musulmai, ko jefa tsoro da razani a cikin zukatan su, ko saboda su isar da labarin su zuwa ga maƙiyan su, da a ce waɗannan munafukai sun mayar da duk wani al'amari na tsaro da tsoro zuwa ga Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) da shugabanni da manyan saahabbai da dakarun yaƙi, su kuma nemi sanin haƙiƙanin al'amari ta wurin su, da waɗannan da suke ƙoƙarin neman labarai da yaɗa su sun san gaskiya a wurin Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) da shugabanni. Lallai ba domin falalar da Allah ya yi maku na tabbatar da zukatanku akan imani, da daƙile fitina, da kuma rahamarsa na damƙa maku dukan dalilan da za su sanya ku sami nasara ba, da mafi yawanku sun faɗa cikin tarkon shaiɗan, babu waɗanda za su tsira daga halakarwarsa sai**

**mutane kaɗan daga cikin ku))** **[an- Nisa'i: 83]**, ma'ana : a koda yaushe suna jirace ne da tsaro, gami da kwanciyar hankalin al'umma, a duk sanda suka ji wani labari da yake da jiɓi da tsaron Musulmai, ko wani abu da suke tsoro sai su yaɗa shi, su bayyana shi da nufin shigar da tsoro, da razani, gami da damuwa a cikin zukata.

Saboda haka, dole ne kowane Mumini mai kishin addininsa da ƙasarsa ya farka, ya yaƙi waɗannan jita – jitar, ya ƙaryata su, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda ya kare mutuncin ɗan uwansa, to kuwa Allah zai kare fuskarsa daga wuta a ranar alƙiyama)**, dole ne mu sani cewa ita kalma amana ce da za a tambayi bawa akanta a gaban Allah Maɗaukakin Sarki a ranar alƙiyama.

Dole ne mu fahimci cewa maƙiyanmu suna amfani da duk wani cigaba wajen yaƙin yaɗa jita – jita, da ɓata nasarori, da jagororin ƙasa masu kishi, da ƙoƙarin cin mutuncin duk wani ɗan ƙasa na gari, suna yin haka ne, domin su rusa daularmu, su sanya ta rusuna, ko ma su tarwatsa ta; domin biyan buƙatun kawunansu, dole ne mu san cewa yanzu haka muna yanayi ne na ƙazamin yaƙi da maƙiya suke kitsa mana shi, jita – jita ne kuma makamashin wannan yaƙin, saboda haka, dole ne mu riƙa ƙoƙarin tabbatar da gaskiyar labarai, gudun kada mu auka ramukan da maƙiyanmu suka haƙa mana, dole ne mu yarda da kawunanmu, mu yarda da shugabanninmu, da sojojinmu da 'yan sandanmu, kada mu kuskura mu miƙa kunnuwanmu ga maƙiya ƙasarmu, da waɗanda suke aiki ba dare ba rana wajen aibata mu, ko kashe mana gwiwa, ko masu son su ganmu a ƙasa, ta hanyar yaɗa ruhin ɗebe ƙauna a cikinmu, lallai wannan

yana nufin mu katange matasanmu, da al'ummarmu da cikakkiyar wayewa ta zamani, su kuma san ƙalubalen da suke fuskantarmu, ta yanda za su bayar da nasu gudummuwar wajen ƙalubalantarsu.

**Ya Allah Ubangiji, ka kyautata ɗabi'unmu, ka kiyaye mana ƙasashenmu, ka kuma datar da mu zuwa ga abubuwan da kake so, ka kuma yarda da su, ka kiyaye ƙasashenmu daga dukan sharri.**

- 40 –

## HATSARIN DA YAKE TATTARE DA SHAYE- SHAYE DA TASIRIN TA'AMULI DA ƘWAYOYI AKAN ƊAN ADAM DA AL'UMMA GABA ƊAYA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin buwayayyen littafinsa mai girma yake cewa: **((Kada ku jefa kawunanku a cikin halaka, ku kyautata domin lallai Allah yana son masu kyautatawa)) [al- Baƙra: 195]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai da hankali ne Allah Maɗaukakin Sarki ya bambance ɗan Adam da sauran halittunsa, wanda saboda hankali ne ake ɗaura wa bawa taklifi, kuma shi ne harsashen tunani, da lura, da tadabburi, lallai Allah mai girma da ɗaukaka ya zargi mutanen da suka wofintar da wannan ni'imar, ba tare da sun ba ta haƙƙinta kamar yanda ya kamata ba, Allah yana cewa: **((Shin ba za su yi aiki da hankali ba ne?)) [Yasin: 68]**, a wani wurin kuma yana cewa: **((Shin ba za ku yi tunani ba ne)) [al-An'am: 50]**, a wani wurin kuma Allah Maɗaukakin Sarki yana

cewa: **((Babu masu hankalta da ita sai masana)) [al- Ankabut: 43],** ya kuma faɗi a wani wurin cewa: **((Lallai mun bayyana maku ayoyinmu ko za ku hankalta)) [al- Hadid: 17],** a wani wurin kuma yana cewa: **((Lallai a cikin wannan abu akwai ayoyi ga masu hankali)) [Taha: 54, 128],** Allah ya ƙara haskaka kabarin Imam al Hassanul Basriy, an ruwaito yana cewa: Da a ce ana sayar da hankali, da mutane sun sanya kuɗinsa da tsada, saboda haka nake mamakin mutumin da yake sanya kuɗi ya sayi abin da zai ɓata shi.

Saboda babban matsayin da addinin Musulunci ya bai wa hankali da tunani ne, Shari'ar Musulunci ta katange hankali da wasu abubuwa da za su ba shi kariya, sai aka haramta duk wani abu da zau cutar da hankali, ko kuma ya yi masa ritaya daga aiki, ya hana shi yin tunani, ko riskar abubuwa a yanda suke a haƙiƙaninsu, Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, shi fa shan kayan maye, da wasannin caca, da karkafa wasu duwatsu domin yanka dabbobi saboda bautan gumaka da kuke yi, da ɗaukan kibau, da duwatsu, ko ganyayyaki domin sanin abubuwan da suke gaibi ne.. duka waɗannan abubuwa ne masu muni matuƙa da zukata suke ƙullewa, abubuwa ne kawai da shaiɗan yake ƙawata wa mai aikata su, saboda haka ku bari domin ku sami kyakkyawar rayuwa a gidan duniya, a lahira kuma ku rabauta da ni'imar aljanna)) [al- Ma'ida: 90].** Idan Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) zai yi wa sahabbansa masu daraja (Allah ya ƙara yarda da su) mubaya'a yakan ce masu: **(Ina yi maku mubaya'a ne akan kada ku kuskura ku haɗa da wani a wajen bauta, kada kuma ku kashe ran da Allah ya haramta ba tare da haƙƙi ba, kada kuma ku yi**

**zina, kada ku yi sata, kada kuma ku sha kowane abu mai sanya maye)**, anan Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa ya yi: **(kada kuma ku sha kowane abu mai sanya maye),** lallai wannan sigar ta game dukan wani abu mai sanya maye, koda kuwa da wani suna ake kiransa, saboda haka duk wani abu da yake gusar da hankali, shin shansa ake yi, ko shaƙa, ko kuma ana shigar da shi ta hanyar allura, to kuwa hukuncinsa daidai yake da hukuncin giya.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya wata tabbatacciyar ƙa'ida da ba ta sauya da sauyin zamani, ko sauyin wuri, ko sauyin yanayi, ko kuma sauyin mutane, wannan ƙa'ida ta bayyana sifar da giya take da shi, kai, da ma duk wani abu mai sanya maye, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wani abu mai sanya maye giya ne, kuma duk wani abu mai sanya maye haramun ne, kuma duk wanda ya sha giya a duniya, bai kuma tuba ga barinta ba, to kuwa ba zai taɓa shan ta lahira ba).**

Da haka ne za mu san cewa lallai giya suna ne da ya game duk wani abu da yake sanya maye, koda kuwa da wani irin suna ake kiransa, shin ruwa- ruwa yake, ko kuwa busasshe, muddin dai ma'anar haramci wanda shi ne maye ya tabbata a tare da shi, mai tsira da aminci yana cewa: **(Abin da mai yawansa ya sanya maye, to har kaɗan ɗinsa ma ya haramta),** a wani wurin kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Da sannu wasu mutane a cikin al'umma ta za su sha giya, amma suna kiranta ba da sunanta ba).**

Saboda tsananta azaba ga duk wanda ya kusanci giya a matsayin mai shanta, ko mai sayar da ita, ko mai sana'anta ta ne Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Allah**

**ya la'anci giya, da mai shan giya, da mai sayar da ita, da mai siyanta, da mai tatse ta, wa wanda aka tatse ma wa, da mai dakonta, da wanda aka yi masa dakon),** a wani wurin kuma yana cewa: **(Duk wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, to kada ya zauna a teburin da ake shan giya akansa).**

Lallai addinin Musulunci ya haramta shan duk wani abu mai sanya maye ne; saboda ya bai wa ɗan Adam kariya a karan kansa, ya kuma bai wa al'umma kariya; domin cuta da halakar da suke auka wa mai shaye- shaye sukan yi mummunan tasiri a rayuwar zamantakewar al'umma, giya tana gusar da hankali, tana kuma tafiyar da kwarjini da mutunci, tana kuma yin ɗai-ɗai da rayuwa, Lallai Sayyiduna Abubakar as-Siddiƙ (Allah ya ƙara yarda da shi) ya haramta wa kansa shan giya, bai taɓa sha ba, koda a zamanin jahiliyya, dalilinsa kuwa shi ne: wata rana ya zo wucewa sai ya ga wani mashayi yana sanya hannunsa a cikin bayan- gida yana kai bakinsa, idan warin ya nushe shi, sai ya kawar da hannunsa, daga nan sai Sayyiduna Abubakar ya ce: "Lallai wannan mutumin bai san abin da yake yi ba", sai kuwa Sayyiduna Abubakar ya sha alwashin haramta wa kansa shan giya.

Bayani ya zo a cikin ruwaya cewa: an tambaye shi (Allah ya ƙara yarda da shi) a bainar sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa: shin ka taɓa shan giya a zamanin jahiliyya? Sai ya ce: Allah ya yi mini tsari, sai aka ce: saboda mene? Sai ya ce: Ina kiyaye mutunci da natsuwa na ne; domin duk wanda ya sha giya, to kuwa ya tozarta mutuncinsa da natsuwarsa, sai wannan labarin ya isa zuwa wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce: **(Abubakar ya faɗi gaskiya, Abubakar ya faɗi gaskiya).**

Babu shakka, abubuwan da ake gani a ƙasa suna tabbatar da cewa, lallai shan kayan maye suna yin sanadiyyar rushewar gida da tozartarsa, suna kuma zamowa silar da za su tunkuɗa iyalai zuwa ga aikata miyagun laifuffuka, suna kuma kawar da kyawawan ɗabi'u da mutuntaka a tare da mai shansu, kuma hakan ne yake kai wa zuwa ga samun munanan ɗabi'u a cikin al'umma, irinsu: neman mata, da yawaita sake – sake tsakanin ma'aurata, da rusa gidaje da dangogi, sannan kuma hakan ya haifar da yaɗuwar laifuffuka mabambanta, irinsu: sace- sace, da kisan kai, da fyaɗe; saboda shi mashayi ba ya tunanin abubuwan da aikinsa zai iya haifarwa, ba ya kallon ƙarshe, ko sakamakon abin da yake aikatawa, babu abin da ya dame shi sai dai kawai ya sami kayan maye ta kowace irin hanya.

Yaƙe- yaƙe nawa ne shan ƙwayoyi suka yi sanadin aukuwarsu? Mawadata nawa ne ƙwaya ta yi sanadin talaucinsu? Masu lafiya nawa ne ta jefa lafiyarsu cikin garari? Masu girma da daraja nawa ne ƙwayoyi suka wulaƙanta su? Shugabanni nawa ne ta ƙasƙantar da su? Sau nawa ƙwaya ta yi sanadiyyar rabuwar miji da mata? Sau nawa ta gadar wa masu shanta da nadama da cizon- yatsa? Bala'o'i da masifu nawa ne ta jawo wa masu shanta? Lallai ita ce asali ɗaukacin zunubai, kuma mabuɗin dukan sharri, kaman yanda ya zo a wasiyyar da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi wa Sayyiduna Abuddarda'i (Allah ya ƙara yarda da shi), a inda yake cewa: **(Kada ka soma ka sha giya; saboda lallai ita ce mabuɗin dukan sharri),** an ruwaito daga Sayyiduna Usman Bn Affan (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: **"Ku nesanci giya; domin lallai ita ce ummul haba'isi".**

Lallai yawan shaye – shaye babban dalili ne na gurɓacewar tarbiyya, da taɓarɓarewar ilimi, da ɗabi'u, da kuma durƙusar da rayuwar zamantakewa da tattalin arziki, bugu da ƙari, kuma su ne dalilan faruwar cututtuka da jiki, da ma na taɓin hankali, irin su: damuwa, da ɓacin- rai, da rashin kwanciyar hankali, da rashin natsuwa, da taɓuwar ƙwaƙwalwa, da yawan mantuwa, da nesantar mutane, da karayar gwiwa, da rashin jin daidai, da sauransu cikin cututtukan da suke da jiɓi da hauka, waɗanda faruwarsu zai wajabta mana jajircewa wajen ƙalubalantar wannan hatsari da yake fata- fata da al'umma, lallai dulmiyar da matasa a cikin hanyar shaye – shaye, yana nufin dulmiyar da ƙasa ce gaba ɗayanta, shigar da rauni ne a cikin ɓangarorin da take da ƙarfi, kuma rusa nagartattun ɗabi'u da kyawawan al'adu ne.

Babban abin da zai sanya mu gane irin girman hatsarin shaye – shaye shi ne : idan muka kalli wanda ya faɗa tarkon shaye – shaye, ya kuma ɗanɗani gubar da ke cikinsa –cikin ƙanƙanin lokaci yake sauya wa daga cikakken ɗan Adam zuwa wata halitta mai tsananin hatsari, zai iya yin sata, zai iya yin kisa, zai iya sayar da addininsa akan hanyarsa ta neman abin da zai natsar masa da jijiyoyinsa, a wani yanayi mai kama da hauka, wannan kawai ya isa ya sanya a tashi tsaye; domin a ba mashayi kariya daga sharrin kansa, a kuma bai wa iyalansa da al'umma gaba ɗaya kariya daga sharrinsa.

Lallai akwai matuƙar buƙatar kowanne daga cikinmu, ya sauke nauyin da yake akansa, wajen kula da matasanmu da 'ya'yanmu, kowa a matsayin da yake a kai, fara tun daga gida, da irin rawar da gida yake takawa wajen tarbiyya, zuwa ƙananan makatantu, da jami'o'i, da wuraren karantarwa, da ma

hukumomi na addini, da kafafen yaɗa labarai mababanta, gudun kada mu sallama 'ya'yanmu a hannun shaye –shaye.. Lallai hatsari kam ya riga tunkaro mu, kuma ƙwaƙwalen 'ya'yanmu, da lafiyar jikkunansu, da na zukatansu, da abin da suka mallaka na dukiyoyi yake son ya lalata, ya kuma yi ɗai-ɗai da su, Saboda haka, ku zo mu haɗa ƙarfi da ƙarfe, mu raini nagartacciyar al'umma da take da kyawawan ɗabi'u, take kuma da ikon cigaba da al'ummanta, suke kuma iya riskar haƙiƙanin hatsarurrukan da suke kewaye da ƙasarsu.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------------

Gadiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawansa da Manzanninsa, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam), da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** A daidai wannan lokaci da aka fara bikin makon daidaita amfani da ruwa, a wannan shekara da muke ciki, muna ƙara tunatar da kawunanmu muhimmancin ni'imar ruwa da Allah ya yi mana, lallai ruwa na cikin manyan ni'imomin Allah Maɗaukakin Sarki, lallai ruwa shi ne asali rayuwa, kuma asalin kowane rayayye, kuma shi ne mafi girman hanyoyin haɓaka tattalin arziki, da bunƙasar albarkatu, Allah Mai girma yana cewa: **((Daga ruwa ne muka samar da rayuwa a cikin komai)) [al- Anbiya'i: 30],** a wani wuri kuma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Za ka ga ƙasa a bushe ƙandas, amma da zaran mun saukar da ruwa, sai rayuwa ta kukkutsa cikinta ta ko'ina, sai ta ƙaru, ta yi tudu; sakamakon ruwa da**

**iska da suka shige ta, sai ta fitar da tsirrai iri- iri masu burge masu gani, inda kyawonsu yake jan hankali, ya kuma sanya farin ciki))** [al- Hajji: 5].

Lallai addinin Musulunci ya muhimmanta girman ni’imar da ruwa yake da shi, ya kuma bayar da umurni a kyautata ta’amuli da shi, ya kuma kwaɗaitar da yin daidaito wajen amfani da shi, ya kuma sanya yin ɓarna da ruwa a matsayin wani nau’i ne cikin nau’o’in zalunci, da wuce-gona - da - iri a cikin abin da yake haƙƙi ne na wasu, wani daga cikin Sahabbai ya zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), domin ya koyi yanda ake alwalla daga gare shi, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya koya masa yanda ake alwalla, ana wanke gaɓoɓi sau uku – uku, sannan ya ce: **(Wannan shi ne alwalla, duk wanda ya yi ƙari akan haka, to kuwa ya munana, ko ya wuce - gona - da - iri, ko ya yi zalunci).**

Lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya wuce ta kusa da Sayyiduna Sa’ad Bn Abuwaƙƙas (Allah ya ƙara yarda da shi) yana alwalla, sai ya ce: **(Wane irin ɓarna ce haka ya Sa’ad?),** sai ya ce: Shin a alwalla ma akwai ɓarna ne, ya Manzon Allah? Sai ya ce: **(Ƙwarai kuwa, koda kuwa kana bakin kogi mai gudana ne).**

Lallai addinin Musulunci yana kallon ruwa a matsayin arziki ne na al’umma, da mutuntaka, kowa yana da haƙƙi a cikinsa, kada a haramta wa kowa amfana da shi, saboda haka ne ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mutane suna tarayya a cikin abubuwa guda uku: ruwa, da wurin kiwo, da wuta).**

Saboda muhimmancin da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake bai wa ruwa ne yake cewa: **(Duk wanda ya haƙa**

**rijiya, to kuwa babu wata halitta da take da hanta: wato mutum, ko aljani, ko tsuntsu da zai sha ruwan ciki face Allah ya ba shi ladan hakan a ranar alƙiyama),** Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Akwai abubuwa guda bakwai da ladansu suke bin bawa, har bayan rasuwarsa yana cikin kabarinsa: wanda ya karantar da ilimi, ko ya jawo teku, ko ya haƙa rijiya, ko ya dasa dabino, ko ya gina Masallaci, ko ya gadar da Alƙur'ani, ko ya bar yaron da zai nema masa gafara bayan rasuwarsa).**

A ƙarshe: Lallai muna ƙara tabbatar da cewa gurɓata ruwa, ko yin ɓarna da shi, ko rashin kiyaye shi, nau'i ne daga cikin nau'o'in ɓarnar da Allah Maɗaukakin Sarki ya hana, a inda yake cewa: **((Kada ku yi ɓarna a bayan ƙasa bayan an gyara ta…)) [al- A'araf: 56, 85],** kowane ɗigo na ruwa daidai yake da rayuwa, kaman yanda yake a matsayin dukiya mai zaman kansa, rasa ruwa, ko yin ɓarna da shi, yana nufin salwantar da arzikin al'umma, wanda wajibi ne a kiyaye shi; saboda haka dole ne gaba ɗayanmu, mu gode wa Allah akan wannan ni'imar ta hanya kiyaye ta, domin godiya akan ni'ima sanadi ne na dawwamar ni'imar da kuma ƙaruwarta, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku tuna lokacin da Ubangijinku ya yi shelan cewa: lallai idan kuka gode, to kuwa tabbas zan ƙara maku)) [Ibrahim: 7].**

**Ya Ubangiji ka kare mana ƙasashenmu da al'ummanmu da matasanmu, da sojojinmu da 'yan sandanmu, da dukan arzikin da ka yi mana, ka kiyaye mu daga barin dukan sharri da abubuwan ƙi, amin.**

- 41 –

## ALAMUN GIRMAN KAI DA TOSHE HANYAR ALLAH

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Da sannu zan juyar da hankulan waɗanda suke girman kai a bayan ƙasa -ba tare da dalili ba- ga barin ayoyi na, idan ma za su ga dukan ayoyi ba za su yi imani da su ba, idan kuma suka ga hanyar shiriya ba za su ɗauke ta a matsayin hanyar bi ba, idan kuma suka ga hanyar halaka sai su ɗauke ta a matsayin hanyar bi, hakan ya faru ne sakamakon sun ƙaryata ayoyinmu, da ma can sun rafkana ga barinsu)) [al- A'araf: 146].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya, shi ne cikakken mabuwayi, mai hikima. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai sakamakon masu girman kai yana da matuƙar muni tun a duniya kafin lahira, shin ɗaiɗaikun mutane ne su, ko kuwa gungun al'ummomi, lallai halakar da al'ummomi da garuruwan da suka yafa rigar girman kai sunna ce cikin sunnonin Allah Maɗaukakin Sarki a cikin halittar, ba kuma za ka taɓa samun sauyi, ko jirkita a cikin sunnar Allah ba, Allah

Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Su kuwa Adawa sai suka yi girman kai a bayan ƙasa, ba tare da dalili ba, suka ce: wane ne ya fi mu ƙarfi? Shin ashe ba su yi tunanin cewa Allah da ya halicce su shi ne ya fi su ƙarfi ba? Su dai kawai suna musanta ayoyinmu ne. Sai kuwa muka aika masu da iska mai ƙarfi a cikin kwanakin nahisai saboda mu ɗanɗana masu azabar ƙasƙanci a rayuwar duniya, lallai wallahi azabar lahira ta fi wannan azaba ta duniya ƙasƙanci, lallai ba za a taɓa taimakonsu ba))** **[Fussilat: 15 – 16]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Akwai alƙaryu masu yawa da mutanen ciki suka yi girman kai, suka kuma bayar da baya ga barin umurnin Ubangijinsu da na manzanninsa, sai muka yi masu hisabi mai tsanani, ta hanyar ƙididdige abubuwan da suka aikata, da kuma tambayarsu a kai, muka kuma yi masu azaba mai tsanani da razani. Sai suka kwankwaɗi sakamakon mummunan aikinsu, lallai ƙarshen al'amarinsu ya zamo asara ne mai yawa))** **[at- Talaƙ: 8- 9]**.

Girman kai shi ne farkon zunubin da aka saɓa wa Allah da shi, wannan kuwa ya faru ne lokacin da Allah Maɗaukakin Sarki ya umurci Mala'iku da su yi wa Annabi Adam (AlaiHis Salam) sujada, suka kuma yi in banda Iblis; Allah mai girma ya ce: **((Ya kai wannan Annabi (SallalLãhu alaiHi wa sallam), faɗi lokacin da muka faɗa wa Mala'iku cewa: Ku durƙusa wa Annabi Adam (AlaiHis-Salãm), kuna masu jinjina masa, da kuma iƙirari da fifikonsa, sai dukan Mala'iku suka bi wannan umurni banda Iblis, shi ya ƙi yin sujadar, da ma can yana cikin masu saɓa wa Allah, da masu kafirce wa ni'imominsa da hikimarsa da saninsa))** **[al- Baƙra: 34]**.

Lallai ana gane masu girman kai ne da sifofinsu a ranar lahira, kaman dai yanda ake gane su da su a duniya, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Sai mutane tozon La'arafi suka kira wasu mutane da suka gane su ta hanyar sifofinsu, suka ce: yanzu mene yawanku da ma abubuwan suke sanya ku girman kai suka tsinana maku?!))** **[al- A'araf: 48]**; saboda haka ne addinin Musulunci ya yi gargaɗi akan mummunan ƙarshen girman kai, ya sanya shi ya zamo ƙofa ce daga cikin ƙofofin yin nesa da rahamar Allah, ya kuma yi alƙawarin narko mai tsananin raɗaɗi ga masu yinsa, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Lallai waɗanda suka ƙaryata ayoyinmu, suka kuma yi masu girman kai ba za a taɓa buɗe masu ƙofofin sama ba, ba kuma za su taɓa shiga aljanna ba, har sai ranar da igiyar da ake turke jirgin ruwa ya shige ta kafar allura (ma'ana: kaman yanda Hausawa suke faɗin cewa: har sai ranar da jakin baba ya yi ƙaho), lallai da haka muke saka wa masu laifi))** **[al- A'araf: 40]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((A ranar lahira kam za ka ga fuskokin waɗanda suka yi wa Allah ƙarya sun yi baƙin- ƙirin, da ma can wutar jahannama ita ce makomar masu girman kai))** **[az- Zumar: 60]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Aljanna da wuta sun yi sa'in'sa, wuta ta ce: masu taurin kai, da masu girman kai suna cikina, sai aljanna ta ce: mutane masu rauni, da miskinai suna cikina, sai Allah ya yi hukunci a tsakaninsu: Ke aljanna rahama ta ce da nake bayar da ita ga wanda na so, ke kuma wuta azaba ta ce da nake azabtar da wanda na so, kuma na yi alƙawarin sai na cika ku dukanku)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(.. shin ba na ba ku labarin su wane ne 'yan wuta ba? su ne: kowane shirgege mai girman kai)**.

Babu shakka, girman kai ɗabi'a ce da take zaune a cikin gurɓatacciyar zuciya, za a iya samun mutumin da yake cikin tsummokara, da ba shi da komai, amma kuma mai girman kai ne shi, za kuma a iya samun mawadacin da aka yalwata masa arzikin duniya, amma kuma yana cikin masu tawadhu'u da ƙasƙantar da kai, da mayar wa Allah da komai, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda duk akwai girman kai a cikin zuciyarsa, koda gwargwadon ƙwayar zarra ne ba zai shiga aljanna ba)**, sai wani mutum ya ce: Lallai mutum yakan so tufafinsa su zamo masu kyau, takalmansa ma zu zamo masu kyau, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai Allah kyakkyawa ne, yana kuma son abu mai kyau, abin da ake nufi da girma kai shi ne: ƙin gaskiya, da wulaƙanta mutane)**, wannan kuwa yana cikin mafi hatsarin cututtukan da suke kama zukata, da masu kama rayuwar zamantakewa, suna rusa rayuwa, da zamantakewa, mai yinsu yaudararre ne akan kansa, da yake yi wa sauran mutane gani-gani, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Babu komai a cikin zukatansu sai girman kai, ba za su iya tsinana komai ba)) [Ghafir: 56].**

Duk da cewa mazaunin girman kai shi ne zuciya, sai dai akwai alamunsa da suke bayyana a ɗabi'un mutane da mu'amalarsu, a cikin waɗannan alamu akwai: **Jin isa a wurin saɓon Allah, da kuma rashin rusuna wa gaskiya,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Idan aka yi masa nasiha da ya ji tsoron Allah, sai hankalinsa ya tashi, yana mai zaton cewa kana son ka rusa girma da darajarsa ne, hakan sai ya sake sanya shi ya aikata zunubin da ka hane shi; saboda taurin-kai da kangara…)) [al- Baƙra: 206],** shi mai girman kai a koda yaushe

ruɗi da jiji da kai su ne suka zuga shi wajen rashin amsar gaskiya, a duk sanda aka kira shi zuwa ga gaskiya, sai ruɗi da jiji da kansa su ƙaru, sai ya auka da kansa cikin halaka, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((.. Azabar jahannama ta ishe shi, tir da wannan matabbaci))** **[al- Baƙra: 206]**, akwai kuma waɗanda suke yi wa umurnin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) girman kai, take kuwa suke cimma sakamakon girman kansu da taurin kansu, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Iyasu Bn Salamata Bn al-Akwa'i (Allah ya ƙara yarda da shi), mahaifinsa ya ba shi labarin wani mutum da ya ci abinci da hannunsa na hagu a gaban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce masa: **(Ka ci da hannunka na dama)**, sai ya ce: ba zan iya ba, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ba kuwa za ta taɓa iyawa ba)**, girman kai ne kawai ya hana shi, sai ya ce: tun daga lokaci bai ƙara iya ɗaga shi zuwa bakinsa ba.

A cikin alamun girman kai akwai: **ɗaga kai,** wato kawar da ido akan abu saboda girman kai, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya hana haka ta bakin Luƙman a lokacin da yake faɗa wa ɗansa cewa: **((Kada ka kawar da fuskarka ga barin mutane, kada kuma ka yi tafiyar taƙama da gadara a bayan ƙasa, lallai Allah ba ya son duk wani mai girman kai, mai kuma yawan alfahari))** **[Luƙman: 18]**, haka ma akwai: **Girman kai da tafiyar gadara,** ma'ana tafiyar taƙama mai cike da jiji da kai, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada kuma ka yi tafiyar taƙama da gadara a bayan ƙasa, duk tsiyarka ba za ka iya huda ƙasa ba, ba kuma za ka iya ƙetare tsawon dutse ba, munanan abubuwan da suke tattare da haka, duka abubuwan ƙi ne a wurin Ubangijinka))** **[al- Isra'i: 37 – 38]**, haka ma akwai: **Yin**

**taƙama da tarkacen duniya da kuma ni'imomin Allah Maɗaukakin Sarki**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wani mutum cikin waɗanda suka gabace ku ya fito cikin ado, yana taƙama, sai Allah ya umurci ƙasa ta kama shi, yana nutsewa a cikinta har zuwa ranar alƙiyama)**, kaman yanda ake yin taƙama da fankama da tufafi, haka ma ana yi da shimfiɗun gida, da motocin hawa, da mallakar manyan gidaje da niyyar fankama da alfahari, da sauransu cikin kayan jin daɗin duniya. Haka ma a cikin alamun girman kai akwai: **Ƙyamatar zama da talakawa da masu rauni saboda wulaƙanta su**, kaman dai yanda mushirikai suka ƙyamaci zama da talakawan cikin sahabbai irinsu: Salman, da Bilal, da Suhaib da makamantansu (Allah ya ƙara yarda da su baki ɗaya), inda suka ce wa Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam): Ka kori waɗannan gudun kada su raina mu, sai Allah Maɗaukakin Sarki ya saikar da: **((Kada ka kori waɗanda suke ambaton Ubangijinsu safe da maraice suna masu neman yardarsa..)) [al-An'am: 52]**, Haka ma a cikin nau'o'in yi wa mutane girman kai akwai: **Taƙaita gayyatar zuwa walima akan mawadata banda talakawa saboda rashin ƙimanta su da yi masu girman kai**, Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: "Mafi sharrin abinci shi ne abincin walima, mawadata kawai ake gayyata a ƙyale talakawa da miskinai". Haka ma a cikin alamun girman kai akwai: **Ƙin yi wa mutane sallama, ko ƙin yin musafaha da waɗanda suke ƙasarsa a matsayi, kawai saboda wulaƙanta su**, lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan fara yi wa yara da manya sallama, ya zo a Hadisi cewa: **(Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya wuce ta wurin wasu yara sai ya yi masu sallama)**.

Haka ma a cikin alamun girman kai akwai: **Naciya wajen faɗa da husuma, da ƙaurace wa sulhu,** lallai babu saɓani akan haramcin Musulmi ya ƙaurace wa ɗan uwansa Musulmi sama da kwanaki uku, saboda yin hakan yanke zumunci ne, da kuma cutarwa gami da ɓarna a cikinsa, akwai kuma alƙawarin azaba ga mai yin haka a ranar lahira, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda duk ya ƙaurace wa ɗan uwansa sama da kwanaki uku, to ɗan wuta ne, sai dai idan Allah da karamcinsa ya jiƙansa)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Sam bai halatta Musulmi ya ƙaurace wa ɗan uwansa sama da darare uku ba, ta yanda za su haɗu wannan ya juya baya, ɗayan ma ya juya baya, wanda ya fi alhairi a cikinsu shi ne wanda ya fara da sallama)**, haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Abubuwa guda huɗu, duk wanda ya sami kansa a cikinsu to lallai shi tsantsar munafuki ne, wanda kuma yake da ɗaya daga cikinsu, to lallai yana da kaso na munafunci, har sai ya bar shi: idan an amince masa ya yi ha'inci, idan kuma zai yi magana ya yi ƙarya, idan kuma ya ƙulla yarjejeniya ya warware, idan kuma ya yi faɗa da wasu ya bututtuke)**.

Lallai girman kai da jiji da kai su ne dalilai na hana mushrikai da yawa shiga cikin addinin Musulunci, da faɗin "La'ilaha illalLahu", Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai sun kasance idan an ce masu "Babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah" sai su ɗaura girman kai..))** **[as- Safat: 35]**, sun kasance suna ƙyamar su bi addinin da ba na iyaye da kakanninsu ba, saboda girman kai ne Yahudawa suka ƙi bin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), duk kuwa da cewa suna da yaƙini akan gaskiyar Annabtarsa, Allah Maɗaukakin Sarki yana

cewa: **((Lallai waɗanda muka ba su littafi sun san shi kaman yanda suka san 'ya'yansu, lallai wasu daga cikinsu tabbas suna sane suke ɓoye gaskiya))** **[al- Baƙra: 146]**, shi ne ma ya sanya Bani Isra'ila suke ƙaryata Annabawansu, suka ma kashe wasunsu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shin yanzu a duk sanda wani manzo ya zo maku da abin da son zuciyarku ba su aminta ba, sai ku yi girman kai, wasunsu ku ƙaryata su, ku kuma kashe wasu?))** **[al- Baƙra: 87]**.

Lallai girman kai shi ne dalilin kafirci, da ƙaryatawar masu ƙaryatawa a cikin al'ummomin da suka gabata, Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗi ta bakin Annabi Nuhu (AlaiHis Salam) cewa: **((Kuma a duk sanda na kira su zuwa ga yin imani da kai, domin ka gafarta masu sai su saka hannuwansu cikin kunnuwansu domin ma kada su ji kirar tawa, su kuma lulluɓe fuskokinsu da tufafinsu domin kada ma su ga fuskata, sun dage akan kafircinsu, sun ji girman kai –ƙwarai-na su amsa kirata**)) **[Nuh: 7]**, haka ma game da jama'ar Annabi Hudu (AlaiHis Salam) Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Su kuwa Adawa sai suka yi girman kai a bayan ƙasa, ba tare da dalili ba, suka ce: wane ne ya fi mu ƙarfi?..))** **[Fussilat: 15]**, Game da jama'ar Annabi Saleh (AlaiHis Salam) kuwa Allah Maɗaukakin Sarki cewa ya yi: **((Sai masu faɗa a jin da suka yi girman kai cikin al'ummarsa suka ce wa masu rauni da suka yi imani daga cikinsu: yanzu kuna da cikakkiyar masaniya akan cewa Saleh manzo ne daga Ubangijinsa? Sai suka ce: mu kam mun yi imani da abin da aka aiko shi da shi.. Sai waɗanda suka yi girman kai suka ce: mu kuma da abin da kuka yi imani da shi ne muka kafirce))** **[al- A'araf: 75 -76]**, game da jama'ar Annabi Shu'aibu (AlaiHis Salam) ne kuma Allah

Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Sai masu faɗa a ji, cikin waɗanda suka yi girman kai cikin jama'arsa suka ce: Lallai ya Shu'aibu za mu fitar da kai da waɗanda suka yi imani da kai daga ƙauyenmu, ko kuma ka dawo cikin addininmu..))** **[al- A'araf: 88],** kaman haka ƙarshen kowace al'umma da ta yi wa umurnin Ubangijinta girman kai ya zamo halaka da taɓewa, tir da wannan ƙarshe, kuma tir za wannan makoma.

Lallai hanyar samun magani ga wanda aka jarabce shi da wannan muguwar cuta, ita ce: ya fara da yi wa zuciyarsa magani, ta hanyar sanin matsayinsa, ya dubi asalin samuwarsa bayan rashi, daga turɓaya, sannan maniyyi, sannan gudan jini, sannan gudar tsoka, sannan ya zama abin da ya zamo, bayan a baya shi ɗin babu ne, kuma ya kamata bawa mai girman kai ya sani cewa za a yi masa uƙuba ne a ranar lahira da akasin abin da yake so, duk wanda aikinsa shi ne yi wa halittar Allah girman kai, da jiji da kai, to za a tashe shi ne a matsayin mafi ƙasƙancin cikinsu, kuma mafi naƙasar cikinsu, Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Za a tashi masu girman kai a ranar alƙiyama tamkar ƙwayoyin zarra da sifar mazaje, ƙasƙanci ya mamaye su ta ko'ina..)**, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Wancan kam gidan lahira ne da muke bayar da shi ga waɗanda ba su nufi girman kai a bayan ƙasa ba, balle ɓarna, lallai ƙarshe mai kyau na masu tsoron Allah ne))** **[al- Ƙasasi: 83]**..

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

---------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Ina shaidawa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu Annabi Muhammadu, bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya Allah ka yi masa salati da salami shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai a cikin alamun toshe hanyar kira zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki akwai: Cin karon da ake samu tsakanin maganganu da ayyuka, da riya cewa ana kan nagartacciyar hanya da masu mayar da hankali akan shiga ta zahiri suke yi, inda suke bai wa shiga ta zahiri muhimmanci akan komai, koda kuwa shi ne jauhari da ainihin abin da ake nufi, kai koda shi wannan mai shiga ta zahirin bai da wani matsayi a fagen mutuntaka, da ɗabi'u masu kyau, da za su ba shi daman yin nagartaccen jagoranci; shi idan rayuwar mai irin wannan shiga ta zahiri ba ta yi daidai da karantarwar Musulunci ba, to tamkar yana rusa addini ne, yana kuma hana mutane shiga cikin addinin Allah Maɗaukakin Sarki, kuma akan ire - iren wannan ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Lallai a cikinku akwai masu korar mutane daga addinin Allah)**.

Idan a zahiri ya bayyana riƙo da addini, duk kuwa da yana da mummunar mu'amala, ko ƙarya, ko yaudara, ko ha'inci da cin amana, ko cin dukiyar mutane ta hanyar ɓarna, to kuwa lallai abin yana da hatsari matuƙa, hasali ma hakan yana shigar da mai yinsa cikin sahun munafukai, kaman yanda ƙungiyoyin tawaye da suke tallata kansu da sunan addinin Allah Maɗaukakin Sarki suke yi, duk kuwa da cewa su ne masu bai wa 'yan ta'adda mafaka, su ne kuma suka fi kowa taimaka masu, da zimmar su kifar da ƙasashe, ko su raunata su, ta

yanda za su ba su daman ɗarewa akan karagar shugabanci a waɗannan ƙasashen, kaman yanda suke riyawa, inda suke aikata komai, duk abin da zai taimaka masu wajen zartar da haka, to halal ne a wurinsu komin muninsa.

Haka ma waɗanda suke taƙaita addini kawai a babin ibadu da yin ijtihadi a ciki, duk kuwa da munanan fahimtar da suka yi wa addini, da wuce gona da iri wajen kafirta Musulmi, da ɗaukan makamai ana yaƙar mutane, kaman dai yanda ya faru da Hawarijawa da suka fi kowa yawan sallah da azumi da ƙiyamullaili, sai dai kash, ba su da isasshen ilimin addini da zai hana su kutsawa cikin jinin mutane, suka yaƙi mutane da takubbansu, da a ce sun nemi ilimi, da ilimin ya hana su aikata haka, saboda addinin Musulunci addini ne na rahama da jinƙai, duk abin da ya yi nesa da rahama da jinƙai, to babu shakka ya yi nesa da addinin Musulunci, saboda haka abin lura shi ne nagartacciyar mu'amala, ba wai kawai magana da baki ba, da ma can ana cewa: Halin mutum ɗaya a cikin mutane dubu, ya fi alhairi akan maganganu dubu akan mutum ɗaya..

**Ya Allah Ubangiji ka nuna mana gaskiya, ka kuma ba mu ikon binta, ka nuna mana ƙarya ka kuma ba mu ikon guje mata..**

- 42 –

## HATSARIN MUNAFUNCI DA HA'INCI GA AL'UMMA DA ƘASASHE

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Munafukai maza da munafukai mata suna ɫaimakon junansu, suna bayar da umurni da aikata munanan abubuwa, suna kuma hana aikata kyawawan ayyuka, suna kuma rowa da arzikin da Allah Maɗaukakin Sarki y aba su, sun manta da Allah, sai Allah ma ya manta da su, lallai munafukai kam su ne fasiƙan da suke yi wa shari'ar Allah tawaye))** **[at- Tauba: 67].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda a cikin Hadisinsa yake cewa: **(Alamun munafuki uku ne: idan zai yi Magana ya yi ƙarya, idan ya yi alƙawari ya saɓa, idan an amince masa ya yi ha'inci**). Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, bayan haka:

Babu shakka Lallai munafunci babbar cuta ne, annoba ne mai matuƙar hatsari, yana halakar sa mutane a matsayinsu na ɗaiɗaiya, ya kuma halakar da al'umma, lallai shi ne mafi hatsarin cututtuka da suke kama zukata, su kuma yi ɗaiɗai da

imani na haƙiƙa, su warware shi tun daga jijiyarsa, su kuma rusa gunshiƙansa, lallai munafunci cuta ce ta zamantakewa da ta ɗabi'u mai matuƙar hatsari ga tsaron ƙasa da kwanciyar hankalin cikinta; saboda haka ne hatsarinsa ya ƙetare hatsarin kafirci da na shirka idan ya kutsa cikin ƙasusuwan al'umma sai ya tsotse mata ɓargo, ya kuma tarwatsa hafin kanta..

Haka ma ha'inci yi wa maƙiya aiki makami ne mai hatsari da yake barazana ga ƙasa da wanzuwarta a tun tale - tale, babban dalili akan haka shi ne, babu wata ƙasa da ta tarwatse aka neme ta aka rasa face sai da aka fara rusa ta ta cikin gida tukunna, maha'intan da ake sayen su da kuɗi domin a cutar da ƙasarsu su ne suke taka babban rawa wajen haka a tsawon tarihin ɗan Adam, a koda yaushe hatsari da yake yi wa ƙasashe barazana ta cikin gida ya fi hatsarin da yake yi masu barazana da waje.

Ya kamata mu sani cewa shi munafunci ya kasu gida biyu ne: akwai babba, akwai kuma ƙarami, Na farko: shi ne babban munafunci, ya kuma fi na biyun hatsari, shi ne munafuncin da mutum yake ƙullewa a zuciya, inda zai bayyanar da Musuluncin a zahirinsa, amma a zuciya ya ƙudurce kafirci, irin wannan munafunci babban dalili ne na dawwama a gidan wuta, hasali ma mai yinsa yana can cikin ƙarƙashin wuta. Na biyu: ƙaramin munafunci, wato munafuncin aiki, shi wannan karkacewa ce ta ɗabii’a, da kuma aikata ɗaya daga cikin alamun munafukai, mutum ya bayyana shin a kirki ne a zahiri, amma a zuciya yana kan saɓanin haka, irin wannan munafunci bay a fitar da mai yinsa daga Musulunci, sai dai alama ce da take nuna cewa ya kama hanyar zuwa ga babban munafunci, muddin dai bai tuba ya bari ba.

Lallai Alƙur'ani mai girma da Hadisai masu tsarki sun bayyana mana sifofin munafukai da halayensu, da kuma irin makirce – makircensu, ba kuma mu ga waɗannan sifofin sun sauya ba a tsawon tarihi, ko bambancin ƙasashe ya sanya su saɓa ba, a cikin alamun da ake gane munafukai akwai:

Ƙarta da saɓa alƙawari, da cin amana, da kuma kafewa a wajen gaba da husuma; lallai waɗanna suna cikin mafiya munin sifofin munafunci da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sifanta su da su, wannan shi ne munafunci na aikace wanda Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana da cewa: (Duk wanda ya kasance cikin abubuwa guda huɗu, to kuwa lallai tsantsan munafuki ne shi, wanda kuma ya kasance a cikin ɗaya daga cikinsu, to kuwa lallai yana da sifar munafunci hai sai ba bar shi: Idan an amince masa ya yi ha'inci, haka ma idan zai yi magana ya yi ƙarya, idan kuma ya yi alƙawari ya saɓa, idan kuma ya yi faɗa ya nace da gaba da husuma), duk wanda waɗannan sifofi, ko ɗaya daga cikinsu suka taru a tare da shi, to kuwa lallai munafuki ne, domin waɗannan sifofi ne da suke wasa da maslahohin mutane, suke kuma rushe su.

A lokuta masu yawa mukan ga munafukai suna ƙarya domin su nuna wa waɗansun su cewa su masu gaskiya ne a maganganunsu da ayyukansu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: ((**Lallai a cikin mutane akwai waɗanda abin da zukatan su suka ƙulle sun saɓa da abin da harsunan su suke furuci da shi, an ba su daɗin-baki wajen tsara magana, maganar su za ta burgeka wajen yin makircin su na janyo amfani a rayuwar duniya, a riyawar su suna ƙarfafa maka cewa, lallai Allah ya san gaskiyar zukatan su akan abin da suka faɗi da harsunan**

**su, kuma tabbas su ɗin nan sun fi dukan sauran mutane tsananin yin husama da kai da kuma tsananta maka))** **[al- Baƙra: 204]**, lallai a cikin Alƙur'ani mai girma a duk inda aka ambaci munafunci da yaudara da cin amana, z aka ga an ambaci ƙarya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai suna yaudarar muminai ne da abin da suke yi, suna kuma zaton cewa Allah suke yaudara, saboda suna riya cewa ba ya riskar abubuwan da suke ɓoye, duk da cewa ya san abin da yake a asirce, da abin da aka yi shi a bayyane, gaskiyar al'amari kansu suke yaudara, saboda cutar aikinsu kansu za ta koma ko-ba-daɗe ko- ba –jima, domin dai duk wanda yake yaudarar waninsa, yake kuma zaton cewa bai sani ba, alhali kuma abin ba haka ba ne, to kuwa kansa yake yaudara.. Waɗannan kam a zukatansu akwai ciwon hassada, da ƙeta, da suke yi wa masu imani; saboda aƙidarsu ta riga ta ɓaci, a dalilin haka ne Allah Ya ƙara masu ciwo akan ciwonsu ta hanyar taimakon da yake yi wa masu gaskiya, hakan kuma ya ƙara baƙanta masu rai, saboda hassadarsu da ƙetarsu gami da taurin-kansu, lallai azaba mai raɗaɗi a duniya da lahira ta tabbata akan waɗannan sakamakon ƙaryatawar da suke yi, da kuma shegen musunsu))** **[al- Baƙra: 9 -10]**, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi gargaɗi akan ƙarya, ya kuma bayyana mummunan tasirin haka a inda yake cewa: **(Ahir ɗinku da yin ƙarya, domin ita ƙarya tana yi wa mai ita jagoranci ne zuwa ga saɓon Allah, saɓon Allah kuma yana isan da mutum zuwa wuta, mutum ba zai gushe ba yana ƙarya, yana kuma zaɓar wa kansa hanyar ƙarya har sai Allah ya rubuta sunansa a matsayin maƙaryaci a wurinsa)**, lokacin da aka tambayin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) akan cewa: Shin mumini

zai iya zama matsoraci? Sai ya ce: **(Ƙwarai kuwa),** sai aka ce masa: shin mumini zai iya zama marowaci? Sai ya ce: **(Ƙwarai kuwa)**, sai aka ce masa: shin mumini zai iya zama maƙaryaci kuwa? Sai ya ce: **(A'a)**. Sayyiduna Abubakar al-Siddiƙ (Allah ya ƙara yarda da shi) ma ya sifanta ƙarya da cin amana a inda yake cewa: "Lallai gaskiya amana ce, ƙarya kuma ha'inci ne.."

Haka ma ha'inci da yi wa maƙiya aiki domin rusa al'umma suke, domin suna rusa duk wani ginshiƙi na soyayya, su kuma kafa ƙiyayya da gaba da nesantar juna gami da rikici da rarrabuwar kawuna, da lalata mu'amala, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana mana cewa shi cin amana ga mai yinsa a ranar alƙiyama ƙasƙanci ne da nadama, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idan Allah Maɗaukakin Sarki ya tara mutanen farko da na ƙarshe a ranar alƙiyama, ana ɗaga wa kowane mayaudari tuta, sai a ce: wannan shi ne yaudarar da wane ɗan wane ya yi..)**, kuma Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) zai yi shari'a da shi a ranar alƙiyama, a inda yake cewa: **(Mutane uku kam zan yi shari'a da su a ranar alƙiyama, duk kuwa wanda na yi faɗa da shi, to kuwa zan yi nasara akansa ranar alƙiyama: mutumin da aka amince masa saboda ni, sannan ya ci amana, da mutumin da ya sayar da ɗa mai 'yanci ya kuma ci kuɗin, da mutumin da ya ɗauki ɗan ƙwadugo ya yi masa aiki, amma kuma ya ƙi ba shi haƙƙinsa)**.

A cikin hatsurra cin amana mafi girma akwai cin amanan ƙasa, da sayar da ita da ɗan kuɗi kaɗan na tarkacen duniya mai zuwa ya wuce, kaman dai yanda ƙungiyoyin masu tsattsauran ra'ayi, da masu mara masu baya, ko masu bin turbarsu suke sayar da mutuncin ƙasarsu da kuɗi kaɗan.

A cikin munanan sifofin da Musulunci ya gargaɗe mu akwai; tsananin gaba da husuma, domin yin haka tushe ne na dukan sharri, kuma asali ne na duka zargi, hanya ce da ake karkace wa gaskiya, ta yanda ake mayar da gaskiya ta koma ɓata, ɓata kuma ta koma gaskiya, lallai Allah Maɗaukakin sarki ya sifanta husuma da tsanani gami da taurin- kai da naciya, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai a cikin mutane akwai waɗanda abin da zukatan su suka ƙulle sun saɓa da abin da harsunan su suke furuci da shi, an ba su daɗin-baki wajen tsara magana, maganar su za ta burgeka wajen yin makircin su na janyo amfani a rayuwar duniya, a riyawar su suna ƙarfafa maka cewa, lallai Allah ya san gaskiyar zukatan su akan abin da suka faɗi da harsunan su, kuma tabbas su ɗin nan sun fi dukan sauran mutane tsananin yin husama da kai da kuma tsananta maka)) [al- Baƙra: 204].** An ruwaito Hadisi daga Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita), ita ma daga Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai mutumin da Allah ya fi ƙi shi ne mai naciyar gaba a husuma)**.

Mafi kusancin sifar da ta fi dacewa da munafuki it ace; mai fuska biyu, hasali ma a wannan zamanin ga su nan sun zarce wannan sifa ƙwarai da gaske, inda suke da fuskoki dubu da ɗaya, su ne mafiya sharrin halittun Allah, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Za ku sami mafi sharrin mutane shi ne mai fuska biyun da zai zo wa waɗannan da wata fuska, ya kuma je wa waɗancan da wata fuskar).**

A cikin alamun munafunci akwai: **Ɓarna a bayan ƙasa, da kuma riya cewa gyara ake yi:** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Idan ɗaya daga cikin shiryayyu ya ce da waɗannan**

**munafukan: kada ku yi ɓarna a bayan ƙasa, ta hanyar toshe hanyar Allah, da yaɗa fitina, da kunna wutar yaƙi da gãbã, sai su wanke kawunansu ga barin ɓarna, su ce: ai mu masu gyara ne, suna yin haka ne saboda tsananin ruɗar kansu da suke yi. Wannan shi ne halin duk wani maɓarnaci, mutumin banza mai ruɗin kansa, ya kan riya cewa ɓarnarsa gyara ce.. A'a, ya ku muminai ku faɗaka, ku kuma lura da cewa, lallai waɗannan su ne maɓarnata na gaskiya, sai dai ba sa ganin ɓarnarsu ne saboda ruɗar kawunansu da suke yi, ba kuma sa hango mummunar makomar da za su faɗa sakamakon wannan ɓarnar)) [al- Baƙra: 11 - 12]**, lallai ɓarna a bayan ƙasa tana da surori masu yawa, a cikinsu akwai: yaɗa ƙarya a cikin ƙasa, da shigar da rauni a cikin zukata muminai masu gaskiya, da dasa gurɓatattun tunani a cikin al'umma, da yaɗa fitina a tsakanin mutane, Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: **((Da ma za su fita yaƙi tare da ku da babu abin da za su tsinana maku in ma ban da sare gwiwa, da kuma sun zare maku himma, suna dai neman fitina ta auka maku, a cikinku kuma akwai masu sauraronsu, lallai Allah yana da cikakkiyar masaniya akan azzalumai)) [at- Tauba: 47]**, haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Suka ce: kada fa ku fita yaƙi da wanna garjin ranar.. ka faɗa masu; ai wutar jahannama ita ce tafi tsananin zafi da a ce suna fahimta)) [at- Tauba: 81]**, haka ma Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai Allah yana sane da masu kawo cikas a cikinku, da masu cewa da 'yan uwansu ku taho wurinmu, kuma ba sa fita zuwa yaƙi cikin tsanani sai ɗan kaɗan)) [al- Ahzab: 18].** A cikin surorin ɓarna akwai tauye haƙƙoƙin mutane, da ƙasƙantar da dajararsu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ku kuskura ku tauye wa mutane**

**haƙƙoƙinsu, kada kuma ku yi girman kai a bayan ƙasa cikin ɓarna))** **[Hud: 85; as- Shu'ara'i: 183]**, haka ma a cikin surorinsa akwai: rusa al'amura, da lalata su, da karkashe mutanen da ba su ji ba, ba su gani ba, da tsoratar da mutanen da suke cikin aminci, da lalata maslahohin mutane, da rashin gabatar da aikin da ya rataya akan wuyan mutum, haka ma akwai cin hanci, da rashawa, da yin alfarma, da cin dukiyoyin mutane ta hanyar ɓarna.

Kasala wajen gabatar da ibada, da yin riya a ciki, musamman mafi alhairi da falala a cikin ibadu, wato sallah, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai su munafukai suna zaton cewa suna yaudarar Allah Maɗaukakin Sarki ne da munafuncin su, suna zaton cewa suna ɓoye masa haƙiƙanin yanda suke, alhalin Allah mai girma da buwaya ne yake yaudarar su ta hanyar yi masu jinkiri da barin su a cikin fagen sharrin su, suna abin da suka ga dama, wanda kuma a lahira za a yi masu hisabi akan abubuwan da suka aikata, lallai waɗannan munafukan suna da alamu guda biyu, ɗaya ta zahiri, ɗayan kuma ta baɗini, ta zahirin ita ce: a duk sanda za su tashi zuwa sallah sukan tashi ne cikin kasala da nauyin jiki, sallar tasu kuma riya ce, ta baɗinin kuma ita ce: ba sa ambaton Allah sai a ƙanƙanin lokaci, domin lallai da suna ambaton sa da kuwa sun yi ban kwana da munafunci))** **[an-Nisa'i: 142]**, haka ma Allah Mai girma yana cewa: **((Babu abin da ya hana a amshi ciyarwar da suke yi daga gare su sai kasancewarsu sun kafirce wa Allah da Manzonsa, ba kuma sa tashi zuwa sallah face suna cike da kasala, ba kuma sa ciyar da dukiyarsu sai zukatansu sun ƙi yin hakan))** **[at- Tauba: 54]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu**

**sallar da tafi yi wa munafukai nauyi kaman sallah Asubahi da ta Isha'i, lallai da sun san abin da yake cikinsu da sun hallara koda da rarrafe ne)**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Jabir Bn Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: wata rana Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fito sai ya ce: **(Ya ku mutane, ahir ɗinku da aikata shirkar ɓoye)**, sai suka ce: Ya Manzon Allah, mene ne shirkar ɓoye? Sai ya ce: **(Mutum ne zai tashi ya dage wajen ƙawata sallarsa saboda yana ganin mutane suna kallonsa, wannan ne shirkar ɓoye).**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

----------------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga cikamakon Annabawansa da Manzanninsa, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam), da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai a cikin alamun munafunci, da tafarfakunsa akwai: haɗa kai da maƙiya, da shirye – shirye tare da su, shirye- shiryen da za su cutar da addini da ƙasa, ta hanyar yi masu leƙen asiri, da cin amanar ƙasa, da kai masu labarai da bayanai, da bayyana masu sirrorin ƙasa, shi munafuki a koda yaushe ɗan leƙen asirin ƙasa ne da yake jiɓinta al'amurransa ga maƙiya ƙasarsa, inda bai damu da cutarwar da zai gadar wa iyalansa, da maƙwabtansa, da ma makusantansa ba, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shin babu waɗanda za su jiɓinta al'amuransu a hannunsu sai waɗannan azzalamai?, Abin mamaki shi ne: za ka ga zukatan waɗanda suke jiɓinta al'amurransu a hannunsu cike suke da cuta ta**

**rauni da munafunci, suna cewa: ai muna jin tsoron kada wani bala'i na bai ɗaya ne ya same mu, su kuma su ƙi kawo mana ɗauki.. Abu ne mai sauƙi Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa Manzonsa (SallalLãhu alaiHi wa sallam) wani buɗi ta hanyar taimakon Musulmai akan maƙiyansu, ko kuma ya tona munafuncin waɗannan munafukan, su kuma su zamo cikin nadama da kaico akan abubuwan da suka ɓoye na kafirci da kokwanto a cikin zukatansu))** **[al- Ma'ida: 52]**, haka ma Allah mai girma yana cewa: **((Ku kuma yi taka-tsantsan da masu kashe-gwiwan da za su sanya ku yi sanyi, domin a cikin waɗanda suke tare da ku akwai masu kashe maku gwiwa wajen fita yaƙi, su kuma ƙi fita filin-daga, idan ba ku yi nasara a wajen jahadi ba, sai waɗannan da suka zauna a gida su rinƙa yi maku dariya, suna cewa: Ni kam lallai Allah ya yi mani ni'ima, saboda haka ban fita zuwa wannan yaƙi tare da su ba. Idan kuma nasara ce daga Allah ta zo maku, kuka sami ganima a yaƙin, waɗannan dai mutanen –cikin damuwa da burin iska- suke cewa: Ina ma a ce muna tare da su a wannan yaƙin, mu ma mu sami babban rabo a cikin wannan ganimar, suna faɗin irin wannan magana kai ka ce babu wata igiya ta soyayya da ta haɗa ku da su))** **[an- Nisa'i: 72 -73]**, lallai shi munafuki yana farin ciki idan wani abin damuwa na sharri ya faɗa wa ƙasarsa, ko 'yan ƙasar, ko idan fitina ta yaɗu a ƙasar, ko wata cuta, ko idan ƙasar ta sami karayar tattalin arziki, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Idan wata ni'ima irin ta nasara, ko ganima, ta zo maku sai su yi baƙin-ciki, idan kuma wata jarrabawa irin ta fari, da rashin nasara a wurin yaƙi, ta same ku, sai su yi farin-ciki, idan har kuka yi haƙuri akan cutarwar su, kuka kuma ji tsoron Allah akan abin da na hana ku, na**

**jiɓinta al'amurran ku a gare su, to, kuwa lallai duk makircin su da adawar su ba za su cuce ku da komai ba; saboda lallai Allah Masanin abin da suke aikatawa ne na makirci, kare maku hakan ba zai gagare shi ba))** **[Ali Imran: 120].**

Amma dai sababbin munafukai na wannan zamanin bayan waɗannan sifofi na ƙarya, da cin amanar ƙasa, da yaudara, da warware alƙawurra da yarjejeniya, da tunzura 'yan ƙasa gami da hure masu kunne, da cin amanar addini, sun haɗa da wasu sababbin nau'uka na yaudara, musamman yin kasuwanci da addini, da yin amfani da shi wajen biyan buƙatunsu da na ƙungiyoyinsu da suka amfani da addini domin ɗarewa akan shugabancin, suna masu lulluɓe kawunansu da bargunan addini a siyasance, inda suke danganta kawunansu zuwa ga imani, a daidai lokacin da suke kore imani ga duk wanda ba su ba, suna yin haka ne domin su rufe sharrin da yake tattare da ayyukansu, bugu da ƙari kuma ga irin yanda su waɗannan sababbin munafukai na zamani suke ha'intar ƙasarsu, da wulaƙanta ƙasar, kai da sayar da ita da tarkacen duniya.

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa waɗannan mutane tanadin azaba mai raɗaɗi, fushin Allah yana nan yana tsumayarsu a duniya da lahira, kuma dukan makircinsu zai koma kansu.

Saboda haka dole ne a tashi tsaye wajen bai wa ƙasashe kariya, da daƙile duk wani sharri da za su kawo.. Ya Allah ka tsarkake zukatanmu daga munafunci, ka kuma nesanta idanuwanmu daga barin ha'inci da cin amana, haka ma ka tsarkake harsunanmu ga barin ƙarya, ka kiyaye mana ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya baki ɗaya.

- 43-

## YI WA UWA BIYAYYA SANADI NE NA SAMUN ALBARKA A DUNIYA DA SAMUN RAHAMA A LAHIRA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Mun yi wa ɗan Adam wasiya da ya kyautata wa iyayensa guda biyu, saboda mahaifiyarsa ce ta ɗaukin cikinsa cikin wahalhalu, an yaye shi ne bayan shekaru biyu.. saboda haka ka gode mini, ka kuma gode wa iyayenka, lallai gare ni za ka komo)) [Luƙman: 14]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai kalmar biyayya, kalma ce da ta ƙunshi dukan nagartattun tadodi, da sifofi masu kyau, da kyawawan ɗabi'u, waɗanda suke gadar da natsuwa a cikin zukata, suke kuma yaɗa soyayya a tsakanin mutane, suke kuma tabbatar da zaman lafiya a cikin rayuwar zamantakewa, lokacin da aka tambayi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) game da biyayya, cewa ya yi: **(Biyayya ita ce kyautata ɗabi'u).**

Babu shakka iyaye biyu su ne suka fi cancanta da a yi masu biyayya a cikin mutane, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya

umurce mu da mu kyautata masu, mu kuma yi masu biyayya, mu rausasa wajen yi masu ma'amala, mu kuma kwantar da kai a gare su.

Idan muka duba littafin Allah mai girma da ɗaukaka, da Sunnar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) za mu ga irin yadda ta kamata dangantaka tsakanin 'ya'ya da iyaye ta kasance, Allah Maɗaukakakin Sarki yana cewa: **((Ubangijinka ya hukunta cewa kada a bauta wa kowa sai shi kaɗai, su kuma iyaye a kyautata masu.. Idan tsufa ta kama ɗaya daga cikinsu, ku dukansu su biyu, to kada ka soma ka yi tir da su, kada kuma ka kuskura ka hantare su, ka dai faɗa masu magana ta karamci.. Ka kwantar masu da kai cikin tausayawa, ka yi addu'a ka ce: Ya Ubangiji ka yi masu rahama kaman yanda suka raine ni tun ina ƙarami))** **[al- Isra'i: 23 -24]**. Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana cewa yi wa iyaye biyu biyayya, da biya masu buƙatunsu shi ne aikin da ya fi komai falala bayan sallah wadda ita ce ginshiƙin addini, kuma mafi girman rukuni a cikin rukunnan Musulunci, lokacin da aka tambayi (SallalLahu alaiHi wa sallam): shin wane aiki ne Allah ya fi so? Sai ya ce: **(Sallah a lokacinta)**, sai aka ce: sai kuma me ne? sai ya ce: **(Sannan yi wa iyaye biyu biyayya),** sai aka ce: sai kuma me ne? sai ya ce: **(Jahadi wajen ɗaukaka kalmar Allah).**

Lallai addinin Musulunci ya ɗaukaka darajar yi wa iyaye biyayya, da kuma kyautata masu, da kulawa da su, sannan kuma ya keɓanci uwa da wata biyayya da kyautatawa da muhimmantawa ta daban, wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce: Ya Manzon Allah, Wane ne ya fi cancanta na kyautata masa a lokacin da

muke tare? Sai ya ce: **((Mahaifiyarka))**, ya ce: sai kuma wa ne?, sai ya ce: **(Sannan mahaifiyarka),** ya ce: sai kuma wa ne?, sai ya ce: **(Sannan mahaifiyarka),** ya ce: sai kuma wa ne?, sai ya ce: **(Sannan mahaifinka).** An ruwaito Hadisi daga Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: Na tambayi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa: wane mutum ne haƙƙinsa yafi girma akan mace? Sai ya ce: **(Mijinta),** sai na ce: wane mutum ne kuma haƙƙinsa yafi girma akan namiji? Sai ya ce: **(Mahaifiyarsa).**

Wannan kam ba abin mamaki ba ne, domin idan uwa ba ta fi kowa cancanta da a biya mata buƙatunta ba, to wane ne ya cancanta? Wane ne ya fi cancanta da ka biya masa buƙatunsa sama da wadda ta ɗauke ka a cikin cikinta har na tsawon watanni tara, ta sha wahalhalu iri- iri a lokacin da za ta haife ka, ta kuma shayar da kai nononta, ta wanke maka ƙazanta da hannunta, ta fifita ka a wajen abinci akan kanta, idan rashin lafiya, ko wata damuwa suka kama ka, takan jin zafi da raɗaɗin da ba sa misaltuwa, da za a ba ta zaɓi, na ta zaɓi: ko dai ka rayu, ko kuma ita ta rasu, da kuwa ta zaɓi ka rayu da sauri.. wane ne ya fi cancanta da a yi masa biyayya sama da wanda Allah Maɗaukakin Sarki da kansa ne ya yi wasici da ita a inda yake cewa: **((Mun yi wa mutum wasici da mahaifansa kan ya kyautata masu ƙwarai da gaske, saboda mahaifiyarsa ce ta ɗauki cikinsa cikin wahala, ta kuma haife shi cikin wahala, watanni talatin ta ɗauka tsakanin ɗaukan cikinsa da yãyénsa tana shan nau'o'i daban- daban na raɗaɗi da wahalhalu)) [al-Ahƙaf: 15].**

Lallai falala ce Ubangiji Allah ya datar da bawa wajen yi wa iyayensa biyayya, musamman uwa, duk wanda Allah ya

shiryatar da shi zuwa ga haka, to kuwa lallai ya ba shi alhairai masu tarin yawa, da falala masu girma, zai haɗu da albarka gami da dacewa a rayuwarsa ta duniya, zai kuma sami lada da rahama gami da gafara da tsira a gobe alƙiyama, babu shakka yi wa uwa biyayya abu ne da yake da falala da riba masu yawa da mai biyayyar zai samu a duniya tun ma kafin a je lahira, a cikin abubuwan da zai samu akwai:

*** Biyan buƙatu, da yaye damuwa, da amsar addu'a,** An ruwaito Hadisi daga Ibn Umar (Allah ya ƙara yarda da su), shi kuma daga Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ya ce: **(A wani lokaci wasu mutane uku suna tafiya, sai ruwan sama ya faɗo, sai kuwa suka fake a wani kogo da yake cikin wani dutse, sai wani dutse ya gangaro ya toshe kofar kogon da suke ciki ya rufe su, sai wasu daga cikinsu suka ce wa saura: ku tuno da ayyukan da kuka yi su saboda Allah shi kaɗai, mu roƙi Allah da su, ko Allah zai yaye mana wannan damuwa, sai ɗaya daga cikinsu ya ce: Ya Ubangiji, lallai ina da iyaye guda biyu da suka tsufa, ina kuma da yara ƙanana, ina yin kiwo saboda su, idan zan je wurinsu sai na tatsi nono na tafi masu da shi, sai in fara da bai wa mahaifa na kafin 'ya'ya na, wata rana sai na makara, ban dawo ba har yamma ta yi, sai na samu sun yi barci, sai na tatso nono kaman yanda na saba, sai na tsaya a kansu, ba na son na tashe su, ba kuma na son in fara bai wa yaran kafinsu, su kuma yaran suna ta juye- juye saboda yunwa a gefen ƙafafuwa na, har alfijir ya keto, Ya Ubangiji idan ka san wannan abu da na yi, na yi shi ne saboda neman yardarka, to ka tunkuɗe mana wannan dutsen ta yadda za mu iya hango sama, sai kuwa Allah ya tunkuɗe masu, suka hango sama…)**, sannan kowane ɗaya daga cikin

abokansa biyu suka roƙi Allah albarkacin ayyukan da suka yi su domin Allah Maɗaukakin Sarki, Allah kuma ya yaye masu wannan ƙunci gami da damuwa da tsanani da suka tsinci kansu a ciki.

Wasu mutane daga cikin al'ummar ƙasar Yaman sun zo wurin Sayyiduna Umar Bn al-Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi), sai ya tambaye su: shin a cikinku akwai Uwaisu Bn Ămir? Har dai sai da ya haɗu da Uwaisu, sai ya ce: kai ne Uwaisu Bn Ămir? Ya ce: Na'am ni ne, ya ce: daga Murad, sannan Ƙarnin ko? ya ce: Na'am, ya ce: Da kana da cutar baras sai Allah ya warkar da kai, ɗan abin da ya yi saura bai wuce faɗin dirhami ba ko? ya ce: Na'am haka ne, ya ce: kana da mahaifiya a raye ko?, ya ce: Na'am haka ne, sai ya ce: Na ji Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Uwaisu Bn Ămir zai zo wurinku tare da tawagogin mutanen Yaman daga Murad, sannan daga Ƙarnin, da yana da cutar baras, sai Allah ya warkar da shi, ɗan abin da ya yi saura bai wuce faɗin dirhami ba, yana da mahaifiya a raye da yake mata biyayya, da a ce zai rantse akan kowane irin abu, to kuwa lallai Allah zai kuɓutar da rantsuwarsa, idan ka sami daman ya nema maka gafarar Allah, to ka nemi hakan)**, ina neman ka nema mini gafara, sai kuwa ya nema masa gafara, sai Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce masa: Ina za ka tafi? Ya ce: garin Kufah, ya ce: Ba na ba ka takarda ka kai wa gwamnan garin ba? ya ce: In kasance a cikin tawagar mutane shi ne na fi so, lallai a maganar Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) game da wannan bawan Allah akwai nuni akan cewa Allah Maɗaukakin Sarki yana amsar addu'arsa ne saboda biyayyar da yake yi wa mahaifiyarsa.

***Babban sakamako da lada,** an ruwaito Hadisi daga Mu'awiyya as-Sulamiy, ya ce: Na zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai na ce: Ya Manzon Allah, Ina son in tafi jahadi tare da kai, na ɗauki wannan mataki ne saboda neman yardar Allah, da kuma neman lahira, sai ya ce: **(Kai kuwa, shin mahaifiyarka tana raye?)** sai na ce: Na'am tana raye, ya ce: **(Ka koma ka yi mata biyayya)**, sai na sake zagayowa ta ɗaya ɓangaren, sai na ce: Ya Manzon Allah, Ina son in tafi jahadi tare da kai, na ɗauki wannan mataki ne saboda neman yardar Allah, da kuma neman lahira, sai ya ce: **(Kai kuwa, shin mahaifiyarka tana raye?)** sai na ce: Na'am tana raye, ya Manzon Allah, sai ya ce: **(Ka koma wurinta ka yi mata biyayya)**, sai na sake biyowa ta gabansa, sai na ce: Ya Manzon Allah, Ina son in tafi jahadi tare da kai, na ɗauki wannan mataki ne saboda neman yardar Allah, da kuma neman lahira, sai ya ce: **(Kai kuwa, shin mahaifiyarka tana raye?)**, sai na ce: Na'am ya Manzon Allah, tana raye, sai ya ce: **(Ka lizimci yi mata biyayya, a wurinta za ka tarar da aljanna)**.

An ruwaito Hadisi daga Ka'ab Bn Ujrat (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: wani mutum ya wuce ta wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai Sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) suka ga irin yanda yake kazar-kazar da nishadi, sai suka ce: ya Manzon Allah, ina ma fisabililLahi yake yi? Sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan ya fito ne domin ya nema wa ƙananan yaransa abinci, to ya fito ne fisabililLahi, haka ma idan ya fito ne saboda ya sami abin da zai iya daukan nauyin iyayensa tsofaffi guda biyu, to ya fito ne fisabililLahi..).**

***Kankare zunubai da munanan ayyuka,** an ruwaito Hadisi daga Ibn Umar (Allah ya ƙara yarda da su), wani mutum ya ce: Ya Manzon Allah, lallai na aikata babban zunubi, shin za a amshi tuba ta kuwa? Sai ya ce: **(Shin kana da mahaifiya a raye?),** sai ya ce: a'a, ya ce: **(Shin kana da Inna a raye?),** ya ce: Na'am, sai ya ce: **(Ka yi mata biyayya).**

***Rabauta da gidan aljanna, da ɗaukaka darajoji,** an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abdullahi Bn Mas'ud (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: na ce: ya Annabin Allah, wane aiki ne yafi kusanta mutum da aljanna? Sai ya ce: **(Sallah a lokacinta)**, na ce: sannan kuma mene ya Annabin Allah? Ya ce: **(Bin iyaye..),** an ruwaito Hadisi daga Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Na yi barci, sai na ganni a aljanna, sai na ji muryar wani makaranci yana karatu, sai na ce: wane ne wannan? Sai mala'iku suka ce: Harisatu Bn an-Nu'uman ne, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: (Haka biyayya take, haka biyayya take), Harisatu mutum ne mai tsananin biyayya wa mahaifiyarsa.**

Ya kamata mu zamo masu yi wa iyayenmu maza da mata biyayya, mu biya masu buƙatunsu, mu kuma sani cewa lallai biyayya da saɓa wa iyaye duka bashi ne, yanda ka yi, za a yi maka, lallai saɓa wa iyaye biyu na cikin zunuban da Allah Maɗaukakin Sarki yake gaggauta yin uƙuba akansu tun a duniya kafin lahira, haka Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya faɗi yana cewa: **(Abubuwa guda biyu Allah yana gaggawar kamu akansu: zalunci da saɓa wa iyaye biyu)**, a wani Hadisin kuma ya ce: **(Mai saɓa wa iyaye, da mai yawan**

**gori, da wanda shan giya ya zama masa jiki duka ba za su shiga aljanna ba).**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Tsira da amincin Allah su tabbata ga shugaban ɗaukacin halitta, ya Allah ka ƙara yi masa salati da salama da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, da duk waɗanda suka bi turbarsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai yi wa iyaye biyu biyayya – musamman uwa- abu ne da ɗaukacin addinai da Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko da su suka haɗu akan wajibcinsa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku tuna lokacin da muka ɗauki alƙawari da Bani Isra'ila a cikin At-taura kan cewa kada ku bauta wa kowa sai Allah, ku kuma kyautata wa iyaye..)) [al- Baƙra: 83],** Mai girma da ɗaukaka ya yi magana da ɗaukacin mutane a wani wurin yana cewa: **((Mun yi wa ɗan Adam wasiya da ya kyautata wa iyayensa guda biyu, saboda mahaifiyarsa ce ta ɗaukin cikinsa cikin wahalhalu, an yaye shi ne bayan shekaru biyu.. saboda haka ka gode mini, ka kuma gode wa iyayenka, lallai gare ni za ka komo)) [Luƙman: 14]..**

Lallai addinin Musulunci ya yanke hanzarin duk wani mutum da zuciyarsa take ƙawata masa ya saɓa wa iyayensa, domin abu ne mai yiwuwa wasu daga cikin matasa su ga cewa sun fi iyayensu riƙo da addini, a dalilin haka sai su rinƙa tsaurara wa iyayen nasu, suna masu munana masu mu'amala,

ya kamata ire- iren waɗannan matasan su sani cewa: lallai addinin Musulunci ya umurce mu da mu kyautata wa iyaye, mu yi masu biyayya, koda kuwa kafirai ne su; saboda ma kada mai saɓa wa iyaye ya kafa hujja da cewa iyayen nasa ba akan shiriya suke ba, saboda haka ne Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Idan suka tirsasa ka akan sai ka haɗa ni da wani abin bauta da ba ka da masaniya akansa, to kada ka bi su a kan haka, amma ka yi masu duk wani abu na kyautatawa a rayuwar duniya, ka yi biyayya ga waɗanda suka jiɓinta al'amurransu zuwa gare ni, a ƙarshe dai dukanku wurina za ku komo, in kuma bayyana maku abin da kuke aikatawa)) [Luƙman: 15],** an ruwaito Hadisi daga Sayyida Asma'u Bnt Abubakar (Allah ya ƙara yarda da su) ta ce: Mahaifiya ta ta zo – a lokacin tana mushrika- a zamanin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), tana son in yi zumunci da ita, sai na tambayi Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), na ce: shin zan iya yin zumunci da mahaifiyata? Sai ya ce: **(Na'am, ki yi zumunci da mahaifiyarki).**

Su iyaye koda kafirai ne, kuma har a lokacin da suke yunƙurin tirsasa maka ka saɓa wa Allah, ko kuma na su fitar da kai daga Musulunci, a cikin haka ne kawai ba a yi masu biyayya, amma duk da haka, wannan ba dalili ne na ka munana masu mu'amala ba, dole ne a kowane irin yanayi ka tsaya a inda Allah Maɗaukakin Sarki ya ba ka umurni, Allah yana cewa: **((Amma ka yi masu duk wani abu na kyautatawa a rayuwar duniya..)) [Luƙman: 15],** dole ne ka fahimci cewa wannan ba wai wata falala ce kake yi masu ba, a'a, wajibi ne akanka, za kuma ka sami zunubi idan ka gaza wajen gabatar da haka, ko kuma idan ma ka ƙi yi.

Lallai aljanna ta tabbata ga wanda duk ya kyautata wa mahaifiyarsa, ya kuma yi iya iyawarsa wajen yi mata biyayya, an ruwaito Hadisi daga Abdullahi Bn Amr (Allah ya ƙara yarda da su), ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Yardar Allah tana cikin yardar iyaye, fushin Allah yana cikin fushin iyaye).**

**Ya Allah Ubangiji, ka taimake mu wajen yi wa iyayenmu maza da mata biyayya, ka gafarta masu, ka yi masu rahama kaman yanda suka raine mu muna ƙanana.**

- 44 –

## RIBATAR LOKUTAN BIYAYYA DA ALHAIRAI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ku yi gaggawa wajen aikata ayyuka na gari; domin ku sami babban gafara daga Allah da yake mallakar al'amurran ku, ku kuma sami shiga aljannar da faɗin ta ya kai faɗin sama da ƙasa, an tattale ta ne saboda masu tsoron Allah da masu nesantar azabarsa.. Su kuwa waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu a lokacin da suke cikin yalwa da ƙunci; da lokacin da suke da iko, ko suke da rauni; domin neman yardar Allah, suke kuma hana zukatansu azabtar da wanda ya munana masu, suke kuma yafiya ga waɗanda suka yi masu laifi, lallai waɗannan suna cikin mutanen kirki masu kyautatawa; kuma lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana bai wa mutanen kirki da masu kyautatawa lada, yana kuma yarda da su)) [Ali Imran: 133 – 134].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya keɓance wasu kwanaki a cikin zamani da wasu falala, inda yake ruɓanya ladan

kyawawan ayyuka a cikinsu, alhairai kuma su yawaita, a kuma ɗaukaka darajoji; Allah Maɗaukakin Sarki ya samar da duka waɗannan tagomashi shi ne; saboda kwaɗaitar da bayinsa wajen dawwamar kusantowa zuwa gare shi, da kyautata tsayawa a ƙofarsa, lallai mai hankali na gaskiya shi ne wanda ya ribaci irin waɗannan lokuta da kyakkyawar niyya, ya kuma kyautata ayyuka a cikinsu, ya kuma fuskanci Ubangijinsa Mai girma da ɗaukaka, yana mai neman hanyoyin da zai yawaita waɗannan ayyuka na alhairai, ya kuma bijiro wa kamfatocin rahamar Allah mai girma da ɗaukaka, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa : **(Lallai Ubangijinku mai girma da ɗaukaka yana da wasu ranaku a cikin kwanakin shekara da suke cike da rahamarsa, saboda haka ku bijiro da kanku zuwa gare su, ta yiwu idan rahamar ta sami wani daga cikinku ya zamo ba zai taɓa taɓewa ba har abada)**.

Babu shakka kan cewa muna rayuwa ne a yanzu haka a cikin waɗannan kwanaki da suke kan gaba wajen daraja da girma, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya yawaita ladan ayyukan alhairi a cikinsu, inda ayyukan lada suka fi yawa a cikinsu, idan muka gwama su da wasunsu, kwanaki ne masu daraja, kuma lokuta ne masu ɗaukaka da Allah Maɗaukakin Sarki ya ɗaukaka sha'aninsu, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana matsayinsu da falalarsu, a cikin waɗannan falala da daraja akwai:

**Lallai Allah Maɗaukakin Sarki a cikin littafinsa mai girma ya rantse da su** a inda mai girma da ɗaukaka yake cewa: **((Ina rantsuwa da hasken alfijir a lokacin da yake korar duhun dare.. Da kuma darare goma da suke sanannu a wurin Allah.. Da duk wani abu da yake biyu-biyu da wanda yake tilo a**

**cikin komai))** **[al- Fajri: 1 -3],** mafi yawan malaman Tafsiri sun bayyana cewa: abin da ake nufi da **"darare goma"** su ne: goman farko na watan Zul Hajji, kuma lallai Allah Maɗaukakin Sarki ba ya rantsuwa da abu sai idan abin mai girma ne, saboda haka, rantsuwa da waɗannan darare girmamawa ne gare su, kuma ɗaukaka matsayinsu ne, da kuma bayyana girman sha'aninsu, da bayani akan falalarsu, da kuma shiryatarwa zuwa ga muhimmancinsu.

A cikin falalar da suke cikinsu, akwai: **bayanin cewa su ɗin kwanaki ne sanannu da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa akansu**: **((Su ambaci sunan Allah a cikin wasu kwanaki sanannu sakamakon irin yanda Allah Maɗaukakin Sarki ya azurta su da dabbobin ni'ima..))** **[al- Hajji: 28]**, lallai kwanaki ne da Musulmi yake samun tattaruwar muhimman ayyukan ibada irinsu: sallah, da sadaka, da azumi, da Hajji, waɗannan ibadu a haɗe ba su tattaru a kowane lokaci ba sai a waɗannan kwanaki.

A cikin falalarsu akwai**: kasancewarsu kwanakin da Allah Maɗaukakin Sarki ya fi so,** Allah Maɗaukakin Sarki yafi son a gabatar da ayyuka na gari a cikinsu sama da wasunsu, lokacin ne na samun riba, da buɗe ƙofofin tsira, fage ne na rige- rige zuwa ga aikata ayyukan alhairi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu ranakun da Allah yafi son a gabatar da ayyuka na gari kaman waɗannan kwanakin)**, yana nufi kwanaki goma na Zul Hajji, sai suka ce : ya Manzon Allah, har da jahadi wajen ɗaukaka kalmar Allah? Sai ya ce: **(Koda kuwa jahadi ne wajen ɗaukaka kalmar Allah, sai dai ga mutumin da ya fita da ransa, da dukiyarsa, bai kuma dawo da komai ba)**, saboda haka, ya kamata Musulmi ya ribaci wannan babban falala, da lada mai girma, ta hanyar ƙara kusantar Allah

Maɗaukakin Sarki da nau'o'i iri- iri na ayyukan biyayya, da ibadu.

Lallai a cikin ayyukan da Allah Maɗaukakin sarki ya fi son a kusance shi da su a cikin waɗannan kwanaki akwai: **Hajjantar ɗakinsa mai alfarma ga wanda duk Allah ya ba shi iko,** Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Hajji na kasancewa ne a wasu watanni da kuka sani, domin dai al'amarin Hajji sananne ne a wajenku tun zamanin Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm), wanda shi ne: watan Shawwal, da Zul- Ƙi'ida, da Zul- Haj, duk wanda ya ƙuduri aniyar aikin Hajji a cikin waɗannan watanni, ya kuma fara shi, to, ya kiyaye ladubbansa, cikin ladubban Hajji: lallai ne mai harama ya tsarkaka ga barin kusantar mata, da saɓo na zagi da makamantan haka, haka ma ya nesanci gardama da ba'a tare da waninsa cikin mahajjata, ya nesanci duk wani abin da zai kai zuwa ga faɗa da husuma, duka wannan saboda mahajjanci ya fita daga harami yana cikin tsarkake zuciya…))** **[al- Baƙra: 197],** Hajji shi ne rukuni na biyar a cikin rukunnan Musulunci, sai an yi shi ne aka cika umurni, kuma da shi ne ake gafarta zunubai, a kuma sake haihuwar bawa ya dawo sabo, inda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Duk wanda ya yi aikin Hajji, bai saki bakinsa wajen zancen batsa ba, bai kuma aikata fasiƙanci ba, to zai dawo tamkar ranar da mahaifiyarsa ta haife shi)**.

Lallai Hajji wani dama ne mai girma na koyan kyawawan ɗabi'u da falala, domin a lokacin ne Musulmai yake rainon ɗabi'ar tsoron Allah Maɗaukakin Sarki a zuciyarsa, ya kuma koyi yanda zai yi wa sha'awarsa, da zuciyarsa burki, ya kuma yi ado da kyawawan ɗabi'u irinsu fifita 'yan uwansa akan

kansa, ba wai yin baba- kere a cikin komai ba, ya kuma koyi wadatuwa da kamewa na zuciya, ba roƙo, da bara, da maula ba, a kuma cikinsa ne Musulmi yake koyan kamewa na harshe, da kuma taƙaituwa a ayyuka masu alfanu, da bin doka da oda, lallai dole ne mahajjanci ya aiwatar da kyawawan ɗabi'un Musulunci a aikace; domin idan ya gama Hajjinsa ya zamo tamkar ɗan makarantar da ya kammala karatunsa, bayan ya mallaki cikakkun kyawawan ɗabi'u, sun kuma riga sun zama masa jiki.

Lallai muna ƙara tabbatar da cewa: ibadar aikin Hajji saƙo ne na zaman lafiya zuwa ga duniya baki ɗaya, Hajji gaba ɗayansa zaman lafiya ne da salama, ɗaukacinsa aminci ne, shi mahajjanci ba ya faɗa, ba kuma ya gardama, ba kuma ya razana abin farauta, ko ya tsora ta su, balle kuma ya kashe su, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah, kada ku kuskura ku kashe abin farauta a lokacin da kuke cikin ihramin Hajji..))**, wannan amincin bai taƙaita kawai da mutane da dabbobi ba, ya ƙetara har zuwa ga tsirrai, lallai wajibi ne mahajjanci ya yi zaman lumana har da tsirrai, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai wannan gari ne da Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya masa hurumi, ba a yanke tsirran cikinsa, ba kuma a kai farmaki wa abin farautar cikinsa, ba kuma a tsintuwa a cikinsa, sai dai da niyyar a miƙa wa mai ita)**, lallai babu shakka, wannan wani horaswa ne ga mahajjanci Musulmi, akan yanda mutane, da dabbobi, da tsirrai za su aminta daga cutarwarsa har bayan ya dawo daga aikin Hajjinsa da ya sauke farali, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya riga ya ba mu labarin cewa Musulmi na haƙiƙa shi ne wanda mutane gaba ɗayansu suka

aminta daga sharrin harshensa, da hannayensa, a inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake faɗi a huɗubarsa ta "Hajjin Ban- kwana": **(Shin ba na faɗa maku wane ne mumini ba? Shi ne wanda mutane suka aminta masa a dukiyoyinsu da rayukansu, shi kuma Musulmi shi ne: wanda mutane suka aminta daga sharrin harshensa da hannayensa, Mujahidi kuma shi ne: wanda ya sabar wa kansa da yi wa Allah biyayya, Mai hijira kuma shi ne: wanda ya ƙaurace wa ayyukan kura- kurai da na zunubai)**.

A cikin ayyuka masu falala da ake son bayi su kusanci Allah Maɗaukakin sarki da su a cikin waɗannan kwanaki masu albarka akwai: **Azumi**, lallai Azumi na cikin manyan ayyukan biyayya, kuma muhimmai wajen neman kusanci da Allah mai girma da ɗaukaka, Allah Maɗaukakin Sarki ya jingina shi da shi; saboda girma gami da darajarsa, yana faɗi a cikin Hadisi Ƙudsiy cewa: **(Dukan ayyukan ɗan Adam nasa ne in banda Azumi, shi kam nawa ne, ni ne kuma zan yi sakayya akansa),** Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda ya yi Azumi na rana ɗaya saboda Allah, Allah zai nesanta shi da wuta kwatankwacin tafiyar shekaru saba'in)**, saboda haka ne aka so Musulmi ya yi Azumi a cikin kwanaki tara na watan Zul- Hajji gwargwadon iko, azumtar waɗannan ranaku suna cikin ayyukan da Allah Maɗaukakin Sarki ya fi so, musamman Azumin ranar Arfa ga waɗanda ba su sami daman zuwa aikin Hajji ba, domin Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya keɓance azumutar ranar Arfa a cikin kwanaki goman Zul Hajji, a inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Ina tsananin kwaɗayin Allah ya sanya Azumin ranar Arfa ya zamo kaffara na shekarar da ta gabata, da shekara mai bi mata)**.

Ranar Arfa ɗaya ce daga cikin ranakun Allah Maɗaukakin Sarki da yake bayyana wa bayinsa da sifofin rahama, da gafara, da 'yanta su ga barin wuta, rana ce da ake amsar addu'a, ake kuma share kura- kurai, Allah Maɗaukakin Sarki kuma ya yi wa mala'iku alfahari da bayinsa da suke a doron ƙasa, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu wata rana da Allah yake yawaita 'yanta bayi ga barin shiga wuta kaman ranar Arfa, lallai Allah yana kusantowa zuwa ga bayinsa, sannan ya yi wa mala'iku alfahari)**, ita ce ranar da Allah ya cika addininsa a ciki, ya kuma kammala ni'imominsa, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa: wani mutum Bayahude ya ce masa: Ya Amiral- Muminina, akwai wata aya a cikin littafinku, kuna karantawa, da mu Yahudawa ta sauka ma wa, da mun sanya ranar saukarta ta zamo ranar idi.. sai ya ce: wace aya? Sai ya ce: **((Lallai kam a yau na cika maku hukunce-hukuncen addininku, haka ma na cika ni'imata a gare ku ta hanyar tabbatar da ku akan addini, na kuma zaɓa maku addinin Musulunci ya zamo shi ne addininku)) [al- Ma'ida: 3]**, sai Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: "Lallai mun san wannan ranar, da ma wurin da aka saukar wa Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) a lokacin yana tsaye a filin Arfa a ranar Juma'a".

Haka ma an so Musulmi ya yawaita ambaton Allah Maɗaukakin Sarki a cikin waɗannan kwanaki, zikiri shi ne rayuwar zukata, da kuma shi ne ake samun natsuwa ta haƙiƙa, Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: **((Su ne waɗanda suka yi imani da Allah, zukatansu kuma suka sami natsuwa, da ma can da zikirin Allah ne zukatan suke samun natsuwa na**

**haƙiƙa))** **[ar- Ra'ad: 28]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu wasu kwanaki da suke da girma a wurin Allah, ko wadda Allah ya fi son a gabatar da ayyukan a cikinsu sama da waɗannan kwanaki goman, saboda haka, ku yawaita yin "Tahlili" (faɗin: La'ilaha illalLahu) da "Takbiri" (Faɗin: Allahu Akbar), da "Tahmidi" (faɗin: Alhamdu lilLah).** Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) yakan yi kabbara daga ƙubbarsa a Mina, mutane da suke cikin Masallaci su ji shi, su kuma yi kabbara da kabbararsa, mutanen da suke kasuwa ma su ɗauka da kabbara, har Mina ta girgiza saboda gunjin **Allahu Akbar**), haka ma Sayyiduna Abdullahi Bn Umar (Allah ya ƙara yarda da su) yakan yi kabbara a Mina a cikin waɗannan ranaku a ƙarshen kowace sallah, kai har ma idan yana kan shimfiɗarsa, da majalisinsa, da idan yana tafiya, saboda haka, an so Musulmi ya bayyana kabbararsa a wannan rana, saboda girmama Allah Maɗaukakin Sarki, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Shin ba na faɗa maku mafi alhairin ayyukanku, da suka fi ɗaukaka darajar, suka kuma fi tsarki a wurin Ubangijinku, suka kuma fi maku alhairi akan ku sadaukar da zinare da dukiya, suka kuma fi ku haɗu da maƙiya a filin daga ku kashe su, su kashe ku ba?, sai muka ce: Na'am, sai ya ce: Zikirin Allah Maɗaukakin Sarki)**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Mu'az Bn Jabal (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa: Babu wani aiki a cikin ayyukan ɗan Adam da ya fi tseratar da shi daga Azabar Allah da ya kai zikirin Allah mai girma da ɗaukaka.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

---------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** A cikin manyan ayyukan da bayi suke kusantar Ubangijinsu mai girma da ɗaukaka a waɗannan kwanakin akwai: **yanka abin layya,** layya ibada ce daga cikin ibadun da ake yi wa Allah Maɗaukakin Sarki, alama ce ta addinin Annabi Ibrahim (AlaiHis Salam), kuma abu ne da yake nuni zuwa ga Sunnar Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam), Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Wannan kam duk wanda ya girmama ibadun Allah, to kuwa lallai yin hakan yana nuna tsoron Allah da yake a cikin zukata..)) [al-Hajji: 32]**, lokacin da aka tambayi Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa: Waɗannan abin layya fa? Sai ya ce: **(Sunnar Babanku Ibrahim ce)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ɗan Adam bai zai yi wani aiki a ranar layya da Allah ya fi so ba sama da zubar da jinin abin layya, lallai za su zo a ranar lahira da ƙahonsu da gashinsu, da kofatansu, lallai jininsu yana zuba ne a wani wuri a wajen Allah kafin ya zuba a ƙasa, saboda haka, ku yi wa juna albishir).**

Lallai layya nau'i ne daga cikin nau'o'in taimakekeniya tsakanin al'umma da take samar da soyayya, da jinƙai, da kuma haɗin kai tsakanin al'umma, lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ga rashi da talauci sun kama mutane, sai

ya ce masu: **(Duk wanda ya yi layya a cikinku kada ya rage wani abu daga cikin abin layyarsa bayan kwanaki uku)**, da shekara mai zuwa ta kewayo, sai suka ce: ya Manzon Allah, shin za mu yi kamar yadda muka yi a shekarar da ta gabata ne? Sai ya ce: **(Ku ci, ku kuma ciyar da wasu, ku kuma adana wani sashe, wancan abin da ya faru a shekarar da ta wuce, mutane suna cikin halin rashi ne na so ku taimaka a ciki)**, a duk sanda aka sami wadata da yalwa, sai a yi amfani da maganar Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yake cewa: **( Ku ci, ku kuma yi sadaka, ku kuma adana wani sashe)**, idan kuma mutane suna cikin ƙunci, da rashi, da talauci, sai a yi aiki da maganar (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yake cewa: **(Duk wanda ya yi layya a cikinku, kada ya rage wani abu daga cikin abin layyarsa bayan kwanaki uku)**.

Ya kamata mu sani cewa kaman yanda layya take tabbatuwa da yanka, haka ma take tabbatuwa da miƙa kuɗin abin layya ga amintattun ƙungiyoyi; domin su rarraba ga waɗanda suka cancanta, musamman ga waɗanda ba su da daman rarrabawa kaman yanda ya kamata, wannan ne zai bayar da dama isar da layyar zuwa ga waɗanda suka cancanta na haƙiƙa, ta hanya **"as - Sukuk"**, hakan kuwa zai ƙara yaɗa amfanin layyar, a gefe ɗaya kuma, ya yawaita ladanta, hakan kuma yakan taimaka wajen isar da alhairi ga waɗanda suka cancanta cikin izza da karama.. Lallai abu ne mai matuƙar kyau mawadata su haɗa tsakanin yin yanka, domin su yalwata wa iyalansu da 'yan uwansu makusanta, da kuma sayen **"as -Sukuk"**; domin yalwata wa sauran mutane, da talakawa a wuraren da suka fi tsananin buƙata..

Haka ma ya kamata Musulmi ya yawaita hanyoyin ayyukan alhairi, da amfaninsu zai koma zuwa ga ɗaukacin mutane, ya yawaita yin sadaka; domin shigar da farin ciki, da annashawa a cikin zukatan talakawa da mabuƙata, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya kwaɗaitar da bayinsa wajen ciyarwa, yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da Allah da ranar lahira, ku ciyar da wani sashe na abin da Allah ya azurta ku ta hanyoyin alhairi, ku yi gaggawan yin haka tun kafin ranar alƙiyama ta zo, ranar da dukanta alhairi ne; domin babu abubuwan da za su kai zuwa ga rikici, ba za ku iya riskar abin da ya kuɓuce maku a duniya ba, kasuwanci ko sadaka ba za su yi amfani a ciki ba, ceton wani koma bayan Allah ba zai yi amfani ba, zaluncin kafirai shi ne zai bayyana a wannan rana, saboda ba su amsa kirar gaskiya ba)) [al- Baƙra: 254]**, ya zo a cikin Hadisi mai girma cewa: **(Dukiya ba ta taɓa naƙasa saboda sadaka ba)**.

Lallai muna matuƙar buƙatar haɗa hannu domin tallafa wa marasa ƙarfi, da kuma jinƙan juna, da kuma damuwa da damuwar wasunmu, saboda mu yi wa maganar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) biyayya, a inda yake cewa: **(Musulmi ɗan uwan Musulmi ne, ba zai zalunce shi ba, ba kuma zai bayar da shi ba, duk wanda ya tsaya wajen biya wa ɗan uwansa buƙatarsa, Allah zai tsaya masa wajen biyan buƙatarsa, duk wanda ya yaye wa Musulmi wani baƙin ciki, Allah zai yaye masa baƙin ciki daga cikin baƙin cikin ranar alƙiyama, duk wanda ya suturta Musulmi Allah zai suturta shi ranar alƙiyama)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Kowane Musulmi akwai sadakar da ta wajaba akansa)**, sai suka ce: ya Annabin Allah, idan ba shi da shi fa? Sai ya ce: **(ya yi aiki da hannunsa, ya amfani kansa, ya kuma**

**yi sadaka)**, sai suka ce: idan bai samu ba fa? Sai ya ce: **(ya taimaki wanda yake cikin matsanancin buƙata)**, sai suka ce: idan bai sami hakan ba fa? Sai ya ce: **(to ya aikata alhairi, ya kuma kame ga barin sharri, hakan ma sadaka ne a gare shi)**..

**Ya Allah Ubangiji ina roƙonka taimaka mana wajen yawaita ambatonka, da gode maka, da kuma kyautata yi maka ibada, amin.**

- 45 –

## ISRA'I DA MI'IRAJI

Godiya ta tabbata ga Allahn da ya yi tafiya da bawansa cikin dare daga Masallaci mai alfarma zuwa Masjidul Aƙsa. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya ƙarfafa Annabawansa (Alaihimus Salam) da mu'ujizozi masu yawa, a cikin waɗannan mu'ujizozin akwai: **mu'ujizar Isra'i da Mi'irajin** da ya yi wa Annabinmu Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam), Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Tsarki ya tabbata ga wanda ya yi tafiyar dare da bawansa daga Masallaci mai alfarma zuwa Masjidul Aƙsa da muka sanya albarka a garuruwan da suke gefensa; saboda mu nuna masa wasu daga cikin ayoyinmu, lallai da ma can shi Allah mai yawan ji da gani ne)) [al- Isra'i: 1]**. Duk wanda zai yi duba ta lura game da wannan mu'ijiza ta Ubangiji, zai ga tana ɗauke da darussa da abubuwan lura masu tarin yawa, kaman: **bayani iko da ƙudurar Allah Maɗaukakin Sarki da ba su da iyaka,** iko da ƙudurarsa mai girma da ɗaukaka sun fi ƙarfin duk wata ƙa'ida,

ko doka, Allah mai girma yana cewa: **((Shi al'amarinsa mai girma da ɗauaka idan ya so abu cewa masa kawai yake yi: kasance, take kuwa sai ya kasance))** **[Yasin: 68]**.

Haka ma akwai: **sauƙi bayan wahala, da yaye damuwa bayan tsanani,** bayan Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya jure nau'o'i mabambanta na cutarwa daga Ƙuraishawa akan hanyarsa ta isar da saƙon Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka, sai ga mu'ijizar Isra'i da Mi'iraji a wani mataki ma karrama shi da ƙarfafa masa gwiwa, wannan wani yaye damuwa ne bayan tsanani, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai a cikin kowane abu mai wahala akwai sauƙi mai yawa da yake mamaye da shi. Lallai a tare da kowane abu mai wahala akwai sauƙi mai tarin yawa))** **[as- Sharhi: 5 – 6]**.

Haka ma akwai: **girman matsayi Ubudiyya,** ma'ana: zamowa bawa na Allah, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Sai Mala'ika Jibrilu (AlaiHis Salam) ya isar wa bawan Allah wahayin da aka yi masa))** **[an- Najmi: 10]**, lallai zamowa bawan Allah, girma ne da karramawa, kuma wannan shi ne manufar Allah Maɗaukakin Sarki ta yin halitta, da kuma aiko ɗaukacin Annabawa.

Haka ma akwai: **bayyana matsayin Masjidul Aƙsa,** domin nan ne wurin da Manzon Allah ya yi Isra'i zuwa gare shi, daga kuma nan ne aka fari tafiyar Mi'iraji zuwa sammai, nan ne farkon alƙibla, kuma Masallaci na uku wajen hurumi, muna roƙon Allah mai girma da ɗaukaka ya ƙarfafi masu zaman ribaɗi a cikinsa da geffansa, ya dawo da shi hannun Musulmai cikin aminci.

Haka ma akwai: **gima da matsayin da sallah take da shi, da bayyana falalarta, da kuma abubuwan da Allah ya keɓance ta**

**da shi**, lokacin da aka yi Isra'i da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), aka kai shi har zuwa ƙololuwa da maƙura, wanda take a sama ta shida.. a lokacin ne akan ba shi abubuwa guda uku: salloli biyar, da ƙarshen Suratul Baƙra, aka kuma gafarta wa duk wanda ya rasu a cikin al'ummarsa ba tare da ya haɗa Allah da wani a wajen bauta ba.

Haka ma akwai: **bayani akan dangantakar da take tsakanin addinai**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(.. Annabawa 'yan uwa ne na uba ɗaya, da mahaifansu mata ne suke da bambanci, amma addininsu ɗaya ne)**, lallai an tattara Annabawa a daren Isra'i da Mi'iraji, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi masu limanci, suka yi maraba da shi, suka yi masa addu'a.

Haka ma akwai: **yin aiki da asbabu,** lokacin da (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya isa Baitul Maƙdisi ya ɗaure Alburaƙ, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(.. Sai na ɗaure ta da tarnaƙin da Annabawa suke ɗaure abin hawansu).**

Haka ma akwai: **fifikon masu gaskiyar imani akan wasunsu**, lokacin da suka ce wa Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi): Ba ka fa ji mutumin naka ba, yana riya cewa an yi tafiyar dare da shi a wannan daren zuwa Baitul Maƙdisi? Sai ya ce: Shin ya faɗi haka? Sai suka ce: ƙwarai kuwa, sai ya ce: Idan dai har ya faɗi haka, to gaskiya ne, sai suka ce: yanzu kai ka gasgata shi akan cewa an yi tafiya da shi a dare ɗaya zuwa Baitul Maƙdisi, ya kuma dawo kafin wayewar gari? Sai ya ce: Ƙwarai kuwa, saboda na riga na gasgata shi a abin da ya fi haka; na gasgata shi game da wahayin da yake zuwa masa daga sama safe da maraice, saboda haka ake kiransa da As-Siddiƙ.

**Wannan kenan, ina neman wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki..**

-------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da amincin Allah su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabinmu Muhammadu da Alayensa da Sahabbansa, da waɗanda suka biyo bayansu.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Kaman yanda Suratul Isra'i ta yi magana game da wannan tafiya mai albarka, haka ma ta yi magana akan kyautata wa iyaye, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai Ubangijinka ya riga ya hukunta kada a bauta wa kowa sai shi, su kuma iyaye a kyautata masu..)) [al- Isra'i: 23],** haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya keɓance uwa da wata kulawa ta musamman, saboda irin ƙoƙarin da take yi wajen ɗaukan ciki, da shayarwa, gami da tarbiyya, mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai mun yi wa ɗan Adam wasici da ya kyautata wa iyayensa biyu, mahaifiyarsa ta ɗauki cikinsa cikin wahala akan wahala..)) [Luƙman: 14]**, lokacin da wani mutum ya tambayi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam): wane ne ya fi cancanta na kyautata masa a cikin mutane? Sai ya ce: **(Mahaifiyarka),** sannan ya ce: sai wane? Sai ya ce: **(Sai mahaifiyarka)**, sannan ya ce: sai kuma wane?, sai ya ce: **(Sai mahaifiyarka)**, sannan ya ce: sai kuma wane?, sai ya ce: **(Sannan mahaifinka)**, Shari'a mai girma ta sanya yi wa uwa biyayya ɗaya ne daga cikin muhimman hanyoyin samun yardar Allah Maɗaukakin Sarki, lallai wani mutum ya zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana neman a yi masa izinin fita jahadi, ya tambaye shi: **(Shin mahaifiyarka**

**tana taye?)**, sai ya ce: Ey, sai ya ce: **(Ka koma ka yi mata biyayya)**, da ya matsa da tambaya, sai ya ce masa: **(Kai kuwa malam, ka lizimci yi mata biyayya, inda take nan aljanna take)**.

Ana yi mata biyayya ne ta hanyar girmama ta, da kuma saka mata da abubuwan alhairi irin yanda ta gabatar, da sanya ta cikin farin ciki, biyayyar kuma tana cigaba har bayan wafatinta ta hanyar yi mata addu'a, da nema mata gafara, da yin sadaka a maimakonta, da yin biyayya ga masoya da ƙawayenta, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai biyayyar da ta fi ƙarfi ita ce: mutum ya sadar da zumunci da abokan mahaifinsa)**.

**Ya Allah Ubangiji ka tabbatar da mu akan addininka, ka kiyaye mana iyayenmu maza da mata, da ƙasarmu, da sauran ƙasashen duniya.**

- 46 –

## TARE DA MU'UJIZAR "ISRA'I DA MI'IRAJI"

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Mun ambaci tsarki Ubangijin da ya yi "Isra'i" da bawansa cikin dare, daga Masjidul harami "Ka'aba" zuwa Masjidul-Aƙsa "Baitul maƙdisi" da muka sanya albarka a dukan garuruwan da suke kewaye da shi; mun yi haka ne domin mu nuna masa ayoyinmu, lallai shi Allah mai yawan ji da gani ne)) [al- Isra'i: 1]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk waɗanda suka bi su da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Babu shakka "Isra'i da Mi'iraji" tafiya ce da take da sirrori masu girma, tafiya ce da ba a taɓa yin makamanciyanta ba a tsawon tarihin Bil'adama, lallai ta faru ne domin a girmama cikamakin Annabawa da Manzanni, domin a yaye wa (SallalLahu alaiHi wa sallam) damuwa, bayan wasu shekaru da -shi da sahabbansa- suka ɗanɗani nau'o'i iri- iri na azaba, da kama- karya, da cutarwa, bayan ba a wuce kwanaki da shiga shekara ta goma da aiko shi ba (SallalLahu alaiHi wa sallam), lokacin da ya yi rashin babban bango da yake jingina da shi,

wato baffansa Abuɗalib, ya kuma rasa matarsa Sayyida Khadija (Allah ya ƙara yarda da ita), baiwar Allah, mai cikakken hankali, da soyayya ga mijinta, wadda wurinta yake komawa a duk sanda wani abu mai tsanani ya tunkaro shi (SallalLahu alaiHi wa sallam).

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ƙara shiga cikin damuwa bayan tafiyar da ya yi zuwa garin "at-Ta'if", inda ya fuskanci wahalhalu masu tsanani a cikin rayuwarsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), bayan irin cutarwar da mutanensa suka yi masa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fita daga garin zuwa garin "at-Ta'if" da tunanin ya sami goyon-baya daga mutanen garin, amma dai a ƙarshe sai suka cutar da shi, sama da yadda mutanensa suka cutar da shi, domin sun sanya bayinsu ne da ƙananan yara, suka yi ta jifansa da duwatsu, abin da har ya yi sanadiyyar zubar masa da jini (SallalLahu alaiHi wa sallam), akan hanyarsa ta dawowa ne ya fuskanci Allah Ubangijinsa da wannan addu'a mai shiga zuciya, da take ɗauke da ma'anar yi wa Allah bauta, da kuma cikakken ƙasƙantar da kai ga Allah Maɗaukakin Sarki, wanda shi kaɗai yake ba shi da abokin tarayya, yana cewa: **(Ya Ubangiji gare ka nake kai ƙarar raunin ƙarfi na, da ƙarancin dabara ta, da wulaƙanta ta a hannun mutane, ya wanda ya fi kowa tausayi, Ubangijin gajiyayyu, kai ne Ubangijina, wurin wa za ka miƙa ni? Shin a hannun manesancin da zai ɗaure mini fuskarsa za ka miƙa ni, ko kuwa a hannun maƙiyin da ka mallaka al'amari na a hannunsa? In dai ba kai ne ka yi fushi da ni ba, babu abin da zai dame ni, sai dai lafiyarka tafi yalwa a gare ni. Ina neman tsari daga hasken zatinka, wanda ya keto wa duffai, ya kuma gyara ɗaukacin al'amurran duniya**

**da na lahira, akan kada ka saukar mini da fushinka, ko kuma fushinka ya sauka a kai na, girma da aminci sun tabbata a gare ka har sai ka yarda, babu dabara, babu ƙarfi sai da gare ka).**

Daga cikin wannan tsanani ne, kwatsam sai ga kyautar Allah Ubangiji mai girma, tafiya ce ta "Isra'i da Mi'iraji", tafiyar da a cikinta Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) sirrori na haƙiƙanin ghaibi, da sirrorin halittu, sirrorin da babu wani mala'ika makusanci, ko Annabi da aka aiko, da ya taɓa samun irin wannan karamci da aka yi wa (SallalLahu alaiHi wa sallam), an kuma yi hakan ne domin a ƙarfafa zuciyarsa, ta yanda zai ƙara samun yaƙini da imani da cewa lallai yana tare da Allah Maɗaukakin Sarki, yana ƙarƙashin kulawarsa da kiyayewarsa, Allah ya jiƙan Imam al-Busiriy da yake cewa:

**"An yi tafiya da kai daga haramin Makka, zuwa haramin Baitul maƙdisi cikin dare, irin tafiyar da cikakken wata ɗan daren goma sha huɗu yake yi a cikin dare mai tsananin duhu..**

**A haka ka kwana, kana hawa muƙamai daga wancan zuwa wannan, har sai da ka kai muƙamin "Ƙãba ƙausaini", babu wanda ya taɓa kai wa, kai ma babu wanda zuciyarsa ta taɓa hararo masa wannan matsayin balle ya nema…**

**Haka ɗaukacin Annabawa da Manzanni suka shugabantar da kai akansu, suka gabatar da kai irin gabatarwar da ake yi wa wanda ake yi masa hidima ga masu yin hidimar.."**

Lallai mu'ujizar "Isra'i da Mi'iraji" tana cikin manyan mu'ujizozi da ayoyin da Allah Maɗaukakin Sarki ya karrama Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) da ita, lallai zai yi kyau mu rusuna a gaban wannan rana mai albarka; domin mu

ɗauki darussa da abubuwan lura a cikin wannan babban abu da ya faru sau ɗaya a cikin tarihin bil'adama:

**Babu shakka, yin riƙo da sababi, ko dalili ba yana nufin rashin dogaro da Allah Maɗaukakin Sarki ba ne,** Allah Maɗaukakin Sarki ya hore wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) wata dabba mai suna "Buraƙa", domin ta zamo masa tsanin da za ta isar da shi zuwa ga wannan tafiya, duk kuwa da cewa Allah Maɗaukakin Sarki yana da cikakken ikon ya gudanar da wannan tafiya, ba tare da bi ta wani tsani, ko hanya ba.. Sannan duk da irin cikakken imani, da yaƙini, da cikakken dogaro da Allah Mai girma da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake da shi, duk da haka, lokacin da ya isa zuwa ga Baitul Maƙdisi, ya ɗaure wannan dabba "Buraƙa" da Allah Mai girma da ɗaukaka ya hore masa ita, saboda ya koya wa al'ummarsa wajibcin aiki da sababi da dalili, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Na ɗaure ta a turken da Annabawa suke ɗaure dabbobinsu)**; Imam an-Nawawi yana cewa: "Ɗaure Buraƙa da ya yi, yana karantar da ɗaukan mataki, da kuma yin amfani da sababi, kuma hakan ba kishiya ne na dogaro da Allah ba".

Shi mumini na gaskiya, yakan yi aiki ne irin na mutumin da yake ganin kaman babu abin da zai iya tseratar da shi, sai ayyukan da yake yi, yakan kuma dogara da Allah, irin dogaron mutumin da ya san cewa babu abin da zai same shi, sai abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya rubuta masa, irin wannan matsakaiciyar fahimta ce ake nufi a Hadisin da (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa –a ɓangare bin sababi da dalili-: **(Idan lokacin tashin alƙiyama ya yi, alhali akwai iccen dabino a hannun ɗaya daga cikinku, idan dai har ya sami dama na ya**

**dasa shi, to ya dasa)**, a ɓangaren dogaro da Allah kuma, yake cewa: **(Da a ce za ku dogara da Allah kaman yanda ya kamata, da kuwa ya azurta ku, kaman yanda yake azurta tsuntsu, suna wayen garin cikinsu wayam, su kuma yammanta cikinsu a cike)**.

**'Yan uwantakar ɗaukacin Annabawa da Manzanni,** lallai ɗaukacin Annabawa suna ɗauke da saƙo ne guda ɗaya a ɓangaren ginshiƙan abubuwa da aƙidu, koda kuwa an sami bambanci a wurin shari'o'i da manhajojin da suka zo da su, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kafin kai ba mu aiko wani Manzo ba, face sai mun yi masa wahayin cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai ni, saboda haka ku bauta mini)) [al- Anbiya'i: 25]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Annabawa tamkar 'ya'yan uba ɗaya ne, mahaifansu mata suna da bambanci, amma dai addininsu ɗaya).**

Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya yi ƙarin haske, akan wasiyyoyi guda goma da suka zo a ayoyin da Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ka ce masu: ku zo in karanto maku abubuwan da Ubangijinku ya haramta maku: ya haramta kada ku haɗa shi da wani a wurin bauta, su kuma iyaye a kyautata masu ƙwarai da gaske, kada ku soma ku kashe 'ya'yanku saboda tsoron talauci, mu ne muke azurta ku, mu kuma azurta su, kada ku kuskura ku kusanci alfasha na zahiri da na baɗini, kada ku soma ku kashe ran da Allah ya haramta, sai dai idan akwai haƙƙi a kai, da wannan ne Allah ya yi maku wasici; domin ku hankalta.. Kada kuma ku kuskura ku kusanci dukiyar maraya ba da nufin inganta ta**

**ba, ku bari har sai ya kai munzalin mallakar hankalinsa, sannan ku ba shi dukiyarsa, ku cika mudu da ma'auni cikin adalci, ba mu ɗaura wa rai wani abu ba, sai wanda za ta iya, idan za ku yi magana ku yi adalci, koda kuwa akan makusancinku ne, ku cika alƙawarin da kuka ɗauka wa Allah, da wannan ne Allah ya yi maku wasici; domin ku samu ku wa'aztu.. Lallai wannan ita ce miƙaƙƙiyar hanya ta, kawai ku bi ta, kada ku soma ku bi sauran hanyoyi, balle su raba ku da hanyarsa, da wannan ne Allah ya yi maku wasici, domin ku samu ku ji tsoron Allah))** **[al- An'am: 151 – 153]**: Sai Ibn Abbas ya ce: "Waɗannan bayyanannun ayoyi ne, ba a ta taɓa share su a cikin dukan shari'o'i, ko addinai da Allah ya aiko ba, dukan su an haramta wa mutane gaba ɗaya, su ne ake kira da **"Ummul kitabi"**, -ma'ana asalin litattafai da harsashensu- duk wanda ya yi aiki da su ya shiga aljanna, wanda kuma ya yi watsi da su zai shiga wuta".

Lallai a cikin manyan ayoyin da Allah Maɗaukakin Sarki ya karrama Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) da su, akwai tattara masa Annabawa da Manzanni da ya yi a "Baitul Maƙdisi", inda ya yi masu limanci, sannan kuma suka tarbi (SallalLahu alaiHi wa sallam) a sama, suna masu yi masa maraba, suna cewa: **(Muna maraba da nagartaccen Annabi, kuma nagartaccen ɗan uwa),** wannan kam shimfiɗa ce ta miƙa ragamar shugabanci a doron ƙasa zuwa ga Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), a gefe ɗaya kuma hakan zartar da alƙawurran da suka ɗauka wa Allah Maɗaukakin Sarki ne a aikace, Allah Mai girma yana cewa: **((Ya kai wannan Annabi (SallalLãhu alaiHi wa sallam), faɗa masu cewa: lallai Allah ya yi alƙawari da duk wani Annabi da aka saukar masa da littafi,**

**aka kuma ba shi ilimi mai amfani cewa idan wani Manzo da da'awarsa ta yi daidai da da'awarsu ya zo masu, lallai za su yi imani da shi, kuma za su taimake shi... Ya yi alƙawari da kowane Annabi akan haka, suka yi iƙirari da haka, suka shaida hakan akan kansu, Allah ma ya shaida hakan akan kansu, suka kuma isar da shi zuwa ga al'ummomin su cewa lallai wannan alƙawari ya wajabta masu yin imani da taimakon wannan Annabi, shin sun riske shi, ko ba su riske shi ba, sai ya zama dole ne al'ummominsu su yi imani da shi, su kuma taimake shi; saboda cika alƙawari da biyayyar da Annabawan su suka ɗauka)) [Ali Imran: 81],** Sayyiduna Aliyu Bn Abuɗalib, da Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) suna cewa: "Allah bai taɓa aiko wani Annabi ba, face ya ɗauki alƙawarin cewa lallai idan Allah ya aiko Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana raye zai yi imani da shi, ya kuma taimaka masa, ya kuma ba su umurnin su ɗauki irin wannan alƙawarin tare da al'ummominsu, cewa lallai idan Allah ya aiko Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) suna raye, to kuwa lallai za su yi imani da shi, su kuma taimaka masa"**.**

**Matsayin masjidul Aƙsa yana kusa da matsayin masjidul haram;** "Isra'in" da aka yi da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) a nan ta tsaya, daga kuma nan ne tafiyar "Mi'iraji" ta fara, zuwa saman sama, har zuwa **"Sidratul muntaha"**, kuma nan ne farkon alƙibla, shi ne kuma harami na uku bayan haramin Makka da haramin Madina, ɗaya daga cikin masallatai guda uku da ake niƙar-gari zuwa gare su; domin yin sallah a cikinsu, da kuma ladan da yake tattare da haka, bugu da ƙari, shi ne masallaci na biyu da aka gina a bayan ƙasa, an ruwaito

Hadisi daga Sayyiduna Abuzarrin (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: Na ce: Ya Manzon Allah, wane masallaci ne aka fara samarwa a bayan ƙasa? Sai ya ce: **(Masallacin harami)**, ya ce: sai na ce: sannan kuma wanne? Sai ya ce: **(Masallacin al-Aƙsa)**, na ce: shekaru nawa ne a tsakaninsu? Ya ce: **(Shekaru arba'in)**, a duk inda sallah ta riske ka a cikinsu ka yi, domin akwai falala a wurin), yin sallah a cikinsa sau ɗaya yafi yin sallah sau ɗari biyar a waninsa, in ba haramin Makka, da na Madina ba, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Falalar sallah a haramin Makka daidai yake da falalar salloli dubu ɗari a wani masallacin da ba shi ba, a Masallaci na kuma, daidai yake da salloli dubu, a masallacin baitul maƙdisi kuma, daidai yake da salloli ɗari biyar);** lallai masjidul Aƙsa, ɗaya ne daga cikin wurare masu tsarki a Musulunci, yana da wani matsayi na musamman a zukatan al'ummar Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam), amana ne da ta rataya a wuyan Musulmai gaba ɗaya, sam bai kamata su yi masa riƙon - sakainar - kashi, ko su yi saƙwa- saƙwa da shi ba, kuma dole ne mu karantar da 'ya'yanmu akan wannan ma'anar, gudun kada al'umma masu tasowa su manta da matsayi gami da tsarkin "masjidul Aƙsa" a wurin ɗaukacin Musulmai.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

--------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya.. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma

Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa.. Ya Ubangiji ka yi masa salati da aminci da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** A farkon watan Afrilu na kowace shekara, duniya takan ware rana; domin tunawa da marayu, lallai karantarwar addininmu na Musulunci ya riga ɗaukacin ƙungiyoyin da bil'adama suka kafa, bai wa marayu kulawa ta musamman, da ba su haƙƙoƙinsu kaman yanda ya kamata, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: ((**Suna tambayarka game da al'amarin marayu, da abin da Musulunci ya wajabta game da su, sai ka ce masu: lallai gyara al'amurran su alhairi ne a gare ku, ku da su, ku shigo da su cikin gidajenku, ku yi cuɗanya da su; saboda manufar gyara al'amurran su, ba ɓata su ko lalata su ba, su 'yan uwanku ne a rayuwar duniya, haka ne zai sanya ku yi cuɗanya da su. Lallai Allah ya san mai niyyar ɓarna a cikinku da mai niyyar gyara, saboda haka ku yi taka-tsantsan. Da Allah ya ga dama, da sai ya tsananta maku, ta yadda zai wajabta maku ɗaukan nauyin kulawa da marayu, ba tare da kun yi cuɗanya da su ba, ko ya ƙyale su ba tare da ya bayyana abin da ya wajaba game da su ba, su tashi suna ƙin sauran al'umma, hakan kuma kamar ɓata al'ummanku ne da tsananta masu, saboda takura masu da ƙasƙantar da su da kuke yi ne zai sa su ƙulle ƙiyayya ga jama'an da suke rayuwa a tsakanin su. Lallai al'amarin Allah buwayi mai rinjaye ne, kuma shi mai yawan hikima ne, ba ya shar'anta komai sai abin da yake akwai maslaharku a ciki))** **[al-Baƙra: 220],** mai lura na tadabburi zuwa ga wannan aya zai ga irin yanda Alƙur'ani mai girma ya yi amfani da kalmar **"Gyara"**, domin ta game ɗaukacin hanyoyin kulawa, da bayar da

muhimmanci, ita kalmar **"Gyara"** a nan, suna ne da ya game duk wani abu da maraya zai iya buƙatarsa, zai iya buƙatar taimako na kuɗi, to gyara a nan shi ne, a ba shi abin da yake buƙata na kuɗi, ko kayan da yake buƙata, ta kuma yiwu ya zamo yana da wadatarsa, amma yana buƙatar tarbiyya gami da kulawa, to a nan gyararsa ita ce: a ba shi kulawa, a kuma tsaya akan tarbiyyarsa, zai kuma yiwu yana buƙatar wanda zai ɗauki dukiyarsa ce cikin amana, ya yi masa kasuwanci da ita, ko kuma wanda zai kula masa da gonarsa, ko wata masana'anta tasa, gyara a nan, shi ne: a sami wanda zai gabatar masa da hakan, ta kuma yiwu ba ya buƙatar duka waɗannan abubuwa da muka lissafa, kawai abin da yake buƙata shi ne wanda zai kwafe makwafin mahaifinsa da ya rasa, wajen nuna masa soyayya, da jinƙai, to a nan ma gyara tana nufin a sami wanda zai yi masa haka, haka ma gyarar tana iya zamowa wajen dawo da shi ne akan hanya madaidaiciya bayan ya karkace, da sake sanya shi a turba ta tarbiyya ta gari, da gyara ɗabi'unsa, lallai ayoyin Alƙur'ani da Hadisan Ma'aiki sun zo ne da irin waɗannan ma'anoni duka, suna kiranmu zuwa ga gyara al'amurran marayu, da kulawa da sha'aninsu.

Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya kyautata wa marainiya, ko maraya da yake ƙarƙashinsa, to kuwa ni da shi a aljanna za mu zamo kaman waɗannan guda biyu –sai ya gwama tsakanin 'yar manuniya da yatsar tsakiya-)**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Gidan da yafi alhairi a cikin gidajen Musulmai, shi ne gidan da yake akwai marayar da ake kyautata masa, mafi sharrin gida a cikin gidajen Musulmai kuma shi ne : gidan da yake akwai marayar da ake musguna**

**masa),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ni da mai rainon maraya –nasa ko na waninsa- kaman haka muke a aljanna, ya yi nuni zuwa da 'yar manuniya da yatsar tsakiya).**

**Ya Allah Ubangiji, ina roƙonka ka sanya mu cikin mutanen da suke sauraron magana, su kuma ɗauki mafi kyawon ciki su yi aiki da ita, lallai waɗannan su ne waɗanda Allah ya shiryatar da su, lallai waɗannan su ne masu tsantsar hankali.**

**- 47 –**

## SAUYA ALƘIBLA DAGA BAITUL MAƘDISI ZUWA BAITUL HARAMI: DARUSSA DA IZINA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ba fuskantar wani sashe a gabãshi, ko yammaci shi ne ƙashin-bayan addini, ko matattara alhairi ba, matattara alhairi yana cikin abubuwa ne masu dama, wasu suna cikin rukunnan ingantacciyyar aƙida ne, wasu kuma suna cikin tushen ayyuka na gari da ibadu. Na farko shi ne: imani da Allah, da ranar tashin alƙiyama, da hisabi, da abubuwan da za su biyo bayan haka a ranar alƙiyama, da imani da mala'iku da littattafan da aka saukar wa Annabawa, da ma su kansu Annabawan. Na biyu shi ne: bayar da dukiya cikin jin daɗin rai ga talakawa, makusanta da marayu da waɗanda buƙatu da rashi suka yi masu yawa, da matafiyan da guzuri ya yanke masu, ba su da abin da zai isar da su zuwa ga manufarsu, da masu roƙon mutane, waɗanda buƙata ta tilasta masu yin haka, da kuma ciyarwa don manufar 'yanta bayi da 'yanta su ga barin bauta. Na uku: kiyaye sallah. Na huɗu: fitar da zakkar da aka wajabta. Na biyar: cika alƙawari a rai da dukiya. Na shida: haƙuri akan cutar da za ta faɗa wa rai, ko dukiya, ko lokacin haɗuwa da abokan gaba a wurin yaƙi. Waɗanda suka haɗa waɗannan aƙidu da ayyuka na alhairi su ne waɗanda suka yi gaskiya**

**cikin imaninsu, su ne waɗanda suka ji tsoron kafirci da ƙasƙanci, suka kuma nesance su))** **[al- Baƙra: 177]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kadai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya, b**ayan haka:**

Lallai kyaututtukan Allah Ubangiji da baiwarsa ga al'ummar Annabi Muhammadu a cikin watan Sha'aban sun fi ƙarfi a ƙirga su, ko a yi masu iyaka, cikin manyan abubuwan da suka faru, muke kuma farin- ciki da su a cikin watan Sha'aban, akwai: sauya alƙibla daga fuskantar "Baitul maƙdisi' zuwa kallon ɗakin Allah mai alfarma, wato "Ka'aba', wannan dai abin da yake a matsayi babban abu da ya faru a cikin tarihin Musulunci; domin a nan ne Allah Maɗaukakin sarki ya amsa buƙatar masoyinsa, kuma zaɓaɓɓe a wurinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), ya cika masa burinsa, da abin da yake fata na fuskantar 'Ka'aba" mai daraja a lokacin da zai yi sallah, inda nan ne alƙiblar kakansa Annabi Ibrahim (AlaiHis Salam).

A da kafin hijira, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana fuskantar "Baitul maƙdisi" ne idan zai yi sallah, kaman yanda Ubangijinsa ya umurce shi, a haka ya cigaba bayan ma ya yi hijira har na tsawon watanni goma sha shida –ko goma sha bakwai-, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana ta fatan a saukar masa da wahayi da zai umurce shi ya juya zuwa fuskantar "Ka'aba', yana fatan Allah ya cika masa wannan buri nasa a cikin zuciyarsa, halin da yake ciki kuma tamkar addu'a yake yi domin samun haka, yana mai tabbacin cewa lallai Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka zai biya masa buƙata, sai kuwa Allah

Maɗaukakin Sarki ya amsa masa, ya ba shi umurnin ya fuskanci "Ka'aba" mai daraja idan zai yi sallah, Allah Mai girma yana cewa: **((Lallai mun ga yadda kake jujjuya idanu sama, kana mai fatan wahayi ya sauka maka game da sauya alƙibla daga "Baitul- Maƙdisi" zuwa "Ka'aba" wanda kake so; saboda ita ce alƙiblar baban Annabawa Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm), baban Yahudãwã da Lãrabãwã, a can ne akwai "Maƙãmu Ibrahim", saboda haka alƙibla ce da ta game kowa, duk kuwa da cewa ta saɓa wa alƙiblar Yahudãwã, to, ga mu za mu ba ka abin da kake buƙata, fuskanci Masallaci Mai Alfarma idan za ka yi sallah, muminai ku ma haka ku fuskance shi a duk inda kuke…)) [al- Baƙra: 144].**

Babu shakka duk wanda ya lura da wannan gagarumin abu da ya faru, na sauya alƙibla, zai riski darussa da izina masu tarin yawa da amfani, da suke nuna girma da darajar da Allah ya yi wa Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam), muhimmin darasin a nan shi ne: **Girman matsayi da muƙamin Annabi a wurin Ubangijinsa,** wannan yana bayyana ne a maganar da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), yana cewa: **((To, ga mu za mu ba ka abin da kake buƙata na sauya alƙibla….)) [al- Baƙra: 144],** wannan kam falala ce da baiwa, gami da karamci, kuma hakan yana nuna irin girma da matsayin Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam), kaman dai da ma yanda ya faɗa masa cewa: ((**Kuma ina rantsuwa cewa lallai da sannu Ubangijinka zai cigaba da ba ka alhairan duniya da na lahira har sai ka gamsu)) [ad- Dhuha: 5],** kuma haka cigaba ne na falalar Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka a gare shi, mene ne ma zai sa hakan ba zai faru ba? bayan shi ne wanda Allah ya haskaka ƙirginsa, ya ce masa: ((**Tabbas mun**

**riga mun haskaka maka ƙirjinka da abubuwan da muka sanya a ciki na shiriya da imani))** **[as- Sharhi: 1]**, ya kuma sauƙaƙe masa duk wani abu da zai yi masa nauyi da wahala, ya ce: ((**Muka kuma sauƙaƙe maka abubuwan da suka yi maka wahala na wahalhalun da'awa, ta hanyar ƙarfafa maka gwiwa, da kuma sauƙaƙe al'amurranka))** **[as – Sharhi: 2]**, ya kuma gafarta masa zunubai, ya ce: ((**Mu ɗin nan –Ya Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa Ălihi wa sallam)- mun yi maka babban buɗi kuma bayyananne, ta hanyar nasarar da gaskiya ta yi akan ɓata.. Saboda Allah ya gafarta maka abin da ya wuce, wanda zunubi ne a matsayi irin naka, da ma abin da ba ka aikata ba…))** **[Fathi: 1 – 2]**, ya kuma tsarkake harshensa, ya ce: ((**Ba ya yin maganarsa akan son zuciya))** **[an- Najmi: 3]**, ya kuma tsarkake zuciyarsa, ya ce: ((**Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa sallam) bai yi ƙarya a abin da ya riga ya gani da idonsa ba))** **[an- Najmi: 11]**, ya kuma yabi hankalinsa, ya ce: ((**Lallai Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa Ălihi wa sallam) bai kauce ga barin hanyar gaskiya ba, bai kuma yi imani da ɓarna ba))** **[an- Najmi: 2]**, ya kuma tsarkake idanuwansa, ya ce: ((**Idanuwan Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ba su karkata ga barin abin da ya gani ba, ba kuma su ƙetare abin da aka ba shi umurnin ya gani ba))** **[an- Najmi: 17]**, ya kuma yabi malaminsa, ya ce: **((Mala'ika mai tsananin ƙarfi ne ya sanar da shi wannan wahayi))** **[an- Najmi: 5]**, ya kuma yabi ɗabi'unsa, ya ce: ((**Lallai kai ɗin nan mai riƙo ne da kyawawan sifofi da kyawawan ayyuka da Allah ya halicce ka a kai))** **[al- Ƙalam: 4]**, ya kuma tsarkake shi gaba ɗaya, ya ce: **((Lallai kuna da abin koyi mai matuƙar kyau a rayuwar Manzon Allah – SallalLahu alaiHi wa sallam))** **[al- Ahzab: 21]**.

Haka ma a cikin muhimman darussan da suke tattare da sauya alƙibla akwai: **wajibcin yin riƙo da manhajin daidaito "al-wasaɗiyya",** wannan babban abu da ya faru shi ne asalin daidaito na "al-wasaɗiyya" a cikin wannan al'umma, a inda Allah Mai girma da ɗaukaka yake cewa: ((**Saboda haka ne muka shiryatar da ku zuwa ga madaidaiciyar hanya, muka sanya ku kuka zamo al'umma mai adalci kuma zaɓaɓɓiya; saboda katartad da ku da muka yi da ingantaccen addini da aiki na gari, mun yi haka ne domin ku zamo masu tabbatar da gaskiya game da shari'o'in da suka gabata…))** **[al- Baƙra: 143].**

Wannan dai daidaiton da ma'anarsa take shiga dukan fagagen -rayuwa, ba tare da wuce - gona - da –iri, ko wofintarwa ba, daidaiton da shi ne adalci da duk wani abu mai kyau, daidaito da yin abu cikin tsari, wajibi ne mu dawo kan wannan daidaito da Allah Maɗaukakin Sarki ya karrama mu da shi, mu zamo masu daidaito na gaskiya a dukan al'amurranmu, inda Allah mai girma yake cewa: **((Kada hannunka ya zamo ƙamƙamo wajen alhairi, ka mayar da shi tamkar an sanya ƙarfe an ɗaure shi a wuyarka, ta yanda ba za ka iya miƙar da shi ba, kada kuma ka zamo mai sakin hannu wajen almubazzaranci da ɓarna, balle ka zamo abin zargi da rowa, mai kuma nidama bayan duk abin da yake hannunka ya fice saboda almubazzaranci da ɓarna..))** **[al- Isra'i: 29]**, mai girma da ɗaukaka ya ƙara cewa: **((Su ne waɗanda idan za su ciyar ba sa yin ɓarna, ba kuma sa yin ƙoro, a koda yaushe suna tsaka-tsakin waɗannan abubuwa guda biyu ne))** **[al- Furƙan: 67].** Imamul Auza'iy (Allah ya ƙara yi masa rahama) ya ce: "Allah Maɗaukakin Sarki bai taɓa bayar da wani umurni a Musulunci ba, face Shaiɗan ya zo maka ta hanyoyi biyu, ba shi da wata

damuwa da duk hanyar da ya sami nasara akanka, duk ɗaya ne a wurinsa: ko dai ta hanyar wuce -gona -da -iri, ko kuma hanyar wofintarwa", saboda haka, wajibi ne mu ɗauki tafarkin daidaito da sauƙaƙawa, ba tafarkin wofintarwa da nuna halin -ko -in -kula ba, mu riƙi tafarkin riƙo da addini da kyawawan ɗabi'u, ba tare da bin turbar tsanani, ko tsattsauran ra'ayi ba.

Sannan shaidar da al'ummar Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) za su yi wa sauran al'ummomi tana nuni zuwa ga wajibcin ita kanta al'ummar ta tsaya tsayin -daka wajen sauke haƙƙoƙin da suke a kanta, domin ta sami cancantar yin wannan shaidar, daidai da wannan karamci da Allah ya yi masu, an ruwaito Hadisi daga Abu Sa'idul Khudriy (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Za a zo da Annabi Nuhu (AlaiHis Salam) a ranar alƙiyama, sai a ce masa: shin ka isar da saƙo kuwa?, sai ya ce: Na'am ya Ubangiji, sai a tambayi al'ummarsa: shin ya isar maku da saƙo? Sai su ce: babu wani mai gargaɗi da ya zo mana, sai ya ce: su wane ne shaidunka? Sai ya ce: Muhammadu da al'ummarsa, sai a zo da ku ku yi masa shaida),** sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya karanta: ((**Saboda haka ne muka shiryatar da ku zuwa ga madaidaiciyar hanya, muka sanya ku kuka zamo al'umma mai adalci kuma zaɓaɓɓiya; saboda katartad da ku da muka yi da ingantaccen addini da aiki na gari, mun yi haka ne domin ku zamo masu tabbatar da gaskiya game da shari'o'in da suka gabata, kuma domin Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya zamo mai faɗa-aji akanku, ta yadda a rayuwar sa ya shiryatar da ku da shiryatarwar sa, bayan wafatin sa kuma sunnarsa ta shiryatar da ku))** **[al- Baƙra: 143].**

Haka ma a cikin muhimman darussa da suke tattare da sauya alƙibla akwai: **Irin yanda muminai suke saurin amsa umurnin Allah Maɗaukakin Sarki, da kuma umurnin Manzonsa (SallalLãhu alaiHi wa sallam)**: lallai wannan abu da ya faru babban alama ne na irin amincewar da Sahabbai suka yi da dukan abubuwan da Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya zo da shi daga Allah mai girma da ɗaukaka, lallai Allah ya haskaka ƙirginsu da gaskiya, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: ((**Game da alƙiblar "Baitul- Maƙdisi" kuwa, wanda muka shar'anta maka na ɗan wani lokaci, mun yi haka ne domin jarraba Musulmai, saboda mu bambance tsakanin wanda zai karɓi haka cikin biyayya, da kuma wanda son zuciya da ta'assubanci wa Lãrabãwã akan abin da Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm) ya bari za su rinjaye shi, har ya kai shi ga saɓa wa umurnin Allah, ya kuma ɓace ga barin hanya madaidaiciya. Lallai umurni da fuskantar "Baitul- Maƙdisi" na cikin al'amurra masu wahala, sai dai kawai ga wanda Allah ya datar da shi da shiriyarsa, bin wannan umurnin yana cikin rukunnan imani…**)) **[al- Baƙra: 143]**, sai kuwa suka buga misali na ban mamaki wajen saurin amsa umurnin Allah Maɗaukakin Sarki da umurnin Manzonsa (SallalLãhu alaiHi wa sallam); umurnin Allah na sauya alƙiblar Sallah daga "Masjidul Aƙsa" zuwa "Masjidul Haram", nan take muminai suka amshi wannan umurnin, suka juya –a lokacin suna cikin sallah- cikin imani da biyayya, ba wani ja'in -ja suka fuskanci ɗakin Allah mai alfarma, suka cika sallarsu, ba su ko jira sai sun kammala wannan sallah da suke yi ba, ba su yi wata- wata ba wajen zartar da wannan umurni; nan take suka juya –a lokacin suna halin ruku'i- daga "Baitul maƙdisi" zuwa "Baitul Harami", an

ruwaito Hadisi daga Abdullahi Bn Umar (Allah ya ƙara yarda da su), ya ce: **wata rana mutane suna sallar Asubahi a Ƙuba, sai wani mutum ya zo, ya ce: Lallai an saukar wa da Manzon Allah wahayi a daren nan, an umurce shi da ya fuskanci "Ka'aba", saboda haka, ku juya zuwa ga "Ka'aba", a lokacin suna kallon garin Sham ne, sai suka juya suka fuskanci "Ka'aba".**

A cikin muhimman darussan da suke tattare da haka akwai: **bayyana muhimmancin sallah da matsayinta, da kuma bayani game da rahamar Allah Maɗaukakin Sarki mai yalwa ga bayinsa;** lallai Alƙur'ani mai girma ya haɗa sallah da wasu abubuwa guda biyu masu girma da suka faru a cikin manyan abubuwan da suka faru a tarihin Musulunci, waɗannan abubuwa su ne: Mu'ujizar "Isra'i" da "Mi'iraji", inda a nan ne aka farlanta sallah a saman saman bakwai a daren "Isra'i" da "Mi'iraji"; domin hakan ya bayyana irin girmanta da matsayinta, haka ma Alƙur'ani mai girma ya haɗa ta da abin da ya faru na sauya alƙibla, ya kuma bayyana ta da lafazin imani, Mai girma da ɗaukaka yana cewa: ((**Lallai kam Allah ba zai taɓa salwantar da ladan imaninku da biyayyarku ba)) [al- Baƙra: 143]**, yana nufin sallolin da kuka yi kafin haka, an ruwaito Hadisi daga Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su), ya ce: lokacin da aka umurci Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) da ya fuskanci "Ka'aba", sai Sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) suka ce: ina matsayin 'yan uwanmu da suka rasu kafin yanzu suna fuskantar "Baitul maƙdisi" wajen sallah? Sai Allah mai girma da ɗaukaka ya saukar da: ((**Lallai kam Allah ba zai taɓa salwantar da ladan imaninku da biyayyarku ba)) [al- Baƙra: 143]**, wannan biyayya ce kuka yi, haka ma wancan

biyayya ce suka yi, a nan an kwantar da hankulan muminai da cewa: lallai sallolin da suka yi suna masu fuskantar "Baitul maƙdisi" duka karɓaɓɓu ne, sannan ayar ta rufe da sanyaya zukatan muminai, ta kuma kwaɗaitar da zukatan mutane baki ɗaya, a inda Allah mai girma ya ce: **((Lallai Allah mai yawan jinƙai da tausayin mutane ne))** **[al- Baƙra: 143]**, idan dai har Allah Maɗaukakin Sarki mai yawan jinƙai da tausayin mutane ne, to kuwa lallai wannan jinƙai da tausayin sai sun fi yawa akan muminai.

A cikin muhimman darussan da suke cikin sauya alƙibla akwai: **Dangantaka ta kud -da -kud da take tsakanin "Masjidul Haram" da yake a Makka, da kuma "Masjidul Aƙsa" da yake a Ƙudus,** da bayyana dangantaka mai ƙarfi da take a tsakaninsu, lallai Masallacin Harami ne farkon Masallacin da aka gina domin yi wa Allah Maɗaukakin Sarki bauta a bayan ƙasa, Masallaci na biyunsa kuma shi ne "Masjidul Aƙsa", an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuzarrin (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: Na ce: Ya Manzon Allah, wane Masallaci ne aka fara samarwa a bayan ƙasa? Sai ya ce: **(Masallacin harami)**, ya ce: sai na ce: sannan kuma wanne? Sai ya ce: **(Masallacin al-Aƙsa)**, na ce: shekaru nawa ne a tsakaninsu? Ya ce: **(Shekaru arba'in, a duk inda sallah ta riske ka a cikinsu ka yi, domin akwai falala a wurin).**

Lallai sauya alƙibla ya haɗa dangantaka mai ƙarfi tsakanin waɗannan Masallatai guda biyu, kaman yanda "Isra'i" da "Mi'iraji" suka haɗa tsakaninsu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Mun ambaci tsarkin Ubangijin da ya yi "Isra'i" da bawansa cikin dare, daga Masjidul harami "Ka'aba" zuwa Masjidul-Aƙsa "Baitul maƙdisi" da muka sanya albarka a**

**dukan garuruwan da suke kewaye da shi; mun yi haka ne domin mu nuna masa ayoyinmu, lallai shi Allah mai yawan ji da gani ne))** [al- Isra'i: 1]..

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati, shi da Alayensa da Sahabbansa, da duk wanda ya bi turba irin tasu har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai rayuwar Annabi (SallalLãhu alaiHi wa sallam) gaba ɗaya ta sifantu da shiga cikin kowane abu da zai zamo alhairi ga al'umma, tabbas (SallalLãhu alaiHi wa sallam) yana da shekaru goma sha biyar a duniya ne ya shiga cikin wata yarjejeniya da aka fi sani da "Halful Fudhul", inda manyan dangogin Ƙuraishawa suka taru a gidan Abdullahi Bn Jad'an, suka yi alƙawarin tsaya wa duk wani wanda aka zalunta cikin mutanen garin da ma baƙi, inda gaba ɗayansu za su haɗa kai wajen ƙwato masa haƙƙinsa, (SallalLãhu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai na halarci wata yarjejeniya a gidan Abdullahi Bn Jad'an, nafi sonta akan a ba ni jajayen raƙuma, da za a kira ni zuwa ga irinta a Musulunci tabbas zan amsa).**

Haka ma (SallalLãhu alaiHi wa sallam) yana da shekaru talatin da biyar a duniya ne ya shiga cikin aikin gayya na sake sabunta gina "Ka'aba", inda ya ɗauke duwatsu a kafaɗunsa

(SallalLãhu alaiHi wa sallam), ya kuma kawo ƙarshen wani yunƙuri na aukuwar fitina mai girma da ta so ta auku tsakanin dangogin Ƙuraishawa, a lokacin da suka yi saɓani akan wanda zai sami falalar ɗaura "Hajrul Aswad" a wurinsa na asali, a ƙarshe dai suka aminta da hukuncin da Annabi (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya yanke, inda kowane dangi suka wakilta wanda zai wakilce su wajen ɗaura "Hajrul Aswad" a wurinsa na asali.

Haka ma lallai Annabi (SallalLãhu alaiHi wa sallam) abin koyi ne, kuma jagora wajen shiga cikin duk wani abu da zai amfani al'umma bayan an aiko shi, abin koyi ne a komai, (SallalLãhu alaiHi wa sallam), shi ne ya fi kowa kyautatawa, ya fi kowa jarumta, ya fi kowa karamci, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Aliyu (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: **Mun kasance idan yaƙi ya yi yaƙi, muka haɗu da maƙiya, sai mu fake bayan Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam), babu wani daga cikinmu da ya fi shi zuwa daf da abokan gaba**. Haka ma (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya yi tarayya da Sahabbansa wajen haƙa ramin Handaƙ.

Lallai Annabi (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya kira al'ummarsa zuwa ga shiga cikin duk wani abu da zai yi amfani, ya kuma gargaɗe su ja da baya, ko nuna halin -ko -in -kula a cikin al'amurra, (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Kada wani daga cikinku ya yarda zamo ɗan –amshin -Shatan da zai riƙa cewa: Ni duk inda mutane suke nan nake, in mutane sun kyautata, ni ma sai na kyautata, idan kuma suka munana, ni ma sai in munana.. Ku dai ku sabar wa kawwunanku da idan mutane suka kyautata, ku ma ku kyautata, idan kuma suka munana, kada ku yi zalunci).**

Shiga cikin al'amurran al'umma masu kyau yana nufin cewa mutum ya fahimci alhaki, gami da nauyin addininsa da na ƙasarsa da suke a kansa, son ƙasa ba wai kawai ya taƙaita a cikin zuciya ba ne, a'a, dole a gani a ƙasa, a aikace, mutum mai shiga cikin ayyukan alhairai da suka shafi al'umma shi ne: wanda yake da ruwa -da -tsaki akan duk wani abu da ya shafi cigaban al'ummarsa, yana tasirantuwa da abin da yake faruwa a gefensa, kaman yanda shi ma yake yi wa al'umma tasiri mai amfani.

Lallai babu shakka a cikin irin wannan tarayya cikin ayyukan alhairi akwai shiga cikin kowane irin shiri da tsari da zai kai zuwa ga gina ƙasa, da kiyaye tsaro da kwanciyar hankalin al'umma, shin ta hanyar ba ta kariya daga barin abokan gaba ne, ko kuwa ta hanyar gabatar da ayyuka tuƙuru cikin nagarta da ƙwarewa, ko ta hanyar taimakawa da tausayawa a tsakanin 'yan ƙasa ɗaya, ko ta hanyar fitowa domin kaɗa ƙuri'u na zaɓe, ko na jin ra'ayi cikin amana, da son ƙasa, abin da hakan yake sanadiyyar ɗaukaka darajar ƙasa daidai da yanda kowane ɗan kishin ƙasa na gaskiya yake ji a zuciyarsa, kaman yanda Ahmad Shauƙiy yake cewa:

"Ƙasa tana da alhairan da ta gabatar a cikin jinin kowane mai 'yanci, tana kuma bin shi bashin haka".

**Ya** Allah **Ubangiji, muna roƙonka ka nuna mana gaskiya, ka kuma ba mu ikon yi mata biyayya, ka nuna mana ƙarya, ka kuma ba mu ikon guje mata, ka kiyaye ƙasashenmu da al'ummominmu da jami'an tsaronmu da suka sadaukar da kawunansu saboda mu, Amin.**

**- 48 –**

## RAMADHAN WATAN IBADA DA AIKI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, Allah mai girma ya shar'anta wajibcin Azumi domin tsarkake zukatanku da daidaita sha'awarku, da fifita ku akan dabbobin da suke bin sha'awarsu, shi wannan wajabta Azumi da aka yi maku kamar yadda aka farlanta wa al'ummomin da suka gabace ku, ba zai yi maku wahala ba, saboda wajibi ne akan mutane baki ɗaya, wajibcin Azumi da tsayawa dominsa duka domin rainon ruhin tsoron Allah a cikinku ne, da kuma ƙarfafa zukatanku da tsarkake su))** **[al-Baƙra: 183]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda a Hadisinsa mai girma yake cewa: **(Duk wanda ya yi Azumin watan Ramadhan cikin imani da neman lada a wurin Allah, to kuwa za a gafarta masa zunubansa da suka gabata**). Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Bayan haka:**

Allah Maɗaukakin Sarki cikin falalarsa ne ya sanya wa bayi wasu lokuta na alhairai, da albarkatu, gami da rahama suke

kwararorowa da bibiyan juna a cikinsu, yake kuma ninninka lada, bayan ya girmama shi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Ubangijinku mai girma da ɗaukaka yana da wata kamfata da yake yi a wasu kwanaki cikin shekara, saboda haka ku bijiro wa wannan kamfata, ta yiwu idan wannan kamfata ta haɗa da mutum ta sanya shi cikin waɗanda ba za su taɓa yin asara ba har abada),** tabbas a cikin mafi girma da albarka gami da falalar waɗannan kwanaki akwai: watan Ramadhan mai albarka; shugaban watanni, kuma jagoransu, ranakunsa duka ranaku ne na alhairai da falala, dararensa kuwa cike suke da tsarki gami da tsabta, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan yi haba- haba da zuwan watan Ramadhan, yakan kuma yi wa sahabbansa (Allah ya ƙara yarda da su) albishir da wannan babban kyauta na Ubangiji, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Watan Ramadhan mai albarka ya zo, Allah ya wajabta maku azumi a cikinsa, a cikinsa ake buɗe ƙofofin aljanna, ake kuma kulle ƙofofin wuta, ake kuma ɗaure shaiɗanu, akwai wani dare a cikinsa da ya fi watanni dubu alhairi, duk wanda aka hana masa alhairinta, to kuwa lallai ya yi asara).**

Sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) sukan roƙi Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya su riski watan Ramadhan, ya kuma taimaka masu wajen gabatar da nagartattun ayyuka a cikinsa, Imam Ibn Rajab (Allah ya yi masa rahama) yakan ce: Da yawa daga cikin salihan bayin Alah (Allah ya ƙara yi masu rahama) sukan share watanni shida suna addu'ar: Allah ya sanya su riski watan Ramadhan, sannan su sake share watanni shida

suna roƙonsa: ya amshi ibadunsu. Imam Yahya Bn Abu Kasir yana cewa: A cikin addu'o'insu akwai: **"Ya Ubangiji ka amintar da ni zuwa watan Ramadhan, sannan ka amintar mini da watan Ramadhan, sannan ka amshi ibadu na cikin aminci"**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Jabir Bn Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da su), Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya hau minbari, da ya hau matakala ta farko sai ya ce: **(Amin),** sannan ya hau ta biyu, sai ya ce: **(Amin),** sannan ya hau ta uku, sai ya ce: **(Amin),** sai sahabbai suka ce: Ya Manzon Allah, mun ji kana cewa : Amin har sau uku? Sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lokacin da na hau matakala ta farko ne Mala'ika Jibril (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zo, ya ce: Lallai bawan da ya riski watan Ramadhan har watan a fita ba a gafarta masa ba, ya yi asara, ni kuma na ce amin…).**

A daidai wannan lokacin da muke shirin tarbar wannan baƙo mai karamci –bayan 'yan kwanaki ƙalilan- ya zamo tilas mu yi koyi da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), da sahabbansa masu girma, mu yi koyi da su a cikin ibadun da suke yi da kuma ayyukan da suke gabatarwa a cikin wannan wata mai albarka; ya kamata kowane Musulmi ya halarto da niyyarsa, ya kuma ƙara jaddada ta, domin da niyya ne ayyukan bayi suke bambanta da juna a wurin Allah Maɗaukakin Sarki; saboda ita ce sirrin amsar ayyuka, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa : **((Lallai aiki ba ya inganta sai da niyya, kowane mutum zai sami abin da ya yi niyya akan aikinsa, duk mutumin da ya yi hijira zuwa ga Allah da Manzonsa, to kuwa ladan hijirarsa na wurin Allah da Manzonsa; duk kuma wanda ya yi hijira saboda neman duniyar da zai samu, ko saboda macen da zai aura; to kuwa**

**sakamakon hijirarsa yana komawa ne zuwa ga abin da ya yi hijirar saboda shi)),** an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: Dukan ayyukan ɗan Adam nasa ne ban da azumi, domin shi kam nawa ne, ni ne kuma zan yi sakayya akansa, azumi garkuwa ne, idan ranar azuminku ya yi, kada ku yi zance batsa, kada kuma ku yi faɗa- faɗa, idan wani ya zage ku, ko ya neme ku da faɗa, to ku ce : mu muna azumi, na rantse da wanda ran Muhammadu yake hannunsa, wallahi bashin bakin mai azumi ya fi ƙamshin almiski a wurin Allah).**

Kaman yanda ya kamata kowane Musulmi ya yawaita ayyukan alhairi da na biyayya a cikin watan Ramadhan mai albarka, ya kuma sifantu da abubuwan da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi wasici da su, yake kuma aikatawa, irinsu: gaggauta buɗa baki, da jinkirta sahur, inda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Al'umma ta ba za su gushe a cikin alhairi ba, matuƙar sun gaggauta buɗa baki, sun kuma jinkirta sahur)**, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ku yi sahur, domin akwai albarka a cikin sahur),** haka ma ya kamata a nesanci yin ɓarna da almubazzarancin abinci da abin sha, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ku kuma ci, ku sha, kada ku kuskura ku yi ɓarna, domin lallai Allah ba ya son masu ɓarna)) [al- A'araf: 31],** Mai tsira da aminci yana cewa: **(Ɗan Adam bai taɓa cika wani masaki mafi sharri da ya kai cikinsa ba, 'yan lomomin da za su sanya ya ji ƙarfi sun ishi ɗan Adam, amma idan ya zama dole sai ya ci da yawa: to ya sanya kashi ɗaya cikin uku ya**

**zamo na abinci, na biyun na abin sha, na ukun kuma na numfashi).**

Abu ne mai matuƙar kyau masu hali su muhimmanta buƙatun talakawa a cikin wannan wata mai karamci, watan Ramadhan wata ne na karamci, da baiwa, da gabatar da kyaututtuka, wata ne da ma’anar tausayi, da jinƙai suke bayyana a aikace, tausayi da jinƙan marayu, da zawarawa, da talakawa, da miskinai, inda watan yake zamowa sanadiyyar shigar da farin - ciki da murna a cikin zukatansu, saboda haka koyi ne da Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam) a cikin dukan halayensa, musamman ma a watan Ramadhan, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: **Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yafi kowa kyauta, kuma kyautarsa a watan Ramadhan yafi na kowane wata a lokacin da Mala’ika Jibril yake haɗuwa da shi, kuma yana haɗuwa da shi ne a dukan dararen watan Ramadhan suna darasin Alƙur’ani, wallahi Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yafi sakakkiyar iska yawan kyauta),** wannan kyauta, da baiwar ba wai sun taƙaita ne kawai a kyautar dukiya ba, a’a, abin ya wuce haka, baiwarsa ta game duka ɓangarorin biyayya, da sada zumunci, da tausayi da soyayya, da kiyaye haƙƙoƙi da wajibai.

Haka ma ya kamata kowane Musulmi ya yaiwata ibadu irinsu: karatun Alƙur’ani, da tunani na tadabburi a cikinsa, da yawaita sallar dare “ƙiyamul-lail”, saboda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya raya dararen watan Ramadhan cikin imani da neman samun lada, za a gafarta masa zunubansa da suka gabata),** haka ma

(SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya raya daren lailatul- ƙadri cikin imani da neman samun lada, za a gafarta masa zunubansa da suka gabata),** an ruwaito Hadisi daga Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita), ta ce: Wani dare Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fito a tsakiyarsa, sai ya yi sallah a Masallaci, sai wasu mutane suka bi shi, suka yi sallah tare da shi, da safe mutane suka labarta wa junansu, sai suka taru da yawan da yafi na jiya, suka yi sallah tare da shi, mutane da suka wayi gari, sai labarin haka ya ƙara yaɗuwa, a dare na uku sai yawan mutane ya ƙara ƙaruwa, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fito suka bi shi sallah, a dare na huɗu kuwa sai Masallacin ya cika maƙil, ba masaka tsinke, sai ya fito sallar Asuba kawai, da ya idar da sallar, sai ya juyo ya fuskanci mutane, ya yi kalmar shahada, sannan ya ce: **(Bayan haka; ba wai ban san matakin da kuka ɗauka ba ne, kawai dai na ji tsoron kada a farlanta maku ne, ku kuma gajiya akanta),** sannan daga baya Sayyiduna Umar Bn al-Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ga muhimmancin ya haɗa mutane ƙarƙashin makaranci ɗaya a zamanin halifancinsa, an ruwaito daga Abdurrahman Bn Abdulƙariy, ya ce: a wani dare na watan Ramadhan na fito zuwa Masallaci tare da Umar Bn al-Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi), sai ga mutane gungu – gungu a rarrabe, wani yana sallah shi kaɗai, wani kuma ya yi wa wasu 'yan jama'an limanci, sai Sayyiduna Umar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Ina ganin da zan haɗa dukan waɗannan mutanen ƙarƙashin limancin makaranci ɗaya da zai fi alhairi, sai kuma ya yi azama, ya haɗa su ƙarƙashin limancin Sayyiduna Ubayyu Bn Ka'ab (Allah ya ƙara yarda da

shi), saboda kwaɗayinsa na tsayar da Sunna, da kuma samar da haɗin kan Musulmai.

Babu shakka, azumi na gaskiya shi ne kamewa ga barin dukan saɓon Allah, da aikata zunubai da laifuffuka, masu azumi nawa ne da ba su da komai a cikinsa in banda ɗan banzan yunwa da ƙishirwa?, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Sau da yawa akan sami mai azumin ba shi da komai a cikin azuminsa banda tsantsar yunwa da ƙishirwar banza, sau da yawa akan sami mai ƙiyamul-lailin da ba shi da komai a ƙiyamul- lallinsa sai hana ido barci),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk bai bar maganar ƙarya da aiki da ita ba, to babu ruwan Allah da barin cin abinci da abin sha da ya yi),** Sayyiduna Jabir Bn Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: Idan kana azumi, to kunnenka, da idanuwanka, da harshenka su ma su kame ga barin yin ƙarya da abubuwan da aka haramta, ka nesanci cutar da hadimi, ka zamo mai natsuwa da kwarjini a gaba ɗayan ranar azuminka, kada ka sanya ranar azuminka ta zamo ba ta da wani bambanci da sauran ranakunka, ya kamata Musulmi ya yi iya iyawarsa wajen sanya azuminsa ya zamo azumi ne na haƙiƙa, muddin dai yana son samun sakamakon azumin, wanda shi ne : **Tsoron Allah Maɗaukakin Sarki.**

Wajibi ne mu san cewa watan Ramadhan mai albarka, wata ne na jajircewa, da ƙoƙari wajen gabatar da ayyuka, kada ƙoƙarinmu da ayyukanmu a watan Ramadhan su gaza ƙoƙarinmu da ayyukanmu a wanin watan Ramadhan, muna masu riya cewa akwai gajiya, gami da wahala, mutane da yawa sukan fake da kasala da lalaci, su yawaita barci a ranakun Ramadhan, inda hakan yake sanadiyyar wofintar da

maslahohin mutane a cikin wannan wata mai karamci, duka waɗannan sun saɓa da manufofin da saboda su ne aka shar’anta azumi; wato: tsoron Allah, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, Allah mai girma ya shar’anta wajibcin Azumi domin tsarkake zukatanku da daidaita sha’awarku, da fifita ku akan dabbobin da suke bin sha'awarsu, shi wannan wajabta Azumi da aka yi maku kamar yadda aka farlanta wa al’ummomin da suka gabace ku, ba zai yi maku wahala ba, saboda wajibi ne akan mutane baki ɗaya, wajibcin Azumi da tsayawa dominsa duka domin rainon ruhin tsoron Allah a cikinku ne, da kuma ƙarfafa zukatanku da tsarkake su)) [al- Baƙra: 183],** babu yanda za a yi tsoron Allah ya tabbata ga wanda kasala gami da lalaci suka aure shi, tsoron Allah yana samuwa ne ta hanyar ƙara yawaita ibadu da ayyuka, da kuma ikhlasi da sanya Allah Maɗaukakin Sarki a cikin komai.

A cikin manyan sifofin da mai azumi ya keɓanta da su akwai hararo Allah Maɗaukakin Sarki a cikin komai, hakan ma yana nufin har wurin bayar da haƙƙoƙin da suke rataye da aiki, domin mai sanya ido a cikin sallarka, da azuminka, da kamewarka ga barin cin abinci da shan abin sha, shi ne dai kuma mai sanya ido akan sauke nauyin aiki, ko yunƙurin ƙaurace wa mas’uliyyar aiki da kake yi.

Ganin cewa wajibi ne mai azumi ya kiyaye wajen cin halal in dai har yana buƙatar a amsa masa addu’ar da yake yi, to lallai ya kamata ya riski cewa idan ya amshi albashi ba tare da ya bayar da haƙƙoƙin aikin da yake a kansa ba, to haramun yake ci, domin ya amshi albashi ne ba tare da ya gabatar da aiki ba, ko kuma ya saɓa da sharaɗi, ko yarjejeniyar da aka ƙulla,

wadda take da jiɓi da aikin da yake yi, shin aikin na gwamnati ne, ko kuma na kamfani, duka babu bambanci.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-----------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai aiki da ibada ɗan- juma ne da ɗan jummai, ibada aiki ne, aikin da aka yi shi saboda Allah Maɗaukakin Sarki ibada ne, babu yanda za a yi su rabu da juna, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya RasulalLahi – SallalLahu alaiHi wa sallam- ka ce masu: Ku yi aiki kawai, Allah da Manzonsa da muminai ne da sannu za su gani, da kuma sannu za a mayar da ku zuwa ga masanin abubuwan da suke a ɓoye da na sarari, ya ba ku labarin abubuwan da kuke aikatawa)) [at- Tauba: 105]**, mai lura da tarihin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), da tarihin sahabbansa tsarkaka masu daraja, da ma tarihin Musulunci gaba ɗaya zai ga cewa watan Ramadhan wata ne na aiki tuƙuru da samar da sakamako, hasali ma ai nasarori masu yawa da buɗe garuruwa da Musulmai suka yi sun faru ne a wannan wata mai albarka, wata ne da ya cancanci a kira shi da sunan **"watan samun nasarori da buɗe garuruwa"**, a cikinsa ne aka yi nasara a yaƙin Badar al-

Kubra, yaƙin da ya rarrabe tsakanin gaskiya da ƙarya, inda Allah Maɗaukakin Sarki ya karrama muminai da nasara daga wurinsa, duk kuwa da rashin yawansu, da kuma ƙarancin tattalinsu, Allah mai girma yana cewa: ((**Allah Mai girma ya tunatar da muminai ni'imar nasarar da ya ba su a yaƙin Badar, lokacin da suka yi haƙuri, sai ya tabbatar masu da cewa: lallai shi ne ya taimake su a wajen yaƙin, lokacin da suke da ƙaranci adadi, da kuma ƙarancin makamai, ya kuma neme su da su yi masa biyayya da ɗa'a; domin su gode masa akan wannan ni'ima.. Nasarar ta kasance ne lokacin da Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya ce wa muminai: shin taimakon da Ubangijin ku ya yi maku na sauko da Mala'iku dubu uku daga gare shi; domin su ƙarfafe ku, bai isa ya kwantar maku da hankali, ya kuma sanya maku natsuwa ba?. Ey, lallai wannan ƙari ya isa ya sanya zukatanku su natsu, idan kuka yi haƙuri a wannan yaƙi, kuka kuma yi riƙo da tsoron Allah, idan maƙiyanku suka zo maku nan-take Ubangijinku zai ƙara maku Mala'iku adadin su ya kai dubu biyar da zai saukar da su daga wurinsa domin su ƙarfafe ku.. Allah Mai girma bai sanya wannan ƙari na Mala'iku ba, face su zama maku albishir ne na nasara; saboda zukatanku su natsu, amma fa babu wata nasara sai wadda ta zo daga Allah, wanda shi ne yake sanya komai a inda ya dace da shi, shi ne kuma yake tsara bautar bayinsa muminai))** **[Ali Imran: 123 -126].**

A watan Ramadhan ne aka yi **"Fathu Makka"**, wanda shi ne buɗi mafi girma da Allah Maɗaukakin Sarki ya karrama Manzonsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) da muminai da shi, ya kuma turbuɗe hancin shirka da mushrikai.. A wannan zamanin ma ne aka sami nasarar **"Ranar goma ga watan Ramadhan",**

wanda ta yi daidai da shida ga watan Oktoba, inda Allah ya datar da ƙasar Misra da kwato ƙasarta da karamarta, taken da sojojin Misra suka yi ta rerawa shi ne: **"Allahu Akbar"**, tare da yin azumi da ƙiyamul-laili da karatun Alƙur'ani da yawaita addu'o'i na gaskiya, sai kuwa ga bayyananniyar nasara, inda aka fatattaki azzalumai, domin bai wa addini da ƙasa da kuma mutunci kariya, hakan ya zamo darasi ga duk wanda zuciyarsa take raɗa masa takalar Misra da zalunci.

Babu abin da muka fi buƙata sama da dawo da ruhin watan Ramadhan a cikin dukan ɓangarorin rayuwarmu, domin mu sami cikakkiyar nasara, da ƙarfafa rukunnan gaskiya, da haƙƙi, da adalci, da bai wa ƙasa da mutunci gami da karama kariya, saboda al'ummarmu su dawo da matsayinsu, da kuma kwarjininsu a idon duniya, wannan kam ba zai tabbata ba sai an daidai sahu, an haɗa kai, an tattaru akan manufa ɗaya, sannan kuma a zage dantse wajen jajircewa a aiki da ƙoƙari, da kuma gabatar da alhairai ga dukan mutane.

**Ya Allah Ubangiji ka yi mana albarka a cikin watan Sha'aban, ka kuma kai mu watan Ramadhan, sannan ka amsa mana ibadunmu ya Ubangijin talikai.**

**- 49 –**

## RAMADHAN: WATAN 'YANTA BAYI GA BARIN WUTA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, Allah mai girma ya shar'anta wajibcin Azumi domin tsarkake zukatanku da daidaita sha'awarku, da fifita ku akan dabbobin da suke bin sha'awarsu, shi wannan wajabta Azumi da aka yi maku kamar yadda aka farlanta wa al'ummomin da suka gabace ku, ba zai yi maku wahala ba, saboda wajibi ne akan mutane baki ɗaya, wajibcin Azumi da tsayawa dominsa duka domin rainon ruhin tsoron Allah a cikinku ne, da kuma ƙarfafa zukatanku da tsarkake su)) [al-Baƙra: 183]**.. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda a Hadisinsa mai girma yake cewa: **(Duk wanda ya yi Azumin watan Ramadhan cikin imani da neman lada a wurin Allah, to kuwa za a gafarta masa zunubansa da suka gabata**). Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Allah Maɗaukakin Sarki ya keɓance watan Ramadhan mai albarka da wasu kyaututtuka, da baiwa da babu su a cikin sauran watanni, a cikin waɗannan kyatuttuka akwai **yanda Allah ya sanya shi ya zamo watan shiriya** da a cikinsa ne aka saukar da dukan litattafan Allah mai girma da ɗaukaka, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Waɗannan kwanaki su ne watan Ramalan mai girma da daraja wajen Allah, lallai Allah ya saukar da Alƙur'ãni mai girma a cikinsa, yana shiryatar da mutane ne zuwa ga shiriya da bayanansa na dalla-dalla, da suke isar da mutane zuwa ga alhairi, masu kuma rarrabe tsakanin gaskiya da ɓata a zamunna da saƙonni..)) [al- Baƙra: 185]**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(An saukar da "Suhfu Ibrahim" ne a daren farko na watan Ramadhan, an kuma saukar da Attaura ne a shida ga watan Ramadhan, an kuma saukar da Injila a sha uku ga watan Ramadhan, an saukar da Zabura a sha takwas ga watan Ramadhan, an saukar da Alƙur'ani a ashirin da huɗu ga watan Ramadhan).**

A cikin waɗannan kyaututtuka akwai: **kasancewarsa watan addu'a:** Lallai addu'a ɗaya ne daga cikin manyan hanyoyin yi wa Allah biyayya da ɗa'a, tana cikin mafi girman hanyoyin da bawa yake kusantar Ubangijinsa Allah Maɗaukakin Sarki, idan muka lura da littafin Allah Maɗaukakin Sarki da kyau, za mu ga inda ayar da take magana akan addu'a ta zo a tsakiyar ayoyin da suke magana akan azumi, a inda Allah mai girma da ɗaukaka yake cewa: **((Ya Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa sallam)- idan bayi na suka tambaye ka suka ce: shin Allah kusa yake da mu, ta yadda ya san abin da muke ɓoyewa da wanda muke bayyanarwa da abin da muke bari? Ka ce masu:**

**lallai ni ina kusa da su, sama da yadda suke zato, dalili kuwa shi ne addu'ar mai addu'a tana iso mini a lokacin da yake yi, haka-zalika kuma ni ne nake amsata a lokacinta, idan dai har na amsa masu, to ni ma su amsa mini da imani da biyayya. Lallai hakan shi ne shiriyarsu da katarin su))** [al- Baƙra: 186], a wani nunin zuwa ga cewa lallai akwai fatan mai ƙarfi na amsar addu'ar mai azumi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mai azumi yana da lamunin amsar addu'arsa),** a wani wurin kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mutane uku ba a ƙin amsar addu'arsu: shugaba mai adalci, da mai azumi a lokacin da yake buɗa- baki, da addu'ar wanda aka zalunta, zai sanya ta saman girgije, a kuma buɗe mata ƙofofin sama, Ubangiji Mai girma da buwaya ya ce: Na rantse da izza ta, wallahi sai na taimake ki, koda kuwa bayan wani lokaci ne).**

Ta yiwu mafi girma da muhimmancin sifar da Allah Maɗaukakin Sarki ya keɓanci watan Ramadhan da ita, ita ce: **kasancewarsa watan 'yanta bayi ga barin shiga wuta,** a inda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Idan daren farko na watan Ramadhan ya kama akan ɗaure shaiɗanu da kangararrun aljannu, a kuma kulle ƙofofin wuta, ba za a buɗe koda ƙofa ɗaya ba, a kuma buɗe ƙofofin aljanna, ba za a kulle koda ƙofa ɗaya ba, mai shela kuma zai yi shela ya ce: ya mai neman alhairi, ka kusanto, ya mai neman sharri ka taƙaita, Allah yana da waɗanda yake 'yanta su ga barin shiga wuta),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Allah Maɗaukakin Sarki yana da bayin da yake 'yantawa ga barin shiga wuta a kowane lokacin buɗa- baki, wato a kowane dare),** abin da ake nufi da **"'yantawa ga barin shiga**

**wuta"** shi ne : duk wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya yi masa wannan baiwa da ni'ima masu girma, to har abada ba zai shiga wuta ba.

Lallai azumi ƙofa ce daga cikin ƙofofin alhairai, ibada ce da take katange bawa ga barin azabar wuta, saboda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Azumi kam garkuwa ne da bawa yake katange kansa ga barin shiga wuta)**, a wani wurin ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu bawan da zai yi azumi saboda Allah a wata rana, face Allah ya nesanta shi da wuta kwatankwacin kamu saba'in a wannan ranar).**

An ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Mu'az Ibn Jabal (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce, wata rana ina tare da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) a wata tafiya, sai da na kasance kusa da shi a lokacin da ake tafiya, lokacin da na ga daga ni sai shi, sai na ce: ya Manzon Allah, faɗa mini aikin da zai shigar da ni aljanna, ya kuma nesanta ni da wuta. Ya ce: **(Tabbas ka tambayi abu mai girma, sai dai duk da haka, abu ne mai sauƙi ga wanda Allah Maɗaukakin Sarki ya sauƙaƙe masa: ka bauta wa Allah kada ka haɗa shi da kowa, ka tsayar da Sallah, ka bayar da Zakka, ka azumci watan Ramadhan, ka hajjanci ɗakin Allah)…** sannan ya ce: **(shin ba na nuna maka ƙofofin alhairi ba?: Azumi garkuwa ne, sadaka tana share kura-kurai kamar yadda ruwa yake kashe wuta..).** Haka ma Azumi ɗaya ne daga cikin waɗanda Allah Maɗaukakin Sarki yake amsar ceto daga gare su a ranar alƙiyama, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Azumi da Alƙur'ani suna ceton bawa a ranar alƙiyama, Azumi yana cewa: Ya Ubangiji, na hana shi abinci, da sha'awa a tsawon rana, saboda haka, ka ba**

**ni cetonsa, Alƙur'ani ma yana cewa: Na hana shi barci da daddare, saboda haka, ka ba ni cetonsa),** ya ce: **(Sai su yi ceto).**

Haka ma azumi dalili ne **na samu gafara daga Allah,** hanya ne daga cikin hanyoyin aljanna, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa bayinsa masu azumi alƙawarin samun gafara, da kuma lada mai girma, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai waɗanda suka miƙa wuya cikin maza da mata, da masu gasgata samuwar Allah da Annabtar Annabi cikin maza da mata, da masu biyayya cikin maza da mata, da masu gaskiya wajen maganganu da ayyuka da ƙuduri cikin maza da mata, da masu haƙuri da juriyar ɗaukan wahalhalu saboda Allah a cikin maza da mata, da masu ƙasƙantar da kawunansu saboda Allah a cikin maza da mata, da masu yin sadaka da dukiyoyinsu ga mabuƙata a cikin maza da mata, da masu azumin farilla da na nafila a cikin maza da mata, da masu kiyaye al'aurarsu ga barin duk wata dangantaka da ba ta halatta ba a cikin maza da mata, da masu ambaton Allah da yawa da zukatansu da harsunansu a cikin maza da mata, duka waɗannan Allah ya tanadar wa zunubansu gafara, da kuma lada mai girma akan ayyukan da suke yi)) [al- Ahzab: 35],** Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya yi Azumin watan Ramadhan cikin imani da neman lada a wurin Allah, to kuwa za a gafarta masa zunubansa da suka gabata),** a wani wurin ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya raya dararen watan Ramadhan cikin imani da neman samun lada, za a gafarta masa zunubansa da suka gabata),** hasali ma akwai wani dare guda ɗaya, da duk wanda aka azurta shi da raya shi, da kuma karatun Alƙur'ani, da addu'a, aka kuma datar da shi wajen yi

wa Allah mai girma da ɗaukaka biyayya a cikinsa, to kuwa lallai za a gafarta masa zunubansa da suka gabata, wannan dare shi ne: daren **"Lailatul – Ƙadri",** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya raya daren lailatul- ƙadri cikin imani da neman samun lada, za a gafarta masa zunubansa da suka gabata).**

A lokacin da (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake bayani akan cewa azumi hanya ce daga cikin hanyoyin shiga aljanna, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(A cikin aljanna akwai wani ɗaki da ake ganin cikinsa ta waje, wajensa ma ta ciki, Allah ya tanadar da shi ne ga wanda ya ciyar da abinci, ya kuma tausasa magana, ya kuma yi azumi a bibiye da juna, sannan ya yi sallah a lokacin da mutane suke barci),** an ruwaito Hadisi da Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi), ya ce: wata rana Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya tambayi Sahabbai cewa: **(Wane ne a cikinku ya wayi gari da azumi?)**, sai Sayyiduna Abubakar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Ni ne, sai ya ce: **(Wane ne a cikinku yau ya raka janaza?),** sai Sayiduna Abubakar ya ce: Ni ne, sai ya ce: **(wane ne a cikinku yau ya ciyar da miskini?)** sai Sayyiduna Abubakar ya ce: Ni ne, sai ya ce: **(wane ne a cikinku ya tafi gaishe da mara lafiya a yau?)** Sayyiduna Abubakar ya ce: Ni ne, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Waɗannan ɗabi'u ba su taɓa tattaru a tare ga mutum ba, face ya shiga aljanna),** haka ma lokacin da Sayyiduna Abu Umamatul Bahiliy (Allah ya ƙara yarda da shi) ya zo wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana tambayarsa cewa: Ya Manzon Allah, ka umurce ni da wani aiki da zai yi sanadiyyar shigar da ni

aljanna, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ka kula da azumi, domin ba shi da kama).**

Lallai azumi sirri ne tsakanin bawa da Ubangijinsa da babu wanda ya san haƙƙiƙaninsa, mai azumi yakan keɓanta daga shi sai Allah Maɗaukakin Sarki, babu mai ganinsa, zai iya aikata abin da Allah ya haramta masa a azumi, amma kuma sai ya kame bai aikata hakan ba, saboda yana da cikakkiyar masaniyar cewa: lallai yana da Ubangijin da yake riskar gaba ɗayan al'amurransa, sai ya bari saboda tsoron uƙubarsa, da kuma kwaɗayin samun ladansa, da kuma tabbacin da yake da shi na cewa lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana tare da shi, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Shin ba ka san cewa lallai Allah ya san abin da yake a sammai da abin da yake a ƙasa ba, babu wata ganawa ta sirri da take gudana tsakanin mutane uku, face ya zama na huɗunsu wajen sanin abin da suke ganawar da shi, ko mutane biyar, face ya zamo na shida, kai, da ma waɗanda ba su kai haka ba, da ma waɗanda suka wuce haka, face yana tare da su, ya san abin da suke ganawa akansa a duk inda suke, sannan kuma zai ba su labarin duk abin da suka aikata a ranar alƙiyãma, lallai Allah yana da cikakkiyar masaniya akan komai))** **[al- Mujadala: 7].**

Lallai azumi yana cikin ibadun da suka sami girma saboda Allah mai girma da ɗaukaka ya danganta su da shi, ya kuma nuna cewa shi ne zai yi sakayya akansa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: Dukan ayyukan ɗan Adam nasa ne ban da azumi, domin shi kam nawa ne, ni ne kuma zan yi sakayya akansa),** a wata ruwayar kuma ya ce: **(Dukan ayyukan ɗan Adam ana ninninka su, kowane aiki na gari ana ninninka shi da**

**kwatankwacinsa guda goma, har su kai zuwa ninki ɗari bakwai, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: ban da azumi, domin shi kam nawa ne, ni ne kuma zan yi sakayya akansa..),** saboda haka ne malamai suka ce: darajar azumi a cikin ibadu ta kai daraja, tun da Allah ya ce **(Azumi kam nawa ne),** wasu suka ce: dalilin wannan dangantaka shi ne: ba a taɓa yi wa wanin da ba Allah Maɗaukakin Sarki ba ibadar azumi, azumi ibada ne na Allah shi kaɗai, riya ba ta shiga cikinsa, wasu kuma suka ce: shi ne ibadar da Allah Maɗaukakin Sarki ya fi so.

Mai azumi a koda yaushe yana hararo Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka, yana kwaɗayin ya ribaci wannan wata mai albarka, domin ya gabatar da kansa zuwa ga kamfatar da Allah Maɗaukakin Sarki yake yi a cikinsa, ko zai samu a shigar da shi cikin waɗanda Allah yake 'yantawa ga barin shiga wuta.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakon Annabawansa da Manzanninsa, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam), da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai azumin da yake zamowa dalilin samun 'yanci daga barin shiga wuta shi ne: azumin da yake hana mai yinsa aikata mummunan aiki, ya kuma shiga tsakaninsa da saɓon Allah, ya kuma gadar masa da tsoron Allah da yake shi ne ainihin manufar azumi, ba zai ci haram ba, ba kuma zai keta alfarmar mutuncin mutane ba, ba zai ci naman kowa ba, ba kuma zai yaɗa gulma da annamimanci ba,

ba kuma zai yi shaida akan ƙarya ba, ba kuma zai furta komai ba, sai abin da Allah Maɗaukakin Sarki ya yarda da shi, ba zai sakanya mummunan aiki da wani mummunan aikin irinsa ba, zai dai sakayya ne da aikin da ya fi kyau, zai sifantu da sifofin masu azumi, Allah Mɗaukakin Sarki yana cewa: **((Idan suka ji yasasshen zance sai su kawar da kai ga barinsa..)) [al- Ƙasasi: 55],** Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Su ne waɗanda suke kawar da kai ga barin yasasshen zance..)) [al- Muminuna: 3],** haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ka aikata aikin da yafi kyau; domin ka kawar da mummuna..)) [al- Muminuna: 96],** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: (**Azumi garkuwa ne, idan ranar azuminku ya yi, kada ku yi zance batsa, kada kuma ku yi faɗa- faɗa, idan wani ya zage ku, ko ya neme ku da faɗa, to ku ce : mu muna azumi…),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Azumi fa ba shi ne kamewa ga barin ci da sha kawai ba, azumi na haƙiƙa shi ne kamewa ga barin yasasshen zance da batsa...),** lallai a cikin dalilan da suke sanyawa a sami ʻyanci ga barin shiga wuta, akwai: mutum ya kiyaye mutuncin ɗan uwansa Musulmi a bayan idonsa, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Duk wanda wanda ya kare naman ɗan uwansa a lokacin da ake gibarsa, to lallai Allah zai ʻyanta shi ga barin shiga wuta).**

Lallai mai azumi na gaskiya da zai amfana da ladan azumi shi ne: wanda tasirin azuminsa yake bayyana a cikin tsarin gudanar da rayuwarsa, da mu'amalarsa da mutane, domin azumin yana sanya mutum ya saba da riƙe ragamar zuciyarsa, da samun iko akanta, da yi mata burki da kaffa- kaffa, har sai ta isa zuwa ga alhairai da jin daɗin duniya da na lahira, lallai zuciya aba ce mai yawan bayar da umurni da aikata

mummunan aiki, sai dai kawai wanda Allah ya kiyaye, idan mutum ya sakar mata ragama, sai ta dulmiyar da shi cikin halaka, idan kuma ya sami iko akanta, ya mallake ta, sai ya iya isar da ita zuwa ga mafi girman manufa da abin nema, wannan kuwa ba zai samu ba sai ga wanda ya yi azumi na haƙiƙa, yana mai halarto da girman Ubangijinsa a cikin hakan, inda cikinsa, da al'aurarsa, da harshensa, da ma dukan gaɓoɓinsa za su kame ga barin duk wani abu da Allah Maɗaukakin Sarki ya haramta.

Haka ma mai azumi na gaskiya shi ne wanda yake kyautata aikinsa, ya kuma yi shi saboda Ubangijinsa, ya kuma shagaltu da neman ya sami karɓuwa a wurin Allah, ga KhalilulLahi nan, shugabanmu Annabi Ibrahim (AlaiHis salam) yana roƙon Ubangijinsa akan ya amshi aikinsa, a lokacin da yake gudanar da wani muhimmin aikin da Allah ya ba shi umurni, wanda shi ne gina Ka'aba mai daraja, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ka ambaci lokacin da Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm) da ɗansa Annabi Isma'il (AlaiHis-Salãm) suke gina ginshiƙan "Ka'aba" suna roƙon Allah mai girma da cewa: Ya Ubangijinmu, mahaliccinmu, kuma maƙaginmu, ka karɓa mana wannan aiki namu da muka yi shi dominka, lallai kai ne kake jin addu'armu, kuma kai ne mafi sanin gaskiyar niyyarmu..)) [al- Baƙra: 127].**

Sayyiduna Aliyu (Allah ya ƙara yarda da shi) yakan ce: Ku fi muhimmanta karɓuwar aiki, akan aikata aikin kansa, shin ba ku ji Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ai Allah yana karɓar aiki ne kawai daga masu tsoron Allah)) [al- Ma'ida: 27]** ba ne?..

**Ya Ubangiji Allah ka sanya mu cikin bayin da za ka 'yanta su ga barin shiga wuta, ka kuma sanya mu cikin waɗanda za ka amshi ayyukansu.**

## - 50 –

## RAMADHAN: WATAN BAIWA DA KARAMCI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Su kuwa waɗanda baiwa take cikin ɗabi'insu, daɗin rai sukan yi wajen ciyarwa dare da rana a fili da ɓoye, ladansu na nan wajen Ubangijinsu, tsoron gaba ba zai same su ba, ba kuma za su yi baƙin-ciki akan wani abu da ya wuce su ba)) [al- Baƙra: 274].**. Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda a Hadisinsa mai girma yake cewa: **(Babu wata rana da bayi za su wayi gari, face akwai Mala'iku guda biyu da suke saukowa, ɗayansu ya ce: Ya Ubangiji ka bai wa mai ciyarwa makwafin abin da yake ciyarwa, ɗayan kuma ya ce: Ya Ubangiji ka bai wa ƙanƙamo rariyar- hannu).** Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai addinin Musulunci addini ne na kyawawan ɗabi'u da manyan tadodi, a cikin waɗannan kyawawan ɗabi'u da addininmu mai girma ya yi kira zuwa gare su, ya kuma kwaɗaitar da mutane akan aikata su akwai: **ɗabi'ar baiwa da karamci,** ɗabi'a ce daga cikin ɗabi'un Manzanni, sifa ce daga cikin sifofin salihan bayi, da ita ce soyayya, da ƙauna, gami da

ganin darajar juna suke yaɗuwa a cikin mutane, hakan kuma sai ya yi sanadiyyar samar da ƙaƙƙarfar al'umma, mai haɗin kai, da ta ginu akan taimakon juna, da gabatar da kyaututtuka da baiwa, sai ikhlasi da cika alƙawari su mamaye ta ta ko'ina, hakan ya kai zuwa ga tabbatar da maganar Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yake cewa: **(Misalin muminai wajen soyayyar junansu, da jinƙan junansu, da tausayin junansu tamkar jiki ne da idan wata gaɓa ta cutu, duka sauran jikin zai kamu da rashin barci, da kuma zafin ciwo)** a cikinsu.

Karamci sifa ce daga cikin sifofin Allah Mai girma da ɗaukaka, hasali ma suna ne daga cikin sunayensa kyawawa, mun ambaci tsarkin Allah mai yawan baiwa da kyaututtukan da ba ya taɓa ƙulle ƙofarsa, kyautarsa da baiwarsa kuma ba sa taɓa ƙarewa, ba kuma ya korar mai roƙonsa, ba kuma ya bayar da wanda ya ƙaunaci wani abu daga gare shi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah mai yawan karamci ne, yana kuma son karamci, yana son manyan kyawawan ɗabi'u, yana kuma ƙin munanansu),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah mai yawan karamci ne, yana kuma son karamci, mai yawan baiwa ne, yana kuma son baiwa..)**, an ruwaito a cikin Hadisi Ƙudsi Allah yana cewa: **(…Ya ku bayina, dukanku ɓatattu ne, sai wanda na shiryatar, ku nemi shiryatarwa ta, sai na shiryatar da ku. Ya ku bayina, dukanku mayunwata ne, sai wanda na ciyar, ku nemi ciyarwa ta, sai na ciyar da ku. Ya ku bayina, dukanku huntaye ne marasa tufafi, ku nemi tufatarwa ta, sai na tufatar da ku. Ya ku bayina, lallai ku ɗin nan kuna yin kura-kurai a dare da rana, ni kuma ina gafarta zunubi gaba ɗaya, ku nemi gafara ta, sai na gafarta maku…. Ya ku bayina,**

**da a ce na farkonku, da na ƙarshenku, da mutanenku, da aljannunku za su tsaya a wuri ɗaya, su roƙe ni, in kuma bai wa kowa abin da ya roƙa, hakan ba zai rage komai daga abin da yake wuri na ba, sai kamar abin da allura za ta rage idan aka sanya ta a cikin kogi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Hannun Allah a cike yake, yawan ciyarwa baya tauye shi, kyauta ne ba dare ba rana, shin ba ku ga abubuwan da ya ciyar ba ne tun lokacin da ya halicci sammai da ƙasa, lallai ba su iya tauye abin da yake hannunsa ba)**.

Lallai Alƙur'ani mai girma ya bayyana mana cewa kyauta da baiwa halaye ne na Annabawa da Manzanni, a ƙissar Annabi Ibrahim (AlaiHis Salam) Allah mai girma yana cewa: **((Shin ka san ƙissar mala'iku, baƙin Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm) da ya karrama su!. A lokacin da suka shiga wurinsa sai suka ce: Amincin Allah ya tabbata a gare ku. Shi ma ya ce: Amincin Allah ya tabbata a gare ku, duk da dai ku jama'a ne da ba a ganeku ba. Sai ya tafi wurin iyalansa a ɓoye, sai ya zo masu da ɗan mariƙi ƙosasshe a gashe. Sai ya kusantar da shi zuwa gare su, ba su ci ba, sai ya ce –yana mamakin halinsu- shin ba za ku ci ba?.)) [az- Zariyat: 24 – 27]**, saboda yawan karamci da baiwarsa ake yi masa laƙabi da shugaban masu tarbar baƙi.

Lallai Ubangijin girma da ɗaukaka ya kwaɗaitar da mu wajen girmama junanmu, muddin dai muna son mu zamo cikin masu samun karamcinsa da falalarsa, a inda Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((Kada mutanen kirki masu dukiya a cikinku su rantse akan hana kyautatawarsu ga waɗanda suka cancanta cikin 'yan uwa makusanta, da miskinai, da waɗanda suka yi hijira saboda Allah, da sauransu ta kowane irin dalili da ya shafe su, kaman idan sun yi masu ba daidai ba, kamata ya yi**

**su yafe masu, su kawar da kai ga barin mayar masu da martani, idan dai har kuna son Allah ya yafe kura-kurenku, da munanan ayyukanku, to ku ma ku aikata abin da kuke son Ubangijinku ya yi maku ga waɗanda suka munana maku, ku ladabtu da ladubbansa, shi dai kam mai yawan gafara da rahama ne))** **[an- Nur: 22]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai halin waɗanda suke bayar da dukiyoyinsu wajen yi wa Allah biyayya da hanyoyin alhairi, suka kuma sami ladan Allah akan haka, ladan kuma ninkin-ba-ninkin, ya yi kama da halin mutumin da ya shuka iri ne a ƙasa mani'imciya, irin kuma ya tsirar da 'yar ƙaramar bishiya mai zangarniyoyi bakwai, cikin kowace zangarniya akwai ƙwaya ɗari. Wannan sura ce ta yawan abin da Allah zai ba shi na sakamakon ciyarwa a duniya, Allah yana ninninka haka ga wanda ya ga dama, domin shi mai yalwar falala ne, yana kuma da cikakken sanin wanda ya cancanta da wanda bai cancanta ba))** **[al- Baƙra: 261]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Ba fuskantar wani sashe a gabãshi ko yammaci shi ne kashin-bayan addini, ko matattara alhairi ba, matattara alhairi yana cikin abubuwa ne masu dama, wasu suna cikin rukunnan ingantacciyyar aƙida ne, wasu kuma suna cikin tushen ayyuka na gari da ibadu. Na farko shi ne: imani da Allah, da ranar tashin alƙiyama, da hisabi, da abubuwan da za su biyo bayan haka a ranar alƙiyama, da imani da mala'iku da littattafan da aka saukar wa Annabawa, da ma su kansu Annabawan. Na biyu shi ne: bayar da dukiya cikin jin daɗin rai ga talakawa, makusanta da marayu da waɗanda buƙatu da rashi suka yi masu yawa, da matafiyan da guzuri ya yanke masu, ba su da abin da zai isar da su zuwa ga manufarsu, da**

**masu roƙon mutane da buƙata ta tilasta masu yin haka..))** **[al-Baƙra: 177]**, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Suna kuma ciyar da abinci -duk da suna so suna kuma matuƙar buƙatarsa- ga matalaucin da ya gajiya wajen nema, da ƙaramin yaron da ya rasa mahaifansa, da fursinan yaƙin da ba ya mallakar komai. Suna kuma faɗi a cikin zuciyarsu cewa: muna ciyar da ku ne kawai saboda biɗar yardan Allah, ba ma son ku ba mu wani abu a maimakonsa, ko ku yi mana kyauta, haka ma ba ma son yabo daga gareku. Mu muna tsoron Ubangiji ne game da wata rana da fuskoki a cikinta za su yi matsanancin murtukewa. Sai kuwa Allah ya katange su ga barin tsanance-tsanancen wannan rana, a sa'ilin da fuskokin kãfirai suke murtukewa, sai Allah ya haskaka fuskokinsu, ya kuma sanya farin-ciki da annashuwa a cikin zukatansu))** **[al-Insan: 8 – 11]**, Annabinmu (SallalLahu alaihi wa sallam) yana cewa: **(Ka ciyar, Allah zai yalwata maka).**

Lallai watan Ramadhan wata ne na baiwa, da karamci, da kyaututtuka, da kuma tallafa wa marasa ƙarfi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) shi ne yafi kowa yawan kyauta da baiwa, kyautarsa da baiwarsa kuma sun fi yawa a watan Ramadhan, Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: **Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yafi kowa kyauta, kuma kyautarsa a watan Ramadhan yafi na kowane wata a lokacin da Mala'ika Jibril yake haɗuwa da shi, kuma yana haɗuwa da shi ne a dukan dararen watan Ramadhan suna darasin Alƙur'ani, wallahi Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yafi sakakkiyar iska yawan kyauta)**.

Ganin cewa Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kwaɗaitar da mu akan mu ciyar da abinci a kowane irin hali, a inda yake cewa: **(Ya ku mutane, ku yaɗa sallama, ku kuma ciyar da abinci, ku kuma yi sallah a lokacin da mutane suke barci, in kun yi haka sai ku shiga cikin aljanna cikin aminci)**, kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kwaɗaitar wajen karrama baƙo a kowane lokaci, a inda yake cewa: **(Wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya karrama baƙonsa..)**, to kuwa lallai a wani wurin (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana cewa ladan ciyar da abinci, da karrama baƙo a cikin watan Ramadhan ya fi girma da yawa, a inda yake cewa: **(Wanda duk ya buɗe bakin mai azumi za a rubuta masa irin ladansa, amma ba zai rage ladan mai azumin da komai ba)**, wannan lada ne da duk wani wanda ya ciyar da mai azumi a lokacin buɗe baki zai same shi, sawa'un mai azumin mawadaci ko talaka, makusanci ne, ko aboki da sauransu, tun da (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Mai azumi)**, to kuwa wannan kalma ta game kowa da kowa. Bayan ciyar da talakawa, da biya masu buƙatunsu ma akwai wata manufar Shari'a da za a iya fahimta daga maganar Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), wannan manufa kuwa ita ce: ƙara ƙarfafa dangantaka, da sada zumunci tsakanin mutane a cikin wannan wata na sadar da zumunci da biyayya, inda za su taru akan kaɓaki guda ɗaya na iyali, da kaɓakin dangi, da kaɓakin abokai, da kaɓakin abokan aiki da abokan sana'a.

Haka ma a cikin wannan Hadisin za a fahimci game duk wanda ya ciyar da mai azumi a haƙiƙa, ta hanyar gayyatarsa zuwa ga buɗa baki, ko ya samar masa da abinci, ko kuma ya yi hakan a hukunce, ta hanyar bai wa mai azumi sadaka, ko

kyautar abin da zai yi buɗa baki da shi, ko abin da zai taimaka masa wajen tattalin buɗa bakinsa, manufar Hadisin dai guda biyu ne: Na farko: Ɗaukan nauyin marasa ƙarfi, ta yanda ba za a sami mai jin yunwa, ko mabuƙaci, ko marashi a tsakaninmu ba a cikin wannan wata na karamci, na biyu kuma: ƙara sanya soyayya da ƙarfafa rayuwar zamantakewa tsakanin mutane, musamman a cikin wannan wata na falala.

Lallai Sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) sun buga mana babban misali wajen baiwa, da kyauta, gami da karamci da dukiya, da ma rai; domin neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki, musamman a lokutan tsanani da buƙata; saboda tabbatar da tsarin tallafa wa marasa ƙarfi, da kuma taimakekeniya, gami da tausayin juna, ga 'yan ƙabilar Ash'ari nan sun sami yabon Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sakamakon irin yanda suke tallafa wa marasa ƙarfin cikinsu, da kuma irin yanda suke taimakekeniya da junansu, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai idan guzurin Ash'ariyyawa ya ƙare a lokacin da suka tafi yaƙi, ko abincin iyalansu a cikin gari ya yi ƙaranci, sai su harhaɗa abin da ya rage masu a wuri ɗaya, sannan su sake rabawa a tsakaninsu daidai wa daidai, su kam daga gare ni suke, ni ma daga gare su nake)**.

An ruwaito daga Anas Bn Malik (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Abu Ɗalhat shi ne ya fi mutanen al'Ansar dukiya, kuma dukiyar da ya fi so a cikin arzikinsa ita ce: "Bairuha'u" (wata gona ce da a cikinta akwai rijiya mai wannan sunan) tana fuskantar Masallaci ne, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan shiga ya sha ruwa mai a daɗi a ciki, sai Anas (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: lokacin da wannan ayar: **((Ya**

**ku muminai, ba za ku taɓa samun cikakken alhairi da yardar Allah da kuke nema ba, sai kun bayar da abin da kuke so, kun ciyar da su ta hanyoyin alhairai mabambanta…)) [Ali Imran: 92]**, ta sauka, sai Abu Ɗalhat ya tashi ya tafi wurin Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), ya ce: Ya Manzon Allah, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar maka da: **((Ya ku muminai, ba za ku taɓa samun cikakken alhairi da yardar Allah da kuke nema ba, sai kun bayar da abin da kuke so, kun ciyar da su ta hanyoyin alhairai mabambanta…)) [Ali Imran: 92]**, kuma lallai mafi soyuwar dukiya ta a wurina shi ne "Bairuha'u", na bayar da shi sadaka saboda Allah, ina kwaɗayin samun ladansa da alhairansa a wurin Allah Maɗaukakin Sarki, ga shi nan –Ya Manzon Allah- ka sanya shi a duk inda Allah ya so, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ai kuwa Tubarkallah, wannan dukiya ce mai riba, wannan dukiya ce mai riba, lallai na ji abin da ka faɗa, amma ina ganin ka bayar da ita ga makusantanka)**, sai Abu Ɗalhat ya ce: zan yi hakan ya Manzon Allah, sai kuwa Abu Ɗalhat ya rarraba wa makusantansa da 'ya'yan baffansa).

An ruwaito daga Ibn Umar (Allah ya ƙara yarda da su) cewa: an bai wa wani daga cikin sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) kyauta kan tunkiya, sai ya ce: (lallai wane da iyalansa sun fi ni buƙatar wannan), ya ce: aka aika masa, haka shi ma wanda aka aika masa ya aike da shi zuwa ga wani, har ya zagaya gidaje bakwai, sannan ya dawo wurin na farko, sai wannan ayar: **((Suna fifita wasunsu akan kansu koda kuwa suna cikin matsananciyar buƙata)) [al- Hashri: 9]** ta sauka, lallai sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) suna rige-rige a tsakaninsu a fagen baiwa da kyauta, suna musabaƙa

wajen ciyarwa, da gabatar da ayyukan alhairai; suna masu amsa umurnin Allah Maɗaukakin Sarki, da umurnin Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), suna kuma kwaɗayin samun abubuwan da Allah Maɗaukakin Sarki ya tanadar wa masu baiwa da yawan kyauta.

Lallai muna matuƙar buƙatar sifantuwa da wannan babban ɗabi'a, mu kuma yi nesa da duk wata tada ta rowa, da ƙoro, da son kai, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mutumin da ya kwana a ƙoshe, amma makwabcinsa na kusa ya kwana da yunwa, alhalin yana sane, to lallai bai yi imani da ni ba)**, a wani wurin kuma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa; **(Ya kai ɗan Adam, ka yi kyauta da abin da ya ƙaru akan buƙatarka shi ne ya fi maka alhairi, in kuma ka maƙe shi hakan sharri ne a gare ka, idan kuma ba ka mallakar sama da abin da kake buƙata, a nan babu zargi, ka fara bayarwa ga waɗanda nauyinsu yake a kanka, hannun bayarwa ya fi hannun karɓa alhairi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda yake da ƙarin abin hawa, to ya bayar da shi ga wanda ba shi da abin hawa, wanda yake da ƙari a guzurinsa, to ya bayar da shi ga wanda ba shi da guzuri)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakon Annabawansa da Manzanninsa, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam), da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai sadaukar da rayuka shi ne mafi girman baiwa da kyauta, sifa ce ta masu karamci, haka ma ɗabi'a ce ta masu hankali, shi ne a ƙololuwar muƙamin fifita wasu akan kai, shi ne kuma mafi darajar baiwa da karamci, wani mawaƙi yana cewa:

"Yana kyauta da rayuwarsa a lokacin da marowaci yake alkinta ta, ita kuwa kyauta ta rayuwa ita ce ƙarshen kyauta".

A cikin nau'o'in karamci da rai, akwai: ƙoƙarin da dakaru suke yi akan iyakar ƙasa, wajen bai wa ƙasarsu, da al'ummarsu, da mutuncinsu kariya, sun tsaya cikin haƙuri da juriya saboda neman lada a wurin Allah Maɗaukakin Sarki, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Zaman bayar da kariya ga ƙasa saboda Allah na rana ɗaya ya fi duniya da abubuwan da suke cikinta alhairi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idanuwa guda biyu kam wuta ba za ta shafe su ba: idon da ya yi kuka saboda tsoron Allah, da idon da ya kwana gadi saboda Allah)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Babu ƙafar bawan da za ta yi ƙura saboda Allah, sannan kuma wuta ta shafe ta)**, lallai baiwa da rayuwa abu ne da yake tabbatar wa mutumin da ya yi hakan samun babban rabo a duniya da lahira, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku yi riƙo da haƙuri, ku kuma yi jajircewar da za ku rinjayi maƙiyan ku da shi, ku kuma yi ribaɗi, wanda shi ne toshe gaba ɗayan kafofi domin kare kai, ku ji tsoron Ubangijin ku, idan kuka yi haka, akwai yiwuwar ku sami babban rabo)) [Ali Imran: 200].**

Babu shakka watan Ramadhan wata ne na nasarori, a cikinsa ne aka yi nasara a **yaƙin Badar al-Kubra,** yaƙin da ya rarrabe tsakanin gaskiya da ƙarya, inda Allah Maɗaukakin

Sarki ya karrama muminai da nasara daga wurinsa, duk kuwa da rashin yawansu, da kuma ƙarancin tattalinsu, idan aka gwada da tanadin da maƙiyansu suka yi, Allah mai girma yana cewa: **((Allah Mai girma ya tunatar da muminai ni'imar nasarar da ya ba su a yaƙin Badar, lokacin da suka yi haƙuri, sai ya tabbatar masu da cewa: lallai shi ne ya taimake su a wajen yaƙin, lokacin da suke da ƙaranci adadi, da kuma ƙarancin makamai, ya kuma neme su da su yi masa biyayya da ɗa'a; domin su gode masa akan wannan ni'ima.. Nasarar ta kasance ne lokacin da Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya ce wa muminai: shin taimakon da Ubangijin ku ya yi maku na sauko da Mala'iku dubu uku daga gare shi; domin su ƙarfafe ku, bai isa ya kwantar maku da hankali, ya kuma sanya maku natsuwa ba?. Ey, lallai wannan ƙari ya isa ya sanya zukatanku su natsu, idan kuka yi haƙuri a wannan yaƙi, kuka kuma yi riƙo da tsoron Allah, idan maƙiyanku suka zo maku nan-take Ubangijinku zai ƙara maku Mala'iku adadin su ya kai dubu biyar da zai saukar da su daga wurinsa domin su ƙarfafe ku.. Allah Mai girma bai sanya wannan ƙari na Mala'iku ba, face su zama maku albishir ne na nasara; saboda zukatanku su natsu, amma fa babu wata nasara sai wadda ta zo daga Allah, wanda shi ne yake sanya komai a inda ya dace da shi, shi ne kuma yake tsara bautar bayinsa muminai)) [Ali Imran: 123 – 126].**

A watan Ramadhan ne aka yi **"Fathu Makka"**, a shekara ta takwas bayan hijira, a wannan buɗin ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya buga babban misali na kyawawan ɗabi'u, musamman a ɓangaren yafiya, da kawar da kai, da kuma sassauci, da tausayi, lokacin da (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya

tattara waɗanda suka cutar da shi, suka kuma fitar da shi daga garinsa, suka shirya maƙarƙashiyar kashe shi, sannan ya ce masu: **(Me kuke tunanin zan yi maku?)** sai suka ce: alhairi, kai ɗan uwa ne mai karamci, ɗan ɗan uwa mai karamci. Sai ya ce: **(Ku tafi na yafe maku)**.

A watan Ramadhan na shekarar 1397 bayan hijira, wadda ta yi daidai da ranar shida ga watan Oktoba, 1973 ne aka yi yaƙin **"Goma ga watan Ramadhan"**, yaƙin izza da karama, inda Allah Maɗaukakin Sarki ya bai wa gwarazan sojojin Misra nasarar rusa dukan tatsuniyoyin da sojojin maƙiya suka yi ta yaɗawa, na cewa ba za a taɓa iya cin nasara a kansu ba, sojojin Misra sun yi masu dukar kawo wuƙa, suka kuma tirsasa girman kansu ya rusuna, suka kuma tilasta wa ƙasashen duniya girmama Misra da sojojinta, taken da sojojin Misra suke rerawa a lokacin yaƙin shi ne **"Allahu Akbar"**, tare da yin azumi da ƙiyamul-laili da karatun Alƙur'ani da yawaita addu'o'i na gaskiya, sai kuwa ga bayyananniyar nasara, inda aka fatattaki azzalumai. A nan dole ne mu tuna da irin sadaukar da kai da Misra da sojojinta suka yi, na samar da manyan shahidai da suka shayar da ƙasarsu da jinanansu wajen bai wa addini, da ƙasa, da mutunci kariya.

Har yanzu sojojin Misra su ne masu bai wa ƙasar, da ma ƙasashen Larabawa, da na Muslunci kariya, har yanzu suna yaƙi da 'yan ta'adda masu yaɗa sharri a bayan ƙasa, suna kuma sadaukar da rayukansu wajen kare ƙasa, da tabbatar da tsaro, da izza da karama, suna kuma kwaɗayin samun shahada kaman yanda waninsu yake kwaɗayin rayuwa, a koda yaushe a shirye suke da su miƙa rayuwarsu wajen kare ƙasa, da yanke

hannayen duk wanda yake yaɗa sharri da ɓarna, yake kuma kawo barazana a cikin tsaron ƙasa, da kwanciyar hankalin 'yan ƙasa, a tsawon tarihi ma su ne garkuwar al'umma, kuma takobinta na yaƙi, tarihi ya kiyaye wannan.

**Ya Ubangiji Allah ka azurta zukatanmu da tsoron Allah, ka tsarkake mana su, kai ne fiyayyen masu tsarkake zukata, kai ne majiɓincin al'amurransu, kuma mahaliccinsu.**

**- 51 –**

## RAMADHAN: WATAN IMANI DA SAMAR DA GWARAZA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((A cikin waɗannan mutanen da suka yi imani da Allah akwai gwarazan da suka yi wa Allah alƙawari jajircewa wajen yin yaƙi a tawagar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), suka kuma cika wannan alƙawari da suka ɗauka, a cikinsu akwai waɗanda suka sami shahada, haka ma akwai waɗanda suke a raye suna tsumayar samun wannan muƙamin, ba su sauya wannan alƙawari da suka ɗauka da kansu ba, ba kuma su rage masa ƙarfi ba)) [al-Ahzab: 23].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai imani da Allah Maɗaukakin Sarki yana cikin manyan ni'imomin da Allah mai girma yake yi wa bawa, Allah mai tsarki yana cewa: **((Sai dai Allah ya sanya soyayyar imani a cikin zukatan kamilallun cikinku, ya kuma ƙawata shi a ciki, haka ya sanya su suka bar ƙawata abin da bai kamata ba, ya**

**kuma sanya maku ƙin inkarin ni'imomin Allah, da fita kan iyakar shari'arsa da saɓa umurninsa. Waɗannan –su kaɗai- su ne waɗanda suka san hanyar shiriya, suka kuma tabbata a kai, duka saboda falala da karamci daga Allah, wannan kuma ni'ima ce babba daga Allah zuwa gare su, ilimin Allah ya mamaye komai, Allah kuma mai cikakkiyar hikima ne wajen zartad da komai)) [al- Hujrat: 7 – 8],** babu wani tantama akan cewa watan Ramadhan shi ne watan imani na haƙiƙa, dalilin haka ne ma ayoyin Azumi a cikin Alaƙur'ani mai girma suka fara da kira da sifar imani, Allah mai girma yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani, Allah mai girma ya shar'anta wajibcin Azumi domin tsarkake zukatanku da daidaita sha'awarku, da fifita ku akan dabbobin da suke bin sha'awarsu, shi wannan wajabta Azumi da aka yi maku kamar yadda aka farlanta wa al'ummomin da suka gabace ku, ba zai yi maku wahala ba, saboda wajibi ne akan mutane baki ɗaya, wajibcin Azumi da tsayawa dominsa duka domin rainon ruhin tsoron Allah a cikinku ne, da kuma ƙarfafa zukatanku da tsarkake su)) [al- Baƙra: 183].**

Shi kuwa imani na ainihi shi ne gasgata dukan abubuwan da suka zo daga Allah Maɗaukakin Sarki, da kuma yin aiki a ƙarƙashin wannan gasgatawar, shahararren Hadisin Jibril (AlaiHis Salam) ya zo mana da bayani akan haƙiƙanin imani da ya zamo dole zuciyar mumini ta ƙudurta, lokacin da ya tambayi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) akan imani, sai ya ce masa: **(Ka gasgata samuwar Allah, da samuwar Mala'ikunsa da littattafansa da Manzanninsa, da ranar lahira, ka kuma yi imani da ƙaddara ta alhairi da ta sharri)**, imani bai taƙaita akan kalma kawai ba, shi imani na haƙiƙa shi ne wanda ya sami wuri

a cikin zuciya, sannan kuma aiki ya gasgata shi, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai muminai na gaskiya da a koda yaushe suke cikin hali na tsoron Allah, da yi masa biyayya, su ne waɗanda idan an ambaci Allah Maɗaukakin Sarki, zukatansu suke ƙyarma, su kuma cika da kwarjininsa, saboda haka ne ma a duk sanda aka karanta masu ayoyin Alƙur'ani mai girma sai imaninsu ya ƙara ƙarfi da tabbata, su kuma ƙara miƙa- wuya, da kuma ilimi, ba sa dogara da kowa sai Allah da ya halicce su, yake kuma ba su kariya da arziki.. Su waɗannan muminai na gaskiya ɗin suna tsayar da sallah, suna masu cika rukunnanta, cikin tsoron Allah da miƙa-wuya, domin su kasance a koda yaushe cikin ambatonsa, suna kuma ciyar da wani sashe na arzikin da Allah ya ba su a fagen jahadi, da biyayya, da taimakon marasa ƙarfi.. Lallai masu waɗannan sifofi su ne muminai na gaskiya..)) [al- Anfal: 2 - 3]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Musulmi shi ne wanda sauran Musulmai suka tsira daga harshensa da hannunsa, mumini kuma shi ne wanda mutane suka amince masa akan dukiyarsu da rayukansu)**.

Duk wanda ɗabi'unsa, da ayyukansa suka kauce wa umurnin Allah Maɗaukakin Sarki da haninsa, to kuwa lallai ya kauce ga barin hanyar imani, saboda haka ne ma Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Mazinaci ba ya yin zinarsa a lokacin da yake a matsayin mumini, haka ma mashayin giya ba ya shan giyarsa a lokacin da yake a matsayin mumini, haka ma ɓarawo ba ya satarsa a lokacin da yake a matsayin mumini)**.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kore cikar imani ga duk wanda yake cutar da maƙwabcinsa, ko kuma ya

kwana a ƙoshe alhali maƙwabcinsa ya kwana da yunwa kuma yana sane, saboda shi imani dole ne ya haɗu da aiki, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(wallahi bai yi imani ba, wallahi bai yi imani ba, wallahi bai yi imani ba.. Sai aka ce: wane, ya Manzon Allah? Sai ya ce: wanda maƙwabcinsa bai aminta daga cutarwarsa ba)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mutumin da ya kwana a ƙoshe, amma maƙwabcinsa na kusa ya kwana da yunwa, alhalin yana sane, to lallai bai yi imani da ni ba)**.

Imani na haƙiƙa shi ne wanda yake kiyaye mai shi daga kutsawa cikin haƙƙoƙin wasu, da zaluntarsu, yake kuma tsarkake zuciyar mai shi daga barin ƙeta da hassada, da son kai, da ƙiyayya, da yaudara, da ha'inci, da cin hanci da rashawa, da ɓarna, shi ne yake tsaftace da daidaita ɗabi'un mai shi, a kuma ga tasirinsa a cikin ayyukansa, da duk wani matsi nasa a cikin rayuwa, da mu'amalarsa da ɗaukacin halittun Allah, ya zamo mai tausayi ga mutane, da dabbobi da ma abubuwa marasa rai, duka saboda neman yardar Allah shi kaɗai, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Suna kuma ciyar da abinci -duk da suna so suna kuma matuƙar buƙatarsa- ga matalaucin da ya gajiya wajen nema, da ƙaramin yaron da ya rasa mahaifansa, da fursinan yaƙin da ba ya mallakar komai. Suna kuma faɗi a cikin zuciyarsu cewa: muna ciyar da ku ne kawai saboda biɗar yardan Allah, ba ma son ku ba mu wani abu a maimakonsa, ko ku yi mana kyauta, haka ma ba ma son yabo daga gareku))** **[al- Insan: 8 – 9]**.

Shi imani tamkar wata bishiya ce da jijiyoyinta suka kafu a cikin ƙasa, rassanta kuma suka yi sama, idan har jijiyoyinta suka tabbata, suka kuma yi ƙarfi, sai ta fitar da 'ya'ya da izinin

Ubangijinta, shi kuma azumi na gaskiya yana fitowa ne daga asalin wannan imanin, sai ya gadar wa zuciya da natsuwa gami da kwanciyar hankali, da kuma halarto da Allah Maɗaukakin Sarki a cikin komai, **sai ka ga mai azumi na gaskiya ba ya ƙarya**; saboda an yi hannun riga tsakanin azumi da ƙarya, azumi yana matakin ƙololuwar halarto da Allah Maɗaukakin Sarki ne a ɓoye kafin ma a sarari, sirri ne da yake tsakanin bawa da Ubangijinsa, ita kuwa ƙarya babban alama ce ta munafunci, hasali ma ita ce babban alamarsa, saboda haka ne ƙarya ta yi hannun riga da haƙiƙanin azumi, ba za su taɓa yin inuwa ɗaya ba, ko dai mutum ya zamo mai azumi, ko kuma dai ya zamo maƙaryaci, saboda haka ne Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Wanda duk bai bar maganar ƙarya da aiki da ita ba, to babu ruwan Allah da barin cin abinci da abin sha da ya yi),** haka ma lokacin da aka tambayi Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa: **Shin mumini zai iya zama matsoraci? Sai ya ce: (Na'am), aka ce masa: Shin mumini zai iya zama marowaci? Sai ya ce: (Na'am), aka ce masa: shin mumini zai iya zama maƙaryaci? Sai ya ce: (A'a)**.

Lallai imani da Allah yana da wani ɗanɗano na musamman, babu masu jin wannan ɗanɗanon sai waɗanda suka yarda da Allah, da zukatansu suka cika da imani, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mutumin da ya yarda da Allah a matsayin Ubangiji, ya kuma yarda da Musulunci a matsayin addini, ya kuma yarda da Muhammadu a matsayin manzo, lallai ya ɗanɗani daɗin imani)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Abubuwa uku kam, duk wanda yake akansu ya sami daɗin imani: Ya zamo ya fi son Allah da Manzonsa akan kowa, ya**

**zamo idan zai yi so wani ya so shi saboda Allah, sannan ya ƙyamaci komawa cikin kafirci bayan Allah ya tsamo shi daga cikinsa kaman yanda yake ƙyamatar a jefa shi a cikin wuta)**.

Imani da kyawawan ɗabi'u ɗan juma ne da ɗan jummai, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Waɗanda imaninsu ya fi cika su ne waɗanda suka fi kyawawan ɗabi'u, masu kuma sauƙin kai, suke kuma ɗebe wa mutane kewa, mutane kuma suke ɗebe masu kewa, suke kuma yawan kusantar mutane, sam babu alhairi a tare da wanda ba ya kusantar mutane, mutane ma ba sa kusantarsa)**, lallai imani haske ne, ibada ma haske ne, duk wanda ya ɗanɗani daɗin imani, da garɗin ibada dole ne ya zamo mai sauƙin kai, da kyautata mu'amala, ba zai taɓa yi wa halittun Allah girman kai ba, ba zai murtuke masu fuskarsa ba, ba kuma zai yi masu ƙarfa- ƙarfa ba, ba zai saka mummunan abu da aka yi masa da mummuna ba, a'a, zai yi haƙuri ne ya kuma yafe, saboda haka ne (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Idan ranar azuminku ya yi, kada ku yi zance batsa, kada kuma ku yi faɗa- faɗa, idan wani ya zage ku, ko ya neme ku da faɗa, to ku ce : mu muna azumi)**, dole ne duk wani mai hankali ya sani cewa: ta yiwu ibadunsa su gaza shigar da shi aljanna, amma tabbas kyawawan ɗabi'unsa, da rangwamensa, da kyautata mu'amalarsa da mutane zai shigar da shi aljanna, ƙarƙashin wannan ma'anar ne Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(An yi wa wani mutum da ya gabace ku hisabi, ba a sami wani aikin alhairi a tare da shi ba, kawai dai yakan cakuɗa da mutane kasancewarsa mawadaci, yakan bai wa yaransa umurnin cewa: su ƙyale duk wanda yake cikin halin**

**rashi, sai Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: (Mu ne muka fi cancanta da yin haka akansa, shi ma ku ƙyale shi)**.

A nan muna son mu ƙara tabbatar da cewa: shi imani na gaskiya wani haske ne da Allah Maɗaukakin Sarki yake sanya shi a cikin zuciyar bawa, sai ya gadar masa da hikima da yaƙini, ya zamo yana gani ne da hasken Allah Maɗaukakin Sarki, an ruwaito Hadisi daga Anas Bn Malik (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: **wata rana Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fito, sai wani matashi daga cikin mutanen "al-Ansar" da ake kira da "Harisat Bn an- Nu'uman" ya zo, sai ya ce masa: (Harisat, yaya ka wayi gari? Sai ya ce: Na wayi gari ne a matsayin mumini na gaskiya, ya ce; Sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: (Ka fa duba abin da kake faɗi, domin kowace gaskiya tana da haƙiƙa, mene ne haƙiƙanin imaninka?) sai ya ce: Na nesanta zuciyata ga barin duniya, sai na raya dare na, na kuma yi azumi da rana, kai ka ce ina kallon al'arshin Ubangijina ƙiri – ƙiri, kai ka ce ina kallon mutanen aljanna suna ziyartar juna, kai ka ce ina kallon 'yan wuta suna adawa da junansu a ciki, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: Lallai ka gani, to ka dage (har sau biyu), bawa ne da Allah ya haskaka imani a cikin zuciyarsa)**.

Imani yana da sassa masu yawa, ya kamata kowane mumini ya yi iya bakin ƙoƙarinsa wajen riƙo da shi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Imani ya kasu gida saba'in da wani abu, ko sittin da wani abu, kashin da ya fi girma shi ne faɗin "La'ilaha illalLah", mafi ƙaranci kuma shi ne kawar da abin da zai cutar daga hanya, kunya ma kaso ne daga cikin imani)**, lokacin da wani mutum ya tambayi Imamul

Hassan al-Basriy (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa: kai mumini ne? sai ya ce masa: shi imani iri biyu ne, amma in kana tambaya ta akan imani da samuwar Allah, da imani da mala'iknsa da litattafansa, da Manzanninsa, da aljanna da wuta, da tashin alƙiyama da hisabi, to lallai ni mumini ne, amma idan kana tambaya ta game da maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **((Lallai muminai na gaskiya da a koda yaushe suke cikin hali na tsoron Allah, da yi masa biyayya, su ne waɗanda idan an ambaci Allah Maɗaukakin Sarki, zukatansu suke ƙyarma, su kuma cika da kwarjininsa, saboda haka ne ma a duk sanda aka karanta masu ayoyin Alƙur'ani mai girma sai imaninsu ya ƙara ƙarfi da tabbata, su kuma ƙara miƙa- wuya, da kuma ilimi, ba sa dogara da kowa sai Allah da ya halicce su, yake kuma ba su kariya da arziki.. Su waɗannan muminai na gaskiya ɗin suna tsayar da sallah, suna masu cika rukunnanta, cikin tsoron Allah da miƙa- wuya, domin su kasance a koda yaushe cikin ambatonsa, suna kuma ciyar da wani sashe na arzikin da Allah ya ba su a fagen jahadi, da biyayya, da taimakon marasa ƙarfi.. Lallai masu waɗannan sifofi su ne muminai na gaskiya..))** **[al- Anfal: 2 – 3]** ne, to wallahi ban sani ba, shin ina cikinsu, ko kuwa a'a".

Lallai imani na gaskiya yana gadar wa mai shi da cikakken tsaro da aminci, da kuma nagartacciyar rayuwar da da ma can ba ta samuwa sai da imani, Allah mai girma yana cewa: **((Wanda duk ya aikata ayyuka na gari cikin maza da mata alhalin yana da cikakken imani, to kuwa tabbas za mu raya shi rayuwa mai matuƙar kyau..))** **[an- Nahl: 97]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Waɗanda suka yi imani, zukatansu kuma suka natsu da ambaton Allah, kai lallai**

**tabbas da ambaton Allah ne zukata suke samun natsuwa..))** **[ar- Ra'ad: 28]**, Allah ya jiƙan wanda yake cewa:

"Idan imani ya salwanta babu sauran aminci, babu duniya ga wanda bai raya addini ba.. duk wanda ya yarda da rayuwar da babu addini a cikinta, to kuwa lallai ya yi mata abota ne da ƙarewa".

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

---------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Kasancewar watan Ramadhan watan imani bai hana shi zama watan samar da gwaraza ba, domin lallai azumi makaranta ne da a aikace take fitar da gwaraza na haƙiƙa, Ahmad Shauƙiy yana cewa: "Azumi haramta wa kai wasu abubuwa ne da shari'a ta kawo, haka ma horas da kai ne akan zama da yunwa, da kuma tsoron Allah da miƙa wuya a gare shi, duk wani abubuwa da aka farlanta yana da hikimar da ya sanya aka yi haka, zahirin wannan hukuncin azabtar da kai ne, amma baɗininsa jinƙai ne, yana haifar da tausayi, yana kuma kwaɗaitar da yawaita yin sadaka, yana karya ɗabi'ar girman kai, yana kuma koyar da haƙuri, yana sunnanta yawaita yin biyayya da ɗa'a, ta yanda wanda ya saba

da ƙoshi zai ji yunwa, a kuma hana mawadaci wasu hanyoyinsa na jin daɗi, har ya san irin abin da rashi yake gadarwa, yaya kuma raɗaɗinsa yake idan ya kama mutum".

Lallai idan muka duba Alƙur'ani mai girma za mu ga cewa lallai Allah Maɗaukakin Sarki bai bayar da sifar gwarzantaka ga kowa ba, sai ga waɗanda suka cika sharuɗɗanta, wanda a cikin sharuɗɗan akwai: **cika alƙawarin da aka yi wa Allah Maɗaukakin Sarki**, ba tare da sauyawa, ko jirkitawa, ko karkacewa ba, Allah Mai girma yana cewa: **((A cikin waɗannan mutanen da suka yi imani da Allah akwai gwarazan da suka yi wa Allah alƙawari jajircewa wajen yin yaƙi a tawagar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), suka kuma cika wannan alƙawari da suka ɗauka, a cikinsu akwai waɗanda suka sami shahada, haka ma akwai waɗanda suke a raye suna ƭsumayar samun wannan muƙamin, ba su sauya wannan alƙawari da suka ɗauka da kansu ba, ba kuma su rage masa ƙarfi ba)) [al- Ahzab: 23],** haka ma gwaraza na haƙiƙa su ne waɗanda suka sayar da rayukansu da dukiyoyinsu ga Allah Ubangijin talikai, hakan yana bayyana ne wajen sadaukar da rayuwa da dukiya saboda ɗaukakar addini, da ƙasa, gami da mutunci, duka saboda neman yardar Allah, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai Allah ya sayi rayukan muminai, da dukiyoyinsu daga gare su, akan lallai zai ba su aljanna, suna yaƙar waɗanda suka auka masu da yaƙi fisabililLahi, su kashe, a kuma kashe su, lallai Allah ya yi masu alƙawari na gaskiya a cikin littattafan Attaura da Injila da Alƙur'ani, wane ne kuwa ya kai Allah cika alƙawarin da ya yi, saboda haka albishir ɗinku da wannan kasuwanci da kuka yi da shi, lallai wannan shi ne rabo mafi girma)) [at- Tauba: 111].**

Lallai watan Ramadhan wata ne na raya Masallatai, da ƙiyamullaili, kuma duka biyun ginshiƙai ne na gina gwaraza, Allah mai girma yana cewa a lokacin da yake fuskantar da magana zuwa ga Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam): **((Ya kai mai lulluɓe kai da tufafinsa. Ka tashi da daddare ka yi sallah a mafi yawan dare, ban da ɗan kaɗan daga ciki. Ka tashi tsawon rabin dare, ko ka ɗan taƙaita kaɗan daga rabin daren, ta yadda zai kai kashi ɗaya bisa uku (1/3) na dare. Ko ka yi ƙãrí kaɗan akan rabin daren ta yadda zai zamo ka tashi a kashi biyu cikin uku (2/3) na daren, ka karanta Alƙur'ãni Mai girma a cikin tsanaki, kana mai bayyanar da haruffansa, kana kuma tsayawa a wajajen tsayawa, ka yi cikakken karatu ba tare da tawaya ba. Ya kai wannan Manzo, lallai da sannu za mu saukar maka da Alƙur'ãni da yake ƙunshe da umurni da hani da wajiban ayyuka masu yi wa zukata nauyi da wahala. Lallai ibadar da ake yinta da daddare tafi tabbata a cikin zuciya, ta kuma fi bayyanar da magana, sakamakon natsuwa da tsarki da dare yake da su)) [al- Muzammil: 1- 6]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((A cikin wasu ɗakuna da Allah ya bayar da umurnin a ɗaukaka sunansa, ana yi masa tasbihi safiya da maraice. Gwaraza ne da kasuwanci, ko saye da sayarwa ba sa hana su ambaton Allah, da tsayar da sallah, da bayar da zakka, suna jin tsoron wata rana da idanuwa da ƙwaƙwale suke jujjuyawa)) [an- Nur: 36 – 37]**, haka ma Allah mai girma ya sifanta 'yan aljanna da cewa: **((Sun kasance suna barci kaɗan ne da daddare, a mafi yawan daren kuma suna tashi domin gabatar da ibada. A ƙarshe-ƙarshen daren kuma suna neman gafara)) [az- Zariyat: 17 – 18]**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kafaɗunsu suna nesantar**

**shimfiɗu, suna roƙon Ubangijinsu a hali na tsoron azabarsa da kuma kwaɗayin rahamarsa, suna kuma ciyarwa daga cikin abin da muka azurta su da shi. Babu rai da ya san abin da aka tanadar masa na jin daɗi sakamakon abubuwan da suke aikatawa))** **[as- Sajada: 16 -17].**

Lallai ƙiyamullai na cikin abubuwan da suka kamata mu kiyaye su, musamman a goman ƙarshe na watan Ramadhan, saboda koyi da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), yakan ƙara ƙoƙari a waɗannan kwanaki goma, sama da yanda yake yi a sauran kwanaki, an ruwaito Hadisi daga Sayyida A'ishat (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: **(Idan goman ƙarshe ya shigo, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan zage- dantse, ya raya dare, ya kuma tashi iyalansa)**, ma'anar yana zage- dantse shi ne: ya ƙara ƙoƙari wajen ibada, wasu kuma suka ce: yana nesantar mata, (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: **(Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan haɗa tsakanin sallah da barci a cikin kwanakin ashirin da suke yi saura a cikin Ramadhan, amma idan kwanaki goma suka rage sai ya zage- dantse ya ɗaura ɗamara)**, a wata ruwayar kuma cewa ta yi: **(Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana ƙara ƙoƙari a goman ƙarshe na Ramadhan da ba ya yi irinsa a cikin waninsa).**

Lallai watan Ramadhan yana samar da gwaraza ta hanyar taka wa zuciya burki, da samun natsuwa, da farkar da zukata, da daidaita rayuwa, da kyautata ayyuka, da ɗaukaka kyawawan ɗabi'u na mutuntaka da suke taka - rawa wajen samar da nagartaccen mutum, yanda zai zamo mai tsayawa daidai akan hanya a cikin rayuwa, ya kiyaye haƙƙoƙin da suke a kansa, ya kuma bayar da wajibai da suka rataya a wuyansa,

ya kuma yi aiki tuƙuru wajen samar da dukan alhairai ga kansa, da ƙasarsa, da al'ummarsa, a kuma ƙarashe hakan ya yi tasiri wajen samun kwanciyar hankulan al'umma, da cigabanta, soyayya, da ƙauna, da tausayin juna, da makamantan haka cikin ɗabi'un da suka bayar da gudummuwa wajen cigaban al'umma su yaɗu.

Lallai ya kamata mu mayar da hankali wajen ribatar waɗannan kwanakin da yawaita zikiri, da addu'o'i, da karatun Alƙur'ani mai girma, da ƙara himma cikin duk wani abu da zai ƙara kusanta mu da Allah Maɗaukakin Sarki, saboda kada mu tsinci kawunanmu cikin waɗanda aka haramta masu alhairan waɗannan kwanaki masu albarka, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Ubangijinku yana da wasu kamfata da yake yi a cikin wasu ranaku na shekara, saboda haka ku bijiro da kawunanku zuwa gare su, ta yiwu idan wannan kamfata ta sami ɗaya daga cikinku ya zamo ba zai taɓa yin asara ba har abada).**

**Ya Ubangiji Allah ka amsa mana, domin kai ai yawan ji ne, mai kuma cikakkiyar masaniya akan komai, ka amshi tubarmu, domin kai mai yawan amsar tuba ne, mai kuma yawan rahama.**

## - 52 –

## RAMADHAN: WATAN BIYAYYA DA SADA ZUMUNCI DA SAMUN RAHAMAR ALLAH

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Ba fuskantar wani sashe a gabãshi, ko yammaci shi ne kashin-bayan addini, ko matattara alhairi ba, matattara alhairi yana cikin abubuwa ne masu dama, wasu suna cikin rukunnan ingantacciyyar aƙida ne, wasu kuma suna cikin tushen ayyuka na gari da ibadu. Na farko shi ne: imani da Allah, da ranar tashin alƙiyama, da hisabi, da abubuwan da za su biyo bayan haka a ranar alƙiyama, da imani da mala'iku da littattafan da aka saukar wa Annabawa, da ma su kansu Annabawan. Na biyu shi ne: bayar da dukiya cikin jin daɗin rai ga talakawa, makusanta da marayu da waɗanda buƙatu da rashi suka yi masu yawa, da matafiyan da guzuri ya yanke masu, ba su da abin da zai isar da su zuwa ga manufarsu, da masu roƙon mutane da buƙata ta tilasta masu yin haka, da kuma ciyarwa don manufar 'yanta bayi da 'yanta su ga barin bauta. Na uku: kiyaye sallah. Na huɗu: fitar da zakkar da aka wajabta. Na biyar: cika alƙawari a rai da dukiya. Na shida: haƙuri akan cutar da za ta faɗa wa rai ko dukiya, ko lokacin haɗuwa da abokan gaba a wurin yaƙi. Waɗanda suka haɗa waɗannan aƙidu da ayyuka na alhairi su ne waɗanda suka yi gaskiya**

**cikin imaninsu, su ne waɗanda suka ji tsoron kafirci da ƙasƙanci, suka kuma nesance su)) [al- Baƙra: 177].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai watan Ramadhan mai albarka, wata ne na yawaita biyayya da ɗa'a, wata ne na kyaututtuka, da rahama, da suke zuwa daga Allah Maɗaukakin Sarki, wata ne na azumi da ƙiyamullaili, da sada zumunci, da soyayya, wata ne na taimakekeniya akan ɗa'a, da tsoron Allah, wata ne da ake jarraba haƙurin Musulmi, a kuma jarraba yi domin Allahnsa, da kuma irin yanda yake halarto da Allah Maɗaukakin Sarki a cikin al'amurransa, mai azumi yakan jure wa yunwa da ƙishirwa, ya kuma yi wa sha'awarsa burki, ya kuma ɗauki haƙuri akan cutarwar da yake fuskanta, a gefe ɗaya kuma, yana ƙara kusantar Ubangijinsa ta hanyar ayyukan ɗa'a da biyayya mabambanta, irinsu: karatun Alƙur'ani mai girma, da zikirin Allah, da ƙiyamullaili, da sadaka, da sulhu a tsakanin mutane, yakan aikata duk wani abu na alhairi da zai amfani ƙasa da 'yan ƙasa, duka waɗannan suna cikin kyautatawar da suke jawo wa bawa rahamar Ubangiji Allah mai girma da ɗaukaka, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai rahamar Allah tana kusa da masu kyautatawa)) [al- A'araf: 56]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai wannan alhairin taskoki ne, kuma waɗannan taskoki suna da mabuɗai, madalla da bawan da Allah ya sanya ya zamo mabuɗin alhairi, makullin**

**sharri.. Bone ya tabbata ga bawan da Allah ya sanya ya zamo makullin alhairi, mabuɗin sharri)**.

Lallai watan Ramadhan mai albarka, wani farfajiya ne na gasa wajen ayyukan alhairi da biyayya, inda bayi suke gasa da tsarkakan ayyukansu, wajen ƙara samun kusanci da Allah Mabuwayin Sarki, haka Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake kasancewa a duk sanda watan Ramadhan ya kama, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: **Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yafi kowa kyauta, kuma kyautarsa a watan Ramadhan yafi na kowane wata, a lokacin da Mala'ika Jibril yake haɗuwa da shi, kuma yana haɗuwa da shi ne a dukan dararen watan Ramadhan suna darasin Alƙur'ani, wallahi Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yafi sakakkiyar iska yawan kyauta)**.

Ramadhan fage ne mai faɗi na gabatar da ayyukan biyayya, musamman ciyar da abinci, da yake sifa ce daga cikin sifofin wannan wata mai karamci, kai ma sifa ce cikin sifofin addininmu mai girma, Sayyiduna Abdullahi Bn Salam (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zo Madina, mutane sun yi cincirundo sun tafi wurinsa, ni ma ina cikin waɗanda suka yi cincirundon, lokacin da na ga fuskarsa na san cewa lallai wannan ba fuskar maƙaryaci ba ne, na ji shi yana cewa: **(Ya ku mutane, ku ciyar da abinci, ku kuma yaɗa sallama, ku kuma sada zumunci, ku kuma yi sallah a lokacin da mutane suke barci, sai ku shiga aljanna cikin aminci)**; wannan magana ta Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ta ƙunshi ɗabi'u guda huɗu, uku daga cikinsu suna da dangantaka ne da alaƙar da take tsakanin mutane;

waɗanda su ne: ciyar da abinci, da yaɗa sallama, da sadar da zumunci, na huɗun kuma yana da jiɓi ne da dangantakar da take tsakanin bawa da Ubangijinsa; wato sallah cikin dare a lokacin da mutane suke barci, haka ma wani mutum ya tambayi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) akan: wane aiki ne ya fi alhairi a Musulunci? Sai ya ce: **(Ka ciyar da abinci, ka kuma yi sallama ga waɗanda ka sani da waɗanda ba ka sani ba)**.

Ya kamata mutum kada ya raina, ko wulaƙanta duk wani aikin alhairi, domin bai da masaniya akan wane aiki ne Allah Maɗaukakin sarki zai amsa daga gare shi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Kada ka kuskura ka raina wani abu daga cikin ayyukan alhairi, kai ko da ka taimaka da bakin igiya ne, kai ko da hancin takalmi ne, kai ko da ka zuba ruwan gugarka ne a ƙwaryar mai neman ruwan sha, kai ko da ka kawar da wani abu ne da yake cutarwa daga barin kan hanyar mutane, kai ko da ka haɗu da ɗan uwanka ne kana fara'a, kai ko da ka haɗu da ɗan uwanka ne ka yi masa sallama, kai ko da ka ɗebe wa mutanen da suke cikin damuwa kewa ne a bayan ƙasa, idan wani ya zage ka da wani abu da ya sani a tare da kai, wanda kai ma ka san irin haka a tare da shi, to kai kada ka zage shi, sai ka sami ladansa, shi kuma ya ɗauki zunubinsa, duk abin da kunnenka ya ji daɗin sauraronsa, to ka yi aiki da shi, haka ma duk abin da kunnenka ba su ji daɗin sauraronsa ba, to ka nesance shi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wajibi ne kowane Musulmi ya yi sadaka)**, sai aka ce: Idan bai sami abin da zai yi sadakar ba fa? Sai ya ce: **(Ya yi aiki da hannunsa ya sami abin da zai amfani kansa, sannan kuma ya yi sadaka)**, sai

aka ce: idan bai da ikon yin aikin fa? Sai ya ce: **(Ya taimaka wa wanda buƙata ta tilasta masa)**, aka ce: idan bai yi ba fa? Sai ya ce: **(Ya bayar da umurnin aikata alhairi da adalci)**, aka ce: idan bai iya yin hakan ba fa? Sai ya ce: **(Ya kame ga barin aikata sharri, domin hakan ma sadaka ne a gare shi)**.

Anan muna ƙara tabbatar da cewa: kalmar "biyayya" ta game dukan ɗabi'un alhairi, da duk wani aiki da yake yardar da Allah Maɗaukakin Sarki, yake kuma amfanar mutane, abin da kuma ya tattara duka waɗannan shi ne "kyawawan ɗabi'u"; saboda haka ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Biyayya ita ce: kyawawan ɗabi'u)**, haka ma cika alƙawari, da yaba kyauta ga waɗanda suka yi, ɗabi'a ce mai asali da babu masu sifantuwa da ita sai masu hankali da nagarta, Allah ya ƙara rahama ga wanda yake cewa:

"Lallai cika alƙawari ga mutum mai karamci wajibi ne, a koda yaushe zargi yana tattare da wanda yake karya alƙawari.. a koda yaushe mutum mai karamci yakan yi adalci ga dukan waɗanda yake rayuwa da su, shi kuwa la'ananne a koda yaushe nesa da adalci yake".

Wani ma yana cewa:

"Lallai a duk sanda mutane masu karamci suka sami wadata, nan take suke tunawa da waɗanda suka yi cuɗanya da su a lokacin ƙunci".

A cikin manyan ɗabi'un biyayya akwai: **sadar da zumunci tsakanin 'yan uwa da makusanta da maƙwabta, da ma mutane baki ɗaya**, hakan babban hanya ne na tabbatar da soyayya, da kyakkyawar dangantaka, da yaɗa ɗabi'ar tausayi a tsakanin ɗaukacin mutane, lallai husuma, da masu husuma ba su da wuri a cikin farfajiyar watan Ramadhan, tun da dai watan

Ramadhan wata ne na sadarwa, a jeren farko na abubuwan da za a sadar kuwa akwai abubuwa guda biyu: **sadar da zumunci,** lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana matsayin haka a Hadisi Ƙudsiy da ya ruwaito daga Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka da yake cewa: **(Ni ne Allah, ni ne kuma Arrahman, na halicci mahaifa, na kuma samo mata suna daga cikin sunaye na, duk wanda ya sadar da ita, zan sadar da shi da rahama, wanda kuma duk ya yanke ta zan yanke shi ga barin rahama)**, sannan Annabinmu ya ce: **(In kuna so, ku karanta maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: ((Ya ku munãfukai, da ma me ake jira daga gare ku a lokacin da kuka kawar da kawunanku ga barin yi wa Allah biyayya banda yin ɓarna a bayan ƙasa, da yayyanke zumunta? Waɗannan su ne waɗanda Allah ya nesanta su ga barin rahamarsa, sai ya kurumtar da su ga barin jin gaskiya, ya kuma makantar da idanuwarsu ga barin ganin hanyar shiriya. Shin sun makance ne ba sa fahimtar shiryatarwa ta Alƙur'ãni Mai girma!, A'a, a zukatansu dai ne akwai abin da yake katange su ga barin yin tunani na lura a cikinsa)) [Muhammad: 22 – 24],** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ana bijiro da ayyuka a kowace ranakun Litini da Alhamis, a cikin waɗannan kwanaki guda biyu, sai Allah ya gafarta wa duk mutumin da bai haɗa da Allah da wani a wajen bauta ba, banda wanda akwai husuma da gaba tsakaninsa da ɗan uwansa, sai a ce: ku ƙyale waɗannan biyun har sai sun yi sulhu a tsakaninsu)**.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya sada zumunci a cikin ginshiƙan imanin da ya yi kira zuwa gare su (SallalLahu alaiHi wa sallam) tun farkon aiko shi a matsayin

Annabi, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Amru Bn Abasat, ya ce: Na shiga wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) – yana nufin a farko farkon Annabta-, sai na ce masa: kai wane ne? Sai ya ce: **(Ni Annabin Allah ne)**, sai na ce: mene ake nufi da Annabin Allah? Sai ya ce: **(Ɗan saƙon Allah)**, sai na ce: (Allah ne ya aiko ka? Sai ya ce: **(Na'am haka ne),** sai na ce: da mene ya aiko ka? Sai ya ce: **(A kaɗaita Allah kada a haɗa shi da kowa wajen bauta, a kuma karya gumaka, a sadar da zumunci)**, haka (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kuma sanya zumunci ya zamo alama cikin alamomin imani, a inda yake cewa: **(Duk wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya sadar da zumuncinsa)**, haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya tabbatar da haka a inda yake cewa: **((Mazumunta su ne suka fi cancanta da juna a cikin littafin Allah)) [al- Anfal: 75; al- Ahzab: 6].**

Ɗaya ɓangaren na sadarwar kuwa shi ne: **sada zumunci da duk waɗanda kake rayuwa da su**, kada ka yarda ka yanke zumunci da kowa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Sam bai halatta mutum ya ƙaurace wa ɗan uwansa sama da darare uku ba, ta yanda za su haɗu: wannan ya kawar da kansa, ɗayan ma ya kawar da kansa, wanda ya fi alhairi a cikinsu shi ne wanda ya fara yin sallama)**, ma'anar "farawa da sallama" ba wai ta taƙaita ne da fara yin sallama idan sun haɗu a hanya kawai ba, ma'anar ita ce sallama da dukan ma'anonin da take ɗauke da su, ya zamo sallama ce ta haƙiƙa, ba wai ta je ka na yi ka ba, ba sallama da harshe, ƙiyayya a zuciya ba, a'a, sallama da zuci, da sallama tare da abokai, da 'yan uwa da maƙwabta, da abokan aiki, da na sana'a, da mutane, da dabbobi, kai har da ma abubuwa marasa rai, da dukan halittu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku**

**waɗanda kuka yi imani da Allah, ku zamo masu son zaman lafiya tsakaninku da juna baki ɗaya, kada ku tayar da ƙabilancin zamanin jahiliyya da makamantan haka, na abubuwan da suke zama sanadiyyar rikici da saɓani a tsakanin ku, kada ku bi hanyar shaiɗan wanda take tunkuɗa ku zuwa ga rabuwar kawuna, lallai shi maƙiyinku ne mai kuma bayyanar da gaba))** [al- Baƙra: 208]**.**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai hikimar Allah Ubangiji mai girma da ɗaukaka ta hukunta sanya kwanaki goma na ƙarshe a watan Ramadhan su zamo dama ne ga mai kyautatawa na ya ƙara yawaita ayyukan alhairi, haka ma dama ce ga wanda ya taƙaita a baya; domin ya cike naƙasun da ya kuɓuce masa, kwanaki ne da suke cike da rahama da kyaututtukan Allah Ubangiji, da yake bai wa bayinsa, ya kamata kowane Musulmi ya bijiro da kansa zuwa ga wannan rahama ta Allah Maɗaukakin Sarki, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Ubangijinku yana da wasu kamfata da yake yi a cikin wasu ranaku na shekara, saboda haka ku**

**bijiro da kawunanku zuwa gare su, ta yiwu idan wannan kamfata ta sami ɗaya daga cikinku ya zamo ba zai taɓa yin asara ba har abada);** saboda haka ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya keɓance waɗanan kwanaki da ƙarin ibadu da yi wa Allah biyayya, da kuma ƙara kusanci da shi mai girma da ɗaukaka.

A cikin abubuwan da ya kamata mu mayar da hankali a kansu wajen raya kwanaki goman ƙarshe na watan Ramadhan akwai: **Himma wajen raya dare**, muna masu koyi da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam), domin (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan ƙara ƙoƙari a cikin kwanaki goman ƙarshe na Ramadhan da bai yin irin wannan ƙoƙarin a wasunsu, an ruwaito Hadisi daga Sayyida A'ishat (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: **(Idan goman ƙarshe ya shigo, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan zage- dantse, ya raya dare, ya kuma tashi iyalansa)**, haka ma a wata ruwayar tana cewa: **(Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yakan haɗa tsakanin sallah da barci a cikin kwanakin ashirin da suke yi saura a cikin Ramadhan, amma idan kwanaki goma suka rage sai ya zage- dantse ya ɗaura ɗamara)**.

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya keɓance darare goma na ƙarshen watan Ramadhan da wani dare mafi girma da falala, wato **"Lailatul- Ƙadri"**; Allah ya yi haka ne domin ya karrama al'ummar masoyinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam), an ruwaito Hadisi daga Mujahid (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa: Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ambaci wani mutum daga Bani Isra'ila da ya ɗauki makami domin ɗaukaka addinin Allah har na tsawon watanni dubu, sai ya ce: sai mutane suka yi mamakin haka, ya ce: Sai Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar da:

**((Mu kam mun saukar da Alƙur'ãni ne a wani dare mai daraja da girma. Kai dai ba ka san dare mai daraja da girma ba ne!. Ai wannan daren mai daraja da girma, matsayinsa da darajarsa ya zarce watanni dubu, saboda Allah ya keɓance shi da saukar da Alƙur'ãni** Mai **girma!. Mala'iku, har da Jibrilu (Alaihimus-Salam) suna sauka ƙasa a cikinsa da izinin Allah, saboda dukanin wani umurni.. Wannan dare aminci ne ga barin duk wani abu mai cutarwa, har zuwa lokacin fitowar alfijiri)) [al- Ƙadar: 1 – 5]**, yin ibada a cikin wannan daren da ikhlasi ya fi yin jahadi wajen ɗaukaka kalmar Allah har na tsawon watanni dubu.

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana cewa tsayuwar wannan dare, babban sanadi ne na gafarta zunubai, a inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Wanda duk ya raya daren Lailatul Ƙadri cikin imani, da neman lada a wurin Allah, to za a gafarta masa zunubansa da suka gabata)**, saboda haka ya kamata kowane Musulmi ya dage wajen raya wannan dare mai daraja, yana mai neman samun kusanci da Allah Maɗaukakin sarki, yana kuma kwaɗayin samun gafara daga gare shi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zaburar da mu akan mu nemi wannan dare a cikin mara na goman ƙarshe (ashirin da ɗaya, da ashirin da uku, da ashirin da biyar, da ashirin da bakwai, da ashirin da tara), saboda yawan baiwa, da kyaututtuka, gami da karamcin Ubangiji da suke cikinsa, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ku nemi lailatul Ƙadri a cikin mara na goman ƙarshen watan Ramadhan)**, a wata ruwayar kuma ya ce: **(Ku nemi shi a goman ƙarshe na Ramadhan –yana nufin lailatul Ƙadri- ana fatan ya zamo daren ashirin da tara, ana fatansa a**

**daren ashirin da bakwai, ana fatansa a daren ashirin da biyar)**.

A cikin muhimman ayyuka na gari a cikin waɗannan kwanakin akwai: **fitar da Zakkar - kono "Zakkatul Fiɗri"**, wanda aikinta shi ne tsarkake mai azumi, da kuma toshe uwar hanjin talakawa da miskinai, an ruwaito Hadisi daga Abdullahi Ɓn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: **(Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya farlanta zakkar kono ne domin ta tsarkake mai azumi daga barin yasassun zantuka, da na batsa da ya yi, hakan kuma ya zamo hanya ta ciyar da miskinai, wanda ya fitar da ita kafin sallah, to ya bayar da zakkarsa an kuma karɓa, wanda kuma ya bayar bayan sallah, to sadaka kawai ya yi)**.

Haka ma a cikin akwai **ƙara himma wajen yawaita addu'a**: Duk da cewar watan Ramadhan gaba ɗayansa wata ne na amsar addu'a, sai dai an fi fatan amsar addu'o'i a kwanaki goman ƙarshe na cikinsa, an ruwaito Hadisi daga Ummul-muminina A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: Na ce: ya Manzon Allah, idan Allah ya sanya na san cewa ga daren lailatul Ƙadri, mai zan roƙa? Sai ya ce: **(Ki ce: Ya Ubangiji lallai kai mai yawan yafiya da karamci ne, kana kuma son yafiya, ina roƙonka ka yafe mini)**.

Lallai ya kamata mu mayar da hankali wajen ribatar waɗannan kwanaki masu falala, da wannan dare na lailatul Ƙadri mai albarka da yawaita zikiri, da addu'o'i, da karatun Alƙur'ani mai girma, da ƙara himma cikin duk wani abu da zai ƙara kusanta mu da Allah Maɗaukakin Sarki, saboda kada mu tsinci kawunanmu cikin waɗanda aka haramta masu alhairan waɗannan kwanaki masu albarka, lallai duk wanda aka

haramta masa rahama a wannan dare, to kuwa lallai ya yi cikakkiyar asara, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Allah yana da wani dare a cikin da ya zarce watanni dubu alhairi, duk wanda aka haramta masa alhairansa, to kuwa lallai ya yi cikakkiyar asara..)**.

**Ya Ubangiji, lallai kai mai yawan yafiya da karamci ne, kana kuma son yafi, ina roƙonka ka yafe mana.**

**- 53 –**

## BAYAN IBADUN RAMADHAN SAI KUMA ME NE?

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Lallai waɗanda suka ce: Allah shi ne Ubangijnmu, suna masu iƙirari da kaɗaituwarsa, sannan suka tsaya ƙyam akan Shari'arsa, mala'iku ne suke sauka zuwa gare su daga lokaci zuwa lokaci, suna ce masu: kada ku ji tsoron sharrin da zai same ku, kada kuma ku yi baƙin ciki akan alhairin da zai kuɓuce maku, a yi masu albishir da aljannar da aka yi masu alƙawari ta bakin Annabawa da Manzanni)) [Fussilat: 30].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda a cikin Hadisinsa mai girma yake cewa: **(Fiyayyen aiki a wurin Allah Maɗaukakin Sarki shi ne wanda aka dawwama ana yinsa, koda kuwa kaɗan ne)**, ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai mai lura da sunnonin Allah, da tsarinsa na halitta zai riski irin yanda kwanaki, da watanni, gami da shekaru suke saurin wucewa, rayuwa gaba ɗayanta ba ta wuce wasu ƙididdigaggun numfashi da za su dakata a lokacin da Allah ya hukunta ba, wannan kuwa ba ƙaramin abin lura ba ne ga masu

tunani da lura, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shi Allah shi ne ya sanya dare da rana domin su rinƙa kwafe makwafin juna, ya kuma yi haka ne saboda mai son ya tuna Allah ya tuna da shi, ko mai son ya gode masa shi ma ya gode masa)) [al- Furƙan: 62]**, haka ma yana cewa: **((Kada ka nemi a gaggauta kama su, mu ƙididdige masu kwanakinsu muke yi)) [Maryam: 84].**

Ganin cewa ɗan Adam a wannan duniya a sarƙafe yake da ayyukansa; saboda Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai mutum ba shi da wani abu face sakamakon abin da ya aikata.. Kuma da sannu za a bayyana aikinsu a ranar alƙiyãma kowa ya gani; saboda a girmama wanda ya kyautata ayyuka, a kuma ƙasƙantar da wanda ya munana.. Sannan a saka wa mutum akan aikinsa da cikakken sakamako)) [an- Najmi: 39 -41]**, ya zama wajibi ga mai hankali ya dage wajen yin ɗa'a da biyayya, ya kuma dawwama akai har Allah Maɗaukakin Sarki ya azurta shi da kyakkyawan ƙarshe, ta yanda zai haɗu da Allah mai girma a matsayin yardadden Allah, saboda shi ɗan Adam ba shi da masaniya akan: shin ta wace ƙofa ta biyayya ce Allah zai amsa daga gare shi, domin dai Allah ya ɓoye rahamarsa ne a cikin yi masa biyayya, ashe ba Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Wani mutum yana tafiya akan hanya, sai ƙishirwa mai tsanani ya kama shi, sai ya sami wata rijiya, ya shiga ciki ya sha ruwa, bayan ya fito sai ga wani kare yana lallage, yana cin taɓo saboda tsananin ƙishi, sai mutumin ya ce: lallai wannan karen yana matuƙar jin ƙishi kaman yanda na ji, sai ya shiga rijiyar ya cika ƙafar takalminsa da ruwa, ya riƙe shi da bakinsa, har ya fito, sai kuwa ya shayar da wannan karen, Allah ya gode masa, ya kuma gafarta masa),** a wata

ruwayar kuma: **(Sai Allah ya gode masa, ya kuma shigar da shi aljanna)** ba?

Haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya ɓoye fushinsa a cikin saɓonsa, ɗan Adam bai san da wane irin saɓo ne Allah zai kama shi, ya kuma yi masa uƙuba ba, ashe ba Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ne ya ce: **(Wata mata ta shiga wuta saboda wata magiya da ta ɗaure, ita ba ta ba ta abinci ba, ba kuma ta barta ta ci ƙwari a bayan ƙasa ba)?**, lallai abin lura a cikin ayyuka shi ne ƙarshe, kaman yanda mai gaskiya abin gasgatawa, wanda ba ya furuci akan son zuciya ya bayyana, a inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Lallai ta yiwu a sami bawa ya aikata aikin da mutane suke ganin aiki ne na ‘yan aljanna, amma kuma tabbas shi ɗan wuta ne, ta kuma yiwu ya aikata aikin da mutane suke ganin aiki ne na ‘yan wuta, amma kuma tabbas shi ɗan aljanna ne, abin lura a cikin ayyuka shi ne ƙarshe)**; saboda haka ne (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake roƙon Allah Maɗaukakin Sarki ya ba shi kyakkyawan ƙarshe, yana mai karantar da al’ummarsa haka, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Anas (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana yawan faɗin: **(Ya mai jujjuya zukata, ina roƙon ka tabbatar da zuciya ta akan addininka)**, sai na ce: Ya Manzon Allah, lallai mun yi imani da kai, mun kuma yi imani da abin da ka zo mana da shi, shin kana ji mana tsoro ne? sai ya ce: **(Ey, lallai zukata suna hannun Allah ne, yana kuma jujjuya su yanda yake so)**.

Babu shakka, masu hankali da basira sun san cewa lallai Ubangijin Ramadhan shi ne Ubangijin Shawwal, kuma Ubangijin sauran watanni, da kwanaki, da sauran zamunna, da

wurare, saboda haka, idan watan Ramadhan ya shuɗe da alhairai, gami da albarka, da rahamar da suke ƙunshe a cikinsa, mene ne kuma yake cikin watan Shawwal?. Lallai duka ƙofofin alhairi suna nan a buɗe, domin Ubangijin girma da ɗaukaka bai gushe ba da daddare yana maraba da tubar wanda ya munana aiki da rana, da rana kuma yana maraba da tubar wanda ya munana aiki da daddare, wannan kuwa yana faruwa a cikin watan Ramadhan, da watan Shawwal, da watan Zul Ƙida, kai a ma kowane lokaci, har sai rana ta fito daga mafaɗarta, an ruwaito Hadisi daga Abu Musa al-Ash'ariy (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Lallai Allah Maɗaukakin Sarki yakan shimfiɗa rahamarsa da daddare, domin wanda ya munana aiki da rana ya tuba, yakan kuma shimfiɗa ta da rana domin wanda ya munana aiki da daddare ya tuba, har sai lokacin da rana ta fito daga mafaɗarta)**.

Duk da cewa an buɗe ƙofofin aljanna a watan Ramadhan, haka za su cigaba da kasancewa a buɗe har bayan Ramadhan, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa: lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ana buɗe ƙofofin aljanna a ranar Litini da ranar Alhamis, a kuma gafarta wa duk wani bawa da bai haɗa Allah da wani a wajen bauta ba, sai dai wanda akwai gaba tsakaninsa da ɗan uwansa, sai a ce wa Mala'iku: ku ƙyale waɗannan biyun har sai sun yi sulhu a tsakaninsu),** babu shakka, duk wanda ya ɗanɗana shi ne yake sani, wanda kuma ya sani shi ne yake kutsawa, wanda kuma ya kutsa zai isa zuwa ga manufa da matsayi, duk wanda ya ɗanɗani daɗin azumi da

ƙiyamullaili da karatun Alƙur'ani mai girma ba zai taɓa barin waɗannan ibadun bayan watan Ramadhan ba.

Lallai malamai masana sun bayyana cewa a cikin alamun amsar ayyuka akwai: mutum ya ji yana son yin aiki da ƙara cigaba da yinsa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai muminai na gaskiya da a koda yaushe suke cikin hali na tsoron Allah, da yi masa biyayya, su ne waɗanda idan an ambaci Allah Maɗaukakin Sarki, zukatansu suke ƙyarma, su kuma cika da kwarjininsa, saboda haka ne ma a duk sanda aka karanta masu ayoyin Alƙur'ani mai girma sai imaninsu ya ƙara ƙarfi da tabbata, su kuma ƙara miƙa- wuya, da kuma ilimi, ba sa dogara da kowa sai Allah da ya halicce su, yake kuma ba su kariya da arziki))** **[al- Anfal: 2]**, haka ma Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar da littafin da ma'anoninsa da lafuzzansa suka yi kama da juna wajen isa matuƙa a gagara da mu'ujiza, da kuma tsarin hukunce – hukunce, wa'azi da hukunce – hukunce suna kai-komo a cikinsa, kaman yanda ake yawan maimaita tilawarsa, fatun waɗanda suka jin tsoron Ubangijinsu suna raurawa a duk sanda suka yi ana karanta ayoyin azaba da narkon cikinsa, sannan kuma fatun nasu da zukatansu sukan yi laushi a lokacin da ake ambaton Allah, lallai wannan littafi da yake ƙunshe da waɗannan sifofi haske ne na Allah da yake bayar da shi ga wanda ya so, ya datar da shi zuwa ga hanyar imani da shi, duk wanda Allah ya ɓatar da shi – sakamakon sanin da ya yi na cewa da ma can zai juya wa gaskiya baya- to kuwa lallai babu wani mai shiryatarwa da zai tsamo shi daga wannan ɓata))** **[az- Zumar: 23]**, duk wanda ya rayu tare da Alƙur'ani a cikin watan Ramadhan, ba zai taɓa iya

ƙaurace masa bayan watan Ramadhan ba, kaman yanda wanda ya saba da ƙiyamullaili, ya kuma ɗanɗani daɗinsa shi ma ba zai taɓa iya ƙaurace masa bayan watan Ramadhan ba, wanda ya ɗanɗani daɗin yawaita kyauta, da baiwa, da ciyarwa saboda Allah a cikin watan Ramadhan, to shi ma ba zai taɓa iya ƙaurace masu bayan Ramadhan ba, idan mutum ya saba da wani aiki na biyayya da ɗa'a a cikin watan Ramadhan, to ya kamata ya cigaba da bin wannan turba a tsawon shekara, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kwaɗaitar da mu akan rashin barin azumi bayan shuɗewar watan Ramadhan, hasali ma ya ƙarfafe mu akan azumtar watan Shawwal, azumin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kira shi da "bibiya", yana cewa: **(Duk mutumin da ya yi azumin watan Ramadhan, sannan ya bibiye shi da azumi shida a cikin watan Shawwal, daidai yake da wanda ya azumci shekara gaba ɗayanta)**.

Lallai azumi na gaskiya shi ne wanda ya gadar wa mai shi da tsoron Allah Maɗaukakin Sarki, idan Allah Mai girma zai yi bayanin sofofin masu tsoron Allah da sakamakonsu cewa yake yi: **((Lallai waɗanda suka bi Allah, suka kuma ji tsoronsa za su ji daɗinsu a cikin aljanna da idanuwan ruwa da ba a iya misalta su.. Suna amsar abubuwan da Ubangijinsu ya ba su na lada da karramawa, lallai su a duniya suna kyautata bayar da abubuwan da aka nema daga gare su kafin wannan lokaci.. Sun kasance suna barci kaɗan ne da daddare, a mafi yawan daren kuma suna tashi domin gabatar da ibada.. A ƙarshe-ƙarshen daren kuma suna neman gafara))** **[az- Zariyat: 15 – 18]**, Allah bai keɓance haka da watan Ramadhan kawai ba, haka ma lokacin da Allah yake sifanta masu ƙiyamullaili cewa ya yi: **((Kafaɗunsu suna nesantar shimfiɗu, suna roƙon Ubangijinsu**

**a hali na tsoron azabarsa, da kuma kwaɗayin rahamarsa, suna kuma ciyarwa daga cikin abin da muka azurta su da shi. Babu rai da ya san abin da aka tanadar masa na jin daɗi sakamakon abubuwan da suke aikatawa)) [as- Sajada: 16 – 17]** bai taƙaita haka da watan Ramadhan banda waninsa ba; a'a, ya sanya shi a matsayin falala ce gamammiya da take a cikin dukan kwanaki da watanni.

Saboda haka, ya zama wajibi ga Musulmi ya cigaba da gabatar da ayyuka na gari, ya tsaya ƙyam akan hanyar yi wa Allah Maɗaukakin Sarki biyayya, ya dawwama wajen halarto da Ubangiji a cikin komai, Allah mai girma yana cewa: **((Ka tsaya ƙyam akan madaidaiciyar hanya kaman yanda aka umurce ka, kai da waɗanda suka tuba tare da kai, kada ku wuce gona da iri, lallai Allah yana da cikakkiyar masaniya akan abin da kuke aikatawa)) [Hud: 112],** haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shin ba ka san cewa lallai Allah ya san abin da yake a sammai da abin da yake a ƙasa ba, babu wata ganawa ta sirri da take gudana tsakanin mutane uku, face ya zama na huɗunsu wajen sanin abin da suke ganawar da shi, ko mutane biyar, face ya zamo na shida, kai, da ma waɗanda ba su kai haka ba, da ma waɗanda suka wuce haka, face yana tare da su, ya san abin da suke ganawa akansa a duk inda suke, sannan kuma zai ba su labarin duk abin da suka aikata a ranar alƙiyãma, lallai Allah yana da cikakkiyar masaniya akan komai)) [al- Mujadala: 7].**

An ruwaito daga Sufyan Bn Abdullahi as- Saƙafi ya ce: Na ce: ya Manzon Allah, ka faɗa mini wani abu a Musulunci da ba zan tambayi wani bayanka ba? sai ya ce: **(Ka ce: Na yi imani da Allah, sannan ka tsaya ƙyam akan hanya madaidaiciya),** lallai

tsayawa ƙyam akan madaidaiciyar hanya, da dawwama akanta sifa ce ta bayin Allah muminai, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai waɗanda suka ce: tabbas Ubangijinmu shi ne Allah shi kaɗai, suka kuma kyautata aiki, to, lallai babu tsoron kada wani abu mai muni ya same su, ba kuma za su yi baƙin-ciki saboda wani abu ya kuɓuce masu ba))** **[al- Ahƙaf: 13],** haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Lallai waɗanda suka ce: Allah shi ne Ubangijnmu, suna masu iƙirari da kaɗaituwarsa, sannan suka tsaya ƙyam akan Shari'arsa, mala'iku ne suke sauka zuwa gare su daga lokaci zuwa lokaci, suna ce masu: kada ku ji tsoron sharrin da zai same ku, kada kuma ku yi baƙin ciki akan alhairin da zai kuɓuce maku, a yi masu albishir da aljannar da aka yi masu alƙawari ta bakin Annabawa da Manzanni))** **[Fussilat: 30].**

Imamul Hasanul- Basriy (Allah ya ƙara yarda da shi) yana cewa: "Lallai a cikin sakamakon kyakkyawan aiki akwai: sake samun daman aikata wani kyakkyawan aikin bayansa, haka ma a cikin uƙubar mummunan aiki akwai: sake samun daman aikata wani mummunan aikin a bayansa, idan Allah ya yi na'am da bawa, sai ya datar da shi wajen yi masa ɗa'a da biyayya, ya kuma nesanta shi da saɓo", duk wanda ya aikata kyakkyawan aiki, sannan ya bibiye shi da wani kyakkyawan aikin, to haka alama ne na an karɓi kyakkyawan aikinsa na farko, wanda kuma ya aikata kyakkyawan aiki, sannan ya bibiye shi da mummunan aiki, to hakan alama ne na rashin karɓar kyakkyawan aikinsa na farko, domin biyayyar da ta gabata takan jawo wata biyayyar ce, wannan yana cikin albarkar kyakkyawan aiki, mummunan aiki ma irinsa yake janyowa.

Lallai muna ƙara tabbatar da cewa: dawwama akan gabatar da ayyukan biyayya, da ibadu, biyayya ne ga maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **((Ka dawwama wajen bauta wa Ubangijinka har mutuwa ta zo maka))** **[al- Hujrat: 99]**, kuma hakan biyayya ne ga maganar Allah mai girma da yake cewa: **((Idan ka kammala al'amurran kira, da na jahadi, to ka ƙara himma wajen ibada kada ka gajiyar da kanka akai.. Kuma zuwa ga Ubangijinka shi kaɗai ne kawai ya kamata ka fuskantar da buƙatunka))** **[as- Sharhi: 7 – 8]**, ma'ana dai: idan ka kammala wata ibada da ɗa'a, to ka fara wata ibada da ɗa'ar kana mai neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki, wannan shi ne abin da Annabinmu mai girma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake aikatawa, **(An tambayi Ummul Mu'uminina Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) cewa: Ya Ummul Mu'uminina, yaya Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake gabatar da ayyukansa ne, shin yakan keɓance wasu kwanaki da wani abu? Sai ta ce: A'a, aikinsa yana yi a dawwame ne)**, a wata ruwayar kuma ta ce: **(Idan ya yi wani aiki sai ya tabbata a kansa)**.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-----------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da

Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai dawwama akan yi wa Allah Maɗaukakin Sarki biyayya, da halarto da shi a cikin komai alamu ne da suke nuna za a yi ƙarshe mai kyau, domin ingantacciyar muƙaddima ce take iya isar da mai ita zuwa ga ingantaccen sakamakon da ake fata, lallai wasu daga cikin malamai sun fahimci haka a cikin maganar Allah Maɗaukakin Sarki da yake cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani ku ji tsoron Allah, tsoron da ya kamata, ta hanyar aikata abin da aka bayar da umurnin a aikata, da nesantar abin da aka hana, ku dawwama cikin Musulunci har zuwa lokacin da za ku haɗu da Allah)) [Ali Imran: 102]**, a tafsirin wannan ayar suka ce, abin da ake nufi shi ne: ku kiyaye Musuluncinku, ku kuma dawwama akan gabatar da ayyuka na gari, da tsoron Allahnku kaman yanda ya kamata, domin rayuwarku ta tafi akan haka, ku mutu akai, a kuma tashe ku akansa, lallai sunnar al-Karimu babban Sarki a cikin halittarsa, ta tafi ne akan cewa: duk wanda ya rayu akan wani abu, to akansa zai mutu, a kuma tashe shi a kai.

A Hadisi kuma, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ba za taɓa ji wa wani rauni a hanyarsa ta ɗaukaka kalmar Allah ba –Allah kaɗai ya san wanda ake ji wa rauni dominsa- face ranar alƙiyama ya zo da launi irin launin jini, amma ƙamshinsa na almiski ne),** lokacin da (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ga mutumin da taguwarsa ta harbe shi a lokacin da yake cikin harami, (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa ya yi: **(Ku yi masa wanka da ruwa, da magarya, ku kuma yi masa likkafani da tufafinsa, kada ku rufe kansa, kada kuma ku**

**shafa masa turare, domin Allah zai tashe shi a matsayin mai harami ne a ranar alƙiyama)**.

Haka ma a cikin dalilan da suke janyo kyakkyawan ƙarshe akwai: gaskiyar bawa da yake yi wa Ubangijinsa, domin gaskiyar niyya ita ce take isar da bawa zuwa ga manufa, babban abin da zai tabbatar da haka shi ne: labarin Balaraben ƙauyen da ya zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), ya yi imani da shi, ya kuma bi shi, sannan ya ce: ina son in yi hijira tare da kai, sai kuwa Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya damƙa shi a hannun wani daga cikin Sahabbansa, lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi rabo da shi, sai aka ba shi, sai ya ce: mene ne wannan? Sai suka ce masa: rabo ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi da kai, sai ya amsa, ya zo wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da shi, sai ya ce: mene ne wannan? Sai ya ce: **(Na yi rabo da kai ne)**, sai ya ce: Ni ba saboda wannan na bi ka ba, na bi ka ne akan a harbe ni da kibiya ta nan –ya yi nuni zuwa ga maƙogwaronsa-, na mutu na shiga aljanna, sai ya ce: **(In dai da gaske kake yi wa Allah, Allah kuwa zai gasgata ka),** ba a daɗe ba sai kuwa aka tafi yaƙi da maƙiya, aka ɗauko shi aka kawo wa Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) an harbe shi da kibiya a inda ya nuna, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Shin shi ne kuwa?)** sai suka ce: Na'am, sai ya ce: **(Ya yi wa Allah gaskiya ne sai kuwa Allah ya gasgata shi),** sai kuwa (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi masa likkafi da alƙyabbarsa, ya kuma shiga gaba ya yi masa sallah, a cikin abin da ya bayyana a cikin sallar da ya yi masa an ji yana cewa: **(Ya Ubangiji, wannan bawanka ne da ya fita ya yi hijira saboda**

**kai, aka kuma kashe shi a matsayin shahidi, ni ina yi masa shaida akan haka)**.

Kai madalla da bawan da Allah ya datar da shi wajen yi masa biyayya, ya kuma kyautata masa ayyukansa da ɗabi'unsa, ya kuma taimaka masa wajen biya wa mutane buƙatunsu, da yaye masu baƙin ciki, da yaɗa alhairi a cikin al'umma da ƙasa baki ɗaya, idan akwai abin da hakan yake nunawa, bai wuce irin yanda Allah ya yarda da shi, da kuma datarwar da Allah ya yi masa ba, domin kyakkyawan ƙarshe na nufin cewa lallai Allah yana son alhairi da bawa, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Anas (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Idan Allah ya yi nufin alhairi da bawansa, sai ya yi amfani da shi)**, sai aka ce: ta yaya zai yi amfani da shi, ya Manzon Allah? S**ai ya ce: (Zai datar da shi wajen aikata aikin alhairi kafin mutuwa)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Idan Allah ya nufi alhairi da bawansa sai ya ƙawata shi kafin mutuwarsa)** sai aka ce: mene ne ma'anar a ƙawata shi kafin mutuwarsa? Sai ya ce: **(Ya buɗe masa hanyoyin yin aikin mai kyau kafin mutuwarsa har ya yarda da shi)**.

**Ya Allah Ubangiji, muna roƙon ka azurta mu da tuba kafin mutuwa, a lokacin mutuwa kuma muna roƙon ka azurta mu da shahada, bayan mutuwa kuma ka azurta mu da aljanna da ni'imominta.**

**- 54-**

## DARUSSA DAGA HUƊUBAR HAJJIN BAN- KWANA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Lallai kam a yau na cika maku hukunce-hukuncen addininku, haka ma na cika ni'imata a gare ku ta hanyar tabbatar da ku akan addini, na kuma zaɓa maku addinin Musulunci ya zamo shi ne addininku)) [al- Ma'ida: 3].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko Manzonsa (SallalLahu alaiHu wa sallam) da shiriya, gami da addinin gaskiya; domin ya fitar da mutane daga duhu zuwa haske, ya kuma yi masu waigi daga faɗawa cikin ɓata, zuwa shiriya, ya bi da su ta gwadaben tsira, da jin daɗin duniya, da na lahira, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kira su zuwa ga kyawawan ɗabi'u, da zaɓaɓɓun tadoji, ya isar masu da saƙon Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka kamar yadda ya kamata, a kuma cikakkiyar sura, lallai a tsawon rayuwarsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) dasa kyawawan ɗabi'u na mutuntaka ya yi, ta

hanyar maganganunsa, da ayyukansa, da abubuwan da ya tabbatar.

Lokacin da Allah Maɗaukakin Sarki ya bai wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) umurnin aikin Hajji, wanda shi ne rukuni na biyar cikin rukunnan Musulunci, Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya tsaya a dutsen Arfa, akan fã, a wani gagarumin taro na mutane - a lokacin-, yana mai bayyana wa sahabbansa, da al'ummomin da za su zo a bayansu yanda ake aikin Hajji, yana kuma dasa ɗabi'un tausayi, da mutuntaka, da ya kwashe tsawon rayuwarsa yana kira zuwa gare su, a daidai lokacin da (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake hararo ajalinsa, da kusantowar ƙarshen rayuwarsa, saboda haka huɗubarsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) ta ƙunshi darussa masu girma, kuma masu yawa, da kuma isassun izina da dukansu manhaji ne na rayuwar bil'adama baki ɗaya..

A cikin waɗannan darussa akwai: **Tabbatar da ƙa'idojin adalci da daidaito tsakanin ɗaukacin mutane,** Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ya ku mutane, lallai Ubangijinku ɗaya ne, haka ma babanku ɗaya ne, ku sani Balarabe ba shi da wata falala akan wanda ba Balarabe ba, haka ma wanda ba Balarabe ba ba shi da wata falala akan Balarabe, jan mutum ba shi da wata falala akan baƙin mutum, haka ma baƙin mutum ba shi da wata falala akan jan mutum, sai ta tsoron Allah, lallai mafi karamci a cikinku shi ne wanda ya fi tsoron Allah...)**; lallai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya tsoron Allah da kyawawan ayyuka su zamo ma'aunai na fifiko, da haka (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi wa maganar Allah Maɗaukakin Sarki biyayya ne a inda yake cewa: **((Ya ku mutane, lallai mun halicce ku ne daga asali ɗaya wanda**

**dukanku kuke daidai da juna, wannan asali kuwa shi ne Annabi Adam da Hauwa'u (Alaihimas-Salãm), ta hanyar auratayya ne kuma muka mayar da ku al'ummomi masu yawa da ƙabilu mababbanta; domin ku san juna, ku kuma yi taimakekeniya a tsakaninku, lallai wanda ya fi matsayi a wurin Allah duniya da lahira shi ne wanda ya fi ku tsoron Allah, tabbas ilimin Allah ya game komai, ƙwararre ne kuma wanda babu wani abu komin ƙanƙantarsa da zai ɓuya masa a cikin dukan al'amurra..)) [al- Hujrat: 13]**, Mutane gaba ɗayansu daidai da juna suke wajen haƙƙoƙi da wajibai, ba tare da bambanci na wadata, ko wariya ta ƙabilanci ba, wannan shi ne adalci wanda shi ne haƙiƙanin ma'auni na tsayar da gaskiya, da daidaiton al'ummomi, Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Idan za ku yi magana ku yi adalci, koda akan makusanta ne..)) [al-An'am: 152]**, Haka ma Maɗaukakin Sarki ya ce: **((Idan za ku yi hukunci a tsakanin mutane, to dole ne ku yi hukuncin cikin adalci..)) [an- Nisa'i: 58]**, Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Kada laifin wasu mutane ya hana ku yi masu adalci, lallai ne ku yi adalci, domin hakan shi ne ya fi kusa da tsoron Allah...)) [al-Ma'ida: 8].**

Haka ma a cikin waɗannan darussa akwai: **alfarmar jini, da ta dukiya, da ta mutunci,** an ruwaito Hadisi daga Abdurrahman Bn Abi Bakrat (Allah ya ƙara yarda da shi), daga babansa, cewa: wata rana Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya zauna akan taguwarsa, wani mutum yana jan akalarta, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wace rana ce wannan?)** Sai muka yi shiru, har sai da muka zaci cewa zai kira da sunan da ba nasa ba, sai ya ce: **(Ba ranar sallar layya ba ce?)** sai muka ce: ƙwarai da gaske, sai ya ce: **(wane wata ne**

**wannan?)**, sai muka yi shiru har sai da muka zaci zai kira shi da sunan da ba nasa ba, sai ya ce: **(Ba watan Zul Hajji ba ne?)** sai muka ce: ƙwarai da gaske, sai ya ce: **(To ku sani, lallai jininku, da dukiyoyinku, da mutuncinmu suna da alfarma a tsakaninku da juna, kaman dai yanda wannan ranar take da alfarma, a kuma wannan wata naku, a kuma wannan garin naku, wanda ya sami halarta ya isar wa wanda bai sami halarta ba, domin ta yiwu wanda ya ji ya isar wa wanda ya fi shi fahimta)**, lallai a wannan wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya faɗakar da sahabbansa, ya kuma ankarar da su da waɗannan kalmomi nasa masu cike da azanci, da suka ƙunshi kyawawan salon Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da suke nuni zuwa ga girman alfarmar jini, da dukiyoyi, da mutunci, da kuma irin kariyar da Allah ya ba su, mai nuna haramcin yi masu ta'annuti da kowane irin nau'i na ta'adi da ta'annuti, lallai addinin Musulunci yana kira ne zuwa ga samar tsaro da kwanciyar hankali, da zaman lafiya da lumana, yana son ɗaukacin mutane su rayu cikin natsuwa da kwanciyar hankali, ba tare da wani bambanci, ko nuna wariya ga wani mutum akan wani ba, koda kuwa daga wani jinsi, ko launi, ko addini yake, domin Shari'ar Musulunci ta bai wa kowane mutum irin wannan kariya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Kada ku kuskura ku kashe ran da Allah ya ba ta kariya sai dai idan akwai dalili da Shari'a ta sanya, da wannan ne Ubangijinku yake yi maku wasici ko za ku hankalta))** **[al- An'am: 151]**, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya sanya kashe rai guda ɗaya ba tare da dalili na Shari'a ba, daidai yake da kashe ɗaukacin mutane, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Wanda duk ya kashe rai ba ta dalilin ƙisasi ba, ko**

**kawai saboda ɓarna a bayan ƙasa, to tamkar ya kashe ɗaukacin mutane ne, wanda kuma ya raya rai tamkar ya raya ɗaukacin mutane ne..))** **[al- Ma'ida: 32]**, saboda ƙarfafa alfarmar da jini yake da shi, da kuma cewa laifi ne mai girma a zubar da shi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) a ƙarshen wannan huɗuba ya sake yin gargaɗi mai tsanani akan haramcin taɓa shi, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Kada ku yarda ku koma kafirai da za su riƙa kashe junansu bayan wafati na)**.

Kaman yanda addinin Musulunci ya haramta yi wa rayuka kowane irin ta'annuti, haka ma ya haramta yi wa dukiyoyi kowane irin nau'i na ta'annuti da zalunci, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai Allah ya haramta maku cin dukiyar waninku –a kowane lokaci- ba tare da haƙƙi ba, kada wani daga cikin ku ya halatta dukiyar waninsa ba ta ɗaya daga cikin fuskokin da Allah ya shar'anta ba, irinsu: gado, da kyauta, da ingantaccen kasuwanci wanda yake halatta mallaka. Zai yiwu waninku ya yi rikici da ɗan uwansa akan dukiya, alhali kuma ba shi da gaskiya, ya shigar da ƙara zuwa ga sarki ko alƙali; domin a yi masa hukuncin da zai amfane shi, ya kuma ƙwace dukiyar ɗan uwansa ta hanyar ɓatacciyar sheda, ko ta ƙarya, ko ta hanyar cin-hanci da rashawa, wanda yake abu ne mai muni, tir da abin da ya aikata, da ma abin da ya jawo wa kansa na mummunan sakamako))** **[al- Baƙra: 188]**, saboda bai wa dukiya kariya ne Shari'ar Musulunci ta haramta sata, ta kuma sanya uƙuba mai tsauri akan yin sata, Allah mai girma yana cewa: **((Hukuncin ɓarawo, da ɓarauniya shi ne ku yanke hannayensu a matsayin sakamakon abin da suka aikata, wannan uƙuba ce daga Allah, lallai Allah mabuwayi ne mai cikakken hikima))** **[al- Ma'ida: 38]**, haka ma Shari'a ta

haramta ƙwace wa mutane filaye da zalunci ta kowane irin nau'i, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya yi zalunci na filaye koda gwargwadon taƙi ɗaya ne, Allah zai nannaɗe masa shi tun daga ƙasan bakwai ya ɗauka ranar alƙiyama).**

Haka ma Musulunci ya haramci cin mutunci, da kutsawa ciki ta kowane irin hanya, babu wani bambanci tsakanin mutuncin Musulmi, da na wanda ba Musulmi ba, Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗi a lokacin da yake haramta zina cewa: **((Kada ku kuskura ku kusanci zina, domin dai lallai zina mummunan abu ne, kuma tir wa hanyarta)) [al- Isra'i: 32],** haka ma Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya haramta yi wa mata masu aure ƙazafi, hasali ma yin haka yana cikin manyan laifuffuka, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ku nesanci aikata abubuwa guda bakwai masu dulmiyar da mutane a cikin wuta)**, aka ce: ya Manzon Allah, mene su kuwa? Sai ya ce: **(…. Da yi wa matan aure da ba su ji ba ba su gani ba, kuma muminai ƙazafi..)**, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya hana zagi da cin mutunci, hasali ma ya kira hakan da suna "fasiƙanci", mai tsira da aminci yana cewa: **(Zagin Musulmi fasiƙanci ne, yaƙarsa kuwa kafirci ne).**

Haka ma a cikin darussan akwai: **kira zuwa ga haɗin kai, da gargaɗi akan rarrabuwar kawuna,** Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana faɗi a cikin wannan huɗuba tasa cewa: **(.. Lallai shaiɗan ya ɗebe ƙaunar a bauta masa a wannan gari naku har zuwa ranar alƙiyama, ya dai yarda da ƙasƙantattun ayyuka da za ku yi, saboda haka ku kiyaye shi a cikin addininku..)**, saboda haka, mu haɗa kawunanmu, gaba ɗayanmu mu yi riƙo da hanyar Allah Maɗaukakin Sarki, domin

mu amsa kiransa mai cewa: **((Ku yi riƙo da igiyar Allah gaba ɗayanku, kada ku kuskura ku rarraba..))** **[Ali Imran: 103]**, da inda yake cewa: **((Ku yi wa Allah da Manzonsa biyayya, kada ku kuskura ku yi rikici, sai rashin nasara ta same, kuma ƙarfinku ya tarwatse..))** **[al- Anfal: 46]**, lallai ya kamata mu sani cewa, lallai husuma da rarraba kawuna ba su daga cikin addinin Allah, Allah Maɗaukakin sarki yana cewa: **((Lallai waɗanda suka rarraba kawuna a cikin addininsu, suka zamo ƙungiya – ƙungiya ba ka tare da su cikin komai..))** **[al- An'am: 159]**, addinin Musulunci yana kira ne zuwa ga haɗin kai, ya kuma haramta rikici da rarrabuwan kawuna.

A cikin darussan ma akwai: **wajibcin riƙo da littafin Allah Maɗaukakin Sarki, da Sunnar Manzonsa (SallalLahu alaiHi wa sallam),** a cikin wannan huɗuba, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(.. Lallai na bar maku abin da ba za ku taɓa ɓacewa ba a cikinku, idan kuka yi riƙo da shi, wato littafin Allah, kuma lallai za a tambaye ku akai na..)**, littafin Allah Maɗaukakin Sarki shi ne dawwamammiyar mu'ujiza, ɓata ba ya iya shiga cikinsa ta kowace irin hanya, ba kuma ya sauyawa sakamakon sassauyawar shekaru da zamunna, da shi, gami da Sunnar Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ne Allah Maɗaukakin Sarki ya daƙile son zuciya, ya kuma kawo ƙarshen rikici na saɓani, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Ya ku waɗanda kuka yi imani da abin da Annabi Muhammadu (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya zo da shi, ku yi wa Allah Maɗaukakin Sarki biyayya, ku kuma yi wa Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) biyayya, da waɗanda suke jagorancin al'amurranku cikin Musulmai masu tsayar da gaskiya da adalci, da masu zartad da Shari'ar Allah**

**Maɗaukakin Sarki, idan kun sami saɓani a tsakaninku, to, ku bijiro da saɓanin ga littafin Allah mai girma da sunnar Manzonsa mai tsarki, domin ku san hukuncinsa; saboda Allah Maɗaukakin Sarki ya riga ya saukar maku da littafinsa, Manzonsa (SallalLãhu alaiHi wa sallam) kuma ya bayyana maku hukunce-hukuncensa, akwai hukuncin abin da kuka yi saɓani akai a cikinsa, wannan shi ne ma'anar imaninku da Allah da ranar lahira, shi ne kuma ya fi alhairi a gare ku, saboda da shi ne za ku shiryu zuwa ga adalci cikin abin da kuka sami saɓani, shi ne kuma ƙarshe mafi kyau, domin yana hana saɓanin da yake kaiwa zuwa ga jayayya da ɓata..)) [an-Nisa'i: 59]**, lallai riƙo da littafin Allah, da riƙo da sunnar Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) alamu ne na imani, hujja ce ta tsoron Allah, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Na rantse da Ubangijinka ba za a taɓa sanya su cikin muminai na gaskiya masu yi wa Allah biyayya ba, har sai sun sanyaka ka zamo alƙali a tsakaninsu cikin abin da suka yi saɓani, sannan kuma ya zama babu wata damuwa a cikin zukatansu cikin hukuncin da ka yi, su kuma yi masa biyayya irinta muminai masu gasgatawa..)) [an- Nisa'i: 65].**

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da

Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Babu shakka huɗubar Ban - kwana ita ce yarjejeniyar da ta fara kiyaye haƙƙoƙin ɗan Adam ta farko a duniya, saboda abin da take ƙunshe da shi na dokokin mutuntaka, da suke kiyaye wa ɗan Adam karamarsa, suke kuma kiyaye masa tsaronsa da zaman lafiyarsa, a cikin muhimman darussan da huɗubar take ɗauke da su akwai: **bayyana matsayi, gami da darajar mace a cikin Shari'ar Musulunci,** lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi wasici da a kula da mace, ya kuma yi hakan ne saboda girmama ta, da kuma bayyana matsayinta da darajarta, lallai mata 'yan uwan maza ne, dukansu suna da haƙƙoƙi da wajibai a tare da juna, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Lallai kuna da haƙƙoƙi akan matanku, su ma suna da haƙƙoƙi akanku..)**.

Lallai addinin Musulunci ya karrama mace a matsayinta na uwa, da 'yar uwa, da 'ya, da mata, ya kuma ba ta haƙƙoƙin da za su kiyaye mata jin daɗin duniya, da na lahira, su kuma kiyaye ta, ya tsare mata karamarta ta mutuntaka, lokacin da aka tambayi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) cewa: Wane ne ya fi cancanta da na abokance shi da kyautatawa? Sai ya ce : **(Mahaifiyarka)**, sai ya ce: sannan wane?, sai ya ce: **(sannan mahaifiyarka)**, sai ya ce: sannan wane?, sai ya ce: **(Sannan mahaifiyarka)**, sai ya ce: sannan wane?, sai ya ce: **(sannan mahaifinka)**. Haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda duk yake da 'ya'ya uku mata, ya yi haƙuri da su, ya ciyar da su ya shayar da su, ya kuma yi masu tufafi gwargwado samu da wadatarsa, za su zamo masa kariya ga**

**barin shiga wuta a ranar alƙiyama)**, a wata ruwayar kuma: **(Wanda duk ya ɗauki ɗawainiyar 'ya'ya mata guda biyu, ko 'ya'ya mata uku, ko 'yan uwa mata biyu, ko 'yan uwa mata uku har zuwa lokacin rabuwa da su (a lokacin aurensu), ko ya mutu ya barsu zan zamo ni da shi kamar waɗannan guda biyu, ya yi nuni zuwa ga 'yan yatsunsa guda biyu, manuniya da yatsar tsakiya)**, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ina yi maku wasici da mata, lallai an halicci mace ne daga haƙarƙari, kuma mafi karkacewar abu a cikin haƙarƙari shi ne samansa, idan ka yi himmar miƙar da shi ya karye, idan kuma ka bar shi ya cigaba da zama a karkace, saboda haka nake yi maku wasici da mata akan dukan alhairi)**; kalmar "alhairi" da ta zo a cikin Hadisin ta game dukan komai da komai, ta kuma katange duk wani abin da ba alhairi ba, tana nuni da wajibcin sifantuwa da mafiya girman ɗabi'un mazakuta a lokacin da maza za su yi mu'amala da mata.

Lallai muna matuƙar buƙatar zartar da waɗannan kyawawan ɗabi'u da suke ƙunshe da dukan alhairai ga bil'adama a aikace, babu shakka, babu wata yarjejeniya da ta gabace ta a tarihin ɗan Adam, domin ita ce ta kafa ƙa'idojin haƙƙoƙin bil'adama, ta kuma shata ginshiƙan ɗabi'un mutuntaka da idan mutane suka yi masu duba ta tadabburi, suka kuna fahimce su, kana suka yi aiki da abin da suke ciki, da kuwa hakan ya zamo babban dalili na jin daɗinsu na duniya, da na lahira..

**Ya Allah Ubangijinmu ka amsa mana ibadunmu, lallai kai mai ya ji ne, mai kuma cikakkiyar masaniya, ka karɓi**

**tubarmu, domin dai kai mai yawan amsar tuba ne, mai kuma yawan jinƙai da tausayi..**

## - 55 –

## BAYAN AIKIN HAJJI SAI KUMA ME NE?

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Lallai waɗanda suka ce: Allah shi ne Ubangijnmu, suna masu iƙirari da kaɗaituwarsa, sannan suka tsaya ƙyam akan Shari'arsa, mala'iku ne suke sauka zuwa gare su daga lokaci zuwa lokaci, suna ce masu: kada ku ji tsoron sharrin da zai same ku, kada kuma ku yi baƙin ciki akan alhairin da zai kuɓuce maku, a yi masu albishir da aljannar da aka yi masu alƙawari ta bakin Annabawa da Manzanni)) [Fussilat: 30].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi ka*-+ɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, wanda a cikin Hadisinsa mai girma yake cewa: **(Fiyayyen aiki a wurin Allah Maɗaukakin Sarki shi ne wanda aka dawwama ana yinsa, koda kuwa kaɗan ne)**, ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai mai lura da sunnonin Allah, da tsarinsa na halitta zai riski irin yanda kwanaki, da watanni, gami da shekaru suke saurin wucewa, rayuwa gaba ɗayanta ba ta wuce wasu ƙididdigaggun numfashi da za su dakata a lokacin da Allah ya hukunta ba, wannan kuwa ba ƙaramin abin lura ba ne ga masu

tunani da lura, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Shi Allah shi ne ya sanya dare da rana domin su rinƙa kwafe makwafin juna, ya kuma yi haka ne saboda mai son ya tuna Allah ya tuna da shi, ko mai son ya gode masa shi ma ya gode masa)) [al- Furƙan: 62].**

Ganin cewa da karɓaɓɓen aikin Hajji ne Allah Maɗaukakin Sarki yake yafe zunubai, mutum ya zamo tamkar ranar da mahaifiyarsa ta haife shi, a inda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake cewa: **(Duk wanda ya yi aikin Hajji bai yi zantukan batsa ba, bai kuma yi fasiƙanci ba, zai komo tamkar ranar da mahaifiyarsa ta haife shi)**, to dole ne mai hankali ya ribaci wannan falala da Allah ya yi masa ta hanyar nesantar sauran ayyukan zunubi, ya fuskanci Allah da tsarkakakkiyar zuciya mai cike da ikhlasi.

Ya kamata zuciyar mahajjanci ta cika da ganin girman ni'imar da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi masa tun da ya ba shi daman gabatar da wannan ibada, ya kuma san cewa lallai hakan yana buƙatar gode wa wanda ya yi masa wannan ni'ima ta hanyar **dawwama akan aikata ayyukan alhairi,** lallai ayyukan ɗa'a da biyayya ba su taƙaita kawai da wani lokaci, ko wuri ba, a'a, abubuwa ne da suke cigaba matuƙar ɗan Adam yana raye, ya kuma cika sharuɗɗan zama mukallafi, wannan ne tadar Annabinmu mai karamci (SallalLahu alaiHi wa sallam), lallai dawwama akan ayyukan biyayya, da na ibadu yi wa maganar Allah Maɗaukakin Sarki biyayya ne a inda yake cewa: **((Ka bauta wa Ubangijinka tsawon rayuwa har mutuwa ta zo maka)) [al- Hujrat: 99]**, da maganarsa mai girma da ɗaukaka da take cewa: **((Idan ka kammala al'amurran kira da na jahadi, to ka ƙara himma wajen ibada kada ka gajiyar da kanka akai..**

**Kuma zuwa ga Ubangijinka shi kaɗai ne kawai ya kamata ka fuskantar da buƙatunka)) [as- sharhi: 7 – 8]**, ma'ana idan ka gama wata ibada da biyayya, to ka shagaltu da wata ibadar kana mai neman yardar Allah Maɗaukakin Sarki.

Lallai dawwama akan aiki na gari na cikin manyan ayyukan da Allah mai girma da ɗaukaka ya fi so, kuma hakan dalili ne na kyakkyawan ƙarshe, an ruwaito Hadisi daga Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) tana cewa: Na tambayi Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) akan wane aiki ne Allah ya fi so? Sai ya ce: **(Wanda aka dawwama ana yi koda kuwa kaɗan ne),** kai madalla da wanda Allah ya datar da shi zuwa ga yi masa biyayya, ya kuma kyautata aikin nasa da ɗabi'unsa, sannan ya tsaya da gaske wajen biya wa mutane buƙatunsu, da yaye masu damuwa, da yaɗa alhairi a cikin al'umma da ƙasa baki ɗaya.

Idan Allah Maɗaukakin Sarki ya datar da mumini zuwa ga gabatar da ibadar aikin Hajji, wannan ba yana nufin ya gabatar da ƙarshen biyayya ba ne, hasali ma akwai ayyukan alhairi masu tarin yawa da da zai iya kusantar Allah mai girma da buwaya da su, kaman yawaita ibadu da nafilfili: sallah da azumi da tsayawa wajen samar da maslahar bayi da na ƙasa, da rainon marayu, da gaisar da marasa lafiya, da sauransu cikin ayyukan da za su ɗaukaka darajarsa da matsayinsa a wurin Allah Maɗaukakin Sarki, an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: (**Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: Duk wanda ya ƙi waliyyi na, to ina sanar da shi ya shirya yaƙi da ni, bawana bai taɓa kusanta da ni da wani abu da ya fi abin da na farlanta masa ba, bawana ba zai gushe yana kusanta ta da nafilfili ba, har sai na so shi, idan na so shi**

**zan zama masa jinsa da yake ji da shi, da ganinsa da yake gani da shi, da hannunsa da yake riƙe abu da shi, da ƙafarsa da yake tafiya da ita, idan ya roƙe ni, wallahi zan ba shi, idan kuma ya nemi tsari na, wallahi zan tseratar da shi).**

Haka ma ya kamata tasirin aikin Hajji ya bayyana a cikin **kyawawab ɗabi'un mahajjanci da mu'amalolinsa,** wannan kam yana cikin alamomin cewa an amshi aikin Hajjinsa, ya yi wa mutane mu'amala da ɗabi'u masu kyau, kuma na gari, ya kuma cike taƙaitawar da yake yi kafin aikin Hajjinsa, hakan ya bayyana a cikin mu'amalarsa tare da iyalansa: uba da uwa da mata da 'ya'ya, da sadar da zumunci, da makamantan haka cikin ayyukan alhairi da biyayya a tare da ɗaukacin mutane, Allah mai girma yana cewa: **((Kai, lallai mutane sun yawaita magana akan al'amarin alƙibla, kai kã ce ita ce alhairi ita ɗaya kacal, wannan kuma ba shi ne gaskiya ba, ba fuskantar wani sashe a gabãshi ko yammaci shi ne kashin-bayan addini ko matattara alhairi ba, matattara alhairi yana cikin abubuwa ne masu dama, wasu suna cikin rukunnan ingantacciyyar aƙida ne, wasu kuma suna cikin tushen ayyuka na gari da ibadu. Na farko shi ne: imani da Allah, da ranar tashin alƙiyama, da hisabi, da abubuwan da za su biyo bayan haka a ranar alƙiyama, da imani da mala'iku da littattafan da aka saukar wa Annabawa, da ma su kansu Annabawan. Na biyu shi ne: bayar da dukiya cikin jin daɗin rai ga talakawa, makusanta da marayu da waɗanda buƙatu da rashi suka yi masu yawa, da matafiyan da guzuri ya yanke masu, ba su da abin da zai isar da su zuwa ga manufarsu, da masu roƙon mutane da buƙata ta tilasta masu yin haka, da kuma ciyarwa don manufar 'yanta bayi da 'yanta wuyayensu ga barin bauta. Na**

**uku: kiyaye sallah. Na huɗu: fitar da zakkar da aka wajabta. Na biyar: cika alƙawari a rai da dukiya. Na shida: haƙuri akan cutar da za ta faɗa wa rai ko dukiya, ko lokacin haɗuwa da abokan gaba a wurin yaƙi. Waɗanda suka haɗa waɗannan aƙidu da ayyuka na alhairi su ne waɗanda suka yi gaskiya cikin imaninsu, su ne waɗanda suka ji tsoron kafirci da ƙasƙanci, suka kuma nesance su))** **[al- Baƙra: 177]**.

Dole ne ibadar aikin Hajji ta bar wani tasiri a cikin ɗabi'un mahajjanci, domin dai ibadar Hajji ba surkulle da babu wata manufa a cikinta ba, hasali ma ibada ce da aka shar'anta domin da ɗaukaka girman ɗan Adam, ta kai shi zuwa ga ƙololuwar ɗabi'u, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Hajji na kasancewa ne a wasu watanni da kuka sani, domin dai al'amarin Hajji sananne ne a wajenku tun zamanin Annabi Ibrahim (AlaiHis-Salãm), wanda shi ne: watan Shawwal da Zul- ƙi'ida da Zul- haj, duk wanda ya ƙuduri aniyar aikin Hajji a cikin waɗannan watanni, ya kuma fara shi, to, ya kiyaye ladubbansa, cikin ladubban Hajji: lallai ne mai harama ya tsarkaka ga barin kusantar mata, da saɓo na zagi da makamantan haka, haka ma ya nesanci gardama da ba'a tare da waninsa cikin mahajjata, ya nesanci duk wani abin da zai kai zuwa ga faɗa da husuma, duka wannan saboda mahajjanci ya fita daga harami yana cikin tsarkake zuciya, ya yi ƙoƙari matuƙa wajen aikata alhairi da neman lada daga Allah ta hanyar aikata ayyuka na gari, lallai Allah yana da cikakken masaniya game da haka, zai kuma saka masa akan haka, ku yi guzuri da tsoron Allah da bin umurninsa da nesantar haninsa saboda lahirarku, lallai wannan shi ne fiyayyen guzuri, ku ji tsoron Allah akan abin da kuke**

**aikatawa da wanda kuke bari, kamar dai yadda hakan shi ne aiki da hankali da hikima, kada ku gurɓata ayyukanku da tabban son zuciya da neman duniya))** **[al- Baƙra: 197]**, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya zo wannan ɗaki, bai yi zantuttukan batsa ba, bai kuma yi fasiƙanci ba zai koma tamkar yadda mahaifiyarsa ta haife shi)**, an tambayi Imam al-Hasanul Basriy (Allah ya ƙara masa rahama) cewa: shin karɓaɓɓen aikin Hajji ba shi da sakamako sai aljanna? Sai ya ce: alamar tabbatar haka shi ne ya dawo yana mai gudun duniya, yana kuma kwaɗayin lahira, aka sake tambayarsa: shin sakamakon aikin Hajji shi ne gafarta zunubai? Ya ce: alamar tabbatar haka shi ne ya ƙaurace wa munanan ayyukan da yake yi.

Idan ibada ba ta yi tasiri a cikin ɗabi'un ɗan Adam ta hanyar kyautata su ba, to lallai ba ta da wani ƙima a duniya, balle har a amfana da ita a ranar lahira, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Shin ko ku san wane ne muflisi?)**, sai suka ce: Ya Manzon Allah, muflisi a cikinmu shi ne: shi ne wanda ba shi dukiya, da kayan alatu na duniya, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Muflisi a cikin al'umma ta shi ne wanda a ranar alƙiyama zai zo da sallarsa da azuminsa da zakkarsa a cike, amma kuma ya zagi wannan, ya kuma yi wa wancan ƙazafi, ya ci dukiyar wannan, ya zubar da jinin wancan, ya daki wannan, a biya wannan daga cikin kyawawan ayyukansa, wancan ma daga kyawawan ayyukansa, har sai idan kyawawan ayyukansa sun ƙare kafin a gama biyan kura-kuran da ya tafka, sai a ɗauko zunubansu a jibga masa, sannan a jefa shi cikin wuta)**, haka ma lokacin da aka tambayi (SallalLahu alaiHi wa sallam): Ya Manzon Allah, lallai ana faɗin

yawan sallar wance da azuminta, da sadakarta, amma dai tana cutar da maƙwabtanta da harshenta, sai ya ce: **(‘yar wuta ce)**, aka ce: wance kuma ana faɗin ƙarancin azuminta da sadakarta da sallarta, amma dai tana sadaka da kwanukan cikwi, ba kuma ta cutar da maƙwabtanta da harshenta, sai ya ce: **(‘yar aljanna ce)**.

A cikin abubuwan da ya kamata bawa ya kiyaye akwai: **kyakkyawan ƙarshe,** abin da hakan yake nufi shi ne: Allah Maɗaukakin Sarki ya datar da bawansa kafin wafatinsa da nesantar ayyukan da za su sanya Allah ya yi fushi da shi, ya kuma sauƙaƙa masa hanyoyin tuba daga zunubai sa saɓon da ya aikata, ya kuma fuskancin Allah da ayyuka biyayya da na alhairi, sannan mutuwa ta riske shi yana kan wannan kyakkyawan yanayi.

Ganin cewa ɗan Adam a duniya yana dogaro ne da ayyukan da yake ne ya sanya datar da shi akan ayyukan alhairi da dawwama akansu har zuwa ƙarshen rayuwa alama ce da take nuna cewa ya yi kyakkyawan ƙarshe, kaman dai yanda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) y aba mu labari a inda yake cewa: **(Lallai abin lura a cikin ayyuka shi ne ƙarshe)**, a wata ruwayar kuma ya ce: **(Ayyuka tamkar masaki ne, idan ƙasansa ya yi daɗi, samansa ma zai yi daɗi, idan ƙasansa ya lalace, samansa ma sai ya lalace)**; saboda haka, dole ne kowane mutum ya yi aiki tuƙuru saboda ƙarshensa ya yi kyau, ya shirya gamuwa da Allah mai girma da ɗaukaka da kyawawan ayyuka, kaman yanda Alƙur’ani mai girma ya fuskantar da mu zuwa ga haka a inda Allah yake cewa: **((Duk wanda yake fatan ya haɗu da Ubangijinsa, to ya aikata ayyuka na gari, kada ya haɗa bautar Ubangijinsa da bautar komai))** **[al- Kahfi: 110]**, duk wanda ya ji

tsoron Allah Maɗaukakin Sarki, ya kuma yi wa umurninsa biyayya, ya nesanci abubuwan da ya hana, to kuwa lallai Allah ya datar da shi zuwa ga ayyukan alhairi, sannan kuma a haka zai amshi ransa, kaman yanda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana haka a inda yake cewa: **(Idan Allah yana son bawansa da alhairi sai ya yi amfani da shi)**, sai aka ce: Ya Manzon Allah, yaya ne Allah zai yi amfani da shi? Sai ya ce: **(Zai datar da shi da ayyuka na gari ne kafin ya mutu),** a wata ruwayar kuma ya ce: **(Idan Allah yana son bawansa da alhairi sai ya zaƙaƙa shi)**, sai aka ce: mene ne ma'anar **"ya zaƙaƙa shi"**? sai ya ce: **(Allah zai buɗa masa akan wani aiki na gari kafin ya rasu, sannan a karɓi rayuwarsa akan haka)**, abin lura a ayyuka shi ne ƙarshensu, duk wanda Allah mai girma da ɗaukaka ya datar da shi da ayyukan biyayya da na ibadu, ya kuma dawwama akan ayyukan alhairi har zuwa cikawarsa, to kuwa lallai ya yi kyakkyawan ƙarshe, yana cikin masu arzikin lahira da za su rabauta da aljanna, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai waɗanda suke da rabon arziki a lahira aljanna ce mazauninsu, za kuma su dawwama muddin sammai da ƙasa suna nan har zuwa yanda Ubangijinka ya so, wannan kyauta ce da babu ƙwauro a ciki)) [Hud: 108].**

A cikin darussan da za mu ɗauka daga aikin Hajji, sawa'un ga mahajjanci ne, ko wanda ba mahajjanci ba akwai: cikakkiyar sallama wa Allah Maɗaukakin Sarki a komai, tare da riƙo da asbab, da kuma imani da cewa lallai gaba ɗayan al'amari na Allah ne, kuma duk abin da Allah ya ƙaddara zai kasance, ko mene ne kuwa wannan abin, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Sam bai kamata mumini da mumina su zamo suna da zaɓi idan Allah da Manzonsa suka hukunta wani al'amari a**

**cikin abubuwan da suka shafe su ba, duk wanda ya saɓa wa Allah da Manzonsa, to babu shakka ya ɓace, ɓacewar ma ta fili))** **[al- Ahzab: 36]**, haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Duk abin da Allah ya buɗa wa mutane na jinƙai, to babu wanda ya isa ya hana, haka ma abubuwan da ya hana babu mai iya tunkuɗa masu su bayan shi, lallai shi Allah mabuwayi ne mai cikakkiyar hikima))** **[Fatir: 2]**, haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Idan Allah ya nufe ka da wata cutarwa, babu mai iya yaye maka ita sai shi, haka ma idan ya nufe ka da wani alhairi, lallai shi mai iko ne akan komai.. Shi ne gagararren da yake saman bayinsa, shi ne mai yawan hikima, kuma cikakken masani))** **[al- An'am: 17 – 18]**, lallai cikakkiyar sallama wa Allah Maɗaukakin Sarki alama ce ta imani, ginshiƙi ne a cikin ginshiƙan Musulunci, kuma hakan ba zai tabbata ba sai idan mutum ya kyautata wa Allah Maɗaukakin Sarki zato, idan ya yarda da abin da Allah ya ƙaddara, ya sallama al'amarinsa zuwa ga Allah, to a lokacin zai ji daɗi da ni'imar yarda, ya kuma sami natsuwa da aminci.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

---------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwa Musulmai:** Lallai mahajjanta sun ribata –da ikon Allah- da gafarta zunubansu, Allah ya yaba kai- komonsu, ya kuma ba su lada akan ayyukansu, saboda haka a kiyaye yaudaruwa da yabon mutane, shi aikin Hajji ba laƙabi ne da mutum yake samu ba, ba kuma dalili ne na fankama da alfahari a tsakanin mutane ba, ya kamata mahajjanci ya zamo mai tawadhi'u, da jin kunya bayan dawowarsa, lallai aikin Hajji farali mai girma, ladansa yana da yawa, duk wanda ya gabatar da shi, ya ɗauki wahalhalunsa zai ji daɗin haka a cikin zuciyarsa, hakan kuma zai yi tasiri a cikin rayuwarsa ta hanyar ƙasƙantar da kai ga Allah Maɗaukakin Sarki, da ƙasƙantar da kai wa bayin Allah, ba zai taɓa bari girman kai ya shige shi ba, ba kuma zai taɓa yarda ji-ji da kai ya kutsa cikin aikin biyayya da ya gabatar ba, babu wani aiki da mumini zai yi shi cikin ikhlasi, da gaskiya wajen niyya face ya sake sanya shi yin hoɓɓasa wajen gabatar da wani aiki na biyayya, da ibadun da suke a sama da wanda ya yi, da haka zai ta samun ɗaukaka daga ibada zuwa wata ibadar, daga biyayya zuwa wata biyayyar, har dai ya kai zuwa ga matakin Ihsani, lallai wannan alama ne na cewa an karɓi aikin ɗa'a da ya gabatar a baya.

Lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana mana cewa su muminai da suke gaggawa wajen gabatar da ayyukan alhairi a kullum suna tsaka- tsaki ne, tsakanin tsoron kada ya zamo ba a amshi aikinsu ba, da kuma fata gami da kwaɗayin an amsa, inda kuma za su sami lada akansa, Allah mai girma yana cewa: **((Lallai su ne waɗanda abin tausayi ne su saboda tsoron Ubangijinsu.. kuma su ne waɗanda suke imani da ayoyin Ubangijinsu.. kuma su ne waɗanda ba sa haɗa wani da Ubangijinsu a wurin bauta.. kuma su ne waɗanda suke yin**

**sadaka da abin da Allah ya ba su, zukatansu kuma suna cike da tsoron cewa lallai za su koma zuwa ga Ubangijinsu, waɗannan kam su ne masu yi rige- rige wajen aikata alhairi, su kam sun yi zarra a ciki)) [al- Muminuna: 57 – 61]**, Imam Ibn Kasir (Allah ya ƙara masa rahama) yana cewa: "Ma'ana: duk da kyautatawarsu, da imaninsu, da kuma ayyukansu na gari, amma suna tsoro Allah Maɗaukakin Sarki, suna cikin razani na kada su sauya, an ruwaito Hadisi daga Ummul muminina Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: Ya Manzon Allah, shi maganar Allah Maɗaukakin sarki: **((Kuma su ne waɗanda suke yin sadaka da abin da Allah ya ba su, zukatansu kuma suna cike da tsoron cewa lallai za su koma zuwa ga Ubangijinsu)) [al- Muminuna: 60]**, su ne waɗanda suke sata, da zina, da shan giya, alhalin suna tsoron Allah? Sai ya ce: **(A'a, ya 'yar Abubakar, ya 'yar as- Siddiƙ, wanda yake sallah, yake kuma azumi, yake sadaka ake nufi, shi ne wanda yake jin tsoron Allah Maɗaukakin Sarki).**

Lallai mumini na gaskiya ba ya damuwa da yawan ibadu da nafilfili, kaman yanda yake damuwa da amsar aikinsa, ko rashin amsa, gwargwadon irin yanda waɗannan ibadun suka yi tasiri a cikin rayuwarsa, lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya umurci Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) da yin aiki da ƙoƙari wajen biyayya, kada ya ga ƙanƙancin wani aiki balle ya daina, kada kuma ya ga yawan wani aiki balle ya ruɗe shi, lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ba mu labarin cewa ji-ji da kai abu ne da yake halakar da mai yi, ya kuma lalata masa ayyukan da ya gabatar, an ruwaito Hadisi daga Ibn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: (Abubuwa masu halakarwa

guda uku ne: mutum ya riƙa ji-ji da kansa, da tsananin rowa da mai shi yake yi masa biyayya, da kuma son zuciya da ake binsa).

**Ya Allah Ubangiji, muna roƙonka ka taimake mu wajen ambatonka, da gode maka, da kyautata yi maka bauta, ka kuma datar da mu zuwa ga bin hanyoyin yi maka biyayya da ibada.**

**- 56 –**

# MA’ANAR HIJIRA TSAKANIN JIYA DA YAU

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((In ma ba ku taimaka wa Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ba, to ku sani tabbas Allah ya riga ya taimake shi a lokacin da kafirai suka fitar da shi daga garin Makka su biyu, lokacin da suke cikin kogo da yake faɗa wa abokinsa cewa: kada ka damu, lallai Allah yana tare da mu, sai Allah ya saukar masa da natsuwa, ya kuma ƙarfafe shi da rundunar da ba ku iya ganinta, ya kuma sanya kalmar kafirai ta zamo a ƙasa, lallai kalmar Allah ita ce a sama, tabbas Allah cikakken mabuwayi ne, mai kuma cikakkiyar hikima)) [at- Tauba: 40].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lokacin da Ƙuraishawa suka tsananta wajen cutar da sahabban Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) a garin Makka, Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam) -a shekara ta biyar da aiko shi- ya yi masu izinin yin hijira zuwa Habasha, yana mai ce masu: **(Lallai akwai Sarki a ƙasar Habasha da ba a iya zaluntar kowa a ƙarƙashin mulkinsa, ku**

**tafi can zuwa har Allah ya kawo waraka, da mafita daga halin da kuke ciki)**, sai wasu daga cikin Sahabbai suka fita zuwa can, suka sauka a ƙasar, suna masu amfana da alhairanta, da kuma kyakkyawan maƙwabtaka, suka sami aminci yin addininsu, suka bauta wa Ubangijinsu, har zuwa lokacin da suka sami labarin cewa mutanen Makka sun shiga Musulunci, sai suka ɗauki matakin sake komawa garin Makka, da suka ga saɓanin abin da aka faɗa masu, suka kuma sake fuskantar cutarwa da tsangwama, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sake yi masu izinin yin hijira a karo na biyu zuwa Habasha, jagoran wannan tawaga ta masu hijira shi ne Sayyiduna Ja'afar Bn Abuɗalib (Allah ya ƙara yarda da shi).

Lokacin da Ƙuraishawa suka san cewa Musulmai suna cikin kariya da aminci ƙarƙashin wannan adalin Sarki, sai suka nufi su sake sanyawa a dawo da su a karo na biyu, sai suka aika wa da Najjashi da ɗan saƙo, suna masu neman ya sallama su a hannunsa, sai ya ce masu: **A'a, wallahi ba zan sallama mutanen da suka fake a gari na ba, mutanen da suka zaɓi su yi maƙwabtaka da ni akan kowa, lallai sai na kira su na ji ta bakinsu,** daga nan ne Sayyiduna Ja'afar Bn Abiɗalib (Allah ya ƙara yarda da shi) ya tsaya domin ya mayar da martani akan ƙarai-rayin da Ƙuraishawa suka tafka, da abubuwan da suka riya, sai ya ce: **Ya mai martaba Sarki, a da mu mutane ne da muke bauta wa gumaka, muna cin mushe, muna halatta abubuwan da aka haramta, muna aikata alfasha, muna yanke zumunci, muna cutar da maƙwabta, mai ƙarfi a cikinmu yana danne mai rauni, a haka muke, har Allah ya aiko mana da Manzo daga cikinmu, mun san danginsa, da gaskiyarsa, da amanarsa, da kamewarsa, sai ya kira mu zuwa ga Allah domin**

**mu kaɗaita shi, mu kuma bauta masa, mu kuma ƙaurace wa abubuwan da mu da iyayenmu muke bauta wa maimakonsa na duwatsu da gumaka, ya kuma umurce mu da yin gaskiya wajen magana, da kiyaye amana, da sadar da zumunci, da kyautata maƙwabtaka, da kamewa ga barin abubuwan da aka haramta da jinanai, ya kuma hana mu aikata alfasha, da zancen ƙarya, da cin dukiyar maraya, da yi wa kamammun mata ƙazafi, ya umurce mu da mu bauta wa Allah shi kaɗai, kada mu haɗa shi da kowa, ya umurce mu da yin sallah, da zakka, da azumi,** -Sayyiduna Ja'afar (Allah ya ƙara yarda da shi) ya kawo al'amurran Musulunci- sannan ya cigaba da cewa: **Sai muka gasgata shi, muka yi imani da shi, muka kuma bi shi akan abin da ya zo da shi, muka bauta wa Allah shi kaɗai, ba mu haɗa shi da wani a wajen bauta ba, muka nesanci abubuwan da ya haramta mana, muka halatta abubuwan da ya halatta mana, sai mutanenmu suka tsangwame mu, suka cutar da mu, suka fitine mu a cikin addininmu, kawai saboda su dawo da mu zuwa ga bautan gumaka koma bayan bautan Allah, mu kuma halatta munanan abubuwan da a da muke halattawa, da suka tsangwame mu, suka kuma zalunce mu, suka wahalar da mu, suka hana mu yin addininmu, sai muka fita daga garinmu zuwa garinka, muka zaɓi mu maƙwabtace ka akan wani ka, mun yi ƙwaɗayin zama a ƙarƙashinka, ya mai martaba Sarki, mun kuma yi fatan cewa ba za a iya zaluntar mu a lokacin da muke ƙarƙashin mulkinka ba,** sai Najjashi ya ce masa: **Shin kana tare da wani abu cikin abubuwan da ya zo da shi?** Sai Ja'afar ya ce masa: **ƙwarai kuwa,** sai Najjashi ya ce: **karanto mini na ji, sai ya karanta nasa farkon suratu Maryam,** ta ce: Najjashi ya yi kuka har

gemunsa ya jiƙe, haka ma Pastocin da suke tare da shi sun yi kuka saboda karatun da suka ji, sannan Najjashi ya ce: **Wallahi wannan maganar ta fito ne daga hasken da Annabi Isah ya zo da shi, ku tafi abin ku, wallahi ba zan sallama ku zuwa gare su ba har abada.**

Lallai wanda ya kalli waɗannan Hijira guda biyu zuwa Habasha da idon basira zai fahimci cewa lallai hijirar Musulman farko ba ta kasance daga ƙasar kafirci zuwa ƙasar Musulunci ba ne, domin asali ne shi bai wa ƙasashe kariya, da rashin barin su a hannun azzalumai, ko 'yan ta'adda, hijirar ta kasance ne daga ƙasar da tsoro ya cika zukatan mutane, zuwa ga ƙasar aminci da tsaro, saboda Najjashi a lokacin ba Musulmi ba ne, kawai dai adalin Sarki ne da mutane suka sami aminci a cikin addininsu, da rayukansu, da dukiyoyinsu, sakamakon maƙwabtaka da shi, saboda haka ne aka ce: **"Allah Maɗaukakin Sarki yana taimako ƙasa mai adalci koda kuwa ta kafirai ce, yana kuma ƙin taimakon ƙasa azzalima koda kuwa ta Musulunci ce", mulki zai iya dawwama da kafirci, amma ba zai dawwama da zalunci ba,** ita azzalumar ƙasa ba za ta taɓa dawwama ba, koda kuwa shugabanta Musulmi ne, lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya adalin shugaba a babban matsayi na ƙololuwa a ranar alƙiyama, zai zamo a farkon mutane bakwai da Allah Maɗaukakin Sarki zai yi masu inuwa da al'arshinsa a ranar da babu wata inuwa sai tasa, da adalcinsa ne ɗaukacin al'umma take gyaruwa, da kuma zaluncinsa ne al'umma take ɓaci.

Da Allah Maɗaukakin Sarki ya yi wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) izinin yin hijira zuwa garin Madina, (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bar garin Makka ne cikin

nasara da taimakon Allah mabuwayin Sarki, saboda hijira wani sauyi ne mai ma'ana saboda gina daula, da kuma samar da rayuwar tare cikin zaman lafiya da 'yan uwantaka, da kuma samar da haɗin kai, da daidaita sahu, saboda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sami damar isar da saƙon Ubangijinsa mai girma da ɗaukaka zuwa ga halittu, saboda haka ne Allah Maɗaukakin Sarki yake cewa: **((In ma ba ku taimaka wa Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ba, to ku sani tabbas Allah ya riga ya taimake shi a lokacin da kafirai suka fitar da shi daga garin Makka su biyu, lokacin da suke cikin kogo da yake faɗa wa abokinsa cewa: kada ka damu, lallai Allah yana tare da mu, sai Allah ya saukar masa da natsuwa, ya kuma ƙarfafe shi da rundunar da ba ku iya ganinta, ya kuma sanya kalmar kafirai ta zamo a ƙasa, lallai kalmar Allah ita ce a sama, tabbas Allah cikakken mabuwayi ne, mai kuma cikakkiyar hikima))** **[at- Tauba: 40].**

A shekara ta takwas bayan hijira ne Allah Maɗaukakin Sarki ya buɗe wa Annabinsa (SallalLahu alaiHi wa sallam) garin Makka, ya ɗaura shi akan garin ƙarara a fili, inda mutane suka shiga cikin addinin Allah ƙungiya – ƙungiya, daga nan sai ma'anar hijira ta sauya daga ƙuntatacciyar ma'ana, zuwa ma'ana mai faɗi da yalwa, ta zamo ba ta da iyaka, domin ta game ɗaukacin ɓangarorin rayuwa, bayan buɗe garin Makka sai hijira daga gari zuwa gari, ko daga ƙasa zuwa ƙasa ta kwaranye, da ma an buƙaci irin wannan hijirar a lokacin rauni, don dai Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Lallai waɗanda Mala'iku suke tambayar su da cewa: mene ne kuke yi har kuka yarda da rayuwar ƙasƙanci da wulaƙanci haka, kuka zalunci kanku? Sai su amsa masu da cewa: mu ɗin raunana ne**

**marasa ƙarfi a bayan ƙasa, wasu mutane ne suke ƙasƙantar da mu. Sai Mala'iku su ce masu: shin ƙasar Allah ba ta da yalwa ne, balle ku yi hijira, maimakon cigaba da zama a cikin ƙasƙancin da kuke ciki? Lallai makomar ire-iren waɗannan mutane da suke aminta su rayu a cikin ƙasƙanci, duk kuwa da suna da ikon gusawa, ita ce azabar jahannama, kuma lallai ita ce mafi munin makoma. Sam bai kamata Musulmi ya rayu cikin ƙasƙanci ba, kamata ya yi ya rayu cikin girma da karamci)) [an- Nisa'i: 97],** hukuncin hijira ya sauya ne bayan buɗe garin Makka, inda Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Babu hijira bayan buɗe garin Makka, abin da ya rage kawai shi ne jahadi da niyya)**.

Da Safwan Bn Umayya ya Musulunta, aka ce masa: babu batun addini ga duk mutumin da bai yi hijira, a lokacin yana cikin garin Makka, sai ya ce: ai kuwa ba ma zan koma gida ba, har sai na fara zuwa Madina, ya kuwa tafi Madina, ya sauka a wurin Sayyiduna Abbas Bn Abdulmuɗallab (Allah ya ƙara yarda da shi), sannan daga baya ya tafi wurin Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam), sai ya ce; **(Abu Wahbi, mene yake tafe da kai?)** sai ya ce: cewa aka yi: babu batun addini ga duk mutumin da bai yi hijira, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Abu Wahbi, ka koma garin Makka ku tattaba akan addininku, lallai hijira ta kwaranye, abin da ya rage kawai shi ne jahadi da niyya),** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Musulmi na gaskiya shi ne wanda sauran Musulmai suka tsira daga sharrin harshensa, da na hannunsa, mai hijira na gaskiya kuma shi ne wanda ya ƙaurace wa abubuwan da Allah ya hana)**.

Duk da cewa hijira na wuri daga garin Makka zuwa Madina ta ƙare daga lokacin da aka buɗe garin Makka, sai dai dukan manyan ma'anoni, da manufofin hijira suna nan har yanzu, su ne kuma suka kamata mu kiyaye su, domin dai tabbas Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya bayyana mana cewa ita hijira sauyi ne mai ma'ana, zuwa ga abin da ya fi falala da kyau, kaman sauyi daga zaman banza, da rashin aikin yi, da kasala, zuwa ga himma, da aiki, da ƙoƙari, da kyautata aiki, daga son kai, da ta'assubanci na jahiliyya, zuwa ga fifita wani akan kai, da nuna 'yan uwantakar mutuntaka ta gaskiya, da imani da bambance – bambancen da ake da su, da kuma haƙƙin ɗan Adam na ya zaɓi abin da yake so, da 'yancin yin addini, da kyautata muƙwabtaka, da kuma aiki tuƙuru wajen gina ɗan Adam a fagen imani, da ilimi, da tunani, da ɗabi'u, da tattalin arziki, da zamantakewa, gini mai kyau da nagarta da zai ba shi daman gina daula, ya kuma sana'anta cigaba, ya kuma biya buƙatun ɗaukacin bil'adama, ya kuma kiyaye karamar ɗan Adam a matsayinsa na ɗan Adam.

Lallai cikakkiyar fahimtar ma'anar hijira tana nufin: lallai hijirar da ba za ta taɓa yankewa ba komin daren daɗewa ita ce: hijira daga jahilci zuwa ilimi, daga ɓata zuwa shiriya, daga munanan ɗabi'u zuwa kyawawan ɗabi'u, daga ɓarna zuwa gyarar da duka za su bayar da gudummuwa wajen gina cigaba, da sake raya ɗaukacin duniya, domin dai addinimu addini ne na gini da raya duniya gaba ɗaya, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah shi ne ya halicce ku daga ƙasa, ya kuma nemi da ku raya doron ƙasa..)) [Hud: 61]**, lallai al'ummarmu al'ummar aiki ne ba al'ummar kasala ba, al'ummar gini ne, ba al'ummar

rusawa da lalatawa ba, al’ummar cigaba ba ne, har abada cibaya ba sifarta ba ce.

Ya zama dole ga kowane Musulmi da yake son addininsa, yake kuma alfahari da shi ya yi aiki wajen ɗaukaka addininsa, da izzar ƙasarsa, yana mai nesantar kowane irin nau’i na karkacewa, da shirme, da wuce gona da iri, kaman dai irin hijirar da ƙungiyoyin ‘yan ta’adda suke yi, suna riya cewa jahadi suke yi a ƙarya, suka ɗaga tutocin ƙarya na yaudara, ko hijira ba bisa ƙa’ida ba da take kai wa zuwa ga halaka, ko ƙasƙanci da wulaƙanci, irin wannan hijira laifi ne a doka, kuma zunubi ne a shari’ance; domin alfarmar ƙasashe tamkar alfarmar gidaje ne, kaman yanda bai halatta ka shiga gidan mutum ba sai da izininsa, haka ma bai halatta ka shiga kowace ƙasa ba sai ta hanyar da doka ta amince, kaman yanda babu wanda yake son a shiga masa ƙasar ta ɓarauniyar hanya, ya kamata shi ma kada ya shiga ƙasar wasu, ko ya lamunci a shiga ƙasar wasu ta ɓarauniyar hanya.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** A wannan lokaci mai muhimmanci ba za mu manta mu tunatar da cewa: lallai watan

Allah Ubangiji “al-Muharram” ɗaya ne daga cikin watanni masu alfarma, an so a yawaita azumi a cikinsa; Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Fiyayyiyar sallah bayan ta farilla ita ce sallah a cikin dare, kuma fiyayyen azumi bayan na watan Ramadhan shi ne azumin watan Ubangiji Allah al-Muharram)**, musamman azumin ranar Ashura, saboda Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Game da Azumin Ashura, ina fatan da shi Allah ya yafe zunuban shekarar da ta gabace shi)**, lokacin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya dawo zuwa garin Madina ya ga Yahudawa suna azumi a ranar Ashura, sai ya ce: **(Wannan fa?)**, sai suka ce: Rana ce mai muhimmanci, rana ce da Allah ya tseratar da Bani Isra'ila daga sharrin maƙiyinsu, sai Annabi Musa ya yi azumi a cikinsa, sai ya ce: **(Ni na fi ku kusa da Annabi Musa)**, sai ya yi azumi, ya kuma umurci mutane da su yi azumi a ranar. Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) ya ce: lokacin da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi azumin ranar Ashura, ya kuma yi umurni da a yi azumi a ranar, sai suka ce: Ya Manzon Allah, ai rana ce da Yahudawa da Kiristoci suke girmamawa, sai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi sallam) ya ce: **(Idan shekara mai zuwa ta zo -in Allah ya yarda- za mu yi ranar tara ga wata)**, ma'ana za mu haɗa ranakun tara da goma ga wata, mu yi azumin, lallai sunna ne yin azumi a ranar goma ga watan al-Muharram, cikan wannan sunna shi ne a haɗe ranakun tara da goma ga watan.

**Muna roƙon Allah ya datar da mu zuwa ga abin da yake so, ya kuma yarda da shi, ya kuma sanya sabuwar shekara a wannan karo ta zamo shekarar ƙaruwar alhairai, da albarka, da nasara, da buɗi ga ɗaukacin ƙasashen Musulmi..**

- 57 –

## DAGA CIKIN DARUSSAN HIJIRAR ANNABI AKWAI:

## GINA SABUWAR DAULA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **((Lallai waɗanda suka yi imani na gaskiya, imanin da ya kai su ga yin Hijira domin taimakon addini da jahadi saboda ɗaukaka kalmar addini, lallai waɗannan su ne suke sauraron babban lada daga Allah, koda kuwa sun gaza a wasu wurare, domin lallai Allah mai yawan gafara ne, yana gafarta zunubai, kuma mai yawan rahama ne, yana yi wa bayinsa rahama da shiriya da lada)) [al- Baƙra: 218].** Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya, shi ne mai yawan buɗi, kuma mai cikakken sani. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa, mai kyawawan ɗabi'u. Ya Ubangiji, ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa, masu fararen gaɓoɓin alwalla a ranar alƙiyama, da duk waɗanda suka bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, b**ayan haka:**

Lallai Hijirar Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam) daga garin Makka zuwa Madina wani babban abu ne

da ya kawo sauyi a tarihin ɗan Adam a doron ƙasa, muna matuƙar buƙatar mu amfana da dukan ma'anonin da take ƙunshe da su wajen cigaban al'umma, da gina kyakkyawar rayuwa, lallai Hijira tamkar wani madambaci ne da ya rarrabe tsakanin gaskiya da ƙarya, kuma sauyi ne mai ma'ana wajen gina ƙasa akan tobulan adalci da daidaito da 'yancin yin addini, da kiyaye karamar ɗan Adam, da kuma dasa fahimtar zaman lafiya da rayuwar tare, da kuma samun dangantaka mai kyau tsakanin al'ummomin da suke rayuwa a ƙasa ɗaya, da kuma bayar da cikakkiyar gudummuwa wajen samar da tattalin arziki mai ƙarfi ta kowace hanya, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya gina daula akan wasu ginshiƙai masu ƙarfi, muhimmai daga cikin sun haɗa da:

**Gina Masallaci:** Lallai farkon aikin da Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya fara da shi bayan ya isa garin Madina, shi ne gina Masallaci; domin dangantakar bawa da mahaliccinsa shi ne ginshiƙin komai, ingantaccen sifantuwa da addini shi ne muhimmin dalili na samar da nagartaccen mutumin da yake gina ƙasa, ba mai rusawa ba, yake kuma raya doron ƙasa ba mai lalata ba, gwargwadon kauce wa nagartaccen karantarwar addini, ko yi masa mummunan fahimta gwargwadon samun kafa mai muni a cikin al'umma, haka ma Masallaci yana da saƙo na ilimi, da na zamantakewa da suke ƙara tabbatar da kyawawan ɗabi'u a rayuwa, da kuma bayar da gudummuwa wajen hidimta wa al'umma.

**Gina tattalin arziki:** Lallai tattalin arziki mai ƙarfi muhimmin jigo ne cikin jiga-jigan daula, ginshiƙi ne mai ƙarfi da ƙasa ba za ta iya gina komai ba idan babu shi, da ƙarfin tattalin arziki ne ƙasashe suke iya sauke nauyinsu na cikin-gida

da na waje, suke kuma iya samar da nagartacciyar rayuwa ga 'yan ƙasa, a duk sanda tattalin arzikinsa ya yi rauni, to kuwa talauci da cututtuka, da rashin tabbas a rayuwa, da ƙaruwar matsaloli ne za su yaɗu, ɗabi'u za su gurɓace, laifuffuka za su yawaita, kuma hakan zai zamo wata dama ce ga maƙiya da suke jiran kowace irin dama, domin su yi amfani da ita wajen durƙusar da ƙasa, da jefa ta cikin ruɗani da rikicin da ba su da iyaka.

Saboda haka ne Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya yi aiki wajen yanda al'ummar Madina za su mallaki tattalin arziki mai ƙarfi da zai ba su daman biyan buƙatun al'ummarsu, da kuma bai wa kawunansu kariya, da kuma tabbatar da zaman lafiya da tsaro, da raya ƙasa, kaman yanda addinin Musulunci ya zo da shi, a dalilin haka ne Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya samar da babbar kasuwa a garin Madina, domin ta zamo wajen samun arziki na halal ta hanyar kasuwanci, ta kuma zamo cibiya na masu sana'o'i, da samar da abubuwan buƙata, wannan kasuwa da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya samar shi ake kira da sunan **"Kasuwar al-Manakhat"**, an ruwaito Hadisi daga Aɗa'u Bn Yasar, ya ce: Lokacin da Sayyiduna RasululLahi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya nufi samar da kasuwa a garin Madina, sai ya tafi kasuwar "Bani Ƙainaƙah", sannan ya zo kasuwar Madina ya buga wurin da ƙafarsa, ya ce: **(Wannan ce kasuwarku, ba za a ƙuntata ba)**, manyan sahabbai sun shiga cikin mabambanta hada- hadar kasuwanci, ba su lamunci su rayu a ƙarƙashin taimakon da yake zuwa masu daga 'yan uwansu mutanen Madina ba; an ruwaito Hadisi daga Sayyiduna Abdurrahman Bn Auf (Allah ya ƙara yarda da shi)

ya ce: Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya haɗa 'yan uwantaka tsakanin Abdurrahman Bn Auf da Sa'ad Bn ar-Rabi' a lokacin da suka zo Madina, inda Sa'ad ya ce wa Abdurrahman; Ni ne na fi kowa arziki a garin Madina, zan raba dukiya ta biyu… sai ya ce: Allah ya yi maka albarka a cikin iyalanka, da dukiyarka, kawai dai ina ne kasuwa?.

Saboda lallai duk al'ummar da ba ta iya samar wa da mallakan abincinta, da tufafinta, da magangunanta, da makamanta ba, to kuwa ba ta iya mallakan komai cikin sha'aninta, ba ta da ra'ayin kanta, ba ta da wata daraja da ƙima, masu hikima suna cewa: **Ka kyautata wa duk wanda ka ga dama, sai ka zamo sarkinsa, ka wadatu ga barin duk wanda ka ga dama, sai ka zamo sa'ansa, ka buƙaci duk wanda ka ga dama, sai ka zama bawansa.** Lallai addininmu mai daraja ya karantar da mu cewa, lallai hannu da yake a sama, yafi hannun da yake a ƙasa alhairi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Hannun sama yafi hannun ƙasa alhairi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Mai bayarwa shi ne a sama, mai roƙo kuma shi ne a ƙasa)**, kuma ko shakka babu, kan cewa wannan ma'anar ta game al'ummomi, da ma'aikatu, da iyalai, da ɗaiɗaikun mutane a tare baki ɗaya, babu wanda bai san muhimmancin dukiya wajen gudanar da al'amurran rayuwa, da cigaban al'umma, da samar da hanyoyin rayuwa masu nagarta, da ɗaukakar al'umma a matakai na cigaba ba, alhairin Allah ya kai zuwa ga Amirus Shu'ara'i, Malam Ahmad Shauƙiy da yake cewa:

"Da ilimi da dukiya ne mutane suke iya gina mulkinsu, ba a taɓa gina mulki akan jahilci da talauci ba".

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya sanya ƙa'idojin da za su tsara waɗannan mu'amalolin, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya kwaɗaitar da jama'a wajen rangwame da sauƙin kai wajen saye da sayarwa, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Allah ya yi rahama ga mutum mai sauƙin kai wajen saye, da sayarwa, da wajen biyan bashi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya hori Musulmai da yin gaskiya da riƙon amana, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Ɗan kasuwa mai gaskiya kuma amintacce yana tare da Annabawa da siddiƙai da shahidai)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya haramta ɓoye kayan buƙata zuwa su yi tsada a fito da su, (SallalLahu alaiHi wa sallam) yana cewa: **(Duk mutumin da ya ɓoye abinci saboda ya yi tsada har na tsawon darare arba'in, to lallai ba shi ba Allah, Allah ma ba shi ba shi)**, kai hasali ma (SallalLahu alaiHi wa sallam) da kansa ne yake bin kasuwa domin sanya ido akan yanda ake saye da sayarwa, yana mai nusar da mutane zuwa ga abin da zai kawo gyara a cikin al'amurransu, an ruwaito Hadisi daga Abuhuraira (Allah ya ƙara yarda da shi) cewa:  Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya wuce ta wani tarin abinci, sai ya shigar da hannunsa a ciki, sai ya ji danshi a ciki, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ya kai mai wannan abinci, mene ne kuma wannan?)**, sai ya ce: Ya Manzon Allah, ruwan sama ne ya jiƙa shi, sai (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ba sai ka sanya shi a sama ta yanda mutane za su gani ba?!)**, sannan (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Wanda ya yi mana algushi ba shi tare da mu)**.

**Yarjejeniyar Madina:** Lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya gina daula mai ƙarfi bayan ya yi hijira, inda ya

bayyana ginshiƙanta a **"Yarjejeniyar Madina"**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa sallam) bai tsaya kawai a haɗa 'yan uwantaka tsakanin mutanen da suka yi Hijira da mutanen Madina masu masaukin baƙi -duk da saɓani da rikicin da suke tsakaninsu- ba, sai da ya kai ga gina 'yan uwantaka ta mutuntaka a wajen shata wannan yarjejeniya ta Madina, wadda ita ce mafi girman kundin tsarin rayuwar zamantakewa da ɗan Adam ya taɓa fitarwa a tarihin bil'adama; ta tabbatar da dukan haƙƙoƙi da wajibai ga ɗaukacin 'yan ƙasa, ta kuma shimfiɗa rayuwar zaman lafiya tsakanin ɗaukaci mazauna ƙasa, a gefe ɗaya kuma, da tsakaninsu da sauran bil'adama a duk inda suke, abin da har ya ba ta daman zama mafi girman yarjejeniya ta mutuntaka a fahimtar rayuwar tare a tarihin ɗan Adam a doron ƙasa, abin da zai tabbatar da haka shi ne : yarjejeniyar da Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ƙulla tare da Yahudawan Madina, da ma wasunsu, inda ya bai wa Yahudawa dukan haƙƙoƙin da Musulmai suke da su na tsaro, da zaman lafiya, da 'yanci, da bayar da kariya na haɗin gwiwa, a cikin muhimman dokokin wannan yarjejeniya akwai: **(Lallai Yahudawa za su rinƙa biyan kuɗi tare da Muminai muddin suna yaƙi a ƙarƙashin tuta ɗaya, kuma lallai Yahudawan Bani Auf da Muminai al'umma ce guda ɗaya, Yahudu za su yi addininsu, haka ma Musulmai za su yi addininsu, bayinsu da kawunansu duka, sai dai wanda ya yi zalunci, ko ya aikata laifi),** a cikin dokokin akwai lamunin 'yancin yin addini, da 'yancin tsaro, da bayar da kariya na bai ɗaya wajen ƙalubalantar duk wanda ya nufi garin Madina da zalunci.

Haka yana nufin cewa: lallai daular Musulunci a garin Madina ta isa ɗaukacin Musulmai, da ma waɗanda ba

Musulmai ba, domin duk wani haƙƙi da muke da shi, to su ma suna da shi, duk kuma wani abu da ya wajaba a kanmu, to su ma ya wajaba akansu, muddin dai sun kiyaye dokokin ƙasa waɗanda su ne suka kiyaye ɗaukacin haƙƙoƙi da wajibai, musamman haƙƙin zaman lafiya, da rashin yin ta'adi da zalunci, da rashin karya dokokin zamantakewa **"kundin tsarin mulki"** da su ne suka tsattsara dangantakar da take tsakanin ɗaukacin mutane.

Lallai rayuwar zaman lafiya tsakanin gaba ɗayan mutane wajibi ne da addini ya gindaya, tilas ne na zamantakewa da rayuwar ɗan Adam ta yau da kullum ta tabbatar, kuma hakan ba zai tabbata ba sai idan ɗaukacin 'yan ƙasa sun ji suna da haƙƙoƙi da wajibai iri ɗaya ba tare da bambanci akan addini, ko ƙabila, ko waninsu ba, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Babu tilas a cikin al'amarin addini, tuni gaskiya ta bambanta da ƙarya...)) [al- Baƙra: 256].**

Lallai Annabi (SallalLahu alaiHi wa sallam) da sahabbansa sun zartar da haka a aikace, ba su tirsasa wa kowa shiga addini ba, ba kuma su taɓa rushe wa kowa Coci, ko wurin bautar Yahuduwa, ko ma kowane irin wurin bauta ba, hasali ma wuraren bauta suna da kariya ta musamman a wurin Musulmai, domin addinin Musulunci ya bayar ɗa 'yancin yin addini ga kowa da kowa, babu wanda ya isa ya sauya wannan tsari na bambanci da saɓani; domin babu wanda ya isa ya sauya abin da Allah ya so, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Da a ce Ubangijinka ya so da ɗaukacin waɗanda suke a doron ƙasa sun yi imani, shin kai yanzu tirsasa mutane za ka yi har sai sun yi imani?!)) [Yunus: 99]**, girmama aƙidu da haƙƙoƙi da wajibai, rukuni ne mai girma wajen kafa daula, hakan kuma

yana da tasiri wajen dangantakar al'ummomin da mabambanta mazauna, kowace al'umma tana da aƙida da ƙa'idojin da take girmamawa, ta kuma wajabta wa kanta binsu, tana kuma kallonsu a marsayi mafi girma akan waɗanda ba su ba, kuma tabbas addinin Musulunci ya hana mu cutar da ma'abota wasu addinai na daban da kowane irin abu da zai zama ɓatanci ne ga abubuwan da suke bauta wa, ko ma a gare su su kansu; domin a asali addinai sun zo ne domin jin daɗin bil'adama, Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: **((Kada ku kuskura ku zagi waɗanda suke bauta wa abubuwan da ba Allah ba, balle har su zagi Allah saboda rashin sani, da haka muka ƙawata wa kowace al'umma ayyukan da take yi, sannan a ƙarshe dukansu za su koma zuwa ga Ubangijinsu, shi kuma ya ba su labarin akan abubuwan da suke aikatawa..))** **[al- An'am: 108].**

Haka ma addinin Musulunci ya sanya biyayya da kyautata maƙwabtaka a cikin zukatan mabiyansa, musamman a tsakaninsu da waɗanda ba Musulmai ba, Nassoshi da yawa sun zo sun tabbatar da haka, inda suke bayyana irin yanda ya kamata al'ummar Musulmai su rayu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **((Allah Maɗaukakin Sarki bai hana ku yin taimakekeniya da waɗanda ba su yaƙe ku saboda addininku ba, ba kuma su fitar da ku daga gidajenku saboda haka ba, bai hana ku kyautata masu, ku kuma yi masu adalci ba, lallai Allah yana son masu adalci..))** **[al- Mumtahanat: 8].**

Lallai addinin Musulunci ya umurci mabiyansa da su kiyaye kyakkyawar mu'amala tare da waɗanda ba Musulmai ba, su kuma kula da abubuwan da suka yi imani da shi har a wurin tattaunawa da jidali, ya kuma kwaɗaitar da su akan yin jidalin ma ya zamo da abin da ya fi kyau, Allah Maɗaukakin Sarki

yana cewa: **((Kada ku kuskura ku yi jayayya da Ahlul Kitabi sai da abin da ya fi kyau, in ba waɗanda suka yi zalunci a cikinsu ba, ku dai kawai ku ce: mun yi imani da abin da aka saukar mana, da wanda aka saukar maku, Ubangijinmu da Ubangijinku ɗaya, kuma mu shi muka miƙa wuyanmu zuwa gare shi)) [al- Ankabut: 46].**

Da haka ne wannan yarjejeniya ta Madina ta zamo abin koyi wajen kiyaye karamar ɗan Adam, wadda take aiki wajen kiyaye haɗin kan 'yan ƙasa wajen gina daula, da samar da cigaba, da kiyaye maslahar bil'adama.

**Wannan kenan, ina nema wa kai na da ku gafara daga Allah Maɗaukakin Sarki.**

-------------------------------

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Ina shaida wa babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammadu, bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ya Ubangiji ka yi masa salati da tsira, da albarka, shi da Alayensa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Ya 'yan uwana Musulmai:** Lallai ƙasa tana da babban matsayi da daraja, son ƙasa, da jinta a cikin zuciya, da ba ta kariya abu ne da yake da dangantaka da fiɗirar da Allah ya halicci ɗan Adam akai, hakan wajibi ne da addinin Musulunci mai tsarki ya tabbatar, zamantowa ɗan ƙasa na gari kuma ya farlanta haka, ɗaukacin shari'o'in Allah suka ƙarfafa, lallai Annabi (SallalLahu alaiHi sa sallam) ya buga babban misali wajen kishin ƙasa, da ɗamfara zuciya akanta, a inda (SallalLahu alaiHi wa sallam) yake faɗa wa garinsa na farko "Makka", a

lokacin da yake shirin Hijira zuwa Madina cewa: **(Wane gari ne ya kai ki daɗi, na kuma fi so a zuciya ta, ba domin jama'anki sun fitar da ni ba da ban fita ba)**, lokacin da (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya riga ya yi Hijira zuwa garin Madina, ya zauna a can, ya roƙi Allah ya sanya masa son wannan gari nasa na biyu, ya kuma tabbatar da tsaro gami da kwanciyar hankali a ciki, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa sallam) ya ce: **(Ya Allah Ubangiji, ka sanya mana son Madina kaman yanda muke son Makka, ko ma fiye da haka)**..

Lallai dangantakar da take tsakanin addini da ƙasa, dangantaka ce ta cika juna, ba ta kishiya ba, lallai kiyaye ƙasashe ɗaya ne daga cikin manyan manufofin Shari'a, da kiyaye su ya zama wajibi, babu yanda za a sami tattalin arziki mai ɗorewa ba tare da tabbataccen tsaro mai ɗorewa ba, bai wa ƙasa kariya, da sadaukar da kai dominta abu ne da Shari'a ta buƙata, hakan wajibi ne akan duk wanda yake rayuwa a cikinta, yake kuma shan inuwarta, son ƙasa bai taƙaita kawai a cikin zuciya ba, a'a, dole ne a gan shi a aikace, ta yanda zai amfani mutum a shi ɗaya, da kuma al'umma; dole ne a sadaukar da kai domin ƙasa ta wanzu cikin ƙarfi da izza.

Lallai kishin ƙasa na haƙiƙa ba shi ne tuta da ake yawan ɗagawa, ko taken da ake rerawa ba, shi kishin ƙasa imani ne da aiki gami da baiwa, kishin ƙasa tsari ne na rayuwa, da jin ƙasa a cikin zuci, da kuma jin ƙalubalen da take fuskanta, da damuwa da damuwarta, da kuma yin farin ciki idan ta cin ma manufofinta, da kuma zama a cikin shiri a koda yaushe domin sadaukar da kai dominta.. Kai madalla da gwarazan da suka gasgata abin da Allah ya yi masu alƙawari, suka sadaukar da

rayukansu saboda Allah a wajen kare ƙasashensu, da ɗaukaka darajarsu..

**Ya Allah Ubangiji, ka kiyaye mana ƙasashenmu, da al'ummominmu, da jami'an sojojinmu, da 'yan sandanmu daga dukan sharri, ka mayar wa duk wani mai makirci, da maƙetaci, da mai hassada da aniyarsu.**

## Abubuwan da suke ciki


| | | |
|---|---|---|
| | Gabatarwa …………………………………………………………………….. | **3** |
| 1. | Dalilai Gami Da Tasirin Kasancewa Tare Da Allah Mai Girma Da Buwaya ……………………………………………………………………. | **5** |
| 2. | Wannan Shi Ne Musulunci.. …………………………………………….. | **17** |
| 3. | Sakamakon Da Imani Yake Gadarwa ………………………………. | **28** |
| 4. | Ma'anar Aiki Na Gari Da Mummunan Aiki ……………………….. | **39** |
| 5. | Ambaton Allah Da Tasirinsa Wajen Daidaita Ɗan Adam …….... | **52** |
| 6. | Muhimmancin Da Alƙur'ani Ya Bai Wa Kyawawan Ɗabi'u ….. | **63** |
| 7. | Kyawawan Ɗabi'u Na Mutuntaka A Suratul Hujrat …………… | **78** |
| 8. | Sunnar Manzon Allah Da Matsayinta A Shari'a …………………. | **86** |
| 9. | Rayuwar Annabi (S.A.W) Misali Ne Na Ingantaccen Musulunci.. ………………………………………………………………... | **96** |
| 10. | Shaidar Annabi Ga Sahabbansa Da Falalarsu: Darussa Da Izina ……………………………………………………………………………. | **106** |
| 11. | Kayatacciyar Sura Ta Rayuwar Sahabbai.. ……………………….. | **118** |
| 12. | Musulunci Aiki Ne Da Ɗabi'a: Misalai Daga Rayuwar Tabi'ai.. ……………………………………………………………………… | **129** |
| 13. | Rangwame Da Sauƙi: Manyan Alamu Na Girman Shari'ar Musulunci …………………………………………………………………. | **141** |
| 14. | Haƙƙoƙin Iyaye Da Makusanta ………………………………………. | **153** |
| 15. | Wajibin Ɗalibi Da Na Malami …………………………………………. | **164** |
| 16. | Al'ummar Iƙra'.. Al'ummar Kyautata Aiki: Tsakanin Malaman Al'umma Da Malaman Fitina ……………………………... | **174** |
| 17. | Na'uyi Da Alhakin Da Allah Ya Ɗaura Akan Bayi (Mas'uliyya) ……………………………………………………………….. | **184** |
| 18. | Ma'anar Yarjejeniyar Bayar Da Aminci A Wannan Zamani … | **195** |
| 19. | Kiyaye Al'amurra Da Maslahar Al'umma Na Bai Ɗaya.. ……… | **205** |
| 20. | Kasuwanci: Ka'idoji Da Ladubba …………………………………… | **218** |
| 21. | Ruhin Aiki Cikin Jama'a Da Ka'idojinsa …………………………. | **229** |

| | | |
|---|---|---|
| 22. | Dalilai Na Zahiri Da Na Baɗini Wajen Yaye Bala'i.. Da Wajibcin Yi Wa Shugabanni Biyayya ………………………………… | **239** |
| 23. | Gudanar Da Komai Akan Ka'idar Bin Sababi: Sunna Ce Ta Allah Maɗaukakin Sarki …………………………………………….... | **245** |
| 24. | Rangwame Aƙida Ne Da Tsarin Rayuwa …………………………… | **254** |
| 25. | Ladubba Na Bai Ɗaya Da Tasirinsu Wajen Cigaban Al'umma ……………………………………………………………………….. | **264** |
| 26. | Ladubba Da Haƙƙoƙi Na Bai Ɗaya Da Tasirinsu Wajen Gina Al'umma Da Cigaba ……………………………………………………. | **275** |
| 27. | Gina Ingantaccen Tattalin Arziki Da Tasirinsa Wajen Wanzar Da Kwanciyar Hankalin Al'umma ……………………….... | **286** |
| 28. | Fiƙhun Gina Kasashe …………………………………………………… | **295** |
| 29. | Amfanar Al'umma A Ma'aunin Shari'a …………………………… | **306** |
| 30. | Ma'anar Shahada Tsakanin Gaskiya Da Karya ………………..... | **316** |
| 31. | Ma'anar Shahada Da Matsayin Shahidai ………………………….. | **326** |
| 32. | Falalar Shahada Da Alhakin Iyalan Shahidai Akanmu ……….. | **333** |
| 33. | Matsayin Shahidai Da Sadaukar Da Kai Wajen Kare Kasa … | **345** |
| 34. | Abokantaka Da Tasirinsa Wajen Gina Al'umma ……………….. | **355** |
| 35. | Himma Mai Girma Ita Ce Hanyar Cigaban Al'ummomi ………. | **368** |
| 36. | Ginshiƙan Gina Kasashe …………………………………………….... | **379** |
| 37. | Haɗin Kan Kasa Ne Hanyar Samun Karfinta …………………….. | **389** |
| 38. | Haƙƙoƙin Matasa Da Wajibansu ……………………………………. | **398** |
| 39. | Hatsarin Yaɗa Kare- Rayi Da Jita – Jitaa Cikin Al'umma …….. | **407** |
| 40. | Hatsarin Da Yake Tattare Da Shaye- Shaye Da Tasirin Ta'amuli Da Kwayoyi Akan Ɗan Adam Da Al'umma Gaba Ɗaya ……………………………………………………………………….. | **420** |
| 41. | Alamun Girman Kai Da Toshe Hanyar Allah …………………….. | **429** |
| 42. | Hatsarin Munafunci Da Ha'inci Ga Al'umma Da Kasashe …… | **440** |
| 43. | Yi Wa Uwa Biyayya Sanadi Ne Na Samun Albarka A Duniya Da Samun Rahama A Lahira …………………………………………... | **451** |
| 44. | Ribatar Lokutan Biyayya Da Alhairai ……………………………... | **461** |
| 45. | Isra'i Da Mi'iraji ………………………………………………………….. | **473** |

| | | |
|---|---|---|
| 46. | Tare Da Mu'ujizar "Isra'i Da Mi'iraji" ……………………………... | **478** |
| 47. | Sauya Alƙibla Daga Baitul Maƙdisi Zuwa Baitul Harami: Darussa Da Izina ………………………………………………………... | **489** |
| 48. | Ramadhan Watan Ibada Da Aiki …………………………………….. | **501** |
| 49. | Ramadhan: Watan 'Yanta Bayi Ga Barin Wuta ………………… | **512** |
| 50. | Ramadhan: Watan Baiwa Da Karamci …………………………….. | **523** |
| 51. | Ramadhan: Watan Imani Da Samar Da Gwaraza ……………... | **536** |
| 52. | Ramadhan: Watan Biyayya Da Sada Zumunci Da Samun Rahamar Allah ………………………………………………………………. | **549** |
| 53. | Bayan Ibadun Ramadhan Sai Kuma Me Ne? ……………………. | **561** |
| 54. | Darussa Daga Huɗubar Hajjin Ban- Kwana ……………………. | **573** |
| 55. | Bayan Aikin Hajji Sai Kuma Me Ne? ………………………………... | **584** |
| 56. | Ma'anar Hijira Tsakanin Jiya Da Yau ………………………………. | **596** |
| 57. | Daga Cikin Darussan Hijirar Annabi Akwai: Gina Sabuwar Daula ……………………………………………………………………. | **605** |